
بسم الله الرحمن الرحيم

Gabatarwa

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Tsira da amincin Allah su tabbata ga cikamakin annabawa da manzanni, Annabinmu Muhammad da Iyalansa da Sahabbansa da waɗanda suka bi tafarkinsa da kyautatawa har zuwa tashin ƙiyama.

Bayan haka:

Huɗuba a musulunci wani abu ne mai asali a tarihin al'ummar musulmai. Huɗubar juma'a ta daɗe tana taimakawa wajen gina al'umma da haskaka zukatansu, da shiryar da duk wanda yake cikin ɗimuwa. Tana kuma zaburar da al'umma tare da faranta wa duk wani mai riƙo da addininsa rai, tana kuma ƙara masa ƙarfin gwiwa. Huɗuba minbari ne na masu wa'azi, kuma it ce tutar da suke ɗagawa a koda yaushe. Kamar yadda ta zama hanyar nasiha da faɗakarwa da karantarwa. Ta hanyarta jahili kan samu ilimi, wanda ya manta ta hanyarta yakan tuna, sannan tana amsa fatawar mai yin fatwa. Mai huɗuba yakan taɓo duk wasu matsalolin al'umma, yakan yi tsokaci akan abubuwa sababbi da kan faru, ta hanyar kwaɗaitarwa da tsoratarwa, da yin amfani da ƙissoshi da karin magana, da dogaro bisa tabbatattun al'amura tare da wasu darussa, da jan hankali da lallashi. Wannan yakan sa mutum ya ƙara jaddada imaninsa, ya kammala nakasar dake tare da shi. Mai laifi kuma ya tuba, duk wani wanda ya sauka daga kan hanya ya komo kanta, mai barci ya farka, mai son zuciya ya watsar da son zuciyarsa. A samu kyakkyawan haɗin kai wanda zai taimaka wajen ba wa addinin Allah kariya da yaɗa shi. Ɗaukakar da musulmai suka rasa ta dawo. Wannan aiki ba ƙaramin aiki ba ne, aiki ne mai cike da mahimmanci da daraja. Kai lalle huɗuba ba ƙaramin aike ne ba inda a ce mutane sun fahimci hakan.

Matsayin Huɗuba A Musulunci

Huɗuba a musulunci tana da babban matsayi da tasiri, da manufa da saƙo da rawar da take takawa. Kaɗan daga cikinsu su ne:

1. Babban abin da yake fito da mahimmacin huɗuba shi ne, kasancewarta tana daga cikin aikin fiyayyen halitta gaba ɗaya wato Annabi Muhammad (S.A.W.) da kuma manyan malamai da masu wa'azi a cikin wannan al'umma.
2. Kasancewarta ɗaya daga cikin ibadu a musulunci da ake yenta a mafificiyar rana wato juma'a, sannan a guri mafi tsarki a doron ƙasa wato masallatai.
3. Hanya ce ta isar da kira, tana kunshe da umarni da kyakkyawan aiki da hana mummuna. Kuma hanaya ce ta tarbiyya da karantarwa da kawo gyara cikin al'umma.
4. Hanya ce ta zaburar da jama'a da gamsar da su, da dasa musu son gaskiya a zukatansu. Domin tana ƙunshe da kalmomi masu cike da gaskiya waɗanda sauraronsu yake da tasiri matuƙa a zukata fiye da rubutacciyar magana.
5. Kuma wata damace babba ga masu kira zuwa ga Allah. Domin halartar sallar juma'a wajibi ne akan kowa, hakanan sauraron ita kanta huɗubar wajibi ne. Bugu da ƙari kuma babba da yaro, mai ilimi da marar ilimi, mai kuɗi da talaka, kowa da kowa dole ne ya zo sallar juma'a, kuma duk sati ƙaruwa suke ba sa

raguwa.

6. Hakanan huɗuba a yau ita ce mafi dacewar hanya ta fahimtar da mutane sahihin addini, da kuma mayar da martini ga maƙiya Allah waɗanda kulluma suke cara don rikirkita hankalin mutane da dulmiyar da su cikin hanayar ɓarna.

Bayanin Hukunce-Hukuncen Huɗubar Juma'a a Taƙaice

Na Ɗaya: Hukuncin Huɗubar Sallar Juma'a:

Malamai sun kasu gida biyu wajen sharɗanta huɗuba a sallar Juma'a:

Na farko: Su ne Mafi yawan malamai, Hanafiyya da yawancin Malikiyya da Shafi'iyya da Hanbaliyya suna ganin huɗuba sharaɗi ce ga ingancin sallar jama'a.

Kashi na biyu: su kuma suna ganin mustahabbi ce, ba wajibi ba.

Amma magana mafi inganci ita ce maganar farko, wato maganar mafiya yawan malamai. Domin Annabi (S.A.W) bai taɓa fashin huɗubar juma'a ba. Kuma akan haka magabata suke, tare da inkari ga wanda ya saɓawa hakan.

Yin huɗuba biyu Sharaɗi shi ne, kamar yadda aka karbo hadisi daga Abdullahi ɗan Umar, Allah ya yarda da shi ya ce, Annabi (S.A.W.) ya kasance yana yin huɗuba guda biyu, kuma yana zama a tsakaninsu.

Na Biyu: Sharuɗɗan Huɗuba:

1. Niyya, domin faɗar Annabi (S.A.W.) cewa, "Dukkan ayyuka sai da niyya, kuma kuwane mutum yana da abin da ya niyyata". Bukhari ne ya ruwaito shi. Kuma ita ma kamar sauran ibadu ce, don haka dole sai an yi niyya.
2. Dole ne a samu mahalarta huɗubar, domin tabbatar manufarta ta faɗakarwa da wa'azi.
3. Kuma a gabatar da ita bayan shigar lokacin sallar juma'a.
4. A fara da ita kafin sallah, don koyi da Manzon Allah (S.A.W.).
5. Kuma liman ya gabatar da ita a tsaye matuƙar dai yana da ikon hakan.
6. Dole ne ya ya ɗaga muryarsa, don ta hakane za a ji abin da yake faɗa.
7. Kuma ya yi ta da larabci, idan yawancin wanɗanda suke sauraronsa masu jin larabci ne, domin yin haka zai ƙara zaburarwa akan koyan harshen larabci da kuma rashin saɓawa abin da Mazon Allah (S.A.W.) ya yi. Idan kuma yawancin masu sauronsa ba sa jin larabci to sai ya yi ta da harshen da suke fahimta, domin manufar huɗuba ita ce kuyarwa da faɗakarwa ba wai kawai a yi huɗubar ba a tashi. Sai ya riƙa jan ayoyinta da larabci yana fassarawa da yaren da ake fahimata.
8. Jerentawa tsakanin ɓangarorin huɗubar da kuma ita kanta sallar.

Na Uku: Rukkunnan Huɗubar Juma'a:

Magana mafi rinjaye ta malamai, ita ce huɗuba ba ta da wasu rukunnai. Duk sa'adda aka yi abin da ake kira huɗuba a al'adance to shi ke nan an yi huɗuba. Sai dai yana daga cikin kamalar huɗuba ta haɗa abubuwa kamar haka:

1. Godiya da kirari ga Allah.
2. Kalmar shahada.
3. Salati ga Annabi.
4. Wa'azi.
5. Karanta wani abu daga cikin Kur'ani.
6. Wasici da tsoron Allah.

Na Huɗu: Sunnonin Huɗubar Juma'a:

1. Yinta akan Minbari, domin koyi da Manzon Allah (S.A.W.). Kuma a sunna ana son minbari ya zama mai matattakala uku ne, domin haka ne Manzon Allah (S.A.W.) yake.
2. Idan liman ya shigo masallaci sai ya yiwa jama'a na ciki sallama kafin ya hau minbari. Kuma ba a samu Annabi (S.A.W.) yana yin nafila ba yayin da ya shigo cikin masallaci ba kafin juma'a. domin da zararar ya shigo ake kiran sallah, sannan ya yi huɗuba.
3. Idan kuma liman ya hau minbari sai ya yi sallama ga ɗaukakin mutane. An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi ya ce, Manzon Allah ya kasance idan ya hau Minbari sai ya yi sallama.
4. Ya zauna akan minbari har sai ladan ya gama kiran sallah.
5. Kiran Sallah ɗaya ne lokacin da liman ya hau minbari, kamar yadda yake a zamanin Manzon Allah (S.A.W.) da zamanin Abubakar da Umar (R.A.). Domin yanzu sha'ani gane shigar lokaci ya sauƙaƙa ba kamar da ba. Don haka babu buƙatar yin kiran sallah na farko wanda Usman (R.A.) ya ƙara domin sanar da mutane kusantowar lokaci.
6. Ana so ya buɗe huɗubasa da "Khuɗubatul Haajah". Ga yadda ma'anar lafazinta yake: " Yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammadu bawansa ne manzonsa ne. (Yaku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron Allah yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Yaku waɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammadu (S.A.W.). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (a addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta".

7. Yana da kyau motsin jikin mai huɗuba ya dace da yanayin huɗubarsa. Yana daga cikin sunnar Manzo Allah (S.A.W.) idan yana huɗububa idanunsa sukan yi ja, sautinsa ya yi sama, fushinsa ya tsananta. An karɓo hadisi daga Jabir bn Abdullahi ya ce, “Manzon Allah (S.A.W.) ya kasance idan yana huɗuba idanunsa sukan yi ja, sautinsa kuma ya yi sama, fushinsa ya tsananta, kai ka ce yana yiwa sojoji ne gargaɗi, yana cewa, “Barkanku da safiya! barkanku da yammaci!”.
8. Ana son taƙaita huɗuba da tsawaita sallah. An karɓo hadisi daga Ammar ɗan Yasir ya ce, “Na ji Manzon Allah yana cewa, tsawon sallar mutum da gajartar huɗubarsa alama ce ta zufin iliminsa. Don haka ku tsawaita sallah, ku gajarta huɗuba. Kuma lalle wani bayanin sihiri ne”.
9. Ɗan gajeren zama tsakanin huɗubobi biyu. A ɗan wannan taƙaitaccen zaman babu wata sunna daga manzon Allah da ake gudanarwa. Wanda ya ga zai yi addu’a yana iya yi, amma da sharaɗin kada ya dami masallata da addu’arsa, kuma kada kowa ya riƙa ɗaga hannunsa yana addu’a, har ma a zaci yin haka wata sunna ce a sallar juma’a, alhalin ba haka ne ba.
10. Ya halatta idan liman yana huɗuba ya yi magana da wani a cikin masallata har idan ya zamanto akwai buƙatar hakan. Kamar wani ya shigo masallaci sai kawai ya zauna ba tare da ya yi raka’a biyu ba, sai liman ya faɗakar da shi akan hakan. Kamar yadda Manzon Allah (S.A.W.) ya ce, “ Idan ɗayanku ya zo ranar juma’a ya tarar liman yana huɗuba, to ya yi sallah raka’a biyu, kuma ya taƙaita su”.
11. Kada liman ya ɗaga tafikan hannayensa sama yayin da yake addu’a. Sai dai zai ɗaga yatsansa ne sama, kamar yadda Muslim ya ruwaito daga Husain ɗan Abdurrahman ya ce, “ Haƙiƙa na ga Manzon Allah idan yana addu’a ba ya wuce ya ɗaga ɗan yatsansa kamar haka, sai ya ɗaga yatsarsa manuniya. Sai dai idan addu’ar roƙon ruwa zai yi to yakan ɗaga dukkan hannayensa biyu”.

Siffofon Kwarren Mai Huɗuba, Da Dabarun Huɗuba Na Farko: A karankansa:

1. Ya zama mai ikhlasi ga Allah ta’ala, domin faɗar Allah da yake cewa: (Kuma ba a umarce su ba face sai da su bautawa Allah suna masu tsantsanta addini gare shi).[Al-bayyinah:5].
2. Koyi da Annabi (S.A.W.) a maganarsa da huɗubarsa: Allah yana cewa: (Ka ce, in kun kasance kuna son Allah, to ku bi ni Allah zai so ku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Kuma Allah mai gafara ne mai jin ƙai).[Ali Imran: 31].
3. Sifantuwa da kyawawan halaye, da nisantar munana, da abin da zai kai gare su na magana ko aiki, don ya zama abin koyi ga jama’a, kuma shugaba jagora.
4. Mumini shi ne wanda yake sabawa da jama’a, suma su saba da shi. Don haka ƙwararren mai huɗuba shi ne wanda jma’arsa ke sonsa shi ma yana son su, yana musu hidima, su kuma suna ƙaunar zama tare da shi. Mai hikimi cikin dukkan abubuwansa. Mai haƙuri da juriya da sanin yadda zai ɓullowa kurakuransu.

5. Maganarsa ta dace da aikinsa. A koyi musulunci daga wajensa a aikace, kamar yadda Allah ya ce, (Ya ku waɗanda suka yi imani don menene kuke faɗar abin da ba kwa aikatawa).
6. Nisantar ƙabilanci da ƙungiyanci da ‘yanƙasanci. Kada ya karkata ga komai sai ga littafin Allah da sunna da addinin gaskiya. Allah yana cewa, (Kuma ku riƙe igiyar Allah gaba ɗaya kada ku rarrabu).
7. Ya riƙa cuɗanya da jama’ar da yake zaune tare da su, tare da haƙuri akan duk wani abu da zai gani daga gare su na ɓacin rai. Rayuwarsa a tsakankanunsu ta zama fassar ce a aikace ta huɗubobin da yake musu. Don ya zama abin koyi a wajensu.
8. Ya riƙa sakin fuska da walwala ga masallata. Ya nuna kyawawan halaye. Domin shi abin koyi ne a wajensu, kuma aikinsa aiki ne mai martaba sosai. Yana a makwafin Annabi ne (S.A.W). Idan har ya farauci zukatan masu sauraronsa to za su amfana da abin da yake faɗa musu.

Na Biyu: A Cikin Huɗubarsa:

1. Kyakkyawan shiri bakin gwargwado. Da tattauna abubuwan da za su taimaka wajen gina musulmi na haƙiƙa, tare da magance matsalar rashin aiki da hukunce-hukuncen musulucni. Ga hanyar shirya huɗuba kamar haka:
   - Ya shirya abin da zai faɗa shiri mai kyau.Iidan zai iya rubutwa to hakan zai fi.
   - Ya karanta huɗubar sama da sau ɗaya kafin ya hau minbari, domin kalmomin da yi yi amfani da su, su yi laushi a bakinsa.
   - Ya tsara yadda zai furta kalmomin huɗubarsa, domin akwai inda zai ɗaga murya, da kuma inda ya kamata ya yi ƙasa-ƙasa da muryarsa.
2. Ya yi amfani da lafiyyayen harshe da ingantattun kalmomi. Allah yana cewa: “Lalle mun saukar da shi abin karatu na larabci domin ku hankalta”. Idan masu sauraronsa larabawa ne to ya kamata ya zama yana magana da larbaci gangariya. Idan kuma ba larabawa ba ne, to ya zama mai fasaha cikin yaren da yake masu huɗuba da shi. Nagartar harshensa zai kasance cikin abubuwa kamar haka:
   - Sa ayar magana idan ya dace a tsaya.
   - Yin amfani da sahihan kalmomi.
   - Ya bayyana sautinsa sosai.
   - Ya yi amfani da kwarewa wajen isar da sako.
   - Kada ya riƙa sauri diyawa ko sannu-sannu diyawa ta yadda za a kasa fahimtarsa.
1. Yana da kyau huɗubar juma’a ta zama akan wata fitacciyar matashiya guda ɗaya, wadda ta dace da lokacin da ake gabatar da huɗubar. Idan ana dab da shiga azumi ne sai ya yi huɗuba akan shigowar watan azumi da kuma bayanin wani abu na hukunce-hukuncensa. Idan kuma ana kusa da fara aikin hajji sai ya yi magana akan hajji, da kuma falalar goman farko ta zulhijjah.

2. Dole ne gabobin huɗubarsa su kasance a tsare ɗaya bayan ɗaya. Ta yadda mai sauraro zai iya gano ina ya dosa da huɗubarsa, sannan idan y agama, mai sauraro ya zamana ya fahimcin huɗubar sosai.
3. Ya riƙa raba kallonsa wajen masu sauraronsa. Ya kalli gabansa ya kalli damansa, da hangunsa cikin natsuwa.
4. Hakanan yanayin jikinsa da sautinsa da fuskarsa su yi daidai da yanayin maganar da yake yi.
5. Samun kyakkyawar alaƙa tsakanin ma'anar huɗuba da sautin mai huɗuba, wajen ƙaransa da fitarsa da gaggawarsa. Saboda haka ne Manzon Allah (S.A.W.) ya kasance idan yana huɗuba sai idanuwansa su yi ja, muryarsa ta yi sama, fushinsa ya tsananta, kai ka ce yana yiwa wata rindina gargaɗi ne, yana cewa: "Barkanku da asuba! Barkanku da yamma!"
6. Ya gusarwa da masu sauraro ƙosawa wajen sauraronsa ta hanyar caccanza murya da zai riƙa yi akai-akai, ya ɗaga muryarsa wani lokaci, wani lokaci kuma ya yi ƙasa-ƙasa da ita. Ya maimaita wasu jumlolin maganarsa, ta yadda mai sauraronsa zai riƙa binsa cikin nashaɗi da walwala.
7. Yin waƙafi inda ya dace a yi waƙafi. Domin duk sa'adda ya zama mai huɗuba ba ya shan lumfashi cikin huɗubarsa to a gaskiya ba ta da daɗin sauraro. Ko yaya mai huɗuba ya zama yana ɗan waƙafi cikin huɗubarsa to babu shakka wannan zai jan yo hankalin masu sauraronsa.
8. Gaurayawa tsakanin cizawa da hurawa. Kada ko dayaushe maganarsa ta zama ta ban tsoro ce, haka kuma kada ko yaushe ya riƙa maganar falala da kwaɗaitarwa, a'a kamata ya yi ya taɓo nan ya taɓo can. Kamar yadda Allah ya ce: (Ka sanar da bayina cewa, lalle ni ni ne mai yawan gafara mai yawan jin ƙai, kuma lalle azabata ita ce azaba mai raɗaɗi".
9. Kwarewa wajen amfani da ƙissoshi, kamar yadda Allah ya ce: (Ka faɗa musu ƙissoshi, ko wala alla sa yi tunani". Daga cikin labaran da zai riƙa amfani da su akwai ƙissoshi Annabi (S.A.W.) Allah yana cewa, "Lalle kuna da kyakkyawan abin koyi dangane da Manzon Allah". Da ƙissoshin annabawa, tsira da amincin Allah ya tabbata a gare su, da na sahabbai Allah ya yarda su. Sannan ya riƙa amfani da labarurrukan abubuwan da suke faruwa a cikin al'ummarsa. Domin ƙissa tanada tasiri ba ƙanƙani ba.
10. Amfani da hujjojin na hankali a inda ya dace, kamar yadda Allah ya yi amfani da su cikin littafinsa Alƙur'ani, hakanan Manzonsa ya yi amfani da su cikin sunnarsa.
11. Idan ya zo ambaton wani abu mai mahimmanci a huɗubarsa, to yana da kyau, kodai ya rage saurin maganarsa kaɗan, ko kuma ya ɗan sassauto muryarsa, ko ya maimaita maganarsa, ko ya ɗan yi shiru kaɗan kafin ya faɗe ta. Ya nesanci dogon waƙafi ba tare da buƙatar haka ba.
12. Ya tabbata ya yi tsab-tsab kafin ya fita masallaci, ya yi wanka ya sanya turare, ya sa kaya masu kyau, kamar yadda ya zo a hadisin Abu Sa'eed Al-Kudhri, ya ce, na shaida manzon Allah (S.A.W.) ya ce: "Wajibi ne akan kowane

balagagge ya yi wankan (Juma'a), kuma ya yi aswaki, ya sanya tirare idan ya samu". Kuma ya ce, "Menene zai hana ɗayanku ya samu tufafin zuwa sallar Juma'a guda biyu banda tufarsa ta fita sana'arsa, in har Allah ya hore masa".

Shawarwarin Da Aka Bayar Akan Huɗubar Juma'a A Taron Makka Na Shekarar Hijira 1395

Na ɗaya: Manufofin huɗuba ya kamata su zama kamar haka:

1. Wa'azi da tunanar da mutane Allah da hisabinsa da sakamakonsa a ranar lahira. Da kuma faɗakar da su abin da zai raya musu zukatansa, da kira zuwa ga alheri, da umarni da kykkyawan aiki da hana mummuna.
2. Ilimantar da musulmi haƙiƙanin addininsu daga littafin Allah da sunnar Manzon Allah (S.A.W.) tare da ba da kulawa ta musamman game da sha'anin halayya da ɗabi'u, ba tare da wuce iyaka ba ko sakaci.
3. Gyarawa mutane fahimtarsu game da musulunci, da kuma mayar da martini akan ƙarerayi na maƙiya musulunci ta hanyar hikima da gamsarwa, ba tare da zagi ko cin mutunci ba. Da kuma fuskantar wasu baƙin aƙidu waɗanda suke rushe ginin musuluci ta hanyar gabatar da kykkyawar fahimta ta musulunci, saboda shi ne addinin da Allah ya zaɓarwa wannan al'umma. Tare da fito da gamammiyar koyarwarsa da ta shafi komai na rayuwa.
4. Alaƙanta huɗuba da abin da mutane suke ci na rayuwa da kuma ba da ƙarfi akan cututtuka da ke damun al'umma, da kuma warware matsalolin da suke addabar jama'a, ta hasken shari'ar musulunci, tare da ba muhimmanci na musamman game da al'amuran mata musulmai, duba da yadda maƙiya musulunci suke ta kai masu farmaki iri-iri.
5. Amfani da damammaki da suke maimaituwa duk shekara, kamar azumin Ramadan, da aikin hajji, da sauran abubuwa da suke jan hankulan musulmi suke sanya su kwaɗayin ilimi da zai haskaka musu hanya.
6. Tabbatar da 'yan uwantaka ta musulunci da haɗin-kan musulmi, da yaƙi da ƙabilanci da mazhabci da ɓangaranci da sauran abubuwa masu raba kan al'umma. Da ba da mahimmanci akan al'amuran da suka shafi duniyar musulmi da ma wadda ba ta musulmin ba, don musulmi ya zamanto koda yaushe yana tunanin 'yan uwansa musulmi a ko-ina a duniya.
7. Raya ruhin Jihadi a zukatan al'umma da zaburar da su akan fafutukar ba wa musulunci da ƙasashensa da guraren ibadunsa kariya. Da ba da kariya ga su kansu musulmi da mutuncinsu, da rayukansu, da gusar da duk wani gunki dake ƙoƙarin kawo wa musulunci cikas.

Na Biyu: Dole ne a guji amfani da huɗubar juma'a wajen farfaganda ga wani mutum, ko wata jam'iyyar siyasa, ko wata gwamnati. A gudanar da huɗuba don Allah kaɗai, don isar da addininsa da ɗaukaka kalmarsa kamar yadda Allah ya ce: (Kuma lalle masallatai na Allah ne don haka kada ku kira wani tare da Allah

a cikinsu).

Na Uku: Ya kamata kada a ce za a tilasta wa wani limami amfani da wata matacciyar huɗuba da wani mai mulki zai tsara masa. A'a a ba shi cikakkiyar damar zaɓin abin da zai yi huɗuba akansa, ta hanyar amfani da hankalinsa da abin da ya karanta a littafin Allah da sunnar manzon Allah (S.A.W.).

Na Huɗu: Wajibi ne akan Malamai da masu wa'azi su tsaya su zaɓi irin batutuwa da ya kamata a gina huɗuba akansu. Ta hanyar fito da dalilai na Kur'ani, da Hadisi, da Sirah, da kuma tarihin musulunci, da amfani da karin magana da waƙen hikima. Don su zama a hannun limamai a ko-ina a duniya, suna amfani da su wajen rubuta huɗuba.

Na Biyar: Wajibi ne wajen shirya huɗuba a dogar a kan littattafai masu inganci, a guji amfani da hadisai masu rauni da na ƙarya.

Na Shida: Wajibi ne harshen da za a yi huɗuba da shi a ƙasashen larabawa ya kasance larabci ne mai kyau da sauƙin fahimta. Idan kuma a ƙashen da ba sa magana ne da labarci to a yi amfani da harshen ƙasar bayan an gabatar da sauran rukunan huɗubar cikin harshen larabci.

Na Bakwai: Lalle mai huɗuba ya nisaci ƙaƙale da ife-ife da duk wani abu marar ma'ana wajen gabatar da huɗubarsa.

Na Takwas: Kada mai huɗuba ya tsawaita huɗubarsa, har masu saurarensa su ƙosa da jinsa. Kada kuma ya kasa ba da haƙƙin bayanin abin da yake shi ne babban jigo na huɗubarsa.

Na Tara: Duk abin da aka riga aka faɗa akan huɗubar juma'a to shi ne abin da za a lura da shi a huɗubar idi guda biyu, tare da yin la'akari da abin da ya danganci shi kansa idin. Kuma ya dace ita huɗubar idi ta kasance ta taɓo batutuwa dadama.

Shawarwari Ga Masu Huɗuba Game Da Yadda za su amfana Da Wannan Littafin.

1. Wannan littafi ya ƙunshi matakai ne na farko da ya kamata mai huɗuba ya fara da su. Domin kuwa fagen mai huɗuba ya dogara ne akan zurfin iliminsa da tinaninsa. Don haka dole ne ga ko wane limami ya ci gaba da neman ilimi na Kur'ani da Hadisi.
2. Kafin huɗuba dole ne kowane mai huɗuba ya la'akari da lokacin da ya dace da wannan huɗubar, kada ya yi ta kafin lokacinta, ko ya barta har lokacinta ya wuce sannan ya yi ta. Kamar huɗubar taryar watan azumin Ramadana, ya kamata ta kasance a juma'ar ƙarshe ta watan Sha'aban, ko ta zama a farkon juma'a ta Ramadan.
3. Yana da kyau mai huɗuba ya faɗaɗa karatunsa game da matashiyar huɗubarsa, kada ya taƙaita akan abin da yake cikin huɗubar kawai. IIimi ɗaukake ce ta duniya da lahira. Kamar yadda Manzon Allah (S.A.W.) ya ce: (Fifikon mai ilimi akan mai ibada (marar ilimi) kamar fifikon da ke tskanina ne da mafi ƙasƙancinku). Tirmizi ya ruwaito shi.

4. Ya wajaba mai huɗuba ya kwatanta abin da zai yi huɗuba akansa, kafin ya hau minbari. Saboda miryar mai huɗuba da motsin jikinsa da hawan sautinsa da sauƙarsa suna da matuƙar tasiri ga masu sauraronsa.
5. Mai huɗuba zai iya kawo labaran wasu abubuwa da suka faru a cikin al'ummarsa don masu sauraronsa su fahimci cewa, lalle huɗubarsa ya yi tane domin su.
6. Muna ba mai huɗuba shawarar ya karanta huɗubarsa kafin ya hau minbarinsa sau uku zuwa biyar. Kuma ya riƙa ɗaga muryarsa ya yi kamar yana gabatar da huɗubar ne a lokacin. Ya kula da inda ya kamata ya tsaya, da inda zai yi sauri da yadda zai furta wasu kalmomi.
7. Daga ƙarshe…. Ikhlasi da sa Allah a zuciya shi ne babban dalilin cin nasar limamin juma'a a huɗubarsa. Don haka ya kamata ya sa Allah a zuciyarsa tun lokacin da zai fara shirya huɗubarsa har zuwa sanda zai sauko daga kan minbari. Magabata suna cewa: (Marar ikhlasi dole ne ya riƙa tintiɓe).

FALALAR WANDA YA TABBATAR DA TAUHIDI

Manufofin huɗubar

- Bayanin muhimmancin tauhidi da falalarsa.
- Bayani kan cewa tauhidi shi ne sinadarin tsirar bawa ranar tashin ƙiyama, da kuma yafe masa laifukansa.
- Bayani kan cewa tauhidi sababin juyar da bala'i da fitina ne.
- Bayani kan muhimmancin sanin tauhidi, da kuma shirka da nau'ikanta.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga shirrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammad bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku waniɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammad (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Bayan haka, ya ku bayin Allah! Ina yi muku wasiyya, da ni kaina, da tsoron Allah a ɓoye, da kuma a fili. Sannan ku sani cewa, zuciyar mumini ba ta gyaruwa, sai da wani abu mai girma, kuma babu wanda zai kuɓuta daga duniya, sai da tabbatar da shi. Allah ya yi bayanin sa a cikin littafinsa, kuma Manzon Allah (ﷺ) ya yi bayanin sa a cikin sunnarsa, bayani mai warkarwa, mai gamsarwa, shi ne kaɗaita Allah mai girma, da bautata masa shi kaɗai, babu mai tarayya da shi, da kuma tsantsanta aiki gare shi.

Tauhidi shi ne tushe mai girma, wanda sama da ƙasa suka tsaya a kansa. Ubangiji ya ce,

﴿ لَوۡ كَانَ فِيهِمَآ ءَالِهَةٌ إِلَّا ٱللَّهُ لَفَسَدَتَاۚ فَسُبۡحَٰنَ ٱللَّهِ رَبِّ ٱلۡعَرۡشِ عَمَّا يَصِفُونَ ٢٢ ﴾ [الأنبياء: ٢٢].

(Da a ce akwai abubuwan bauta a cikinsu (sama da ƙasa), ba Allah ba, da sun ɓaci. Tsarki ya tabbata ga Allah Ubangijin al-arshi, daga abin da suke siffantawa).

Saboda da shi ne aka halicci bil Adama da iskokai, kuma aka aiko manzanni, tsira da aminci su tabbata a gare su. Allah ya ce:

﴿ وَمَا خَلَقْتُ ٱلْجِنَّ وَٱلْإِنسَ إِلَّا لِيَعْبُدُونِ ﴿٥٦﴾ ﴾ [الذاريات: ٥٦].

(Ban halicci aljannu da bil Adama ba, sai don su bauta mini).

Ma'ana, don su kaɗaita ni.

Kuma saboda shi ne, har yau, aka halicci aljanna da wuta. Duk wanda ya tabbatar da shi, sannan ya mutu, zai shiga aljanna; duk wanda bai tabbatar da shi ba, ba zai shiga aljanna ba.

Daga Uthman, Allah ya yarda da shi, ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Duk wanda ya mutu, alhali yana sanin cewa babu abin bautawa bisa cancanta, sai Allah, zai shiga aljanna." [Muslim ya rawaito shi].Kuma saboda shi ne jihadi ya tsayu.

Tauhidi yana da falaloli masu yawa. Daga cikinsu: Lallai yana kankare laifuka, kuma yana hana ma'abocinsa ya dawwama a wuta. An rawaito daga Ubadah, Allah ya yarda da shi, daga Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Duk wanda ya shaida babu abin bauta bisa cancanta, sai Allah, halin kasancewarsa shi kaɗai, babu mai tarayya da shi, kuma lallai Muhammad bawansa ne, Manzonsa ne, kuma Isa bawan Allah ne, Manzonsa ne, kuma kalmarsa ce da ya jefa wa Maryam, kuma ruhi ne daga gare shi. Kuma aljanna tabbas ce, kuma wuta tabbas ce, Allah zai shigar da shi aljanna, bisa abin da ya kasance na aiki." [Bukhari ya ruwaito shi]

Kuma yana daga cikin falalarsa, da shi ne bawa yake kusantuwa zuwa ga Ubangijisa. Allah Ta'ala ya ce:

﴿ إِنَّ ٱلدِّينَ عِندَ ٱللَّهِ ٱلْإِسْلَٰمُ ﴾ [آل عمران: ١٩].

(Haƙiƙa addini a wajen Allah, shi ne musulunci).

Kuma da shi ne cikakken aminci yake samuwa, da kuma cikakken shiriya ga bawa, a duniya da lahira. Ubangiji ya ce,

﴿ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَلَمْ يَلْبِسُوٓا۟ إِيمَٰنَهُم بِظُلْمٍ أُو۟لَٰٓئِكَ لَهُمُ ٱلْأَمْنُ وَهُم مُّهْتَدُونَ ﴿٨٢﴾ ﴾ [الأنعام: ٨٢].

(Waɗanda suka ba da gaskiya, kuma ba su cuɗanya ban-gaskiyarsu da zalunci ba, irin waɗannan suna da cikakken aminci, kuma su ne shiryayyu).

Kuma Allah ya ce,

﴿ لَا يَحْزُنُهُمُ ٱلْفَزَعُ ٱلْأَكْبَرُ وَتَتَلَقَّىٰهُمُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ هَٰذَا يَوْمُكُمُ ٱلَّذِى كُنتُمْ تُوعَدُونَ ﴿١٠٣﴾ ﴾ [الأنبياء: ١٠٣].

(Firgici mafi girma, ba ya baƙanta musu zuciya, kuma mala'iku suna tarbar su, suna cewa, "Wannan shi ne yininku, wanda kuka kasance ana alƙarwanta muku).

Kuma yana daga cikin falalar tauhidi, shi ne, gwargwadon yadda ka tabbatar da tauhidi, ka tsantsanta ibada ga Allah, kuma ka nesanci shirka ta fili da ta ɓoye, gwargwadon yadda za ka samu aminci da shiriya. Don haka, za ka ga mumini, wanda ya kaɗaita Allah, ya fi mutane samun aminci a duniya, kuma ya fi mutane samun aminci a lahira. Kamar yadda kuma, tauhidi sanadi ne na juyar da bala'i da fitintinu. Ubangiji yana cewa,

﴿ إِنَّكُمْ وَمَا تَعْبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ حَصَبُ جَهَنَّمَ أَنتُمْ لَهَا وَٰرِدُونَ ﴿٩٨﴾ ﴾ [الأنبياء: ٩٨].

(Lallai ku, da kuma abin da kuke bautawa, koma-bayan Allah, makamashin

jahannama ne….” har a zuwa faɗinsa, “Haƙiƙa waɗanda kalmar yabo ta rigaya gare su, daga gare mu, su waɗanda ake nesantawa ne daga gare ta).

Ga Annabin Allah, Ibrahim, badaɗin Allah, Allah ya raba shi da wuta, a lokacin da aka jefa shi a cikin wuta. Ubangiji ya ce,

﴿ قُلۡنَا يَٰنَارُ كُونِي بَرۡدٗا وَسَلَٰمًا عَلَىٰٓ إِبۡرَٰهِيمَ ٦٩ وَأَرَادُواْ بِهِۦ كَيۡدٗا فَجَعَلۡنَٰهُمُ ٱلۡأَخۡسَرِينَ ٧٠ وَنَجَّيۡنَٰهُ وَلُوطًا إِلَى ٱلۡأَرۡضِ ٱلَّتِي بَٰرَكۡنَا فِيهَا لِلۡعَٰلَمِينَ ٧١ ﴾ [الأنبياء: ٦٩ – ٧١].

(Muka ce, “Ya ke wuta! Ki zama sanyi da aminci a kan Ibrahim. Kuma suka nufi kaidi a gare shi, sai muka tseratar da shi, da Annabi Luɗu, zuwa ƙasa wadda muka sanya albarka a cikinta ga talikai).

Ya ku bayin Allah! Lallai mafiya shiriya cikin mutane, kuma mafiya samun aminci a cikinsu, su ne annabawa da manzanni, saboda tabbatar da tauhidi da suka yi, da kuma tsantsanta bautarsu ga Allah. Ga Annabi Dawud, Allah Ta’ala ya siffanta shi da komawa zuwa gare shi. Ya ce,

﴿ ٱصۡبِرۡ عَلَىٰ مَا يَقُولُونَ وَٱذۡكُرۡ عَبۡدَنَا دَاوُۥدَ ذَا ٱلۡأَيۡدِۖ إِنَّهُۥٓ أَوَّابٞ ١٧ ﴾ [ص: ١٧].

(Ka yi haƙuri a kan abin da suke faɗa, kuma ka ambaci bawanmu Annabi Dawud, ma’aboci ƙarfi. Lallai shi mai yawan komawa ne zuwa ga Allah).

Ku sani, ya bayin Allah, tauhidi ya kasu zuwa gida uku: Tauhidin kaɗaita Allah da aikinsa; tauhidin kaɗaita Allah da aikin bayi, wato ibada; da tauhidin kaɗaita Allah cikin sunayensa da siffofinsa. Haƙiƙa Allah ya haɗa waɗannan nau’ika guda uku, a cikin faɗinsa,

﴿ رَّبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا بَيۡنَهُمَا فَٱعۡبُدۡهُ وَٱصۡطَبِرۡ لِعِبَٰدَتِهِۦۚ هَلۡ تَعۡلَمُ لَهُۥ سَمِيّٗا ٦٥ ﴾ [مريم: ٦٥].

(Ubangijin sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu, ka bauta masa, ka jure wa ibadarsa. Shin ka san wani a matsayin takwara gare shi?).

Kuma tabbatar da tauhidi da rabe-rabensa guda uku, ya zo da dama a cikin Alƙur’ani mai girma. Daga ciki, akwai faɗinsa,

﴿ قُلۡ هُوَ ٱللَّهُ أَحَدٌ ١ ٱللَّهُ ٱلصَّمَدُ ٢ لَمۡ يَلِدۡ وَلَمۡ يُولَدۡ ٣ وَلَمۡ يَكُن لَّهُۥ كُفُوًا أَحَدُۢ ٤ ﴾ [الإخلاص: ١ – ٤].

(Ka ce, “Shi Allah, shi kaɗai ne. Allah wanda ake buƙatuwa zuwa gare shi, bai haifa ba, kuma ba a haife shi ba, kuma babu wani da ya zama tamka gare shi).

Kuma Allah ya ce,

﴿ ٱللَّهُ ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ وَأَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ فَأَخۡرَجَ بِهِۦ مِنَ ٱلثَّمَرَٰتِ رِزۡقٗا لَّكُمۡۖ وَسَخَّرَ لَكُمُ ٱلۡفُلۡكَ لِتَجۡرِيَ فِي ٱلۡبَحۡرِ بِأَمۡرِهِۦۖ وَسَخَّرَ لَكُمُ ٱلۡأَنۡهَٰرَ ٣٢ وَسَخَّرَ لَكُمُ ٱلشَّمۡسَ وَٱلۡقَمَرَ دَآئِبَيۡنِۖ وَسَخَّرَ لَكُمُ ٱلَّيۡلَ وَٱلنَّهَارَ ٣٣ وَءَاتَىٰكُم مِّن كُلِّ مَا سَأَلۡتُمُوهُۚ وَإِن تَعُدُّواْ نِعۡمَتَ ٱللَّهِ لَا تُحۡصُوهَآۗ إِنَّ ٱلۡإِنسَٰنَ لَظَلُومٞ كَفَّارٞ ٣٤ ﴾ [إبراهيم: ٣٢ – ٣٤].

(Allah wanda ya halicci sama da ƙasa, kuma ya saukar da ruwa daga sama, sannan ya fitar da ‘ya’yan itatuwa da shi, don arziki gare ku, kuma ya hore jiragen ruwa, don su gudana a cikin teku, da izininsa, ya kuma hore muku ƙoramu. Kuma ya hore muku rana da wata masu gudu ba ƙaƙƙautawa, kuma ya hore muku dare da yini. Kuma ya ba ku daga duk abin da kuka roƙe shi. Kuma idan za ku lissafa na’imar Allah to ba za ku iya ƙididdige ta ba. Lallai ɗan Adam mai yawan zaluntar kansa ne, mai yawan butulci).

Kuma Allah ya ce,

﴿لَيۡسَ كَمِثۡلِهِۦ شَيۡءٞۖ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡبَصِيرُ ١١﴾ [الشورى: ١١].

(Babu wani abu da yake kamarsa, kuma shi mai ji ne, mai gani ne).

An karɓo daga Abu Huraira, ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Ubangiji ya ce, “Ka ciyar, zan ciyar da kai.” Kuma ya ce, "Hannun Allah a cike yake, ciyarwa ba ta tauye shi, mai yaye dare da rana. Ya ce, “Ku ba ni labari kan abin da Allah ya ciyar, tunda ya halicci sama da ƙasa. Lallai haka bai tauye abin da yake hannunsa ba. Kuma al-arshinsa ya kasance a kan ruwa, sikeli yana hannunsa, yana saukar da shi, yana ɗaga shi.” [Bukhari ya ruwaito shi].

Allah ya yi albarka gare ni, tare da ku, cikin Alƙur’ani mai girma, kuma Allah ya amfanar da ni, da ku, da abin da yake cikinsa, na ayoyi da tunatarwa mai azanci. Shi majiɓincin haka ne, kuma mai iko a kan haka.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah, Ubangijin talikai, kuma tsira da aminci su tabbata ga mafi ɗaukakar Annabawa da Manzanni, Annabinmu, Muhammad, da iyalensa da sahabbansa gabaɗaya.

Bayan haka, ya ‘yan uwa! Lallai tauhidi yana da abubuwan da suke warware shi masu yawa, wajibi ne a kan mutum ya yi taka-tsantsan da su, saboda aukawa cikinsu, yana warware tauhidi, kuma sanadi ne na shigar mutum wuta. Daga ciki, akwai shirka da rabe-rabenta. Babbar shirka tana warware tauhidi gabaɗaya. Karamar shirka kuma tana warware cikar tauhidi.

Haka nan, roƙon wanin Allah buƙatar da Allah kaɗai yake da ikon yin ta, kamar mutum ya nemi aljani ko waliyyi ko shehi, ya yaye masa cuta, ko ya jawo masa amfani, wannan shirka ce mai girma, wadda take warware tauhidi baki ɗaya. Haƙiƙa Manzon Allah (ﷺ) ya nuna cewa, adu’a ibada ce, kamar yadda ya ce, “Adu’a ita ce ibada.” [Tirmizi da Ahmad suka rawaito] Hakanan, yana daga shirka babba, abin da mutane suke yi a yau, na ɗawafi da duƙufa a kan ƙaburan bayin Allah na ƙwarai, da kuma neman biyan buƙata daga gare su, koma-bayan Allah. Allah Ta’ala ya ce,

﴿وَمَنۡ أَضَلُّ مِمَّن يَدۡعُواْ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَن لَّا يَسۡتَجِيبُ لَهُۥٓ إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلۡقِيَٰمَةِ وَهُمۡ عَن دُعَآئِهِمۡ غَٰفِلُونَ ٥﴾ [الأحقاف: ٥]

(Wanene ya fi ɓata, sama da wanda yake roƙon wani koma-bayan Allah, wanda ba zai amsa masa ba, har tashin ƙiyama, su sun shagala ga barin addu’arsu su?).

Daga ciki, akwai zuwa wajen bokaye, da ‘yan tsibbu, da ‘yan duba, da kuma gaskata su cikin abin da suke faɗi na da’awar sanin gaibu. Ubangiji Ta’ala ya ce,

﴿وَإِن يَمۡسَسۡكَ ٱللَّهُ بِضُرّٖ فَلَا كَاشِفَ لَهُۥٓ إِلَّا هُوَۖ وَإِن يَمۡسَسۡكَ بِخَيۡرٖ فَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ١٧﴾ [الأنعام: ١٧].

(Idan Allah ya shafe ka da cuta, babu mai yaye ta, sai shi, idan kuma ya shafe ka da alheri, to shi mai iko ne a kan komai).

Daga ciki, akwai shirka ta nufin wanin Allah, kamar mutum ya nufi duniya, ko son a sani, ko a gani, da aikinsa. Allah Ta'ala ya ce,

﴿ مَن كَانَ يُرِيدُ ٱلْحَيَوٰةَ ٱلدُّنْيَا وَزِينَتَهَا نُوَفِّ إِلَيْهِمْ أَعْمَٰلَهُمْ فِيهَا وَهُمْ فِيهَا لَا يُبْخَسُونَ ﴿١٥﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ لَيْسَ لَهُمْ فِى ٱلْءَاخِرَةِ إِلَّا ٱلنَّارُ ۖ وَحَبِطَ مَا صَنَعُوا۟ فِيهَا وَبَٰطِلٌ مَّا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿١٦﴾ ﴾ [هود: ١٥ – ١٦].

(Duk wanda yake nufin rayuwar duniya da adonta, za mu cika musu ayyukansu a cikinta, su ba za a tauye su a cikinta ba. Irin waɗannan ba su da komai a lahira, sai wuta, abin da suka aikata a cikinta ya rushe, kuma abin da suka kasance suna aikatawa lalatacce ne).

Daga ciki, akwai shirka ta biyayya. Ita ce biyayya ga abin halitta wajen halatta abin da Allah ya haramta. Allah Ta'ala ya ce,

﴿ ٱتَّخَذُوٓا۟ أَحْبَارَهُمْ وَرُهْبَٰنَهُمْ أَرْبَابًا مِّن دُونِ ٱللَّهِ ﴾ [التوبة: ٣١].

(Sun riƙi malamansu, da masu bautarsu, iyayen giji, koma-bayan Allah).

Kamar yadda Annabi (ﷺ) ya fassara wa Adiy ɗan Hatim, lokacin da ya tambaye shi. Ya ce, "Ba ma bauta musu!" Sai Manzon Allah (ﷺ) ya nuna masa cewa, bautar ita ce, yi musu biyayya a kan saɓon Allah, da janja hukuncin Allah. Ya ce, "Ba suna haramta abin da Allah ya halatta ba, sai kuma ku ɗauke su a matsayin haram, kuma suna halatta abin da Allah ya haramta, sai ku ɗauke shi a matsayin halal?" Sai ya ce, "Na'am!" Sai ya ce, "Wannan ita ce bauta musu." [Tirmizi da Ɗabarani suka rawaito shi].

Daga cikin akwai shirka ta soyayya wadda take tilasta girmamawa da rusunawa da ƙasƙantar da kai, wanda ba su cancanta a yi su ba, sai ga Allah shi kaɗai. Duk sanda bawa ya yi irin wannan soyayya ga wanin Ubangiji, to haƙiƙa ya yi shirka mai girma. Ubangiji yana cewa,

﴿ وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يَتَّخِذُ مِن دُونِ ٱللَّهِ أَندَادًا يُحِبُّونَهُمْ كَحُبِّ ٱللَّهِ ۖ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ أَشَدُّ حُبًّا لِّلَّهِ ۗ ﴾ [البقرة: ١٦٥].

(Daga cikin mutane, akwai waɗanda suke riƙar kishiyoyi koma-bayan Allah, suna son su, kamar yadda suke son Allah. Su kuwa waɗanda suka yi imani, sun fi tsananin soyayya ga Allah).

Ya ku bayin Allah! Ku sani cewa, Allah Tabaraka Wa Ta'ala, ba ya gafarta a yi shirka da shi. Ubangiji ya ce,

﴿ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَغْفِرُ أَن يُشْرَكَ بِهِۦ وَيَغْفِرُ مَا دُونَ ذَٰلِكَ لِمَن يَشَآءُ ۚ ﴾ [النساء: ٤٨].

(Lallai Allah ba ya gafarta a haɗa wanin Allah da shi, amma yana gafarta abin da yake koma-bayan haka, ga wanda ya so).

Kuma ya ce,

﴿ حُنَفَآءَ لِلَّهِ غَيْرَ مُشْرِكِينَ بِهِۦ ۚ وَمَن يُشْرِكْ بِٱللَّهِ فَكَأَنَّمَا خَرَّ مِنَ ٱلسَّمَآءِ فَتَخْطَفُهُ ٱلطَّيْرُ أَوْ تَهْوِى بِهِ ٱلرِّيحُ فِى مَكَانٍ سَحِيقٍ ﴿٣١﴾ ﴾ [الحج: ٣١].

(Duk wanda ya haɗa wani da Ubangiji, to kamar wanda ya faɗo daga sama ne, sai tsuntsaye suka wabce she, ko iska ta yi wurgi da shi a wani waje mai nisa).

Kuma Ubangiji ya ce,

﴿ إِنَّهُۥ مَن يُشْرِكْ بِٱللَّهِ فَقَدْ حَرَّمَ ٱللَّهُ عَلَيْهِ ٱلْجَنَّةَ وَمَأْوَىٰهُ ٱلنَّارُ ۖ وَمَا لِلظَّٰلِمِينَ مِنْ أَنصَارٍ ﴿٧٢﴾ ﴾ [المائدة: ٧٢].

(Duk wanda ya haɗa Allah da wani, haƙiƙa Allah ya haramta masa shiga aljanna, kuma makomarsa ita ce wuta, kuma azzalumai ba su da mataimaka).

Idan Allah ba ya yarda da shirka, sai dai tauhidi, kuma ba ya gafarta shirka, to lallai azabar masu yin shirka, mai girma ce. Azabarsu ita ce wuta, azabarsu ita ce wulaƙanci a duniya da lahira. Waye a cikinmu - ya bayin Allah - ba ya son kuɓuta a duniya da lahira? Waye a cikinmu, ba ya son ya shiga aljanna ba tare da hisabi ko azaba ba? Waye a cikinmu, ba ya son ya rayu, rayuwa mai daɗi a duniya, kuma ya kuɓuta ranar da dukiya da 'ya'ya ba sa amfani?

Saboda haka, ku lazimta wa kanku tabbatar da tauhidi ga Allah, da tsantsanta bauta gare shi. Kuma ku koyi hakan, kuma ku kula da abin da malaman musulunci da jagororin sunna da jagororin wannan kira suka rubuta a kan waɗannan manya-manyan mas'aloli na tauhidi. Domin, duba littattafan tauhidi, haske ne a cikin zukata, kuma shiriya ce ga rayuwa, kuma a cikin tauhidi nagarta take ga ɗaiɗaikun mutane da al'umma. Kada duniya ta shagaltar da kai ga barin wannan tushe mai girma, wanda ya tattare komai da komai, wanda saboda shi aka aiko Annabawa da Manzanni, kuma saboda shi aka halicci aljanna da wuta. Ku bai wa tauhidi haƙƙinsa, kuma ku gabato wajen koyon sa, tun daga wannan lokacin, tare da niyya ta gaskiya. Ku koyi tauhidi a dunƙule, da kuma a rarrabe, don kada ku auka cikin abinn da mafi yawan mutane suka auka ciki na jahilci ko barin tauhidi.

Ina roƙon Ubangiji, ya inganta mana niyyoyinmu, ya kuma inganta mana addininmu, ya kuma inganta mana duniyarmu. Lallai shi mai kyauta ne, mai karamci.

ADDU'A: MUHIMMANCINTA DA SHARAƊANTA

Manufofin huɗubar

- Bayanin ma'anar addu'a da buƙatuwar halitta zuwa gare ta.
- Bayanin hukunce-hukuncenta da sharadanta da ladubbanta.
- Gargaɗi a kan wasu kurakurai dangane da addu'a

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo ya tabbata ga Allah muna yabon Sa muna neman taimakonsa, muna neman gafararsa, muna neman tsarinsa. Duk wanda Allah Ya shiryar babu mai ɓatar da shi wanda kuma ya ɓatar babu mai shiryar da shi kuma ina shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah shi kaɗai ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammadu bawansa ne manzonsa ne (ya ku waɗanda suka yi imani kuji tsoron Allah yadda ya cancanci a ji tsioronsa, kada ku mutu face kuma musulmi) (ya ku mutane kuji tsoron Ubangijimku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya halicci matar sa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daresu (su biyu) ku ji tsoron allah wanda kuke yi wa junanku magiya dashi (kuma ku kiyaye) zumunci lalle Allah mai kulane daku) (yak u waɗanda kuka yi imani ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi Magana ta daidai, sai Allah ya gyara muku ayyukanku kuma ya gafarta muku zunubanku, wanda yabi Allaha da Manzon Allah haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawun shiriya shiriyar Annami Muhammad (ﷺ) kumamafi sharin al'amura (a addini) ƙagaggunsu. Kuma duk wani ƙagaggen abu (a addini) bidi'a ce, kuma duk warta bidi'a ɓata ce, kuma duk wani bata yana wuta.

Bayan haka;

Ya ku bayin Allah, ku sani cewa dukkan halitta mabuƙata ne zuwa Ubangijinsu wajen janyo musu amfani da ije musu cututtuk, domin gyara addininsu da duniyarsu. Kuma kuma kamalar mutum tana tattare da tabbatar da bautarsa ga Allah mai girma da ɗaukaka, kuma duk sanda bawa ya ƙara tabbatar da bautarsa sai kamalarsa ta ƙaru, kuma darajarsa ta ɗaukaka, kuma Allah mai girma da ɗaukaka yana jarrabar bayinsa da wasu abubuwa masu bijirowa da sukan tura su zuwa ƙofarsa su neman agajjinsa, kuma buƙatuwa zuwa ga Allah, ita ce haƙiƙanin wadatuwarsa. Kuma ƙaunar bauta da babbar manufarta, da kuma ƙasƙantar da kai ga Allah mai tsarkin mulki shi ne ɗaukakar da ba za a iya gasa da ita ba. Kuma addu'a ita ce alamar bauta, Allah yana son bayinsa su roƙe shi a cikin dukkannin buƙatunsu. Domin ya zo cikin Sahih Musulim daga hadisin Abi Zarr, Allah Ya

ƙara yarda a gare shi, Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: “Ya ku bayina dukkaninku ɓatattu ne sai fa wanda na shiryar da shi, to ku nemi shiriyata, zan shiryar da ku. Ya ku bayina dukkanin ku mayunwata ne, sai fa wanda na ciyar da shi, to ku nemi ciyarwata, zan ciyar da ku. Ya ku bayina dukkaninku matsiraita ne, sai fa wanda na tufatar da shi, to ku nemi tufatarwa zan tufatar da ku. Ya ku bayina haƙiƙa kuna yin kuskure da dare da rana, ni kuma in gafarta zunubi baki ɗaya, ku nemi gafara ta zan gafarta muku...”.

Ya ku bayin Allah, ku yi sani cewa, Allah (S.W.T) ya hore hanyoyin samun rabo, kuma ya huwace hanyoyin taɓewa. Kuma ya jera abubuwa masu faruwa a bisa dalilan faruwarsu, kuma ya halicci sakamakon da za su haifar. Kuma babu wani abu da yake hukunta kansa da nufinsa. Da ya so da ya samar da abu ba tare da sababi ba. Allah Ta’ala Ya ce,

﴿ فَعَّالٌ لِّمَا يُرِيدُ ﴿١٦﴾ ﴾ [البروج: ١٦]

(Shi mai aikatawa ne ga abin da ya yi nufi).

Kuma Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿ أَلَا لَهُ ٱلْخَلْقُ وَٱلْأَمْرُ ۗ تَبَارَكَ ٱللَّهُ رَبُّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٥٤﴾ ﴾ [الأعراف: ٥٤].

Ma’ana: (Lalle halitta da umarni na shi ne. Albarkatun Allah sun yawaita. Ubangijin talikai).

Don haka, addu’a dalili ne babba na rabauta da alherai da albarkatai. Kuma dalili ne na na yaye baƙin ciki, da sharri da bala’i. Tirmizi ya ruwaito daga Ibn Umar (R.A) ya ce, “Addu’a tana amfani ga abin da ya sauka, da ma wanda bai sauka ba.”

Addu’a tana daga cikin ƙaddara, kuma sabab ce daga sababbba masu amfani, masu janyo alheri su ije dukkan sharri.

Haƙiƙa Allah ya yi umarni da addu’a a cinkin ayoyi masu yawa, ya ce,

﴿ وَقَالَ رَبُّكُمُ ٱدْعُونِىٓ أَسْتَجِبْ لَكُمْ ۚ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَسْتَكْبِرُونَ عَنْ عِبَادَتِى سَيَدْخُلُونَ جَهَنَّمَ دَاخِرِينَ ﴿٦٠﴾ ﴾ [غافر: ٦٠].

(Kuma Ubangijinka ya ce, ku roƙe ni, na amsa muku. Haƙiƙa waɗanda suke girman kai ga barin bautata za su shiga wutar Jahannama suna ƙasƙantattu).

Ya ku bayim Allah! Ku sani cewa haƙiƙa yin addu’a shi ne: tsananta kwaɗayi ga Allah Ta’ala wajen neman biyan buƙatun duniya da na lahira da yaye baƙin ciki da kaɗe sharri, da bala’i na duniya da lahira. Da addu’a ne bautar Ubangijin talikai takan tabbata, domin ta ƙunshi ratayuwar zuciya da Allah Ta’ala da Ikhlasi gare shi, da rashin waiwayen wani ba shi ba.

Addu’a ta ƙunshi sakankancewa da cewa Allah mai cikakken iko ne, babu wani abu da zai gajiyar da shi, babu wani abu da zai ɓuya a gare shi, mai rahama mai jinƙai. Rayayye ne, mai isa da zatinsa, ma’abocin alheri har abada, ba a iyakance baiwarsa da alherinsa. Taskokin albarkatunsa ba sa ƙarewa.

Addu’a ta ƙunshi buƙaturuwar bawa da tsananin matsiwarsa zuwa Ubangijinsa, waɗannan abubuwa ne haƙiƙanin ma’anar ibada.

Ya ku bayin Allah! Haƙiƙa ɗimbin nassoshi na hadisazan Annabi sun zo game da falalar addu'a. Daga cikinsu akwai abin da Abu Dawud da Tirmizi suka ruwaito daga Nu'uman bn Bashir, Allah ya ƙara yarda a gare su daga Annabi (ﷺ) ya ce: "Addu'a ita ce ibada." Tirmizi ya ce: hadisi ne kyakkyawa ingantacce.

Kuma an karɓo daga Abu Hurairah Allah ya ƙara yarda a gare shi ya ce daga Annabi (ﷺ) ya ce: "Babu wani abu da ya fi girma wajen Allah kamar addu'a." Ahmad da Tirmizi da Ibn Majah da Ibn Hibbana suka rawaito.

Hakanan ana rawaito daga Abu Hurairah (R.A) ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Haƙiƙa Allah mai girma da buwaya yana cewa: "Ni ina wajan zaton bawana gare ni, kuma ni ina tare da shi (da sani na) idan ya ambace ni". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi kuma lafazinsa ne. Haka nan Tirmizi da Nisa'i da Ibn Majah duk sun rawaito shi.

An karɓo daga Ubadah ɗan Samit (R.A) cewa, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Babu wani musulmi a ban ƙasa da zai roƙi Allah da wata addu'a face ya ba shi ita, ko ya kaɗe masa wani mummunan abu a madadinta, matuƙar ba ya roƙi wani abin laifi ba ko yanke zumunci". Sai wani mutum daga cikin mutanen ya ce: "Ashe za mu yawaita ke nan". Sai ya ce: "Allah Shi ne mafi yawaita wa." Tirmizi ya rawaito kuma ya inganta shi.

Ya ku bayi Allah! Ku sani cewa ba a roƙon kowa sai Allah, ba wani mala'ika makusanci ga Allah, ko wani Annabi mursali, ko wani waliyyi nagartacce. Kuma duk wanda ya kirayi wani abin halitta ba Allah ba, Annabi ne ko mala'ika, ko waliyyi, ko aljan, ko kabari, ko makamancinsa, to haƙiƙa ya yi shirka da Allah Ta'ala, cikin ibadarsa, shirka da za ta fitar da shi daga musulunci. Allah Ta'ala Ya ce:

﴿ وَأَنَّ ٱلۡمَسَٰجِدَ لِلَّهِ فَلَا تَدۡعُواْ مَعَ ٱللَّهِ أَحَدٗا ١٨ ﴾ [الجن: ١٨].

(Kuma haƙiƙa masallatai na Allah ne, don haka kada ku kira wani tare da Allah).

Kuma maɗaukakin sarki ya ce,

﴿ وَمَن يَدۡعُ مَعَ ٱللَّهِ إِلَٰهًا ءَاخَرَ لَا بُرۡهَٰنَ لَهُۥ بِهِۦ فَإِنَّمَا حِسَابُهُۥ عِندَ رَبِّهِۦٓۚ إِنَّهُۥ لَا يُفۡلِحُ ٱلۡكَٰفِرُونَ ١١٧ ﴾ [المؤمنون: ١١٧].

(Kuma wanda ya kira yi wanin Ubangijin tare da Allah wanda ba shi da wani dalili (ga bauta masa), lallai to wannan hisabinsa yana wajan ubangijinsa, lallai kafirai ba su rabauta ba).

Kuma Ya ce,

﴿ وَلَا تَدۡعُ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَا لَا يَنفَعُكَ وَلَا يَضُرُّكَۖ فَإِن فَعَلۡتَ فَإِنَّكَ إِذٗا مِّنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ١٠٦ ﴾ [يونس: ١٠٦].

(Kada ka kirawo wani ba Allah ba, wanda ba zai amfaneka ba, kuma ba zai cutar da kai ba, idan kuwa ka aikata haka, to lallai kai kana cikin azzalumai).

Kuma ya ce,

﴿ وَإِن يَمۡسَسۡكَ ٱللَّهُ بِضُرّٖ فَلَا كَاشِفَ لَهُۥٓ إِلَّا هُوَۖ وَإِن يُرِدۡكَ بِخَيۡرٖ فَلَا رَآدَّ لِفَضۡلِهِۦۚ يُصِيبُ بِهِۦ مَن يَشَآءُ مِنۡ عِبَادِهِۦۚ وَهُوَ ٱلۡغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ١٠٧ ﴾ [يونس: ١٠٧].

(Kuma idan Allah ya jarrabe ka da cuta to babu mai yaye maka ita face shi, idan kuma ya nufe ka da alheri to babu mai mai da falalarsa, yana samar wanda ya so

daga bayinsa da shi, kuma shi ne mai gafara mai Jinƙai).

Kuma Allah Ta'ala Ya ce,

﴿ وَيَوۡمَ يَحۡشُرُهُمۡ جَمِيعٗا ثُمَّ يَقُولُ لِلۡمَلَٰٓئِكَةِ أَهَٰٓؤُلَآءِ إِيَّاكُمۡ كَانُواْ يَعۡبُدُونَ ٤٠ ﴾ [سبأ: ٤٠].

(Kuma ranar da zai tashe su gaba ɗaya sannan ya ce da mala'ikunsa, shin waɗannan ku ne suka kasance suna bautawa? Sai su ce tsarki ya tabbata a gare ka, kai ne majiɓincinmu, ba su ba. Kaɗai sun kasance suna bautawa aljannu ne mafi yawancinsu masu ba da gaskiya ne da su.)

Ya ku Musulmi! Haƙiƙa addu'a tana da lokuta na musamman, kuma aka fi ƙaunar amsa ta a cikinsu waɗanda su ne; addu'a a cikin sujjada. Daga Abu Huraira Allah ya yarda da shi, daga Annabi (ﷺ) ya ce, "Lokacin da bawa ya fi kusa da Ubangijinsa, shi ne lokacin da yake sujjada. Don haka, ku yawaita addu'a a cikinta." Muslim ne ya rawaito shi.

Kuma an karɓo daga Ibn Abbas (R.A.), ya ce: MAnzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle haƙiƙa ni an hana ni in karanta Alƙur'ani a cikin ruku'u ko sujjada. Amma ruku'u to ku girmama Ubanjigi a cikinsa. Ita kuma sujjada, to ku yi matuƙar ƙoƙari wajen addu'a a cikinta, lallai ya dace amsa muku." Muslim ne ya rawaito shi.

Daga ciki: akwai tsakanin kiran sallah da iƙama. Domin an rawaito daga Anas (R.A) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ba a mayar da addu'a a tsakanin kiran sallah da iƙama." Tirmizi ne ya fitar da shi, kuma ya ce, hadisi ne kyakkyawa ingantacce.

Kuma gada ciki: akwai yayin da sulusin dare na ƙarshe ya rage. Domin ya zo a cikin sahihin Bukhari, Manzon Allah, tsira da aminci su tabbata a gare shi ya ce: "Ubangijinmu kan sauka (irin saukar da ta dace da shi), kowane dare zuwa saman duniya yayin da sulusin dare na ƙarshe ya rage, sai ya ce "Wane ne zai kira ni na amsa masa? Wane ne zai nemi gafara ta na gafarta masa?".

Daga ciki: akwai ƙarshen sa'a bayan sallar La'asar ranar juma'a. An rawaito daga Abi Huraira (R.A) cewa Manzon Allah (ﷺ) ya ambaci ranar Juma'a sai ya ce "A cikinta akwai wata sa'a babu wani bawa Musulmi da zai dace da ita a tsaye yana sallah, yana roƙon Allah wani abu face ya ba shi. Ya yi nuni da hannunsa yana ƙarantata." Bukhtari da Muslim ne suka rawaito shi.

Ma'abota ilimi suna da mazhabobi da dama wajen tantance wannan sa'ar ta ranar Juma'a. Amma mafi inganci shi ne cewa, ƙarshen sa'a bayan La'asar, kamar yadda yake a cikin hadisin Abi Dawud da waninsa, Annabi (ﷺ) ya ce, (Ranar Juma'a sa'a sha biyu ce, ba za a samun wani Musulmi yana roƙon Allah wani abu a cikinta face ya ba shi. Ku neme ta a sa'a ta ƙarshe bayan sallar La'asar).

Yana daga guraren amsa addu'a da shari'a ta zo da su: Daren Lailatul Kadari, da ranar Arafa, da gurin Hajarul Aswad, da yayin saukar ruwan sama, da bayan sallolin farilla, da lokacin shan ruwa a yayin azumi.

Ya ku bayin Allah! Ku ganimanci falalar Ubangijinku, ku fake zuwa gare shi cikin lamuranku. Ku ɗaukaka tafukanku da ƙasƙan da kai, ko a amsa addu'o'inku! Kuma ku rabauta da yardar Ubangijinku.

Ina faɗar abin da kuke ji kuma ina neman gafarar Allah Maɗaukakin Mai girma ga kaina da ku, da a kuma sauran Musulmi daga kowane zunubi. Lallai shi ne Mai yawan gafara Mai yawan jinƙai.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah wannan da ya shiryar da majiɓintansa ga addinin musulunci, ina yabansa ina gode masa a bisa datarwarsa da shiyarwarsa, ina shaidawa cewa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya ma'abocin buwaya da girma. Kuma ina shaidawa cewa Annabu Muhammad Manzon Allah ne amintacce. Allah ka yi salati da sallama a bisa bawanka da kuma manzonka Muhammadu da alayansa, da sahabansa gabaɗaya.

Ku sani ya ku bayin Allah cewa, addu'a tana da sharuɗɗa waɗanda dole sai an cika su kafin addu'ar bawa ta samu karɓuwa wajen Ubangijin sa, su ne kamar haka;

Na farko: Tsarkake tauhidi ga Allah Ta'ala. Allah Ya ce:

﴿ فَٱدۡعُواْ ٱللَّهَ مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ وَلَوۡ كَرِهَ ٱلۡكَٰفِرُونَ ١٤ ﴾ [غافر: ١٤].

(Don haka ku kira Allah kuna masu tsarkake addini a gare shi, ko da kafirai sun ƙi). Kuma haƙiƙa ya zo a cikin hadisil Kudusi: "Ya kai ɗan'adam haƙiƙa kai da za ka zo mini da cikin ƙasa na zunubai, sannan ka gamu da ni ba ka tara bauta ta da wani abu ba, da na zo maka da kwatankwacinta na gafara." Tirmizi ne ya rawaito shi.

Na biyu: Nisantar haram a cimarka, da abin sha da tufafi; domin Muslim ya rawaito a cikin sahihinsa, daga hadisin Abu Huraira (R.A) cewa, Manzon Allah (ﷺ) ya ce "Ya ku mutane haƙiƙa Allah Ta'ala tsarkakakke ne, ba ya karɓa sai tsarkakkake. Kuma Allah ya umarci Muminai da abin da ya umarci Manzanni da shi, sai ya ce,

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلرُّسُلُ كُلُواْ مِنَ ٱلطَّيِّبَٰتِ وَٱعۡمَلُواْ صَٰلِحًاۖ إِنِّي بِمَا تَعۡمَلُونَ عَلِيمٞ ٥١ ﴾ [المؤمنون: ٥١].

(Ya ku manzanni ku ci daga daɗaɗa, kuma ku aikata aiki na gari, haƙiƙa Ni masani ne da abin da kuke aikatawa). kuma ya ce,

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ كُلُواْ مِن طَيِّبَٰتِ مَا رَزَقۡنَٰكُمۡ وَٱشۡكُرُواْ لِلَّهِ إِن كُنتُمۡ إِيَّاهُ تَعۡبُدُونَ ١٧٢ ﴾[البقرة: ١٧٢].

(Ya ku waɗanda suka yi imani, ku ci daga daɗaɗan abin da muka azurta ku, kuma ku yi godiya ga Allah in kun kasance shi kaɗai kuke bautawa).

Sannan ya ambaci mutum da yake tsawaita tafiya, mai hargitsattsan gashi, mai buɗu-buɗu, yana ɗaga hannayensa zuwa sama, (yana addu'a yana mai cewa): Ya Ubangiji! Ya Ubangiji!! (Alhali) abincinsa haramun ne, abin shansa haramun ne, kuma tufafinsa haramun ne, kuma an ciyar da shi da haramu, to ta yaya za a amsa masa."

Na uku: halartowar zucitya da ƙarfin fata, domin an rawaito daga Abu Huraira (R.A) daga Annabi (ﷺ) ya ce: “Ku roƙi Allah, kuna masu sakankancewa da amsawa, kuma ku sani cewa Allah baya ƙarɓar addu’a daga zuciya gafalalliya mai wasa”. Tirmizi ne ya rawaito shi.

Na Huɗu: ya gabatar da yabo ga Allah da salati ga Annabi (ﷺ) gabannin gabatar da buƙatarsa, sabda abin da ya zo a cikin ingatatcciyar sunna game da haka.

Kamar yadda addu’a ta ke da wasu ladabbai da ya kamata bawa ya lura da su yayin da yake yin addu’a.

Daga waɗannan ladubba akwai:

Ya kasance cikin tsarki, domin addu’a zikiri ce, gashi kuma hadisi ya inganta daga Annabi (ﷺ) cewa, ya yi taimama daga garun wani bango domin amsa sallama, sannan ya ce “Na ƙyamaci na ambaci Allah ba tare da ina cikin tsarki ba” Abu Dawud ne ya fitar da shi.

Daga hannaye, saboda abin da ya zo a cikin hadisi “Haƙiƙa Ubangijinku mai kunya ne, mai karamci ne, yana jin kunyar bayinsa idan suka ɗaga hannayensu zuwa gare shi, su mai da su fayau.” Hakim ne ya fitar da shi, kuma ya inganta shi. Kuma Azzahabi ya goyi bayansa.

Ya ƙarfafa aniyarsa a kan addu’ar, saboda faɗin Annabi (ﷺ): “Idan ɗayanku zai yi addu’a to ya ƙarfafa aniyarsa, kada ya ce "Ya Ubangiji to idan ka so ka ba ni", domin ba mai tilasta masa” Bukhari ne ya fitar da shi.

Ya kirdadi sigogin addu’a da aka rawaito musamman waɗanda suka zo cewa sun ƙunshi Ismul A’azam, domin ya zo a cikin sahihin Ibn Hibbana daga hadisin Abdullahi bn Buraidah daga babansa (R.A.) cewa, Manzon Allah (ﷺ) ya ji wani mutum yana cewa “Ya Ubangiji ni ina roƙonka da cewa ni ina shaidawa kai kaɗai ne Allah, babu abin bautawa da gaskiya sai kai. Kai kaɗai ne abin nufi da buƙata, wanda bai haifa ba, ba a haife shi ba, kuma babu wani da ya kasance tamka a gare shi”, Sai ya ce, “Haƙiƙa in an tambaye Shi da shi yana bayarwa, kuma idan an roke shi da shi, sai ya amsa”. A wani lafazin “Haƙiƙa ka tambayi Allah da sunansa mafi girma.” Hadisi ne ingantacce. A cikin sunana daga hadisin Anas ɗan Malik (R.A) cewa, shi ya kasance tare da Manzon Allah (ﷺ) yana zaune, wani sai ya ce, “Ya Ubangiji, ni ina roƙon ka da cewa yabo ya tabbata a gare ka, babu abin bautawa da gaskiya sai kai, Mai baiwa, maƙagin sammai da ƙassai, ya ma’abocin buwaya da girmamawa ya rayayye, ya tsayayye (da lamuran halitta).” Sai Annabi (ﷺ) ya ce, “Haƙiƙa ya kira Allah da sunansa mai girma, wanda idan an roke shi da shi yake amsawa, kuma idan an tambaye shi da shi yake bayarwa”. (hadisi ne ingantace).

Kuma Bukhari da Muslim sun ruwai daga Ibn Abbas, cewa Manzon Allah (ﷺ) ya kasance yana faɗa yayin baƙin ciki “Babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, Ubangijin Al’arshi mai girma, babu abin bautawa da gaskiya sai Allah Ubangijin sammai da ƙassai, Ubangijin al’arshi mai karamci".,

Ya ku bayin Allah! Ya wajaba mu dauwama kan addu'o'i. Ba wai loakcin da musubu da bala'i suka afko ba kaɗai, sai dai kamar yadda ya zo a cikin hadisin Annabi wanda Abu Hurairah (R.A) ya rawaito daga gare shi mai tsira da amincin Allah, ya ce, "Wanda ya ke son Allah ya karɓa addu'arsa a lokacin tsanani, to ya yawaita addu'a yayin da yake cikin yalwa." Tirmizi ne ya rawaito, kuma Hakim ya inganta shi.

Allah yana cewa,

﴿ أَمَّن يُجِيبُ ٱلْمُضْطَرَّ إِذَا دَعَاهُ وَيَكْشِفُ ٱلسُّوٓءَ وَيَجْعَلُكُمْ خُلَفَآءَ ٱلْأَرْضِ ۗ أَءِلَٰهٌ مَّعَ ٱللَّهِ ۚ قَلِيلًا مَّا تَذَكَّرُونَ ﴿٦٢﴾ ﴾ [النمل: ٦٢].

(Shin wanene wanda yake amsawa mabuƙaci yayin da ya kira shi, kuma yake yaye cuta, kuma yake sanya halifofi a ƙasa. Shin akwai wani abin bauta tare da Allah. Kaɗanne kwarai kuke wa'azantuwa). .

Kuma Allah Ta'ala Ya ce,

﴿ وَإِذَا سَأَلَكَ عِبَادِى عَنِّى فَإِنِّى قَرِيبٌ ۖ أُجِيبُ دَعْوَةَ ٱلدَّاعِ إِذَا دَعَانِ ۖ فَلْيَسْتَجِيبُوا۟ لِى وَلْيُؤْمِنُوا۟ بِى لَعَلَّهُمْ يَرْشُدُونَ ﴿١٨٦﴾ ﴾ [البقرة: ١٨٦].

(Kuma yayin da bayina suka yambayeka game da ni, to ni makusanci ne, ina amsa addu'ar mai addu'a idan ya kirani).

Ina addu'o'in da muke yi kafin salloli, da cikin salloli, da bayan salloli? Ina addu'o'inmu a tarurruka, Ina addu'o'in da muke yi a ciki sirri da keɓancewa da tsakiyar dare da gabanin alfijiri da cikin awoyin ƙarshen na dare, da ranakun masifa, ko lokacin bala'i? A koyaushe, to ina gafallalu? Mu kuwa – in banda waɗanda Allah ya jiƙansu – muna cikinsu. Ina masu addu'a masu ƙasƙantar da kai, mu ga yaya sakankacewarsu da wannan addu'a, ranar da imani yake kafe a cikin zuƙata, ranar da nagarta da istiƙama suke bayyane cikin ɓoyayyun halaye da bayyanannunsu. Ɗayansu ya kasance yana addu'a yana mai yankewa da sakankancewa da amsawar Allah ga wannan addu'a. Har wasu suka shahara tsakanin sahabbai - Allah ya yarda da su - a kan cewa su, ababen amsa addu'ar su ne, kamar yadda ya ke a ƙissar Sa'ad ɗan Abu Waƙƙas.

Ga dai Sa'id ibn Zaid, ɗaya daga goma waɗanda aka yi musu bushara da aljanna. Wata mata ta yi da'awa da ƙage cewa ya ƙwace mata wani yanki na ƙasarta, yayin da aka yi masa magana kan haka, sai ya ce "Yaya haka, alhali ni na ji cewa, wanda ya ƙwaci taku ɗaya na ƙasa ba tare da haƙƙinsa ba, to za a rataya masa shi tun daga ƙasan-bakwai ranar alƙiyama". Sannan ya ce, "Ya Ubangiji idan ƙarya take, to ka makantar da ita, kuma ka sanya ƙabarinta a cikin gidanta. Sai ta makance, kuma ta faɗa wata rijiyarta a cikin gidanta ta mutu.

Hakanan Abu Mu'awiya Al'aswad a lokacin gwabzawa da Rumawa, wani kafiri daga kafiransu ya fito. Wanda cutarsa to tsananta ga Musulmi, sai wani daga cikin musulmi ya zo masa (shi Mu'awiya) sai ya ce "Wannan ya aikata kaza da kaza, ka roƙi Allah a kansa». Sai ya ɗauki mashinsa ya yi addu'a ya ce, "Kuma ba ka yi jifa ba yayin da ka yi jifa sai dai Allah shi ne ya yi jifa". Sannan ya ce "Ina kuke so? Suka ce "Mazakutarsa" Sai suka jefa shi, kuma ba su kuskure gurin da suka faɗa ba. Sai ya kashe maƙiyin Allah (S.W.T).

Wasu mutane ba su gushe ba suna cewa, “Mun yi ta yin addu’a amma ba a amsa mana ba. Don haka mu ba mu ga amfaninta ba». Alhali ba su san cewa su ne ba su cika sharuɗɗan amsa addu’ar ba. Kuma su sun ɓata hanyar addu’ar, da kaɓar addu’ar zuwa ga Allah Mai Buwaya da ɗaukaka, saboda raunin yaƙini da raunin imani, baya ga kau da kai ga barin biyayya da afkawa cikin saɓo.

Ya ku bayin Allah! Ya wajaba musan haƙiƙanin addu’a da muhimmancinta da girmanta a cikin wannan addinin kuma cewa, ita alama ce ta kamalar bautar bawa ga Ubangijinsa, kuma mu lazimci hanya madaidaciyya cikin addu’armu. Mu koyi sonnonin Annabi da ladubban shari’a a cikinta, in mun yi haka Allah zai sanya mu cikin waɗanda ake amsa addu’o’in su ya karɓi ƙasƙan da kanmu, da aikinmu. Lallai Shi ne mai amsawa, kuma mai cancanta ne da amsawa. Allah Ya yi tsira da aminci a bisa Annabi Muhammadu da alayensa da sahabansa baki ɗaya.

RAHAMA

Manufofin huɗubar

- Kwaɗaitar da mutane akan su siffantu da siffar rahama, domin siffa ce da Allah ya siffantu da ita a bisa kamala.
- Shiryar da Mutane abisa fatan samun rahama.
- Nesantar ɗebe tsammani da samun rahama.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo ya tabbata ga Allah muna gode masa muna neman taimakonsa muna neman gafararsa muna neman tsarinsa daga sharrance-sharrancen kawunanmu da kuma munanan aiyukanmu. Wanda duk Allah ya shirye shi babu mai ɓatar da shi wanda duk ya ɓatar da shi babu mai shiryar da shi, ina shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah shi kaɗai ba shi da da abokin tarayya, ina shaidawa kuma Annabi Muhammad bawansane kuma manzonsane.

"Ya ku waɗanda sukai imani kuji tsoron Allah matuƙar tsoronsa kada ku kuskura ku mutu face kuna musulmai".

"Ya ku mutane kuji tsoron Ubangijinku wannan da ya halicceku daga rai guda ɗaya sannan ya halitta masa matarsa daga, ya yaɗa zuriyya daga su biyun maza da mata, don haka ku ji tsoron Allah wannan da kuke yin roƙo da shi da kuma zumunci haƙiƙa Allah ya kasance a kanku mai tsaro".

"Ya ku waɗanda suka yi imani kuji tsoron Allah ku faɗi magana ta dai dai sai Allah ya gyara muku aiyukan ku kuma ya gafarta muku zunubanku duk wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabo mai girma"

Bayan haka:

Ya ku bayin Allah! Haƙiƙa jin ƙai da rahama siffofine guda biyu daga cikin siffofin Ubangiji maɗaukaki, kuma sunayene daga cikin sunayensa mafiya kyau. Kamar yadda sunan "Arrahmaan" ya fi kaiwa matuƙa akan sunan "Arraheem" domin shi sunan "Arrahmaan" yana nufin mai rahma gamammiya da ta shafi dukkanin halittu a nan gidan duniya, da kuma muminai a can gidan lahira. Amma sunan "Arraheem" yana nufin mai rahma ga bayinsa muminai a can ranar alƙiyama. Wannan ita maganar mafiya yawancin malamai.

A cikin rahmarsa ne muke jujjuyawa inda muke so ba tare da iyaka ba. Ubangiji maɗaukaki ya ce,

﴿ مَّا يَفۡتَحِ ٱللَّهُ لِلنَّاسِ مِن رَّحۡمَةٖ فَلَا مُمۡسِكَ لَهَاۖ وَمَا يُمۡسِكۡ فَلَا مُرۡسِلَ لَهُۥ مِنۢ بَعۡدِهِۦۚ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ٢ ﴾ [فاطر: ٢].

(Idan Allah ya buɗe ƙofar rahmarsa ga bayinsa to babu mai riƙeta. Idan kuma ya riƙe ta babu mai buɗe ta bayan shi. Kuma shi ne mabuwayi mai hikima).

Malam Shanƙiyɗiy (R.A) ya ce: "Rahmar da ake nufi a wannan ayar ta haɗa dukkan abin da Allah yake jin ƙan bayi da shi na ni'imarsa ta duniya ko ta lahira, kamar saukar musu da ruwan sama. Kamar yadda Allah (S.W.T) ya ce,

﴿ فَٱنظُرۡ إِلَىٰٓ ءَاثَٰرِ رَحۡمَتِ ٱللَّهِ كَيۡفَ يُحۡيِ ٱلۡأَرۡضَ بَعۡدَ مَوۡتِهَآۚ ﴾ [الروم: ٥٠].

(Ka yi duba izuwa gurbin rahmar Ubangiji, ka ga yadda yake rayar da ƙasa bayan mutuwarta).

Da faɗin Maɗaukakin sarki:

﴿ وَهُوَ ٱلَّذِي يُرۡسِلُ ٱلرِّيَٰحَ بُشۡرَۢا بَيۡنَ يَدَيۡ رَحۡمَتِهِۦٓ ﴾ [الأعراف: ٥٧].

(Shi ne wanda yake turo da iska wacce take mai yin bishara da rahamarsa (ruwan sama)). Ya ce a wani ayar,

﴿ وَرَحۡمَتِي وَسِعَتۡ كُلَّ شَيۡءٖۚ فَسَأَكۡتُبُهَا لِلَّذِينَ يَتَّقُونَ وَيُؤۡتُونَ ٱلزَّكَوٰةَ وَٱلَّذِينَ هُم بِـَٔايَٰتِنَا يُؤۡمِنُونَ ١٥٦ ﴾ [الأعراف: ١٥٦].

(Rahamata ta wadaci dukkan komai. Sannan zan bayar da ita ga waɗannan da suke jin tsorona kuma suke bayar da zakka da waɗannan da suke yin imani a game da ayoyinmu).

Wannan rahamar wadda ta wadaci dukkan komai, rahama ce ta gabaɗaya, domin babu wani abin halitta face wannan rahama ta shafe shi a nan duniya ko kuma a lahira.

Ya ku Musulmi! Haƙiƙa ana buƙatar da mu yi rahama da tausayi a junanmu saboda daliali dadama.

Daga cikin dalilan akwai cewa, Allah shi ne ya umarcemu dayin hakan, don haka ya zama dole a gare mu mu bi umarninsa. Kamar yadda Annabi (ﷺ) ya faɗa a halin yana kan mimbarinsa: "Ku ji ƙai, kuma sai a ji ƙanku. Kuma ku yi gafara kuma sai a yi muku gafara azaba ta tabbata ga masu ƙin jin magana, masu dagewa akan abinda suka aikata na saɓo alhalin sun sani" [Ahmad da Ṭabarani].

Idan muka ɗabi'antu da wannan ɗabi'a mai kyau sai Allah ya kawo wanda zai jiƙanmu a nan duniya da lahira, kuma daman shi Allah shi yake jin ƙan mu. An karɓo daga Abdullahi ɗan Amr ɗan Ass, daga Annabi (ﷺ) ya ce: "Masu jin ƙai Allah mai jin ƙai yana jin ƙansu, don haka ku ji ƙan waɗanda suke ƙasa, sai Allah wanda yake sama ya ji ƙanku". [Imam Ahmad da Abu Dawud da Tirmizi da al-Hakim suka ruwaito shi. Tirmizi ya ce, wannan hadisin kyakkyawa ne ingantacce].

An karɓo daga Jarir ya ce, "Na ji Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: "Duk wanda baya jin ƙan mutane ba, to shi ma Allah ba zai ji ƙansa ba". Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.

Daga cikin nau'ukan rahamar Ubangiji, akwai samar da halittu abisa mafi kyawun tsari da kuma karrama ɗan Adam da fifita shi bisa mafi yawan halittu. Allah maɗaukakin sarki ya ce,

﴿ لَقَدۡ خَلَقۡنَا ٱلۡإِنسَٰنَ فِيٓ أَحۡسَنِ تَقۡوِيمٖ ٤ ﴾ [التين: ٤].

Ma'ana: (Haƙiƙa mun halicci mutum a cikin mafi kyawun zubi).

Sannan da faɗinsa,

﴿ وَلَقَدۡ كَرَّمۡنَا بَنِيٓ ءَادَمَ وَحَمَلۡنَٰهُمۡ فِي ٱلۡبَرِّ وَٱلۡبَحۡرِ وَرَزَقۡنَٰهُم مِّنَ ٱلطَّيِّبَٰتِ وَفَضَّلۡنَٰهُمۡ عَلَىٰ كَثِيرٖ مِّمَّنۡ خَلَقۡنَا تَفۡضِيلٗا ٧٠ ﴾ [الإسراء: ٧٠].

(Haƙiƙa mun girmama 'yan Adam, mun ɗauke su a kan tudu da teku kuma mun azurta su daga daɗaɗa abubuwa, sannan muka fifita su sosai akan dayawa daga cikin waɗanda muka halitta).

Yana daga cikin rahamarsa ya ɗorawa kansa nauyin azurta bayinsa. Bai ɗora nauyin wani akan wani ba. Ba ɗora nayin abin cin ‘ya’ya akan iyayensu ba, hakanan suma iyayen ba bar su da ‘ya’yansu ba. A’a kowa yana rayuwa ne ƙarƙashi inuwar falalarsa da kyautatawarsa. Allah ya ce,

﴿ وَكَأَيِّن مِّن دَآبَّةٍ لَّا تَحۡمِلُ رِزۡقَهَا ٱللَّهُ يَرۡزُقُهَا وَإِيَّاكُمۡۚ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ ٦٠ ﴾ [العنكبوت: ٦٠].

(Da yawa daga cikin halitta ba sa ɗauke da arzikinsu. Allah ne ke azurtasu da kuma ku. Kuma shi ne mai ji kuma masani).

Ubangiji ya ce:

﴿ وَمَا مِن دَآبَّةٍ فِي ٱلۡأَرۡضِ إِلَّا عَلَى ٱللَّهِ رِزۡقُهَا وَيَعۡلَمُ مُسۡتَقَرَّهَا وَمُسۡتَوۡدَعَهَاۚ كُلّٞ فِي كِتَٰبٖ مُّبِينٖ ٦ ﴾ [هود: ٦].

(Babu wata dabba a cikin ƙasa face arzuƙinta na wajen Allah kuma ya san matabbatarta da makwantarta duk wannan yana cikin littafi mabayyani).

Yana daga cikin rahamarsa da ya hore mana duk abin da yake cikin sama da ƙasa domin kyautatuwar rayuwarmu, da kuma tsarin rayuwarmu. Allah ya ce,

﴿ وَسَخَّرَ لَكُمُ ٱلَّيۡلَ وَٱلنَّهَارَ وَٱلشَّمۡسَ وَٱلۡقَمَرۖ وَٱلنُّجُومُ مُسَخَّرَٰتُۢ بِأَمۡرِهِۦٓۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ يَعۡقِلُونَ ١٢ ﴾ [النحل: ١٢].

Ma’ana: “Ya hore muku dare da wuni, da rana da wata da taurari dukkanin wannan da umarninsa. Lalle a cikin wannan akwai ayoyi ga mutanen da suke da hankali).

Allah (S.W.T) ya ce,

﴿ هُوَ ٱلَّذِي خَلَقَ لَكُم مَّا فِي ٱلۡأَرۡضِ جَمِيعٗا ﴾ [البقرة: ٩٢].

(Shi ne wannan da ya halitta muku duk abin da yake bayan ƙasa baki ɗaya).

Ya ku musulmi yana daga cikin rahamar Allah aiko mana da manzanni masu bushara masu gargaɗi. Suna sanar da bayi Ubangijinsu, suna kiransu zuwa ga bautawa Allah shi kaɗai. Suna sanar da su gaskiya, suna tsoratar da bin hanyar ɓata da ɓarna. Allah maɗaukaki ya ce,

﴿ لَقَدۡ أَرۡسَلۡنَا رُسُلَنَا بِٱلۡبَيِّنَٰتِ وَأَنزَلۡنَا مَعَهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡمِيزَانَ لِيَقُومَ ٱلنَّاسُ بِٱلۡقِسۡطِۖ وَأَنزَلۡنَا ٱلۡحَدِيدَ فِيهِ بَأۡسٞ شَدِيدٞ وَمَنَٰفِعُ لِلنَّاسِ وَلِيَعۡلَمَ ٱللَّهُ مَن يَنصُرُهُۥ وَرُسُلَهُۥ بِٱلۡغَيۡبِۚ إِنَّ ٱللَّهَ قَوِيٌّ عَزِيزٞ ٢٥ ﴾ [الحديد: ٢٥].

(Haƙiƙa mun turo manzannin mu da hujjoji bayyanannu, sannan mun saukar musu da littafi da mizani (abin awo), don mutane su tsayar da gaskiya. Muka saukar da ƙarfe, a cikinsa akwai ƙarfi mai tsanani, da kuma abin amfani ga mutane, don Allah ya san waye wanda zai taimake shi da manzanninsa a fake).

Maɗaukakin sarki ya ce,

﴿ رُّسُلٗا مُّبَشِّرِينَ وَمُنذِرِينَ لِئَلَّا يَكُونَ لِلنَّاسِ عَلَى ٱللَّهِ حُجَّةُۢ بَعۡدَ ٱلرُّسُلِۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَزِيزًا حَكِيمٗا ١٦٥ ﴾ [النساء: ١٦٥].

(Manzanni masu bushara da gargaɗi don kada ya kasance mutane suna da wata hujja a wajen Allah bayan manzanni sun zo).

Yana daga cikin rahamarsa da ya yi mana shi ne, turo mana shugaban mutanen farko da na ƙarshe, kuma shugaban masu tsoron Allah Annabi Muhammad (ﷺ) wanda manzancinsa gamammiyar rahama ce ga duniya baki ɗaya. Kuma littafin da aka saukarmasa gargaɗi ne ga duniya duka. Allah maɗaukakin sarki ya ce:

﴿ وَمَآ أَرۡسَلۡنَٰكَ إِلَّا رَحۡمَةٗ لِّلۡعَٰلَمِينَ ١٠٧ ﴾ [الأنبياء: ١٠٧].

(Bamu aiko ka ba face rahama ga mutanen duniya baki ɗaya).

Yana daga cikin rahamarsa ga bayinsa, ita kanta wannan shari’a cikakkiya, mai

cikakken tsari da kamala, mai tattare kyawawan ɗabi'u. Ubangiji ya sanya ta ta zamana ta dace da kowa ne zamani da kowa ce al'umma. Allah ta'ala ya ce,

﴿ ٱلۡيَوۡمَ أَكۡمَلۡتُ لَكُمۡ دِينَكُمۡ وَأَتۡمَمۡتُ عَلَيۡكُمۡ نِعۡمَتِي وَرَضِيتُ لَكُمُ ٱلۡإِسۡلَٰمَ دِينٗاۚ ﴾ [المائدة: ٣].

(A yau ne na cika muku addininku, kuma na cika ni'imata gareku, kuma na yarje muku musulunci shi ne addini).

Allah ya ji tausaya mana da wannan shari'ar haɗaɗɗa, wacce Allah ya ɗauke ƙunci da tsanani daga cikinta, irin wanda yake cikin shari'o'in da suka gabace ta. Allah yana faɗa dangane da siffanta Annabinsa:

﴿ وَيَضَعُ عَنۡهُمۡ إِصۡرَهُمۡ وَٱلۡأَغۡلَٰلَ ٱلَّتِي كَانَتۡ عَلَيۡهِمۡۚ ﴾ [الأعراف: ١٥٧]

(Kuma yana sauke musu nauyi da ƙuƙumin da yake kansu).

Wannan shari'a ce da aka gina ta akan sauƙi da sauƙaƙewa:

﴿ يُرِيدُ ٱللَّهُ بِكُمُ ٱلۡيُسۡرَ وَلَا يُرِيدُ بِكُمُ ٱلۡعُسۡرَ ﴾ [البقرة: ١٨٥].

(Allah yana nufin sauƙi gare ku, baya nufin tsanani).

Annabi (ﷺ) yana cewa sahabbansa: "Ku sassauta kada ku tsananta, kuyi bishara kada ku kore". Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.

Ya ku bayin Allah! Haƙiƙa rahamar Annabi zaɓaɓɓen Allah wacce aka ruwaito ta hanyoyi da yawa kuma wanda yake nesa da wanda yake kusa duk sun shaida da ita. Allah ya yi gaskiya cikin faɗinsa:

﴿ لَقَدۡ جَآءَكُمۡ رَسُولٞ مِّنۡ أَنفُسِكُمۡ عَزِيزٌ عَلَيۡهِ مَا عَنِتُّمۡ حَرِيصٌ عَلَيۡكُم بِٱلۡمُؤۡمِنِينَ رَءُوفٞ رَّحِيمٞ ١٢٨ ﴾ [التوبة: ١٢٨].

(Haƙiƙa wani manzo ya zo muku daga cikinku, duk abin da zai cutar da ku baya son sa, kuma yana yin kwaɗayin alheri a gare ku shi mai tausayi ne mai jin kai dangane da muminai).

Yana daga cikin irin jin ƙan Annabi (ﷺ)

1. Akan abokan gabasa: Yayin da ya kirawo mutanen garin Ɗa'ifa zuwa ga Musulunci sai basu amsa masa ba, suka sanya wawayensu suka cutar da shi, har takai Annabi (ﷺ) ya fito dugadugansa masu albarka suna zubar jini. Allah ya turo Mala'ikan da yake kulawa da duwatsu yana don ya zartar da duk wani umarni da Annabi zai yi masa, yana cewa, "In ka so zan jefo musu manyan duwatsu guda biyu su rufe su". Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Kada ka aikata haka, babu mamaki Allah ya fitar da wanda zai bauta masa daga cikin tsatsonsu".
2. Rahamarsa ga Jahilai: Wani Balaraben ƙauye ya yi fitsari a cikin masallaci, sai sahabbai suka tashi don su hora shi. Sai Ma'aiki ya hana su. Har sai da ya gama fitsarinsa, sannan Manzo Allah (ﷺ) ya ce, "A kawo cukin guga na ruwa a kwarara akan fitsarin". Sannan sai ya ce da sahabbai, "Ku sani fa an taso ku ne don ku zama masu sassauci ba a tasu ku ba don ku zama masu tsanani, don haka ku sassauta kada ku tsananta". Sai ya ce da Balaraben ƙauyen: "Waɗannan masallatan an gina su ne kawai domin ambaton Allah, da Sallah". Bayan wannan baƙauye ya yi samu cikakkiyar tarbiyya ta musulunci ya zan yana cewa, "Na fansheka da uwata da Ubana ya Ma'aikin Allah! Bai kyare ni ba, bai hantare ni ba".

Hakanan kuma wani baƙauyen shi ma ya zo wajen Manzon Allah (ﷺ) ya caka faratansa a kafaɗar Manzon Allah (ﷺ). Annabi ya waiwaya ya kalle shi yana murmushi).

Wani kuma zai bawa Manzon Allah (ﷺ) bashi, sai kuma ya zo karɓar bashinsa kafin wa'adin ya cika, kuma ya ce ya Muhammad ba ni bashina domin ku iyalan Abdulmuɗalib kuna da taurin bashi. har sahabbai su harzuƙa, su tashi domin dukansa, sai Manzon Allah (ﷺ) ya hana su, kuma ya ce "Lalle mai gaskiya yana da ikon magana akan haƙƙinsa".

3. Rahamarsa ga sauran muminai: An karɓo daga Malik ɗan Huwairis (R.A) ya ce: "Mun zo wajen Manzon Allah (ﷺ) kuma mu duka samari ne tsarekun juna. Muka zauna a wajensa har tsawon kwana ashirin. Sai Annabi Muhammad ya fahimci kamar muna da buƙata zuwa ga iyalanmu, sai muka faɗa masa hakan. Ya kasance mai sauƙin hali ne da tausayi. Sai ya ce: "Ku koma wajen iyalanku, ku koyar da su addinin musulunci. Kuma ku yi sallah kamar yadda kuka ganni ina sallah. Kuma idan lokacin sallah ya yi ku umarci ɗayan ku ya yi kiran sallah, sannan babbanku ya yi maku limanci".

Ya ku bayin Allah, ku sani tausayin shugaba akan al'ummar Annabi Muhammad (ﷺ) tilas ne.

Annabi (ﷺ) yana addu'a yana cewa, "Ya Allah duk wanda ya sami wani shuganci na al'ummata, kuma ya tausaya masu, to ka tausaya masa. Wanda ya shugabanci wani al'amari na al'umma ta sannan ya ƙuntata musu, to shi ma ka ƙuntata masa". (Bukhari da Muslim).

Haka kuma musulunci yayi bayanin irin rahamar da za ayiwa dabbobi da kuma hani akan cutar da su kamar:

- Tsare su ba tare da ba su abin ciba: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Wata mata ta shiga wuta saboda wata mage da ta tsare ta har ta mutu. Ba ta ba ta abinci ba, kuma ba ta barta ta nema da kanta ba".
- Haɗa dabbobi faɗa. Yin haka haramun ne. Annabi (ﷺ) ya hana a riƙa haɗa faɗa tsakanin dabba da dabba.
- Koyon harbi akan wata dabba. Yin haka shi ma haramun ne. Domin Manzon Allah (ﷺ) ya tsinewa wanda ya ke koyon harbi akan wani abu mai rai).
- Kashe daba don wasa kwai. Wannan shi ma haramun ne a musulunci. Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle tsuntsu zai nuna rashin yardar sa ranar gobe alƙiyama, ya riƙa cewa "Ya Ubangiji wane ya kashe ni don wasa kwai, ba don ya yi amfani da ni ba".

Kuma har a wajen yanka Manzon Allah ya ce: "Idan za ku yi kisa (hadi) to ku kyautata kisan. Idan kuma za ku yi yanka, to ku kyutata abin yankan. Kuma ɗayanku ya wasa abin yankansa, domin ya hutar da abin da zai yanka".

Sannan Manzon Allah (ﷺ) ya ga wani mutum ya danne akuyarsa da ƙafarsa, kuma yana wasa wuƙarsa, sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce masa: “Tir da kai! Har sau biyu za ka kashe ta!! Mai ya hana ba ka wasa wuƙar ka ba kafin ka danne ta domin yanka?”.

Ina faɗin abinda kuke ji, ina kuma neman gafarar Allah da ni da ku, daga dukkan zunubi, ku nemi gafarar sa domin shi mai gafara ne mai jin ƙai.

Huɗuba Ta Biyu

Yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah tsira da amincin Allah su tabbata ga fiyayyen halitta Annabin Muhammad da alayensa da sahabbansa, da duk waɗanda suka bi tafarkin su har zuwa tashin ƙiyama. Bayan haka:

Ku sani ya ku musulmi, babu wanda yake da tabbacin dawwamar wani hali da yake ciki, domin wadata tana zuwa bayan talauci. Haka kuma talauci yana zuwa bayan wadata. Rashin lafiya tana zuwa bayan lafiya, haka kuma lafiya tana zuwa bayan rashin lafiya. Don haka babu wani hali da yake dawwama ga mutum, Allah (S.W.T) ya na cewa:

﴿ قُلِ ٱللَّهُمَّ مَٰلِكَ ٱلۡمُلۡكِ تُؤۡتِي ٱلۡمُلۡكَ مَن تَشَآءُ وَتَنزِعُ ٱلۡمُلۡكَ مِمَّن تَشَآءُ وَتُعِزُّ مَن تَشَآءُ وَتُذِلُّ مَن تَشَآءُۖ بِيَدِكَ ٱلۡخَيۡرُۖ إِنَّكَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ٢٦ ﴾ [آل عمران: ٢٦].

(Ka ce, Ya Allah mamallakin mulki, kana bayar da mulki ga wanda kake so, kana karɓe mulki ga wanda kake so, kuma kana buwayar da wanda kake so, kuma kana ƙasƙantar da wanda kake so ga hannunka alheri yake. Lallai ne kai akan kowane abu, mai ikon yi ne).

Manzon Allah (ﷺ) ya ga aba Mas’ud ya na dukan ɗansa, sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce masa “Kaji tsoron wanda yafi ka ƙarfi, akan sa”.

Sannan babu makawa sai mun dinga yin wannan tausayin a aikace, kamar yadda wani mutum ya zo wajen Annabin Allah yana kukan ƙeƙashewar zuciyarsa, sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce masa “Ka shafi kan maraya, kuma kaciyar da miskini".

Sannan ka riƙa tuna batun sakamako, domin duk abin da ka yi, shi za a yi maka. Annabi (ﷺ) ya ce, “Duk wanda ya yayewa wani baƙin cikinsa, a nan duniya, to shi ma Allah zai yaye masa baƙin cikinsa a lahira. Sannan kuma duk saurayin da ya taimaki tsoho, shi ma Allah zai haɗa shi da wanda zai karrama shi idan ya tsufa.

Ya ku bayin Allah! Ribar rahama shi ne samun tausayi da soyayya tsakanin ‘yan uwa. Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Misalin muminai wajen soyayyarsu da jin ƙan junansu da da tausyinsu kamar jiki guda ne, idan wata gaba ta kamu da rashi lafiya duk sauran jikin sai ya amsa da rashin barci da zazzabi” [Bukhari ne ya ruwaito].

Kuji tsoron Allah ya ku musulmi, ku sani cewa, ana nemanku da ku yiwa juna rahama da tausayi gwargwadon abin da za ku iya. Kuma mutum ya tausayawa iyalansa da makwabtansa da abokan aikinsa, kada ku taimakawa matanku akan yin sharri ko ‘ya’yanku.

Ku sani yana daga cikin fadin Manzon Allah (ﷺ) yana cewa:“Yana daga cikin girmama Allah ta’ala girmama musulmi mai furfura. da mahaddacin Kur’ani wanda baya ƙetare iyaka ko jafa’i. Da kuma girmama shugaba mai adalci. [Abu Dawud ne ya ruwaito shi].

Ku gu ji fada cikin abin da Manzon Allah (ﷺ) ya hana inda yake cewa, “Baya tare da mu wanda ba ya tausayin na ƙasan mu, kuma bai san mutuncin manyan mu ba”. [Abu Dawud ne ya ruwaito shi].

Yana daga cikin amfanin tausayawa samun rabuta da yardar Allah a nan duniya da lahira. Allah yana cewa,

﴿ وَمَن يُطِعِ ٱللَّهَ وَٱلرَّسُولَ فَأُوْلَٰٓئِكَ مَعَ ٱلَّذِينَ أَنۡعَمَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِم مِّنَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ وَٱلصِّدِّيقِينَ وَٱلشُّهَدَآءِ وَٱلصَّٰلِحِينَۚ وَحَسُنَ أُوْلَٰٓئِكَ رَفِيقٗا ٦٩ ﴾ [النساء: ٦٩].

(Duk wanda ya yi wa Allah da’a da Manzonsa, to wadannan suna tare da wadanda Allah ya yi masu ni’ima daga Annabawa da masu gaskiya da shahidai da salihan bayi. Madallah da wadannan abokan tafiyar. Wannan falalace daga Allah kuma Allah ya isa ya zama masani).

Kwaɗaitarwa Wajen Neman Halal Da Nisantar Haram

Manufofin huɗubar

- Kira zuwa ga neman halal.
- Kwaɗaitarwa akan gudun duniya da nisantar haramun.
- Bayanin falalar neman halal da bala'in da yake cikin neman haramun.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga shirrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammad bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammad (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Yaku 'yan uwana musulmi : Waye a cikinmu ba ya son rayuwa mai daɗi duniya da lahira? Wane ne a cikinmu ba ya son ya zama lami – lafiya a cikin gidansa! Yana da abin da zai ci? Waye a cikinmu yake son ya zama nauyi akan wani!?. To ku taho – Yaku bayin Allah – zuwa abin a zai sa mu samu waɗancan abubuwan, ku taho zuwa ga wani abu mai girma, wanda yake a cikinsa gyaruwar duniya da lahira take, wanna abu kuwa shi ne neman halal da nisantar haramun.

Haƙiƙa Allah Maɗaukakin Sarki ya halatta mana daɗaɗan abubuwa, ya haramta mana munanan abubuwa, masu cutar da jikinmu da hankulanmu, babu ko shakka halal shi ne abin da ya zama mai daɗi a karan – kansa, kuma babu cutarwa a cikinsa, sannan aka same shi ta hanyar da shari'a ta yarda da ita. Haramun kuwa shi ne abin da yake mai cutarwa a karan – kansa, wanda Allah da Manzonsa suka haramta shi, ko kuma aka same shi ta hanyar da shari'a ta haramta.

Bayin Allah, Neman abinci wani abu ne da Allah ya halicci halitta da shi, don haka ya sanya mana rana ta zama lokacin neman abincin, ya sanya mana dare ya zama lokacin hutu gare mu, ya umarce mu da fita da tafiya a bayan ƙasa don neman abinci da cin abin da ya sanya a bayanta na arziƙi.

Manzon Allah (ﷺ) ya nuna falalar neman halal inda yake cewa : “Babu wani abin da mutum zai ci da yafi alheri fiye da abin da ya samu ta hanyar aiki da hannunsa. Annabin Allah Dawud ya kasance yana ci daga abin ya yi da hannunsa” Bukhari ne ya rawaito.

Don haka wadatuwa ga barin mutane da hanyar neman halal abu ne mai girma, ɗaukaka ce babba, Sayyidina Umar ɗan Khaɗɗab (R.A) yana cewa : “Babu wani wuri da nake so mutuwa ta same ni a wajen fiye da wajen da nake saye da sayarwa, don in ciyar da iyalaina”.

A cikin neman halal akwai kare mutunci, da samun dukiya, da samun ɗaukakar da Allah ya yi wa ɗan Adam. An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Ababuwa huɗu idan kana da su, to kada ka damu da duk abin da ka rasa a duniya, (su ne) Kiyaye amana, gaskiyar zance, kyakkyawan hali, da kamewa a wajen abinci”. Imamu Ahmad ne ya rawaito da sanadi kyakkyawa.

Ya ‘yan uwana ku sani cewa neman halal wajibi ne, dole ne, domin babu wani wanda ƙafarsa zata gushe ranar alƙiyama face sai an tambaye shi a ina ya samu dukiyarsa kuma a ina ya kashe ta, don haka wajibi ne akan dukkan musulmi da musulma su kirdadi halal da aiki mai kyau, don su ci halal su ciyar da halal.

Ku yi duba – ya 'yan uwa ga sayyidina Abubakar – Allah ya yarda da shi – yaronsa ya kawo masa wani abinci ya ci, sai yaron ya ce, “Ko kasan a inda na sami wannan abincin?” sai ya ce, “a ina ka same shi” sai yaron ya ce, “Ai na yi wa wani mutum ne bokanci a lokacin jahiliyya, kuma ban iya bokancin ma ba, kurum dai na yaudare shi ne, don haka sai na gamu da shi sai ya bani ladan aikina, to wannan shi ne abin da ka ci!” nan da nan sai Abubukar ya shigar da ɗan ‘yatsan shi cikin bakinsa ya yi amai abin da yake cikinsa”. Bukhari ne ya rawaito.

A wata riwaya cewa ya yi : “Da wannan abun ba zai fita ba sai tare da raina, da na fitar da ran, Allah ina neman uzuri a kan abin da tumbi da jijiyoyi suka ɗauka ya rage bai fito ba”.

Hakanan Sayyidina Umar wata rana ya sha wani nono wanda ya ƙayatar da shi, sai ya cewa wanda ya kawo masa nonon, “a ina ka same shi?” sai ya ce, “Ai na wuce ni da wajen dabbobin sadaka, sai na tatsi nonon dabbobin”, nan da nan sai Umar ya shigar da hannusa cikin bakinsa ya amayar da shi.

Waɗannan su ne bayin Allah nagari waɗanda suke fitar haramun daga cikinsu, haramun ɗin da ya shiga bada saninsu ba, wanda da sun barshi babu komai a kansu, amma duk da haka suka amayar da shi, to me waɗanda suke cika cikinsu da haramun a yau zasu ce!. Inna lillahi Wa inna Ilaihi Raji’un.

Yaku masu sauraro : Haƙiƙa neman haramun yana haifar da munanan ababuwa a cikin al’umma, daga ciki abin da yake haifarwa : akwai yaɗuwar cututtuka, ɗebe

albarka, saukar musiba da bala'i iri iri, karayar arziki, zalunci, gaba, da zaman banza. Kaicon waɗanda suke cin haramun, suke renon 'ya 'yansu da iyalansu da haramun, haƙiƙa irin waɗannan mutane kamar masu shan ruwan kogi ne, suna ƙara sha suna ƙara jin ishirwa, ba sa wadatuwa da abu mai yawa, kaɗan kuma ba ya isarsu, suna bin karkatattun hanyoyin tara arziƙi, cin riba, caca, ƙwace, sata, tauye ma'auni, ɓoye aibin kayan sayarwa, sihiri, bokanci, cin dukiyar marayu da gajiyayyu, rantse – rantsen ƙarya, wasa da hauka, makirci, hanyoyi dai daban – daban karkatattu, sun zama irin mutanen nan da manzon Allah ya yi ishara da zuwansu inda yake cewa : "Zamani zai zo, mutum ya zama ba ya damuwa ta ina kuɗi ya zo masa, ta halal ne ko haram" Bukhari da Nasa'i suka rawaito.

'Yan uwana ma'aikata, 'yan kasuwa, masu sana'a, dillalai da 'yan kwangila dukkan musulmi da musulma, ku sani wajibi ne a kanku ku nemi halal, ku nisanci haramun, ku kiyaye haƙƙoƙin mutane, ku cika alƙawarin dake tsakaninku da Ubangijinku da wanda yake tsakaninku da mutane, ku nisanci ƙarya da algush, da cin dukiyar mutane da hanyar haramun, saboda cin halal ne jiki yake yin kyau, gaɓɓai suke samun nishaɗi, zuciya take gyaruwa, idan kuma an yi addu'a Allah ya amsa.

Yaku 'yan uwana samari : Manzon Allah (ﷺ) ya fifita kowace sana'a akan zaman banza da roƙon mutane, Yana cewa "Na rantse da wanda raina yake hannunsa, ɗayanku ya ɗauki igiyarsa, ya je ya yi itace, ya ɗauko a kan gadon bayansa, ya fi a kan ya je wajen wani mutum ya roƙe shi, ya bashi ko ya hana shi" Bukhari ya rawaito.

Don haka ma Sayyidina Umar – Allah ya yarda da shi – yake cewa : "Babu wani wuri da nake so mutuwa ta same ni a wajen fiye da wajen nake saye da sayarwa don in ciyar da iyalaina". Ya ci gaba da cewa : "Kada ɗayanku ya zauna ya ƙi neman arziƙi, ya riƙa cewa Allah ka azurta ni, alhali kun san sama ba ta yin ruwan zinari ko azurfa".

An tambayi Imam Ahmad – Allah ya yi masa rahama – cewa : "Me zaka ce akan wanda ya zauna a gida ko masallaci ya ce, ba zan yi aiki ba, ina nan har arziƙina ya zo ya sameni" sai Imam Ahmad ya ce, "wannan mutum ne jahili bai san ilimi ba, bai ji Manzon Allah (ﷺ) yana cewa ba : "Haƙiƙa Allah ya sanya min arziƙina a ƙarƙashin takobina ba".

An karɓo daga Hassan ya ce, "Abubuwa biyu masu daɗi ne : abin da mutum ya samu ta hanyar dakon da ya yi a bayansa, da abin da ya samu da hannunsa".

Abu Wa'il – Allah ya yi masa rahama – shi kuma cewa yake : "Dirhamin da na samu ta hanyar kasuwanci ya fi guda goman da na samu ta hanyar kyauta".

Sa'id ɗan Musayyib – Allah ya yi masa rahama – yana cewa : "Babu alheri a tare da wanda ba ya neman dukiya, wadda zai biya bashi da ita, ya kare mutuncinsa, ya sauƙe nauyinsa, in kuma ya mutu ya bar wa magada abin gado".

Wannan fa kaɗan kenan daga cikin irin yadda musulunci yake kwaɗaitar da mabiyansa wajen neman halal da nisantar roƙo da bara da ƙasƙanci da cin haramun. Manzon Allah (ﷺ) yana cewa : "Duk wanda ya yi roƙo (bara) alhali yana da abin

da ya ishe shi, to ranar alƙiyama zai zo da fuskarsa a kerkece kamar an yagushe ta. Sai aka ce, meye abin da zai ishe ɗin? Sai ya ce, “Dirhami hamsin, ko abin da ya yi daidai da shi na zinari”. Abu Dawud da Nasa’i da Ibnu Majah suka rawaito shi.

Da wannan ne zamu gane ƙasƙancin waɗanda ba sa neman na kansu sai dai bara da roƙon mutane, irin waɗannan mutane ba su san cewa neman halal yana da wani daɗi da gardi na musamman ba?, ya aka yi suka yarda suka zama kamar karnuka, suna bin duk abin da aka jefa musu cikin ƙasƙanci da wulaƙanci, ba sa tafiya face hancinsu yana ƙasa yana shinshine – shinshine. Allah Maɗaukakin Sarki ya kare mu, ya yi mana gamo – da – katar. (Ameen).

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah, Kyakkyawan ƙarshe yana ga masu tsoron Allah, Tsira da Aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, Manzon Allah (ﷺ) da iyalansa da Sahabbansa da waɗanda suka bi su gaba ɗayansu, har zuwa ranar sakamako. Bayan haka:

‘Yan uwana masu sauraro : Yana daga cikin abin da zai taimakemu wajen cin halal da barin haramun nisantar duniya, da rashin sa ta a zuciya, Manzon Allah (ﷺ) yana cewa, “Wanda duniya ta zama ita ce himmarsa, Allah zai rarrraba masa al’amarinsa, ya sanya masa talauci a gaban idonsa, ba kuma abin da zai samu na duniya sai abin da aka rubuta masa. Wanda kuwa lahira ce niyyarsa, Allah zai tattara masa al’amarinsa, ya sanya wadatarsa a cikin zuciyarsa, kuma duniya ta zo masa akan dole”. Ibnu Majah ne ya rawaito shi.

Hakanan an rawaito daga Abu Huraira (R.A), Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Bawan dinari ya taɓe, bawan dirhami ya taɓe, bawan riga ya taɓe, in ya samu ya yarda, in kuma bai samu ba ya yi fushi, (To irin wannan mutum) idan ƙaya ta soke shi kada (Allah) ya cire masa. Madallah da bawan da yake riƙe da ragamar dokinsa saboda Allah, kansa ya yi ƙura da gizo, idan yana gadi to zai tsaya wurin gadinsa, idan aka ajiye shi a bayan runduna, to zai tsaya a bayan, idan ya nemi izini ba a yi masa izinin ba (saboda an raina shi) idan ya nemi alfarma ba a yi masa. (To madallah da wannan bawa a kan wancan bawan duniyar). Bukhari ne ya rawaito.

Ku sani – Yaku bayin Allah – cin haramun da tara haramun yana jawo fushin Allah Maɗaukakin Sarki a kan bawa, saboda Allah mai tsarki ne, ba ya karɓar aiki kuwa sai mai tsarki, don haka duk wanda ya tara haramun, ya zama shi ne cin sa da shan sa, to ya sani babu shi ba Allah, ya yi nisa da Allah Maɗaukakin Sarki.

Ibnu Kayyim – Allah ya yi masa rahama – ya ce, “Ba abin da yake sa bawa ya yi abin da Allah ya haramta masa sai abubuwa guda biyu : Abu na farko, munana zato ga Allah, da tunanin cewa idan ya bi Allah, ba zai bashi wani abin alheri ba. Abu na biyu : ya kasance ya san cewa duk wanda ya bar wani abin da Allah ba ya so don Allah, Allah zai canza masa wanda ya fi alheri, amma sai kawai sha’awarsa ta rinjayi haƙurinsa (ya kasa haƙuri), son zuciyarsa ya rinjayi hankalinsa, (sai kawai ya afkawa haramun ɗin). Na farko raunin ilimi ne ya kawo shi, abu na biyu

kuwa raunin hankali da basira”. (Al – Fawa’id shafi na 48).

Yaku musulmi : Yana daga cikin albarkar halal idan mutum ya yi sadaka da shi, Allah yana karɓar wannan sadakar ya reneta, kamar yadda ɗayanku yake renon ɗan goɗiyarsa. An karɓo daga Abu Hurairata – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Wanda ya yi sadaka da wani abu kwatankwacin dabino na halal – Allah ba ya karɓar wani sai mai tsarki – to Allah zai karɓi wannan sadakar da hannunsa na dama, ya reneta kamar yadda ɗayanku yake renon ɗan goɗiyarsa, har ta zama kamar dutse”.Bukhari da Tirmizi da Ibnu Majah.

Ya ‘yan uwa : yana cikin mafi girman abin da yake sa a buɗe ƙofofin rahama da arziƙi ga mutane tsoron Allah Maɗaukakin Sarki, Allah yana cewa :

﴿ وَلَوۡ أَنَّ أَهۡلَ ٱلۡقُرَىٰٓ ءَامَنُواْ وَٱتَّقَوۡاْ لَفَتَحۡنَا عَلَيۡهِم بَرَكَٰتٖ مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلۡأَرۡضِ ﴾ [الأعراف: ٩٦]

Ma’ana : (Da mutanen alƙarya sun yi imani sun ji tsoron Allah da mun buɗe musu abarkatu daga sama da ƙasa) (Al – A’araf : 96).

Don haka dukkan alheri yana cikin tsoron Allah, duk wanda ya ji tsoron Allah, Allah ya isar masa, kuma zai sanya masa mafita daga dukkan wani ƙunci da yake ciki, ya azurta shi da inda baya zato, babu yadda za a yi rayuwa ta yi ƙunci ga wanda ya ji tsoron Allah ya kiyaye dokokinsa.

Yana daga cikin mafi girman gudun duniya barin haramun, babu gudun duniya da tsoron Allah ga wanda yake cin haramun, ko yake mu’amala da haramun, ko yake zaluntar mutane, saboda haka wajibi ne a kanka ya kai – bawan Allah – ka kuɓuta daga zalunci tun gabanin ka biya a ranar da babu dirmahi ko dinari, in kana da aiki na ƙwarai a ɗiba a ba wanda ka zalunta, in baka da shi a ɗebo munanan ayyukan wanda ka zalunta a ɗora maka. Allah ya tseratar damu daga wuta.

Ya ku bayin Allah : Babu wata rai da zata mutu face sai ta cika arziƙinta, don haka ku ji tsoron Allah ku kyautata hanyar neman abincinku, An karɓo daga Jabir – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Kada ku ga jinkirin arziƙi, babu wani bawa da zai mutu, har sai ya cika ƙarshen arziƙinsa, don haka ku kyautata neman halal, ku bar haramun" Ibnu Hibban ne ya rawaito.

Allah ka wadatamu da halal ɗin ka daga barin haramun ɗin ka, ka wadatamu da ɗa'arka mu bar saɓonka, ka wadata mu da falalarka, mu bar wanda ba kai ba. Ya Allah kada ka sa duniya ta zama ita ce babbar burinmu, ko ta zama ita ce ƙarshen iliminka, ko wuta ta zama makomarmu, muna roƙonka cin moriyar duk wani aikin alheri, da kuɓuta daga zunubi. (Ameen).

YIN AIKI DOMIN ALLAH

Manufofin hudubar

- Wajabcin tsarkake ayyuka domin Allah.
- Yana daga cikin sharuddan karɓar aikin mumini.
- Muhimmancinsa da haɗarinsa.
- Tsoratarwa dangane da abubuwan da suke rushe ikhlasi.
- Amfanin yin (Ikhlasi), tsarkake aiki da fa'idojinsa.

Hudduba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammadu bawansa ne manzonsa ne. (Yaku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron Allah yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Yaku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammadu (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (a addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta".

Bayan haka: Ya ku musulmi!

Wanene a cikinmu nan ba ya fatan ya zama karɓaɓɓe a gurin Allah?!

Wanene daga cikinmu a nan yake fatan ayyukansa su zama ƙura abar ɗaiɗaitawa?! ranar tsayuwarsa gaban Ubangijinsa?!

Wanene cikinmu a yau ba ya son ya gan shi cikin 'yan aljannah ranar gobe ƙiyama?!

Babban abin maganarmu a wannan haɗuwa tamu ta yau shi ne magana a kan tsarkake aiki domin Allah, wanda Allah ba ya karɓar ibada sai da shi. Kuma adalinlinshi ne Allah yake ɗaukaka darajar bawa. Ko ya ƙasƙantar da shi.

Allah ba ya karɓar aikin bayi sai idan an yi aikin dominsa. Duk wanda ya aikata aiki ya yi tarayya da Allah a cikin wannan aiki, to Allah ya wadatu ga barin karɓar wannan aikin, duk kuwa yadda wannan aiki yake da yawa. Allah yana cewa:

﴿ إِنَّآ أَنزَلۡنَآ إِلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبَ بِٱلۡحَقِّ فَٱعۡبُدِ ٱللَّهَ مُخۡلِصٗا لَّهُ ٱلدِّينَ ٢ أَلَا لِلَّهِ ٱلدِّينُ ٱلۡخَالِصُۚ ﴾ [الزمر: ٢ – ٣].

“ Haƙiƙa mun saukar maka da littafi da gaskiya, ka bautawa Allah Shi kaɗai kana mai tsarkake aiki dominsa. Ku saurara tsarkakakken addini na Allah ne”.

Hakanan yake cewa:

﴿ قُلۡ أَمَرَ رَبِّي بِٱلۡقِسۡطِۖ وَأَقِيمُواْ وُجُوهَكُمۡ عِندَ كُلِّ مَسۡجِدٖ وَٱدۡعُوهُ مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَۚ ﴾ [الأعراف: ٢٩].

(Ka ce da su, Ubangijina ya yi umarni da tsayar da adalci. Kuma tsayar da fiskokinku a kowane masallaci. Kuma ku bautawa masa kuna masu tsarkake bauta dominsa).

Ya kuma cewa a wani wurin:

﴿ فَٱدۡعُواْ ٱللَّهَ مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ وَلَوۡ كَرِهَ ٱلۡكَٰفِرُونَ ١٤ ﴾ [غافر: ١٤].

(Ku bautawa Allah kuna masu tsarkake addini gare shi, Shi kaɗai, koda ƙafirai sun ƙi).

Hakanan ya sake cewa:

﴿ هُوَ ٱلۡحَيُّ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ فَٱدۡعُوهُ مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَۗ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٦٥ ﴾ [غافر: ٦٥].

(Shi ne rayayye babu abin bauta da gaskiya sai shi. To ku bauta masa kuna masu tsarkake addini gare shi. Gudiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai).

Ya sake cewa,

﴿ وَمَآ أُمِرُوٓاْ إِلَّا لِيَعۡبُدُواْ ٱللَّهَ مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ حُنَفَآءَ وَيُقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَيُؤۡتُواْ ٱلزَّكَوٰةَۚ وَذَٰلِكَ دِينُ ٱلۡقَيِّمَةِ ٥ ﴾ [البينة: ٥].

(Ba a umarce su da komai ba sai su bauta wa Allah suna masu tsarkake addini agare shi. Kuma su tsaida sallah, su ba da zakka, wannan shi ne addinin miƙaƙƙiyar hanaya).

Yin aiki domin Allah shi ne, ka yi aiki domin neman yardar Allah ba ta tare da haɗa shi da wani ba. Ba riya, ba yi don a ji. Idan aiki ya zama haka, to ya lalace, mai yin aikin ma ya halaka.

ImamTirmizi ya fitar da hadisi daga Shufayyu al-asbahi, wata rana ya shigo Madina sai ya ga taron mutane sun kewaye wani mutum. Sai ya ce, «Wanene wanna kuma?». Sai aka ce masa Abu Huraira ne. Sai na matsa kusa da shi na zauna a gabansa yana ba mutane hadisi. Bayan mutane sun watse, sai na ce da Abu Huraira na haɗa ka da Allah ka faɗa mini wani hadisi wanda ka ji shi daga manzon Allah, kuma ka kiyaye shi, kuma ka fahimce shi. Sai Abu Huraira ya ce, «Zan faɗa maka hadisin da na ji daga manzon Allah, kuma na kiyaye shi, na fahimce shi. Sai nan da nan Abu Huraira ya shiɗe. Sannan daga baya ya dawo hayyacinsa. Sai ya sake cewa, «Lallai zan faɗa maka hadisin da na ji daga manzon Allah a wannan gida, ba wani tare damu, daga ni sai shi. Sai ya sake shiɗewa. Sannan ya farfaɗo. Ya shafa ruwa a fuskarsa. Sai ya sake cewa, «Lallai zan faɗa maka hadisin da na ji daga manzon Allah a wannan gida, ba wani tare damu, daga ni sai shi. Sai ya sake shiɗewa. Sannan ya farfaɗo. Ya shafa ruwa a fuskarsa. Sannan ya yi wata sheɗewa mai ƙarfi, har ya kifa da fuskarsa. Na kama shi na riƙe shi a jikina na daɗe. Sai ya farfaɗo. Sai ya ce, «Manzon Allah (ﷺ) ya ba ni labari cewa, ranar

alƙiyama Allah Zai sauko domin hukunci a tsakanin bayi. Kowace al'umma an gurfanar da ita a gaban Allah. Farkon wanda Allah zai kira domin yi masa hisabi mutumin da Allah ya ba shi Alƙur'ani, da mutumin wanda ya mutu a wajen jihadi, da wanda Allah ya ba shi dukiya mai yawa. Sai Allah ya ce da makaranci, "Ban sanar da kai abin da na saukarwa Manzona ba?" Sai ya ce, "Allah Ka sanar da ni". Sai Allah ya ce, "To me ka yi da shi?" Sai ya ce, "Na kasance ina karanta shi dare da rana". Sai Allah ya ce, "Karya kake". Mala'iku ma su ce masa, "ƙarya kake". Allah ya ce,"Ka karanta shi ne don a ce maka makaranci, kuma an faɗa".

Sai a zo da mai dukiya, sai Allah ya ce, "Ban yalwata maka dukiya ba, har ka zamana ba kada buƙata a gurin wani?". Sai ya ce: E, ka yi ya Ubangiji". Sai Allah ya ce, "To me kai da dukiyar da na ba ka"? Sai ya ce, "Na kasance ina sada zumiunci, ina sadaka". Sai Allah ya ce, "Karya kake". Sai mala'iku ma su ce masa, "Karya kake. Sai Allah ya ce, "Ka yi ne don a ce maka mai kyauta, kuma an faɗa". Sai a zo da wanda aka kashe wajen ɗaukaka kalmar Allah. Sai Allah Ya ce da shi, "A kan me aka kashe ka?". Sai ya ce, An umarce ni da yin jihadi don ɗaukaka kalmarka, na yi yaƙi har aka kashe ni". Sai Allah ya ce, "Karya kake". Sai mala'iku su ma su ce masa, "Karya kake". Allah ya ce, "Kwai ka yi ne don a ce maka jarimi, kuma an faɗa.

Abu Huraira, ya ce, "Sai manzon Allah ya buge ni a gwiwoyina ya ce, "ya Aba hurairah, waɗannan su ne mutane uku da za ta fara ƙonawa a ranar alƙiyama".

Ya kamata mu kula da kyau, me ya sa makarancin al'ƙur'ani, alƙur'anin bai cece shi ba? Tun da ƙur'ani yana ceton masu karanta shi. Ba komai ya sa ba, saboda yana karanta al'ƙur'nin ne ba don Allah ba. Haka nan mai dukiya, alherin da yake yiwa mutane bai cece shi ba. Saboda ba don Allah ya yi ba. Haka shi ma wanda ya mutu a wajen jihadi. Wannan wa'azi ne da gargaɗi ga dukkanin mai hankali da lura.

Babbar shirka, ita ce ka sanya wa Allah abokin tarayya ana bauta masa. Mai yin wannan ya fita daga musulunci. Kuma duk aikinsa ya rushe.

Karamar shirka kuwa ita ce, yin aiki ko magana wanda shari'a ta kira shi shirka, duk da cewa ba ya fitar da mutum daga musulunci, kamar riya, ko aiki don aji a faɗa. To wannan yana tauye tauhidin mutum, kuma yana kure ikhlasi. Yana kuma ɓata aiki.

Imam Ahmad ya fitar da hadisi a cikin Musnad ɗinsa, daga Mahmud bn Labid, cewa manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Babban abin da na fi muku tsoro shi ne ƙaramar shirka". Sai sahabbai suka tambaye manzon Allah (ﷺ), Mene ne ƙaramar shirka? Sai ya ce, "Riya. Allah zai ce da su a ranar alƙiyama idan ya sakakwa bayi a kan ayyukansu, "Ku je wajen waɗanda kuke yi domin su, a duniya, ko ka samu sakamakonku a wajensu?".

Ibn Abbas ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Duk wanda ya yi abu don a ji ya zai jiyar game da shi. Hakanan duk wanda ya yi dan a gani, Allah zai nuna shi a gan shi". Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

Sau da yawa mutum zai yi aikin lahira don neman duniya da jin daɗinta. Kamar wanda zai je jihadi don neman ganima, ko neman ilimi don ya samu takardar shaida (Certificate) da samun aiki.

To irin wannan yana da yana biyu:

Na farko: Mutum ya nemi duniya tsantsarta da aikin lahira, ko ya daidaita neman duniyar da neman lahirar. Ko ya rinjayar da neman duniyar akan neman lahirar. To wannan yana rushe ikhlasi da aiki baki ɗaya.

An karɓo daga Ubayyu ɗan Ka'ab, ya ce, "Manzon Allah (ﷺ) ya ce, ka yi wa wannan al'umma bushara da ɗaukaka da kafuwa, da nasara a doron ƙasa. Duk wanda ya yi aikin lahira don neman duniya, to ba shi da rabo a wajen Allah". Ahmad ne ya rawaito.

Na biyu: Ya zamana ya yi akin ƙwarai ya kuma nufi wani abu da shi wanda yana daga cikin manufar shari'a a wannan ibadar, ko ma yana ƙarfa shi mai ibadar. To wannan ya halatta, kuma ba ya rushe ikhlashi. Duk da cewa, ladan mutum a nan ba zai kai kamar ladan wanda ya yi ikhlasi tsantsa ba.

Bin son-ciya kuwa, shi ne mutum ya riƙa bautar Allah saboda wata biyan buƙata ta shi ta karankansa, ba don Allah ba. To hakan yana rushe ikhlasin bawa.

Shi kuma jiji-da-kai, shi ne, mutum ya riga shi wani ne, saboda wani aiki da ya yi, ya ruɗu da wannan aikin. Ya daina tuna ni'imar Allah da ya yi masa kwata-kwata. To wannan ya ma fi riya tsanani da muni. Yana daga cikin shirka ta zuciya wanda yake lizimtar bawa. Domin bala'in da yake tattare da mai jiji-da-kai shi ne, shi yana aikin ibada ne ba don neman kusancin Allah mahalicci ba, a'a yana yin ta ne kawai don biyan buƙatar kansa. Saboda hakane Imamun Nawawi yake cewa: "Ikhlasi yana gamuwa wani lokaci da jiji-da-kai. Duk wanda ya yi jiji-da-kai a aikinsa to aikinsa ya rushe".

Girman kai, shi ne ƙin gaskiya da ganin ka fifiko akan jama'a, saboda jiji-da-kai. Shi ma yana daga cikin shirka ta zuci mai rushe ikhlasi mai ɓata aiki. Domin ba neman kusancin da Allah ya sa shi aikin ba. A'a yana aikin ibadar ne domin biyan wata buƙata ta karankansa. Da kuma ƙoƙarin nuna ya fi kowa, da wulaƙanta mutane.

Wanda duk zai aikata aikin ibada don Allah ya ba shi aljannah, ya tsirar da shi daga wuta wannan ba ya kure ikhlasi.

Bayyana aikin ibada na fili, da ɓoye saɓon Allah, wannan ba ya yiwa ikhlasi tangarɗa. Shari'a ma haka ta fi so. Don haka ba a hana aikata wani aki wanda shari'a ta amince a aikata shi, wai don tsoron riya. A'a za a yi umarni ne da aikata shi tare da yin ikhlasi a cikinsa.

Godewa mutum a kan wani aiki da ya yi domin Allah, ba ya lalata masa aikinsa. Wannan yana daga cikin ribar ƙafa. An karɓo daga Abu Zarr, ya ce, "An ce da manzon Allah, menene matsayin wanda ya yi aikin alheri, sai mutane suka yi ta yabonsa? Sai manzon Allah ya ce, "Wannan yana daga cikin bushara ta gaggawa ga mumini. Muslim ne ya rawaito.

Abubuwan da suke biyo bayan aiki na ibada, kuma waɗanda Allah ya halatta, tare da samuwar ikhlasi da kasancewar bawa ya yi aikinsa na ibada tun farko domin Allah, to waɗannan abubuwa da za su samu ba sa rushe ikhlasi. Kamar mutum ya je hajji ya haɗa da kasuwanci, ko ya sa da zumunci don Allah ya yalwata masa arzikinsa. Ko ba shi da lafiya ya yi sadaka don Allah ya ba sauƙi. Duk waɗannan abubuwa ba sa cin karo da ikhlasi.

Haɗa wata ibada da wata, wannan baya kore ikhlasi. Kamar mutumin da zai yi azumi da niyar neman lada da kuma karya sha'awarsa. Wannan abu ne ma mai kyau a shari'a.

Yin kwalliya don zuwa wajen ibada da haɗuwa da jama'a, wannan shi ma ba ya kore ikhlasi.

Amma da mutum zai riƙa yin abin da bai kamata ba a bainar jama'a da hujjar wai don kada a zarge shi da riya. Wannan kwata-kwata ba daidai ba ne.

Yin ɗa'a ko ƙarawa a kan abin da aka saba lokacin da aka ga masu ibada don koyi da su, wannan bai zama laifi ba, kuma ma ba shi alaƙa da riya ko kaɗan. Yana daga cikin albarkar zama da mutanen kirki. Matuƙar dai bawa ya yi aikinsa don Allah.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Na shai da babu abin bauta da gaskiya sai Allah shi kaɗai. Kuma na shaida lalle Annabi Muhammadu bawan Allah ne kuma manzonsa. Allah ya ƙara tsira a gare shi da sahabbansada alayensa bikiɗaya. Da duk waɗanda suka bi su da kyautatawa har zuwa ranar ƙiyama.

Bayan haka:

Yaku musulmai! Kamar yadda muka yi bayani a baya cewa, ikhlasi yakan cutu da wasu abubuwa, kamar jiji-da-kai, da neman sakamako na duniya akai aikin ibada. To duk wani abu da zai zama cikas ga ikhlasi to shari'a ta tanadin maganinsa.

Maganin jiji-da-kai shi ne mutum ya riƙa ganin baiwar da Allah ya yi masa da falalar da ya yi gare shi. Kuma duk wani abu da zai aikat to daga falalar Allah ne. Allah yana cewa:

﴿ وَلَوْلَا فَضْلُ ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ وَرَحْمَتُهُۥ مَا زَكَىٰ مِنكُم مِّنْ أَحَدٍ أَبَدًا ﴾ [النور: ٢١].

(Ba domin falalar Allah gare ku ba da rahamarsa, to babu wani daga cikinku da zai tsarkaka har abada. Sai dai Allah shi ne yake tsarkake wanda ya so).

Hakanan maganin neman abin duniya akan aikin ɗa'a, wanda yin haka yana cutar da ikhlasi, shi ne, bawa ya san fa cewa shi tsantsar bawa ne ga Allah. Don haka don ya yi wa Ubangijinsa hidima ba zai ce, haƙƙi ne akan Ubangijinsa sai lalle ya biya shi. Duk abin da Ubangiji zai ba shi na sakamako falala ce ta Allah gare shi.

Kamar yadda yana daga cikin abubuwa da suke cutar da ikhlasin bawa, idan ya yi wani aiki ya riƙa jin ya gama gamsuwa da aikin da ya yi. Magnanin irin wannan

lamari abu biyu ne:

Na farko: Ya riƙa hango gajiyawarsa, da kasawarsa, ya kuma gane cewa akwai nasibin shaiɗan da son zuciya a tattare da shi. Duk ƙarancin aiki da wuya ne ka samu shaiɗan ba shi da wani nasibi a cikinsa. An tambayi Manzon Allah game da waiwaye a sallah, sai ya ce, «Wani abu ne da shaiɗan yake sata daga sallar bawa». Ka ga fa wannan waiwaye ni kaɗan ya yi da idonsa, amma ga abin da ya kasance. To ina ga wanda zuciyarsa ce zai ta waiwayi wanin Allah?!

Hanyar magani ta biyu: Ita ce, bawa ya san cewa Allah yana da haƙƙoƙi diyawa akansa saboda kasancewar bawan Allah ne. Kuma bawa bai isa ya ce, zai biya Allah duk haƙƙoƙinsa da suke kansa. To don me ba zai ji kunyar zuwa ga Allah da ɗan aikinsa ba. Don haka wajibi ne ya riƙa tuhumar kansa akai-akai. Duk bawan da ba ya tuhumar kansa akai-akai to wannan jahili ne, mai ruɗar kansa.

Bayin Allah!

Akwai wasu abubuwa da za su taimaka bawa wajen ikhlasinsa bayan taimakon Allah. Waɗannan abubuwa kuwa su ne:

1. Bawa ya sa Allah a zuciyarsa koda yaushe. Ya yi aikinsa domin shi. Ya riƙa neman agajinsa yana cewa: «Ya Hayyu Ya ƙayyum, bi rahmatika Astagith".
2. Abu na biyu mutum ya san cewa, mutane ba sa amfanarwa kuma ba sa cutarwa. Don haka mu ma daina kawo su a tunaninmu yayin da muka wata ibada.
3. Bawa ya guji zuciyarsa mai umartar sa da mummunan aiki. Wacce take neman girma da fariya, da girma da yabo, da wulaƙanta mutane, da nuna musu girman kai, da yi musu izgili.
4. Mu guji shaiɗan la'ananne. Ka mu sake ya biy mana ta inda ba ma tsammani. Kamar wajen hira, ko alfahari, ko nuna kishi ga addini. Ko lokacin da mutane za su riƙa yabonsa suna nu sha'awarsu da abin da yake yi.

Yaku bayin Allah!

Ku riƙa halarto da Allah yayin ayyukanku. Ku sanya sirrinku ya zama ma fi tsarkaka daga zahirinku. Ku sani Allah ya san asiran bayinsa, babu wani abu da yake ɓuye masa a sama ko a ƙasa. Mu Karnta faɗar Allah da yake cewa:

﴿ وَمَا تَكُونُ فِي شَأۡنٖ وَمَا تَتۡلُواْ مِنۡهُ مِن قُرۡءَانٖ وَلَا تَعۡمَلُونَ مِنۡ عَمَلٍ إِلَّا كُنَّا عَلَيۡكُمۡ شُهُودًا إِذۡ تُفِيضُونَ فِيهِۚ وَمَا يَعۡزُبُ عَن رَّبِّكَ مِن مِّثۡقَالِ ذَرَّةٖ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَلَا فِي ٱلسَّمَآءِ وَلَآ أَصۡغَرَ مِن ذَٰلِكَ وَلَآ أَكۡبَرَ إِلَّا فِي كِتَٰبٖ مُّبِينٖ ٦١ ﴾ [يونس: ٦١].

(Babu wani sha'ani da za ka kasance a cikinsa. Kuma babu wani abu da kake karantawa na al'ƙur'ani, ko wani aiki da kuke yi face mun zamo muna halarce lokacin da kuke aikata shi. Kum babu wani da yake ɓuya ga Ubangijinka a ƙasa yake ko a sama, ko mafi ƙanƙanta daga haka, ko mafi girma face yana cikin littafi mabayyani).

RANAR JUMA'A DA HUKUNCE-HUKUNCENTA

Manufofin huɗubar

- Bayanin kan fifita ranar juma'a da shiryar da wannan alu'mma ta Annabi Muhammadu (ﷺ) zuwa gare ta.
- Bayanin hukuncin sallar juma'a da wasu daga ladubbanta.
- Laifin wanda ya ƙi zuwa sallar juma'a.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga shirrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammad bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammad (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Bayan haka:

Ya ku mutane ku ji tsoron Allah, kuma ku sani cewa, Allah yana halittar abin da ya so kuma ya zaɓa, kamar yadda ya ce,

﴿ وَرَبُّكَ يَخۡلُقُ مَا يَشَآءُ وَيَخۡتَارُۗ مَا كَانَ لَهُمُ ٱلۡخِيَرَةُ ﴾[القصص: ٦٨].

(Kuma Ubangijinka yana halittar abin da ya so kuma ya zaɓa. Su ba su kasance suna da zaɓi ba).

Kuma ku sani cewa, Allah Ta'ala yana da hikima isasshiya cikin abin da yake zaɓa, domin Allah yana zaɓar manzanni daga cikin mala'iku, da kuma mutane: Allah yana cewa,

﴿ ٱللَّهُ يَصۡطَفِي مِنَ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةِ رُسُلٗا وَمِنَ ٱلنَّاسِۚ ﴾[الحج: ٧٥].

(Allah yana zaɓar manzanni daga mala'iku da kuma mutane).

Kuma Allah Ta'ala ya zaɓi Makka a bisa ragowar gurare, sannan bayanta ya zaɓi Madina gidan hijirar cikamakin Annabawa. Sannan bayansu ya zaɓi Baitul

–Maƙdisi mazaunar mafiya yawa daga Annabawan da Allah ya ba mu labaransu.

Allah Ta’ala Ya fifita wasu watanni da darare a bisa wasu, domin adadin watanni a wajan Allah watanni goma sha biyu ne a ranar da Allah ya halicci sammai da ƙasa, daga cikinsu akwai guda huɗu waɗanda suke masu alfarma ne; su ne Zul-Ki’ida da Zul-Hijjah da Muharram da Rajab.

Kuma mafificin yini da rana ta fito a cikinsa shi ne, yinin ranar Juma’a don haka ku girmama abin da Allah ya girmama. Allah ya yi muku rahama.

An karɓo daga Aus ibn Aus (R.A.) Annabi (ﷺ) ya ce, "Wanda ya yi wanki, ya yi wanka, ya matsa kusa, ya yi sammako, ya kusanto (liman) ya saurari (huɗuba), zai sami ladan tsayuwar shekara ɗaya da azuminta da dukkan tako da ya yi)). Tirmizi da Nasa'i da suka rawaito shi .

Kuma an karɓo daga Anas ya ce, "An bijiro da sallar Juma'a ga Manzon Allah (ﷺ). Mala'ika Jibrilu ne ya zo masa da ita a tafinsa kamar farin amdubi, a tsakiyarsa akwai wani baƙin ɗigo, sai ya ce: "Menene wannan ya jibrilu?" Ya ce masa, "Wannan ita ce Juma'a Ubangijinka yake bijiro da ita a gare ka; domin ta kasance idi a gareka da alummarka a bayanka, kuma ku kuna da alheri a cikinta, wanda kai ne za ka zama na farkon samunsa, kuma yahuduwa da nasara su zama a bayanka. Kuma a cikinta akwai wata sa'a babu wani bawa da zai yi addu'a a cikinta ta alheri da yake rabonsa ne, face an ba shi, ko ya nemi tsari daga sharri face an ije masa mafi girma daga abin da ya nema, kuma mu a sama muna ambatonsa ranar ƙari...". Ɗabarani ne ya rawaito shi a cikin Al-Ausat da isnadi mai kyau .

Kuma an rawaito daga Abu Hurairata (R.A) ya ce: "Manzon Allah (ﷺ) ya ce: (Mafificin yinin da da rana ta fito a cikinsa shi ne yinin ranar Juma'a; a cikinsa aka halicci Annabi Adam, kuma a cikinsa a ka shigar da shi aljanna, kuma a cikinsa aka fitar da shi daga cikinta). Muslim da Abu Dawud da Nasa'i suka rawaito shi.

An karɓo daga Huzaifa Allah ya yarda da shi ya ce, Manzan Allah (ﷺ) ya ce: (Allah tabaraka wa Ta'ala Ya ɓatar da waɗanda suke gabanin mu ga barin Juma'a, sai Yahudawa suka sami Asabar, Nasara kuma suka sami Lahadi, don haka su bayan mu suke bi, har ya zuwa ranar sakamako. Mu ne na ƙarshe daga ahalin duniya, mu ne na farko a ranar Alƙiyama, waɗanda za a yi wa hukunci gabanin al'ummai), Muslim ne ya rawaito shi .

Yana daga mafi girman abubuwan da Juma'a ta keɓanta da su cewa, tana daga mafi girman salloli a matsayi, mafi ƙarfin farilla, mafi yawan lada. Haƙiƙa musulunci ya ba ta ƙarin kulawa, da isashiyar lura; don haka ya zaburar a kan yin wanka dominta, da tsabta da da yanke duk wani sansane mara daɗi, da fita zuwa gareta cikin mafi kyawun tufafi da mafi cikar kama, da sammako wajan fita zuwa gareta, da kusantowa zuwa ga liman, da tattaro zuciya, waje daya domin sauraren wa'azi da ambaton Allah, a cikin hadisin da Bukhari da Muslim suka rawaito shi daga Abu Hurairata Allah ya ƙara yarda a gare shi cewa, Manzan Allah ya ce: (Duk wanda ya yi wanka ranar Juma'a irin wankan janaba, sannan ya tafi a sa'a ta farko to kamar ya gabatar da rakuma ne (sadaka) har ƙarshan hadisin.

Kuma Hakim ya rawaito kuma ya inganta shi, daga Samrah ɗan Jundubi (R.A.) cewa, Annabin Allah ya ce: "Ku halarto sallar Juma'a, kuma matso kusa da liman, domin mutum ba zai gushe ba yana nesa, har sai Allah ya jinkirta shi a cikin aljanna ko da ya shige ta".

Idan ya halarta ya shagala da ibada da bin ubangiji na daga sallah da zikiri da karatun Alƙur'ani, har lima ya fito.

Yayin da liman ya fito sai ya kasa kunne ya saurari huɗuba, sannan ya yi sallar da tsoron Allah da nutsuwa, da tuntuntuni a kan abin da ake karantawa a cikinta na zancan Allah mai buwaya da ɗaukaka, yayin da ya idar da sallahr farillar sai ya shagla da zikiran da aka shar'anta bayan sallah.

Kuma an sunnanta nafila mai raka'a huɗu a cikin masallaci, ko kuma mai raka'o'i biyu a gidan sa, amma jinkirtata zuwa gida shi ya fi falala domin haka Annabi (ﷺ) ya yi. kamar yadda ya tabbata a cikin Bukhari da Muslimu.

Duk wanda ya kwaɗaita bisa aikata haka kuma ya aiwatar da shi da ikhlasi, to ya cancanci ya sami falalar wannan rana mai albarka, kuma ya sami ladansa mai girma daga mai ni'ima mai karamci, domin haƙiƙa Annabi (ﷺ) ya ce: “Wanda ya yi alwala kuma ya kyautata alwalar, sannan ya zo sallar Juma'a, sannan ya ji kuma ya saurara, za a gafarta masa abin da ke tsakaninsa, da wata Juma'ar (mai zuwa) har da ƙarin kwana uku.” Muslim ne ya rawaito shi a cikin Sahihinsa .

Ya ku bayin Allah! Haƙiƙa shari'a ta yi hani bisa wasu al'amura da suke hana ladan Juma'a, ko tawayar ladanta, kamar jinkiri wajan tafiya zuwa gareta, har sai liman ya fito, da shagaltar da masu sallah ta hanyar tsatsallaka su, domin Annabi (ﷺ) ya ga wani mutum – lokacin da yake huɗuba- yana tsattsallaka mutane sai ya ce masa yana masa inkari, "Ka zauna haƙiƙa ka cutar kuma ka wahalar". Kuma haƙiƙa ana jiye wa wanda ke aikata haka tsoron kada ya shiga dungumin fadin Allah, mabuwayi da ɗaukaka:

﴿ وَٱلَّذِينَ يُؤْذُونَ ٱلْمُؤْمِنِينَ وَٱلْمُؤْمِنَٰتِ بِغَيْرِ مَا ٱكْتَسَبُوا۟ فَقَدِ ٱحْتَمَلُوا۟ بُهْتَٰنًا وَإِثْمًا مُّبِينًا ﴿٥٨﴾ ﴾ [الأحزاب: ٥٨].

(Kuma waɗannan da suke cutar da muminai maza da muminai mata ba tare da wani abu da (su muminan) suka aikata ba, to haƙiƙa sun ɗauki nauyin ƙire da laifi mai girma).

Daga ciki: akwai uzurrawa bayin Allah ta hanyar ɗaga murya da zikiri ko karatun Alƙur’ani, haƙiƙa Manzon Allah (ﷺ) ya hana hakan, da faɗinsa ga sahabbai yayin da suka ɗaga muryarsu da ƙira'a: "Kada sashinku ya baiyana karatun Alƙur'ani a bisa sashi" .

Mafi muni daga haka, idan wannan uzurrawar ta zamo da zance ne a kan lamarin duniya kurum, musamman ma ana cikin huɗuba, domin yana daga cikin hanawa mutum (dacewa), da ƙarancin basira mutum ya shagala ga barin huɗuba da zance, ko wasa, ko waninsa, har ladan Juma'a da falalarta su kuɓuce masa. Haƙiƙa Annabi (ﷺ) ya faɗa wajan yin gargaɗi a kan haka: “Duk wanda ya shafi ƙasa a yayin huɗuba to ya yi wasa”. Muslim ne ya rawaito shi.

Kuma na rawaito daga Abu Hurairata (R.A.) cewa Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Idan ka ce da sahibinka: yi shiru, ranar Juma'a alhali liman yana huɗuba to ka yi yasasshiyar magagana”.

Kuma Imam Ahmad ya rawaito daga Ali ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Duk wanda ya ce ga sahibinsa yayin da liman yake huɗuba: yi shiru to haƙiƙa ya yi yasasshiyar magna. Duk kuwa wanda ya yi yasasshiyar magana, to ba shi da ladan Juma'a" .

Ya ku bayin Allah! Haƙiƙa Manzon Allah ya tsananta wajan gargaɗi game da ƙin halartar sallar Juma'a ba tare da wani uzuri na shari'a ba, yana mai bayyana cewa, wanda ya aikata haka haƙiƙa ya bijirar da kansa ga kamuwa da cutar gafala ta barin Allah, da yin rufi a kan zuciyar sa, duk kuwa wand Allah ya yi rufi a kan zuciyarsa to basirarsa za ta makance, kuma makomarsa ta munana, Muslim ya rawaito cewa, Manzon Allah ya ce:

“Lallai mutane su dai ƙin halartar sallar Juma'a, ko kuwa lalle Ubangiji zai rufe zukatansu, sannan su kasance daga gafalallu”.

Kuma imam Ahmad ya rawaito da Isnadi kyakkyawa, da kuma Hakim, a cikin Sahihinsa daga Abi Katadata (R.A) cewa, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Wanda ya bar Juma’a sau uku ba tare da wata lalura ba, Allah zai yi ɗab'i a kan zuciyarsa”.

To ku ji tsoron Allah, ya ku bayin Allah, kuma ku san irin falala da rahamar da Allah ya yi a kanku, ku tsaya a kan umarninsa ku bar abubuwan da ya hana, ko kwa rabauta da aljannatansa, a ranar gamuwa da shi.

Ina faɗar abin da kuka ji, kuma ina neman gafarar Allah Mai Girma da ɗaukaka, ga kaina da dukkan musulmi, daga kowane irin zunubi. Ku nemi gafararsa, lallai shi mai yawan gafara ne, mai yawan jinƙai.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah, ya umarce mu da lazimtar jam’i da juma’a, kuma ina shaidawa babu abin bautawa da gasikiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammadu bawansa ne, kuma manzonsa ne, Allah ya yi tsira da aminci a gare shi mai tarin yawa. Bayan haka:

Haƙiƙa abin da muka yi cikin lokacin nan da ya shuɗe na daga ladubba da falaloli da abubuwan da juma’a ta keɓanta da su, kamar gulbi ne in an kwatantashi da kogi, kuma kaɗanne daga cikin abu mai yawa.

Yaku bayin Allah! Haƙiƙa Ma’aikin Allah (ﷺ) ya kasance yana cin moriyar ranar Juma’a ta hanyar aikata ayyuka na ƙwarai, ya kasance daga aikina shiriyarsa (ﷺ), girmama wannan rana da darajta ta, da keɓantarta da wasu abubuwa na musamman, kamar karanta Surar (Alif lam mim Assajdat) da (Hal ata alal insani) a sallar Alfijir ɗinsa, saboda sun ƙunshi abin da ya kasance da abin da zai kasance a yininta.

Kuma yan daga cikin abubuwan da ta keɓanta da su: an so yawaita salati ga Annabi (ﷺ) a daranta.

Imam Ibn Alƙaiyim Allah ya jiƙansa yana cewa: "Manzo Allah shi ne shugaban halitta, kuma yinin Juma'a shi ne shugaban ranaku, don haka yin salati a gare shi a wannan rana yana da falala wadda babu irinta. Tare da wata hikimar wadda ita ce: Kasancewar duk wani alheri da al'ummarsa ta samu a duniya da lahira ta same shi ne ta hannunsa. Sai Allah ya tarawa al'ummarsa tsakanin alherin duniya da lahira, don haka mafi girman girmamawa za su samu za su same ta ne ranar Juma'a. Domin a ran nan ne za a tashe su zuwa gidaddajinsu da fadojinsu a cikin Aljanna. Kuma ranar Idi ce a gare su a duniya. Yinin da a cikinsa Allah Ta'ala yake taimakonsu da amsa addu'o'insu da buƙatunsu. Kuma ba ya mai da hannun mai roƙo fayau a cikinsu . Duk wannan kuwa sun san shi ne, kuma ya same su ne saboda shi, kuma ta hanyarsa. Don haka yana daga cikin biyan kaɗan daga cikin haƙƙinsa, mu yawaita salati a gare shi a wannan yini da darensa". Kuma ga shi Allah Ta'ala ya ce,

﴿ إِنَّ ٱللَّهَ وَمَلَٰٓئِكَتَهُۥ يُصَلُّونَ عَلَى ٱلنَّبِيِّۚ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ صَلُّواْ عَلَيۡهِ وَسَلِّمُواْ تَسۡلِيمًا ٥٦ ﴾

[الأحزاب: ٥٦].

"Haƙiƙa Allah da mala'ikunsa suna salati ga Annabi, ya ku waɗanda suka yi imani ku yi salati da sallama mai yawa a gare shi."

Daga cikin akwai karanta sororin (juma'a) da (almunafiƙun) ko (Sabbih) da (Algashiyah) daga ciki; akwai cewa mai tafiya zuwa gareta yana da ladan aiki na shekara, duk taku ɗaya da yayi, duka da a zminta, da tsayuwara daranta.

Daga ciki akwai cewa yana kankare zunubai.

Ya ku bayin Allah! Haƙiƙa yana daga ababuwan da shari'a ta keɓanci wannan yini dashi cewa, a cikinta akwai wata sa'a da babu wani bawa musulmi da zai yi dace da ita, yana roƙon Allah daga alherin duniya da lahira, face Allah ya amsa masa addu'arsa.

Domin an ruwaito daga Abu Huraira (R.A) ya ce: Manzo Allah ya ce "Haƙiƙa a cikin Juma'a akwai wata sa'a babu wani musulmi da zai yi dace da ita yana tsaye yana yin sallah, yana roƙon Allah wani alheri, face sai ya ba shi". Ya yi haka da hannunsa yana alamta ƙarancinta (ma'ana ita sa'ar). Muslim ne ya rawaito shi.

Lallai wannan ta isa kyauta mai girma, kuma dama babba, baiwa gwaggwaɓa, wadda Allah yake buɗa ƙofofinsa ga bayinsa, don su roƙe shi da ita. Hasararre shi ne wanda aka hana shi fallalr wannan yini da albarkar wannan sa'ar mai ɗinbin albarka, wadda take maimaituwa a gare mu a kowane sati. Kuma mafi rinjayen maganganu wajen tantance lokacinta shi ne, daga tsakanin La'asar zuwa faɗuwar rana. Domin an karɓo daga Jabir (R.A) ya ce, Manzon Allah ya ce: "Ranar juma'a sha biyu ce": yana nufin sa'o'i, babu wani musulmi da za a samu yana roƙon Allah mai girma da ɗaukaka wani abu face Allah ya ba shi, don haka ku neme ta a ƙarshen lokaci bayan La'asar".

Ya ku musulmi! Ku yi gasa a kan wannan alheri mai girma, wanda Allah ya sanya shi cikin ranar Juma’a ga wanda ya sunnanta da sunnan Annabi a cikin wannan, ku tsaftacce jukkunanku, ku sanya mafi kyawun tufafin ku, ku yi asuwaki, ku sanya turare, ku yi sammako don ku tafi sallar Juma’a, ku lazimci ladubban Annabi (ﷺ), da tsari na Muhammadiyya. Ku kasance daga masu rigaye zuwa alherai, masu rabauta da mafiya ɗaukakar darajoji, (Wannan falala ce ta Allah da yake ba da ita ga wanda yaso, kuma Allah shi ne ma’abocin falala mai girma). Na ja kunnenku a kan ƙin halartar wannan alheri, da sakaci da waɗannana sunnoni, domin ya zo a cikin sahihin hadisi: "Wasu mutane ba su gushe ba suna jinkirta ta har sai Allah Ya jinkirta su”.

Ina neman tsari da Allah daga shaɗani abin la'annane.

GASKIYA DOKIN KARFE

Manufofin hudubar

- Koyar da gaskiya a mu'amalar jama'a.
- Tsawatarwa daga yin ƙarya.
- Samar da aminciwa tsakanin mutane.

Hudubа Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammadu bawansa ne manzonsa ne. (Yaku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron Allah yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Yaku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammadu (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (a addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta".

Bayan haka,

Ya bayin Allah! Ina yi mana wasiyya da jin tsoron Allah, ni da ku gaba ɗaya. Sannan ku sani asalin tsiyacewar wannan al'umma shi ne rashin yin gaskiya a dukkan al'amura. Tare da cewa gaskiya ita ce tushen dukkan alheri, bisa ga misali gaskiya ita ce ke haifar da tataccen imani na ƙwarai, wanda mai shi yake dogaro da Allah, ya mai da al'amuransa gare shi. Gaskiya ita ke sa bawa ya zama mai haƙuri a kan jarraba, mai godiya yayin samun ni'ima, mai gaggawar aikata alheri, mai ƙauna don Allah, mai ƙiyayya don Allah. Kai babu wata halayyar imani da za ta tabbata face sai da tabbatar gaskiya. Shi ya sa Allah ya umarci bayinsa muminai da jin tsoronsa, da kuma shiga cikin masu gaskiya sai ya ce:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَكُونُواْ مَعَ ٱلصَّٰدِقِينَ ﴿١١٩﴾ ﴾ [التوبة: ١١٩].

(Ya ku waɗanda suka ba da gaskiya, ku ji tsoron Allah, kuma ku zama tare da masu gaskiya).

Abin nufi masu gaskiya a imaninsu, da maganganunsu, da ayyukansu, da alƙawuransa.

Gaskiya na kawo albarka da ƙauna, da aminci cikin al'umma. An karɓo hadisi daga Hakeem bn Hizam ya ce: "Haƙiƙa Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Mai saye da mai sayarwa suna da zaɓin (yiwuwar ciniki ko fasawa) matuƙar dai ba su rabu da juna ba (a yayin ciniki). Idan suka yi gaskiya, kuma suka bayyana komai, sai a sanya musu albarka a cikin cinikinsu. Idan kuma suka yi ƙarya suka rufe gaskiya a cinikin nasu, sai a tafiyar da albarkar cinikin nasu". Bukhari da Muslim suka ruwaito shi.

Tabbatattun abubuwa kaɗai ne ya zama dole su bayyana a cikin tabbatar da mabambantan abubuwan da muke gudanarwa a tsakaninmu, kuma samun yardar Allah ta rataya da haka ne a kodayaushe.

Ambaton gaskiya a cikin Alƙur'ani ya zo a ayoyi masu yawa. Wasu na ambata kwaɗaitarwa a kan gaskiya, wasu kuma nuna zamantowar gaskiya ɗan itaciyar tsoron Allah da yin abu dominsa. Daga cikin ayoyin, ba da jimawa ba aka ambaci ɗaya ba. Sai kuma faɗin Allah maɗaukakin sarki:

﴿ لِّيَجۡزِيَ ٱللَّهُ ٱلصَّٰدِقِينَ بِصِدۡقِهِمۡ ﴾ [الأحزاب: ٢٤].

(Domin Allah ya saka wa masu gaskiya da gaskiyarsu).

Kuma Allah ya ce:

﴿ قَالَ ٱللَّهُ هَٰذَا يَوۡمُ يَنفَعُ ٱلصَّٰدِقِينَ صِدۡقُهُمۡۚ لَهُمۡ جَنَّٰتٞ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدٗاۖ رَّضِيَ ٱللَّهُ عَنۡهُمۡ وَرَضُواْ عَنۡهُۚ ذَٰلِكَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡعَظِيمُ ١١٩ ﴾ [المائدة: ١١٩].

(Allah ya ce, «Wannan ita ce ranar da masu gaskiya, gaskiyarsu za ta amfane su, suna kuma da aljannatai waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, suna madawwama a cikinsu har abada, Allah ya yarda da su, kuma sun yarda da Allah. Wannan shi ne babban rabo).

Don haka gaskiya ce take tseratar da bawa daga azabar Allah a ranar alƙiyama.

Kuma Allah mai girma da buwaya ya ce:

﴿ وَبَشِّرِ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَنَّ لَهُمۡ قَدَمَ صِدۡقٍ عِندَ رَبِّهِمۡۗ ﴾ [يونس: ٢].

(Kuma ka yi wa waɗanda suka imani albishir cewa suna da babban matsayi a wurin Ubangijinsu).

Wato bin gaskiyarsu da gaske shi ya jawo musu samun wannan babban matsayi.

Kuma Allah ya ce,

﴿ وَٱلَّذِي جَآءَ بِٱلصِّدۡقِ وَصَدَّقَ بِهِۦٓ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُتَّقُونَ ٣٣ ﴾ [الزمر: ٣٣].

"Wanda kuwa ya zo da gaskiya kuma ya gaskata ta, waɗannan su ne masu tsoron Allah".

Allah ma kansa ya siffata Kansa da gaskiya, Ya ce:

﴿ قُلۡ صَدَقَ ٱللَّهُ ﴾[آل عمران: ٩٥].

(Ka ce Allah ya yi gaskiya).

Kuma Allah ya ce:

﴿ فَلَوۡ صَدَقُواْ ٱللَّهَ لَكَانَ خَيۡرٗا لَّهُمۡ ٢١ ﴾ [محمد: ٢١].

(To da sun yi wa Allah gaskiya, lallai da hakan ya zama alheri a gare su(.

Kuma Allah ya ce,

﴿ وَجَعَلۡنَا لَهُمۡ لِسَانَ صِدۡقٍ عَلِيّٗا ٥٠ ﴾ [مريم: ٥٠].

(Kuma muka sanya musu ambato na gaskiya, maɗaukaki).

Allah maɗaukaki ya ce:

﴿ إِنَّ ٱلۡمُتَّقِينَ فِي جَنَّٰتٖ وَنَهَرٖ ٥٤ فِي مَقۡعَدِ صِدۡقٍ عِندَ مَلِيكٖ مُّقۡتَدِرِۢ ٥٥ ﴾ [القمر: ٥٤ – ٥٥].

(Haƙiƙa masu tsoron Allah suna cikin aljannatai da ƙoramu a cikin mazaunin gaskiya).

Da kuma faɗin Allah maɗaukakin Sarki:

﴿ وَقُل رَّبِّ أَدۡخِلۡنِي مُدۡخَلَ صِدۡقٖ وَأَخۡرِجۡنِي مُخۡرَجَ صِدۡقٖ ﴾ [الإسراء: ٨٠].

(Kuma ka ce: “Ubangiji ka shigar da ni mashiga ta gaskiya, kuma ka fitar da ni mafita ta gaskiya).

Abin nufi a wannan aya shi ne, ka sanya dukkan wani wurin shiga ta, da fita ta, ya zama cikin biyayya gare ka ne, da neman yardaarka.

Ya bayin Allah! Gaskiya nau’o’i ce da yawa. Akwai gaskiya a magana, da gaskiya a aiki da kuma gaskiya a hali.

Allah maɗaukakin sarki ya ce:

﴿ إِنَّمَا ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ ثُمَّ لَمۡ يَرۡتَابُواْ وَجَٰهَدُواْ بِأَمۡوَٰلِهِمۡ وَأَنفُسِهِمۡ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِۚ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلصَّٰدِقُونَ ١٥ ﴾ [الحجرات: ١٥].

(Haƙiƙa ba wasu ba ne muminai sai waɗanda suka ba da gaskiya da Allah da Manzonsa, sannan ba su yi kokwanto ba, suka kuma yi yaƙi da dukiyoyinsu da rayukansu a cikin hanyar Allah, waɗannan su ne masu gaskiya).

Sannan kuma mafi ɗaukakar matakin gaskiya shi ne matakin Siddiƙanci wato cikar jawuwa ga manzon, tare da cikar tace aiki ga wanda ya aiko Manzon wato Allah.

Ya ku bayin Allah! Ku yi gaskiya, domin haƙiƙa gaskiya tsira ce daga kowane abin ƙi, kuma hanyar isa ce ga ayyukan kirki, ayyukan kirki kuma na shiryarwa zuwa ga aljanna.

Ya ‘yan’uwa masu sauraro ina neman gafarar Allah gare ni da ku daga kowane irin zunubi, kuma ku nemi gafararsa haƙiƙa shi Allah mai yawan gafara ne, mai yawan jinƙai ne.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, kuma kyakkyawan ƙarshe yana ga masu tsoron Allah. Kuma babu uƙuba sai ga azzalumai. Tsira da aminci su tabbata a kan mafi ɗaukakar manzanni, Annabinmu Muhammad, da iyalansa da sahabbansa, da duk wanda ya bi shiriyarsa, kuma ya yi kira irin kiransa har zuwa ranar sakamako.

Bayan haka: Ya ‘yan’uwa musulmai, tabbas musulunci ya kere dukkanin wasu dokoki, kuma ya murƙushe ƙarya da maƙaryata. Karya tambarin ha’inci ce, kai uwa uba ma, ƙarya alama ce daga alamomin munafunci. Manzon Allah ya ce:

“ Alamomin munafuƙi guda uku ne, idan ya yi magana ya yi ƙarya, idan ya yi alƙawari ya saɓa, idan aka amince masa ya yi ha’inci”.

Sannan kuma sam-sam musulunci da ƙarya ba sa haɗuwa, don haka matuƙar dai da imani mai ƙarfi, da kuma tsoron watsi da daraja, da fatali da addini, ba za ka ga musulmi ya ɗabi’antu da ƙarya da yaudara ba.

Ya ku bayin Allah! Duk wanda ya kalli halin da mutane suke rayuwa a cikinsa a yau, zai ga gazawarsu a fili ta ɓangaren gaskiya. Ina ganin ba komai ya jawo haka ba sai raunin imani a zukata da kuma tsananin son duniya. Tabbas Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Gaskiya nutsuwa ce, ƙarya kuwa fargaba ce”. Ahmad da Tirmizi ne suka rawaito shi.

Yana daga cikin ƙarairayi mabayyana: Na farko shi ne ƙaryar iyaye ga ‘ya’yansu, tare da cewa addininmu ya nuna cewa dole ne a guji yin ƙarya a cikin tarbiyyar ‘ya’ya, domin su tashi a cikin gaskiya kuma su saba da ita. Wanda hakan kuma zai sa su ƙarfin hali a wajen faɗar gaskiya da kuma aiki da ita. Sahabin Annabi, Abdullahi Ɗan Amir, ya ce: Wata rana babata ta kira ni, a lokacin ina ƙarami a lokacin Manzon Allah (ﷺ) yana zaune, sai ta ce da ni, "Zo ungo". Sai manzon Allah ya tambaye ta ya ce, "Me za ki ba shi?" Sai ta ce, "Dabino zan ba shi". Sai ya ce da ita, "Da ba ki ba shi komai ba, da an rubuta miki ƙarya”.

Kuma sahabin Annabi, Abu Huraira ya ce: “Haƙiƙa manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Duk wanda ya kira yaro ya ce da shi, zo ungo, sannan sai bai ba shi komai ba, to ya yi ƙarya”.

Ya ke ‘yar’uwa, da irin wannan shiryarwar ta manzon Allah ne ya dace a tarbiyyanci ‘ya’ya domin su sami rainon musulunci tsantsa.

Abu na biyu, shi ne yaɗuwar ƙarya a tsakanin mutane a zantukansu da kuma ayyukansu, ga shi kuma haka na daga cikin manya-manyan zunubai. Allah maɗaukakin sarki Yana cewa:

﴿ فَنَجۡعَل لَّعۡنَتَ ٱللَّهِ عَلَى ٱلۡكَٰذِبِينَ ٦١ ﴾ [آل عمران: ٦١].

(Sannan kuma mu sanya tsinuwar Allah a kan maƙaryata).

Kuma a cikin Sahihul Bukhari da Muslim, an karɓo daga Anas ɗan Malik ya ce: “Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Abubuwa uku duk wanda yake yin su ya zama munafuƙi, idan ya yi zance sai ya yi ƙarya, idan ya yi alƙawari sai ya saɓa, idan kuma aka amince masa ya yi ha’inci".

Abu na uku, yaɗuwar karya alƙawari, ba tare da wani uzuri karɓaɓɓe ba. Kamar misali, ku yi alƙawari da wani ƙarfe takwas, sai ya zo ƙarfe tara ya gabatar maka da uzurin ya biya ne ta wani wuri ya yi saye-saye. Wani babban abin baƙin cikin ka ga waɗanda suke da kama ta kamala da alheri, amma sai ka ga saɓa alƙawari ya zama ba komai ba a wurinsu.

Sannan kuma saɓawa ‘ya’ya alƙawarin sayo musu ko ba su wani abu ma na daga cikin saɓa alƙawari. Abdullahi ɗan Mas’ud ya ce, "Karya ba ta dace ba ko da wasa ko ba da wasa ba. Ko da kuwa wani ya yi wa ɗansa alƙawarin wani abu ne, sannan kuma ya ƙi cika masa.

Abu na gaba shi ne, cin amana da ha'inci. Ma'aikaci ba ya zuwa wajen aikinsa da wuri, kuma in ya je ba ya yin aikinsa yadda ya dace, shi ne karatun jarida, ko kallon talabijin, ko yin waya da amsa ta, kai sai ya rasa wai shin da wane haƙƙi yake karɓar albashin nasa?

Abu na biyar shi ne algus da ɓoye kaya, wato abin sayarwa.

Na shida kuwa shi ne, ƙaryar talauci da kiran babu don son tara abin duniya. An karɓo daga Abu huraira Allah ya yarda da shi ya ce: "manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Wanda yake roƙon mutane don tara abin duniya yana roƙarwa kansa garwashin wuta ne, ko dai ya ƙaranta ko kuma ya yawaita, (shi ya so).

Rufewa juna, a yayin aure, tsakanin mai neman da wacce yake neman aurenta. Kowanne a cikinsu yana ƙoƙarin rufe aibunsa, na halitta ko na halayya. Ya kuma kambama kansa ta ɓangaren yabo wanda hakan na tafiyar da albarkar aure ya lalatar da ita.

Ya bayin Allah! 'yan'uwanmu 'yan kasuwa Allah ya shirye su, su suka fi kowa afkawa a wannan sabo su yi ƙarya game da kuɗin abin sayarwa, su yi a kan samfirin abin sayarwa, wani lokacin ma su haɗa duka. Mafi munin haka kuwa ƙarawa da rantsuwa a kan ƙaryar da suka yi. Allah ka kiyaseh mu wannan ganganci.

Manzon Allah (ﷺ) ya ƙirga wannan saɓo a cikin manya-manyan saɓon da suke halaka masu yin su. An karɓo daga Abdullahi ɗan Amr, daga Annabi, (ﷺ) ya ce: "Manya-manyan laifuka su ne; yin tarayya da Allah, da wulaƙanta iyaye, da kisan kai, da kuma rantsuwar da ke cusa mai yinta cikin wuta, wato rantsuwa a kan ƙarya". Bukhari ne ya rawaito shi.

Ya bayin Allah! Ta yaya kuwa Allah zai sa albarka a kasuwancin maƙaryaci? Don haka mu ji tsoron Allah mu kiyaye shi a kowane hali.

Ya bayin Allah! Bin dokokin Allah dole ne, saboda haka ya zama lallai ku yi riƙo da gaskiya a kowace irin sana'a. Kuma mu dimanci yin gaskiya ga duk abokan hulɗarmu, in mun tabbata a kan haka za mu ga buɗi da yalwar arziƙi a kai a kai. Allah ya ce:

﴿ وَلَوۡ أَنَّ أَهۡلَ ٱلۡقُرَىٰٓ ءَامَنُواْ وَٱتَّقَوۡاْ لَفَتَحۡنَا عَلَيۡهِم بَرَكَٰتٖ مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلۡأَرۡضِ ﴾ [الأعراف: ٩٦].

(Da dai mutanen alƙaryu sun yi imani, sun kuma ji tsoron Allah, to da mun buɗe musu albarkatai daga sama da kuma ƙasa).

Kuma Allah ya ce:

﴿ وَمَن يَتَّقِ ٱللَّهَ يَجۡعَل لَّهُۥ مَخۡرَجٗا ۝٢ وَيَرۡزُقۡهُ مِنۡ حَيۡثُ لَا يَحۡتَسِبُۚ ﴾ [الطلاق: ٢ – ٣].

(Duk wanda ya ji tsoron Allah, zai sanya masa mafita (daga ƙunci), kuma ya azurta shi ta inda ba ya tsammani).

Kuma ƙaya a shaida ɗaya ce daga cikin ƙarairayin da suka wajaba a gujewa. Allah Yana cewa:

﴿ وَٱجۡتَنِبُواْ قَوۡلَ ٱلزُّورِ ۝٣٠ ﴾ [الحج: ٣٠].

(Kuma ku nisanci faɗar shaidar zur).

Allah Ya ƙara faɗa a wata ayar:

﴿ وَلَا تَكۡتُمُواْ ٱلشَّهَٰدَةَۚ وَمَن يَكۡتُمۡهَا فَإِنَّهُۥٓ ءَاثِمٞ قَلۡبُهُۥۗ وَٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ عَلِيمٞ ۝٢٨٣ ﴾ [البقرة: ٢٨٣].

(Kada ku ɓoye shaida, duk kuwa wanda ya ɓoye ta, to haƙiƙa shi mai kangararriyar zuciya ne, kuma Allah masanin abin da kuke aikatawa ne).

Ya bayin Allah! Gaskiya na da matuƙar amfani, a duniya da lahira, daga cikin amfaninta sun haɗar da:

Na farko shigar da mai yinta gidan aljanna. An tambayin Annabi, (ﷺ), menene aikin 'yan aljanna? Sai ya ce, "Gaskiya". Iman Ahmad ne ya rawaito shi.

Na biyu kuɓutar da mai yin ta daga halaka. Ya zo a cikin hadisin mutanen nan da dutse ya toshe musu ƙofar kogon da suka shiga cewa ɗayansu, ya ce da su, "Babu abin da zai tseratar da ku sai gaskiya, kowannenku ya roƙi Allah da abin da ya san ya yi gaskiya a cikinsa. Bukhari ne ya rawaito shi.

Na uku, nagartar zuciya, duk wanda ya yi gaskiya a ayyukansa na fili to tabbas kuwa zuciyarsa na cike da gaskiyar nufi, domin kuwa komai bawa zai yi, to sai nufi ya rigaye shi.

Na huɗu, gadarwa da mai yinta nutsuwa da kwanciyar rai.

Na biyar, kuɓutar da mai yinta daga afkawa cikin fitintinun rayuwa.

Na shida, takan zama ga mai yinta, tushen aikata ayyukan alheri.

Na bakwai, korewa mai yinta siffantuwa da munafurci.

Na takwas, datar da mai yin a wajen hasashe da hangen nesa.

Na tara, ƙarfafar hujjar mai riƙo da ita da kuma yinta.

Na goma, samun yabo da kirari da kyakkyawan ambato daga mutane.

Na sha ɗaya, jawo albarkar kasuwanci da san'o'i.

Allah ka sa mu a cikin bayinka masu gaskiya, kuma ka tsare mu daga yin ƙarya da biyewa masu yinta amin.

Girmamawar Da Musulunci Ya Yi Wa ‘Ya Mace

Manufofin hudubar

- Bayanin halin da mace take ciki kafin zuwan musulunci.
- Bayanin yadda musulunci ya ɗaukaka darajar ‘ya mace.
- Bayanin cewa musulunci ya daidaita mace da namiji a wasu ɓangarori.
- Fito da wuraren da musulunci ya girmama ‘ya mace a cikinsu.
- Ba da amsa ga masu cewa Musulunci ya tauye wa mata haƙƙi.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga shirrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammad bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammad (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Bayan haka : ‘Yan uwa musulmi : Huɗubarmu a yau tana magana ne a kan wani maudu’i da ya shagaltar da duniya gaba ɗaya, kuma a dalilinsa aka jingina wa musulunci da musulmai ci baya da ƙauyanci, , aka tuhunci musulunci da ƙare – ƙaraki da yawa, masu sharri da ɓarna suka ɗauki wannan maudu'i ƙofa ce ta ɓatar da mutane da yaudararsu da kange su daga hanyar Allah, wannan maudu’i shi ne bayanin matsayin ‘ya mace a addinin musulunci.

Babu yadda zamu san irin girmamawa da musulunci ya yi wa ‘ya mace sai mun koma baya, mun san matsayinta a lokacin jahiliyya kafin zuwan musuluncin.

Haƙiƙa ‘ya mace a lokacin Jahiliyya ta zama kamar wani kaya na sayar wa da bai da ƙima da daraja, har ya kai idan an haifa wa mutum ‘ya mace yana baƙin ciki, yana ƙin ta, ba ma ya son ya haɗa ido da mutane saboda kunya da damuwa, daga nan sai ya shiga tunanin ɗayan abubuwa biyu : kodai ya riƙe ta a wulaƙance,

ya yi haƙuri da duk irin wulaƙancin da mutane za su yi masa, ko kuma ya yi mata mummunan kisa, ya binneta da ranta, kamar yadda Allah ya bada labari inda yake cewa :

﴿ وَإِذَا بُشِّرَ أَحَدُهُم بِٱلۡأُنثَىٰ ظَلَّ وَجۡهُهُۥ مُسۡوَدّٗا وَهُوَ كَظِيمٞ ٥٨ يَتَوَٰرَىٰ مِنَ ٱلۡقَوۡمِ مِن سُوٓءِ مَا بُشِّرَ بِهِۦٓۚ أَيُمۡسِكُهُۥ عَلَىٰ هُونٍ أَمۡ يَدُسُّهُۥ فِي ٱلتُّرَابِۗ أَلَا سَآءَ مَا يَحۡكُمُونَ ٥٩ ﴾ [النحل: ٥٨ - ٥٩].

Ma’ana : “Idan an yi wa ɗayansu bushara da ‘ya mace, sai fuskarsa ta yi baƙiƙ ƙirin yana mai fushi, yana ɓoye wa mutane saboda munin abin da aka yi masa bushara da shi, (ya riƙa tunani cewa) zai riƙe ta ne a wulaƙance ko kuwa ya turɓuɗeta ne a cikin ƙasa, ku saurara abin da suke hukunta wa ya yi muni”. (Annahal : 58 – 59).

Don haka Allah ya bada labarin cewa zai bi wa wannan da aka zalunta haƙƙinta daga wanda ya zalunce ta bada wani haƙƙi ba, Allah ya ce,

﴿ وَإِذَا ٱلۡمَوۡءُۥدَةُ سُئِلَتۡ ٨ بِأَيِّ ذَنۢبٖ قُتِلَتۡ ٩ ﴾ [التكوير:٨-٩]

Ma’ana : “Idan aka tambayi wadda aka binne da ranta. Da wane laifi ne aka kashe ta” (At – Takwir : 8 – 9).

Idan kuwa ba su kashe ta ba, sai su wulaƙantar da ita idan ta girma, ba sa bata gado, suna sanya ta cikin kayan da ake gada, Imamul Bukhari – Allah ya yi masa rahama – ya rawaito daga Abdullahi ɗan Abbas – Allah ya yarda da shi – ya ce, “Sun kasance idan mutum ya mutu, waliyyansa suke da haƙƙi a kan matarsa, idan sun ga dama wasu cikinsu su aure ta, ko su aurar da ita, idan kuma sun ga dama ba za su aurar da ita ba, suna ganin su suka fi cancanta da riƙe ta fiye da danginta”, sai aya ta sauka da cewa :

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا يَحِلُّ لَكُمۡ أَن تَرِثُواْ ٱلنِّسَآءَ كَرۡهٗاۖ ﴾[النساء:١٩].

Ma’ana : “Ya ku waɗanda kuka yi imani ba ya halatta ku gaji mata a kan dole”.

Hakanan a lokacin jahiliyya mutum yana iya auren mata da yawa ba adadi, ya munana musu mu’amala. Da musulunci ya zo zai ya haramta haɗa mata fiye da huɗu a lokaci guda, ya kuma sanya sharaɗin haɗawar shi ne idan zai yi adalci tsakaninsu, Allah ya ce,

﴿ فَٱنكِحُواْ مَا طَابَ لَكُم مِّنَ ٱلنِّسَآءِ مَثۡنَىٰ وَثُلَٰثَ وَرُبَٰعَۖ فَإِنۡ خِفۡتُمۡ أَلَّا تَعۡدِلُواْ فَوَٰحِدَةً أَوۡ مَا مَلَكَتۡ أَيۡمَٰنُكُمۡۚ ﴾

[النساء: ٣].

Ma’ana : “Ku auri abin da ya yi muku daɗi na mata, bibiyu, ko uku – uku ko hurhuɗu, idan kuna jin tsoron ba za ku yi adalci ba to ku auri ɗaya, ko (ku wadatu) da abin da damarku ta mallaka”. (Annisa’i : 3).

Idan kuwa mutum ya mutu to shekara guda matarsa zata yi, tana masa takaba, babu fita. Hakanan namiji yana iya sakin matarsa ba tare da wani adadi ba, in ya sake ta, sai ya ƙyale ta sai ta kusa gama idda sai ya dawo da ita, sai kuma ya ƙara sakinta, sai ta kusa gama idda sai ya sake dawo da ita, haka zai ta yi. Har sai da Allah ya ƙayyade adadin saki biyu da mutum zai iya mayar da matansa a cikinsu.

Wannan shi ne irin yanayin da ‘ya mace take rayuwa a cikinsa a jahiliyya kafin zuwan musulunci, kuma haka halinta yake a wurin sauran al’ummu, har musulunci ya zo mace tana cikin irin wannan yanayi da hali, musulunci ya kuɓutar da ita, ya karramata, ya kiyaye mata haƙƙoƙinta, ya daidaita ta da ɗa namiji a wurare da yawa a cikin wajibai na addini, da barin haramun, da wajen bada lada da azaba, Allah ya ce, :

﴿ مَنْ عَمِلَ صَٰلِحًا مِّن ذَكَرٍ أَوْ أُنثَىٰ وَهُوَ مُؤْمِنٌ فَلَنُحْيِيَنَّهُۥ حَيَوٰةً طَيِّبَةً ۖ وَلَنَجْزِيَنَّهُمْ أَجْرَهُم بِأَحْسَنِ مَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿٩٧﴾ ﴾ [النحل: ٩٧].

Ma’ana “Wanda ya yi aiki na ƙwarai daga namiji ko mace yana mumini to zamu raya shi rayuwa mai daɗi, kuma zamu saka musu da mafi kyau abin da suke aikatawa” (Annahal : 97).

Allah ya sake faɗa a wani wurin ya ce, :

﴿ إِنَّ ٱلْمُسْلِمِينَ وَٱلْمُسْلِمَٰتِ وَٱلْمُؤْمِنِينَ وَٱلْمُؤْمِنَٰتِ وَٱلْقَٰنِتِينَ وَٱلْقَٰنِتَٰتِ وَٱلصَّٰدِقِينَ وَٱلصَّٰدِقَٰتِ وَٱلصَّٰبِرِينَ وَٱلصَّٰبِرَٰتِ وَٱلْخَٰشِعِينَ وَٱلْخَٰشِعَٰتِ وَٱلْمُتَصَدِّقِينَ وَٱلْمُتَصَدِّقَٰتِ وَٱلصَّآئِمِينَ وَٱلصَّٰٓئِمَٰتِ وَٱلْحَٰفِظِينَ فُرُوجَهُمْ وَٱلْحَٰفِظَٰتِ وَٱلذَّٰكِرِينَ ٱللَّهَ كَثِيرًا وَٱلذَّٰكِرَٰتِ أَعَدَّ ٱللَّهُ لَهُم مَّغْفِرَةً وَأَجْرًا عَظِيمًا ﴿٣٥﴾ ﴾ [الأحزاب: ٣٥].

Ma’ana : “Haƙiƙa musulmai maza da musulmai mata, muminai maza da muminai mata, masu ƙasƙantar da kai maza da masu ƙasƙantar da kai mata, masu gaskiya maza da masu gaskiya mata, masu haƙuri maza da masu haƙuri mata, masu tsoron Allah maza da masu tsoron Allah mata, masu sadaka maza da masu sadaka mata, masu azumi maza da masu azumi mata, masu kiyaye farjinsu maza da masu kiyaye farjinsu mata, masu ambaton Allah da yawa maza da masu ambaton Allah da yawa mata, Allah ya tanadar musu gafara da lada mai girma”. (Ahzab : 35).

Allah Maɗaukakin Sarki ya fifita namiji ne akan mace a wasu wurare, saboda wasu dalilai da hikimomi da suka sanya hakan, kamar a wajen gado, da shaida da diyya da zaman gida da wajen saki, saboda ɗa namiji yana da tsarin halittar da ‘ya mace ba ta da shi, yana ɗaukar nauyin a rayuwa wanda mace ba ta ɗaukan wannnan nauyin, kamar yadda Allah ya ce, :

﴿ ٱلرِّجَالُ قَوَّٰمُونَ عَلَى ٱلنِّسَآءِ بِمَا فَضَّلَ ٱللَّهُ بَعْضَهُمْ عَلَىٰ بَعْضٍ وَبِمَآ أَنفَقُوا۟ مِنْ أَمْوَٰلِهِمْ ۚ ﴾ [النساء: ٣٤]

Ma’ana : «Maza sune a tsaye akan mata saboda abin da Allah ya fifita sashensu akan sashe da kuma abin da suka ciyar daga dukiyoyinsu» (Annisa’i 34). Ya sake cewa :

﴿ وَلِلرِّجَالِ عَلَيْهِنَّ دَرَجَةٌ ۗ ﴾ [البقرة: ٢٢٨].

Ma’ana : «Maza suna da daraja akan mata» (Baƙara : 228). Haka ma Allah ya sanya wa ‘ya mace rabo a cikin gado, ya ce, :

﴿ لِّلرِّجَالِ نَصِيبٌ مِّمَّا تَرَكَ ٱلْوَٰلِدَانِ وَٱلْأَقْرَبُونَ وَلِلنِّسَآءِ نَصِيبٌ مِّمَّا تَرَكَ ٱلْوَٰلِدَانِ وَٱلْأَقْرَبُونَ مِمَّا قَلَّ مِنْهُ أَوْ كَثُرَ ۚ نَصِيبًا مَّفْرُوضًا ﴿٧﴾ ﴾ [لنساء: ٧].

Ma’ana : “Maza suna da rabo cikin abin da iyaye da makusanta suka bari, haka

ma mata suna rabo cikin abin da iyaye biyu da makusanta suka bari, daga cikin abu mai yawa ko kaɗan, rabo ne yankakke". (Annisa'i 7). Sannan Allah ya ba 'ya mace damar mallaka da sadaka da damar 'yanta wa kamar yadda namiji yake da irin wannan damar, Allah ya ce a cikin ayar da ta gabata «Da masu sadaka maza da masu sadaka mata» ya sanya mata haƙƙin zamar miji, ba za a yi mata aure ba yardar ta ba. Musulunci ya kareta daga wulaƙanta wa, ya hana waɗanda suke so su cutar da ita, waɗanda suke so su ji daɗi da ita ba hanyar shari'a ba. Haka mace take rayuwa a ƙarƙarshin inuwar musulunci da girmamawarsa, ko dai ta zama mata, ko 'yar uwa tana aikinta a rayuwa wanda Allah ya ɗora mata. Wannan shi ne matsayin mace a musulunci, addinin rahama da jin ƙai da kamala.

To abin tambaya a nan ina ne addinin musulunci ya wulaƙanta 'ya mace, ko ya rage mata ƙima da daraja? Yanzu duk waɗannan abubuwan da suka gabata ba girmamawa ba ce da ɗaukakawa ba? Don haka waɗanda suke maimaita maganar maƙiya Allah masu cewa musulunci ya zalunci mace su ji tsoron Allah.

Yaku 'yan uwa musulmi : Ku duba matsayin mace a wajen waɗancan al'ummu da suke kushe musulunci da cewa ya zalunci 'ya mace, ya ƙwace mata haƙƙi, ku saurara ku ji matsayinta a wurinsu, ku auna ku gani shin akwai wata girmamawa?.

Matsayin Mace a wurinsu a yau, ya fi matsayinta a jahiliyya muni, sun maida 'ya mace ta zama araha ana fito da ita tsirara gaban maza, a wuraren da suke taruwa, sun maida su masu hidima a cikin gidaje, ma'aikata a ofisoshi, masu jinyar marasa lafiya a asibitoci, masu tarban mutane a hotels da wuraren sayar da abinci, masu karantar da maza a makarantu, 'yan wasan kwaikwayo a gidajen sinima. Haƙiƙa sun zalunci 'ya mace, sun hanata haƙƙinta na tsayuwar ɗa namiji a kanka wajen ciyarwa da kula da ita, sun rabata da matsayinta a gida da tarbiyyar yara, da samar da iyali, haka suka yanke mata duk wani taimako da zai taimaka mata wajen aikinta da Allah ya halicceta da shi, har sai da suke takura mata ta fito don neman abin da zata ci, ta hanyar sayar da mutuncinta ga duk wani fajiri, suka ɗora mata aikin maza, suka rabata da sitira, suka bar ta tsirara tana bayyana wuraren kyau a jikinta, suka jefata cikin cakuɗuwa da maza, har ta zama abin kwaɗayin duk wani mai kwaɗayi, sun haramta abin da Allah ya halatta, suka halatta abin da Allah ya haramta a cikin haƙƙin mace, sun hana auren mace fiye da ɗaya, wanda hakan shi ne haƙiƙanin maslaha ga mata, saboda namiji zai ɗauki nauyin wani adadi na mata, domin abu sananne cewa adadin mata ya fi na maza a yawa a wurare da dama, amma sai suka taƙaita namiji akan mace ɗaya, sauran matan kuwa suka bar su ga maɓarnata, suna cin abinci ta hanyar sayar da mutuncinsu, ko kuma suna aiki mai wahala, sun ɗaiɗaita su suna neman aikin da za su rayu da shi, koda kuwa a wasu garuruwa ne masu nisa da garinsu.

Haka maƙiya Allah maƙiya 'yan adam suka raba 'ya mace daga dukkan wani taimakon da zai sa ta rayu rayuwar arziƙi, suka saɓuleta daga dukkan haƙƙinta na yau da kullum, don su mayar da ita hanyar ɓarna da lalacewa.

Zaku mamaki – Yaku bayin Allah – idan ku sani cewa duk da waɗannan laifuffukan da maƙiya Allah suka yi wa mata, suna da'awar sune masu taimaka wa mata, masu kare musu haƙƙi, masu neman a basu haƙƙinsu, wani abin mamakin ma shi ne wai har a samu musulmi su zama bakunansu suna maimata abin da suke faɗa, suna yaɗa maganganunsu a jaridu da kafafen yaɗa labarai, suna maimaita maganganun da aka faɗa musu ba tare da sun san ma'anarsu ba.

Allah ya yi mana albarka cikin abin da muka ji, na alƙur'ani da hadisi, haƙiƙa Allah mai iko ne akan dukkan komai.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah, Kyakkyawan ƙarshe yana ga masu tsoron Allah, Tsira da Aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, Manzon Allah (ﷺ) da iyalansa da Sahabbansa da waɗanda suka bi su gaba ɗayansu, har zuwa ranar sakamako. Bayan haka:

Yaku mutane : ku ji tsoron Allah dangane da matanku, haƙiƙa ku an baku kiwo ne, ku sani cewa duk wani abin da ya faru garesu, ku ne abin tambaya. Amma abin baƙin ciki muna jin irin munanan yanayi da wasu mata suke ciki a gidajensu da unguwanninsu, daga cikin irin waɗannan hali : akwai sakaci da hijabi, musammam ma 'yan matan da suka saba fita, suna fita da kaya matsatstsu, waɗanda suke siffata jikinsu, yin haka saɓa wa Allah ne, kuma cin amana ne!.

Ku sani – Yaku magidanta – cewa musulunci ya sanya lada mai yawa akan tarbiyyar 'ya 'ya mata. An karɓo daga Uƙbatu ɗan Amir – Allah ya yarda da shi – ya ce, naji Manzon Allah (ﷺ) yana cewa : "Duk wanda yake da 'ya 'ya mata guda uku, kuma ya yi haƙuri da su, ya tufatar da su daga samunsa, za su zamar masa kariya daga wuta". Bukhari ne ya rawaito shi a cikin (Al'adab) Sheikh Albani ya inganta shi.

Haka ma An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi – Allah ya yarda shi – ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Wanda yake da 'ya 'ya mata guda uku, ya zama yana mai tattaro su, yana isar musu abin da suke nema, yana tausayinsu, to ya wajaba ya shiga Aljannah" sai wani mutum ya ce, "ko guda biyu ne ya Rasulallahi? Sai ya ce, "Ko da biyu ne". Bukhari ya rawaito shi a cikin littafinsa (Al-Adabul Mufrad).

Don haka ku ji tsoron Allah ya waɗanda Allah ya ɗora wa nauyin kula da mata, ku kula da tarbiyyar 'ya 'yanku mata, zaku rabauta, ku azurta duniya da lahira. Ku kiyaye wasiyyar Allah da Manzon Allah (ﷺ) suka yi akan kula da lura da mata.

Sannan ina kira ga 'yar uwa musulma da ki riƙe addininki, addinin da Allah ya girmamaki da shi, ya ɗaukaka matsayinki da shi, ya tsamo ki da shi daga faɗawa da gangarawa zuwa ga halaka, da faɗawa gaban mutanen da suke dabbobi, ku tuna – yake baiwar Allah – a koyaushe meye matsayinki kafin zuwan musulunci, da matsayinki a yau a ƙasashen kafirai.

Ki sani da'awar ci gaba da 'yancin mace ba zata kawo miki alheri ba, kaɗai zata haifar miki da taɓewa da shiga uku. Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa : "Wanda duk ya yi aiki nagari daga namiji da mace yana mai imani to zamu raya shi kyakkyawar rayuwa, kuma zamu saka musu ladansu daga mafi kyan abin da suke aikatawa" (Annahal : 98).

Ki tuna – yake baiwar Allah – irin yadda Allah Maɗaukakin Sarki ya fifita wasu mata saboda biyayyarsu ga Allah da Manzonsa (ﷺ) Ki duba Nana Khadija Allah Ta'ala yake aiko mata da gaisuwa.

An karɓo daga Abu Hurairata – Allah ya yarda da shi – ya ce, Mala'ika Jibrilu ya zo wajen Annabi (ﷺ) ya ce, ya Manzon Allah, ga khadija nan ta zo, tana ɗauke da kwano da abinci a ciki ko abin sha, idan ta zo wajenka, ka isar mata gaisuwa daga Ubangijinta, da kuma daga gareni, ka yi mata bushara da gida a Aljanna na azurfa, wanda babu hayaniya da wahala a cikinsa". Bukhari ne ya rawaito shi.

Yaku Musulmi : Daga abin da ya gabata zamu gane cewa musulunci addini ne mai girma kuma gamamme da ya haɗa komai da komai, babu zalunci ko tawaya cikin abin da Allah ko Manzonsa suka saukar. Musulunci shi ne addinin kaɗai ya girmama ɗan adam ya ɗaukaka martabarsa.

Don haka wajibi ne akan malamai su tashi su bayyyana wa mutane haƙiƙanin wannan addini mai girma, ba a ɓatar da wasu matan ba sai saboda jahilcinsu ga addininsu da abinda yake cikinsa na gyara da ɗaukaka. Allah ya datar damu.

IMANI DA SUNAYEN ALLAH DA SHARHIN WASU DAGA CIKINSU

Manufofin huɗubar

- Kwaɗaitarwa a kan imani da sunayen Allah Ta'ala.
- Sharhin ma'anonin wasu daga cikin sunayen Allah Ta'ala.
- Kwaɗaitarwa a kan yin addu'a da sunayen Allah Ta'ala.
- Bayani a kan cewa sunayen Allah shi ne ya kira kansa da su. Hankali baya gano su.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammadu bawansa ne manzonsa ne. (Yaku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron Allah yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Yaku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammadu (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (a addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta".

Bayan haka:

Ya ku bayin Allah! Yana daga cikin bayar da gaskiya da Allah, bayar da gaskiya da sunayensa mafiya kyau, da siffofinsa mafiya ɗaukaka, ba tare da jirkirta su ba, ko kamanta su da na bayi, ko kore su ba. Ubangiji ya ce,

﴿ وَلِلَّهِ ٱلۡأَسۡمَآءُ ٱلۡحُسۡنَىٰ فَٱدۡعُوهُ بِهَا ﴾[الأعراف: ١٨٠].

(Sunaye mafiya kyau sun tabbata ga Allah, don haka ku roƙe shi da su).

Kuma Ubangiji ya ce,

﴿ وَلَا تَقۡفُ مَا لَيۡسَ لَكَ بِهِۦ عِلۡمٌۚ ﴾ [الإسراء: ٣٦].

(Kada ka bibiyi abin da ba ka da sani a kansa).

Kuma Manzon Allah (ﷺ) ya faɗa a cikin fitaccen hadisinsa, cewa “Ya Ubangiji! Ina roƙon ka da duk wani sunan da yake naka ne, ka ambaci kanka da shi, ko ka saukar da shi a cikin littafinka, ko ka sanar da shi ga wani daga cikin halittarka, ko ka keɓanta da sanin sa cikin sanin gaibu da yake wajenka.” Ahmad da Ibni Hibban suka rawaito shi, kuma hadisi ne ingantacce.

Yana daga cikin sunayen Allah, Allahu: Ma’anarsa: Wanda zukata suke bauta masa, tare da soyayya da ƙauna da girmamawa. Daga ciki akwai Ar-rahman Ar-rahim: Ma’anarsu: Wanda yake jin ƙan bayinsa, sama da yadda mahaifiya take jin ƙan ɗanta. Ba wata rahama da za ta samu, sai daga rahamarsa, ba wata musiba da za a ije ta, sai da rahamarsa. Ubangiji ya ce,

﴿ وَمَا بِكُم مِّن نِّعۡمَةٖ فَمِنَ ٱللَّهِۖ ﴾ [النحل: ٥٣].

(Duk wani abu da yake tattare da ku na ni’ima, daga Allah yake).

Daga cikinsu, akwai Almaliku: Wanda ya mallaki duniya gabaɗayanta, samanta da ƙasanta. Ba wani abu da zai yi motsi, sai da saninsa da yardarsa. Ubangiji ya ce,

﴿ قُلِ ٱللَّهُمَّ مَٰلِكَ ٱلۡمُلۡكِ تُؤۡتِي ٱلۡمُلۡكَ مَن تَشَآءُ ﴾ [آل عمران: ٢٦].

(Ka ce, “Ya Allah, mamallakin mulki! Kana bayar da mulki ga wanda ka so). Kuma Ubangiji ya ce,

﴿ مَٰلِكِ يَوۡمِ ٱلدِّينِ ۝٤ ﴾ [الفاتحة: ٤].

(Mamallakin ranar sakamako).

Kuma yana daga cikin sunayensa, Alƙuddusu: Shi ne wanda ya tsarkaka daga dukkan tawaya da aibuka. Ya halicci halitta gabaɗayanta, wahala ba ta shafe shi ba, ko cuta. Ubangiji ya ce,

﴿ وَلَقَدۡ خَلَقۡنَا ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ وَمَا بَيۡنَهُمَا فِي سِتَّةِ أَيَّامٖ وَمَا مَسَّنَا مِن لُّغُوبٖ ۝٣٨ ﴾ [ق: ٣٨].

(Haƙiƙa mun halicci sammai da ƙasa da abin da yake tsakanin su, cikin kwanaki shida, kumsa wahala ba ta shafe mu).

Daga cikin sunayensa, akwai Alƙawiyyu, Alƙahhaar: Babu wani abin halitta, face sai yana ƙarƙashin ikonsa da tanƙwarawarsa, babu wani mai ji-ji-da-kai, face sai ya risuna ga girmansa da ƙarfinsa. Ubangiji ya ce,

﴿ مَا قَدَرُواْ ٱللَّهَ حَقَّ قَدۡرِهِۦٓ إِنَّ ٱللَّهَ لَقَوِيٌّ عَزِيزٞ ۝٧٤ ﴾ [الحج: ٧٤].

(Ba su girmama Allah yadda ya cancanta su girmama shi ba. Lallai Allah mai ƙarfi ne, kuma mabuwayi).

Yana daga cikin sunayensa, Al-Aliim: Wanda ya san abin da yake ɓoye, kuma ya san abin da yake sarari, da abin da yake cikin teku. Babu wani ganye da zai faɗi, face sai ya sani, babu wata ƙwaya da take cikin duhun ƙasa, ko ɗanyen abu ko busasshe, face yana cikin littafi mabayyani.

Yana daga cikin sunayensa, Al-Aliyyu A’alaa: Maɗaukaki a cikin zatinsa, sama da al-arshinsa, maɗaukaki a cikin siffofinsa. Tsarki ya tabbata a gare shi!

Daga cikin sunayensa, akwai Aljabbaar: Wanda yake ɗora karyayye da mai rauni, kuma yake damƙar mai ƙarfi, ya tanƙwara shi.

Daga cikin sunayensa akwai Alghafuur: Wanda yake gafarta zunubai gabaɗaya, kuma yake lulluɓe aibuka, ko da kuwa suna da yawa. Ya zo a cikin hadisi ƙudusi, Ubangiji ya ce, “Ya ɗan Adam! Matuƙar ka roƙe ni, ka ƙaunaci gafarata, zan gafarta maka, bisa ga abin da ya kasance na laifinka, kuma ban damu ba.” [Tirmizi da Ahmad ne suka ruwaito shi].

Kuma yana daga cikin sunayensa, Alhakiimu: Mai azanci cikin shari’arsa da ƙaddararsa.

Yana daga cikin sunayensa, Alghaniyyu: Mawadacin da zatinsa daga halittunsa baki ɗaya.

‘Yan uwa masu sauraro! Ku sani, yana daga cikin imani da sunayen Allah, roƙon sa da su, kamar yadda Allah ya ce,

﴿وَلِلَّهِ ٱلۡأَسۡمَآءُ ٱلۡحُسۡنَىٰ فَٱدۡعُوهُ بِهَا﴾[الأعراف: ١٨٠].

(Sunaye mafiya kyau sun tabbata ga Allah, ku roƙe shi da su).

Wata rana, Manzon Allah (ﷺ) ya ji wani mutum yana addu’a, yana cewa, “Ya Allah! Lallai ni ina roƙon ka da cewa godiya ta tabbata gare ka, babu abin bauta bisa ga cancanta sai kai kaɗai, babu abokin tarayya gare ka, mai kyauta, maƙagin sama da ƙasa. Ya ma’abocin girma da karamci! Ya rayayyen sarki, kuma tsayayye!!” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Haƙiƙa ya roƙi Ubangiji da sunansa mai girma, wanda idan aka roƙe shi da shi, yake amsawa, kuma idan aka roƙe shi da shi, yake bayarwa.” [Abu Dawud ya rawaito shi].

Ya kai bawan Allah! Ya zama wajibi a kanka, ka riƙa roƙon Allah, da sunayensa da siffofinsa.

Game da faɗar Allah da y ace,“….ku roƙe shi da su.” Sheikh Usaimin yana cewa, “Ka sanya su tsani zuwa ga abin da kake nema. Ka zaɓi sunan da ya dace da buƙatarka: Idan za ka roƙi gafara, sai ka ce, “Ya mai gafara! Gafarta mini.” Bai dace ba ka ce, “Ya mai tsananin uƙuba! Ka gafarta mini.” Yin haka, ya yi kama da ba’a. Sai dai ka ce, “Ka kuɓutar da ni daga azabarka”…"

Ubangiji yana cewa,

﴿وَلِلَّهِ ٱلۡأَسۡمَآءُ ٱلۡحُسۡنَىٰ فَٱدۡعُوهُ بِهَاۖ وَذَرُواْ ٱلَّذِينَ يُلۡحِدُونَ فِيٓ أَسۡمَٰٓئِهِۦۚ سَيُجۡزَوۡنَ مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ١٨٠﴾

[الأعراف: ١٨٠]

(Sunaye mafiya kyau sun tabbata ga Allah, ku roƙe shi da su, ku ƙyale waɗanda suke kangara a cikin sunayensa, da sannu za a saka musu da abin da suke aikatawa).

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah, Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga Manzon Allah (ﷺ) da iyalensa da sahabbansa gabaɗaya.

Bayan haka, ya ku musulmai! Ku dogara kan littafin Allah, da sunnar Manzon Allah (ﷺ) wajen sanin sunayen Allah Ta’ala, saboda bai halatta ga wani ya ambaci Allah, da abin da Allah bai ambaci kansa da shi ba, ko Manzonsa bai ambace shi da shi ba. Saboda sunayen Allah Ta’ala, sai da nassi ake sanin su. Alƙur’ani mai girma, cike yake da sunayen Allah Ta’ala, da siffofinsa. Misali, Allah yana cewa,

﴿ هُوَ ٱللَّهُ ٱلَّذِى لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلْمَلِكُ ٱلْقُدُّوسُ ٱلسَّلَٰمُ ٱلْمُؤْمِنُ ٱلْمُهَيْمِنُ ٱلْعَزِيزُ ٱلْجَبَّارُ ٱلْمُتَكَبِّرُ ۚ سُبْحَٰنَ ٱللَّهِ عَمَّا يُشْرِكُونَ ﴿٢٣﴾ هُوَ ٱللَّهُ ٱلْخَٰلِقُ ٱلْبَارِئُ ٱلْمُصَوِّرُ ۖ لَهُ ٱلْأَسْمَآءُ ٱلْحُسْنَىٰ ۚ يُسَبِّحُ لَهُۥ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۖ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿٢٤﴾ ﴾ [الحشر: ٢٣ - ٢٤].

(Shi Allah, shi ne wanda babu abin bauta bisa cancanta sai shi, Masanin abin da ya ɓuya da abin da ya fito fili, shi ne Mai rahama, Mai jin ƙai. Shi Allah, babu wani abin bauta bisa cancanta sai shi, Mai sarauta, Tsarkakakke, Mai aminci, Mai kuɓutarwa, Tsayayye, Mabuwayi, Mai ƙarfi, Mai ji da kai, tsarki ya tabbata ga Allah ga abin da suke yi na shirka. Shi Allah, shi ne Mai halitta, shi ne Mahalicci, Mai ƙaga halitta, Mai suranta ta, sunaye mafiya kyau sun tabbata gare shi. Abin da yake sama da ƙasa suna tsarkake shi, kuma shi Mabuwayi ne, gwani mai hikima).

Kuma Ubangiji ya ce,

﴿ قُلْ هُوَ ٱللَّهُ أَحَدٌ ﴿١﴾ ٱللَّهُ ٱلصَّمَدُ ﴿٢﴾ لَمْ يَلِدْ وَلَمْ يُولَدْ ﴿٣﴾ وَلَمْ يَكُن لَّهُۥ كُفُوًا أَحَدٌۢ ﴿٤﴾ ﴾ [الإخلاص: ١ – ٤].

(Allah shi kaɗai ne. Allah shi ne wanda zukata suke buƙatuwa zuwa gare shi, bai haifa ba, kuma ba a haife shi ba, kuma ba wani da yake kwatankwacinsa).

Ya zo cikin hadisi, “Haƙiƙa Allah kyakkyawa ne, yana so kyau.” [Ibni Hibban ya rawaito shi].

Kuma Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Lallai Ubangiji mai kunya ne, mai sitirtawa, yana son kunya da sitirtawa. idan ɗayanku zai yi wanka, ya ɓuya.” [Abu Dawud da Nasa’i suka rawaito shi].

Manzon Allah (ﷺ) ya kasance, sau da yawa, yana roƙon Allah da sunayensa mafiya kyau. An karɓo daga Shaddad bin Aus, daga Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Shugaban Istigfari shi ne, “Ya Allah! Kai ne Ubangijina, babu abin bauta bisa cancanta, sai kai. Kai ne ka halicce ni, kuma ni bawanka ne. Kuma ina bisa alƙawarinka da wa’adinka, iyaka iyawata, ina komawa gare ka da ni’imarka, kuma ina komawa gare ka da zunubina, don haka, ka gafarta mini, domin babu wanda zai gafarta zunubai, sai kai. Ina nema tsari daga gare ka daga sharrin abin na aikata.” Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Idan bawa ya faɗi wannan lokacin maraice, sai ya mutu, zai shiga aljanna, ko yana cikin ‘yan aljanna; idan ya faɗa da safe, sai ya mutu a ranar, kwatankwacin haka.” Bukhari ne ya ruwaito shi.

Kuma an karɓo daga Aliyyu bin Abi Ɗalib, ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya kasance, idan ya tashi zuwa sallah, sai ya yi kabbara, sannan ya ce, “Na fuskantar da fuskata ga wanda ya halicci sama da ƙasa, ina mai kaucewa shirka, ina musulmi, kuma ba na aikin mushirikai. Lallai sallata da yankana da rayuwata, ga Allah suke, Ubangijin talikai, ba shi da abokin tarayya. Da haka aka umarce ni, kuma ni ne farkon masu miƙa wuya. Ya Ubangiji! Kai ne sarki, babu abin bautawa bisa cancanta, sai kai. Kai ne Ubangijina, kuma ni bawanka ne, na zalunci kaina, kuma na yi iƙirari da laifina, don haka ka gafarta mini laifukana gabaɗaya, babu mai gafarta laifuka, sai kai. Kuma ka shiryar da ni ga ɗabi’u mafiya kyau, babu mai shiryarwa ga ɗabi’u mafiya kyau, sai kai. Kuma ka kawar mini da munanansu, babu mai tafiyar da munanansu, sai kai. Na amsa kiranka, ya Ubangiji! Alheri

gabaɗayansa yana hannunka, ba a danganta sharri zuwa gare ka. Ni ɗin nan saboda kai nake, kuma zuwa gare ka zan koma. Alherinka ya yawaita, kuma ka ɗaukaka, ina neman gafararka, ina komawa zuwa gare ka." Idan ya yi ruku'i, sai ya ce, "Ya Ubangiji! Gare ka na yi ruku'i, kai kaɗai, kuma da kai na bayar da gaskiya, kai kaɗai, kuma gare ka na miƙa wuya, jina da ganina da ɓargona da ƙashina, sun rusuna gare ka." Idan ya ɗago daga ruku'i, sai ya ce, "Allah ya amsa wa wanda ya gode masa. Ya Ubangijinmu! Godiya ta tabbata gare ka, cikin sama da ƙasa da cikin abin da yake tsakaninsu da cikin abin da ka ga dama, na daga wani abu bayan haka." Idan kuma ya yi sujjada, sai ya ce, "Ya Ubangiji! Gare ka na yi sujjada, kai kaɗai, kuma da kai na bayar da gaskiya, kai kaɗai, kuma na miƙa wuya gare ka, fuskata ta yi sujjada ga wanda ya halicce ta, kuma ya suranta ta, sannan ya kyautata surarta, kuma ya tsaga mata ji da gani. Alherin Allah ya yawaita, mafi kyawun masu halitta." Idan ya yi sallama, sai ya ce, "Ya Ubangiji! Ka gafarta mini abin da na gabatar, da abin da na jinkirtar, da abin da na ɓoye, da abin da na bayyanar, da abin da na wuce gona-da-iri, da abin da kai ne mafi sani da shi gare ni. Kai ne mai gabatarwa, kai ne mai jinkirtarwa, babu abin bautawa bisa cancanta, sai kai." [Abu Dawud da Tirmizi suka rawaito shi].

Ya ku 'yan uwa! A hir ɗinku, kuma ahir ɗinku, da ku ambaci Allah da abin da bai ambaci kansa da shi, ko Manzonsa bai ambace shi da shi ba. Kamar yadda wasu mutane ke yi. Wannan jingina wa Allah ne abin da bai faɗa ba. Haƙiƙa, Allah ya yi hani a kan yin haka. Ya ce,

﴿ قُلۡ إِنَّمَا حَرَّمَ رَبِّيَ ٱلۡفَوَٰحِشَ مَا ظَهَرَ مِنۡهَا وَمَا بَطَنَ وَٱلۡإِثۡمَ وَٱلۡبَغۡيَ بِغَيۡرِ ٱلۡحَقِّ وَأَن تُشۡرِكُواْ بِٱللَّهِ مَا لَمۡ يُنَزِّلۡ بِهِۦ سُلۡطَٰنٗا وَأَن تَقُولُواْ عَلَى ٱللَّهِ مَا لَا تَعۡلَمُونَ ٣٣ ﴾ [الأعراف: ٣٣].

(Ka ce, "Kaɗai dai, Allah ya haramta alfasha, ta fili da ta ɓoye, da laifi, da zalunci ba tare da gaskiya ba. Kuma kada ku haɗa Allah da wani, abin da Allah bai saukar da hujja da shi ba. Kuma kada ku faɗi abin da ba ku sani ba ga Allah."

Kuma Allah ya ce,

﴿ وَلَا تَقۡفُ مَا لَيۡسَ لَكَ بِهِۦ عِلۡمٌۚ ﴾ [الإسراء: ٣٦].

(Kada ka bibiyi abin da ba ka da sani a kansa).

Ya ku musulmai! Ku ji tsoron Allah, kuma ku sani cewa za ku koma gare shi, ko kusa ko nesa. Ku yi riƙo da littafin Allah, da sunnar Manzon Allah (ﷺ), kuma ku roƙi Allah da sunayensa da siffofinsa, domin ya yi narko na wuta ga masu yin girman kai ga hakan. Allah ya ce, "Haƙiƙa waɗanda suke girman kai ga roƙo na, da sannu za su shiga wuta, suna ƙasƙantattu." Kuma ku nemi sanin ma'anonin sunayen Allah, domin suna da matuƙar kyau, kuma sun ƙunshi ma'anoni masu girma.

LAZIMTAR SUNNAR ANNABI (ﷺ)

Manufofin hudubar

- Bayanin haƙiƙanin sonsa (ﷺ).
- Bayanin cewa, ibada ba za ta zama karɓaɓɓiya ba sai ta dace da sunnarsa.
- Bayanin cewa, ma'anar shaidawa Muhammadu manzon Allah ne, shi ne tsantsanta biyayya gare shi.
- Bayanin amfanin lazimtar sunnah.

Hudduba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma mua neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan aiyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar dashi, wanda kuma ya atar babu mai shiryar da shi, kuma ina shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai allah, shi kaɗai ne bashi da abokin taraiya, kuma ina shaidawa cewa Annabi Muhammad bawansane manzonsane, (Yaku waɗanda kuka bada gaskiya kuji tsoron Allah yadda ya cancanta aji tsoronsa, kada ku mutu face kuna Musulmi). (Yaku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicce ku daga rai guda ɗaya kuma ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga gare su (su biyu) kuji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya dashi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku waɗanda suka yi imani kuji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku aiyukanku, kuma ya gafarta muku zunubanku. Wanda ya bi Allah da manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawun shiriya shiriyar Annabi Muhammadu (ﷺ) kuma mafi sharrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta. Baya haka;

Ya ku bayin Allah! A cikin mu waye ba ya son manzon Allah (ﷺ)? Wanene a cikinmu ba ya son kasancewa tare da manzon Allah (ﷺ) a lahira?

Wanene a cikinmu ba ya ƙaunar ceton Almustafa (ﷺ)?

Kowanne daga cikinmu yana fafutuka don rabauta da kusanci da Manzon Allah (ﷺ) da samun cetonsa a ranar alƙiyama, da kusantar Allah da sonsa. Sai dai menene tafarki zuwa a haka, menene hanya mai sadarwa zuwa cim ma waannan buri?

Hayan ɗaya ce babu ta biyu, ita ce, lazimtar biyayya gare shi (ﷺ). Domin son Manzon Allah (ﷺ), Allah ne wanda ya aiko shi da shiriya da addinin gaskiya ya wajabta shi, don haka babu imani ga wanda ba ya son sa. Kuma alama ta farko ta gaskiyar saonsa tana cikin biyayya gare shi, da bin sunnarsa. Allah Ta'ala Ya ce:

﴿ قُلْ أَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَٱلرَّسُولَۖ فَإِن تَوَلَّوْاْ فَإِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ ٱلْكَٰفِرِينَ ٣٢ ﴾ [آل عمران: ٣٢].

(Ka ce, ku bi Allah da manzonsa, idan kuwa suka ba da baya to Allah ba ya son kafirai).

Kuma ya ce:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُواْ ٱلرَّسُولَ وَأُوْلِي ٱلۡأَمۡرِ مِنكُمۡۖ فَإِن تَنَٰزَعۡتُمۡ فِي شَيۡءٖ فَرُدُّوهُ إِلَى ٱللَّهِ وَٱلرَّسُولِ إِن كُنتُمۡ تُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِۚ ذَٰلِكَ خَيۡرٞ وَأَحۡسَنُ تَأۡوِيلًا ٥٩ ﴾ [النساء: ٥٩].

(Ya ku waɗanda suka imani, ku bi Allah ku bi Manzo, da shugabanni a cikinku. Idan kun yi jayayya a cikin wani lamari, to ku mai da shi zuwa ga Allah da Manzonsa, in kun kasance kun yi imani da Allah da ranar lahira, wannan shi ne mafi alhri kuma mafi kyawun makoma).

Kuma Allah yana cewa:

﴿ قُلۡ أَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُواْ ٱلرَّسُولَۖ فَإِن تَوَلَّوۡاْ فَإِنَّمَا عَلَيۡهِ مَا حُمِّلَ وَعَلَيۡكُم مَّا حُمِّلۡتُمۡۖ وَإِن تُطِيعُوهُ تَهۡتَدُواْۚ وَمَا عَلَى ٱلرَّسُولِ إِلَّا ٱلۡبَلَٰغُ ٱلۡمُبِينُ ٥٤ ﴾ [النور: ٥٤].

(Ka ce ku bi Allah ku bi manzo, idan kun juya baya, to abin da aka ɗora masa ne ke kansa, ku kuma abin da aka ɗora muku ne ke kanku. Idan kuwa kuka bi shi kwa shiryu, ba komai yake a kan manzo ba face isarwa mabayyaniya).

Kuma ya ce:

﴿ قُلۡ إِن كُنتُمۡ تُحِبُّونَ ٱللَّهَ فَٱتَّبِعُونِي يُحۡبِبۡكُمُ ٱللَّهُ وَيَغۡفِرۡ لَكُمۡ ذُنُوبَكُمۡۚ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٣١ ﴾ [آل عمران: ٣١].

“Ka ce, in kun kasance kuna son Allah, to ku bi ni, Allah zai so ku, kuma ya gafarta muku zunubanku, Allah mai gafara ne mai jinƙai.”

Allah Ta’ala ya ce:

﴿ وَمَا كَانَ لِمُؤۡمِنٖ وَلَا مُؤۡمِنَةٍ إِذَا قَضَى ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥٓ أَمۡرًا أَن يَكُونَ لَهُمُ ٱلۡخِيَرَةُ مِنۡ أَمۡرِهِمۡۗ وَمَن يَعۡصِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ فَقَدۡ ضَلَّ ضَلَٰلٗا مُّبِينٗا ٣٦ ﴾ [الأحزاب: ٣٦].

(Bai kasance ga wani mumini ko mumina ba idan Allah da manzonsa suka hukunta wani lamari, ya zama suna da zaɓi a lamarinsu ba. Duk wanda ya saɓi Allah da manzonsa, to haƙiƙa ya ɓata, ɓata mabayyani).

Allah maɗaukakin sarki yana cewa:

﴿ إِنَّمَا كَانَ قَوۡلَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ إِذَا دُعُوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ لِيَحۡكُمَ بَيۡنَهُمۡ أَن يَقُولُواْ سَمِعۡنَا وَأَطَعۡنَاۚ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُفۡلِحُونَ ٥١ وَمَن يُطِعِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَيَخۡشَ ٱللَّهَ وَيَتَّقۡهِ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡفَآئِزُونَ ٥٢ ﴾ [النور: ٥١ – ٥٢].

(Kaɗai faɗin muminai idan aka kira su zuwa ga Allah da manzonsa, domin ya yi hukunci a tsakaninsu, shi ne, su ce, mu ji kuma mun bi. Waɗannan su ne masu rabauta. Wanda ya bi Allah da manzonsa kuma ya ji tsoron Allah, ya tsorace shi, to waɗannan su ne masu samun rabo).

Ya ku bayin Allah, hadisai da yawa sun zo suna zaburarwa a kan wajabcin bin sunna Ma’aiki. Ga kaɗan daga cikinsu:

An karɓo daga Irbadh bn Sariyah (R.A), ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya yi mana wa’azi wanda zukata suka raurawa da shi, idanuwa suka zubar da hawaye. Sai muka ce, ya Ma’aikin Allah, kamar ka ce, wa’azi ne na mai ban kwana! Ka yi mana wasiyya. Ya ce, "Ina muku wasiyya da tsoron Allah, da ji da bi, koda an shugabantar muku da bawa a kanku, domin wanda zai rayu a cikinku, to zai ga saɓani mai yawa, don haka na hore ku da bin sunnata da sunnar halifofina shiryayyu ababan shiryarwa, ku cije ta da fiƙoƙinku. Kuma na hane ku da fararrun

lamurra, domin kowace bidi'a ɓata ce". Abu Dawud da Tirmizi da Ibn Hibban, da Ibn Majah suka rawaito shi. Tirmizi ya ce; Hadisi ne kyakkyawa ingantacce.

An karɓo daga Ɗan Abbas (R.A), cewa, Manzon Allah (ﷺ), ya yi huɗuba a yayin hajjin ban kwana sai ya ce, "Haƙiƙa shaiɗan ya yanke ƙauna a bauta masa a ƙasarku, sai dai ya yarda a bi shi a komabayan haka, daga abubuwan da kuke rainawa daga ayyukanku. To ku shiga taitayinku! Haƙiƙa na bar muku abin da in kuka yi riƙo da shi ba zaƙ ku ɓata ba, har abada, littafin Allah da sunnar Annabinsa. Har ƙarshen hadisin. Hakim ne ya rawaito shi kuma ya inganta shi.

Daga Abu Hurairah, Allah ya ƙara yarda a gare shi cewa, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Dukkanin al'ummata za su shiga aljanna sai wanda ya ƙi". Suka ce, ya manzon Allah waye zai ce, ya ƙi? Sai ya ce: "Wanda ya bi ni zai shiga aljanna, wanda ya saɓa min kuwa to ya ƙi", Bukhari ne ya rawaito shi.

Daga Jabir ɗan Abdullahi (R.A) ya ce: "Mala'iku sun zo gurin Annabi (ﷺ) yana barci, sai sashinsu ya ce: Haƙiƙa barci yake. wasu kuwa suka ce; Idon yana barci, amma zuciyar a faɗake take. Suka ce, lallai mutumin naku yana da misali, ku buga masa misali. Sai suka ce; Misalinsa kamar misalin mutum ne da ya gina gida, sai ya sanya kaɓaki a cikinsa, ya aika mai shela, to duk wanda ya amsawa mai shelar zai shiga gidan, kuma ya ci daga wannan kaɓakin, wanda kuwa bai amsa ba, ba zai shiga gidan ba. Kuma ba zai ci daga kaɓakin ba. Sai suka ce; To ku fassara wannan misalin ya fahimce shi. Sai sashinsu ya ce, Shi barci yake. Sashinsu kuma ya ce, lallai idan barci suke, amma zuciyar a faɗake take. Sai suka ce, gidan dai shi ne aljanna, mai kiran kuwa shi ne Muhammadu (ﷺ). to duk wanda ya bi Muhammadu (ﷺ) to ya bi Allah, wanda ya saɓi Muhammadu (ﷺ) to ya saɓi Allah, kuma Annabi Muhammad (ﷺ) shi ne bambancin da ke tsakanin mutane". Bukhari ne ya rawaito shi.

An karɓo daga Abu Rafi'i, (R.A) ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Kada in sami ɗayanku yana kishingiɗe a kan gadonsa, umarnina ya zo masa daga abin da na yi umarni da shi, ko na yi hani a kansa, sai ya ce, Ban sani ba, abin da muka samu a cikin littafin Allah za mu bi shi (in ba haka ba to a za mu bi ba). Ahmad da Abu Dawud da Tirmizi da Ibn Majah ne suka rawaito shi da sanadi ingantacce.

Daga Ibn Mas'ud, (R.A) ya ce; "Tsaka-tsaki a sunna fi alheri sama da kazar-kazar a bidi'a", Hakim ne ya rawaito shi, ya ce, isnadinsa ingatacce ne.

Ya ku bayin Allah! Haka nan maganganu sun zo daga sahabbai a wannan babi kuma suna da yawa. Kaɗan daga cikinsu:

Mujahid yana cewa, mun kasance tare da Ibn Umar Allah ya jiƙansa, a cikin wata tafiya, sai ya wuce ta wani guri, sai ya karkace masa. Sai aka tambaye shi saboda me ka aikata haka? Sai ya ce, "Na ga Manzon Allah (ﷺ) ya aikata haka, sai ni ma na aikata". Ahmad da Bazzar ne suka rawaito da Isnadi kyakkyawa.

Kuma daga Ibn Umar (R.A); cewa shi ya kasance yana zuwa gurin wata bishiya tsakanin Makka da Madina sai ya yi ƙailula a ƙarƙashinta. Sai ya ba da labari cewa Manzon Allah (ﷺ) ya kasance yana aikata haka. Bazzar ne ya rawaito da Isnadin da babu laifi a cikinsa.

Akwai fa'idoji masu ɗimbin yawa da musulmi zai samu a cikin bin sunnar Annabi (ﷺ), Ga kaɗan daga muhimmansu:

A cikin bin sunnar manzon Allah (ﷺ) akwai samun kariya daga faɗawa cikin saɓani wanda marar kyau, ma nisanta bawa daga addini, wanda shi ne alamar rauni, kuma mutum ba zai kuɓuta daga gare shi, ba sai da bin Allah da manzonsa. Allah ta'ata ya ce:

﴿ وَأَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَلَا تَنَٰزَعُواْ فَتَفۡشَلُواْ وَتَذۡهَبَ رِيحُكُمۡۖ وَٱصۡبِرُوٓاْۚ إِنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلصَّٰبِرِينَ ٤٦ ﴾

[الأنفال: ٤٦].

(Kuma ku bi Allah da manzonsa, kuma kada ku yi jayayya sai ku sami karyewa, kuma ƙarfinku ya tafi, ku yi haƙuri, haƙiƙa Allah yana tare da masu haƙuri).

Hakanan a cikin hadisin Irbadh da ya gabata Annabi ya ce, «Ina muku wasiyya da tsoron Allah, da ji da biyayya, koda bawa ne Bahabashe ya zama shugabanku, domin duk wanda ya rayu daga cikinku to zai ga saɓani mai yawa, kuma na gargaɗe ku ga barin fararrun lamura, domin su ɓata ne. Wanda ya riski haka daga cikinku, to na hore ku da bin sunna ta, da sunnar halifofi shiryayyu ababan shiryarwa, ku cije ta da fiƙoƙinku». (Ma'ana, ku riƙe su gangam).

Amfani na biyu; A cikin bin sunna da lazimtar ta, akwai kuɓuta daga rarrabuwar kai, wadda Allah ya yi alkawarin narko ga ahlinta.

Tirmizi ya ruwaito hadisi daga Abdullahi ɗan Umar. Annabi (ﷺ) ya ce; "Haƙiƙa abin da ya zo wa Banu Isra'ila zai zo wa al'ummata, kwabo-da-kwabo, kuma haƙiƙa Banu Isra'ila sun rabu ƙungiya saba'in da biyu. Al'umma ta kuwa za ta kasu zuwa ƙungiya saba'in da uku, dukkansu suna cikin wuta sai ƙugiya ɗaya". Suka ce, wacce ce ya manzon Allah? Ya ce, "Ita ce (wacce take kan) abin da nake kai, ni da sahabbaina".

Amfani na uku; A cikin lazimtar sunna akwai samun shiriya da kuɓuta daga ɓata. An karɓo daga Abu Huraira (R.A) ya ce; Manzon Allah (ﷺ) ya ce; "Haƙiƙa na bar abu biyu a cikinku ba za ku taɓa ɓata bayansu ba, littafin Allah da sunnata, kuma ba za su taɓa rabuwa ba, har sai sun zo gare ni a wajen tafkin alkausara". Hakim da Daruƙuɗni da Baihaƙi ne suka fitar da shi.

Kuma an rawaito daga Ɗan Abbas (R.A) cewa, Manzon Allah (ﷺ) ya yi huɗuba cikin mutane a hajjin ban ikwana sai ya ce "Ya ku mutane haƙiƙa ni na bar muku abin da in kun yi riƙo da shi ba za ku taɓa ɓata ba, littafin Allah da sunnar Annabinsa." Baihaƙi ne ya fitar da shi.

Waɗannan hadisai suna fa'idantar da cewa, a cikin bin sunnar Annabi (ﷺ), a nan kuɓuta take daga ɓata.

Malik Allah ya jiƙansa, ya ce; "Sunna, kamar jirgin ruwan Annabi Nuhu ne, wanda ya hau shi ya tsira, wanda kuwa ya noƙe ya halaka."

Wannan gaskiya ne, domin jirgin ruwan Annabi Nuhu, ba wanda ya hau shi, sai wanda ya gaskata manzanni, wanda bai hau shi ba, ya ƙaryata manzanni. Shi kuwa bin sunna bi ne ga manzancin da ya zo daga Allah. Don haka wanda ya bi shi, kamar wanda ya bi jirgin ruwa ne, zahiri da baɗini, wanda ya ƙi bin manzancin, kamar wanda ya ƙi bin Annabi Nuhu ne da hawa jirgin ruwa tare da shi.

Amfani na huɗu: A cikin sunna akwai shiga cikin tawagar Annabi (ﷺ), a cikin barin ta kuwa akwai fita daga cikin tawagarsa.

Bukhari da Muslim sun ruwaito hadisi daga Anas ɗan Malik (R.A) yana cewa; “Wasu mutane uku sun zo ga matan manzon Allah (ﷺ) suna tambaya game da bautar Annabi (ﷺ). Yayin da aka ba su labari, sai kamar sun ga ƙarancinta, suka ce, ina mu ina Annabi (ﷺ), alhali shi an gafarta masa abin da ya gabata daga zunubansa da abin da ya jinkirta, ɗayansu ya ce, amma ni zan yi sallah tsawon dare har abada. Ɗayan ya ce, ni za yi azumin har abada ba za sha ba. Ɗayan ya ce, ni zan nisanci mata ba za yi aure ba har abada. Sai manzon Allah (ﷺ) ya zo wajen su, ya ce “Ku ne kuka ce kaza da kaza, amma wallahi ni, na fi ku tsoron Allah, sai dai ni ina azumi ina sha, ina sallah in barci, kuma ina auren mata, to duk wanda ya yi bar sunnata ba ya tare da ni.”

Barin sunnar Annabi (ﷺ) mataki biyu ne. Yana iya kasancewa a matsayin saɓo. Yakan kuma iya kasancewa a matsayin kafirci. Wal’iyazu billahi.

Idan ka bar sunnar don sakaci da kasala, ba don ganin cewa akwai naƙasa a cikinta ba, to hukuncinka shi ne gwargwadon irin sunnar da ka bari. In ka bar wajibi ne, to kana da laifin barin wajibi. In kuma Mustahabbi ka bari to haƙiƙa falalar mustahabbi ya kuɓuce maka.

Ku ji tsoron Allah ya bayin Allah ku yi riƙo da igiya mafi aminci ta musulunci, kuma ku yi sani cewa mafi alherin shiriya ita ce shiriyar Annabinku (ﷺ), kuma mafi sharrin lamurra shi ne fararrunsu kuma dukkanin fararrun abubuwa bida’a ce, kuma dukkanin bidi’a ɓata ne, wal’iyazu billah.

Wannan shi ne abin da zan iya faɗa, kuma ina neman gafarar Allah maɗaukaki mai girma ga kaina da ku da sauran musulmi daga dukkan zunubi, ku nemi gafararsa, haƙiƙa shi mai gafara ne mai jinƙai.

Huɗuba Ta Biyu

Yabo ya tabbata ga Allah, Shi ne ƙasaitaccen sarki. Tsira da amincin Allah, su tabbata ga bayinsa da ya zaɓa, bayan haka, ya ku bayin Allah!

Amfani na biyar; cewa a cikin falalar sunna, da binta akwai ‘yantuwa daga hanyoyin shaiɗani. An karɓo daga Ibn Mas’ud (R.A), ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya zana wani zane sai ya ce: “Wannan shi ne tafarkin Allah, sannan sake yin wasu ‘yan ƙananan zane a hagunsa da damansa. Sannan manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Wannan shi ne tafarkina, waɗannan kuma wasu hanyoyi ne, a kan kowace hanya akwai shaiɗani da yake kira zuwa gare shi". Sannan ya karanta faɗar Allah:

﴿ وَأَنَّ هَٰذَا صِرَٰطِي مُسۡتَقِيمٗا فَٱتَّبِعُوهُۖ وَلَا تَتَّبِعُواْ ٱلسُّبُلَ فَتَفَرَّقَ بِكُمۡ عَن سَبِيلِهِۦۚ ذَٰلِكُمۡ وَصَّىٰكُم بِهِۦ لَعَلَّكُمۡ تَتَّقُونَ ١٥٣ ﴾ [الأنعام: ١٥٣].

(Kuma cewa wannan shi ne tafarkina miƙaƙƙe, ku bi shi, kuma kada ku bi wasu hanyoyi, sai su raba ku da tafarkinsa, wannan shi ne abin da ya yi muku wasiyya da shi, tsammaninku za ku ji tsoron Allah).

Duk wanda ya bi sunnar Annabi (ﷺ) ya bi tafarki maidadaici, kuma ya kuɓuta

daga hanyoyin shaiɗanu.

Ibn Taimiyya Allah ya jiƙansa, ya ce: “Mafi yawancin waɗannan hanyoyin ɓatan suna shigo wa wanda bai yi riƙo da littafin Allah da sunna ba. Kamar yadda Zuhri yake cewa, “Malamanmu sun kasance suna cewa, riƙo da sunna shi ne tsira.”

Amfani na shida: A cikin bin sunna akwai samar da addinin da shari’a. Wannan kuwa saboda addini ma’anarsa ka bautawa Allah, kuma kada ka bauta masa sai da abin da ya shar’anta, kuma ba mu da hanyar sanin shar’ah ba tare da Alƙur’ani da sunnar Annabin (ﷺ) ba. Don haka ibadu suka kasance sai yadda shari’a ta tsara su. Babu mamaki da nana A’isha (R.A) ta ce: "Halayensa (ﷺ) suna kasance Alƙur’ani". Sunnarsa (ﷺ) ta kasance ta mamaye dukkanin addini. Ita ce mai bayyana ma’anonin Alƙur’ani mai girma. Allah Ta’ala ya ce:

﴿ وَأَنزَلۡنَآ إِلَيۡكَ ٱلذِّكۡرَ لِتُبَيِّنَ لِلنَّاسِ مَا نُزِّلَ إِلَيۡهِمۡ وَلَعَلَّهُمۡ يَتَفَكَّرُونَ ٤٤ ﴾ [النحل: ٤٤].

(Kuma mun saukar da ambato gare ka domin ka bayyana wa mutane abin da aka saukar musu, tsammaninsu za su yi tunani).

Allah Ta’ala ya ce:

﴿ وَمَآ أَنزَلۡنَا عَلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبَ إِلَّا لِتُبَيِّنَ لَهُمُ ٱلَّذِي ٱخۡتَلَفُواْ فِيهِۖ وَهُدٗى وَرَحۡمَةٗ لِّقَوۡمٖ يُؤۡمِنُونَ ٦٤ ﴾ [النحل: ٦٤].

(Kuma ba mu saukar maka da littafi ba, sai don ka bayyana musu abin da suka yi saɓani a cikinsa, kuma da shiriya, da rahama ga mutane da suke masu imani).

Annabi (ﷺ) ya yi alwala sai ya ce: “Wannan ita ce alwalata, kuma alwalar annabawa gabani na, duk wanda ya ƙara ko ya tauye, to ya munana, ya yi zalunci.”

Kuma Annabi (ﷺ) ya yi salla, kuma ya ce, “Ku yi salla kamar yadda kuka gan ni ina sallah.”

Kuma shi ne ya ce: “Kaɗai an aiko ni ne don in cika kyawawan ɗabi’u”. Kuma shi ne ya ce, “Ku yaɗa sallama a tsakaninku, kuma ku ciyar da abinci, ku yi sallah da dare yayin da mutane suke barci, za ku shiga aljannar Ubangijinku da aminci”.

Amfani na bakwai: A cikin bin ka ga sunna akwai ɗage alamar ƙasƙanci da wulaƙanci daga al’umma, domin sunna ita ce addini, kuma barin addini shi ne musabbabin ƙasƙanci da wulaƙanci.

Ahmad da Abu Dawud sun ruwaito hadisi daga Ibn Umar, ya ce, Mun ji manzon Allah (ﷺ) yana cewa, “Idan kuka yi cinikin eena, kuma kuka riƙi kiwo, kuma kuka raja’a kan noma, kuka bar jihadi, Allah zai ɗora muku ƙasƙancin da ba zai cire muku shi ba har sai kun komo zuwa addininku”.

Cinikin eena shi ne, cinikin da mutum ya sayar wa da wani mutum kaya bashi zuwa wani lokaci, sannan ya sayi kayen daga wajesa a take, da kuɗin da ba su kai abin da ya sayar masa ba.

Don haka komawa sunna, komawa ne zuwa ga addini.

Amfani na takwas: A cikinta akwai bayanin cutar da ta samu wannan al’umma ta Musulmi da kuma bayanin maganinta.

Ahmad da Abu Dawud sun ruwaito hadisi daga Sauban, ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Al’ummomi sun kusa su yi ca a kanku, kamar yadda masu cin abinci

suke yi daka wawa a kan akushisu". Sai wani ya ce, saboda rashin yawanmu ne a lokacin? Sai ya ce: “A’a, ku a lokacin kuna da yawa, sai dai kun zama shara, kamar sharar da ruwa yake korawa. Lallai za a cire kwarjininku daga zukatan abokan gabarku, kuma za a jefa rauni a zukatanku". Wani mai magana ya ce, ya manzon Allah mene ne rauni? Sai ya ce, “Son duniya da ƙin mutuwa”.

Manzon Allah (ﷺ) ya siffanta mana cutar mu da halinmu ya ce, “Lallai al’ummomi sun kusa su yi ca a kanku kamar yadda masu cin abinci suke daka wasoso a kan akushinsu”. Shin wannan bai faru ba?! Wallahi ya faru. Kasashen mulkin mallaka sun yi ca, a kan ƙasashen musulmai. Waɗannan ƙasashe na musulmai, Allah Ta’ala Ya ba su alherai, ya azurta su da alheran ƙoramu, da noma, da fetur, da abubuwa daban daban, amma duk da haka sun riƙa daka wawa a kansu kamar yadda masu cin abinci suke wawa kan akushinsu. Wannan yanayi ba zai rabu da wannan al'umma ba har sai ta koma ga addininta. Komawa ga addinin kuwa shi ne, komawa zuwa ga Alƙur'ani da Sunna.

Amfani na tara: A cikin sunnarsa (ﷺ), akwai samun cikar halaye da kyawawan ɗabi’u na gari. Ahmad ya ruwaito hadisi daga Abu Huraira, ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce,: “Kaɗai an aiko ni ne don in cika kyawawan halaye".

Ibn Abdul Barr, ya ce, "Wannan hadisin Madina ne ingantacce". Kuma nagarta da dukkan alheri da addini, da falala, da kyautayi, da adalci, duk sun shiga cikin wannan ma’ana.

Amfani na goma: Cikin riƙo da sunna akwai tsira daga fitina da azaba mai raɗaɗi.

Allah maɗaukakin sarki ya ce:

﴿ لَّا تَجۡعَلُواْ دُعَآءَ ٱلرَّسُولِ بَيۡنَكُمۡ كَدُعَآءِ بَعۡضِكُم بَعۡضٗاۚ قَدۡ يَعۡلَمُ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ يَتَسَلَّلُونَ مِنكُمۡ لِوَاذٗاۚ فَلۡيَحۡذَرِ ٱلَّذِينَ يُخَالِفُونَ عَنۡ أَمۡرِهِۦٓ أَن تُصِيبَهُمۡ فِتۡنَةٌ أَوۡ يُصِيبَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٌ ٦٣ ﴾ [النور: ١٣].

(Kada ku riƙa kiran Manzon Allah kamar yadda kuke kiran junanku. Haƙiƙa Allah ya san waɗanda suke silalewa don fakewa daga acikinku, don haka masu saɓawa lamarinsa, su kiyayi kada wata fitina ta same su, ko wata azaɓa mai raɗaɗi).

Duk wanda ya saɓawa sunnah! Lallai ya kiyayi: “Lallai waɗanda suke saɓawa lamarinsa su kiyayi kada wata fitina ta same su ko azaba mai raɗaɗi”. Wata fitina ta same su, kamar kafirci ko munafunci ya shiga zuciyarsu, ko su shiga bidi’o’i, sai azaba mai raɗaɗi ta samu su. Saboda haka yana daga cikin falalar bin sunnar manzon Allah (ﷺ), samun tsira daga fitina.

Wani mutum ya zo wajen Imamu Malik ya ce, ya Imam ina son Umara! Sai ya ce, "Ka je ka yi mana!" Ya ce, ina so in yi mata harama daga nan Madina daga masallaci! Sai Malik ya ce, "Ya ɗana! Manzon Allah (ﷺ) ya yi Umara, kuma daga Zulhulaifah ya yi harama. Yin haramarka daga masallaci saɓanin sunna ne. Ina jiye maka tsoron fitina idan ka aikata haka. Sannan ya karanta faɗar Allah:

“Lallai waɗanda suke saɓawa lamarinsa su kiyayi kada fitina ta same su, ko azaba mai raɗaɗi”.

Ya ɗan uwa ka bi sunnar manzon Allah (ﷺ) sak. Ka tsaya kai da fata a kan sha'anin ibada, ba sassauci. Ka tabbata idan har ka ta fi a kan haka, to zuciyarka za

ta gyaru. Hakanan iyalanka da duka danginka.

Gyaruwar iyali gyaruwar mahalli ne.

Gyaruwar mahalli kuwa gyaruwar gari ne duka.

Gyarywar gari kuwa gyaruwar ƙasa ce.

Gyaruwar ƙasa, gyaruwar al'umma ce.

Gyaruwar al'umma gyaruwar duniya gabaɗaya, da izinin Allah.

Ka yi kwaɗayi wajen fara gyara kanka, ka fara da kanka, sannan na kusa da kai, sannan na kusa. Ka san cewa, sunna ita ce tafarki, kuma bin shi zai samar maka da haka. Ina A'uzu billahi minasshaiɗanir-rajim:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُواْ ٱلرَّسُولَ وَأُوْلِي ٱلۡأَمۡرِ مِنكُمۡۖ فَإِن تَنَٰزَعۡتُمۡ فِي شَيۡءٖ فَرُدُّوهُ إِلَى ٱللَّهِ وَٱلرَّسُولِ إِن كُنتُمۡ تُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِۚ ذَٰلِكَ خَيۡرٞ وَأَحۡسَنُ تَأۡوِيلًا ٥٩ ﴾ [النساء: ٥٩].

(Ya ku waɗanda suka ba da gaskiya, ku bi Allah ku bi manzo da shugabanni a cikinku. Idan kun yi jayayya a cikin wani lamari, to ku mai da shi zuwa ga Allah da manzonsa in kun kasance kun yi imani da Allah da ranar lahira, wannan shi ne mafi alhri kuma mafi kyawun makoma)..

KA YI WA MASU HAKURI ALBISHIR

Manufofin hudubar

- Koyar da hakuri.
- Hakuri halayyar mumini ce.
- Sanin kashe-kashen hakuri.
- Hakuri dole ne ga mai son ya rayu a tsaka

Huduba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammadu bawansa ne manzonsa ne. (Yaku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron Allah yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Yaku waɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa hakika ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammadu (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (a addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta".

Bayan haka! Ya bayin Allah! Ku sani Allah ya sanya hakuri tamkar ingarman dokin da ba ya tuntuɓe, tamkar takobin da ba ya dakushewa, tamkar rundunar da ba a taɓa karya ta ba, tamkar ganuwar da ba ta rusuwa. Hakuri da nasara ‘yan’uwan juna ne, kuma duk mutumin da bai riƙi hakuri a matsayin makaminsa a addininsa da duniyarsa ba to ya san da sanin cewa, makiyansa sai sun fatattake shi. Makiyi ne na zuciya ko na shaiɗan ne. Kuma babu wani ƙarfi ga bawan da bai da hakuri. Kamar yadda babu shi babu cin nasara matukar dai ba shi da hakuri a yakinsa da yin gaba da abokin gabansa. Allah yana cewa,

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱصۡبِرُواْ وَصَابِرُواْ وَرَابِطُواْ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ لَعَلَّكُمۡ تُفۡلِحُونَ ٢٠٠ ﴾

[آل عمران: ٢٠٠].

(Ya ku waɗanda suka yi imani, ku yi hakuri, kuma ku jure, kuma ku zama a cikin shiri, kuma ku ji tsoron Allah ko kwa rabauta).

Ya bayin Allah, hakika hakuri igiyar talala ce ta mumini, duk inda ya je zai komo gare shi. Kuma shi dai hakuri ga mumini tamkar wata madogara ce da babu yadda ya iya sai ya dogara da shi. Babu imani cikakke ga wanda ba shi da hakuri.

Duk sanda imani ya yi ƙaranci kuwa to sai ka ga ko da bautar Allahn ma ta zama rabi darabi. Ranar da gari ya yi dadi a yi, ranar da kuma abubuwa suka caɓe a yi biris da ita. Allah ya ce:

﴿ وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يَعۡبُدُ ٱللَّهَ عَلَىٰ حَرۡفٖۖ فَإِنۡ أَصَابَهُۥ خَيۡرٌ ٱطۡمَأَنَّ بِهِۦۖ وَإِنۡ أَصَابَتۡهُ فِتۡنَةٌ ٱنقَلَبَ عَلَىٰ وَجۡهِهِۦ خَسِرَ ٱلدُّنۡيَا وَٱلۡأٓخِرَةَۚ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلۡخُسۡرَانُ ٱلۡمُبِينُ ١١ ﴾ [الحج: ١١].

(Daga cikin mutane akwai wanda yake bauta wa Allah a kan gaɓa, idan alheri ya same shi sai ya gamsu da shi, idan kuma wata musiba ta same shi sai ya juya baya, to ya taɓe duniya da lahira, wannan ita ce hasara mabayyaniya).

Wannan bai samu komai a kasuwancinsa ba sai hasara mai girma da ya yi. Waɗanda suka dace da kyakkyawar rayuwa sun same ta ne a dalilin haƙurinsu. Don haka sun sami manya-manyan matsayi a dalilin godiyarsu ga Allah. Sun ta shi sama da fikafikin haƙuri da na godiya ga Allah zuwa ga aljannatai na ni'ima. Saboda faɗar Allah da yake cewa,

﴿ ذَٰلِكَ فَضۡلُ ٱللَّهِ يُؤۡتِيهِ مَن يَشَآءُۚ وَٱللَّهُ ذُو ٱلۡفَضۡلِ ٱلۡعَظِيمِ ٢١ ﴾ [الحديد: ٢١].

(Wannan falala ce daga Allah, yana bayar da ita ga wanda ya so, Allah kuwa Ma'abocin falala ne mai girma(.

Ya bayin Allah! Haƙuri halayyar cikakkun bayin Allah muminai ce, babu mai jure masa sai wanda Allah ya ƙarfafe shi. Annabawa da manzanni su ne abin koyi a dukkan nau'o'in haƙuri, Imam Ahmad Allah ya rahamshe shi ya ce: "Allah Mai tsarki ya ambaci haƙuri sau casa'in a cikin Alƙur'ani». Sannan kuma Allah Mai girma da buwaya ya yabi masu haƙuri a cikin littafinsa. Kuma Ya ba da labarin cewa ladan da zai ba masu haƙuri, ya fi gaban lissafi, a inda yake cewa:

﴿ إِنَّمَا يُوَفَّى ٱلصَّٰبِرُونَ أَجۡرَهُم بِغَيۡرِ حِسَابٖ ١٠ ﴾ [الزمر: ١٠].

(Haƙiƙa masu haƙuri ne kawai ake cika wa ladansu ba da lissafi ba).

Bayan haka, Allah ya faɗi cewa, yana tare da masu haƙuri da shiryarwarsa, da babban taimakonsa, da kuma bayyanannen buɗinsa, sai ya ce:

﴿ وَٱصۡبِرُوٓاْۚ إِنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلصَّٰبِرِينَ ٤٦ ﴾ [الأنفال: ٤٦].

(Ku yi haƙuri haƙiƙa Allah Yana tare da masu haƙuri).

Kasancewar masu haƙuri na tare da Allah, ya sa suka rabauta da ni'imomin Allah na fili da na ɓoye.

Haka kuma, bayan duk waɗannan bayanai, Allah mai girma da ɗaukaka, ya haɗa shugabanci a addini da haƙuri da sakankancewa sai ya ce;

﴿ وَجَعَلۡنَا مِنۡهُمۡ أَئِمَّةٗ يَهۡدُونَ بِأَمۡرِنَا لَمَّا صَبَرُواْۖ وَكَانُواْ بِـَٔايَٰتِنَا يُوقِنُونَ ٢٤ ﴾ [السجدة: ٢٤].

"Muka sanya shugabanni daga cikinsu (wato banu Isra'ila) suna shiryarwa da umarninmu lokacin da suka yi haƙuri, kuma sun kasance suna sakankancewa da ayoyinmu".

Kari a kan haka Allah ya rantse a kan cewa haƙuri alheri ne ga masu yin sa a inda ya ce:

﴿ وَلَئِن صَبَرۡتُمۡ لَهُوَ خَيۡرٞ لِّلصَّٰبِرِينَ ١٢٦ ﴾ [النحل: ١٢٦].

"Kuma lalle idan kuka yi haƙuri, to babu shakka shi ne mafi alheri ga masu haƙuri".

Kuma komai ƙarfin abokin gaba babu yadda ya iya da bawa mai haƙuri da tsoron Allah. Allah maɗaukaki ya ce:

﴿ وَإِن تَصۡبِرُواْ وَتَتَّقُواْ لَا يَضُرُّكُمۡ كَيۡدُهُمۡ شَيۡـٔٗاۗ إِنَّ ٱللَّهَ بِمَا يَعۡمَلُونَ مُحِيطٞ ١٢٠ ﴾ [آل عمران: ١٢٠].

“Idan kuka yi hakuri kuka ji tsoron Allah, to makircinsu ba zai cuce ku da komai ba. Hakika Allah mai kewaye ce da saninsa ga abin da suke aikatawa.”

Sannan kuma Allah Y a rataye rabautar bawa da hakuri da kuma jin tsoron Allah. Sai Ya ce:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱصۡبِرُواْ وَصَابِرُواْ وَرَابِطُواْ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ لَعَلَّكُمۡ تُفۡلِحُونَ ٢٠٠ ﴾ [آل عمران: ٢٠٠]

(Ya ku waɗanda suka yi imani ku yi hakuri, kuma ku jure, kuma ku zama a cikin shiri, kuma ku ji tsoron Allah ko kwa rabauta).

Bayan haka, Allah ya bayyana ƙaunarsa ga bayinsa masu hakuri. Ya ce,

﴿ وَٱللَّهُ يُحِبُّ ٱلصَّٰبِرِينَ ١٤٦ ﴾ [آل عمران: ١٤٦].

(Allah yana son masu hakuri).

Sannan ya yi wa masu hakuri albishir da abubuwa uku masu daraja fiye da abubuwan da bayi suke hassada a kansu a duniya, Ya ce:

﴿ وَبَشِّرِ ٱلصَّٰبِرِينَ ١٥٥ ٱلَّذِينَ إِذَآ أَصَٰبَتۡهُم مُّصِيبَةٞ قَالُوٓاْ إِنَّا لِلَّهِ وَإِنَّآ إِلَيۡهِ رَٰجِعُونَ ١٥٦ أُوْلَٰٓئِكَ عَلَيۡهِمۡ صَلَوَٰتٞ مِّن رَّبِّهِمۡ وَرَحۡمَةٞۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُهۡتَدُونَ ١٥٧ ﴾ [البقرة: ١٥٥ – ١٥٧].

(Kuma ka yi albishir ga masu hakuri waɗanda idan masifa ta same su sai su ce, mu na Allah ne, kuma mu wurinsa za mu koma. Waɗancan (bayi) gafarar Allah ta tabbata a gare su da rahama, kuma waɗancan su ne shiryayyu).

Sannan kuma babu mai tsira daga wuta, kuma ya rabauta da aljanna sai fa masu hakuri. Allah mai girma da buwaya ya ce:

﴿ إِنِّي جَزَيۡتُهُمُ ٱلۡيَوۡمَ بِمَا صَبَرُوٓاْ أَنَّهُمۡ هُمُ ٱلۡفَآئِزُونَ ١١١ ﴾ [المؤمنون: ١١١].

(Hakika ni na saka musu a yau saboda hakurinsu, hakika kuma su ne marabauta).

Kuma Allah ya keɓanci masu hakuri da godiya da amfanuwa da ayoyinsa inda don tantance su da wannan rabo mai girma, kuma gwaggwaɓa, har sau huɗu a gurare daban-daban. Allah Ya ce,

﴿ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّكُلِّ صَبَّارٖ شَكُورٖ ٣١ ﴾ [لقمان: ٣١].

(Hakika game da wannan akwai ayoyi ga duk mai yawan hakuri mai yawan godiya). Duba surorin Ibrahim da Saba’i da Lukman da kuma Shura, za ka ga hakan.

Ya bayin Allah! Ba wani abu ba ne hakuri face hana kai raki, da hana harshe kokawa, da kuma hana gaɓɓai make-make da kekketa sutura da makamantan haka.

Wani daga cikin nagartattun bayi ya ga wani mutum yana kai kukan matsalarsa ga ɗan uwansa, sai ya ce da shi “To ai kai ka kai ƙaran wanda zai tausaya maka gurin wanda ba zai tausaya maka ba”.

Wannan ya sa aka ce, Mai kai kukansa ga ɗan adam yana kai kukan mai jin ƙai ne (wato Allah) wajen wanda ba zai ji ƙansa ba.

Kai kuka iri biyu ne.

Na farko shi ne, kai kuka ga Allah. Wannan ba ya korewa bawa hakuri. Kamar yadda Annabi Yakub ya yi inda ya ce:

﴿ قَالَ إِنَّمَآ أَشۡكُواْ بَثِّي وَحُزۡنِيٓ إِلَى ٱللَّهِ وَأَعۡلَمُ مِنَ ٱللَّهِ مَا لَا تَعۡلَمُونَ ٨٦ ﴾ [يوسف: ٨٦].

(Ni fa kawai ina bayyana takaicina ne da bakin cikina zuwa ga Allah. Kuma na san wani abu daga Allah wanda ku ba ku sani ba).

Duk da haka kuma ya ce:

﴿ فَصَبۡرٞ جَمِيلٞۖ ﴾ [يوسف: ١٨].

(Na yi haƙuri kyakkyawa).

Na biyu shi ne, Wanda yake cikin wani bala'i ya riƙa nuna damuwarsa da manganarsa ko da yanayinsa. Irin wannan salo ya saɓawa haƙuri, yana ma rushe shi.

Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Babu wata kyauta mafi yalwa da alheri da aka bai wa wani bawa irin haƙuri".

Shi haƙuri tamkar linzami ne ga zuciyar ɗan adam, da zarar aka rasa shi sai zuciya ta bazama.

Ya bayin Allah! Haƙuri kashi uku ne, duba da abubuwan da suka rataya da shi.

Haƙuri na farko shi ne, haƙuri a kan bin Allah, da aiwatar da umarninsa.

Haƙuri na biyu kuwa, shi ne haƙurin barin abubuwan da ake hana na saɓo.

Haƙuri na uku kuma shi ne, haƙuri a kan abubuwan da Allah ya ƙaddara kuma ya hukuntawa bayi ta yadda bawa ba zai yi fushi da haka ba.

Sheikh Abdulƙadir Jilani, Allah Ya yi masa rahama ya ce a cikin littafinsa Fathul Gaib: "Babu makawa ga bawa har sai ya zama mai aikata umarnin Allah, ya kuma nisanci haninsa, sannan ya yi haƙuri da hukuncin Allah".

Da waɗannan ƙashi uku na haƙuri, Luƙman ya yi wa ɗansa wasicci ya ce:
﴿ يَٰبُنَيَّ أَقِمِ ٱلصَّلَوٰةَ وَأۡمُرۡ بِٱلۡمَعۡرُوفِ وَٱنۡهَ عَنِ ٱلۡمُنكَرِ وَٱصۡبِرۡ عَلَىٰ مَآ أَصَابَكَۖ إِنَّ ذَٰلِكَ مِنۡ عَزۡمِ ٱلۡأُمُورِ ١٧ ﴾ [لقمان: ١٧].

(Ya ɗana ka tsayar da sallah, kuma ka yi umarni da kyakkyawan aiki, ko kuma hana mummunan aiki, kuma ka yi haƙuri bisa duk abin da ya same ka, lalle wannan yana daga cikin manyan abubuwa).

Wayayyen mumini ba ya fatan bala'i, sai dai yana haƙuri da shi idan ya afku. An karɓo daga Abdullahi ɗan Abu Auf, Allah ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ya ku mutane kada ku yi fatan haɗuwa da abokan gaba, ku roƙi Allah zaman lafiya, sai dai idan kuka yi kicibis da abokan gaba to ku haƙuri, kuma ku sani haƙiƙa aljanna na ƙarƙashin inuwar takubba". (wato bayan wuya sai dadi).

Abubakar Siddiƙ, Allah ya yarda da shi ya ce: "Na fi son a ƙare ni da lafiya in gode fiye da a jarrabe ni da bala'i in yi haƙuri".

Don haka fatan bala'i ba ya daga cikin koyarwar musulunci. Amma fa idan bala'in ya afku, haƙuri da shi ya zama dole. A kodayaushe al'amarin mumini alheri ne, ko dadi ko wuya, kamar yadda ya tabbata a cikin hadisi na Sahihi Muslim, daga Suhaibu ɗan Sinan ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Mamakin al'amarin mumini, haƙiƙa duk al'amuransa alheri ne a gare shi, kuma babu wani wanda ya dace da haka sai dai muminin. Idan wani abin dadi ya same shi sai ya godewa Allah, hakan sai ya zamar masa alheri. Idan kuma wani abin ƙi ya same shi sai ya yi haƙuri, sai haƙurin ya zama alheri gare shi".

Ya 'yan uwa ku sani! Rayuwa dukkanta jarrabawa ce da gwaji. Allah Ya ce:
﴿ وَنَبۡلُوكُم بِٱلشَّرِّ وَٱلۡخَيۡرِ فِتۡنَةٗۖ وَإِلَيۡنَا تُرۡجَعُونَ ٣٥ ﴾ [الأنبياء: ٣٥].

(Muna jarraba ku da fitinar sharri da ta alhri, kuma gare mu za a dawo da ku.)

Kuma ko da Allah yake jarrabar bayinsa yana jarrabarsu ne don sanin masu

haƙurinsu, da jarumansu, da kuma masu gaskiyarsu, daga waɗanda ba haka ba. Allah ya ce:

﴿ أَمۡ حَسِبۡتُمۡ أَن تَدۡخُلُواْ ٱلۡجَنَّةَ وَلَمَّا يَعۡلَمِ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ جَٰهَدُواْ مِنكُمۡ وَيَعۡلَمَ ٱلصَّٰبِرِينَ ١٤٢ ﴾ [آل عمران: ١٤٢].

(Ko kuna tsammanin za ku shiga aljanna ne tun gabanin Allah bai san waɗanda suka yi jihadi a cikinku ba, kuma tun gabanin bai san masu haƙuri ba).

Kuma Allah ya ce:

﴿ وَلَنَبۡلُوَنَّكُمۡ حَتَّىٰ نَعۡلَمَ ٱلۡمُجَٰهِدِينَ مِنكُمۡ وَٱلصَّٰبِرِينَ وَنَبۡلُوَاْ أَخۡبَارَكُمۡ ٣١ ﴾ [محمد: ٣١].

“Kuma haƙiƙa wallahi za mu jarrabe ku har sai mun san masu jihadi daga cikinku Mu kuma san masu haƙuri, kuma Mu jarraba ayyukanku a zantukanku”. Da dai sauran ayoyi masu kama da waɗannan.

Har wa yau, yana daga ckin hikimar jarrabar bayi, sauƙaƙa musu hanyar samun shahada kamar yadda aya mai zuwa take sanar da haka:

﴿ إِن يَمۡسَسۡكُمۡ قَرۡحٞ فَقَدۡ مَسَّ ٱلۡقَوۡمَ قَرۡحٞ مِّثۡلُهُۥۚ وَتِلۡكَ ٱلۡأَيَّامُ نُدَاوِلُهَا بَيۡنَ ٱلنَّاسِ وَلِيَعۡلَمَ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَيَتَّخِذَ مِنكُمۡ شُهَدَآءَۗ وَٱللَّهُ لَا يُحِبُّ ٱلظَّٰلِمِينَ ١٤٠ ﴾ [آل عمران: ١٤٠].

(Idan wani miki ya same ku, to haƙiƙa miki irinsa ya sami mutanen (a yaƙin Badar), waɗancan kwanaki muna jujjuya su ne a tsakanin mutane, don Allah ya san waɗanda suka ba da gaskiya (daga cikinku) ya kuma sami shahidai daga gare ku. Allah kuwa ba ya son azzalumai. Kuma don Allah ya tsarkake waɗanda suka ba da gaskiya, ya kuma hallakar da kafirai).

Kuma Allah maɗaukakin sarki ya ce,

﴿ وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّمَآ أَمۡوَٰلُكُمۡ وَأَوۡلَٰدُكُمۡ فِتۡنَةٞ وَأَنَّ ٱللَّهَ عِندَهُۥٓ أَجۡرٌ عَظِيمٞ ٢٨ ﴾ [الأنفال: ٢٨].

(Haƙiƙa dukiyoyinku da ‘ya’yanku fitina ne, kuma a wurin Allah lada mai girma yake).

A nan nake cewa Allah ya gafarta min ni da ku da sauran musulmai, ku nemi gafarar Allah, lallai Shi mai yawan gafara ne mai yawan jinƙai.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Tsira da amincin Allah su tabbata ga fiyayyen manzanni Annabinmu Muhammad, da iyalansa da sahabbansa gabaɗaya, bayan haka:

Ya bayin Allah! Annabi (ﷺ) ya kasance yana rainon sahabbansa a kan yin haƙuri ta dukkan nau’o’insa. Kuma haka na bayyana a fili ƙarara, idan muka dubi irin zaman Annabi da sahabbansa a garin Makka. An karƃo hadisi daga Khabbab Ɗan Aratt. Ya ce; Mun kaiwa Manzon Allah (ﷺ) kuka, yana mai ta da kansa da wani mayafinsa a inuwar Ka’aba. Sai muka ce masa, ba za ka nema mana taimakon Allah (a kan abokan gabarmu ba), ba ka yi mana addu’a ba. Sai ya ce tabbas cikin waɗanda suka gabace ku a kan kama mutum a haƙa rami a ƙasa a sa shi a ciki, sannan a zo da zarto a sa shi a kansa, a raba shi gida biyu, ko a riƙa tsefe naman jikinsa da kum ɗin ƙarfe, amma duk da haka ba zai bar addininsa ba. Na rantse da Allah al’amarin wannan addini zai cika har matafiyi ya tafi zuwa Hadaramaut (cikin ƙasar Yaman), daga Sana’a' ba ya tsoron komai sai Allah.

Sannan da fargabar kura ta far wa dabbobinsa. Sai dai ku kuna da gaggawa ne".

Abin nufi a nan, su yi haƙuri a kan addininsu, kamar yadda waɗanda suka gabata suka yi haƙuri. Kuma da sannu azabar da kafirai suka yi musu za ta gushe.

Ya bayin Allah! Ta kowane hali mutum ba ya wadatuwa daga haƙuri, domin kuwa yana jujjuyawa ne tsaknin abin da ya wajaba ya yi, da wanda ya wajaba ya bari da kuma abin da aka ƙaddara masa mai gudanuwa a kansa kwatsam. Ga kuma ni'ima da ta zama dole ya godewa Allah a kanta. Idan kuma a kodayaushe bawa bai fita daga waɗannan halaye haƙuri ya zamar masa dole har zuwa ranar mutuwa.

Hadisai da maganganun magabata a kan falalar haƙuri suna da yawa. Ga kaɗan daga ciki:

An karɓo daga Ummu salama ta ce na ji manzon Allah tsira da amincin Allah yana cewa: "Babu wani musulmi da wata masifa za ta same shi sai ya faɗi abinda Allah ya umarce shi da shi: "Daga Allah muke, kuma ga Allah za mu koma, ya Allah ka ba ni ladan jarrabata kuma ka maye min da abin da ya fi ta. Face sai Allah ya maye masa da abin da ya fi ta.

Ummu salamah ta ce, yayin da Abu Salamah (mijinta) ya rasu sai na ce wane Musulmi ne ya fi Abu Salamah, gida na farko da suka yi ƙaura zuwa ga Manzon Allah, sannan duk da haka sai na faɗa, sai Allah ya musanya mini da Manzon Allah.

An karɓo daga Abu Huraira, ya ce; haƙiƙa Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Wanda Allah yake nufinsa da alheri, sai ya jarrabe shi.

An karɓo daga A'isha Allah ya yarda da ita ta ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Babu wata musiba da za ta sami mumini face sai Allah ya kankare masa laifukansa ta dallilinta hatta daidai da ƙaya idan ya taka".

Ya ɗan'uwa mulumi! Ka yi haƙuri da maƙoci, ka yi masa alheri, kuma ka daurewa cutarwarsa. Bayan haka ka yi haƙuri da wanda yake ƙarƙashinka. Sannan dole sa an yi haƙuri da iyali, don haka ka yi haƙuri da matarka a kan kurakuranta.

Ya 'yar'uwa, ke ma sai kin yi haƙuri da mijinki. Shugaba ma sai ya yi haƙuri da waɗanda yake shuganbata. A dunƙule dai haƙuri ya zama dole ga dukkan mutane. Wanda ya yi haƙuri zai haɗu da alheri mai ɗinbin yawa, wanda kuma ya rasa haƙuri to haƙiƙa ya rasa alheri mai tarin yawa.

Ina roƙon Allah dacewa gare ni da ku gaba ɗaya, tare da neman taimakonsa a kan dukkan alheri, domin shi mai cikakken iko ne a kan kowane abu.

Nasiha Da Amana

Manufofin huɗubar

- Bayyana cewa addini nasiha ne.
- Bayanin me ake nufi da nasiha.
- Bayanin ma'anar amana da yadda ake kiyayeta.
- Bayanin falalar nasiha da yadda ake yin ta.
- Tsoratarwa akan sakaci da amana da yin nasiha.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga shirrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammad bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammad (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

'Yan uwana musulmi a yau huɗubarmu tana magana ne akan wata matashiya mai girma, wadda dukkan musulmi da musulma suke da buƙatar ta, kuma Manzon Allah (ﷺ) ya siffata ta da cewa itace addini gaba ɗaya, sannan wannan matashiya ita ce aikin annabawa gabaɗayansu, wannan matashiya kuwa ita ce Nasiha.

Abin da ake kira nasiha shi ne nufin mutum da alheri kamar yadda Imamul Khaɗɗabi da waninsa suka faɗa. Nasiha ita ce tushen wannan addini, Manzon Allah (ﷺ) yana cewa : "Addini nasiha ne, addini nasiha ne, addini nasiha ne, sai muka ce "ga wa?" Sai ya ce, "Ga Allah, ga littafinsa, ga Manzonsa, ga shugabannin musulmi, da sauran da gama - garinsu". A duk lokacin da bawa ya yi nasiha ga waɗannan abubuwa to ya cika addini, wanda duk kuwa ya gaza nasiha ga wani abu daga cikin waɗannan abubuwa, haƙiƙa ya rasa wani abu na addininsa gwargwadon abin da ya gaza a cikinsa.

Nasiha ga Allah ita ce imani da shi, tsarkake zuciya yayin bautarsa, da gaskiyar nufi wajen neman yardarsa, ta yadda mutum zai zama haƙiƙanin bawa ga Allah, mai yarda da abin da ya hukunta, mai wadatuwa da abin da ya bayar, mai kamanta umarninsa, mai nisantar son zuciyarsa, mai tsarkake gaba ɗayan addini gare shi, ba ya nufin riya ko son a ji.

Nasiha ga littafin Allah ita ce, karanta shi, da kamanta umarninsa, da nisantar abubuwan da ya hana, da gasgata labaransa, da ba shi kariya daga canzawar masu canzawa da karkacewar karkatattu, da ƙudurce wa shi zancen Allah ne, ya jefa shi ga Jibrilu, shi kuma ya sauka da shi ga Manzon Allah (ﷺ).

Nasiha ga Manzon Allah (ﷺ) tana nufin ƙauna da so gare shi, biyayya gare shi a fili da ɓoye, taimakonsa yana rai ko bayan ya bar duniya, gabatar da maganganunsa da shiriyarsa a kan magana da shiriyar kowane mutum.

Nasiha ga shugabannin musulmi kuwa ita ce, yin biyayya da gaskiya gare su, da shriyar da su zuwa ga abin da yake alheri ne ga al'umma cikin addininta da duniyarta, da taimakonsu wajen yin aiki da haka, yi musu ɗa'a da biyayya akan duk abin da suka umarta, matuƙar ba su umarni da saɓon Allah ba. Allah Maɗaukakin Sarki ya ce, :

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُواْ ٱلرَّسُولَ وَأُوْلِي ٱلۡأَمۡرِ مِنكُمۡۖ ﴾ [النساء: ٥٩].

Ma'ana : «Yaku waɗanda kuka yi imani, ku bi Allah, ku bi Manzo da ma'abota al'amari a cikinku».

Nasiha ga sauran gama – garin musulmi ita ce, ka so musu irin abin da kake so wa kanka, ka ɓuɗe musu ƙofofin alheri ka kwaɗaitar da su a kanta, ka rufe musu ƙofofin sharri tare da tsoratar da su daga barinsu, ka yi soyayya da 'yan uwantaka tsakaninka da muminai, ka yaɗa kyawawan ayyukansu, ka suturta munanan ayyukansu, ka taimaki wanda aka zalunta a cikinsu, da wanda yake zaluncin, ka taimaki wanda aka zalunta ta hanyar kare shi daga zalunci, shi kuma wanda yake zaluncin da taimake shi ta hanyar hana shi zaluncin.

A duk lokacin da al'umma suka tsaya a kan waɗannan abubuwa, nasiha ga Allah, ga littafinsa, ga Manzonsa, ga shugabannin musulmi da sauran musulmin, to zasu rayu rayuwa mai kyau abar yabo.

Bayin Allah : Daga abin da ya gabata zai bayyana garemu cewa nasiha ta haɗa addini gaba ɗayansa, tushensa da reshensa, haƙƙoƙin Allah da Manzonsa, da haƙƙoƙin bayin Allah. Sai dai abin tambaya a nan shi ne :

Ina nasiha ga wanda ya tozarta haƙƙoƙin Allah, ya kutsa cikin abubuwan da ya haramta, ina nasiha ga ma'abota ha'inci da algush a cikin mu'amala!? Ina nasiha ga wanda yake so ɓarna ta yaɗu a cikin musulmi, ko kuma yake bibiyar al'aurarsu don ya gano abin da suke aikata wa a ɓoye?. Babu ko shakka waɗannan babu su babu nasiha, sun yi nisa daga gareta. Madallah ga masu nasiha, Tir da taɓewa ga masu algush. Ku ji tsoron Allah – Yaku bayin Allah – ku kamanta abubuwan da ya umarta a yi.

Yaku ‘yan uwana masu sauraro : Ku sani cewa wajibi ne akan duk wanda zai yi nasiha ya lura da waɗannan abubuwa masu zuwa :

1. Nasiharshi ta zama don Allah, kada ya yi don a ji, ko don a gani, saboda duk aikin da aka yi ba don Allah ba, Allah baya karɓar shi, baya bada lada a kanshi. Allah yana cewa,

﴿ وَمَآ أُمِرُوٓاْ إِلَّا لِيَعۡبُدُواْ ٱللَّهَ مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ ﴾ [البينة: ٥].

2. Ma’ana : «Ba a umarce su sai dai su bautawa Allah suna masu tsarkake addini gare shi».
3. Ya zama ya san abin da zai yi nasiha a kai, saboda ba a hukunci a kan abu har sai an san shi.
4. Ya zama amintacce ne, domin babu nasiha ga wanda yake maha’inci.
5. Nasihar ta zama a ɓoye, mai mulki za a yi wa ko kuma talaka, don gudun tozartawa. Amma Idan nasihar a ɓoye ba ta yi amfani ba, to babu laifi a bayyanata, musamman ma idan ta shafi saɓawa abubuwan shari’a waɗanda aka haɗu a kansu.
6. Ba sharaɗi ba ne wanda zai yi nasiha ya zama ya fi kowa ilimi, ko ya fi kowa daraja, ko adalci. Imam Ishaƙ ɗan Ahmad yana cewa : “Da a ce wanda yake da ilimi kaɗan ba zai hana mai ilimi da yawa mummunan aiki ba, to da umarni da kyakkyawan aiki ya ruguje, da mun zama kamar Bani – Isra’ila waɗanda Allah ya ce a kansu “Sun kasance ba sa hana mummunan aiki idan su aikata shi” don haka wanda aka fi falala zai iya yin inkari ga wanda ya fi shi falala, fajiri zai iya hana mutumin ƙwarai mummunan aiki”.

Bayin Allah : Haƙiƙa duk wanda yake bin tarihin magabatanmu na ƙwarai zai ga yadda suka buga kyakkyawan misalai wajen yi wa juna nasiha da karɓar nasihar in an yi musu, an rawaito cewa babban tabi’in nan Imam Alhasan Al-Basriy ya ga wani mutum yana dawowa daga wurin jana’iza, sai ya ce masa, “Kana ganin wannan mamacin da zai dawo duniya zai yi aiki na ƙwarai kuwa?” sai mutum nan ya ce, “Kwarai kuwa” Sai Alhasul Basri ya ce da shi, “To in shi bai dawo ya yi ba, kai ka yi” wato in shi bai da ikon dawo wa duniya ya yi aiki na ƙwarai, saboda ya mutu, ƙasa ta binne shi, ya zama a cikinta, to kai ka yi tun gabanin ka zama a matsayinsa, ya zama babu damar ƙara aiki na ƙwarai.

Khalifofin nan shiryayyu sun kasance suna yi wa junansu nasiha a ɓoye, suna farin ciki da ita in an yi musu, ba sa girman kai wajen karɓarta. Sayyidin Abubakar – Allah ya yarda da shi – yana cewa : “Babu alheri a tare da mu idan bamu karɓi nasiha ba, ku kuma mutane babu alheri a tare da ku idan baku yi mana nasiha ba”.

Sayyidina Umar ɗan Khaɗɗab – Allah ya yarda da shi – ya ce, “Allah ya jiƙan mutumin da faɗa min kura – kuraina”. Akan wannan tsari shugabannin musulmi daga cikin magabata suka tafi.

Allah ya yi mana albarka cikin abin da muka ji, daga Alƙur’ani da Sunnah, ya yi mana gafara, haƙiƙa shi mai iko ne akan komai.

Godiya ta tabbata ga Allah, Kyakkyawan ƙarshe yana ga masu tsoron Allah, Tsira da Aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, Manzon Allah (ﷺ) da iyalansa da Sahabbansa da waɗanda suka bi su gaba ɗayansu, har zuwa ranar sakamako. Bayan haka:

‘Yan uwana musulmi : yana daga cikin abin da ya kamata a ambata a wannan wuri amana, domin kuwa amana nauyi ne mai girma, wanda Allah ya bijirar da shi ga sammai da ƙassai da duwatsu amma suka ƙi ɗauka. Allah yana cewa :

﴿ إِنَّا عَرَضۡنَا ٱلۡأَمَانَةَ عَلَى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَٱلۡجِبَالِ فَأَبَيۡنَ أَن يَحۡمِلۡنَهَا وَأَشۡفَقۡنَ مِنۡهَا وَحَمَلَهَا ٱلۡإِنسَٰنُۖ إِنَّهُۥ كَانَ ظَلُومٗا جَهُولٗا ٧٢ ﴾ [الأحزاب: ٧٢].

Ma’ana : “Haƙiƙa mu mun bijirar da amana ga sammai da ƙassai da duwatsu amma sai suka ƙi ɗaukarta, suka ji tsoronta, sai ɗan adam ya ɗauke ta, lallai shi mai yawan zalunci ne da jahilci” (Al-Ahzab : 72).

Amana tana nufin mutum ya lazimci haƙƙoƙin da Allah ya ɗora masa, ya bauta masa kamar yadda ya shar’anta, hakanan ya lazimci kiyaye haƙƙin bayin Allah ba tare da sakaci ba, kamar yadda kake so mutane su kiyaye maka haƙƙoƙinka ba tare da sakaci ba, saboda mu ‘yan adam mun ɗauki nauyin kiyaye amana a wuyanmu, mun lazimci ta, za a kuma tambaye mu a kanta ranar alƙiyama, kaico, wace amsa zamu bayar in an tambaye mu a wannan rana mai girma.

Yaku Musulmi : Allah Maɗaukakin sarki ya umarce mu mayar da amana ga ma’abotanta, idan kuma zamu yi hukunci tsakanin mutane to mu yi hukunci da adalci, waɗannan abubuwa guda biyu amana ba ta tsayuwa sai da su, mayar da amana ga masu ita, da hukunci tsakanin mutane da adalci.

Sannan kowa da kowa ya sani amana tana shiga cikin dukkan komai, shugaba ko sarki mai kiwo ne a kan talakawansa, kuma za a tambaye shi a kansu. Magidanci mai kiwo ne a kan iyalanshi, kuma za a tambaye shi akan abin da yake kiwo. Mace mai kiwo ce a gidan mijinta, kuma za a tambaye ta akan wannan abin da aka ba ta kiwo. Kai! Dukkaninku masu kiwo ne, kuma dukkaninku sai an tambayeku a kan abin da aka baku kiwo, kamar yadda Manzon Allah (ﷺ) ya faɗa.

Ya ‘yan uwa musulmi : Amana a fahimtar magabata bata tsaya a kan mayar da dukiya ba, ko kiyaye alƙawari kaɗai ba, a'a ta yalwaci komai da komai, gabas da yamma, ita ce bishiyar tauhidi, kuma ɗan itacen imani nunanne, sannan inuwa ce a tsananin zafin rana, guzuri ga matafiya.

Amana ce tsayar da shari'ar Allah a cikin rayuwar mutane, sallah amana ce, idan bawa ya tozarta ta, to zai tozarta abin da ba ita ba, Anas ɗan Malik ya fashe da kuka yayin da ya ga an tozarta sallah a zamanin mulkin Hajjaj kamar yadda imamul Bukhari ya rawaito a cikin ingantaccen littafinsa. Babin da yake magana a kan tozarta sallah ga barin lokacinta. An karɓo daga Zuhuri – Allah ya yi masa rahama – ya ce, na shiga wurin Anas ɗan Malik a garin Dimashƙa, yana kuka, sai na ce da shi, "Me ya saka kuka?, sai ya ce, "Babu wani abu da na sani wanda na

riska sai sallah, to ita ma sallar ga shi an tozartata". Zakka amana ce, Sayyidina Abubakar Assidiƙ ya yaƙi waɗanda suka hanata, ya siffata su da waɗanda suka yi ridda. Azumi amana ne, Manzon Allah (ﷺ) yana cewa "idan ranar azumin ɗayanku ce, kada ya yi batsa, kada ya yi hayaniya, idan wani ya zage shi ko ya yi faɗa da shi, ya ce masa, "Ni mutum ne da yake azumi". Hajji amana ne, Allah yana cewa : "Duk wanda ya shiga hajji to babu batsa, babu fasiƙanci, babu jayayya a cikin hajji". Kira zuwa ga Allah amana ne.

Amana tabbata ce akan ambaton Allah, da cika alƙawarin ga Manzon Allah (ﷺ), sannan kuma da dauwama akan addini har zuwa ƙarshen rayuwa. Sarki Hiraƙla ya tambayi Abu Sufyan dangane da sahabban Manzon Allah (ﷺ) ya ce masa, "Shin ana samun wani daga cikinsu yana yin ridda ga barin addininsa?" Sai Abu Sufyan ya ce, "A'a" Sai Sarki Hiraƙla ya ce, "Haka imani yake idan ya cakuɗu da zuciya". Bukhari ne ya rawaito.

Amana kiyaye haƙƙoƙin bayin Allah ce, kamar yadda Annabi Yusuf (A.S) ya amsa wa sarki yayin da yace, "A yau kai wajenmu tabbatacce ne amintacce". Sai ya ce, "Ka sanya ni akan taskokin ƙasa haƙiƙa ni mai kiyayewa ne kuma masani".

Amana bin iyaye ce, da kiyaye dukiyoyin musulmi, da kare musu mutunci. Amana kula da kiyaye ji ce, da yi wa gani hisabi, da bibiyar zuciya. Allah yana cewa :

﴿ إِنَّ ٱلسَّمۡعَ وَٱلۡبَصَرَ وَٱلۡفُؤَادَ كُلُّ أُوْلَٰٓئِكَ كَانَ عَنۡهُ مَسۡـُٔولٗا ﴾ [الإسراء : ٣٦].

Ma’ana : “Kada ka bibiyi abin da baka ilimi a kanshi, haƙiƙa ji da gani da zuciya dukkansu ababen tambaya ne”. (Al-isra’I : 36).

Amana kiyaye ilimi ne da riwaya, kamar yadda malamai suke cewa, «Wannan ilimi addini ne, don haka ku duba wurin wa zaku karɓi addininku».

Amana tashi ne da kula da haƙƙoƙin musulmi, ɗaukan nauyin buƙatun talakawa ne da miskinai, hidima ce ga mabuƙata, haka siffar Manzon Allah (ﷺ) take, kamar yadda Nana A’isha – Allah ya yarda da ita – ta ce, “A’a wallahi Allah ba zai tozarta ka ba har abada, saboda kai kana sada zumunci, kana ɗaukar nauyin wanda bai da shi, ka bawa wanda ba ya da shi, ka taimako a kan abubuwan gaskiya”. Bukhari.

Amana cika alƙawari ne a kan abin da Alƙur’ani da sunnah suka ɗora wa mutum, bin umarninsu da tsayuwa akan iyakarsu. Don haka yana cikin ha’intar Allah da Manzonsa a zagi sahabban Manzon Allah (ﷺ), a kafirta sahabban nan guda biyu masu girma Abubakar da Umar, alhali ayoyin Alƙur’ani suna furuci da Allah ya yarda da su, Manzon Allah (ﷺ) yana cewa : “kada ku zagi sahabbaina”. Allah ya jiƙan babarmu uwar muminai A’ishatu – Allah ya yarda da ita – yayin da take cewa Urwatu “Ya ɗan ‘yar uwata, an umarce su ne su yi sahabbai istigfari, amma sai suka zage su”. Muslim ne ya rawaito.

Amana adalci ce, da sanya mutane a matsayinsu, ba da tauye musu haƙƙi ba, kamar yadda Allah ya ce,

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ كُونُواْ قَوَّٰمِينَ لِلَّهِ شُهَدَآءَ بِٱلۡقِسۡطِۖ وَلَا يَجۡرِمَنَّكُمۡ شَنَـَٔانُ قَوۡمٍ عَلَىٰٓ أَلَّا تَعۡدِلُواْۚ ٱعۡدِلُواْ هُوَ أَقۡرَبُ لِلتَّقۡوَىٰۖ ﴾ [المائدة : ٨].

Ma’ana : «Yaku waɗanda kuka yi imani ku kasance masu tsayuwa saboda Allah, masu yin shaida da gaskiya, kada ƙin wasu mutane ya sanya ku ƙi adalci, ku yi adalci don shi ne mafi kusanci ga tsoron Allah».

Hakanan amana ce kada ku ɗaukaka wulaƙantacce, kada kuma mu yabi ƙananan mutane, kada ba jiɓinta lamari ga waɗanda ba ma’abotansa ba, kada mu girmama jahilai, mu hukunta su a cikin lamarin addininmu da duniyarmu, duk yin wannan yana cikin cin amana wanda yake tafiyar da jin daɗin rayuwa da ginshiƙinta.

Amana shaida ce don Allah, da nasiha ga musulmi, da bayyana gaskiya, wannan ya sa da aka tambayi Hafiz Aliyyu ɗan Madini dangane da babansa Abdullahi ɗan Ja’afar sai ya ce, «Babana yana da rauni (a haddarsa)».

Amana barin ƙarya ce da da’awar ƙarya, domin duk wanda zai siffatu da abin da ba na shi ba kamar wanda ya sanya rigar zur ce. Imam Azzabiy ya faɗa a cikin littafinsa (Siyar) da Ibnu Kasir a cikin (Albidaya wan nihaya) suka ce, “Abu Abdullahil Hakim Annaisaburiy ya kasance yana karantar da mutane littafin da Alhafiz Abdulganiy ɗan Sa’id ya yi masa gyara cikin wasu kurakurai da ya faɗa a cikinsu a cikin littafinsa (Almadkhal), kai! Bai ma tsaya nan ba, har sai da ya aika masa da godiya akan wannan nasiha da ya yi masa. Daga nan AbdulGaniy ɗan Sa’id ya ce, “Zai gane cewa lallai Hakim mutum ne mai hankali”.

Bayin Allah : Saboda girman amana da kyawunta Annabawan Allah suke siffata kansu da riƙon amana. Annabi Hud (A.S) yana cewa mutanensa :

﴿ أُبَلِّغُكُمْ رِسَٰلَٰتِ رَبِّي وَأَنَا۠ لَكُمْ نَاصِحٌ أَمِينٌ ﴿٦٨﴾ ﴾ [الأعراف: ٦٨].

Ma’ana : (Ina isar muku da saƙon Ubangijina kuma ni mai nasiha ne gareku amintacce) (Al-a’araf : 68).

Haka ma Annabi Luɗ, Salihu, da Nuhu, suka faɗa wa mutanensu inda kowannensu yake cewa :

﴿ إِنِّي لَكُمْ رَسُولٌ أَمِينٌ ﴿١٦٢﴾ ﴾ [الشعراء : ١٦٢].

Ma’ana : (Haƙiƙa ni Manzo ne gareku kuma amintacce). Manzon Allah (ﷺ) saboda amanarsa aka ce masa “Al-amin” a garin Makkah tun gabanin a aiko shi ya zama Manzo.

Ku ji tsoron Allah – bayin Allah – Shashenku ya yi wa sashe nasiha, saboda addinin gaba ɗaya nasiha ne, babu alheri ga al’aummar da ba nasiha a tsakaninta. Sannan ku mayar da amana ga masu ita, ku sani Allah zai tambayeku abin da ya baku kiwo, a ranar da dukiya da ‘ya’ya ba sa amfani sai wanda ya je wurin Allah da zuciya kuɓutacciya.

Kwaɗaitarwa Wajen Neman Ilimi Da Aiki Da Shi

Manufofin huɗubar

- Kwaɗaitarwa wajen neman ilimi mai amfani da aiki da shi.
- Faɗakarwa a kan ladubban neman ilimi.
- Tsoratarwa daga jahiltar addini.
- Kira zuwa ga gyara manhajar karantarwa.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga shirrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammad bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammad (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Ya ku ‘yan uwana musulmi ku sani cewa addinin musulunci addini ne na ilimi. Umarni da neman ilimi shi ne farkon abin da Allah Maɗaukakin Sarki ya umarci Annabinsa (S.A.W) da shi, yayin da ya saukar masa da faɗinsa :

﴿ ٱقۡرَأۡ بِٱسۡمِ رَبِّكَ ٱلَّذِي خَلَقَ ١ خَلَقَ ٱلۡإِنسَٰنَ مِنۡ عَلَقٍ ٢ ٱقۡرَأۡ وَرَبُّكَ ٱلۡأَكۡرَمُ ٣ ٱلَّذِي عَلَّمَ بِٱلۡقَلَمِ ٤ عَلَّمَ ٱلۡإِنسَٰنَ مَا لَمۡ يَعۡلَمۡ ٥ ﴾ [العلق: ١ - ٥].

Ma’ana : (Ka yi karatu da sunan Ubangijinka da ya yi halitta. Wanda ya halicci mutum daga gudan jini. Ka yi karatu kuma Ubangijinka shi ne mafi karamci. Wanda ya sanar da alƙalami. Ya sanar da mutum abin da bai sani ba). (Alaƙ : 1 – 5)

Addinin musulunci ya kwaɗaitar da mabiyansa akan neman ilimi, domin ba zai yiwu mutum ya bauta wa Allah ba sai da ilimi. Allah maɗaukakin Sarki yana cewa :

﴿ إِنَّمَا يَخۡشَى ٱللَّهَ مِنۡ عِبَادِهِ ٱلۡعُلَمَٰٓؤُاْ ﴾ [فاطر: ٢٨].

Ma’ana : (Kaɗai waɗanda suke jin tsoron Allah daga cikin bayinsa su ne masu ilimi).(Faɗir : 28). Ya sake cewa :

﴿ قُلۡ هَلۡ يَسۡتَوِي ٱلَّذِينَ يَعۡلَمُونَ وَٱلَّذِينَ لَا يَعۡلَمُونَۗ إِنَّمَا يَتَذَكَّرُ أُوْلُواْ ٱلۡأَلۡبَٰبِ ٩ ﴾ [الزمر: ٩]

Ma’ana : (Shin waɗanda suka sani da waɗanda ba su sani ba za su yi daidai?). (Azzumar : 9). Ya kuma umarci Annabinsa da ya nemi ƙarin ilimi, ya ce :

﴿ وَقُل رَّبِّ زِدۡنِي عِلۡمٗا ﴾ [طه: ١١٤].

Ma’ana : “Ka ce Ubangiji ƙara min ilimi”. (Ɗaha : 114) Ya ɗaga darajar muminai masu ilimi a kan muminai waɗanda ba su da ilimi, Allah ya ce :

﴿ يَرۡفَعِ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مِنكُمۡ وَٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡعِلۡمَ دَرَجَٰتٖۚ وَٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ خَبِيرٞ ١١ ﴾ [المجادلة: ١١].

Ma’ana : (Allah yana ɗaga darajar waɗanda suka yi imani daga cikinku da waɗanda aka ba wa ilimi). (Al- Mujadalah : 11).

An karɓo daga Kasir ɗan Kaisi ya ce, ina zaune tare da Abud Darda’i a masallacin Dimashƙa, sai wani mutum ya zo wajensa ya ce masa, Ya Abud Darda’i na zo wajenka ne daga Madinar Manzon Allah (S.A.W) saboda wani hadisi da aka ce min kana faɗa daga Manzon Allah (S.A.W), kuma babu wata buƙata da ta kawo ni nan sai wannan. (wato jin wannan hadisin) Sai Abud Dar’da’i ya ce, “Na ji Manzon Allah (S.A.W) yana cewa : “Duk wanda ya bi wata hanya yana neman ilimi a cikinta, to Allah zai sanya shi akan hanya daga cikin hanyoyin Aljannah, kuma haƙiƙa Mala’iku suna sanya fika – fikansu ga ɗalibin ilimi, don yarda da abin da yake nema, sannan duk wanda yake sama da ƙasa yana nema wa malami gafara, har ma da kifayen da suke cikin ruwa. Falalar malami a kan mai bauta kamar falalar wata ne a daren goma sha huɗu a kan sauran taurari, kuma haƙiƙa malamai magada Annabawa ne, Annabawa kuwa ba su bar gadon dinari ko dirhami ba, kaɗai sun bar gadon ilimi ne, duk kuwa wanda ya kama shi, to ya kama rabo mai girma”. Abu Dawud ne ya rawaito.

A cikin wannan hadisi akwai dalili bayyananne akan falalar ilimi da masu ilimi, saboda hadisin ya nuna ilimi hanya ce daga cikin hanyoyi zuwa Aljannah, kuma Mala’iku suna shimfiɗa fika – fikansu ga ɗalibin ilimi saboda yarda dawaɗanda suke sama da ƙasa suna nema masa gafara, har da kifayen da suke cikin kogi, to shin yanzu akwai wata falala da daraja da tafi wannan da aka ambat – Yaku bayin Allah.

Haƙiƙa – ya ku bayin Allah – fahimtar addini alama ce dake nuna Allah ya nufi bawa da alheri, An karɓo daga Mu’awiya – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (S.A.W) ya ce, “Duk wanda Allah ya nufe shi da alheri sai ya fahimtar da shi addini. Allah ne mai bayar wa, ni kuma mai rabawa ne. Wannan al’umma ba za ta gushe ba, tana maɗaukakiya akan duk wanda ya saɓa mata, har sai lamarin Allah ya zo, tana maɗaukakiya” Bukhari da Muslim.

Kai! Saboda falalar ilimi da darajarsa ya halatta a yi hassada (gifɗa) a kansa, An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas’ud – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah

(S.A.W) ya ce, “Ba a yin hassada sai a kan abubuwa guda biyu (su ne) Mutumin da Allah ya bashi dukiya, kuma ya bashi dama wajen kashe ta a kan gaskiya, da mutumin da Allah ya bashi hikima (ilimi) yake hukunci da ita, kuma yake koyar da ita” Bukhari ne ya rawaito.

Muɗarrif ɗan Shikhkir yana cewa : “Falalar ilimi ta fi falalar aiki, mafi alheri a cikin addininku shi ne tsantseni”. (Ibnu Abdul – Barri ne ya rawaito a cikin “Jami’ul Bayanil Ilmi”.

Imam Shafi’i yana cewa : “Neman ilimi ya fi sallar nafila zama wajibi”.

Wata rana Sayyidina Umar ɗan Khaɗɗab – Allah ya yarda da shi – yana Madina, sai ga Nafi’u ɗan Haris Alkhuza’i – gwamnan shi na Makka – ya zo wajensa, sai Umar ya ce masa : “Wa ka bari a can madadinka?” sai ya ce, “Na bar wani bawa ne barrarre (wato wanda aka ‘yanta) sai sayyidina Umar ya ce, “Ka sanya Bawa!?” Sai ya ba shi amsa ya ce, “Saboda shi makarancin Alƙur’ani ne, kuma ya san ilimin gado” sai Umar ya ce, “Haƙiƙa Annabi (S.A.W) ya ce, Allah yana ɗaga wasu mutane da wannan littafi (Alƙur’ani) yana kuma ƙasƙanta wasu mutane da shi”.

Ya kai ɗalibi, ka sani ilimi yana da wasu ladubbai da sukan sanya shi ya zama ibada ga Allah, daga cikinsu akwai tsarkake niyya, (ma’ana neman ilimi don Allah, ba don son iyawa ba, ko birge mutane), ya zo a hadisin Abu Hurairata – Allah ya yarda da shi – Manzon Allah (S.A.W) ya ce : “Duk wanda ya nemi ilimin da ake nema don Allah (wato ilimin addini) ya zama bai koye shi ba sai don ya samu duniya, to ba zai ji ƙanshin Aljannah ba ranar alƙiyama”. Abu Dawud ya rawaito. A wani hadisin da Muslim ya rawaito, Manzon Allah ya ce, “Alƙur’ani hujja ne gareka ko a kanka”.

Ibnu Jama’a – Allah ya yi masa rahama – ya ce, “Ka sani cewa duk abin da aka ambata na falalar ilimi da malamai to ya tabbata ne a kan malamai masu aiki da iliminsu, masu biyayya da tsoron Allah, waɗanda suka nufi Allah da iliminsu, da samun kusanci zuwa ga Aljannah, ba waɗanda suka nemi shi da mummunan niyya ba, ko don wani abu na duniya, na mulki, ko dukiya, ko kuma don alfahari ga abokai da mabiya” (Tazkiratus Sami’i)

Hakanan ana so ɗalibi ya himmatu da abin da ya fi mahimmanci, ya fara hardace Alƙur’ani da Tajwidinsa, sannan ya karanci Sunnah, ya yi aiki da abin da ya sani daidai gwargwadon iyawarsa. Sannan ya aikata abin da ya sani daidai ikonsa.

Imamu Ash-Shafi’i – Allah ya yi masa Rahama – yana cewa : “Ilimi ba shi ne abin da aka hardace ba, a’a ilimi shi ne wanda ya yi amfani”. Saboda haka ilimi ingantance shi ne ilimin da ya gadar wa da mai shi tsoron Allah, da nutsuwa, da tsoron Allah, da ƙasƙantar da kai. Sayyidina Umar – Allah ya yarda da shi – ya ce “Ku koyi ilimi, ko koyi nutsuwa tare da shi”.

Allah ya yi mana Albarka cikin abinda muka ji, na Alƙur’ani da Hadisi, Shi Allah Mai iko ne akan dukkan komai.

Godiya ta tabbata ga Allah, Kyakkyawan ƙarshe yana ga masu tsoron Allah, Tsira da Aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, Manzon Allah (S.A.W) da iyalansa da Sahabbansa da waɗanda suka bi su gaba ɗayansu, har zuwa ranar sakamako. Bayan haka:

'Yan Uwana Masu Sauraro, Ga wasu misalai daga rayuwar magabatanmu na ƙwarai wajen jajircewa a kan neman ilimi, sun bada duk abin da suka mallaka wajen ganin sun sami ilimi :

Babban Malamin hadisin nan mai suna Abdur-Rahman ɗan Abi Hatim yana bamu labarinsa yana cewa "Ba a samun ilimi da hutun jiki, mun zauna wata bakwai a garin Misra, bamu ci abinci mai romo ba, muna neman ilimi, domin kuwa muna sammako da sassafe zuwa majalisin malamai, mu zauna har zuwa azzahar, bayan azzahar kuma sai mu tafi wani majalinsin, haka ma da la'asar har zuwa dare, idan dare ya yi, sai mu zauna mu riƙa rubuta abin da muka koyo, muna gyarawa, don haka ba mu da wani lokaci da zamu gyara wani abinci (mai romo mu ci). A tare da ni akwai wani abokina ɗan garin Khurasana, ina amfani da littafinsa, yana amfani da nawa, duk abin da na rubuta ba ya rubutawa, abin da ya rubuta ba na rubutawa.

Wata rana muka yi sammako zuwa wajen wani malami, sai aka ce mana, baya da lafiya, don haka sai muka dawo, a hanya muka ga wani kifi, ya ƙayatar da mu, muka saye shi, muna zuwa gida sai lokacin zuwa wajen wani malami ya yi, saboda haka bamu samu damar gyara kifin nan ba, muka wuce zuwa majalisi, bamu gushe ba muna kai – kawo zuwa wajen malamai har tsawon kwana uku, bamu gyara kifin nan ba, har ya kusa ya lalace, saboda haka muka cinye shi ɗanye!!". Sai ka ce da Abdur-Rahman, ai zaku iya bawa wani ya gyara muku shi, sai ya ce, "Ina muka samu damar yin hakan". (Siyar J13/ sh 266).

Imam Shu'uba ɗan Hajjaj – Allah ya yi masa rahama – ya yi tattaki daga garinsa Basrah zuwa Makkah, zuwa Madinah sannan ya dawo garinsa, saboda ya gano ingancin hadisi ɗaya tak!!.

Ya 'yan uwa masu sauraro : Kaɗan kenan daga cikin ƙisoshin malamai magabata wajen neman ilimi, don haka wajibi ne a kanmu mu tashi mu nemi ilimi, kada mu ruɗu da kawunanmu, mu zama shugabanni kafin lokaci, domin duk wanda ya yarda ya zama shugaba tun yana ƙaraminsa to alheri mai yawa zai wuce shi, kamar yadda Imam Shafi'i yake faɗa. Yana daga cikin abin da yake tiamaka wa ƙasƙantar da kai, don haka ka yi ƙoƙari a koyaushe ka riƙa jin kai ɗalibin ilimi ne, kuma zaka fa'idantu da kowa, wanda bai kai ba, da wanda yake sa'anka, da wanda yake samanka.

Sa'id ɗan Jubair – Allah ya yi masa rahama – yana cewa : "Mutum ba zai gushe ba yana malami matuƙar yana koyo, idan ya bar koyo, ya ji cewa shi ya wadatu da abin da ya sani to a lokacin ya fi zama jahili". (Tazkiratus Sami'i)

Da yawa daga cikin magabata suna fa'idantuwa da junansu, Imam Al – Humaidiy – Allah ya yi masa rahama – ɗalibin Imamu Ash – Shafi'i ne – ya ce "Na abokanci

Shafi'i daga Makka zuwa Misra, Ina ƙaruwa da shi a wasu mas'aloli, shi kuma yana ƙaruwa da ni a hadisi".

Imam Ahmad ɗan Hanbal – Allah ya yi masa rahama – ya ce, "Imam Shafi'i ya ce da mu, ku kun fi ni sanin hadisi, don haka idan hadisi ya inganta, to ku faɗa min don in yi aiki da shi".

Yaku 'yan uwana musulmi, ku nisanci jahilci, haƙiƙa jahili matacce ne tun kafin ya mutu, ku nemi ilimin addini, domin da shi ne duniya da lahira suke gyaruwa.

A ƙarshe ina kira ga duk wani mai kishin wannan addini na musulunci da waɗanda nauyi yake kansu da su gyara manhajar karatu, musamman ma a ɓangaren addini, saboda wallahi wannan manhajar ba zata yaye ɗalibai ba sai raunana, babu ilimin addini ingantacce a cikinsa, abin da yake cikinsa na cutarwa yana yawa, maffi munin abin da yake cikinsa kuwa wannan aƙida ta Ash'ariyya, wadda ta saɓa wa Alƙur'ani da sunnah da abin da magabata na ƙwarai suke kai, saboda haka ya wajaba akan masu kishin addini, da duk waɗanda suke da iko su gyara wannan tsarin, tun kafin lokaci ya wuce.

Ku ji tsoron Allah yaku bayin Allah, ku koyi addininku, kamar yadda ubangijinku ya umarce ku, ku sani aikin ibada ba ya karɓuwa har sai ya zama daidai kuma nagari, ba zai zama daidai nagari ba har sai an gina shi akan ilimi ingantacce.

DOGARO GA ALLAH

Manufofin huɗubar

- Bayanin ma'anar Tawakkali, da kuma mahimmancinsa ga mutum musulmi.
- Bayanin cewa, tawakkali wani ɓangare ne na imani.
- Bayanin a kan cewa, riƙo da sababai ba ya kore tawakkali.
- Haɗa zukatan bayi da Ubangijinsu, da bayani cewa, duk bayi masu buƙatuwa ne zuwa ga Allah.
- Jan-kunne a kan camfa wasu watanni ko kwanaki da wasu al'adu na jahiliyya waɗanda suke rushe tawakkali.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammadu bawansa ne manzonsa ne. (Yaku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron Allah yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Yaku waɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammadu (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (a addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta".

Bayan haka:

Ya ku 'yan uwa! Lallai neman arziki buƙata ce da Allah ya kimsa a cikin dukkan abubuwa masu rai, ba ɗan Adam kawai ba. Saboda haka, da zarar alfijir ya keto, za ka ga mutane suna shirye-shiryen tafiya wajen neman arziki, kama daga manoma, 'yan kasuwa, masu sana'o'in hannu, ma'aikata, kowa za ka ga yana ƙoƙari, yana fafutika wajen neman rufin asiri. Wahalar da hakan yake da shi, yakan sa ɗan Adam wani lokaci, ya bi karkatattun hanyoyi, don cin ma muradinsa. Sai dai, addinin musulunci, bai yarda da haka ba, bai yarda musulmi ya fake da ojoro da algus, ko wulaƙanta kai, ko zalunci, don ya samu abin da yake buƙata na tarkacen wannan duniya mai ƙarewa ba. To idan haka ne, ina mafita? Ina maganin

wannan bala’i na neman tara dukiya, ko ta wane hali da aka jarrabi wasu daga cikin mutanen da suke rayuwa kan wannan ƙwallon duniya tamu: Suna zaluntar junansu? Lallai mu sani- ya bayin Allah - mafita tana cikin dogaro ga Allah, mai arzutawa, mai bayarwa, wanda idan ya bayar, ba wanda ya isa ya hana, idan kuma ya hana, ba wanda ya isa ya bayar.

Wannan aƙida ta dogaro ga Allah, ita ce Manzon Allah (ﷺ) ya cusa a cikin zukatan sahabbansa, kamar yadda yake cewa, “Da za ku dogara ga Allah, gaskiyar dogaro da shi, da ya arzuta ku, kamar yadda yake arzuta tsuntsaye. Su fita da safe, cikinsu wayam, su dawo da yamma, cikinsu ya cika dam.” Hadisi ne ingantacce, Tirmizi da Ibn Majah ne suka ruwaito shi.

Allah akbar! Dogaro ga Allah, shi ne kaɗai ita ce mafita wajen samun yardar Allah. A neman arziki, mutum ya fita nema tare da cikakkiyar dogara ga Allah.

Ya ‘yan uwa! Ku duba ku ga yadda tsuntsaye suke yi: Su fita, alhali cikinsu wayam, amma su dawo cikinsu damdam, saboda tsabar dogaro ga Allah.

Ya ku ‘yan uwa! Lallai dogaro ga Allah, abu ne mai girma, kuma Allah ya umarci bayi baki ɗaya, da su dogara da shi, ko a wane irin yanayi suke. Allah yana cewa,

﴿ وَلِلَّهِ غَيۡبُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَإِلَيۡهِ يُرۡجَعُ ٱلۡأَمۡرُ كُلُّهُۥ فَٱعۡبُدۡهُ وَتَوَكَّلۡ عَلَيۡهِۚ وَمَا رَبُّكَ بِغَٰفِلٍ عَمَّا تَعۡمَلُونَ ١٢٣ ﴾ [هود: ١٢٣].

(Abin da ya ɓuya a sama da ƙasa na Allah ne, kuma gare shi ake mayar da al’amari baki ɗaya, don haka ka bauta masa shi kaɗai, kuma ka dogara da shi. Allah ba mai gafala ba ne game da abin da kuke aikatawa).

Kuma Allah yana ce wa Manzonsa (ﷺ),

﴿ وَتَوَكَّلۡ عَلَى ٱللَّهِۚ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ وَكِيلٗا ٣ ﴾ [الأحزاب: ٣].

(Ka dogara ga Allah. Allah ya isa abin dogaro a kai).

Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Wasu mutane za su shiga aljanna, zukatansu kamar zukatan tsuntsaye.”

Wato masu dogaro ga Allah, ko kuma sanyin rai.

Ya ku ‘yan uwa! Dogaro ga Allah iri biyu ne:

Na farko, dogaro ga Allah wajen samun buƙatun rayuwa, da abin duniya, ko ije wata musiba ko larura.

Na biyu, dogaro ga Allah wajen sanin abin da Allah yake ƙauna, kuma ya yarda da shi, na imani da yaƙini da jihadi da da’awa da makamancin haka. Kuma tsakanin waɗannan nau’i guda biyu, akwai fifiko da rata mai yawa. Duk sanda bawa ya dogara ga Allah, dogaro iri na biyu, to Allah zai isar wa bawa, dogaro irin na farko. Amma idan ya dogara na farko, ban da na biyu, to Allah zai isar masa, amma ba kamar irin na biyu ba. Don haka, tawakkalin da ya fi girma, shi ne dogaro ga Allah wajen neman shiriya, da tace tauhidi, da kaɗaita biyayya ga Manzon Allah (ﷺ). Kuma wannan shi ne dogaro da Allah irin wanda Annabawan Allah suka yi.

Ya ‘yan uwa! Ya kamata mu sani, mutum ya daina bin matakin da Allah ya tsara don faruwa, ko kuma samun wani abu, ba ya cikin dogaro ga Allah. Kamar mutum ya zauna, ba tare da ya tashi, ya nemi arziki ba, ya ce ya dogara ga Allah, idan Allah ya ƙaddara zai zama mawadaci, zai zama, ko da kuwa bai wahala ba. Wannan rashin fahimtar abin da ake ce wa dogaro ga Allah ne, da taɓewa, da asara. A nan, tilas ne mutum ya tashi, ya bi matakan da suka zama wajibi, don samun wani abu. Kamar yadda hadisi ya nuna, shi mai dogaro ga Allah, yana da sifa biyu: Ta farko, fafutikar neman abin da yake buƙata; na biyu, dogaro ga Allah, da sakankancewa a kan cewa Allah ne kaɗai mai bayarwa. Duk wanda ya rasa waɗannan siffofi guda biyu, to bai dogara ga Allah ba, kuma ya yi asara babba. Lallai dogaro ga Allah, shi ne matattarar imani.

Ya ku ‘yan uwa! Lallai abin mamaki ne ga mutumin da ya san yana da buƙata, ko da yaushe ga Allah, amma ya ƙi dogara da shi: Ya san ya matsu zuwa gare shi, amma ba ya neman taimakonsa; ya san komai yana hannunsa, amma ba ya nema daga gare shi; ya san cewa yana tsananin tausayin bayinsa, amma zuciyarsa ta ƙi nutsuwa da shi. Lallai bawa, ya kamata ka sa ni cewa, babu wani abu da za ka samu, sai ka wahala, kuma ka dogara ga Allah. Lallai duk wanda ya dogara ga Allah, ya ishe shi. Duk wanda ya nemi taimakonsa, ya ɗamfaru da shi, zai inganta masa addininsa da rayuwarsa. Duk wanda ya ruɗu da kansa, zuciyarsa ta katse daga mahaliccinsa, ya taɓe, ya gama yawo. Sau tari za ka ga marar galihu mai rauni ya dogara ga Allah, Allah ya ƙarfafe shi. Hakanan sau tari za ka ga wanda yake ji da ƙarfi ya dogara ga ƙarfinsa. Amma ƙarfin bai tsinana masa komai ba yayin da yake cikin matsananciyar buƙata. Babu sa'ada ga ɗan adam sai cikin bautar Allah ta'ala. Don haka shi ne gatansa shi ne mai taimakonsa.

Ya ku muminai, ku sani mumin ba shi da gata sai wajen Allah ta’ala, shi ne ƙarfinsa shi ne gatansa.

Allah yana cewa,

﴿ إِنَّمَا ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ٱلَّذِينَ إِذَا ذُكِرَ ٱللَّهُ وَجِلَتۡ قُلُوبُهُمۡ وَإِذَا تُلِيَتۡ عَلَيۡهِمۡ ءَايَٰتُهُۥ زَادَتۡهُمۡ إِيمَٰنٗا وَعَلَىٰ رَبِّهِمۡ يَتَوَكَّلُونَ ٢ ﴾ [الأنفال: ٢].

(Kaɗai dai, masu imani, su ne waɗanda idan aka ambaci Allah, zukatansu sukan ji tsoro, kuma idan aka karanta musu ayoyin, sai su ƙara musu ban-gaskiya, kuma ga Ubangijinsu shi kaɗai, suke dogaro).

Allah ya amfane mu da abin da muka ji, ya ba mu damar aiki da shi. Alhamdu lillaahi rabbil aalamiin….

Huɗuba Ta Biyu

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah. Tsira da amincin Allah su tabbata ga fiyayyen halitta Annabi Muhammad da alayensa da sahabbansa da waɗanda suka bi tafarkinsa suka yi koyi da sunnarsa, har zuwa tashin ƙiyama. Bayan haka:

Ya ‘yan uwa! Lallai tilas a kan bawa, ya bi matakai, amma ba zai dogara da su ba, sai dai ya dogara ga Ubangijinsu. Manzon Allah (ﷺ) ya fi kowa dogaro ga Allah, amma yana bin duk wani mataki da ya zama wajibi. Bari ma, Allah ne yake umartarsa, shi da sahabbai, da yin haka, kamar yadda Allah yake cewa,

﴿ وَأَعِدُّواْ لَهُم مَّا ٱسۡتَطَعۡتُم مِّن قُوَّةٖ وَمِن رِّبَاطِ ٱلۡخَيۡلِ تُرۡهِبُونَ بِهِۦ عَدُوَّ ٱللَّهِ وَعَدُوَّكُمۡ ﴾ [الأنفال: ٦٠].

(Ku yi tanadin abin da za ku iya, na ƙarfi da turkakkun dawaki, da za ku razana maƙiyan Allah kuma maƙiyanku da su).

Ya ku ‘yan uwa! Ya kamata ku sani, yana daga cikin abin da yake kore dogaro ga Allah, camfe-camfe, ko dai da ranaku da watanni, ko da dabbobi, ko tsuntsaye, ko kuma masu nakasa a jiki, kamar kutare, da tafiya wajen bokaye, da ‘yan tsibbu, da matsafa, da ‘yan duba, da makamantansu.

Ya ku ‘yan uwa! Ku sani, lallai dogaro ga Allah shi kaɗai, da fawwala al’amura zuwa gare shi, shi kaɗai, da ƙudurta cewa shi kaɗai ne yake amfanarwa ko cutarwa, da nesantar duk wani camfi, abubuwa ne da suka zama wajibi mutum ya ƙudurce a cikin zuciyarsa. Kamar yadda Allah ya ce,

﴿ وَإِن يَمۡسَسۡكَ ٱللَّهُ بِضُرّٖ فَلَا كَاشِفَ لَهُۥٓ إِلَّا هُوَۖ وَإِن يُرِدۡكَ بِخَيۡرٖ فَلَا رَآدَّ لِفَضۡلِهِۦۚ يُصِيبُ بِهِۦ مَن يَشَآءُ مِنۡ عِبَادِهِۦۚ وَهُوَ ٱلۡغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ١٠٧ ﴾ [يونس: ١٠٧].

(Idan Allah ya shafe ka da wata cuta, babu mai yaye ta, sai shi, idan kuma ya shafe ka da wani alheri, babu mai iya ture falalarsa. Yana samun wanda ya so daga cikin bayinsa da ita, kuma shi mai gafara ne, mai jin ƙai).

Kuma Allah ya ce,

﴿ قُل لَّا يَعۡلَمُ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ ٱلۡغَيۡبَ إِلَّا ٱللَّهُۚ ﴾ [النمل: ٦٥].

(Ka ce, “Ba wanda ya san gaibu cikin sama da ƙasa, sai Allah).

Ya ‘yan uwana a cikin addinin musulunci! Haƙiƙa Allah ya ɗaukaka wannan al’umma, kuma ya tsabtace ta daga dukkan dattin jahiliyya. Mu sani, ‘yan uwa, yana cikin raunin imani, da rashin dogaro ga Allah, abin da muke gani mutane suna aikatawa a yau. Ka ga wani ya gina rayuwarsa gabaɗaya a kan taurari da watanni: Idan tauraro kaza ya zo, akwai sa’a a ciki; idan wata kaza ya zo, ba sa’a a ciki. Kai ma, har ma a wata kaza, ba a yin aure ko tafiya. Lallai wannan yana daga cikin shirka. Allah ya kiyaye mu. Irin waɗannan mutane, sai ka rasa da wane addini suka yi imani. Kai sai ka ce, ina ma tunaninsu yake? Wane irin tunani suka yi? Waɗannan abubuwa da suke camfawa, su kansu ba za su iya amfanar da kansu ba, ko cutarwa, ballantana su amfanar da wani. Kuma Manzon Allah (ﷺ) ya faɗa a cikin hadisi, “Cuta ba ta yaɗuwa da kanta, ba camfi, ba ƙwanƙwami, ba camfi da watan Safar.”

Ya ‘yan uwa! Irin wannan faɗakarwa da ake yi, ba ana yi don komai ba ne, sai don nasiha ga bayin Allah, sai don yaɗuwar da waɗannan abubuwa suka yi a cikin al’umma, kuma sai don kada masu raunin imani su faɗa cikin waɗannan ƙazaman aƙidu, da ruɓaɓɓun al’adu. Kuma tilas ne malamai da ɗalibai, su tsaya tsaye wajen tsamo mutane daga cikin irin wannan ruɗu, da rashin nutsuwa na camfi, zuwa ga

kwanciyar hankali da nutsuwa ta addini da ingantacciyar aƙida. Allah yana cewa, ﴿ وَلَئِن سَأَلْتَهُم مَّنْ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ لَيَقُولُنَّ ٱللَّهُۚ قُلْ أَفَرَءَيْتُم مَّا تَدْعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ إِنْ أَرَادَنِىَ ٱللَّهُ بِضُرٍّ هَلْ هُنَّ كَٰشِفَٰتُ ضُرِّهِۦٓ أَوْ أَرَادَنِى بِرَحْمَةٍ هَلْ هُنَّ مُمْسِكَٰتُ رَحْمَتِهِۦۚ قُلْ حَسْبِىَ ٱللَّهُۖ عَلَيْهِ يَتَوَكَّلُ ٱلْمُتَوَكِّلُونَ ﴿٣٨﴾ ﴾ [الزمر: ٣٨].

(Ka ce, “Ku ba ni labari kan abin da kuke kira, koma-bayan Allah. Idan Allah ya nufe ni da wata cuta, shin su za su yaye cutarsa, ko kuwa idan ya nufe ni da jin ƙai, shin za su riƙe rahamarsa?” Ka ce, “Allah ya wadace ni, gare shi ne masu dogaro suke dogara).

HAƊARIN MUMMUNAR SHIGA GA ‘YA MACE MUSULMA

Manufofin huɗubar

- Bayanin yadda za a magance wannan matsalar.
- Umartar mata musulmai da su kame kansu.
- Toshe ƙofofin fitina da suka yaɗu a wannan zamani.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga shirrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammad bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Allah Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku waniɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammad (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Bayan haka:

Ya ku bayin Allah! Ku sani lallai yana daga cikin rahamar Allah ta’ala, da ya rufe wa bayinsa ƙofofin sharri, ya toshe duk wata ƙofa ta fitina, da saɓon Allah. Wanda duk ya buɗe wannan ƙofa kuwa, to zai faɗa cikin saɓon Allah da zunubi. Sannan kuma abu ne sananne ga kowanne mutum irin haɗarin da ƙasashen musulmi suka faɗa na fitsarar mata, da shiga ta rashin kunya da gujewa hijabi, da bayyana kwalliyarsu ga mazajen da ba nasu ba. Babu shakka wannan abu ne da yake jawowa al’umma fushin Allah da azabarsa idan ba su tashi sun gyara halinsu ba.

Ya ku jama’ar musulmi, ku yi aiki da umarnin Allah, ku tilastawa matanku kyakkyawar shiga, da sutura ta musulunci, wanda hakan zai sa su sami kuɓuta, ku ma ku kuɓuta. Allah ta’ala yana cewa:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ قُل لِّأَزۡوَٰجِكَ وَبَنَاتِكَ وَنِسَآءِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ يُدۡنِينَ عَلَيۡهِنَّ مِن جَلَٰبِيبِهِنَّۚ ذَٰلِكَ أَدۡنَىٰٓ أَن يُعۡرَفۡنَ فَلَا يُؤۡذَيۡنَۗ وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُورٗا رَّحِيمٗا ٥٩ ﴾ [الأحزاب: ٥٩].

(Ya kai wannan Annabi ka gayawa matanka da ‘ya’yanka mata, da matan muminai, su lulluɓe jikinsu da mayafansu, don da haka ne za a gane su, kuma ba za a cutar da su ba. Lallai Allah mai yawan gafara ne mai jinƙai).

A nan Allah ta’ala yana umartar mata musulmai da su lulluɓe jikinsu da sutura ta musulunci wato hijabi, ta haka ne za a gane cewa su mata ne kamammu. Ba za su fitini mutane ba da kyan da Allah ya yi musu, kuma su ma ba za a fitine su ba, ta hanyar maganar banza.

Don haka ku ji tsoron Allah ya ku musulmai. Ku hana wawayenku yin wauta. Kuma ku hana matanku aikata abin da Allah ya haramta. Ku umarce su da sanya hijabi da sutura ta musulunci, kuma ku tsoratar da su fushin Allah. Kamr yaddda ya tabbata a hadisi, Imam Ahmad da Abu Dawud da Tirmizi suka rawaito shi, daga Abubakar Siddiƙ (R.A), cewa manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: “Lallai idan mutane suka ga azzalumi yana zalunci, kuma ba su hana shi ba, to ba da daɗewa ba Allah zai lulluɓe su da uƙubarsa.” Allah ta’ala Ya faɗa a cikin littafinsa:

﴿ لُعِنَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنۢ بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ عَلَىٰ لِسَانِ دَاوُۥدَ وَعِيسَى ٱبۡنِ مَرۡيَمَۚ ذَٰلِكَ بِمَا عَصَواْ وَّكَانُواْ يَعۡتَدُونَ ٧٨ كَانُواْ لَا يَتَنَاهَوۡنَ عَن مُّنكَرٖ فَعَلُوهُۚ لَبِئۡسَ مَا كَانُواْ يَفۡعَلُونَ ٧٩ ﴾ [المائدة: ٧٨ – ٧٩].

(An la’anci waɗanda suka kafirta daga cikin Banu Isra’ila, a kan harshen Dawud da Isa ɗan Maryam saboda saɓo da suka yi, kuma sun kasance suna ƙetare iyaka. Sun kasance ba sa hana junasu wani mummunan aiki da suka aikata, lallai tir da abin da suka kasance suna aikatawa). Kuma ya tabbata a hadisi wanda Imamu Ahmad ya rawaito daga Abdullahi ɗan Mas’ud (R.A), Annabi (S.A.W), ya karanta wannan ayar sai ya ce: “Na rantse da wanda raina yake hannunsa, lallai ku yi umarni da kyakkyawan aiki, kuma lallai ku hana mummuna, kuma lallai ku tursasa shi ya bi gaskiya, idan ba haka ba kuwa, Ubangiji ya sassaɓa tsakanin zuciyarku kuma ya la’ance ku kamar yadda Ya la’ance su”. Kuma ya tabbata daga Annabi (S.A.W) ya ce: “Duk wanda ya ga mummunan abu to ya sauya shi da hannunsa, idan ba zai iya ba to ya sauya shi da harshensa, idan kuma ba zai iya ba to ya ƙi shi a zuciyarsa. Wannan shi ne mafi raunin imni”. Allah ta’ala ya umarci mata da zaman gida da daina yawace-yawacen shirme, Ya hana su karairaya murya ga mazajen da ba nasu ba, domin yin haka yana jawo fitina da ɓarna. Allah ta’ala ya ce:

﴿ يَٰنِسَآءَ ٱلنَّبِيِّ لَسۡتُنَّ كَأَحَدٖ مِّنَ ٱلنِّسَآءِۚ إِنِ ٱتَّقَيۡتُنَّ فَلَا تَخۡضَعۡنَ بِٱلۡقَوۡلِ فَيَطۡمَعَ ٱلَّذِي فِي قَلۡبِهِۦ مَرَضٞ وَقُلۡنَ قَوۡلٗا مَّعۡرُوفٗا ٣٢ وَقَرۡنَ فِي بُيُوتِكُنَّ وَلَا تَبَرَّجۡنَ تَبَرُّجَ ٱلۡجَٰهِلِيَّةِ ٱلۡأُولَىٰۖ وَأَقِمۡنَ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتِينَ ٱلزَّكَوٰةَ وَأَطِعۡنَ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥٓۚ ﴾ [الأحزاب: ٣٢ - ٣٣].

(Ya ku matan Annabi, ba daidai kuke da kowacce mace ba, idan kun ji tsoron Allah, don haka kada ku karairaya murya wajen magana sai wanda yake da cuta a cikin zuciyarsa ya yi kwaɗayi. Kuma ku yi maganar da ta dace. Kuma ku zauna a cikin gidajenku kada ku yi tamɓele irin tamɓelen jahiliyyar farko, kuma ku bi Allah da manzonsa) .

A cikin waɗannan ayoyi masu girma Allah ta’ala ya yi hani ga matan Annabi, iyayen muminai waɗanda su suka fi kowacce mace tsarkaka, da kada su karairaya muryarsu yayin magana ga mazajen da ba nasu ba, domin kada su ba wa wani mai mugun nufi dama har ya nemi maganar banza da su. Kuma ya umarce su da su zanuna a gidajensu kada su dinga caɓa ado suna bi gwadabe-gwadabe kamar matan jahiliyya na farko, domin yin haka shi yake haddasa zinace-zinace a cikin al’umma. To idan har Allah ta’ala zai faɗawa matan Annabi iyayen muminai wannan maganar, ya ja kunnensu a wannan aya, tare da girman imaninsu da falalarsu da ɗaukakarsu, to kuwa babu shakka sauran mata muminai su ne suka fi cancanta a yi wa irin wannan gargaɗi. Kuma Allah ta’ala ya ce:

﴿وَإِذَا سَأَلْتُمُوهُنَّ مَتَٰعًا فَسْـَٔلُوهُنَّ مِن وَرَآءِ حِجَابٍ ۚ ذَٰلِكُمْ أَطْهَرُ لِقُلُوبِكُمْ وَقُلُوبِهِنَّ ۚ﴾ [الأحزاب: ٥٣].

(Kuma idan za ku tambaye su wani abin amfani, to ku tambaye su ta bayan shamaki, yin haka shi ya fi tsarki ga zukatanku da kuma zukatansu).

Wannan aya ta fito ƙarara ta nuna wajabicin mata su tsare kansu daga mazajen da ba nasu ba. Ta kuma nuna cewa yin haka shi zai magance aukuwar fitina tsakanin maza da mata.

Ya ku bayin Allah lallai hijabin mace yana da sharuɗɗai guda takwas. Ga su kamar haka:

Ya rufe dukkani jikin ‘ya mace, domin faɗar Allah da yake cewa su lulluɓe jikinsu da mayafansu.

Kada ya hijabin ya kasance shi karankansa kwalliya ne, wato a yi masa ado da launi iri-iri ko kayan ado na musamman ta yadda zai dinga jan hankalin maza. Allah ta’ala yana cewa:

﴿وَلَا يُبْدِينَ زِينَتَهُنَّ إِلَّا مَا ظَهَرَ مِنْهَا ۖ﴾ [النور: ٣١].

(Kuma kada su bayyana adonsu, sai dai abin da ya riga ya bayyan).

Ma’anar abin da ya riga ya bayyana shi ne, adon da ya riga ya bayyana ba da gangan ba. Don haka, duk hijabi mai kwalliya to ba hijabi ba ne a musulunci.

1. Ya kasance mai kauri ba shara-shara ba, yadda zai riga nuna jikin mace. Hadisi ya tabbata daga Abu Huraira, (R.A) cewa, manzon Allah (S.A.W) ya ce; “Wasu mutane kala biyu ‘yan wuta ne, ban caɓa ganinsu ba, na farko wasu mutane a ɗauke da bulalai, tamkar jelar shanu, za su riƙa dukan mutane da su, da kuma wasu mata sanye da tufafi amma tsirara suke, masu tafiya suna karairaya, suna rangaji, kawunansu kai ka ce tozon raƙuma ne masu rangaji. Faufau ba za su shiga aljanna ba, ba za su taɓa jin ƙanshita ba, ga shi kuwa ƙamshinta a na jiyo shi daga tafiya mai tsawon kaza da kaza”.

   Duk matar da za ta yi shigar da ba za ta rufe mata jikinta ba, kuma a na ganin gashin kanta a waje, ko a na ganin ƙwaurinta a fili, to irin waɗanan mata ko su suna ganin sun sanya sutura, to tsirara suke yawo. Kuma an la’ance su, ba kuma za su shiga aljanna ba.
2. Sharaɗi na haɗu: Hijabin ya zama burmeme mai faɗi, ba matsattse ba, wanda zai riƙa nuna hoton dirin mace ba. An karɓo hadisi daga ɗan Usama ɗan Zaid, ya ce, mahaifinsa Usama ya ce: “Manzon Allah (S.A.W) ya sanya min wata

tufa mai kauri, wadda Dihya Alkalbi ya ba shi kyauta. Sai ni kuma na ba wa matata ta sa. Sai manzon Allah (S.A.W) ya ce: “Me ya hana kai ba ka sa ta ba?” Sai na ce, matata na ba wa take sawa. Sai Annabi (S.A.W.) ya ce, “To ka umarce ta ta sa wata rigar a ƙasanta, domin ina jin tsoron ta riƙa nuna dirinta”. Imam Ahmad ne ya rawaito shi.

3. Kada hijabin ya zamana yana ƙanshin turare, saboda hadisai masu yawa da suka tabbata daga Manzo (S.A.W), yana hana mata fita suna ƙanshin turare. An karɓo daga Abu Musa al-Ash’ari (R.A) ya ce, Manzon Allah (S.A.W), ya ce, duk matar da ta sa turare ta wuce ta gaban maza don su ji ƙanshinta, to karuwa ce”. Nasa’i da Ɗan Kuzaimah da Ɗan Hibban ne suka rawaito.
4. Kada ya yi kama da tufafin maza. An karɓo hadisi daga Abu Huraira, (R.A) ya ce, Manzon Allah (S.A.W), ya la’anci namijin da yake shigar mata, da kuma macen da take shigar maza. Abu Dawud ne da Nasa’i suka rawaito shi.
5. Sharaɗi na bakwai shi ne, kada ya yi kama da tufafin kafirai mata. Saboda a ƙa’idar shari’a ba ya halatta ga mace ko namiji su kwaikwayi shiga irin ta kafirai a lokutan ibadojinsu, ko kuma a lokutan idinsu, ko a suturunsu na yau da gobe. An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (R.A), ya ce, manzon Allah (S.A.W), ya ce, “Duk wanda ya yi kama da wasu mutane to yana daga cikinsu. Imam Ahmad ne ya rawaito shi. Don haka ba ya dacewa ga ‘ya mace ta riƙa yawo kanti-kanti da kaya irin na kafiran kasashen yamma don yin kwalliya da irinsu.
6. Sharaɗi na takwas, kada ya zama sutura ce ta shuhura. Ita ce duk wata shiga da mutum zai yi domin ya shahara da ita a gurin mutane. An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (R.A) ya ce, manzon Allah (S.A.W) ya ce, “Duk wanda ya sanya taguwar shuhura a nan duniya, Ubangiji zai sanya masa taguwar ƙasƙanci rana goɓe alƙiyama, sannan ya babbaka shi da wuta.” Abu Dawud ne da Ibn Majah suka rawaito shi.

Don haka, wajibi ne ga kowanne musulmi ya ga cewa, hijabin matarsa da na ‘ya’yansa mata sun cika waɗannan sharuɗɗan, domin faɗar ma’aiki (S.A.W) “Dukkaninku masu kiwo ne, kuma kowannenku za a tambaye shi game da abin kiwonsa”.

Kuma Allah ta’ala yana cewa:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ قُوٓاْ أَنفُسَكُمۡ وَأَهۡلِيكُمۡ نَارٗا وَقُودُهَا ٱلنَّاسُ وَٱلۡحِجَارَةُ عَلَيۡهَا مَلَٰٓئِكَةٌ غِلَاظٞ شِدَادٞ لَّا يَعۡصُونَ ٱللَّهَ مَآ أَمَرَهُمۡ وَيَفۡعَلُونَ مَا يُؤۡمَرُونَ ٦ ﴾ [التحريم: ٦].

(Ya ku waɗanda suka yi imani ku tsare kawunanku da iyalanku daga shiga wuta, mutane da duwatsu ne makamashinta. Mala’ikun da suke tsaronta mala’iku ne masu kaushin zuciya, ƙarfafa, ba sa saɓawa Allah a abin da ya umarce su, kuma suna aikata abin da ya sa su).

Hakan nan, wajibi ne ga bawa ya ji tsoron Ubangijinsa, ya kiyayi saɓa masa, Allah ta’ala yana cewa:

﴿ قُل لِّلۡمُؤۡمِنِينَ يَغُضُّواْ مِنۡ أَبۡصَٰرِهِمۡ وَيَحۡفَظُواْ فُرُوجَهُمۡۚ ذَٰلِكَ أَزۡكَىٰ لَهُمۡۗ إِنَّ ٱللَّهَ خَبِيرُۢ بِمَا يَصۡنَعُونَ ٣٠ وَقُل لِّلۡمُؤۡمِنَٰتِ يَغۡضُضۡنَ مِنۡ أَبۡصَٰرِهِنَّ وَيَحۡفَظۡنَ فُرُوجَهُنَّ وَلَا يُبۡدِينَ زِينَتَهُنَّ إِلَّا مَا ظَهَرَ مِنۡهَاۖ وَلۡيَضۡرِبۡنَ بِخُمُرِهِنَّ عَلَىٰ جُيُوبِهِنَّۖ ﴾

[النور: ٣٠ – ٣١]

(Kuma ka gaya wa muminai maza su kame ganinsu, kuma su kiyaye farjinsu, wannan shi ne ya fi tsaki gare su, lallai Allah mai yawan sani ne ga abin da suka aikatawa. Kuma ka gayawa muminai mata su kame ganinsu su kuma kiyaye farjinansu kada su bayyana adonsu ai abin da ya bayyana. Su rufe ƙirajansu da lulluɓinsu).

Ina nemawa kaina tare da ku da sauran muminai gafarar Allah daga kowanne zunubi, don haka ku nemi gafararsa, lallai shi mai yawan gafara ne mai jinƙai.

Huɗuba Ta Biyu

Dukkan yabo da kirari sun tabbata ga Ubangijin talikai, kuma kyakkyawan ƙarshe yana ga masu tsorn Allah. Babu ta’addanci sai a kan azzalumai. Tsirada amincin Allah su tabbata ga fiyayyen halitta bakiɗaya, Annabinmu Muhammad da alayensa da sahabbansa, waɗanda suka bi tafarkinsa har zuwa tashin ƙiyama.

Bayan haka, ya ku bayin Allah, abu ne da kowa ya sani irin yadda mata a yau suke caɓa kwalliya da shiga irin ta fitsara da rashin kunya da sa matsattsun kaya, masu fito da al’aura. Suna yawo da su tsakanin mazaje. Al’amarin da yake haddasa fitintunu iri-iri da fasadi kala-kala a cikin al’umma. Haka nan yana daga cikin abubuwan da ke jawo fasadi, shi ne keɓantar namiji da matar da muharramarsa ba. Alhali hadisi ya tabbata daga Abu Sa’idul Kudri (R.A) ya ce, Manzon Allah (S.A.W), ya ce: “Ba ya halatta ga macen da ta yi imani da Allah da ranar lahira, ta yi bilaguron mai tafiyar kwana uku ko fiya, face suna tare da maharraminta; babanta ko ɗan’uwanta, ko mijinta, ko kuma ɗanta, ko kuma kowane ɗaya daga muharramanta”. Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.

Kuma Imamu Ahmad da Tirmizi da Hakim sun ruwaito hadisi cewa, Manzon Allah (S.A.W.) ya ce, “Babu wani mutum da zai kaɗaita da wani mace, face shaiɗan ne na ukunsu”.

Ya ku Musulmi ku ji tsoron Allah, ku hana matanku shiga ta fitsara da watangaririya a cikin gari, da nuna kwalliya da tsiraici. Ku hana shiga irin ta maƙiya Allah, Nasara da Yahudu, da masu kwaikwayonsu. Ku sani cewa, rashin magana a kan wannan sha’ani daidai yake da aikata, don haka idan uƙubar Allah ta sauka, za ta shafi kowa da kowa. Allah ya tsare mu.

Ya ku musulmi! Babu shakka cewa, nauyin da yake kan shugabanni da alƙalai da malamai, da shugabannin ƙungiyoyi, ba ƙarami ba ne. Ya ɗara nauyin da yake kan wasu, kuma haɗarin da yake cikin rashin maganar a kan wannan batu ba ƙaramin haɗari ne ba. Duk da cewa, ya kamata a sani ba su kaɗai ke da alhakin yin magana da tsawatarwa a kan wannan lamari ba. A’a, duk wani musulmi yana da

ruwa da tsaki cikin fafutukar ganin an kawar da irin waɗannan laifuka. Musamman dattawa da manyan gari, da iyayen matan su kansu, da mazajensu na aure. Dole ne duk a tashi tsaye wajen jan-kunne mai tsanani ga duk wacce za ta nemi yaɗa irin wannan fasadi. Idan mun yi haka, to muna sa ran Allah zai yaye mana bala'in da muke ciki, ya shiryar da mu tare da matanmu daidaitaccen tafarki.

Ya ke 'yar uwa musulma. Ki ji tsoron Allah, ki komo kan hanya, tun gabanin ranar ƙin dillanci ba ta zo ba, ranar da ido zai rena fata. Ki sani azabar Allah mai tsanani ce. Kuma duniya ba matabbata ce ba. Ki kiyayi jin kunyar lahira gaban halittun farko da na ƙarshe.

Allah ya datar da mu gabaɗaya ga abin da yake so kuma ya yarda da shi. Kuma muna roƙon Allah ya kare mana 'yan matan muslmi daga kaidin masu kaidi, da dakon masu mugun nufi. Ka sanya su daga cikin mata salihai, masu koyi da salihan mata na gari, masu guje wa duk wata ɓarna, masu aiki da Alƙurani da Hadisan Ma'aiki (S.A.W.).

Tsarki ya tabbata ga Ubangijinka, Ubangiji mai izza ga barin abin da suke siffantawa. Kuma aminci ya tabbata ga Manzanni, kuma yabo da godiya da kirari su tabbata ga Allah Ubangijin halittu.

Bin Iyaye Da Barin Saɓa Musu

Manufofin huɗubar

- Umarni da bin iyaye da falalarsa a addinin musulunci.
- Umarni da kyautata wa iyaye koda kafirai.
- Bayanin yadda ake bin iyaye da kyautata musu.
- Jan – kunne kan saɓawa iyaye.
- Bayyana makomar saɓawar iyaye.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga shirrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammad bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammad (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Bayan haka : ‘Yan uwana musulmi a yau zamu tattauna ne akan wani al’amari mai girma, haƙƙi ne da Allah ya haɗa haƙƙinsa da shi a wurare da dama a cikin Alƙur’ani mai girma, kuma babu tsira ko rabauta ga wanda duk ya tozarta wannan haƙƙi, wannan haƙƙi kuwa shi ne haƙƙin iyaye.

Haƙƙin iyaye a musulunci, haƙƙi ne mai girma, saboda haka ma Allah Maɗaukakin Sarki ya haɗa shi da haƙƙinsa a wurare da dama a cikin alƙur’ani mai girma, kamar faɗin Allah :

﴿ وَٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ وَلَا تُشۡرِكُواْ بِهِۦ شَيۡـٔٗاۖ وَبِٱلۡوَٰلِدَيۡنِ إِحۡسَٰنٗا وَبِذِي ٱلۡقُرۡبَىٰ وَٱلۡيَتَٰمَىٰ وَٱلۡمَسَٰكِينِ ﴾

[النساء: ٣٦].

Ma’ana : (Ku bauta wa Allah kada ku yi shirka da shi da wani abu, sannan ku kyautata wa iyaye da makusanta da marayu da Miskinai) (Annisa’i: 36).

Da faɗinsa :

﴿ وَقَضَىٰ رَبُّكَ أَلَّا تَعۡبُدُوٓاْ إِلَّآ إِيَّاهُ وَبِٱلۡوَٰلِدَيۡنِ إِحۡسَٰنًاۚ ﴾ [الإسراء : ٢٣].

Ma’ana : “Ubangijinka ya hukunta kada ku bauta wa kowa sai shi kaɗai, kuma a kyautata wa iyaye) (Al- Isra’i : 23).

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas’ud – Allah ya yarda da shi – ya ce, na tambayi Manzon Allah (ﷺ) na ce, “wane aiki ne Allah ya fi so?” sai ya ce, “Sallah akan lokacinta” sai na ce, “Sannan me?” sai ya ce, “Bin iyaye” sai na ce, “Sannan me?” sai ya ce, “Jihadi a kan tafarkin Allah”. Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

An sake karɓo wa daga gare shi – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Yardar Allah tana tare da yardar iyaye, fushin Allah yana tare da fushin iyaye”. Tirmizi da Ibnu Hibban suka rawaito.

Waɗannan ayoyi da hadisai suna tabbatar mana da wajabcin bin iyaye da kyautata musu.

Ya uwana musulmi : Haƙƙin iyaye yana dauwama ko da iyayen sun mutu, kamar yadda yake ba ya saraya koda iyayen kafirai ne, wajibi ne ɗa ya yi musu biyayya da abu mai kyau, wanda ba saɓon Allah ba. Allah Maɗaukakin Sarki ya ce :

﴿ وَوَصَّيۡنَا ٱلۡإِنسَٰنَ بِوَٰلِدَيۡهِ حَمَلَتۡهُ أُمُّهُۥ وَهۡنًا عَلَىٰ وَهۡنٖ وَفِصَٰلُهُۥ فِي عَامَيۡنِ أَنِ ٱشۡكُرۡ لِي وَلِوَٰلِدَيۡكَ إِلَيَّ ٱلۡمَصِيرُ ١٤ وَإِن جَٰهَدَاكَ عَلَىٰٓ أَن تُشۡرِكَ بِي مَا لَيۡسَ لَكَ بِهِۦ عِلۡمٞ فَلَا تُطِعۡهُمَاۖ وَصَاحِبۡهُمَا فِي ٱلدُّنۡيَا مَعۡرُوفٗاۖ وَٱتَّبِعۡ سَبِيلَ مَنۡ أَنَابَ إِلَيَّۚ ثُمَّ إِلَيَّ مَرۡجِعُكُمۡ فَأُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ١٥ ﴾ [لقمان: ١٤ – ١٥].

Ma’ana : “Mun yi wa mutum wasiyya da iyayensa, mahaifiyarsa ta ɗauke shi rauni akan rauni, ɗaukan cikinsa da yaye shi shekaru biyu, ka gode min da iyayenka, gareni makoma take. Idan suka tilastaka a kan ka yi shirka da ni cikin abin da baka ilimi a kai, kada ka bi su, ka zauna da su a duniya da kyakkyawa, ka bi hanyar wanda ya mayar da lamarinsa gareni, gareni makomarku take, sai in baku labarin abin da kuke aikatawa”. (Luƙman : 14).

Sannan an karɓo daga Asma’u ‘yar Abubakar – Allah ya ƙara mata yarda – ta ce, mahaifiyata ta zo wajena ziyara a lokacin tana arniya bata musulunta ba, sai na tambayi Annabi (ﷺ) na ce masa : “Mahaifiyata ta zo wajena tana son (ganina) ko (ya halatta) in sada zumuncinta?” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Eh, ki sada zumuncinta” (ma’ana ki tarbeta, ki ba ta masauki). Bukhari ne ya rawaito.

Bin iyaye da kyautata musu yana daga cikin manya – manyan ayyukan da suke kusantar da mutum ga Allah Maɗaukakin Sarki, kuma dalili ne da yake sa Allah ya yaye wa mutum musiba da bala’i, kamar yadda labarin mutanen nan guda uku da suka shiga kogo dutse ya rufe su take nuna wa, yayin da suka cewa junansu “kowa ya yi kamun ƙafa a wurin Allah da wani aiki na alheri da ya yi, ko Allah ya fitar da mu daga cikin wannan musiba” nan da nan ɗayansu ya yi kamun ƙafa a wurin Allah da barin wani aikin saɓo da ya yi, sai dutsen ya ɗan buɗe kaɗan. Na biyun ma ya yi kamun ƙafa da kiyaye amana da ya yi, sai dutsen ya ƙara buɗe wa kaɗan. Na ukun shi kuma ya yi kamun ƙafa da bin iyayensa da yake yi, ya ce, “Ya Allah!, haƙiƙa ni na kasasance ina tare da iyayena tsofaffi guda biyu, da mata ta da ‘ya ‘yana, ina yi wa iyayena kiwon dabbobi, idan na tafi kiwo na tatso nonon dabbobin

nan, ina fara bawa iyayena su sha, sannan in bawa iyalina, sai wata rana na yi nisa wurin kiwo, ban dawo ba sai da yamma, na sami iyayen nan nawa sun yi barci, na tatsi nonon nan kamar yadda na saba, na zo da shi, na tsaya a kansu ina jiran su farka in fara ba su, domin ba na son in tashe su daga barcin da suke yi, kuma ba na son in fara bawa 'ya 'yana kafin in ba su. Haka na tsaya ina jiransu' 'ya'yana suna ta kuka a kusa da ni, amma ban ba su ba, har sai da asuba ta yi, iyayena suka farka na fara ba su, sannan na bawa 'ya'yana. Ya Allah idan na yi wannan don neman yardarka ka buɗe mana ƙofa, sai Allah ya buɗe musu ƙofa har suka riƙa ganin sama,suka fito suka ci gaba da tafiya".

A wannan hadisi mai girma za mu ga yadda wannan bawan Allah ya yi kamun ƙafa da bin iyayensa, kuma Allah ya yaye masa halin ƙunci da yake ciki.

Ya 'yan uwana musulmi : Yana daga cikin haƙƙin iyaye a kan ɗansu ya sassauta musu magana, ya yi musu magana mai daɗi, ya ciyar dasu, ya tufartar dasu idan faƙirai ne, saboda Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa:

﴿ إِمَّا يَبْلُغَنَّ عِندَكَ ٱلْكِبَرَ أَحَدُهُمَآ أَوْ كِلَاهُمَا فَلَا تَقُل لَّهُمَآ أُفٍّ وَلَا تَنْهَرْهُمَا وَقُل لَّهُمَا قَوْلًا كَرِيمًا ﴿٢٣﴾ وَٱخْفِضْ لَهُمَا جَنَاحَ ٱلذُّلِّ مِنَ ٱلرَّحْمَةِ وَقُل رَّبِّ ٱرْحَمْهُمَا كَمَا رَبَّيَانِى صَغِيرًا ﴿٢٤﴾ ﴾

[الإسراء: ٢٣ - ٢٤].

Ma'ana : "Idan ɗayansu ko kuma su duka biyun suka tsufa tare da kai, to kada ka ce musu tir, kada ka yi musu tsawa, ka faɗa musu magana mai girma (mai daɗi). Ka sassauta musu fika – fikan rahama, ka ce ya Ubangiji ka yi musu rahama kamar yadda suka rene ni ina ƙarami". (Al – Isra'i : 23 – 24).

Hakanan yana daga cikin haƙƙinsu ya sada zumuncinsu da zumuncin abokansu, domin ya inganta cewa Abdullahi ɗan Umar – Allah ya yarda da shi – yana da jaki da yake hawa idan ya gaji da hawan raƙumi, kuma yana da wani rawani da yake ɗaure kansa da shi. Wata rana yana tafiya akan wannan jakin a cikin garin Makkah, sai wani mutumin ƙauye ya wuce ta kusa da shi, sai Abdullahi ɗan Umar ya cewa mutumin ƙauyen nan, "Ashe ba kai ne wane ɗan wane ba?" ya ce, "Ni ne" sai Abdullahi ɗan Umar ya bashi jakin nan ya ce, "hau, ga kuma rawani ka sanya a kanka". Sai wasu daga cikin Abokan Abdullahi ɗan Umar suka ce, "Allah gafarta malam, mun ga ka baiwa wannan mutumin ƙauyen jakinka da kake hutawa a kansa, da rawaninka da kake ɗaure kanka da shi, ya ya haka?". Sai ya ce musu : "Saboda ni na ji Manzon Allah (ﷺ) yana cewa : "Yana cikin mafi kyan aikin alherin mutum ya sada zumuncin waɗanda mahaifinsa yake son su bayan ya mutu. To baban wannan mutumin ƙauyen abokin Umar ne (mahaifina). Muslim ne ya rawaito wannan hadisi.

Allahu Akbar!. 'Yan uwa ku duba ku ga yadda Abdullahi ɗan Umar ya girmama ɗan abokin mahaifinsa, saboda waccan hadisi da ya ji a wajen Manzon Allah (ﷺ) to a yau me waɗanda suke cin mutuncin iyayensu za su faɗa wa Allah a gobe ƙiyama!, idan ya zamana ɗan abokin mahaifinka ka girmama shi, ina ga Abokin mahaifinka, to kuma ina ga mahaifanka!!.

'Ya 'yan uwana musulmi : Magabatanmu na ƙwarai sun buga kyawawan

misalai a wajen bin iyayensu.

Muhammad ɗan Sireen – Allah ya yi masa rahama – ya kasance idan mahaifiyarsa tana magana sai ya ƙasƙantar da kansa ya yi shiru.

Ibnu Auf – Allah ya yi masa rahama – ya ce, : Wani mutum ya shigo wajen Muhammad ɗan sireen a lokacin yana gaban mahaifiyarsa, sai wannan mutumin ya ce, “me ya sami Muhammad ne, ko bai da lafiya ne?” sai suka ce masa : “a’a, haka yake idan yana gaban mahifiyarsa”.

Aliyu ɗan Aliyu ɗan Husain jikan Manzon Allah (ﷺ) – Allah ya yi masa rahama – yana ɗaya daga cikin manya – manyan tabi’ai, ya kasance mai tsananin biyayya ga mahaifiyarsa, har wata rana aka ce da shi, “kana tsananin bin mahaifiyarka, har ma mun ga ba ka iya cin abinci tare da ita a kwano ɗaya”, sai ya ce musu : “ina tsoron kada in kai hannuna kan wani abin da ta yi sha’awa a abincin, in zama na saɓa mata”.

Hakanan Imam Haywa ɗan Shuraih – ɗaya daga cikin manya – manyan malaman tabi’ai – ya kasance idan yana zaune yana bada karatu, mahaifiyarsa ta kira shi, ta ce ya je ya ba kaji abinci, sai ya tashi da gaggawa ya bar almajiransa a zaune.

Waɗannan kaɗan kenan daga cikin misalan yadda magabata na ƙwarai suke bin iyayensu, to a yau me yasa matasanmu suke sakaci da bin iyayensu, har ka samu a cikinsu wanda yake saɓawa iyayensa saboda kawai ya samu yardar abokinsa!,

Saboda haka ina muku wasiyya – yaku yara – da ku yi wa iyayenku wasiyya, ku yi ƙoƙarin samun yardarsu da sanya musu farin ciki duniya da lahira, ka sani ya kai ɗan uwa me mahifinka yake buƙata a wajenka fiye da ka tsaya kusa da shi yayin da yake buƙatar hakan, ka taimake shi a lokacin da yake son taimakon, ba fa wani abu da mahaifiyaka take so a wajenka fiye da kalmar tausaya wa, da magana mai daɗi da so da girmamawa. Allah mai girma da buwaya yana cewa :

﴿ وَقَضَىٰ رَبُّكَ أَلَّا تَعْبُدُوٓاْ إِلَّآ إِيَّاهُ وَبِٱلْوَٰلِدَيْنِ إِحْسَٰنًا ۚ إِمَّا يَبْلُغَنَّ عِندَكَ ٱلْكِبَرَ أَحَدُهُمَآ أَوْ كِلَاهُمَا فَلَا تَقُل لَّهُمَآ أُفٍّ وَلَا تَنْهَرْهُمَا وَقُل لَّهُمَا قَوْلًا كَرِيمًا ﴿٢٣﴾ وَٱخْفِضْ لَهُمَا جَنَاحَ ٱلذُّلِّ مِنَ ٱلرَّحْمَةِ وَقُل رَّبِّ ٱرْحَمْهُمَا كَمَا رَبَّيَانِى صَغِيرًا ﴿٢٤﴾ ﴾ [الإسراء: ٢٣ - ٢٤].

Ma’ana : “Ubangijinka ya hukunta kada ku bauta wa kowa sai shi kaɗai, kuma a kyautata wa iyaye. Idan ɗayansu ko kuma su duka biyun suka tsufa tare da kai, to kada ka ce musu tir, kada ka yi musu tsawa, ka faɗa musu magana mai girma (mai daɗi). Ka sassauta musu fika – fikan rahama, ka ce ya Ubangiji ka yi musu rahama kamar yadda suka rene ni ina ƙarami”. (Al – Isra’i : 23 – 24).

Allah ya yi mana albarka cikin abin da muka ji, na alƙur’ani da hadisi, haƙiƙa Allah mai iko ne akan dukkan komai.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah, Kyakkyawan ƙarshe yana ga masu tsoron Allah, Tsira da Aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, Manzon Allah (ﷺ) da iyalansa

da Sahabbansa da waɗanda suka bi su gaba ɗayansu, har zuwa ranar sakamako. Bayan haka:

Yaku ‘yan uwana musulmi : Saɓa wa iyaye yana daga cikin manya – manyan zunubai, waɗanda suke jefa mutum cikin wutar Jahannama.

An karɓo daga Abu Bakrata – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Ba na baku labarin mafi girman zunubai ba? Ya faɗi haka har sau uku. Sai muka ce “Bamu labari ya Rasulallahi” Sai Manzon Allah ya ce, “Shirka da Allah, saɓawa iyaye..” Bukhari da Muslim.

Hakanan An karɓo daga Abdulallahi ɗan Umar – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Mutane uku Allah ba zai kalle su ba ranar alƙiyama, Mai saɓa wa iyayensa, da mai dauwama akan shan giya, da mai gori”. Nasa’i ne ya rawaito shi.

Yana daga cikin haɗarin saɓawa iyaye Allah Maɗaukakin Sarki yana gaggauta azabarsa tun a nan duniya kafin lahira, Manzon Allah (ﷺ) yana cewa : “Babu wani zunubi da ya cancanta Allah ya gaggauta wa mai yinsa uƙuba a duniya, haɗe da abin da aka tanadar masa na azaba a lahira, irin ƙetare iyaka (zaluntar wani) da saɓa wa iyaye” Imamu Ahmad ne ya rawaito.

Yana cikin saɓawa iyaye ɗaga murya sama da ta su, da yanke musu magana idan suna yi, da yi musu tsawa, da tilasta su a kan wani abin da basu yi niyya ba, da yi musu mummunan kallo na wulaƙanci, kamar yana kallon maƙiyinsa da ɗaya daga cikin 'ya'yansa da yake yi wa tsawa.

Yana cikin saɓa wa iyaye jinkirta biya musu buƙata, da ja musu rai har su gaji da tambaya su haƙura. Allah yana cewa :

﴿ فَلَا تَقُل لَّهُمَآ أُفٍّ وَلَا تَنۡهَرۡهُمَا وَقُل لَّهُمَا قَوۡلٗا كَرِيمٗا ﴾ [الإسراء: ٢٣].

Ma’ana : “ Kada ka ce musu tir, kada ka yi musu tsawa, ka faɗa musu magana mai girma (mai daɗi).”

Ku ji tsoron Allah – Yaku bayin Allah – ku kiyayi saɓawa iyaye, ku guji gabatar da wasu akan iyaye, saboda babu wani zunubi da Allah yake gaggauta azabarsa kamar saɓawa iyaye, kuma abin da mutum ya yi shi za a yi masa.

An samu wani mutum da ya ɗauki babansa tsoho ya tafi da shi can cikin sahara, cikin daji, sai uban ya ce wa ɗan “Ya kai ɗana ina zaka da ni ne? sai ɗan ya ce, “Ai na gaji da zama da kai ne” sai uban ya ce, “to me zaka yi min yanzu?” sai ya ce, “Ina so in yanka ka ne!!?” sai uban nan ya ce wa ɗansa “idan kuwa haka ne, to matsa da ni wajen wanncan dutsen?” sai ɗan ya ce, “A! saboda me?” sai uban ya ce, “Saboda ni ma a can na kashe nawa mahaifin a wajen wancan dutsen, don haka nima ka kashe ni a can, kuma kai ma zaka samu cikin ‘ya ‘yanka wanda zai kashe ka a nan!!”. Haka sakamako yake irin abin da aka aikata.

Don haka wajibi ne a kanmu – Musulmi – mu yi wa iyayenmu biyayya kamar yadda Allah ya yi umarni, mu kyautata musu daidai gwargwadon ikonmu, da haka ne zamu samu rabauta a duniya da lahira.

Umarni Da Kyakkyawan Aiki Da Hani Daga Mummuna

Manufofin huɗubar

- Bayyana ma’anar Umarni da kyakkyawan aiki da hani ga Mummuna.
- Tsoratarwa daga Baƙin halaye munana.
- bayanin matakan hana mummunan aiki.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga shirrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammad bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammad (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Ya ku bayin Allah! A yau huɗubarmu tana magana ne akan wani babban al’amari, wanda Allah Maɗaukakin Sarki ya umarce mu da shi, kuma yana daga cikin mafi girman aikin Annabawa da Manzanni, dashi ne Allah ya sanya wannan al’umma ta zama mafi alherin al’ummun da aka fitar wa mutane, wannan lamari ba komai ba ne face umarni da kyakkyawan aiki da hani daga mummuna.

Umarni da kyakkyawan aiki yana nufin umarni da abin da Allah da Manzonsa (S.A.W) suke so, da abin da shari’a ta yarda da kyansa, Hani daga mummunan aiki kuwa yana nufin hana abin da Allah da Manzonsa suka hana, kuma shari'a ta bayyana muninsa.

Allah Maɗaukakin Sarki ya umarci bayinsa da umarni da kyakkyawan aiki, da hani da mummuna inda yake cewa :

﴿ وَلۡتَكُن مِّنكُمۡ أُمَّةٞ يَدۡعُونَ إِلَى ٱلۡخَيۡرِ وَيَأۡمُرُونَ بِٱلۡمَعۡرُوفِ وَيَنۡهَوۡنَ عَنِ ٱلۡمُنكَرِۚ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُفۡلِحُونَ ١٠٤ ﴾ [آل عمران : ١٠٤].

Ma’ana : “A samu wasu jama’a daga cikinku suna kira zuwa ga alheri sannan suna umarni da kyakkyawan aiki kuma suna hana mummunan aiki, waɗannan sune waɗanda suka rabauta” (Ali – Imaran: 104).

A wani wurin Allah Maɗaukakin Sarki ya bayyana cewa wannan alumma ita ce mafi alherin al’ummun da aka samar a cikin mutune, saboda umarninta da kyakkyawan aiki da hani daga mummunan aiki, Allah ya ce :

﴿ كُنتُمۡ خَيۡرَ أُمَّةٍ أُخۡرِجَتۡ لِلنَّاسِ تَأۡمُرُونَ بِٱلۡمَعۡرُوفِ وَتَنۡهَوۡنَ عَنِ ٱلۡمُنكَرِ وَتُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِۗ ﴾

[آل عمران: ١١٠].

Ma’ana : “Kun kasance mafiya alherin al’umma da aka fitar wa da mutane, kuna umarni da kyakkyawan aiki kuma kuna hana mummunan aiki, sannan kuna yin imani da Allah) (Al- Imaran : 110).

Manzon Allah (S.A.W) ya bayyana mana cewa umarni da kyakkyawan aiki da hana mummunan aiki wajibi ne na shari’a, da shi ne al’umma take tsira daga azabar Allah, An karɓo daga Huzaifa ɗan Yamani – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (S.A.W) ya ce, “Na rantse da wanda raina yake hannunsa, ko dai ku yi umarni da kyakkyawan aiki, ku hana mummunan aiki, ko kuma kuna kusa da Allah ya aiko da azaba a kanku, uƙuba daga gare shi, sannan ku roƙe shi ba za a amsa muku ba” Tirmizi ne ya rawaito shi, ya ce, “Hadisi ne mai kyau”.

Haka nan an karɓo daga Nu’uman ɗan Bashir – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (S.A.W) ya ce, “Misalin wanda yake kula da iyakokin Allah (ba ya afka wa cikinsu) da wanda yake faɗa wa cikinsu, kamar mutane ne suka yi kuri’a wajen hawan jirgin ruwa, sai wasu suka samu damar hawa saman jirgin, wasu kuma suka samu ƙasa, sai wanda suke ƙasa idan za su sha ruwa sukan wuce ta wajan waɗanda suke zaune a sama, (sai waɗannan na ƙasan suka ce) me zai hana mu fasa wajenmu (wato ƙasa) ba sai mu cutar da na samanmu ba (wajen zuwa shan ruwa). To idan (na saman) suka ƙyale su suka yi abin suka yi niyya (na fasa jirgin) sai su halaka gaba ɗaya, idan kuwa suka hana su to zai su tsira su da su gaba ɗaya”. Bukhari ne ya rawaito wannan hadisi.

Yaku ‘yan uwa musulmi : babu addini ga mutumin da zai ga iyakokin Allah ana keta su ba tare da ya hana ba, Imam Ibnul Kayyim – Allah ya yi masa rahama – yana cewa : «Wana irin addini ne da alheri ga wanda zai ga abubuwan da Allah ya haramta ana keta su, iyakokin Allah ana tozarta su, addinin Allah ana barinsa, sunnar Annabi (S.A.W) ana ƙin ta, amma zuciyar da kwance sanyi ƙalau, harshensa ya yi shiru, haƙiƙa duk wanda yake haka to wannan shaiɗan ne kurma, kamar wanda yake faɗin ɓarna yake shaiɗan mai magana. Shin akwai wani bala’i a addini face yana fitowa daga irin waɗannan, waɗanda idan abincinsu da shugabancinsu sun kuɓuta, to ba ruwansu da abin da ya faru ga addini. Zaɓaɓɓe a cikin irin waɗannan mutane shi ne wanda yake yin ɗan fushi. Amma da za a taɓa ɗaya daga cikin irin waɗannan mutane akan dukiyarsa ko matsayinsa, da ka ga yadda zai yi ta kai –

kawo, ya kashe dukiyarsa, ya yi duk wani ƙoƙarinsa, ya bi dukkan matakan nan da ake bi na hana mummunan aiki guda uku iya bakin ƙoƙarinsa, to irin waɗannan mutane - haɗe da rasa ƙima da daraja da suka yi a wajen Allah, da gamuwa da fushinsa – an jarrabe su a nan duniya da babban bala'i, shi ne mutuwar zuciya, domin kuwa duk lokacin da zuciya ta zama rayayya, to lokacin ne ta fi yin fushi don Allah da Manzonsa, kuma tafi taimakon addini".

Yana daga cikin abin da yake nuna mahammancin wannan aiki – yaku bayin Allah - yana ɗaya daga cikin manya – manya al'amura, kuma yana kare al'umma daga halaka, sannan sharaɗi ne daga sharuɗɗan da Allah yake tabbatar da bayinsa ya ba su nasara a bayan ƙasa da shi, Allah ya ce – yana mai yabon bayinsa muminai - :

﴿ ٱلَّذِينَ إِن مَّكَّنَّٰهُمْ فِي ٱلْأَرْضِ أَقَامُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتَوُا۟ ٱلزَّكَوٰةَ وَأَمَرُوا۟ بِٱلْمَعْرُوفِ وَنَهَوْا۟ عَنِ ٱلْمُنكَرِ ﴾ [الحج: ٤١].

Ma'ana : "waɗanda idan muka tabbatar da su a bayan ƙasa sai su tsaida sallah, su bada zakka, su yi umarni da kyakkyawan aiki su hana mummuna" (Hajji : 41)

Allah Subhanahu Wa Ta'ala ya ce a wani wurin daban :

﴿ فَلَوْلَا كَانَ مِنَ ٱلْقُرُونِ مِن قَبْلِكُمْ أُو۟لُوا۟ بَقِيَّةٍ يَنْهَوْنَ عَنِ ٱلْفَسَادِ فِى ٱلْأَرْضِ إِلَّا قَلِيلًا مِّمَّنْ أَنجَيْنَا مِنْهُمْ ۗ وَٱتَّبَعَ ٱلَّذِينَ ظَلَمُوا۟ مَآ أُتْرِفُوا۟ فِيهِ وَكَانُوا۟ مُجْرِمِينَ ﴿١١٦﴾ ﴾ [هود: ١١٦].

Ma'ana : "Ba don waɗanda suka rage a cikin ƙarnonin da suka gabata ba, suna hana ɓarna a bayan ƙasa, sai dai ƙaɗan daga cikin waɗanda muka tseratar daga cikinsu, waɗanda suka yi zalunci suka bi abin da aka jiyar da su na daɗi suka zama masu laifi". (Hud : 116)

A wani wurin a Alƙur'ani Allah ya nuna ba ya halakar da al'umma matuƙar akwai masu wa'azi a cikinta. Ya ce,

﴿ وَمَا كَانَ رَبُّكَ لِيُهْلِكَ ٱلْقُرَىٰ بِظُلْمٍ وَأَهْلُهَا مُصْلِحُونَ ﴿١١٧﴾ ﴾ [هود: ١١٧].

Ma'ana : "Ba zai yiwu ba Ubangijinka ya halakar da Alƙarya alhali mutanenta suna yin gyara". (Hud : 117).

Yaku masu sauraro : Haƙiƙa a cikin watsi da wannan aiki akwai haɗari mai girma, da mummunan sakamako a kan ɗaiɗaikun mutane da al'umma, domin kuwa Allah ya yi alƙawarin azaba akan duk waɗanda suka ba da baya, suka ƙi wannan aiki, suka yi sakaci da shi.

An karɓo daga Huzaifa ɗan Yamani – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (S.A.W) ya ce, "Na rantse da wanda raina yake hannunsa, ko dai ku yi umarni da kyakkyawan aiki, ku hana mummunan aiki, ko ya kusata Allah ya aiko da azaba a kanku, uƙuba daga gare shi, sannan ku roƙe shi ba za a amsa muku ba" Tirmizi ne ya rawaito shi

An karɓo daga Zainab matar Annabi (S.A.W) ta ce, "Ya Manzon Allah yanzu za a iya halaka mu alhali a cikinmu akwai mutanen ƙwarai?" Sai Manzon Allah ya ce mata : "Kwarai kuwa, idan laifi ya yawaita".

Allah Maɗaukakin Sarki kuma ya tsine wa Bani Isra'il yayin da suka bar umarni

da kyakkyawan aiki da hana mummuna. Allah ya ce :

﴿ لُعِنَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنۢ بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ عَلَىٰ لِسَانِ دَاوُۥدَ وَعِيسَى ٱبۡنِ مَرۡيَمَۚ ذَٰلِكَ بِمَا عَصَواْ وَّكَانُواْ يَعۡتَدُونَ ٧٨ ﴾ [المائدة: ٧٨]

Ma’ana : “An tsine wa waɗanda suka kafirta daga cikin bani Isra’il akan harshen Dawud da Isa ɗan Maryam, saboda abin da suka yi na saɓo kuma sun kasance suna ƙetare iyaka. Sannan sun kasance ba sa hana duk wani mummunan aikin da suka aikata, tir da abin da suka kasance suna aikatawa”. (Ma’ida : 78).

Yaku musulmi : Kafin mutum ya canza mummunan aiki ya wajaba a kansa ya lura da waɗannan abubuwa masu zuwa :

1. Ya zama abin da za a hana ɗin, abu ne da shari’a ce ta hana shi, kada ka hana abin da Allah ya yi umarni da shi, ko ya halatta wa bayinsa, babu wani abin ƙi sai wanda shari’a ta ƙi shi, ta hana shi.
2. Ya zama abin da zai hana ɗin akwai shi, (ba wai zato ake yi cewa za a iya yin kaza ba), kada ka hana abin da babu shi.
3. Ya zama abin ƙin ya fito fili daga wajen mai aikatawa, ba bin didddigi aka yi ba don gano abin, saboda Allah ya hana bin diddigin mutane.
4. kada ya zama abin da zai hana yana cikin mas’alolin da malamai suka yi ijtihadi a cikinsu, abubuwan da nassi a cikinsu, ko kuma akwai nassi ɗin amma ɓoyayye ne ba a fili yake ba.

Waɗanda sune abubuwan da ya kamata mai hani ga mummunan aiki ya kula da su yayin da yake wannan aiki.

Allah ya ce :

﴿ وَلۡتَكُن مِّنكُمۡ أُمَّةٞ يَدۡعُونَ إِلَى ٱلۡخَيۡرِ وَيَأۡمُرُونَ بِٱلۡمَعۡرُوفِ وَيَنۡهَوۡنَ عَنِ ٱلۡمُنكَرِۚ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُفۡلِحُونَ ١٠٤ ﴾ [آل عمران: ١٠٤].

Ma’ana : “A samu wasu jama’a daga cikinku suna kira zuwa ga alheri sannan suna umarni da kyakkyawan aiki kuma suna hana mummunan aiki, waɗannan sune waɗanda suka rabauta” (Ali – Imaran : 104).

Allah Maɗaukakin Sarki ya yi mana albarka a cikin abin da muka ji na ayoyi da hadisai, domin shi mai iko ne akan dukkan komai.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah, Kyakkyawan ƙarshe yana ga masu tsoron Allah, Tsira da Aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, Manzon Allah (S.A.W) da iyalansa da Sahabbansa da waɗanda suka bi su gaba ɗayansu, har zuwa ranar sakamako. Bayan haka:

Yaku ‘yan uwa musulmi : Canza mummunan aiki yana da matakai waɗanda Manzon Allah (S.A.W) ya bayyana su a cikin hadisin da Imam Muslim ya rawaito daga Abu Sa’id Al-khuduriy – Allah ya yarda da shi –, ya ce, na ji Manzon Allah (S.A.W) yana cewa : “Duk wanda ya ga mummuna abu daga cikinku, to ya canza shi da hannunsa, idan ba zai iya ba, to da harshensa, idan ba zai iya ba, to da

zuciyarsa (wato ya ƙi abun) wannan shi ne mafi raunin imani".

Hakanan Manzon Allah (S.A.W) ya ƙara fito da waɗannan matakai a fili a cikin hadisin Abdullahi ɗan Mas'ud – Allah ya yarda shi – ya ce, Manzon Allah (S.A.W) ya ce : "Babu wani Annabi da Allah ya aiko shi gabanina face yana da tatattun mabiya daga cikin al'ummarsa, da sahabbai da suke riƙo da sunnarshi, suna koyi da umarninsa, sannan sai wasu su biyo bayansu, suna faɗin abin da ba sa aikata wa, suna aikata abin da ba a umarce su ba, duk wanda ya yi jihadi a kansu da hannunsa to wannan mumini ne, wanda ya yi jihadi a kansu da harshensa wannan ma mumini ne, wanda ya yi jihadi a kansu da zuciyarsa shi ma mumini ne. Amma bayan wannan to babu wani imani ko da daidai da ƙwayar zarra" (muslim ne ya rawaito).

Babban Malamin nan Ibnu – Kayyim yana cewa : "Haƙiƙa Annabi (S.A.W) ya shar'anta wa al'ummarsa wajabcin hana mummunan aiki, saboda a samu abin da Allah da Manzonsa suke so, amma idan hana mummnan aiki zai kawo samuwar abin da ya fi shi muni, yafi shi zama abin ƙi a wajen Allah da Manzonsa to ba ya dacewa a hana wannan mummunan aikin, duk da cewa Allah ba ya son wannan aiki, kuma ba ya son masu yin sa. Misalin irin wannan kuwa kamar inkari ga masu mulki ta hanyar fito – na – fito da tawaye gare su, saboda hakan shi ne asalin duk wata fitina da sharri. Sahabbai sun nemi izinin Manzon Allah (S.A.W) wajen yaƙar shugabannin da suke jinkirta sallah ga barin lokacinta, suka ce "Ba ma yaƙe su ba?" Sai Manzon Allah (S.A.W) ya ce : "A'a matuƙar dai suna yin sallah" sannan ya ce, "Duk wanda ya ga wani abin ƙi daga shugabansa to ya yi haƙuri, kada ya cire hannunsa daga yi masa ɗa'a".

Ya ci gaba da cewa : "Duk wanda ya lura da abin da ya gudana na manya da ƙananan fititntinu a cikin musulunci zai ga barin wannan asali (na bin shugabanni) shi ne asalinta, da rashin haƙuri a kan wani mummunan abu, sai aka nemi kawar da shi, sai hakan ya haifar da aikin da ya fi shi muni. Manzon Allah (S.A.W) ya kasance yana ganin abin ƙi a Makkah amma ba zai iya kawar da su, har ma lokacin da Allah ya bashi damar buɗe Makka da mayar da ita garin musulunci ya yi niyyar ya canza ɗakin ka'aba ya mayar da shi akan ginin Annabi Ibrahim, amma tsoron abin da zai faru wanda ya fi wannan girma ya hana shi yin hakan, duk da yana da ikon yi ɗin, saboda zai yiwu Kuraishawa ba za su iya ɗaukar hakan ba, saboda sababbin shiga musulunci ne, wannan ya sa ma Manzon Allah (S.A.W) bai yi umarni da amfani da hannu wajen inkari ga shugabanni ba, saboda abin da zai iya faruwa wanda ya fi abin da suke kai muni. Hana mummunan aiki yana da matakan huɗu :

1. Kodai mummunan aikin ya gushe, kishiyarsa (aikin alheri) ya maye gurbinsa.
2. ko kuma mummunan aikin ya yi ƙaranci, koda bai gushe gaba ɗaya ba.
3. ko kuma ya gushe gaba ɗaya, wani mummunan abu irinsa ya maye gurbinsa.
4. ko kuma wanda yafi shi sharri da muni ya maye gurbinsa.

To a mataki na ɗaya da na biyu an shar'anta (a kawar da mummunan aiki a cikinsu), na uku kuwa sai a duba a ga abin da ya dace, amma mataki na huɗu

haramun ne a (kawar da mummunan aiki a wannan yanayi). (Duba littafin I'ilamul Muwaƙƙien).

'Yan uwa musulmi : Ku sani cewa mai umarni da aiki kyakkyawa sharaɗi ne a samu waɗannan sharuɗɗai a tare da shi:

1. Ya zama musulmi mai tsoron Allah.
2. Ya zama balagagge, domin umarni da kyakkyawan aiki da hani ga mummuna ba ya wajaba akan yaro ƙarami.
3. Ya zama mai adalci, kuma mai ilimi, musamman ma akan abin da zai umarta ko ya hana ɗin.
4. Ya zama zai iya yin umarnin da hanin, saboda iko wajen yin abu shi ne abin da yake kawo a ɗora wa mutum aiki.

Ku ji tsoron Allah bayin Allah, ku yi abin da ya wajabta muku shi na umarni da aiki mai kyau, da hana mummunan aiki, sai ku rabauta, ku nisanci kawar da kai daga barin wannan aiki mai girma, saboda kawar da kai ga barin wannan aikin yana jawo sharri da ɓarna ga al'umma da ƙasa gaba ɗaya. Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa :

﴿ فَلَوۡلَا كَانَ مِنَ ٱلۡقُرُونِ مِن قَبۡلِكُمۡ أُوْلُواْ بَقِيَّةٖ يَنۡهَوۡنَ عَنِ ٱلۡفَسَادِ فِي ٱلۡأَرۡضِ إِلَّا قَلِيلٗا مِّمَّنۡ أَنجَيۡنَا مِنۡهُمۡۗ وَٱتَّبَعَ ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ مَآ أُتۡرِفُواْ فِيهِ وَكَانُواْ مُجۡرِمِينَ ١١٦ ﴾ [هود: ١١٦].

Ma'ana : "Ba don waɗanda suka rage a cikin ƙarnonin da suka gabata ba, suna hana ɓarna a bayan ƙasa, sai dai ƙaɗan daga cikin waɗanda muka tseratar daga cikinsu, waɗanda suka yi zalunci suka bi abin da aka jiyar da su na daɗi suka zama masu laifi". (Hud : 116).

Ina roƙon Allah Ta'ala ya yi mana gafara, ya sanya mu cikin waɗanda suke umarni da kyakkyawan aiki suke hana mummuna. Haƙiƙa Allah Mai iko ne akan komai.

RAYUWA BAYAN MUTUWA

Manufofin huɗubar

- Abin da zai kasance bayan mutuwa na al'amuran ranar alƙiyama.
- Zaburarwa a kan kyawawan ayyuka da tsoratarwa ga barin munanan ayyuka.
- Kira i zuwa gaggauta tuba kafin lokaci ya ƙurewa ɗan adam.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammadu bawansa ne manzonsa ne. (Yaku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron Allah yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Yaku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammadu (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (a addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta".

Bayan haka: Ya ku bayin Allah!

Da yawa daga cikin mutane suna zaton idan sun mutu aka binne su shi ke nan rayuwa ta ƙare daga nan. Wannan fahimta an gina ta a kan kuskure babba kuma mummuna. Mutum bayan ya mutu yana shiga wata sabuwar rayuwa. Akwai rayuwa ta zaman ƙabari, da rayuwa ta bayan hisabi. Za mu ɗan yi tsokaci a cikin littafin Allah da Hadisai ingantattu a kan wannan al'amari. Tare da fito da al'amarin a fili na abin da zai kasance bayan mutuwa.

Idan mutum ya mutu, an binne shi, farkon rayuwar da zai fara fuskanta shi ne fitinar ƙabari.

Hadisi ya tabbata a cikin Bukhari da Muslim daga Anas ɗan Malik, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Idan baya ya mutu an sa shi a cikin ƙabarinsa yana jin motsin takalman waɗanda suka kawo shi. Sai mala'iku biyu su zo masa. Sai su zaunar da shi, su ce masa, "Me za ka ce dangane da wannan mutum? To mumini sai ya ce, "Na shaida haƙiƙa shi bawan Allah ne, kuma manzonsa ne". Sai a ce da shi kalli

mazauninka na wuta, amma yanzu Allah ya sauya maka shi da gida a aljanna". Sannan duk zai gansu a lokaci ɗaya.

Katada ya ce, Manzon Allah ya ce: "Za a buɗe masa ƙabarinsa tsawon zira'i saba'in za a ce da kafiri, ko munafiƙi, "Me za ka ce dangane da wannan mutum?" Sai ya ce, "Kawai ni ma ina faɗar abin da na ji mutane suna faɗa". Za a ce masa, "Ba ka sani ba, kuma ba ka karanta ba. Sai a doke shi da wata guduma ta ƙarfe, zai yi wata ƙara mai ƙarfi duk wanda yake wajen zai ji ta, in ban da mutum da aljan".

An karɓo daga Abu Ayyub ya ce, "Wata rana manzon Allah ya fito bayan rana ta faɗi, sai ya ji wata murya, sai ya ce: "Yahudawa ne ake gana musu azaba a ƙabari". Bukhari da Muslim ne suka ruwaito.

Shi ya sa a kowanne lokaci Manzon Allah (ﷺ) ya yi salla sai ya nemi tsari daga azabar ƙabari. Kuma ya umarci al'ummarsa da yin hakan.

Sannan bayan haka, sai a shiga yiwa kafiri da munafiki azaba. Shi kuma mumini a sa shi cikin ni'ima. Don haka bawa wace irin amsa ka tanadarwa wannan rana. Domin kuma rana ce da babu makawa sai ta zo.

Bayan haka kuma sai Allah ya tayar da duk waɗanda suka mutu daga ƙaburburansu. Shi ya sa Allah Yake cewa:

﴿ أَوَلَمۡ يَرَ ٱلۡإِنسَٰنُ أَنَّا خَلَقۡنَٰهُ مِن نُّطۡفَةٖ فَإِذَا هُوَ خَصِيمٞ مُّبِينٞ ٧٧ وَضَرَبَ لَنَا مَثَلٗا وَنَسِيَ خَلۡقَهُۥۖ قَالَ مَن يُحۡيِ ٱلۡعِظَٰمَ وَهِيَ رَمِيمٞ ٧٨ قُلۡ يُحۡيِيهَا ٱلَّذِيٓ أَنشَأَهَآ أَوَّلَ مَرَّةٖۖ وَهُوَ بِكُلِّ خَلۡقٍ عَلِيمٌ ٧٩ ﴾ [يس: ٧٧ – ٧٩].

(Shin mutum baya gani ne mun halicce shi daga ɗugon miniyyi amma sai ga shi ya zama mai bayyana husuma. Mutum ya buga mana misali ya manta halittarsa, ya ce, «Wane ne zai raya ƙasusuwa alhalin sun rititтike?». Ka ce, «Wanda ya ƙagi halittarsu a farko shi ne zai raya su. Kuma shi masani ne ga dukkan halitta).

Sannan daga nan sai Allah ya tara halittu duka don yin hisaba, kamar yadda ya ce:

﴿ وَلَقَدۡ جِئۡتُمُونَا فُرَٰدَىٰ كَمَا خَلَقۡنَٰكُمۡ أَوَّلَ مَرَّةٖ وَتَرَكۡتُم مَّا خَوَّلۡنَٰكُمۡ وَرَآءَ ظُهُورِكُمۡۖ وَمَا نَرَىٰ مَعَكُمۡ شُفَعَآءَكُمُ ٱلَّذِينَ زَعَمۡتُمۡ أَنَّهُمۡ فِيكُمۡ شُرَكَٰٓؤُاْۚ لَقَد تَّقَطَّعَ بَيۡنَكُمۡ وَضَلَّ عَنكُم مَّا كُنتُمۡ تَزۡعُمُونَ ٩٤ ﴾ [الأنعام: ٩٤].

Haƙiƙa kun dawo mana kuna ɗaiɗaikunku, kamar yadda muka halicce ku a farko karo. Kuma kun bar duk abin da muka hore muku a can bayanku Kuma duk waɗanda kuke riyawa cewa za su cece ku ba mu gan su ba tare da ku. Babu wata alaƙa da ta rage a tsakaninku. Abin da kuke riyawa shi ne mai cetonku ya ɓace muku ba kwa ganinsa).

Sannan Allah zai ta shi kafirai akan fuskokinsu. Duk sun makance, su zama kurame kuma bebaye. Allah ya ce:

﴿ وَنَحۡشُرُهُمۡ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ عَلَىٰ وُجُوهِهِمۡ عُمۡيٗا وَبُكۡمٗا وَصُمّٗاۖ مَّأۡوَىٰهُمۡ جَهَنَّمُۖ كُلَّمَا خَبَتۡ زِدۡنَٰهُمۡ سَعِيرٗا ٩٧ ﴾ [الإسراء: ٩٧].

Ma'ana: (Za mu tattara su a ranar ƙiyama a kan fuskokinsu suna makafi, kuma bebaye, kuma kurame. Makomarsu jahannama ce, duk sa'adda ta mutu sai mu ƙara rura musu ita).

A wannan lokaci ne mai cike da ban tsoro za ka ga kafirai da munafukai suna masu ƙanƙan da kai, idanuwansu sun zazzaro, babu wani mai magana sai fa wanda

Allah ya ba shi dama. Zukatansu sun zama fanko. Allah yana cewa:

﴿ وَلَا تَحْسَبَنَّ ٱللَّهَ غَٰفِلًا عَمَّا يَعْمَلُ ٱلظَّٰلِمُونَ ۚ إِنَّمَا يُؤَخِّرُهُمْ لِيَوْمٍ تَشْخَصُ فِيهِ ٱلْأَبْصَٰرُ ﴿٤٢﴾ مُهْطِعِينَ مُقْنِعِي رُءُوسِهِمْ لَا يَرْتَدُّ إِلَيْهِمْ طَرْفُهُمْ ۖ وَأَفْـِٔدَتُهُمْ هَوَآءٌ ﴿٤٣﴾ ﴾ [إبراهيم: ٤٢ – ٤٣].

(Kada ka yi tammanin cewa, Allah ya gafala da abin da azzalumai suke aikatawa. Kawai yana musu jinkiri ne domin wata rana da idanuwa za su zazzaro. Suna masu gaggawa, suna ɗaga kawunansu. Idanuwansu ba sa ƙiftawa. Kuma zukatansu duk sun zama iska).

Hakanan yana cewa:

﴿ يَوْمَ يَقُومُ ٱلرُّوحُ وَٱلْمَلَٰٓئِكَةُ صَفًّا ۖ لَّا يَتَكَلَّمُونَ إِلَّا مَنْ أَذِنَ لَهُ ٱلرَّحْمَٰنُ وَقَالَ صَوَابًا ﴿٣٨﴾ ﴾ [النبأ: ٣٨].

(Ranar da Mala'ika Jibrila zai tsaya, tare da mala'iku sahu-sahu. Ba sa iya magana sai wanda Allah Mai rahama ya yi masa izini, kuma ya faɗi maganar da take daidai).

Zukata a rannan za su zo maƙoshi, suna cike da tashin hankali. Azzalumai a wannan rana ba su da wani mai cetonsu, ko wani abokin arzuki da za a saurare shi. Tsawon wannan rana ya kai tsawon shekara hamsin na lissafin duniya.

An karɓo daga Abi Hurairata ya ce, manzon Allah ya ce: "Mutane za su yi gumi ranar alƙiyama wasu har yakan kai tsawon zira'i saba'in a ƙasa, wasu kuma gumin ya yi mus linzami har zuwa kunnuwansu". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

Yaku bayin Allah!

Daga wannan lokaci kuma sai a taho da ba yi zuwa ga Allah, babu wani abu da zai ɗoye wa masa. Allah yana cewa:

﴿ يَوْمَئِذٍ يَصْدُرُ ٱلنَّاسُ أَشْتَاتًا لِّيُرَوْا۟ أَعْمَٰلَهُمْ ﴿٦﴾ ﴾ [الزلزلة: ٦].

(A wannan yini ne mutane za su fito daban-daban, don a nuna musu ayyukansu).

Sai kuma a fara hisabi, Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: "Za a zo da kafiri ranar ƙiyama a ce masa inda kana da kwatankwacin duniyar nan na zinari za ka iya ba da shi ka fanshi kawunanka? Sai ya ce, "Na'am". Sai Allah ya ce, "An tambaye ka abin da bai kai haka ba ba ka bayar ba".

A wata riwayar: "Na neme ka da abin da ya fi wannan sauƙi a lokacin da kake cikin tsatson Adam, cewa, kada ka haɗa komai da ni, amma ka ƙi sai da ka yi shirka". Bukhari da Muslim ne suka ruwaito.

Ya zo a hadisi cewa: "Babu wani daga cikinku face Allah ya yi masa magana shi da shi, ba tare da tafinta ba. Mutum zai kalli damansa ba abin da zai gani sai abin da ya aikta. Haka zai sake kallon hagunsa ba zai ga komai ba sai abin da ya aikata. Sannan ya kalli gabansa ba abin da zai gani sai wuta tana ci. Don haka ku ji tsoron shiga wuta ko da da tsagin dabino ne, ko kuma da kyakkyawar kalma". Bukhari da Ibn Majah ne suka rawaito.

Sanan daga nan ne sai a ba za takardun ayyuka, Allah yana cewa:

﴿ وَوُضِعَ ٱلْكِتَٰبُ فَتَرَى ٱلْمُجْرِمِينَ مُشْفِقِينَ مِمَّا فِيهِ وَيَقُولُونَ يَٰوَيْلَتَنَا مَالِ هَٰذَا ٱلْكِتَٰبِ لَا يُغَادِرُ صَغِيرَةً وَلَا كَبِيرَةً إِلَّآ أَحْصَىٰهَا ۚ وَوَجَدُوا۟ مَا عَمِلُوا۟ حَاضِرًا ۗ وَلَا يَظْلِمُ رَبُّكَ أَحَدًا ﴿٤٩﴾ ﴾ [الكهف: ٤٩].

Ma’ana: (Kuma za a aje littafi, a wannan lokaci za ka ga masu laifi a tsorace saboda halin da suke ciki. Kuma suna cewa, “Ya kaiconmu, wanene irin littafi ne wannan? Ba ya barin ƙaramin laifi da babba sai ya lissafa su. Kuma suka samu abin da suka aikata a halarce. Kuma Ubangijin ba zai zalunci wani ba).

To fa a nan ne mutane za su kasu kashi biyu, wasu za su karɓi littafinsu da dama, wasu za su karɓa da hagu.

﴿ فَأَمَّا مَنْ أُوتِيَ كِتَٰبَهُۥ بِيَمِينِهِۦ فَيَقُولُ هَآؤُمُ ٱقْرَءُوا۟ كِتَٰبِيَهْ ﴿١٩﴾ إِنِّى ظَنَنتُ أَنِّى مُلَٰقٍ حِسَابِيَهْ ﴿٢٠﴾ فَهُوَ فِى عِيشَةٍ رَّاضِيَةٍ ﴿٢١﴾ فِى جَنَّةٍ عَالِيَةٍ ﴿٢٢﴾ قُطُوفُهَا دَانِيَةٌ ﴿٢٣﴾ كُلُوا۟ وَٱشْرَبُوا۟ هَنِيٓـًٔۢا بِمَآ أَسْلَفْتُمْ فِى ٱلْأَيَّامِ ٱلْخَالِيَةِ ﴿٢٤﴾ وَأَمَّا مَنْ أُوتِيَ كِتَٰبَهُۥ بِشِمَالِهِۦ فَيَقُولُ يَٰلَيْتَنِى لَمْ أُوتَ كِتَٰبِيَهْ ﴿٢٥﴾ وَلَمْ أَدْرِ مَا حِسَابِيَهْ ﴿٢٦﴾ يَٰلَيْتَهَا كَانَتِ ٱلْقَاضِيَةَ ﴿٢٧﴾ مَآ أَغْنَىٰ عَنِّى مَالِيَهْ ﴿٢٨﴾ هَلَكَ عَنِّى سُلْطَٰنِيَهْ ﴿٢٩﴾ ﴾ [الحاقة: ١٩ - ٢٩].

(Duk wanda aka ba shi littafinsa da hannun damarsa zai ce, ku karɓi littafina ku karanta. Ni da na tabbatar da cewa, zan gamu da hisabina. To shi yana cikin rayuwa yardadda. Yana cikin aljannah maɗaukakiya. ‘ya’yan itatuwanta dab-da-dab suke. Ku ci ku sha kuna masu jin daɗi saboda abin da kuka aikata a kwanakinku da suka shuɗe. Amma kuma wanda aka ba shi littafinsa a hannunsa na hagu, sai ya ce, ya kaico na ina ma ba a ba ni littafi na ba. Kuma ban san menene hisabi na ba. Ina ma mutuwa ta gama da ni. Dukiyata ba ta wadatar da ni komai ba. Ikona ya ɓace mini).

Sannan Allah Zai yi umarni a sanya mizani domin auna ayyukan bayi.

Allah yana cewa:

﴿ وَنَضَعُ ٱلْمَوَٰزِينَ ٱلْقِسْطَ لِيَوْمِ ٱلْقِيَٰمَةِ فَلَا تُظْلَمُ نَفْسٌ شَيْـًٔا ﴾ [الأنبياء: ٤٧].

Ma’ana: (Kuma za mu san ya ma’aunai na adalci domin ranar ƙiyama, to ba za a zalucni wata rai wani abu ba).

Sannan bayan haka kowa zai zo ya wuce ta kan siraɗi kamar yadda ya zo a hadisi, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Za a zo da wata gada a sanyata a kan doron jahannama. Sai muka ce, "Ya Manzon Allah Wacce iri gada kuma?' Sai ya ce: " Gada ce mai tsansti da zamiya. Da ƙugiyoyi akanta da ƙayar tsidahu masu faɗi. Irin waɗanda ake samunsu a Najdu. Larabawa suna ce musu: Sa'adan. Mumini zai wuce ta kan wannan siraɗi kamar walƙiya, wani kuma kamar iska, wani kuma kamar ingarman doki. Wani ya tsira ya kuɓuta. Wani kuma ya kukkuje a wuta. Har na ƙarshesu ya zo ya wuce da jan ciki. Bukhari ne ya ruwaito. Abu Sa’id ya ce: “Wannan gadar ta fi gashi sirantaka, kuma ta fi takobi kaifi.

Bayan an gama bi ta kan siraɗi, za a zo a yi ƙisasi da hisabi a tsakannin bayi. Farkon abin da Allah zai fara ƙasasi akansa shi ne jinannaki.

Allah zai keɓe muminai a kan wata gada tsakanin wuta da aljanna, sai Allah Ya yi ƙisasi a tsakaninsu, a bisa abin da suka zalunci kawunansu a gidan duniya. Idan Allah Ya tsarkakar da su, sannan sai a sa su a aljanna.

An karɓo da ga Abu Sa'id Al-Khudri ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Muminai za su kuɓuta daga shiga wuta. Sai a zo a dakatar da su a kan wata gada tsakanin aljannah da wuta. A yi musu ƙisasi; abin da sashinsu ya zalinci sashi da shi a duniya. Har sai an tace su, kuma a tsarkake su, sai a yi musu izinin shiga aljannah".

Bukhari da Muslim ne suka ruwaito.

Yaku Musulmi!

Duk waɗannan fa al'amura tabbatattu ne, kuma tabbas za su faru. Babu wani shakku. Ko tababa, a kan faruwarsu, babu abin da ya rage illa mu tashi mu farka daga wannan dogon baccin da muke ciki.

Ya zama dole a kan duk wanda Allah Ya ara masa wani ɓangare na mulkinsa da ya ji tsoron Allah kar ya yi zalunci. Kar ya kasance marar damuwa da halin da waɗanda yake shuganci suke ciki. Suna kwana da yunwa, kai kuwa kana ƙoshi. Kar bar su suna zama abin farautar miyagun mutane. Ya za ka fuskanci wannan rana idan ka jewa Ubangiji da irin wannan hali? Ka tuna faɗar Manzon Allah (ﷺ) da yake cewa:

"Babu wani mai kiwo da Allah zai ba shi kiwo ya je masa yana mai cin amana, face ya shiga wuta".

Ya ku waɗanda Allah ya ba su shugabanci, gwamnoninku da 'yan majalisinku da ciyamominku, ku ji tsoron Allah a kan amanar da Ya ba ku. Kowa ya duba ya ga me ya tanadar domin waccan rana. Ranar hisabi, ranar tonon asiri, ranar da-na-sani.

Haka kuma su waɗanda ake shugabanta kowa ya daina ɓarna da sakaci a wajen aiwatar da umarnin Allah, a dinga yin salla a kan lokaci. Ku daina ƙarya da sata da zamba da ƙeta da ha'inci. Kowa ya ribaci lokacinsa da ƙuruciyarsa da lafiyarda domin Ubangiji yana nan a madakata.

Dukkan Yabo da kirari sun tabbata ga Allah Ubangijin Halittu. Tsira da amincin Allah su tabbata ga shugaban manzanni, kuma fiyayyen haltta, annabin tsira, annabin rahma, Annabinmu Muhammadu da alayensa da sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkin addininsu da koyarwarsa har zuwa ranar alƙiyama. Bayan haka:

Yaku bayin Allah!

Allah Yana cewa:

﴿ وَكَذَٰلِكَ أَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡكَ قُرۡءَانًا عَرَبِيّٗا لِّتُنذِرَ أُمَّ ٱلۡقُرَىٰ وَمَنۡ حَوۡلَهَا وَتُنذِرَ يَوۡمَ ٱلۡجَمۡعِ لَا رَيۡبَ فِيهِۚ فَرِيقٞ فِي ٱلۡجَنَّةِ وَفَرِيقٞ فِي ٱلسَّعِيرِ ٧ ﴾ [الشورى: ٧].

(Hakanan mun yi maka wahayin wannan Alƙur'ani da harshen Larabci, domin ka gargaɗi mutanen Makkah da kewayenta. Ka gargaɗesu da ranar tattara halittu, babu kowanto game da wannan rana. Wasu za su kasance a aljannah, wasu kuma a cikin wutar Sa'ira).

Allah ya ce a cikin Suratul Hudu:

﴿ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةٗ لِّمَنۡ خَافَ عَذَابَ ٱلۡأٓخِرَةِۚ ذَٰلِكَ يَوۡمٞ مَّجۡمُوعٞ لَّهُ ٱلنَّاسُ وَذَٰلِكَ يَوۡمٞ مَّشۡهُودٞ ١٠٣ وَمَا نُؤَخِّرُهُۥٓ إِلَّا لِأَجَلٖ مَّعۡدُودٖ ١٠٤ يَوۡمَ يَأۡتِ لَا تَكَلَّمُ نَفۡسٌ إِلَّا بِإِذۡنِهِۦۚ فَمِنۡهُمۡ شَقِيّٞ وَسَعِيدٞ ١٠٥ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ شَقُواْ فَفِي ٱلنَّارِ لَهُمۡ فِيهَا زَفِيرٞ وَشَهِيقٌ ١٠٦ خَٰلِدِينَ فِيهَا مَا دَامَتِ ٱلسَّمَٰوَٰتُ وَٱلۡأَرۡضُ إِلَّا مَا شَآءَ رَبُّكَۚ إِنَّ رَبَّكَ فَعَّالٞ لِّمَا يُرِيدُ ١٠٧ ﴾ [هود: ١٠٣ - ١٠٧].

"Haƙiƙa a cikin wannan akwai aya ga duk wanda yake tsoron ranar lahira. Wannan yini ne da Allah yake tara mutane cikinsa Kuma yini ne da ake halartarsa.

Ba ma jinkirta shi sai don wani ajali ƙididdigagge. Ranar da za ta zo, babu wata rai da za ta yi magana sai da izininsa. Daga cikinsu akwai ɗan wuta, akwai ɗan aljanna. Bayi na ƙwarai suna cikin aljanna suna masu dawwama a cikinta, dawwamar sama da ƙasa, wannan kyauta ce ba mai yankewa ba. Waɗanda kuma suka yi aikin tsiya to suna cikin wuta masu dawwama ne a cikinta dauwamar sama da ƙasa. Lalle Ubangijinka mai aikata abin da ya ga dama ne).

Kuma Allah yana cewa:

﴿ وَسِيقَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ إِلَىٰ جَهَنَّمَ زُمَرًاۖ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءُوهَا فُتِحَتۡ أَبۡوَٰبُهَا وَقَالَ لَهُمۡ خَزَنَتُهَآ أَلَمۡ يَأۡتِكُمۡ رُسُلٞ مِّنكُمۡ يَتۡلُونَ عَلَيۡكُمۡ ءَايَٰتِ رَبِّكُمۡ وَيُنذِرُونَكُمۡ لِقَآءَ يَوۡمِكُمۡ هَٰذَاۚ قَالُواْ بَلَىٰ وَلَٰكِنۡ حَقَّتۡ كَلِمَةُ ٱلۡعَذَابِ عَلَى ٱلۡكَٰفِرِينَ ٧١ قِيلَ ٱدۡخُلُوٓاْ أَبۡوَٰبَ جَهَنَّمَ خَٰلِدِينَ فِيهَاۖ فَبِئۡسَ مَثۡوَى ٱلۡمُتَكَبِّرِينَ ٧٢ وَسِيقَ ٱلَّذِينَ ٱتَّقَوۡاْ رَبَّهُمۡ إِلَى ٱلۡجَنَّةِ زُمَرًاۖ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءُوهَا وَفُتِحَتۡ أَبۡوَٰبُهَا وَقَالَ لَهُمۡ خَزَنَتُهَا سَلَٰمٌ عَلَيۡكُمۡ طِبۡتُمۡ فَٱدۡخُلُوهَا خَٰلِدِينَ ٧٣ ﴾ [الزمر: ٧١ – ٧٣].

Haka Allah zai kora ‘yan wuta zuwa jahannama jama’a-jama’a. Har sai zo mata sai a boɗe ƙofofinta, kuma masu gadinta su ce musa: “Shin manzanni daga cikinku ba su zo muku suna karanta muku ayoyin Ubangijinku ba, kuma suna gargaɗinku haɗuwarku da wannan yinin ba?”Sai suka ce, E, sun zo. Sai dai kalmar azaba ta riga ta tabbata akan kafirai. Sai a ce musu ku shiga ƙofofin jahannama, kuna masu dauwama a cikinsu har abada. Tir da makomar masu girman kai. Kuma a ka ja waɗanda suka ji tsoron Ubangijinsu jama’a-jama’a zuwa aljannah. Har sai idan sun zo mata alhalin an buɗe ƙofofinta. Sai kuma masu gadinta su ce musu, “Aminci ya tabbata a gare ku, kun ji daɗi. Ku shiga aljannah kuna masu dauwama a cikinta har abada”).

Yaku bayin Allah!

Ku ji tsoron Allah. Ku sani mafi darajarmu a wajen Allah shi ne mafi tsoronsa. Duk wanda aikinsa ya daƙilar da shi, to dangantakarsa ba za ta ciyar da shi gaba ba. Ku sani Allah yana lissafa muku ayyukanku da kuke yi, don haka duk wanda ya samu alheri to ya godewa Allah. Wanda kuma ya sami kishiyar wannan to kar ya zargi kowa sai kansa.

GARGAƊI A KAN BIDI'A

Manufofin huɗubar

- Bayanin haɗarin bidi'a addini.
- Gargaɗin mutane game da ƙirƙirar bidi'a a addini.
- Bayanin wasu daga cikin abubuwan da suke jawo bidi'a a addini.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma mua neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan aiyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar dashi, wanda kuma ya atar babu mai shiryar da shi, kuma ina shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai allah, shi kaɗai ne bashi da abokin taraiya, kuma ina shaidawa cewa Annabi Muhammad bawansane manzonsane, (Yaku waɗanda kuka bada gaskiya kuji tsoron Allah yadda ya cancanta aji tsoronsa, kada ku mutu face kuna Musulmi). (Yaku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicce ku daga rai guda ɗaya kuma ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga gare su (su biyu) kuji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya dashi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku waɗanda suka yi imani kuji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku aiyukanku, kuma ya gafarta muku zunubanku. Wanda ya bi Allah da manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawun shiriya shiriyar Annabi Muhammadu (ﷺ) kuma mafi sharrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Bayan haka, ku ji tsoron Allah - ya ku muminai – don ku samu rahama. Ku yi guzuri daga kyawawan ayyuka ko kwa rabauta. Ku rigayi kwanakinku da ayyukanku domin a cikin yankewar kwanaki akwai izina, kuma a cikin saurin shuɗewar kwanaki akwai tunatarwa. Allah ya jiƙan bawan da ya yi imani da Allah kuma ya tsaya ƙyam a kan atafarki, kuma duniya ba ta shagaltar da shi daga lahira ba!

Ya ku musulmai, haƙiƙa Allah ta'ala ya aiko manzonsa Muhammadu (ﷺ) a lokacin da sawun manzanni ya ɗauke, yayin da ɓata ya kama ƙasa, duhu ya tsananta, halittu suka ruɗe a cikin wautar jahiliyya, da hanyoyin makanta. Ba su san wani abu gaskiya ba. Sai manzancin Annabi da aikensa ya zamo su. Yana ɗauke da saƙon fitar da mutane daga son zuciya da bin hanyar iyayensu zuwa bin sa da bin sunnarsa.

Yayin da Annabi (ﷺ) ya tashi yana mai bushara da gargaɗi a cikin mutane, kuma mai kira zuwa ga Allah, kuma fitila mai haske, nan da nan shaƙiyyai suka shiga yaƙarsa. Suka fuskanci kiransa da kafirci. Sai da Allah Ta'ala ya ɗaukaka kalmarsa ya bayyana addininsa. Manzon Allah (ﷺ) ya aikata abin da Allah ya wajabta masa. Allah ya shiryi al'umma da shi zuwa gaskiya, ya tseratar da halittu da yawa a sandiyyarsa. Annabin (ﷺ) bai rasu ba har sai da ya isar da manzanci, ya ba da amana, ya yi nasiha ga al'umma, ya cika addini, ya bar mu a kan tafarki tantarwai, wanda daresa kamar ranarsa ne. Ya ji tsoron kada mutane su koma zuwa ga son zuciyarsu, su bar bin sa, ko su bi wasu su bar sunnarsa, don haka ya gargaɗe su, ya tsoratar da su, ya ba da labarin bayyanar fitintunu da ɓacewar sunnoni, da yaɗuwar bidi'a. Ya yi gargaɗi da a guji ma'abota soye-soyen zukata, waɗanda suka farraƙa addini, suka rarrabu bayan rasuwar Annabi (ﷺ) .

Bayan wuce 'yan shekaru da wafatin Manzo (ﷺ) sai masu fifita hankali suka bayyana, ƙarƙashin jagorancin Mu'utazilawa. Haka masu Sufaye suka wuce gona da iri. Kawarijawa suka fito, Murji'awa suka faso kai. Kungiyoyi suka rarrabu. Wasu mutane suka juya wa hanyar sunna baya. Suka ruɗe a cikin ɓata. Babban musabbabin ɓacewar waɗannan ƙungiyoyi duka kuwa shi ne barin sunna da rinjayar son zuciya, da miƙa ragama ga hankali, da bin ra'ayin iyaye, da watsi da gaskiya saboda shaihunai da shugabanni. Waɗannan su ne 'yan huɗu na bidi'a, kuma ƙungiyar gaba da sunna, wato son zuciya, da miƙa ragama ga tsantsar hankali, da makauniyar biyayya, da jahilci.

Don haka ne, dalilai suka yawaita daga Alƙur'ani da sunnah da zantuttukan sahabbai da tabi'ai da shuwagabannin shiriya, suka tabbatar da hujjoji masu nuna fifikon dawwama a kan sunna sama da komai. Haka nan da bin shiriyar Annabi (ﷺ) da nisantar bidi'a da fararrun abubuwa. Haƙiƙa Alƙur'ani mai girma ya cika da ayoyin biyayya da ɗa'a ga Manzo (ﷺ), da kuma cewa, bin Annabi (ﷺ) shi ne alamar soyayya ta gaskiya. Allah yana cewa:

﴿ قُلۡ إِن كُنتُمۡ تُحِبُّونَ ٱللَّهَ فَٱتَّبِعُونِي يُحۡبِبۡكُمُ ٱللَّهُ وَيَغۡفِرۡ لَكُمۡ ذُنُوبَكُمۡۗ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٣١ ﴾ [آل عمران: ٣١].

(Ka ce idan kun kasance kuna son Allah, to ku bi ni Allah ya so ku, kuma ya gafarta musku zunubanku).

Da faɗinsa:

﴿ وَإِن تُطِيعُوهُ تَهۡتَدُواْ ﴾[النور: ٥٤].

(Idan kun bi shi kwa shiriya).

Haka nan yana cewa,

﴿ وَمَآ ءَاتَىٰكُمُ ٱلرَّسُولُ فَخُذُوهُ وَمَا نَهَىٰكُمۡ عَنۡهُ فَٱنتَهُواْ ﴾[الحشر: ٧].

(Abin da manzo ya zo muku da shi to ku karɓe shi, kuma abin da ya hane ku ga barinsa to ku hanu).

Kuma babu wani abu bayan bin Annabi (ﷺ) sai bin son zuciya:

﴿ فَإِن لَّمۡ يَسۡتَجِيبُواْ لَكَ فَٱعۡلَمۡ أَنَّمَا يَتَّبِعُونَ أَهۡوَآءَهُمۡۚ وَمَنۡ أَضَلُّ مِمَّنِ ٱتَّبَعَ هَوَىٰهُ بِغَيۡرِ هُدٗى مِّنَ ٱللَّهِۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ٥٠ ﴾ [القصص: ٥٠].

(To idan ba su amsa maka ba, to ka sani cewa suna bin son zuciyarsu ne, kuma

wane ne mafi ɓata daga wanda ya bi son zuciyarsa ba tare da shirya daga Allah ba, lalle Allah ba ya shiryar da mutanen da suke azzalumai).

Ma'abota son zuciya, su ne masu kawar da kai ga barin sunnoni. Allah ya ce,

﴿ وَمَنۡ أَعۡرَضَ عَن ذِكۡرِي فَإِنَّ لَهُۥ مَعِيشَةٗ ضَنكٗا وَنَحۡشُرُهُۥ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ أَعۡمَىٰ ١٢٤ ﴾ [طه: ١٢٤].

(Kuma duk wanda ya kau da kai ga barin ambatona, to yana a rayuwa mai ƙunci, kuma za mu tashe shi a ranar alƙiyama yana makaho).

Haka nan ahalin bidi'a suke cikin ƙunci da matsi da takura, babu yalwar ƙirji, ba nutsuwa. Domin shiriya ba ta kasancewa face a cikin biyayya ga Annabi (ﷺ):

﴿ فَمَنِ ٱتَّبَعَ هُدَايَ فَلَا يَضِلُّ وَلَا يَشۡقَىٰ ١٢٣ ﴾ [طه: ١٢٣].

(Duk wanda ya bi shiriya ta, to ba zai ɓata ko ya wahala ba).

Nana A'isha, ta ce manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Duk wanda ya farar da wani abu a cikin al'amarinmu wannan, abin da babu shi, to an mayar masa". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi. A cikin riwayar Muslim, "Wanda ya aikata wani aiki ba da umarninmu ba, to an mayar masa".

An karɓo daga Jabir (R.A) ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya kasance idan zai yi huɗuba sai idanunsa su yi ja, sautinsa ya ɗaukaka, fushisa ya tsananta, kamar ka ce mai gargaɗin runduna ne, yana cewa, "Barkanku da safiya! Barkanku da yamma". Kuma yana cewa: "An aiko ni alhali abin da ya rage ga tashin alƙiyama kamar wɗannan biyun ne". Sai ya haɗa tsakanin 'yan yatsunsa biyu, (manuniya da na tsakiya)".

Kuma yana cewa (ﷺ) "Bayan haka, haƙiƙa mafi alherin zance shi ne littafin Allah, kuma mafi alherin shiriya, shiriyar Muhammadu. Kuma mafin sharrin lamura ƙagaggunsu, kuma dukkani bidi'a ɓata ce". Muslim da Ibn Majah da waninsa ne suka rawaito shi.

Kuma na karɓo daga Anas ɗan Malik (R.A) ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Haƙiƙa Allah ya toshe tuba daga duk wani mai yin bidi'a har sai ya bar bidi'arsa". Ɗabarani ne ya rawaito shi, kuma salsalarsa kyakkyawa ce. Haka nan daga Irbadh ɗan Sariya ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ina yi muku kashedi da fararrun abubuwa, domin duk wani fararren abu ɓata ne". Ahmad da Tirmizi da Ibn Majah da Ibn Hibban ne suka rawaito shi. Kuma Tirmizi ya ce, "Hadisi ne kyakkyawa ingantacce".

Ya ku bayin Allah! Haƙiƙa lazimtar sunnah shi ne shaidawa Annabi Muhammad (ﷺ), manzon Allah ne. Kuma shi ne bin manzon (ﷺ) a cikin abin da ya yi umarni da shi da gaskata shi a cikin abin da ya ba da labari, da nisantar abin da ya yi hani da gargaɗi a kansa. Kuma kada a bautawa Allah sai da abin da ya shar'anta. Don haka bai halatta a nemi kusanci zuwa ga Allah da wani addini ko ibada wanda ba manzon Allah (ﷺ) ne ya shar'anta ba. In ba haka ba za ta zama karɓaɓɓiya a gurin Allah ba. Allah ya ce,

﴿ أَمۡ لَهُمۡ شُرَكَٰٓؤُاْ شَرَعُواْ لَهُم مِّنَ ٱلدِّينِ مَا لَمۡ يَأۡذَنۢ بِهِ ٱللَّهُ ﴾ [الشورى: ٢١]

(Ko kuma suna da wasu abokan tarayya ne da suka shar'anta musu wani abu na addini wanda Allah bai yi izini da shi ba).

Don haka bai halatta a bi wasu maganganu da suka saɓawa sunna ba komai girman mafadinsu. Kuma kowa a kan iya karɓar maganarsa ko a mayar da ita banda Manzon Allah (ﷺ), kamar yadda Imamu Maliku ya fada, Allah ya rahamshe shi. Kuma haƙiƙa Imamus Shafi'i, Allah ya jikan sa, ya ce: "Malamai sun hadu a kan cewa duk wanda sunnar manzon Allah (ﷺ) ta bayyana a gare shi, ba shi da hurumin ya barta saboda maganar wani mutum". Imamu Ahmad Allah ya jikansa ya ce: "Ina mamakin mutane da suka san Isnadi da ingancinsa, amma suke tafiya zuwa ga ra'ayin Sufyanu. Alhali Allah Ta'ala yana cewa:

﴿ فَلۡيَحۡذَرِ ٱلَّذِينَ يُخَالِفُونَ عَنۡ أَمۡرِهِۦٓ أَن تُصِيبَهُمۡ فِتۡنَةٌ أَوۡ يُصِيبَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٌ ٦٣ ﴾ [النور: ٦٣].

(Kuma wadanda suka saɓa umarninsa, su ji tsoron kada wata fitina ko azaba mai radadi ta same su).

Shin ka san ko mene ne fitinar? Fitinar ita ce, shirka, wataƙila shi idan ya mayar da sashin maganarsa, wani abu daga karkata ta, ya fadawa zuciyarsa ya hallaka». Karshen maganar Imam Ahmad ke nan.

Ya ku musulmai! Kamar yadda musulunci yake, shi ne miƙa wuya ga Allah, da saduda gare shi tare biyayya. To haka nan idan aka samu wani hadisi ya ingata daga wanda ba ya kuskure ya wajaba a sallama masa, a miƙa wuya gare shi. Allah yana cewa,

﴿ وَمَا كَانَ لِمُؤۡمِنٖ وَلَا مُؤۡمِنَةٍ إِذَا قَضَى ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥٓ أَمۡرًا أَن يَكُونَ لَهُمُ ٱلۡخِيَرَةُ مِنۡ أَمۡرِهِمۡۗ وَمَن يَعۡصِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ فَقَدۡ ضَلَّ ضَلَٰلٗا مُّبِينٗا ٣٦ ﴾ [الأحزاب: ٣٦].

(Kuma ba zai yiwu ga mumini ko mumina ba idan Allah da Manzonsa suka hukunta wani abu, ya zama suna da wani zaɓi daga lamarisu. Kuma duk wanda ya saɓawa Allah da manzonsa, haƙiƙa ya ɓata ɓata mabayyani).

Ya ku musulmai! Shi kuwa saɓanin sunna, shi ne rarrabuwa a cikin addini, da ɓata mabayyani, Allah yana cewa,

﴿ وَأَنَّ هَٰذَا صِرَٰطِي مُسۡتَقِيمٗا فَٱتَّبِعُوهُۖ وَلَا تَتَّبِعُواْ ٱلسُّبُلَ فَتَفَرَّقَ بِكُمۡ عَن سَبِيلِهِۦۚ ذَٰلِكُمۡ وَصَّىٰكُم بِهِۦ لَعَلَّكُمۡ تَتَّقُونَ ١٥٣ ﴾ [الأنعام: ١٥٣].

(Kuma wannan shi ne tafarkina madaidaici, to ku bi shi, kuma kada ku bi wasu hanyoyi sai su raba ku da tafarkinsa).

Saboda duk wanda ya ƙetare abin da aka umarce shi da shi, to babu shakka ya yi shisshiga, kamar yadda Alƙur'ani ya nuna, Allah yana cewa,

﴿ فَٱسۡتَقِمۡ كَمَآ أُمِرۡتَ وَمَن تَابَ مَعَكَ وَلَا تَطۡغَوۡاْۚ إِنَّهُۥ بِمَا تَعۡمَلُونَ بَصِيرٞ ١١٢ ﴾ [هود: ١١٢].

(Ka daidaita kamar yadda aka umarce ka, da wanda ya tuba tare da kai, kuma kada ku yi shisshigi, lalle shi mai gani ne ga abin da kuke aikatawa).

Kuma haƙiƙa yin bauta da abin da mutum yake ganinsa mai kyau ne, kuma yake karkata zuwa gare shi, ba tare da wani dalili ko shiriya ba, shi ne haƙiƙanin bin son zuciya. Allah

yana cewa,

﴿ أَرَءَيۡتَ مَنِ ٱتَّخَذَ إِلَٰهَهُۥ هَوَىٰهُ ﴾ [الفرقان: ٤٣].

(Yanzu ka ga wanda ya riƙi son zuciyarsa shi ne abin bautarsa?!)

Kuma yana cikin hadarin shiga cikin wandanda Allah yake cewa game da su:

﴿ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ طَبَعَ ٱللَّهُ عَلَىٰ قُلُوبِهِمۡ وَٱتَّبَعُوٓاْ أَهۡوَآءَهُمۡ ﴿١٦﴾ ﴾ [محمد: ١٦].

(Waɗannan su ne Allah ya yi rufi a kan zukatansu, kuma suka bi son zicuyarsu).

Haƙiƙa Annabi (ﷺ) ya ambaci bid'a a matsayi ɓata. Domin haƙiƙa shi ɗan bidi'a yana ɓata ne a cikin bin son zuciya. Yakan ɗauki dalilai masu rikitarwa a mariƙa ta son zuciya da sha'awa, ba mariƙa ta miƙa wuya zuwa hukunce-hukuncen Allah ba. Sai ya sanya son zuciya da kyautata abin, shi ne abin nemansa na farko, su kuma sauran dalilai ya nemi su goya masa baya. Sai ya aje dalilan a kan abin da ya dace da hankalinsa da son zuciyarsa. Don haka Allah mai buwaya da ɗaukaka ya ce,

﴿ يُضِلُّ بِهِۦ كَثِيرٗا وَيَهۡدِي بِهِۦ كَثِيرٗا ﴾[البقرة: ٢٦].

(Yana ɓatar da mutane da yawa da shi, kuma yana shiryar da mutane da dadama da shi).

Kuma Allah Ta'ala Ya yi gargaɗi game da ma'abota ɓata wajen kafa dalili, kamar yadda Allah Ta'ala Ya ce:

﴿ هُوَ ٱلَّذِيٓ أَنزَلَ عَلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبَ مِنۡهُ ءَايَٰتٞ مُّحۡكَمَٰتٌ هُنَّ أُمُّ ٱلۡكِتَٰبِ وَأُخَرُ مُتَشَٰبِهَٰتٞۖ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ فِي قُلُوبِهِمۡ زَيۡغٞ فَيَتَّبِعُونَ مَا تَشَٰبَهَ مِنۡهُ ٱبۡتِغَآءَ ٱلۡفِتۡنَةِ وَٱبۡتِغَآءَ تَأۡوِيلِهِۦۖ وَمَا يَعۡلَمُ تَأۡوِيلَهُۥٓ إِلَّا ٱللَّهُ ﴾[آل عمران: ٧].

(Shi ne wanda ya saukar maka da littafi, a cikinsa akwai ayoyi wanda ma'anar su take a fili, wasu kuma masu rikitarwa. To amma su waɗanda karkata take a cikin zukatansu sai su riƙa bin abin da yake da rikitarwar, don neman fitina, da neman fassararsa, ba wanda ya san fassararsa sai Allah).

Ya ku bayin Allah! Haƙiƙa wani ba shi da ra'ayi bayan sunnar Manzon Allah (ﷺ). An karɓo daga ɗan Abbas (R.A), ya ce, "Wanda ya farar da wani ra'ayi da ba ya cikin littafin Allah, kuma sunnar manzon Allah ba ta zartar da shi ba, bai san abin da yake kai ba, yayin da ya gamu da Allah mai buwaya da ɗaukaka".

Malam Shaɗibi - Allah ya jiƙansa - ya ce: "Haƙiƙa ɗan bidi'a ana jefa masa ƙasƙanci a duniya, da fushin Allah. Saboda faɗinsa maɗaukakin sarki:

﴿ إِنَّ ٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُواْ ٱلۡعِجۡلَ سَيَنَالُهُمۡ غَضَبٞ مِّن رَّبِّهِمۡ وَذِلَّةٞ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَاۚ وَكَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلۡمُفۡتَرِينَ ﴿١٥٢﴾ ﴾ [الأعراف: ١٥٢].

(Lalle waɗanda suka riƙi ɗan maraƙi, fushi da ƙasƙanci a rayuwar duniya za su same su. Kuma haka muke sakawa masu ƙirƙirar ƙarya).

Wannan ya haɗe su mutanen Annabi Musa da makamantansu, domin bidi'o'i dukkaninsu ƙirƙirar ƙaya ne ga Allah". Karshen maganar Shaɗibi.

Ibnul Majishuna ya ruwaito daga Imamu Malik - Allah ya jiƙansa - yana cewa, "Wanda ya ƙirƙiri wata bidi'a a musulunci da yake ganinta kyakkyawa to haƙiƙa ya riya cewa Mahamma ya ha'inci manzanci. Domin Allah Ta'ala yana cewa:

﴿ ٱلۡيَوۡمَ أَكۡمَلۡتُ لَكُمۡ دِينَكُمۡ ﴾ [المائدة: ٣].

(Yau na cika muku addininku).

To abin da bai zama addini ba a wancan lokaci, ba zai zama addini ba a yau". Karshen maganar Maliku.

Kuma Annabi (ﷺ) ya ba da labari kamar yadda yake cikin sahihi Muslim cewa, duk masu musanyawa da masu canjawa za a kore su a fatattake su daga bakin

tafkinsa.

Haƙiƙa bidi'o'i suna rusa addini ingantacce. Kuma wasu mutane ba za su ƙirƙiri wata bidi'a ba face Allah ya cire musu kwantankwacinta daga sunna. Wannan sananne ne, ana ganinsa ƙuru-ƙuru, domin kana ganin kwaɗayin wasu mutane kan bidi'o'i fararru, da barinsu ga sunnon tabbatattu, ko ma wajibai. Kamar yadda kake ganin nishaɗin tashohin rediyo da na talabijin, da na tauraron ɗan adam wajen nuna waɗannan bidi'o'i da yaɗa su, tare da irin saɓawa addinin da ke ciki, suna nuna ibadunsu kai tsaye, wanda gama gari ke ruɗuwa da su. Suna zaton cewa addini ne, musamman idan masu dangatuwa ga ilimi da malanta suka shiga ciki. Don haka malamai su ji tsoron Allah kada su zama fitina ga muminai.

Allah ya yi albarka gare ni da ku a cikin Alƙur'ani da sunna, kuma ya amfane ni da ku da abin da ke cikinsu na ayoyi da hikima. Ina neman gafarar Allah ga kaina da ku!

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah, Ubangijin talikai, Allah ya yi tsira a bisa mafi darajar manzanni, Muhammadu (ﷺ) da alayensa da sahabbansa gabaɗaya. Bayan haka:

Haƙiƙa yana daga abin da yake jefa mutane cikin tarkon bidi'a da son zuciya, kwaikwayon iyaye da manya, ko bin kurakuran malamai. Ko kuma tsantsar ra'ayin biyayya ga shugabanni.

An karɓo daga Muƙatil ɗan Hayyan Allah Ya jiƙansa ya ce, "Ma'abota son zuciya su ne guba a cikin al'ummar Muhammadu (ﷺ). Suna ambaton Annabin (ﷺ) da ahalin gidansa, da wannan sai su riƙa samun yabo daga jahilan mutane, daga nan sai su jefa su a cikin halaka. Sun yi kama da mutumin da yake shayar da guba a matsayin zuma. Yana daga cikin tsofaffin hujjoji da shaiɗan yake ƙawatawa mutane hanyoyinsa da su don ya don ya raba su da gaskiya da sunna, su ne makauniyar biyayya ga iyaye da shugabanni, da tsattsauran ra'ayi a wajen bin su, ko da sun kaucewa shiriya; wannan tsohuwar hanya ce da ɓatattu suke kafa hujja da ita, tun shekaru aru-aru. Ga shi Allah Ta'ala ya ba da labari game musayar Annabi Ibrahim da mutanensa yayin da ya ce musu:

﴿ مَا تَعۡبُدُونَ مِنۢ بَعۡدِي قَالُواْ نَعۡبُدُ إِلَٰهَكَ وَإِلَٰهَ ءَابَآئِكَ إِبۡرَٰهِـۧمَ وَإِسۡمَٰعِيلَ وَإِسۡحَٰقَ إِلَٰهٗا وَٰحِدٗا وَنَحۡنُ لَهُۥ مُسۡلِمُونَ ١٣٣ ﴾ [البقرة: ١٣٣].

(Me kuke bautawa? Sai suka ce, muna bautawa gumaka ne, mukan dukufa wajen butarsu. Ya ce, shin suna jin ku yayin da kuke kiransu, ko suna amfanarku ko suna cutarwa? Suka ce kaɗai mun sami iyayenmu ne haka suke aikatawa).

A nan sai suka kauce daga ba da amsar tambayar, suka kafa hujja da biyayyar iyayensu. A cikin wata surar kuma:

﴿ أَمۡ ءَاتَيۡنَٰهُمۡ كِتَٰبٗا مِّن قَبۡلِهِۦ فَهُم بِهِۦ مُسۡتَمۡسِكُونَ ٢١ بَلۡ قَالُوٓاْ إِنَّا وَجَدۡنَآ ءَابَآءَنَا عَلَىٰٓ أُمَّةٖ وَإِنَّا عَلَىٰٓ ءَاثَٰرِهِم مُّهۡتَدُونَ ٢٢ وَكَذَٰلِكَ مَآ أَرۡسَلۡنَا مِن قَبۡلِكَ فِي قَرۡيَةٖ مِّن نَّذِيرٍ إِلَّا قَالَ مُتۡرَفُوهَآ إِنَّا وَجَدۡنَآ ءَابَآءَنَا عَلَىٰٓ

أُمَّةٍ وَإِنَّا عَلَىٰٓ ءَاثَٰرِهِم مُّقۡتَدُونَ ﴿٢٣﴾ قَٰلَ أَوَلَوۡ جِئۡتُكُم بِأَهۡدَىٰ مِمَّا وَجَدتُّمۡ عَلَيۡهِ ءَابَآءَكُمۡۖ قَالُوٓاْ إِنَّا بِمَآ أُرۡسِلۡتُم بِهِۦ كَٰفِرُونَ ﴿٢٤﴾ ﴾ [الزخرف: ٢١ – ٢٤].

(Shin ko kuwa mun ba su wani littafi ne wanda suke riƙo da shi? Kaɗai cewa suka yi, mu mun sami iyayenmu a kan wani addini, kuma mu masu bin su ne sau-da-ƙafa. Haka yake, ba mu aiko da wani mai gargaɗi a gabaninka a cikin wata alƙarya ba, face masu morewa a cikinta sun ce, haƙiƙa mu mun tarar da iyayenmu a kan wani addini, kuma mu masu bin su ne sau-da-ƙafa. Ya ce, ko da na zo muku da mafi shiriya daga abin da kuka sami iyayenku a kai? Suka ce, haƙiƙa mu masu kafircewa ne da abin da aka aiko ku).

To ku ji tsoron Allah ya ku Musulmai. Ku bi abin da aka saukar muku daga Ubangijinku, kuma kada ku bi wasu majiɓinta ba shi ba. Ku sani cewa saɓawa sunna a zahiri alama ce ta riya a baɗini.

Ya ku bayin Allah! Haƙiƙa akwai ɓarnace-ɓarnace masu yawa a cikin bidi'a.

1. Bidia' tana rusa addini ingantacce ta maye gurbin sunna. Domin Darimi ya ruwaito da ingantaccen isnadi, daga Hassan ɗan Aɗiyya Almuharibi, Allah ya jiƙansa, ya ce, "Wasu mutane ba za su ƙirƙiri wata bidi'a a cikin addinisu ba, face Allah ya cire musu sunna kwankwacinta. Sannan ba za a dawo musu da ita ba har tashin alƙiyama." Don haka ne ma za ku tarar da 'yan bidi'a suna nacewa (bidi'arsu) fiye da yadda suke nacewa a kan sunna. Domin shaiɗan ya ƙawata musu bidi'a».
2. Kuma za ka ga ɗan bidi'a yana ganin cewa, addini yana buƙatar ƙari. Don haka shi yana nufin ya kammala addini da bidi'arsa. In ba haka ba da yana ganin cewa addinin cikakke ne, to ai da bi yi bidi'a ba.
3. Har ila yau, 'yan bidi'a ƙyamar sunna suke yi. Kuma ba su da wata himma da kazar-kazar wajen aiki da sunna. Suna kaza-kazar ne wajen aikata bidi'a. Don haka za ka tarar da su suna ciyar da dukiyoyinsu, suna wahalar da jikkunansu, suna tozartar da lokutansu a cikin raya bidi'a.
4. Sannan bidi'a na dawo wa da mutane jahiliyya cikin rayuwarsu. Sanna sukan haifar da rarrabuwa a saɓani. Kowace ƙungiya na ganin abin da take a kai ya fi na ɗayar, kamar yadda Allah Ta'ala yake faɗa:

﴿ كُلُّ حِزۡبِۭ بِمَا لَدَيۡهِمۡ فَرِحُونَ ﴿٣٢﴾ ﴾ [الروم: ٣٢].

(Kowace ƙungiya na alfahari da abin da ke gurinsu).

Kuma kamar yadda Tsarkakakken Sarki ya ce:

﴿ وَلَا تَتَّبِعُواْ ٱلسُّبُلَ فَتَفَرَّقَ بِكُمۡ عَن سَبِيلِهِۦۚ ﴿١٥٣﴾ ﴾ [الأنعام: ١٥٣].

(Kuma kada ku bi wasu hanyoyi, sai su raba ku da tafarkinsa)

Su kuwa sunnoni suna tattara mutane ne, su haɗa tsakanin zukatansu, sai su zama 'yan uwa masu son juna a kan turba ɗaya, da addini ɗaya. Suna masu aiki da faɗinsa Maɗaukakin sarki:

﴿ وَٱعۡتَصِمُواْ بِحَبۡلِ ٱللَّهِ جَمِيعٗا وَلَا تَفَرَّقُواْ ﴾ [آل عمران: ١٠٣].

(Kuma ku yi riƙo da igiyar Allah gabaɗaya, kada ku rarraba).

1. Bidi’a tana gadar da girman kai, da ƙin gaskiya. Shi ɗan bidi’a idan aka kira shi zuwa gaskiya, ba zai yadda ba. Sai dai ya riƙe bidi’arsa gangam, ya kuma yi dukkanin wani yunƙuri domin kare ta.
2. Bidi’a tana ɓata addini nagartacce. Wannan kuwa shi ne burin shaiɗanun mutane da aljanu daga kafirai da munafukai maƙiya addini. Suna ƙoƙarin ɓata shi ta dukkan hanyoyi. Mafi muhimmancin makami da suke amfani da shi, a wajen rushe addini shi ne bidi’o’i da camfe-camfe don su munana musuluncin da su. Su rufe fuskar ingantaccen addini da su, har wanda bai san haƙiƙar Musulunci ba, sai ya yi zaton cewa musulunci tarin camfe-camfe ne da tilin gurɓatattun ibadu. Sai wanda yake nufin shiga cikinsa ya fasa. Bugu da ƙari, su waɗanda ke yayata bidi’o’i suna girbar wasu amfanoni na abin duniya daga yaɗa bidi’a, ko su sami damar biyan sha’awoyinsu na haram. Sau nawa ake kashe kuɗi wajen raya waɗannan bidi’o’i, nawa ne aka keta na mutunci saboda cuɗanya tsakanin maza da mata ba tare da mai tsawatarwa ko mai kwaɓa ba? Don haka ya wajaba ga malamai da masu huɗuba su gargaɗi mutane daga gare ta.

Ya ku mutane! Haƙiƙa sahabban Manzon Allah (ﷺ) sun kasance suna gargaɗi game da bidi’a. Labari ya zo ga Abdullahi ɗan Mas’ud (R.A) cewa Ibn Amru bn Utba, tare da wasu abokansa sun gina wani masallaci a bayan garin Kufa. Sai Abdullah ya ba da umarnin a je a rusa shi. Sannan labari ya sake iske shi cewa, su dai waɗanna mutane suna taruwa a wata nahiya ta masallacin Kufa, suna wani irin tasbihi da tahlili da kabbara. Sai Abdullahi ya sanya rigarsa mai haɗe da hula, sannan ya tafi ya zauna a wajensu. Yayin da ya fahimci abin da duk suke yi, sai ya yaye hular rigar, sannan ya ce, "Ni ne Abu Abdurrahman". Sannan ya ci gaba da cewa: “Haƙiƙa ku, ko dai kun fi sahabban Manzon Allah (ﷺ) ilimi, ko kuma kun zo da bidi’a ce da zalunci. Sai Amru bin Utbah ya ce, "Muna istigfari ne sau uku". Sannan wani mutum daga Bani Tamim ya ce, "Wallahi ba mu fi sahabban Muhammadu (ﷺ) ilmi ba, kuma ba mu zo da bidi’a ta zalunci ba, mun haɗu ne kawai muna zikiri". Sai ɗan Masu'ud ya ce, "Tabbas kun yi. Na rantse da wanda ran ɗan Mas’udu yake hannunsa, wallahi da za ku kama hanyar sahabbai, haƙiƙa da kun san in riga na muku fintinkau. Idan kuwa kun ruɗe kun saki hanya, dama ko hagu, to kun ɓata, ɓata mai nisa".

Don haka ku ji tsoron Allah Ya bayin Allah, su sani cewa Musulmi yana da wadatuwa da alheri mai yawa a cikin abin da ya tabbata daga Annabi (ﷺ). Saboda haka kada ku waiwaya zuwa abin da yake saɓanin haka na bidi’o’i da abin da bai tabbata daga ruwayoyi ba. Abin da Annabinku (ﷺ) yake kai, da magabatan al’umma, ya ishe ku.

ABOTA TA KWARAI DA TASIRINTA GA MUTUM

Manufofin huɗubar

- Tarbiyyantar da musulmi a kan al'adun musulunci.
- Umarni da abokantakar mumina na ƙwarai da nisantar miyagun abokai.
- Mai da hankali a kan tarbiyyar 'ya'ya mata da sa ido a kan ƙawayensu.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammadu bawansa ne manzonsa ne. (Yaku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron Allah yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Yaku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammadu (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (a addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta".

Bayan haka: Ya bayin Allah! Haƙiƙa musulunci addni ne da yake da nagartattun ɗabi'u, don haka ya dace da ɗabi'un da ba a gurɓata su ba. Ya kuma dace da ɗabi'un da suke masu kyawu. Musulunci shi ne maganin gurɓatattun ɗabi'u, kamar yadda ya tabbata a hadisin da Bukhari da Muslim suka rawaito na Abu Huraira mai ɗauke da cewa: "Duk wani ɗa asali ana haihuwarsa ne a kan ɗabi'un ƙwarai, sai dai iyayensa su Yahudantar da shi, ko su Kiristantar da shi, ko kuma su maguzantar da shi".

Kamar yadda aka halittawa Annabi Adamu, Hawwa'u don ya sami nutsuwa da hutu da ita, Allah bai bar shi, shi kaɗai ba. Allah Ya ce:

﴿ هُوَ ٱلَّذِى خَلَقَكُم مِّن نَّفْسٍ وَٰحِدَةٍ وَجَعَلَ مِنْهَا زَوْجَهَا لِيَسْكُنَ إِلَيْهَا ۖ ﴾ [الأعراف: ١٨٩].

(Allah shi ne wanda ya halicce ku daga rai ɗaya (shi ne Annabi Adam) ya kuma halicci matarsa daga jikinsa don ya sami nutsuwa da ita).

Musulunci ya yi aiki tuƙuru don tabbatar da wanna kyakkyawar ɗai'a ta rayuwa tare da mutane. Don haka hukunce-hukuncensa dadama suka ƙunshi tattaruwa cikin jama'a da gudanar da su tare. Kamar sallar Juma'a, jam'in salloli, da idi biyu da kuma sallar kisfewar rana ko wata.

Yana daga abubuwanda ke ƙara bayyana mana haka ƙarara a fili yunƙurin da Annabi (ﷺ) ya yi na ƙone gidajen marasa zuwa jam'in salla. An karɓo daga Abu Huraira, Allah ya yarda da shi ya ce: "Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Tabbas da na yi niyyar na sa ladani ya kira sallah, sannan in umarci wani ya jagoranci yi wa mutane salla, ni kuma in tafi da wasu jama'a ɗauke da ɗaurin itatuwa zuwa ga waɗanda ba sa zuwa salla a jam'I, in ƙone gidajensu da wuta". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

Haka kuma Manzo (ﷺ) ya kwaɗaitar da matafiyi a kan yin tafiya a cikin ayari, ya kuma kira matafiyin da yake tafiya shi kaɗai da shaiɗani. Kamar yadda ya zo cikin hadisin Abdullahi ɗan Amr cewa, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Matafiyi shi ɗaya jal shaiɗani ne, matafiya su biyu kuma shaiɗanu biyu ne, matafiya uku kuwa sun zama ayari. Maliku da Tirmizi da Abu Dawud da Nasa'i ne suka rawaito shi, Sheikh Albani kuma ya inganta shi.

Bisa ga ɗabi'ar mutum, yana son binnanci, kuma ba ya so rayuwa shi kaɗai, don haka yake jin kamar ya zamar masa dole a sami taimakekeniya a tsakaninsa da wani, kamar yadda ya zamar masa dole ya yi hulɗa tare da wasu. Kwatsam sai musulunci ya zo ya ƙarfafi wannan ɗabi'a ya shar'anta wasu ibadu da ba a yinsu sai a cikin ayari, kamar irin su sallar jam'i da juma'a da idi biyu da sauransu.

Yana daga tilas ɗin rayuwa, shi ne, mutum ya zaɓawa kansa abokin hulɗa tare da shi, wanda zai riƙa nusar da shi da tunatar da shi a duk lokacin da ya shagala ko ya manta. Wanda kuma zai riƙa sanar da shi abin da ya jahilta.

Kuma a kodayaushe akan gane mutum ne da abokin hulɗarsa. Kamar yadda wani mawaƙi yake cewa: Ina kana son ka san mutum to kalli abikinsa. Duk aboki da abokinsa yake koyi. Idan abokin asharari ne to maza ka guje shi, idan kuwa na kirki ne to ka matse shi, sai ka shiriya.

Ya bayin Allah! Haƙiƙa Allah ya shar'anta mana ƙaunatarsa da ƙaunatar manzonsa da kuma muminai, kuma tabbatuwar hakan na daga mafi ƙarfin igiyar imani.

Kamar yadda Allah ya tilasta mana yin ƙiyayyar duk wani abu da ya saɓa Allah da Manzonsa. Allah maɗaukaki yana cewa:

﴿ إِنَّمَا وَلِيُّكُمُ ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱلَّذِينَ يُقِيمُونَ ٱلصَّلَوٰةَ وَيُؤۡتُونَ ٱلزَّكَوٰةَ وَهُمۡ رَٰكِعُونَ ٥٥ وَمَن يَتَوَلَّ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ فَإِنَّ حِزۡبَ ٱللَّهِ هُمُ ٱلۡغَٰلِبُونَ ٥٦ ﴾ [المائدة: ٥٥ – ٥٦].

(Haƙiƙa Allah ne majiɓincin al'amuranku da Manzonsa da kuma muminai waɗanda suka ba da gaskiya, waɗanda kuma suke tsai da salla da ba da zakka, suna masu ƙanƙantar da kai, duk kuwa wanda ya jiɓinci Allah da manzonsa da kuma waɗanda suka ba da gaskiya, to haƙiƙa rundunar Allah su ne masu rinjaye).

Yana daga cikin amfanin imani da waɗandann ayoyi zaɓawa kai abokan ƙwarai. Allah ya ce:

﴿ لَّا تَجِدُ قَوۡمٗا يُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ يُوَآدُّونَ مَنۡ حَآدَّ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَلَوۡ كَانُوٓاْ ءَابَآءَهُمۡ أَوۡ أَبۡنَآءَهُمۡ أَوۡ إِخۡوَٰنَهُمۡ أَوۡ عَشِيرَتَهُمۡ ﴾[المجادلة: ٢٢].

(Ba za ka sami mutanen da suka ba da gaskiya da Allah da ranar lahira ba suna ƙaunar waɗanda suke gaba da Allah da manzonsa ba, ko da kuwa sun kasance iyayensu ne, ko ‘ya’yansu, ko ‘yan uwansu ko kuma danginsu).

Irin abin da wannan aya ta ƙunsa na tsawatarwa da hani kan ƙaunata da jibintar maƙiyan Allah da manzonSa ya zo a wasu ayoyin daban kamar faɗin Allah Maɗaukaki:

﴿ قَدۡ كَانَتۡ لَكُمۡ أُسۡوَةٌ حَسَنَةٞ فِيٓ إِبۡرَٰهِيمَ وَٱلَّذِينَ مَعَهُۥٓ إِذۡ قَالُواْ لِقَوۡمِهِمۡ إِنَّا بُرَءَٰٓؤُاْ مِنكُمۡ وَمِمَّا تَعۡبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ كَفَرۡنَا بِكُمۡ وَبَدَا بَيۡنَنَا وَبَيۡنَكُمُ ٱلۡعَدَٰوَةُ وَٱلۡبَغۡضَآءُ أَبَدًا حَتَّىٰ تُؤۡمِنُواْ بِٱللَّهِ وَحۡدَهُۥٓ ﴾ [الممتحنة: ٤].

“Haƙiƙa kyakkyawan abin koyi ya kasance a gare ku game da (Annabi) Ibrahim da waɗanda suke tare da shi, lokacin da suka ce da mutanensu, ba mu ba ku kuma, ba mu ba abin da kuke bauta wanda ba Allah, mun kafirce muku kuma ƙiyayya da gaba sun bayyana tsakaninmu da ku har abada sai sanda kuka ba da gaskiya da Allah Shi kaɗai”.

Da kuma faɗin Allah:

﴿ مُّحَمَّدٞ رَّسُولُ ٱللَّهِۚ وَٱلَّذِينَ مَعَهُۥٓ أَشِدَّآءُ عَلَى ٱلۡكُفَّارِ رُحَمَآءُ بَيۡنَهُمۡۖ ﴾ [الفتح: ٢٩].

(Muhammadu Manzon Allah ne, kuma waɗanda suka ba da gaskiya da shi masu tsanani ne a kan kafirai, kuma masu tausayin junansu ne).

Da kuma faɗinsa:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مَن يَرۡتَدَّ مِنكُمۡ عَن دِينِهِۦ فَسَوۡفَ يَأۡتِي ٱللَّهُ بِقَوۡمٖ يُحِبُّهُمۡ وَيُحِبُّونَهُۥٓ أَذِلَّةٍ عَلَى ٱلۡمُؤۡمِنِينَ أَعِزَّةٍ عَلَى ٱلۡكَٰفِرِينَ ﴾ [المائدة: ٥٤].

(Ya ku waɗanda kuka ba da gaskiya, duk wanda ya yi ridda daga cikinku ya bar addininsa to da sannu Allah zai zo da wasu mutane da yake son su, su ma suke son sa, masu ƙasƙantar da kai ga muminai, masu tsananta wa kafirai).

Da kuma faɗinsa:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ قَٰتِلُواْ ٱلَّذِينَ يَلُونَكُم مِّنَ ٱلۡكُفَّارِ وَلۡيَجِدُواْ فِيكُمۡ غِلۡظَةٗۚ وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلۡمُتَّقِينَ ١٢٣ ﴾ [التوبة: ١٢٣].

(Ya ku waɗanda suka yi imani ku yaƙi kafiran da suke kusa da ku, kuma su sami tsanani daga gare ku).

Da kuma faɗinsa:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ جَٰهِدِ ٱلۡكُفَّارَ وَٱلۡمُنَٰفِقِينَ وَٱغۡلُظۡ عَلَيۡهِمۡ ﴾ [التحريم: ٩].

(Ya kai wannan Annabi ka yaƙi kafirai da munafuƙai, kuma ka tsananta musu).

Da dai wasu ayoyi daban-daban waɗanda ba waɗannan ba.

Ke nan waɗannan nassoshi na bayyana mana wajabcin riƙar abokan ƙwarai da yin watsi da miyagun abokai.

Ya bayin Allah! A kodayaushe mai hankali yana gujewa miyagun abokai, kamar yadda yake gujewa zaki saboda ya san babu alheri tare da su, kuma duk wanda ke zama da su ya haɗu da taɓewa. Bisa ga misali kalli faɗin Allah maɗaukaki:

﴿ وَيَوۡمَ يَعَضُّ ٱلظَّالِمُ عَلَىٰ يَدَيۡهِ يَقُولُ يَٰلَيۡتَنِي ٱتَّخَذۡتُ مَعَ ٱلرَّسُولِ سَبِيلٗا ٢٧ يَٰوَيۡلَتَىٰ لَيۡتَنِي لَمۡ أَتَّخِذۡ

فُلَانًا خَلِيلًا ﴿٢٨﴾ لَّقَدْ أَضَلَّنِي عَنِ ٱلذِّكْرِ بَعْدَ إِذْ جَآءَنِيۗ وَكَانَ ٱلشَّيْطَٰنُ لِلْإِنسَٰنِ خَذُولًا ﴿٢٩﴾ ﴾
[الفرقان: ٢٧ – ٢٩].

(Ranar da azzalumi zai rika cizon yatsunsa yana cewa: “Kaicona ina ma na bi hanya tare da Manzo! Kaicona ina ma da ban riki wane aboki ba? Hakika ya ɓatar da ni daga bin Alkur’ani bayan ya zo mini». Kuma shaiɗan ya kasance mai taɓar da mutane ne).

Sannan kuma hakika Manzon Allah (ﷺ) a lokaci guda ya kwaɗaitar da al’umma a kan zama da abokan kwarai, ya kuma tsawata a kan zama da miyagun abokai. Kamar a cikin hadisin da aka karɓo daga Abu Musa Allah ya yarda da shi ya ce: Hakika manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Kwatankwacin zama da abokin kwarai, da mugun aboki kamar zama da mai sayar da turare ne, da zama da makeri. shi mai sayar da turare ko dai ya sam maka, ko ka saya, ko kuma ka ji kamshi. Shi kuwa makeri ko dai ya kona maka sutura, ko kuma ka ji kauri”. Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

Malam Muhallab ya ce: “A cikin wannan hadisin akwai bayanin albarkar zama da mutanen kirki. Da ambaton aikin alheri. Da kuma kara kaimi a kan yin aikin kwarai. Don haka ne ma Manzo ya yi umarni da zama da malamai da kuma lazimtar guraren ambaton Allah. Manzo (ﷺ) ya kwatanta abokin kwarai da mai sayar da turare wanda idan bai sam maka ba, to ba za ka rasa jin kamshi ba".

Ba ku ji abin da Lukmanu ya ce wa ɗansa ba: “Kai ɗana ka zauna da malamai, kuma ka matse su da gwiwoyinka, hakika Allah na raya zukata da hasken hikima kamar yadda yake raya kekasasshiyar kasa da ruwan sama".

Ya kuma cewa, da shi: “Mai yiwuwa ne ka dace da samun rahama idan rahama ta sauka gare su, (wato su malaman), wannan shi ne amfanin zama da masu martaba da yin kiciɓis da su".

Haka ma malam Aini ya samo bayani daga wani malami cewa: “Ka zauna da wanda zamanka da shi zai sa ka karu a addininka, ko ka karu da ilimi, ko aikin kwarai da ake yi, ko kuma wata kyakkyawar ɗabi’a da yake da ita. Hakika idan mutum yana zama da wanda zama da shi ke sa shi tuna lahira, to kuwa ba makawa Allah zai datar da shi da samun wani gwargwado na alherin da hakan ke samarwa. To in kuwa haka ne yi kokari ka sami abokin zaman zikiri da karatun Alkur’ani. Abin nufi dai hana zama da wanda za a cutu da zama da shi a addinince, ko kuma a duniyance. Sannan kuma da kwaɗayin zama da wanda za a karu da shi a addini da rayuwa".

Shi ma wani bawan Allah ya ce: “Ka nisanci mugun aboki, ka datse igiyar alaka da shi, idan kuwa ba yadda ka iya da shi, to ka san dabarar zama da shi. Ka nace wa abokin kirki ka guji jayayya da shi, ka dace da samun tatacciyar kauna, matukar dai ba za ka yi ja-in-ja da shi ba. Duk mutumin da ke yin abin kirki ga wanda kirki bai dame shi ba, to kuwa zai tarar da abin kirkin da ya yi a banza an yi watsi da shi. Allah yana da aljanna mai faɗin sammai, sai dai fa kuma a zagaye take da abubuwan ki.

Ya Allah! Ka gafarta min dukkanin zunubina, da na masu sauraro na, da na dukkan musulman duniya gabaɗaya, haƙiƙa kai mai yawan gafara mai yawan jinƙai.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga Annabinmu Muhammad da iyalansa da sahabbansa da wanda ya bi hanyarsa har zuwa ranar sakamako.

Bayan haka: Ya bayin Allah! Babu shakka ribar abokantakar ƙwarai a bayyane take, a fili ƙarara ga ɗaiɗaiku, da ayarin jama'a, kuma daga haka ake samun nagartar daidaituwa, daga mutum ɗaya da jama'a. Samuwar nagartar jama'a shi ke yawaita albarkatun da Allah ke yin buɗinsu ta sama da ƙasa, kamar yadda Allah ya ce game da mutanen alƙaryu:

﴿ وَلَوۡ أَنَّ أَهۡلَ ٱلۡقُرَىٰٓ ءَامَنُواْ وَٱتَّقَوۡاْ لَفَتَحۡنَا عَلَيۡهِم بَرَكَٰتٖ مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلۡأَرۡضِ وَلَٰكِن كَذَّبُواْ فَأَخَذۡنَٰهُم بِمَا كَانُواْ يَكۡسِبُونَ ٩٦ ﴾ [الأعراف: ٩٦].

(Da dai mutanen alƙaryu sun ba da gaskiya sun kuma ji tsoron (Allah) to ba shakka da mun buɗe musu ƙofofinn albarkatai ta sama da kuma ƙasa, sai dai sun ƙaryata, sai muka kama su da abin da suka kasance suna aikatawa).

Imamul Baghawi ya ce: "Wato da an yi ta saukar da ruwan sama, kuma a yi ta fitar da tsirrai daga ƙasa, a kuma yaye fari da yunwa".

Ya 'yanuwa! Dukkanin 'yan aljanna abokan ƙwarai ne, kamar yadda Allah maɗaukaki ya ce:

﴿ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ كَانَتۡ لَهُمۡ جَنَّٰتُ ٱلۡفِرۡدَوۡسِ نُزُلًا ١٠٧ ﴾ [الكهف: ١٠٧].

(Haƙiƙa waɗanda suka ba da gaskiya, suka kuma yi ayyuka na gari to aljannar firdausi ce mmasaukinsu).

Da kuma faɗinsa:

﴿ وَنَزَعۡنَا مَا فِي صُدُورِهِم مِّنۡ غِلٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهِمُ ٱلۡأَنۡهَٰرُۖ ﴾ [الأعراف: ٤٣].

(Kuma mun zare abin da yake cikin zukatansu na ƙullata ƙoramu suna gudana ta ƙarƙashinsu).

Kuma dai Allah yana cewa:

﴿ وَنَزَعۡنَا مَا فِي صُدُورِهِم مِّنۡ غِلٍّ إِخۡوَٰنًا عَلَىٰ سُرُرٖ مُّتَقَٰبِلِينَ ٤٧ لَا يَمَسُّهُمۡ فِيهَا نَصَبٞ وَمَا هُم مِّنۡهَا بِمُخۡرَجِينَ ٤٨ ﴾ [الحجر: ٤٧ – ٤٨].

"Muka cire abin da ke cikin zukatansu na ƙullata (suka zama) 'yan uwa (suna) bisa gadaje suna fuskantar juna. Wata cuta ba za ta same su ba, kuma ba za a fitar da su daga cikinta ba".

Ya bayin Allah! Haƙiƙa magabata Allah ya jiƙansu da rahama sun fahimci wannan batu yadda ya kamata kuma sun ba shi cikakkiyar kulawa kamar yadda Annabi ya raine su a kan hakan.

Imamul Bukhari ya rawaito hadisi cikin sahihin littafinsa, wanda aka karɓo shi daga Abi Juhaifa ya ce manzon Allah ya ƙulla 'yan uwanta tsakanin Salman

da Abid Darda'i, sai Salman ya ziyarci Abid Darda'i, sai ya ga Ummid Darda'i, daƙal-daƙal, sai ya ce da ita, "Ke kuwa me ya same ki"? Ta ce: "Ɗan uwanka Abud Darda'i ba shi da buƙatar duniya" (wato bai damu da mace ba). Sai Abud Darda'i ya zo, sai ya dafa masa abinci sannan ya ce masa, "Ci abinci, ni ina azimi". Sai shi kuma ya ce, "Ba zan ci ba har sai in ka ci". Sai ya ci. Da dare ya yi sai Abud Darda'i ya tafi yin tsaiwar dare, sai Salman ya ce da shi, "Kwanta ka yi bacci". Sai ya kwanta ya yi barci. Sannan ya kuma tafiya zai yi tsaiwar dare, sai ya ƙara cewa da shi, "Kwanta ka yi barci". Yayin da kashin ƙarshe na dare ya shiga, Salman sai ya ce: "Tashi yanzu". Sai suka tsahi suka yi sallah. Sai Salman ya ce da shi: "Tabbas Ubangijinka yana da haƙƙi a kanka, iyalanka ma suna da haƙƙi a kanka, to ka bai wa duk wani mai haƙƙi haƙƙinsa". Sai ya je wajen Annabin ya ambata masa haka, sai Annabin (ﷺ) ya ce: "Salman ya yi gaskiya".

Ku duba ku gani- ya bayin Allah-! Ya ya suka kasance suna taimakon juna a kan abin kirki da tsoron Allah, to haka fa 'yan'uwantaka ta gari take.

Ya bayin Allah! Ku sani haƙiƙa duk inda watsattsun abokai suke ba sa wani abin kirki, sai dai su hana ka bin hanyar Allah. Bisa ga misali, kalli labarin mutuwar Abu Ɗalib, da irin yadda miyagun abokai suka hana shi yin imani. Ya zo cikin littafin Bukhari, an karɓo daga Sa'id ɗan Musayyib, daga babansa, Allah ya yarda da shi, ya ce, "Yayin da mutuwa ta zowa Abu Ɗalib, Manzon Allah (ﷺ) ya zo wajnsa, sai ya tarar da Abu Jahil, da Abdullahi ɗan Abu Umayya ɗan Mugirah, sai ya ce: "Ya baffa! Ka ce, La'ilaha illal lah, kalma ce da zan tsaya maka a dalilinta a wajen Allah". Sai Abu Jahil da Abdullahi ɗan Umayya suka ce: "Yanzu a ce ka ƙyamaci addinin (babanka) Abdulmuɗɗalib?!" Manzon Allah bai gushe ba yana bijirar masa kalmar shahada, su kuma suna maimaita faɗa masa abin da suka faɗa, har dai Abu Ɗalib a ƙarshen ya ce musu "Ina nan kan addinin (babana) Abdulmuɗɗalib". Ya ƙi faɗar La'ilaha ilal lah. Manzon Allah ya ce: "Wallahi zan nema maka gafarar Allah matuƙar dai ba a hana ni nema maka ba". Sai Allah ya saukar da faɗarsa:

﴿ مَا كَانَ لِلنَّبِيِّ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَن يَسۡتَغۡفِرُواْ لِلۡمُشۡرِكِينَ وَلَوۡ كَانُوٓاْ أُوْلِي قُرۡبَىٰ مِنۢ بَعۡدِ مَا تَبَيَّنَ لَهُمۡ أَنَّهُمۡ أَصۡحَٰبُ ٱلۡجَحِيمِ ١١٣ ﴾ [التوبة: ١١٣].

(Bai kamata ba ga Annabi da waɗanda suka yi imani su riƙa nema wa mushirikai gafara, koda kuwa makusanta ne, bayan sun gane cewa su 'yan wuta ne).

Kuma Allah ya saukar da aya mai zuwa a kan batun imanin Abi Ɗalib sai ya ce da ManzonSa (ﷺ):

﴿ إِنَّكَ لَا تَهۡدِي مَنۡ أَحۡبَبۡتَ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ يَهۡدِي مَن يَشَآءُۚ ﴾ [القصص: ٥٦].

(Haƙiƙa kai ba za ka iya shiryar da wanda kake so ba, sai dai Allah yana shiryar da wanda ya so).

Ya ku iyaye dukkaninku makiyaya ne, kuma kowannenku abin tambaya ne game da abin da aka ba shi kiwonsa. Kuma Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: "Babu wani bawa da Allah zai ba shi kiwon wasu ababen kiwo a wayi gari ya mutu a ranar mutuwarsa yana mai ha'intar ababen kiwonsa, face sai Allah ya haramta

masa shiga aljanna”.

Haƙiƙa yana daga cikin ha'inci, uba ya bar ɗansa sasakai ba ya tambayar ina ɗansa ya tafi, a ina ya kwana, kuma tare da wa yake kai kawo, sannan kuma uba bai san ɗansa yana karaɗe gari daddare da shaiɗanun mutanen da suke saɓule masa addininsa da kuma gurɓata masa hankali ba.

Don haka ahir da miyagun abokai, da kuma mugayen abokan zama. Dole ne a kan matsahi ya zaɓi abokan ƙwarai daga mutanen kirki masu hankali da nagarta waɗanda za su riƙa taimaka masa a kan gaskiya kuma suna nuna masa ita.

Ina neman tsarin Allah daga sharrin shaiɗan la'ananne:

﴿ مَّنۡ عَمِلَ صَٰلِحٗا فَلِنَفۡسِهِۦۖ وَمَنۡ أَسَآءَ فَعَلَيۡهَاۗ وَمَا رَبُّكَ بِظَلَّٰمٖ لِّلۡعَبِيدِ ٤٦ ﴾ [فصلت: ٤٦].

(Duk wanda ya yi aiki nagari, to kansa ya yi wa, wanda kuma ya munana a kansa ya yi wa, Ubangijinka ba mai zaluntar bayi ba ne).

SADA ZUMUNCI

Manufofin huɗubar

- Bayyana haƙiƙanin sada zumunci.
- Bayanin falalar sada zumunci.
- Tsoratarwa da razanarwa akan yanke zumunci.
-

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga shirrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammad bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammad (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Ya ‘yan uwa : A yau huɗubarmu tana magana ne akan wani abu mai girma, abu ne da Allah yake shinfiɗa arziki da shi, ya jinkirta ajali saboda shi, ya sanya albarka da shi a dukiyar mutum, wannan abu kuwa ba komai ba ne face sada zumunci.

Sada zumunci shi ne kyautata wa makusanta, waɗanda su ne Iyaye da ‘yan uwa maza da mata, da ma duk waɗanda mutum yake da zumunci da su, ta ɓangaren babansa, ko babar shi, ko ta ɓangaren ɗansa ko ‘yarsa.

Ayoyi masu yawa da hadisai sun nuna wajabcin sada zumunci, da haramcin yanke zumunci da bayanin falalar kyautatawa ‘yan uwa.

Allah Maɗaukakin Sarki ya yabi waɗanda suke sada abin da Allah ya ce a sada shi, a cikin littafinsa mai girma inda yake cewa :

﴿ وَٱلَّذِينَ يَصِلُونَ مَآ أَمَرَ ٱللَّهُ بِهِۦٓ أَن يُوصَلَ وَيَخۡشَوۡنَ رَبَّهُمۡ وَيَخَافُونَ سُوٓءَ ٱلۡحِسَابِ ٢١ ﴾ [الرعد: ٢١].

Ma’ana : “Da waɗanda suke sada abin da Allah ya yi umarni da shi, suna tsoron Ubangijinsu, sannan suna tsoron mummunan hisabi”. (Ar-Ra’ad : 21).

Allah ya kushe waɗanda suke yanke abin da Allah ya yi umarni da a sadar da shi, kushewa mai tsanani ya ce :

﴿ وَٱلَّذِينَ يَنقُضُونَ عَهۡدَ ٱللَّهِ مِنۢ بَعۡدِ مِيثَٰقِهِۦ وَيَقۡطَعُونَ مَآ أَمَرَ ٱللَّهُ بِهِۦٓ أَن يُوصَلَ وَيُفۡسِدُونَ فِي ٱلۡأَرۡضِ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمُ ٱللَّعۡنَةُ وَلَهُمۡ سُوٓءُ ٱلدَّارِ ٢٥ ﴾ [الرعد: ٢٥]

Ma’ana : “Da waɗanda suke warware alƙawarin Allah bayan ƙullashi, kuma suke yanke abin da Allah ya yi umarni da a sada shi, suna ɓarna a bayan ƙasa, waɗannan suna da la’ana da mummunan gida” (Ar-ra’ad : 25).

Allah Maɗaukakin Sarki ya yi wasiyya da a kyautata wa makusanta inda yake cewa :

﴿ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ ٱلَّذِي تَسَآءَلُونَ بِهِۦ وَٱلۡأَرۡحَامَۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلَيۡكُمۡ رَقِيبٗا ﴾ [النساء: ١]

Ma’ana : “Ku ji tsoron Allah wanda kuke magiya da shi, kuma ki kiyaye zumunci, haƙiƙa Allah mai kula ne a kanku”. (Annisa’I : 1).

Waɗannan ayoyi masu girma suna umarni da a sada zumunci, suna hana yanke zumunci, amma sai dai abin takaici da dama daga cikin musulmi a yau sun yanke zumuncinsu, kamar ba su taɓa jin waɗannan ayoyi ba.

Bayin Allah : Yanke zumunci laifi ne babba, Allah Maɗaukakin Sarki ya yi alƙawarin yanke albarkar duk wanda yake yanke zumunci. An karɓo daga Abu Hurairata – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Allah ya halicci halitta, da ya gama, sai zumunci ya ce, wannan (Ya Ubangiji) shi ne wurin fakewar mai yanke zumunci a wurinka” Sai Ubangiji ya ce, “Kwarai kuwa, amma ba zaka yarda ba (Ya kai zumunci) in sada duk wanda ya sada ka, in yanke duk wanda ya yanke ka ba?” sai zumunci ya ce, “Na yarda ya Ubangiji” Sai Allah ya ce, “na baka wannan”. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce, in kuna son tabbatar da haka ku karanta faɗin Allah : “Ashe bai kusata ba, in kun bada baya ku yi ɓarna a bayan ƙasa ku yanke zumunciku ba”. Bukhari ne ya rawaito.

An karɓo daga Anas ɗan Malik – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Zumunci jijiya ce da take haɗe da Al’arshi, ta yi magana da harshe mai kaifi ta ce, “Ya Allah ka sadar da wanda ya sadar da ni, ka yanke wanda ya yankeni” Sai Allah ya ce, “Ni ne mai rahama mai jinƙai, na tsago wa zumunci suna daga sunana (Arahim), wanda duk ya sada shi zan sada shi, wanda kuwa ya yanke shi zan yanke shi” Bukhari ne ya rawaito shi a cikin littafin “Al-adab”.

Waɗannan hadisai suna nuna cewa duk wanda yake sada zumunci Allah zai sada shi da alheri da albarka, wanda kuwa ya yanke zumunci Allah zai yanke masa alheri da albarka.

Sada zumunci yana ɗaya daga cikin halayen Manzon Allah (ﷺ) kamar yadda Abu Sufyan yake siffata shi da cewa : “Ya kasance yana umartarmu da sallah da gaskiya, da kamewa da sada zumunci”. Bukhari ne ya rawaito shi. Don haka sada zumunci yana ɗaya daga cikin abubuwan da Manzon Allah ya fara kiran mutane zuwa gareshi.

Ya ‘yan uwa : Sada zumunci mataki – mataki ne, wani matakin ya fi wani : Da farko : gamammen sada zumunci, shi ne sada zumuncin wanda addini da tsoron

Allah ya ya haɗa ku, ana yin wanna sada zumuncin ne ta hanyar yi wa juna nasiha, da shawara, da son juna, da adalci, da bawa juna haƙƙinsu, da barin cutarwa, da sauransu. Mataki na biyu : Shi ne sada zumuncin wanda kuke da kusanci da shi, ‘yan uwanka da sauransu.

Yaku bayin Allah : Sada zumunci sababi na ƙaruwar rayuwa, da yawan dukiya, alƙawari ne daga mai gaskiya abin gasgata wa, wanda baya magana da son zuciya, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Wanda duk yake so a buɗaɗa masa arziƙinsa, a jinkirta masa rayuwarsa, to ya sada zumuncinsa”. Bukhari da Muslim

Manzon Allah (ﷺ) ya bayyana cewa sada zumunci na haƙiƙa shi ne wanda zai sada zumuncinsa yayin da shi aka yanke masa, amma wanda zai sada kamar yadda ake sada na shi, to wannan ya yi ramuwa ne kawai, duk da cewa sada zumunci ne amma dai wanda ya sada zumuncin ‘yan uwan da suka yanke masa ladansa ya fi girma. Manzon Allah (ﷺ) yana cewa : “wanda yake ramuwa ba mai cikakken sada zumunci ba ne, cikakken mai sada zumunci shi ne wanda idan an yanke zumuncin yake sada shi”.

Ya ‘yan uwana musulmi : A cikin sada zumunci akwai ɗimbin alheri da fa’idoji da Allah ya tattara a ciki, daga cikinsu :

- Sada zumunci alama ce ta cikar imani da kyan musuluncin mutum.
- Sada zumunci dalili ne da yake sa a yawaltar arziki da albarkar rayuwa.
- Sada zumunci ya kan sa bawa ya samu yardar Allah Maɗaukakin Sarki.

Kaɗan kenan daga fa’idojin sada zumunci a addinin musulunci. Saboda haka magabatanmu na ƙwarai suka ba da kyakkyawan misali wajen bayanin mahimmancinsa.

Sayyidina Umar ɗan Khaɗɗab – Allah ya yarda da shi – yana cewa, “Ku san dangantakarku, sannan ku sada zumuncinku, Wallahi za a samu mutumin da tsakaninsa da ɗan uwansa akwai wani abu, amma da ya san irin dangantakar da take tsakaninsu ta jini da ‘yan uwantaka, da ba zai iya keta masa mutunci ba”. (Duba Tafsirin Imamuɗ Ɗabari J 1/ sh 144).

Imam Aɗa’u ɗan Rabah – Allah ya yi masa rahama – ya ce, “Wallahi in sanya dirhami ɗaya a wajen taimakawa makusantana, ya fi min guda dubu da zan sanya su a wata buƙata” Sai wani ya ce masa “Ya baban Muhammad idan ‘yan uwan nawa suna da wadata irin tawa fa?” Sai ya ce, “Koda sun fika wadata”. (Duba littafin Makarimul Aƙlaƙ na Ibnu Abi Dunya sh 62).

Imam Sa’id ɗan Musayyib – Allah ya yi masa rahama – ya ce yayin da ya ga ya bar wasu kuɗaɗe “Ya Allah ka sani, ban tara waɗannan kuɗin ba sai don in kiyaye addinina da dangantaka da su. Babu alheri ga wanda ba ya tara dukiyar da zai biya bashinsa da ita, ya sada zumuncinsa, ya kuma kame mutuncinsa”. (Duba littafin Al-aadabush Shar’iyya na Ibnu Muflih J3/sh 269).

Imam Amru ɗan Dinar – Allah ya yi masa rahama – yana cewa : “Babu wani taku da ya fi girman lada fiye da takun mai sada zumunci, sai dai takun da aka yi zuwa farilla”.

Wannan kaɗan kenan daga cikin maganganun magabata na ƙwarai da suke nuna mahimmanci sada zumunci a musulunci. Kuma wannan yana nuna haɗarin da wanda ba ya sada zumunci yake ci!.

Muna roƙon Allah Maɗaukakin Sarki ya sanya mu cikin masu sada zumuncinsu, haƙiƙa shi mai iko ne aka haka.

Allah ya yi mana albarka cikin abin da muka ji, daga Alƙur'ani da Sunnah, ya yi mana gafara, haƙiƙa shi mai iko ne akan komai.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah, Kyakkyawan ƙarshe yana ga masu tsoron Allah, Tsira da Aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, Manzon Allah (ﷺ) da iyalansa da Sahabbansa da waɗanda suka bi su gaba ɗayansu, har zuwa ranar sakamako. Bayan haka:

Ya ku musulmi : Kamar yadda sada zumunci yake da lada mai girma, hakanan yanke zumunci yake tattare da laifi mai girma, na farko dai mai yanke zumunci ba zai shiga Aljannah ba, An karɓo daga Jubair ɗan Muɗ'im, – Allah ya yarda da shi – ya ce, na ji Manzon Allah (ﷺ) yana cewa : "Mai yanke zumunci ba zai shiga Aljannah ba". Bukhari ne ya rawaito.

Hakanan mai sada zumunci ana yanke masa to kamar wanda ake watsa yashi ne mai tsananin zafi a fuska. An karɓo daga Abu Huraira – Allah ya yarda da shi – ya ce, wani mutum ya zo wajen Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Ya Manzon Allah, ina da 'yan uwa waɗanda nake sada zumuncinsu, amma su suna yanke min, ina kyautata musu, amma su suna munana min, suna min wauta amma ina haƙuri da su" Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "In haka ne kuwa, to haƙiƙa kamar kana watsa musu yashi ne mai tsananin zafi, kuma ba za ka gushe ba kana tare da mataimaki daga wajen Allah matuƙar kana kan haka".

Imam Annawawi – Allah ya yi rahama – ya ce, "Abin da ake nufi kamar kana ciyar da su wani yashi ne mai zafi, an kamanta irin abin da zai same su na raɗaɗi da irin abin da yake samun wanda yake cin yashi mai tsananin zafi".

Yana daga cikin uƙubar yanke zumunci ya kan jawo la'antar Ubangiji Allah Maɗaukakin Sarki da azabarsa. Allah ya ce:

﴿ فَهَلۡ عَسَيۡتُمۡ إِن تَوَلَّيۡتُمۡ أَن تُفۡسِدُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَتُقَطِّعُوٓاْ أَرۡحَامَكُمۡ ٢٢ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ لَعَنَهُمُ ٱللَّهُ فَأَصَمَّهُمۡ وَأَعۡمَىٰٓ أَبۡصَٰرَهُمۡ ٢٣ ﴾ [محمد: ٢٢ - ٢٣].

"Ashe bai kusata ba, in kun bada baya ku yi ɓarna a bayan ƙasa, ku yanke zumunciku ba. To waɗannan su ne waɗanda Allah ya tsine wa, ya kurmantar da su, ya makantar da ganinsu". (Muhammad : 22).

﴿ وَٱلَّذِينَ يَنقُضُونَ عَهۡدَ ٱللَّهِ مِنۢ بَعۡدِ مِيثَٰقِهِۦ وَيَقۡطَعُونَ مَآ أَمَرَ ٱللَّهُ بِهِۦٓ أَن يُوصَلَ وَيُفۡسِدُونَ فِي ٱلۡأَرۡضِ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمُ ٱللَّعۡنَةُ وَلَهُمۡ سُوٓءُ ٱلدَّارِ ٢٥ ﴾ [الرعد: ٢٥].

Ma'ana : "Da waɗanda suke warware alƙawarin Allah bayan ƙullashi, kuma suke yanke abin da Allah ya yi umarni da a sada shi, sannan suna yin ɓarna a

bayan ƙasa, waɗannan suna da la'ana da mummunan gida" (Ar-ra'ad : 25).

Mafi girman yanke zumunci shi ne yanke zumuncin iyaye, sannan sai waɗanda suka fi kusa da mutum, sai waɗanda suke bin su, haka dai, don haka Manzon Allah (ﷺ) yake cewa : "Ba zan faɗa muku mafi girman zunubai ba (ya faɗa har sai uku), sai suka ce : "faɗa mana ya Manzon Allah" Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Shirka da Allah, sai saɓa wa iyaye…". Babu ko shakka wannan hadisi yana nuna mana girman yanke zumuncin iyaye, kasancewarsa cikin mafi girman zunubai!.

Daga cikin uƙubar yanke zumunci ana gaggauta wa mai yin sa uƙuba a duniya tun kafin zuwansa lahira, Manzon Allah (ﷺ) yana cewa : "Babu wani zunubi da ya fi cancanta Allah ya gaggauta wa mai yin sa uƙuba a duniya – duk da irin abin da aka tanadar masa a duniya – fiye da yanke zumunci da ƙetare iyaka".

Yaku masu sauraro : Ma'abota zumunci mataki – mataki ne, ga su kamar haka :

1. Ma'abota daidaitu da addini da tsoron Allah, waɗannan ana sada zumuncinsu, da abubuwan da suka gabata, zumuncin nasu gamamme ne ko keɓantacce ne.
2. Ma'abota bidi'a, fasiƙai, fajirai, to waɗannan sun kasu gida biyu :
   - Waɗanda suke bayyana bidi'arsu da fasiƙancinsu da fajircinsu, suna kira zuwa ga hakan, to waɗannan ana ƙaurace musu gaba ɗaya, kuma ƙaurace wa waɗannan yana daga cikin mafi girman kusanci ga Allah, ba ya dacewa a sassauci a cikinsa, Sai dai idan a cikin ƙaurace musu akwai wata musiba ko bala'i da zai iya samun mutum to ba laifi mutum ya zauna da su a matsayin larura, don gudun cutarwarsu.
   - Waɗanda suke ɓoye bidi'arsu da fasiƙancinsu, waɗannan za a yi musu mu'amalar da ake wa musulmin da ba a san halinsa ba.
3. 'Yan uwan da suke kafirai ne, suma sun kashi biyu :
   - Waɗanda ake yaƙi da su, waɗannan ba a sada zumuncinsu ana yanke musu gaba ɗaya, sai dai don gudun sharrinsu.
   - Waɗanda ba a yaƙi da su, waɗannan ana sada zumuncinsu, ana kyautata musu, kamar yadda hadisin Nana Asma'u ya nuna.

Ku ji tsoron Allah – Yaku bayin Allah – ku sada zumuncinku da ziyara da bada kyauta, da ciyarwa, ku sada zumuncinku da tausaya wa da jin ƙai juna, da sakin fuska, da girmamawa, zaku rabauta duniya da lahira, ku kiyayi yanke zumunci, saboda hakan sababin bala'i ne da hasara duniya da lahira.

TSORO DA KYAKKYAWAN FATA

Manufofin huɗubar

- Bayani a kan ma’anar tsoro da kyakkyawan fata.
- Fa’idarsu da muhimmancinsu a rayuwar ɗan adam musulmi.
- Umarni da jin tsoro da yin kyakkyawan fata.
- Falalar jin tsoron Allah, da kuma kykkyawan fata

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammadu bawansa ne manzonsa ne. (Yaku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron Allah yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Yaku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammadu (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (a addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta".

Bayan haka: Ya ku bayin Allah!

Haƙiƙa ayyuka na zukata suna daga cikin manyan abubuwa. Kuma suna da girman lada da babbar uƙuba. Ayyukan gaɓɓai suna tafiya kafaɗa da kafaɗa da ayyukan zukata. Zuciya ita sarauniya ce ta gangar jiki.

Abin da ake nufi da daidaiton zuciya shi ne, kaɗaita Allah Ta'ala, da girmama shi, da son shi da tsoron shi, da kykkyawan fatan rahmar shi da yi masa biyayya da gujewa saɓa masa.

Muslim ya ruwaito daga Abu Hurairata Allah ya yarda da shi ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle Allah ba gangar jikinku yake kallo ba, ko dukiyoyinku, a'a yana kallon zukatanku ne da ayykanku).

Imam Hasanul Basri ya ce da wani mutum: “Ka magance zuciyarka, babban abin da Allah Yake so ga bayi shi ne, guruwar zukatansu".

Yana daga cikin ayyukan zukata wanda yake zaburar da gaɓɓai a wajen yin kyawawan ayyuka, shi ne cusa mata tsoron Allah da kwaɗayin rahamarsa. Domin tsoron Allah shi yake yi wa zuciya jagora a wajen aiki na ƙwarai, tare da kare ta daga munanan ayyuka. Kyakkyawan fata kuma yana yi wa zuciya jagor wajen neman yardar Allah sakamakonsa, tare da zaburar da ita zuwa ga ayyukan ƙwarai, da hana ta munanan ayyuka.

Tsoron Allah yana kare ziciya daga bin sha'awe-sha'awenta, da yi tawata mata akan bin hanyar halaka. Yana kuma tura ta zuwa ga duk wani abu da zai gyara ta ta samu rabauta. Tsoron Allah wani ɓangare ne na kaɗaita Allah, saboda haka bai kamata wani ya ji tsoron wani ba irin tsoron da yake wa Allah. Yin hakan wani nau'i ne na shirka.

Allah ya yi umarni da aji tsoronsa, ka da a ji tsoron kowa sai shi. Allah ya cewa:

﴿ إِنَّمَا ذَٰلِكُمُ ٱلشَّيۡطَٰنُ يُخَوِّفُ أَوۡلِيَآءَهُۥ فَلَا تَخَافُوهُمۡ وَخَافُونِ إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَ ١٧٥ ﴾ [آل عمران: ١٧٥].

(Haƙiƙa shedan ne yake tsoratar da masoyansa. Don haka kar ku ji tsoronsu, ni kaɗai za ku ji tsorona, in dai kun kasance muminai(.

Hakanan yana cewa:

﴿ فَلَا تَخۡشَوُاْ ٱلنَّاسَ وَٱخۡشَوۡنِ وَلَا تَشۡتَرُواْ بِـَٔايَٰتِي ثَمَنٗا قَلِيلٗاۚ ﴾ [المائدة: ٤٤].

(Kada ku ji tsoron mutane, ni kaɗai za ku ji tsoro. Kada ku saida ayoyin Allah da ɗan kuɗi kaɗan).

Ya zo a hadisin Anas Ɗan Malik ya ce: Manzon Allah ya yi mana huɗuba ya ce: "da kun san abin da na sani da kun yi kuka diyawa, kuma kun yi dariya kaɗan». Sai sahabban Manzon Allah suka rife fuskokinsu da mayafansu sun kuku. Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

Kalmar tsoro tana nufin zuciyar bawa ta riƙa firgita tana razana da tunanin uƙubar Ubangijin Allah akan aikata wani aiki na haram, ko barin wani aiki na wajibi. Ko gazawa wajen aikata aikin mustabbi. Da jin tsoron daga Allah ya ƙi karɓar aikin mutum da ya yi na kirki. Don haka irin wannan tsoron ya gadarwa da zuciya gujewa ayyukan haramun, da gaggawa wajen aikata alheri.

Amma kalmar Khashyah, tana nufin tsoro Allah tare da ilimin saninsa da ganin girmansa. Shi ya sa Allah ya yi amfani da ita inda yake cewa:

﴿ إِنَّمَا يَخۡشَى ٱللَّهَ مِنۡ عِبَادِهِ ٱلۡعُلَمَٰٓؤُاْ ﴾ [فاطر: ٢٨].

(Kaɗai waɗanda suke tsoron Allah su ne malamai).

Ya zo cikin Hadisin Bukhari da Muslim, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle ni na fi ku tsoron Allah, na fi ku taƙawa gare shi).

Ya ku Musulmi!

Allah ya yi alƙawarin kyakkyawan lada ga duk wanda ya ji tsoronsa, kuma ya kame kansa ga barin bin son zuciya. Allah ya ce:

﴿ وَأَمَّا مَنۡ خَافَ مَقَامَ رَبِّهِۦ وَنَهَى ٱلنَّفۡسَ عَنِ ٱلۡهَوَىٰ ٤٠ فَإِنَّ ٱلۡجَنَّةَ هِيَ ٱلۡمَأۡوَىٰ ٤١ ﴾ [النازعات: ٤٠ – ٤١].

(Duk wanda ya ji tsoron tsayuwarsa a gaban Ubangijinsa, kuma ya hana kansa bin son zuciya, to lalle aljanna ce makomarsa).

Kuma haka yake cewa:

﴿ وَلِمَنۡ خَافَ مَقَامَ رَبِّهِۦ جَنَّتَانِ ﴿٤٦﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿٤٧﴾ ذَوَاتَآ أَفۡنَانٖ ﴿٤٨﴾ ﴾ [الرحمن: ٤٦ - ٤٨].

(Wanda duk ya ji tsoron tsayuwa gaba ga Ubangijinsa to yana da aljanna guda biyu ma'abociyar kyawawa rassa).

Imam Aɗa'u ya ce kowane reshe ya haɗa kaloli na kayan marmari.

Allah ya sake cewa:

﴿ وَأَقۡبَلَ بَعۡضُهُمۡ عَلَىٰ بَعۡضٖ يَتَسَآءَلُونَ ﴿٢٥﴾ قَالُوٓاْ إِنَّا كُنَّا قَبۡلُ فِيٓ أَهۡلِنَا مُشۡفِقِينَ ﴿٢٦﴾ فَمَنَّ ٱللَّهُ عَلَيۡنَا وَوَقَىٰنَا عَذَابَ ٱلسَّمُومِ ﴿٢٧﴾ إِنَّا كُنَّا مِن قَبۡلُ نَدۡعُوهُۖ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلۡبَرُّ ٱلرَّحِيمُ ﴿٢٨﴾ ﴾ [الطور: ٢٥ - ٢٨].

)Sai wani ɓangare daga cikin 'yan aljanna ya fuskanci wani ɓangaren suna masu tambayar junansa. Suka ce, «Da mun kasance a duniya muna cikin iyalanmu, muna masu tsoro, sai Allah ya yi mana baiwa ya tserar da mu daga azaba ta guba mai ƙuna. Da ma mun kasance muna bauta masa, haƙiƙa shi Ubangiji ya kasance mai karɓar addu'ar bawa ne mai jinƙai).

Wannan ya nuna mana cewa duk wanda ya ji tsoron Allah zai kumutar da shi daga duk wani abin ƙi, kuma ya yi masa baiwar kykkyawan ƙarshe.

Magabata sun kasance tsoron Allah yana rinjayarsu, tare da kyautata ayyuka. Kuma suna fatan samun rahamar Allah. Wannan yasa suka zama masu halin ƙwarai, masu kyawawan ayyuka.

Wata rana Umar ɗan Khaɗɗab Allah ya yarda da shi ya fita yana ran gadi dadaddare, sai ya jiyo wani mutum yana karanta suratuɗ-Ɗur. Sai ya sauka daga kan jakinsa, ya jingina da garu. Ya yi rashin ta tsawon wata ɗaya mutane na zuwa dubo shi. Ba wanda ya san mai yake damunsa.

Amirul muminina Aliyu (R.A), yake cewa a wani lokaci bayan gama sallar Asuba: "Haƙiƙa na ga sahabban manzon Allah, ban ga wani abu da yake kama da su ba. Haƙiƙa sun kasance suna wayar gari idanuwansu da fuskokinsu sun yi hazo-hazo, da ƙura-ƙura. Goshinsu sun yi tabo kamar gwiwar akuya. Sun kwana suna masu tsaiwa da sujjada ga Ubangijinsu. Idan sun wayi gari suna masu ambaton Allah. Suna layi kamar bishiyar da iska take kaɗawa. Idanuwansu na zubar da hawaye har rigunan jikinsu su jiƙe sharkaf saboda kuka». Abu Nu'aim ne ya ruwaito shi a littafin Hilyah.

Abu Hafs yake cewa: «Tsoron Allah bulalarsa ce da yake dawo da bijarrun bayinsa da ita». Hakanan yake cewa: «Tsoro Allah fitila ce a cikin zuciya».

Abu Sulaiman yana cewa: «Duk zuciyar da ta rasa tsoro a cikinta ta lalace kuma ta ruguje».

Tsoro na ƙwarai shi ne wanda yake zaburar da baya a kan aiki na ƙwarai, kuma ya hana aiki mummuna. Haka idan tsoro ya wuce ƙa'ida, to sai ya haifarwa mutum ɗebe ƙauna daga rahamar Allah.

Ibn Rajab yana cewa: tsoron da ya sanya mai shi sauke nauyin abin da aka ɗora masa, ya nisanci zunubai, to wannan shi ne abin da ake bukata na wajibi. In ya ƙaru ta yadda ya zaburar da shi wajen nafilfili to wannan duk ya zama falala. Idan kuma ya ƙaru akan haka, har ya gadarwa da mai shi rashin lafia ko ma mutuwa, kuwa wata damuwa ta dindindin wanda za hana shi yin wani kazarkazar to wani

tsoron ba ya da kyau».

Musulmi yana tsakanin tsoro biyu. Tsoron abin da ya riga ya wuce bai son mai Allah zai yi masa akansa ba. Da kuma tsoron abin da zai zo nan gaba bai son mai Allah zai hukunta masa ba.

Amma kyakkyawar fata shi ne kwaɗayin rahamar Allah, tare da yin aiki na ƙwarai, da kame kai daga aikata haramun. Haƙiƙa kwaɗayi da kyakkyawan fata ba ya kasancewa ga mutum, sai idan an gabatar da aiki na ƙwarai, an guji aikata munanan ayyuka, ko an tuba daga aikata su. Amma mutum ya ba aikin da wajaba akansa, ya riƙa bin soye-soyen zuciyarsa, yana kuma fatan samun rahamar Allah, to wannan shi ne ake cewa, amince makircin Allah, Allah kuma yana cewa:

﴿ أَفَأَمِنُواْ مَكۡرَ ٱللَّهِۚ فَلَا يَأۡمَنُ مَكۡرَ ٱللَّهِ إِلَّا ٱلۡقَوۡمُ ٱلۡخَٰسِرُونَ ٩٩ ﴾ [الأعراف: ٩٩].

(Shin sun amince wa makircin Allah ne. To babu wanda zai amincewa makircin Allah sai mutanen da suka asararru).

Allah ya yi bayanin cewa, kykkyawan fata shi ne wanda yake tare da kykkyawan ayyuka. Idan babu kyawawan ayyuka to babu shi. Allah yana cewa:

﴿ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَتۡلُونَ كِتَٰبَ ٱللَّهِ وَأَقَامُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَأَنفَقُواْ مِمَّا رَزَقۡنَٰهُمۡ سِرّٗا وَعَلَانِيَةٗ يَرۡجُونَ تِجَٰرَةٗ لَّن تَبُورَ ٢٩ ﴾ [فاطر: ٢٩].

“Haƙiƙa waɗanda suke karanta littafin Allah suka tsaida sallah, kuma suka ciyar daga abin da muka azurta su a ɓoye da sarari, suna kwaɗayin kasuwanci wanda babu asara a cikinsa).

Hakanan yana cewa:

﴿ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَٱلَّذِينَ هَاجَرُواْ وَجَٰهَدُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ أُوْلَٰٓئِكَ يَرۡجُونَ رَحۡمَتَ ٱللَّهِۚ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٢١٨ ﴾ [البقرة: ٢١٨].

(Haƙiƙa waɗanda suka yi imani, kuma suka yi hijira, suka yi jihadi don ɗaukaka kalmar Allah, to waɗannan su ne masu kwaɗayin rahamar Allah. Kuma Allah mai yawan gafara ne mai yawan jin ƙai).

Duk wanda ya ɗora kwaɗayinsa ga wanin Allah to haƙiƙa ya yi shirka.

Allah yana cewa:

﴿ فَمَن كَانَ يَرۡجُواْ لِقَآءَ رَبِّهِۦ فَلۡيَعۡمَلۡ عَمَلٗا صَٰلِحٗا وَلَا يُشۡرِكۡ بِعِبَادَةِ رَبِّهِۦٓ أَحَدَۢا ١١٠ ﴾ [الكهف: ١١٠].

(To duk wanda ya kasance yana fatan kyakkyawar haɗuwa da Ubangijinsa, sai ya yi aiki na ƙwarai, kuma kada ya haɗa wani da bautar Ubangijinsa).

Haƙiƙa kwaɗayi wata hanya ce zuwa ga Ubangiji. Ya zo a hadisi Manzon Allah ya ce, «Allah Ta’ala Ya ce: «Ni ina nan inda bawana yake zatona. Kuma ina tare da shi idan ya ambace ni». Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

Yaku musulmi! Ku sani cewa, Duk wani da ba ya aika aikin kwarai amma ya ce yana fatan samun rahamar Ubangijinsa to yana yaudarar kansa ne. Allah kuma ya hana hakan. Allah yana cewa:

(Ya ku mutane, lalle alkawarin Allah gaskiya ne. To don haka kada rayuwar duniya ta ruɗe ku, kuma ka da mai ruɗi ya ruɗe ku).

Bayin Allah! Wannan shi ne abin da ya sauwaƙa za ku ji shi daga gareni ina neman gafarar Allah gare ni da ku bakiɗaya. Ku nemi gafararsa, lalle shi mai yawan gafara ne mai karɓar tuba.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah bisa kyautayinsa, da gamon katar ɗinsa baiwarsa. Tsarki ya tabbata gare shi. Tsira da aminci su tabbata ga shugaban halitta Annabinmu Muhammad wanda yake kira zuwa ga yardar Allah. Tsira da aminci su tabbata gare shi shi da sahabbansa da alayensa da mu tare su har zuwa tashin ƙiyama. Bayan haka:

Yaku Musulmi! Ku sani cewa:

Babban abin da ake buƙata ga bawa shi ne ya haɗa tsoro da kwaɗayi. Wannan shi ne halin annabawa da dukkanin bayi salihai.

Allah yana cewa:

﴿ إِنَّهُمۡ كَانُواْ يُسَٰرِعُونَ فِي ٱلۡخَيۡرَٰتِ وَيَدۡعُونَنَا رَغَبٗا وَرَهَبٗاۖ وَكَانُواْ لَنَا خَٰشِعِينَ ٩٠ ﴾ [الأنبياء: ٩٠].

Ma’ana: (Lelle su sun kasance suna gaggawa wajen aikata alheri, kuma suna bauta mana tare da kwaɗayi da tsoro. Kuma sun kasance masu ƙasƙantar da kai ne gare mu).

Hakan Yana cewa:

﴿ تَتَجَافَىٰ جُنُوبُهُمۡ عَنِ ٱلۡمَضَاجِعِ يَدۡعُونَ رَبَّهُمۡ خَوۡفٗا وَطَمَعٗا وَمِمَّا رَزَقۡنَٰهُمۡ يُنفِقُونَ ١٦ ﴾ [السجدة: ١٦].

(Jikkunansu suna nesa daga shimfuɗunsu. Suna bauta Ubangijinsu, suna masu tsoro masu kwaɗayi. Kuma suna ciyarwa daga abin da muka azurta su).

Idan bawa ya san faɗin rahamar Allah da faɗin jinƙansa, da kuma yadda yake ya fe manya-manyan zunubai, to sai ya sa kwaɗayi a wajen neman rahamar Allah. Idan kuma ya san azabarsa da tsananin kamunsa, da hisabinsa, da abubuwan tsoro na ranar ƙiyama, da irin dangogin azaba na wutar jahannama, to sai ya firgita ya tsorata ya guji saɓa masa. Saboda haka ya zo cikin hadisin Abu Huraira, Manzon Allah ya ce: “Da bawa mumini ya san abin da ke wajen Allah na uƙuba, da ba wanda zai sa ran samun rahamarsa ba. Da a ce kafiri ya sa abin da ke wajen Allah na jinƙai, da babu mai ɗebe ƙauna daga aljannarsa. Muslim ne ya rawaito shi.

A ayoyi dadama Ubangiji ya haɗa maganar gafara da azaba a guri ɗaya. Kamar inda yake cewa:

﴿ وَإِنَّ رَبَّكَ لَذُو مَغۡفِرَةٖ لِّلنَّاسِ عَلَىٰ ظُلۡمِهِمۡۖ وَإِنَّ رَبَّكَ لَشَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ ٦ ﴾ [الرعد: ٦].

(Haƙiƙa Ubangijinka mai gafara ne ga mutane a bisa zalincinsu. Kuma mai matsanancin uƙuba ne).

Imamul Gazali ya hakaito daga Makahul al-Dimashƙi ya ce, «Duk wanda ya bautawa Allah da tsoro kaɗai ya zama kawariji. Wanda ya bauta masa da kwaɗayi shi kaɗai to ya zama Murji’i. Wanda kuwa ya bauta masa da soyayya kaɗai to ya zama zindiƙi. Wanda ya bauta masa da tsoro da kwaɗayi da soyayya, wannan shi

ne mai kaɗaita Allah kuma bin tafarkin sunna». [Ihya'u Ulumud-Din].

Ibnul Kayyim ya ce, zuciya kamar tsuntsu ce, soyayya shi ne kan. Tsoro da kwaɗayi su ne fukafukan, duk lokacin da kai da fukafukai suka yi lafiya, to sai tashin tsuntsun ya yi kyau. Idan aka yanke kan to tsuntsu ya tashi daga aiki. Idan kuma ya rasa fukafukansa biyu, to duk wani abin farauta za zo ya cimma masa. Sai dai magabata suna son ƙarfafa fiffiken tsoro sama da fiffiken kwaɗayi yayin da suke cikin ƙoshin lafiyarsu. Lokacin mutuwarsu kuma sai sukan ƙarfafi fiffiken fata sama da fiffiken tsoro. Soyayyar Allah ita ce abin hawan, shi kuma fata shi ne gaba yana kira, shi tsoro yana korawa, Allah kuma shi zai kai bawansa gida lafiya da baiwarsa da karamcinsa».

Ya ku musulmi! ku ji tsoron Allah, ku yi fatan samun rahamarsa da tsoron azabarsa. Ku saurari faɗin Allah da yake cewa:

﴿ ٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ وَأَنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٩٨ ﴾ [المائدة: ٩٨].

(Ku sani lalle Allah mai tsananin uƙuba ne. Kuma lalle Allah mai yawan gafara ne kuma mai jin ƙai).

Bukhari da Muslim sun ruwaito daga An-Nu'uman Ibn Bashir Allah ya yarda da su, ya ce, Na ji Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: "Wanda ya fi 'yan wuta samun sauƙin azaba, wani mutum ne da za a sa masa garwashin wuta a ƙarƙashin tafin ƙafarsa, ƙwaƙwalwarsa tana tafarfasa saboda su. Ba a ya zaton akwai wanda ya fi shi ɗandanar azaba, alhalin shi ne ya fi kowa samun sauƙin azaba".

Muslim ya ruwaito daga Mugirah bn Shu'ubah Allah ya yarda da shi, shi kuma daga Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Annabi Musa ya tambayi Ubangijinsa ya ce: "Ya Ubangiji wane ɗan aljanna ne ya fi ƙaƙantar matsayi? Sai ya ce, wani mutum ne da zai zo bayan 'yan aljanna sun shiga aljanna, sai a ce masa: Shiga aljanna. Sai ya ce, Ta yaya duk kowa ya shige gidansa. Kowa ya karɓi rabonsa. Sai a ce, "Ka gamsu a ba ka kwatankwacin mulkin wani sarki mai mulki na duniya?". Sai ya ce, "Allah na yarda a ba ni". Sai Allah ya ce, "An ba ka kamar wannan, da kwatankwacinsa, da kwatankwacinsa, da kwatankwacinsa, da kwatankwacinsa'. Sai a ta biyar ya ce, "Ya Ubangiji na fa gamsu". Sai Ubangiji ya ce, "Kana da kwatankwacin haka har sau goma. Kuma am ba ka duk abin da ranka ke sha'awa, idanka ke gani ya ji daɗi". Sai ya ce, "Ya Ubangiji na gamsu".

To a zamani irin wannan da zukata suka ƙeƙashe, san duniya ya cika su. Mutane suka daina jin tsoron saɓawa da aukawa zunubi, to ya kamata a rinjayar da fiffiken tsoro, domin zukata su daidaita. Idan kuma bawa ya zo mutuwa to sai ya rinjayar da janibin fata da kwaɗayin samun rahama, kamar yadda Manzon tsira yake cewa: "Kada ɗayanku ya mutu face yana kyautata zatonsa ga Ubangijinsa".

Don haka – Ya ku bayin Allah - tsoron Allah yana buƙatar tsayawa a zo da haƙƙin Allah ta'ala. Mutum ya guji sakaci akansu, kuma bawa ya nisanci zaluntar bayin Allah, ya ba su duk wani haƙƙi na su, kada ya yi musu wasa ko ya tozarta haƙƙin wani. Kuma tsoron Allah yana hana bawa sakin jiki wajen bin sha'awar ransa, ko aikata haramun. Kuma ya zama yana taka-tsantsan game da duniya da fitintinunta, kuma yana begen lahira da ni'imarta.

KARATUN ALKUR'ANI DA LADUBBANSA

Manufofin huɗubar

- Bayanin falalar koyon karatun Alƙur'ani
- Gargaɗin mutane daga shagalta ga barin Alƙur'ani
- Bayanin ladubban karanta Alƙur'ani

Huɗuba Ta Farko

Yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa dag sharrin kawukanmu da munanan ayyukanmu, wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda ya ɓatar babu mai shiryar da shi, kuma ina shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne bashi da abokin taraiya. Kum aina shaidawa cewa, Annabi Muhammadu bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda sukayi imani kuji tsoron Allah yadda ya cancani aji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane kuji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya halicci matarasa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga gare su (su biyu). Ku ji tsoron allah wanda kuke yi wa juna magiya da shi, (kuma ku kiyaye zumunci, lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku waɗanda suka yi imani kuji tsoron allah kuma ku faɗi magana ta daidai, sai allah ya gyara muk uaiyukanku, kum aya gafarta muku zunubanku, wanda yabi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lale mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawun shiriya shiriyar Annabi Muhammadu (ﷺ) kuma mafi sharrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (a addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duk wani ɓata kuma yana wuta.

Bayan haka;

Ya ku bayin Allah: Zancen mu game da littafin Allah, rabautarku na tare mafita daga fitinu. A cikinsa akwai labarin abin da ke gabanin ku, da ƙissar abin da ke bayanku, da hukuncin abin da ke tsakaninku. Shi ne tantancewa, ba wargi ba. Wanda ya bar shi don tsaurin kai sai Allah ya karya shi. Wanda ya nemi shiriya ba a cikin sa ba sai Allah ya ɓatar da shi. Shi ne igiyar Allah mai ƙwari. Ambato mai hikima. Tafarki madaidaici, shi ne wanda soye-soyen zukata ba sa karkacewa da shi, harasa ba su rikicewa da shi, malamai ba sa ƙoshi da shi. Ba ya tsufa saboda yawan karantawa, abubuwan mamakinsa basa ƙarewa. Wanda ya yi magana da shi ya yi gaskiya. Wanda ya yi aiki da shi zai sami lada, wanda ya yi hukunci da shi ya yi adalci, wanda ya yi kira zuwa gare shi ya yi kira zuwa tafarki madaidaici. Wannan shi ne littafin Allah; ku mai da hankali wajen koyansa da karanta shi da tunani a cikinsa, ku sanar da 'ya'yanku shi, ku raine su a kan karanta shi da sonsa, har su saba da shi, sai halayensu su tsarkaka, zukatansu su tsarkaka, su kasance

daga mahaddatansa, domin yaro idan ya koyi Alƙur’ani zai balaga yana mai sanin abin da yake karantawa a sallarsa, kuma haddace Alƙur’ani a yarinta ya fi haddace shi bayan an girma, kuma yafi zama a ƙwaƙwalwa, yafi kafuwa da tabbatuwa, domin koyo a yarinta kamar zane ne a kan dutse.

Ya ku bayin Allah, ku ji tsoron Allah, ku himmatu da wannan littafi Allah mai buwaya da ɗaukaka ya ce:

﴿ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَتۡلُونَ كِتَٰبَ ٱللَّهِ وَأَقَامُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَأَنفَقُواْ مِمَّا رَزَقۡنَٰهُمۡ سِرّٗا وَعَلَانِيَةٗ يَرۡجُونَ تِجَٰرَةٗ لَّن تَبُورَ ٢٩ لِيُوَفِّيَهُمۡ أُجُورَهُمۡ وَيَزِيدَهُم مِّن فَضۡلِهِۦٓۚ إِنَّهُۥ غَفُورٞ شَكُورٞ ٣٠ ﴾ [فاطر: ٢٩ - ٣٠].

(Haƙiƙa waɗanda suke karanta littafi kuma suka tsaida sallah, kuma suka ciyar daga abin da muka azurta su a ɓoye da sarari, suna fatan wani kasuwanci da ba zai taɓe ba. Domin ya cika musu ladansu kuma ya ƙara musu daga falalarsa, lalle shi mai yawan gafara ne mai yawan godiya).

Kuma Allah ta’ala ya ce:

﴿ وَرَتِّلِ ٱلۡقُرۡءَانَ تَرۡتِيلًا ٤ ﴾ [المزمل: ٤].

(Kuma ka kyautata karuntun alƙur’ni iya kyautatawa).

Bukhari ya ruwaito cikin sahihinsa daga Usman ɗan Affan ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Mafi alherinku shi ne wanda ya koyi Alƙur’ani kuma ya koyar da shi".

Kuma daga Aisha (R.A) ta ce: Manzon Allah ya ce, “Wanda yake karanta Alƙur’ani alhali yana ƙwararre a karatunsa yana tare da mala’iku jakadun Allah, masu girma, masu biyayiya. Wanda kuwa yake karanta shi yana in’ina cikinsa, yana masa wahala to yana da lada biyu). Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

Kuma Muslim ya rawaito daga Abu Umamata Al-Bahili ya ce, Na ji Manzon Allah (ﷺ) yana cewa, "Ku karanta Alƙur’ani, domin shi zai zo ranar Alƙiyama yana mai ceto ga ma’abotansa".

Kuma an karɓo daga Abu Hurairah, daga Annabi (ﷺ) ya ce, "Wasu mutane ba za su taru ba a wani ɗaki daga ɗakunan Allah ta’ala suna karanta littafin Allah, suna bitarsa a tsakaninsu, face nutsuwa ta sauko musu, rahama ta lulluɓesu, mala’iku sun kewayesu, Allah ya ambace su cikin waɗanda ke wajansa". Muslim ne ya rawaito shi. Kuma an karɓo daga Abu Hurairata, Annabi (ﷺ) ya ce, (Za a zo da mahaddacin Alƙur’ani ranar Alƙkiyama sai Alƙur'anin ya ce, "Ya Ubangiji ka yi masa ado". Sai a sanya masa kambin girma. sannan ya sake cewa, "Ya Ubangiji ka ƙara masa". Sai a sanya masa rigar girma. Sannan ya sake cewa: "Ya Ubangiji ka yarda da shi". Sai ya yarda da shi. sai a ce masa: Yi karatu ka ƙara ɗaukaka, sai ya ƙara samun kyakkyawan aiki da kowace aya da ya karanta". Tirmizi ne ya rawaito. Kuma hadisi ne kyakkyawa.

Wannan wani abu ke nan daga falalar karanta Alƙur’ani da abin da mai karatun Alƙur’ani yake da shi na lada. Kuma shi ne wasiyyar Annabi (ﷺ) wadda ya yi mana wasiyya da ita, kamar yadda Imamu Ahmad ya rawaito daga Abu Sa’id cewa, Annabi (ﷺ) ya ce, (Ina maka wasiyya da tsoron,Allah, domin shi ne kan kowane abu, kuma na hore ka da jihadi domin shi ne rahbaniyancin Musulunci.

Kuma ka lazimci ambaton Allah da karanta Alƙur'ani, domin shi ne ruhinka a sama da matsayinka a ƙasa). Albani ya inganta shi.

Ya ku bayin Allah, haƙiƙa karatun Alƙur'ani yana da ladubba daga cikinsu akwai:

1. Ikhlasi ga Allah (S.W.T) domin Annabi (ﷺ) ya bamu labari game da waɗanda za a rura wuta da su ranar Alƙiyama su mutum uku ne: a cikinsu akwai mai karanta Alƙur'ani, Annabi (ﷺ) ya ce game da da su, "Lallai Allah idan ranar Alƙiyama ta yi zai sauko zuwa bayi, domin yin hukunci tsakanin su, kowace al'umma tana durƙushe, farkon wanda za a kira shi ne mutumin da ya haddace Alƙur'ani, da mutumin da aka kashe a tafarkin Allah, da mutum mai yawan dukiya. Sai Allah ya ce da makaranci, Shin ban sanar da kai abin da na saukarwa Manzona ba? Sai ya ce, haka ne ya Ubangiji ka sanar dai. Sai ya ce, to me ka aikata? Sai ya ce, na kasance ina tsayuwa da karatunsa lokutan dare da rana. Sai Allah ya ce masa, ka yi ƙarya, Mala'iku ma su ce masa, ƙarya kake. Allah ya ce da shi, kawai ka yi nufin a ce, ai wane makaranci ne, kuma an faɗi haka. Sannan sai a ja shi zuwa wuta wa'iyazu billahi.
2. Ya karanta shi bisa tsarki. babu shakka kuwa karatunsa bisa tsarki shi ya fi daga karanta shi ba tsarki.
3. Daga ciki akwai: Yin asuwaki; domin Sayyidina Ali yana cewa, "Haƙiƙa bakunan ku hanyoyi ne na Alƙur'ani, don haka ku daɗaɗa su da yin aswaki" Ibn Majah ne ya ruwaito. Kuma annabi (ﷺ) ya ce, (Haƙiƙa bawa idan ya tashi yana sallah sai Mala'ika ya zo masa ya tsaya bayansa, don ya ji Alƙur'ani, ya kusanto, ba zai gushe ba yana saurare har ya sanya bakinsa a kan bakinsa, don haka ba zai karanta Alƙur'anin ba sai ayar ta shige cikin Mala'ikan). Baihaƙi ne ya rawaito shi daga Aliyu (R.A). kuma Albani ya inganta shi.

Yana daga fa'idojin aswaki ga mai karatun Alƙur'ani cewa ba zai fitar da wata ƙazanta daga bakinsa ba da zata cuci Mala'ika da ya zo sauraronsa.

4. Daga ciki akwai, neman tsarin Allah daga shaiɗan la'ananne, domin Allah ta'ala ya ce:

﴿ فَإِذَا قَرَأْتَ ٱلْقُرْءَانَ فَٱسْتَعِذْ بِٱللَّهِ مِنَ ٱلشَّيْطَٰنِ ٱلرَّجِيمِ ﴿٩٨﴾ ﴾ [النحل: ٩٨].

(Kuma idan za ka karanta Alƙur'ani to ka nemi tsari da Allah daga shaiɗani tsinanne).

Wasu malamai suka ce: wajibi ne karanta isiti'aza yayin karatun Alƙur'ani, saboda zahirin umarni. Sauran malamai kuwa suka ce, Mustahabi ne.

Sigar da aka fi so ita ce:

(أعوذ بالله السميع العليم من الشيطان الرجيم من همزه ونفخه ونفثه).

Ma'ana: (Ina neman tsari da Allah mai ji masani, daga shaiɗan la'ananne, daga zungurinsa da busarsa da tofinsa).

Kamar yadda hakan ya tabbata daga Annabi (ﷺ).

5. Daga ciki: akwai yin bisimillah. Ya wajaba mai karatu ya kiyaye karanta bisimillah a farkonkon kowace sura ban da (Bara'a). Domin ya tabbata cewa

Annabi (ﷺ) ana sanin ƙarwewar sura (a karatunsa) da fara sura ta gaba da bisimillah, sai a guri ɗaya shi ne tsakanin Anfal da Bara'a.

6. Daga ciki akwai karanta Alƙur'ani dalla-dalla. Domin Allah ta'ala ya ce:

﴿ وَرَتِّلِ ٱلْقُرْءَانَ تَرْتِيلًا ﴿٤﴾ ﴾ [المزمل: ٤].

(kuma ka kyautata karatun Alƙur'ani iyakar kyautatawa).

Ummu salama ta siffanta karatun Manzon Allah (ﷺ) da cewa, karatu ne da ake rarrabe shi harafi bayan harafi.

Bukhari ya ruwaito daga Anas cewa, an tambaye shi game da karatun Annabi (ﷺ)? Sai ya ce, "Ya kasance yana jan karatunsa". Sannan ya karanta "Bismillahir Rahmanir Rahim), yana mai jan "Allaah" - Ma'ana ja na ɗabi'a wato harka biyu - yana jan "Arrahman", yana jan (Arrahim). Bukhari da Muslim sun ruwaito daga Ibn Mas'ud cewa, wani mutum ya ce masa, Ni nakan karanta Almufassal (wato daga Hujurat zuwa Nass) cikin raka'a ɗaya. Sai Abdullahi ya ce, "Gaggatsa karatu kamar kana gaggatsa waƙa"? Yana masa inkarin saurin karatun. Haƙiƙa wasu mutane suna karanta Alƙur'ani amma ba ya wuce ƙashin haƙarƙarinsu. Idan Alƙur'ani ya shiga zuciya ya kafu a cikinta sai to zai yi amfani.

7. Daga cikin akwai kyautata murya da Alƙur'ani; An karɓo daga Barra'u (R.A) ya ce, "Na ji Annabi (ﷺ) yana karanta wattini wazzzaitun a cikin sallar isha'i, ban taɓa jin wanda ya fishi kyan sauti ko ƙira'a ba". Bukhari ne ya ruwaito.

Domin fadinsa (ﷺ) "Ku kyautata Alƙur'ani da sautukanku, domin kyakkyawan sauti yana ƙarawa Alƙur'ani kyawu". Hakim ne ya ruwaito shi daga Bara'u bn Azib. A wata ruwayar, (Kyan murya ado ne ga Alƙur'ani) Albani ya inganta shi daga hadisin Ibn Mas'ud.

8. Yana daga cikin ladubban karatun Alƙur'ani rera shi: Wannan yana bin abin da aka ambata na kyautata sauti. Domin Annabi (ﷺ) ya ce, "Ba ya daga cikinmu wanda ba ya rera karatun Alƙura'ni ba". Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi daga Sa'ad bn Abi waƙƙas. Hakanan hadisin da Annabi yake cewa, "Allah bai yi sauraro ga wani abubu ba kamar yadda yake sauraro ga wani Annabi mai kyan sauti da ya ke rera karatun Alƙur'ani). Bukhari ne ya ruwaito shi daga Abu Hurairata.

Ya ku bayin Allah,

9. Yana daga ladubban tilawa tsayawa a kan ayoyi. Koda tana da alaƙa da ta gabonta wajan ma'ana. Domin ya zo a hadisi sahih daga Annabi (ﷺ) cewa ya kasance yana yayyanka karatunsa aya aya. Alhamdulillahi Rabbil Alamin, sai ya tsaya. Arrahmain rahim, sai ya tsaya. Imam Ahmad ya ruwaito shi daga Ummu Salamah.
10. Yana daga cikin su, kada wani mutum ya ɗaga muryarsa da karatunsa a kan na ɗan'uwansa, domin ɗaga murya a cikin wannan hali cutarwa ne ga maƙocinsa. Ya zo a cikin hadisin Annabi (ﷺ) ya ce, (Kowane daga cikinku mai ganawa ne da Ubangijinsa, don haka kada sashinku ya cuci shashi. Kada sashinku ya ɗaga (murya) bisa sashi wajen karatu).

11. Sannan idan ya ji gyangyaɗi to sai dakata da karatun. Domin Ahmad da Muslim sun rawaito, daga Abu Hurairah daga Annabi (ﷺ) ya ce: (Idan ɗayanku ya tashi da dare, sai karatun Alƙur'ani ya rikice masa a harshansa, bai san mai yake cewa ba, to ya kwanta). yana nufin: Ya je ya yi barci, don kada ya cakuɗa Alƙur'ani da wani abu, ko ayoyi su cakuɗe masa, ya gabatar da wasu ya jinkintar da wasu, ko ya yi shirme ya faɗi wasu haruffan da ba su ciki, da makamancin wannan. To zararar ya ji barci zai kama shi, to ya wajaba ya je ya kwanta.
12. Sannan kada ya karanta Alƙur'ani a ruku'i ko sujjada. Saboda faɗinsa (ﷺ): (Haƙiƙa ni an hana ni karanta alƙur'ani a ruku'i, ko sujjada. Shi ruku'i ku girmama Ubangiji a cikinsa. Ita kuwa sujjada ku yi ƙoƙarin yin addu'a (a cikin ta), tabbas a amsa muku). Dalilin wannan, shi ne abin da Shaihul Islam-Allah ya ji ƙansa- yake cew, "Shi ruku'i da sujjada suna daga guraren ƙasƙan da kai, don haka bai kamata a karanta Alƙur'ani a wajan ƙasƙantar da kai ba, tasbihi ne kawai, da tsarkake Allah (S.W.T) a cikinsu".

In afaɗar abin da kuke ji, ina neman gafarar Allah gare ni da ku da sauran Musulmi daga dukkan zunubi, lallai shi mai gafara ne mai jin ƙai.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah, tsira da aminci su tabbata ga mafi ɗayantakar manzanni Annabinmu Muhammadu da alayensa, da sahabbansa gaba ɗaya.

Yaku bayin Allah, haƙiƙa yana daga abin da ya kamata ga mai karatun Alƙur'ani yayi kuka yayin karatu domin Allah ta'ala ya ce yana yaban muminai da haka: (kuma suna kifuwa bisa haɓoɓinsu suna kuka, kuma yana ƙara musu tsoron Allah).

Kuma an karɓo daga Ibn Mas'ud ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce min: "Ka karanta min Alƙur'ani". Na ce, Yanzu na karanta maka bayan kai aka saukarwa? Ya ce: "Ni ina son na ji shi daga wani na". Sai na karantam masa suratun Nisa'i har na zo in da Allah ya ke cewa,

﴿ فَكَيۡفَ إِذَا جِئۡنَا مِن كُلِّ أُمَّةِۭ بِشَهِيدٖ وَجِئۡنَا بِكَ عَلَىٰ هَٰٓؤُلَآءِ شَهِيدٗا ٤١ ﴾ [النساء: ٤١].

Ma'ana: (To yaya lamarinsu zai kasance yayin da muka zo da mai shaida daga kowa ce al'umam kuma muka zo da kai mai shaida a kansu) Sai ya ce: «Ya ishe ka hakanan). Sai ga idanunsa suna zubar da hawaye. Bukhari ya rawaito.

Wani sahabi ya ce, (Na zo wa Annabi (ﷺ) ya na sallah, cikinsa na da ƙugi kamar ƙugin tukunyar tasa a kan wuta). Yana nufin saboda kuka. Nasa'i ne ya rawaito.

Daga cikin ladubban karatun Alƙur'ani akwai buƙatar tuttuntuni a kan ma'anoninsa yayin karatunsa. Wannan kusan shi ne mafi muhimmancin ladaban karatun Alƙur'ani gaba ɗaya, kuma shi ne amfanin karatun na haƙiƙa. Ga shi Allah ta'ala ya ce:

﴿ كِتَٰبٌ أَنزَلۡنَٰهُ إِلَيۡكَ مُبَٰرَكٞ لِّيَدَّبَّرُوٓاْ ءَايَٰتِهِۦ وَلِيَتَذَكَّرَ أُوْلُواْ ٱلۡأَلۡبَٰبِ ٢٩ ﴾ [ص: ٢٩].

(Litatafi ne da muka saukar da shi mai albarka domin su yi tuntuntuni game da ayoyinsa, kuma domin ma'abota hankali su wa'azantu).

Shi kuwa ba ya samuwa sai ga wanda ya yi tunani cikin zancen Allah mai girma da ɗaukaka, ya halarto da girmansa (S.W.T) ya yi la'akari cikin zantuttukan Alƙur'ani, ya halarto cewa, yana karatu ne da niyyar fhaimta da aiki da abin da yake karantawa. Amma mai karanta Alƙur'ani da harshe, yayin da zuciyarsa ta ke wani gurin ba zai sami amfanin da ake samu daga karatun Alƙur'anin ba. Allah ya ce,

﴿ أَفَلَا يَتَدَبَّرُونَ ٱلْقُرْءَانَ أَمْ عَلَىٰ قُلُوبٍ أَقْفَالُهَآ ﴿٢٤﴾ ﴾ [محمد: ٢٤].

(Yanzu ba za su yi tuntuntuni cikin Alƙur'ani ba, koko a kan zukatan su akwai kwaɗuna ne).

An karɓo daga Huzaifah, ya ce, Na yi sallah tare da Annabi (ﷺ) wani dare sai ya fara karatun Baƙara, sai na ce, Zai yi ruku'u wajan aya ta ɗari, sai ya zarce; na ce zai yi ruku'u wajan aya ta ɗari biyu, sai ya zarce, na ce, zai yi raka'a guda ne da ita, sai ya wuce ya fara Nisa'i ya karance ta, ya fara Ali Imrana ya karantata, yana karatu a hankali, idan ya zo ayar tasbihi, sai yayi tasbihi, idan ya zo ayar roƙo sai ya roƙa, idan ya zo ayar neman tsari, sai ya nemi tsari, sannan ya yi ruku'u...). Nasa'i ne ya rawaito shi.

Haƙiƙa Annabi (ﷺ) ya ba mu labarin Khawarijawa, da cewa su mutane ne da suke karanta Alƙur'ani, amma ba ya wuce maƙogwaransu. Hakanan Manzon Allah (ﷺ) ya ce, (Wanda ya karanta Alƙur'ani a ƙasa da kwana uku ba zai fahimce shi ba).

Ana tuntuntuni ne don aiki: An karɓo daga Abu Abdurrahman as-Sulami ya ce: wanda yake karanta mana Alƙur'ani daga sahabban Annabi (ﷺ) ya ba mu labari cewa su sun kasance suna karantar ayoyi goma daga Manzon Allah (ﷺ), ba sa ci gaba da wasu goman har sai sun ko yi abin da ke cikin waɗannan na ilimi da aiki, suka ce, Sai mu ka koyi Ilimi da aiki tare.

Ya ku bayin Allah; Idan mai karatun Alƙur'ani ya zo wajan sujjadar tilawa zai yi sujjada. Abu Hanifa ya ce, wajibi ce. Amma magana mafi rinjaye maganar Umar (R.A) cewa sujjadar tilawa mustahabbi ce ba wajibi ba. Kuma wannan ita ce maganar jamhurun malamai, siffar sujjadar shi ne ya yi kabbara ya yi sujjada.

Ya halatta mai karatu ya karanta Alƙur'ani a zaune, ko a tsaye, ko a tafe, ko kwance, duk wannan ya halatta, domin Allah ta'ala ya ce,

﴿ ٱلَّذِينَ يَذْكُرُونَ ٱللَّهَ قِيَـٰمًا وَقُعُودًا وَعَلَىٰ جُنُوبِهِمْ وَيَتَفَكَّرُونَ فِى خَلْقِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ﴾

[آل عمران: ١٩١].

(Waɗannan da suke ambaton Allah a tsaye, da zaune, da kuma kishingɗe, suke tunani cikin halittar sammai da ƙasa).

Sai dai da zai zauna yana mai ƙasƙantar da kai, da ya,fi da ya zauna yana mai kishingiɗa kan gefensa. Annabi (ﷺ) ya kasance yana zaman harɗe bayan sallar Alfijir ya fuskanci alƙibla yana ambaton Allah har rana ta fito.

Kuma yana daga ladaban karanta Alƙur'ani, kada ya saukw Alƙur'ani a ƙasa da kwana uku; saboda faɗinsa (ﷺ) "Wanda ya karanta Alƙur'ani cikin ƙasa da kwana uku ba zai fahimce shi ba". Abu Dawud da Tirmizi da Ibn Majah suka rawaito shi daga Ibn Umar (R.A).

Ya ku bayin Allah! A yau Haƙiƙa mafiya yawan mutane a yau sun shagala daga koyon Alƙur'ani. Manya sun shagala da duniya, yara sun shagala da karatun boko a makarantun da ba sa bawa koyar da Alƙur'ani isasshan lokaci, ko kulawa da ta kamata, kuma babu malamai da za su ɗauki alhakin kula da karatunsa. Ragowar lokutan yaran kuwa ana asarar sa ne a wasa, abin da ya haifar da jahiltarsu ga Alƙur'ani, da nesantar su daga gare shi. Har ka ga mutum yana ɗauke da wata babbar shaidar karatu, amma ba zai iya karanta aya ɗaya ta littafin Allah daidai ba. Har lamarin ya kai ga masallatar dadama sun rasa limamai saboda ƙarancin makaranta alƙur'ani. Dalilin haka, na farko watsi da iyaye suka yi da 'ya'yansu, da rashin damuwarsu da wannan ɓangare. Ɗayansu bai san menene halin ɗansa yake ciki ba dangane da Alƙur'ani ba. Har musulmi dadama suka ƙauracewa Alƙur'ani. Wannan shi ne abin da Manzo (ﷺ) ya kai kokensa, da faɗinsa:

﴿ وَقَالَ ٱلرَّسُولُ يَٰرَبِّ إِنَّ قَوۡمِي ٱتَّخَذُواْ هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانَ مَهۡجُورٗا ٣٠ ﴾ [الفرقان: ٣٠].

(Ya Ubangiji haƙiƙa mutane na sun riƙi wannan Alƙur'ani a matsayin abin ƙauracewa).

Ibn Kasir – Allah ya jiƙansa – ya ce, barin bibiyar ma'anarsa da fahimtarsa yana daga ƙaurace masa. Barin aiki da shi, da kamanta umarce-umarcensa, da nisantar hane-hanensa yana daga nisantar sa, karkata daga gare shi zuwa waninsa na daga waƙa ko magana ko wasa ko wani zance ko wata ɗariƙa wacce ba ta Alƙur'ani ba, yana daga cikin ƙaurace masa.

Ya ku bayin Allah! Haƙiƙa dole ne a koyi Alƙur'ani daga Malamai da suka iya karanta shi. Mutum ba zai wadatu da tashin baƙinsa daga cikin Mushafi ba, domin koyar Alƙur'ani daga bakin mai koyarwa ƙwararre shi ya fi kyau, ya fi tabbatar da kiyayewa; domin ba za a iya koyansa ta hanyar karatun rubutunsa ba, sabonda kamar yadda kowa kan iya gani, mutane dadama daga waɗanda suka koyi alƙur'ani ta hanyar karanta shi ba tare da malami ba, sukan yi ta tabka kurakurai wajen karanta shi. Saboda haka dole ne ya sami malami da ya ƙware da zai nuna masa lafazan Alƙur'ani. Haƙiƙa tsangayoyi da makarnatun allo sun yi yawa na koyar da Alƙur'ani. Sai dai abin takaici babu mai gudanar da su, face mutanen da suka haddace Alƙur'ani babu tantancewa ko tajwidi, ba sa kyautata karatun koda aya ɗaya karatu ingantacce abin kyautatawa, tare da rashin kulawarsu da tarbiyyar Almajirai da ke hannunsu, da barinsu sasakai kamar tumaki suna yawo a titina, da gidajen mutane, babu isasshan abinci, ba kiwon lafiya, ba makwanci mai kyau, duk wannan da sunan Alƙur'ani. Wannan wallahi aiki ne da yake munanawa Alƙur'ani, yake munanawa musulunci, ya sanya maƙiya Musulunci suna kallan wannan mummunan aiki da ake aikatawa waɗannan ƙananan yara a matsayin ɓangare na wajban Musulunci, kuma ɗaya daga abubuwan da ake buƙata domin haddace Alƙur'ani, alhali musulunci ba ruwansa da duk wannan. Ya wajaba ga

Gwamnonin jihohin musulmi su kula da nauyin da ya rataya a wuyansu game da wannan lamari, su kawo mafita ta karshe, su tserar da musulunci da Alƙur'ani daga laifin mutane jahilai. Koƙarin da ake yi game da wannan kaɗanne idan anyi la'akari da girman matsalar da haɓakarta. Mafificiyar hanya ita ce wayar da kan Musulmi da iyayan yara, musamman a karkara da ƙauyuka, da samar da makarantun haddace Alƙur'ani isassu waɗanda za su ginu a kan tushen shari'ah nagarta.

Ya ku bayin Allah; Wanda ya koyi littafin Allah to ya kiyaye shi, ya yawaita karanta shi da tuntuni a cikins, da fhaimtarsa cikin ƙasƙantar da kai da halarto da zuciya. Manzon Allah (ﷺ) ya ce: (Wanda ya karanta harafi daga littafin Allah yana da ladan kyakkyawan aiki ɗaya, shi kuwa kyakkywan aiki yana da ladan goma kwatankwacinsa, ba zance Alif-Lam-Mim, harafi ɗaya ne. Sai dai Alif harafi ne – Lam harafi ne, Mim harafi ne). Tirmizi ne yarawaito kuma ya ce hadisi ne ingantacce.

Ibnul Kaiyim – Allah ya ji ƙansa – ya ce, "Ka lura da zancan Alƙur'ani kaga wani sarki wanda mulki duk nasa ne, ya bo duka nasa ne, ragamomin lamurra a hannunsa suke duka, yana yiwa bayinsa nasiha, ya shiryar da su a bisa abin da farin cikinsu da rabautar su ke ciki, yake ƙwaɗaitar da su cikinsa, yana gargaɗinsu daga abin da hallakarsu ke ciki. Yana sanar musu da kansa da sunayansa da siffofinsa. Ya soyu zuwa gare su da ni'imominsa da falalolinsu. Ya tuna musu da ni'imominsa akansu, ya umarce su da yin abin da za su cancanci cikamakinta da su. Ya tuna musu da abin da ya tanadar musu na karama in sun bi shi, da abin da ya tanadar musu na uƙuba in sun saɓe shi. Ya ba su labarin yadda yake yi da masoyansa da maƙiyansa, da ya ya ƙarshan waɗannan da waɗancan. Ya buga misalai, ya nau'anta dalilai da hujjoji. Yana kira zuwa gidan aminci. Ya ambaci siffofinsa da kyawunsa. Yana gargaɗi game da gidan hallaka, yana tunatarwa da azabarsa da muninta. Ya tunatar da bayinsa buƙatuwarsu zuwa gare shi, kuma cewa su ba za su iya wadatuwa daga barinsa dai dai da ƙiftawar ido. To idan zukata suka ga sarki mai girma, mai rahama, mai kyauta, mai kyawu, a cikin Alƙur'ani don me ba za su so shi ba?

Shi Alƙur'ani mai tunatawa mutane Allah ne, mai kusantarwa zuwa gare shi ne, don haka ya wajaba musulmi ya kula da koyansa da yawaita karanta shi, domin shi haske ne da waraka da rahama, da ni'ima, da shiriya, da banbancewa tsakanin gaskiya da ƙarya, da ambato mai hikima da dalili.

IMANI DA KADDARA

Manufofin huɗubar

- Bayani a kan ma’anar imani da ƙaddara. Da kasancewarsa rukuni ne na imani.
- Bayani a kan cewa, ƙaddara ba hujja ba ce wajen saɓon Allah.
- Bayani abin da ya wajaba a kan bawa idan ƙaddara ta same shi.
- Gargaɗi a kan waɗɗanda suka ɓace game da sha’anin ƙaddara.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga shirrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammad bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammad (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Bayan haka, ya ‘yan uwa! Maganarmu a yau ta shafi ɗaya daga cikin rukunan imani guda shida, wanda duk wanda bai yi imani da shi ba, ko kuma ya yi musu a kansa, to Allah ba zai karɓi ayyukansa ko ƙanana, ko manya ba. Shi ne bayar da gaskiya da ƙaddara. Rukuni ne mai girma, wanda ta hanyarsa mutum yake samun nutsuwa a rayuwarsa, ya kuma sami amsoshi game da abubuwa da yawa, da suka shige masa duhu. Allah yana cewa,

﴿ إِنَّا كُلَّ شَيۡءٍ خَلَقۡنَٰهُ بِقَدَرٖ ﴿٤٩﴾ ﴾ [القمر: ٤٩].

(Mun halicci komai da ƙaddara). Kuma Allah yana cewa,

﴿ ٱلَّذِي خَلَقَ فَسَوَّىٰ ﴿٢﴾ وَٱلَّذِي قَدَّرَ فَهَدَىٰ ﴿٣﴾ ﴾ [الأعلى: ٢ – ٣].

(Shi ne wanda ya yi halitta, kuma ya daidaita ta, kuma shi ne wanda ya ƙaddara abubuwa, kuma ya shiryar da su).

Kuma Allah yana cewa,

﴿ وَخَلَقَ كُلَّ شَيۡءٖ فَقَدَّرَهُۥ تَقۡدِيرٗا ﴿٢﴾ ﴾ [الفرقان: ٢].

“Kuma ya halicci kowane abu, kuma ya ƙaddara shi, ƙaddarawa.”

Ayoyi da suke tabbatar da wannan rukuni, sun fi a ƙirga, kuma a cikin sunnar Manzon Allah (ﷺ) ma wuri daban-daban, ya tabbatar da wannan rukuni mai girma. Misali, a cikin hadisin da mala’ika Jibrilu ya zo wajen Annabi (ﷺ), yana tambayar sa, da ya tambaye shi kan imani, sai ya ce, “Imani shi ne, ka bayar da gaskiya da Allah, da mala’ikunsa, da littattafansa, da Manzanninsa, da ranar ƙarshe, da yarda da ƙaddara, mai daɗi da mara daɗi.” Sai Jibrilu ya ce, “Ka yi gaskiya!” Muslim ne ya ruwaito.

Ya ku ‘yan uwa! Abin da ake nufi da ƙaddara, shi ne ilimin Allah Ta’ala, wanda ya rigaya tun fil-azal, da abubuwa kafin su auku, kuma Allah ya rubuta su daki-daki, kafin ya halicci sama da ƙasa, da shekara dubu hamsin, kuma babu abin da zai auku, face da ganin damarsa, kuma shi ya halicce shi. Wannan shi ne bayar da gaskiya da ƙaddara wajen sahabbai, kuma shi ne bayar da gaskiya a wajen ahlussunnah. Don haka, tilas ne ga duk wani musulmi, ya yarda cewa babu wani abu da zai faru cikin mulkin Allah, wanda sai daga baya Allah zai san shi. A’a, Allah ya rigaya, ya san komai, tun fil-azal, kuma ya rubuta shi a allon ƙaddara (lauhil mahfuuz), kamar yadda ya zo a hadisin, kuma kamar yadda Allah yake cewa,

﴿ إِنَّ ذَٰلِكَ فِي كِتَٰبٍ ۚ إِنَّ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٌ ٧٠ ﴾ [الحج: ٧٠].

“Lallai hakan, yana cikin littafi, lallai hakan mai sauƙi ne wurin Allah.”

Don haka, babu wani abu da zai auku, face sai Allah ya ga dama, kuma idan zai auku, zai auku ne, kamar yadda Allah ya zartar. Allah yana cewa,

﴿ وَمَا تَشَآءُونَ إِلَّآ أَن يَشَآءَ ٱللَّهُ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلِيمًا حَكِيمًا ٣٠ يُدۡخِلُ مَن يَشَآءُ فِي رَحۡمَتِهِۦ ۚ وَٱلظَّٰلِمِينَ أَعَدَّ لَهُمۡ عَذَابًا أَلِيمَۢا ٣١ ﴾ [الإنسان: ٣٠ - ٣١].

(Ba kwa nufin aikata wani abu, sai Allah ya yi nufi. Lallai Allah masani ne, mai azanci, yana shigar da wanda ya yi nufi cikin rahamarsa).

Ya ɗan uwa! Ka sani, babu tilas ga ɗan Adam kan ayyukansa, a aƙida ta musulunci. Mutum yana da dama, da kuma zaɓi, na ya aikata abin da ya ga dama, kamar yadda yake cewa,

﴿ وَهَدَيۡنَٰهُ ٱلنَّجۡدَيۡنِ ١٠ ﴾ [البلد: ١٠].

(Kuma mun shiryar da shi hanyoyi biyu).

Wato na alheri, da na sharri. Don haka, shi ɗan Adam, shi ne yake zaɓar abin da ya ga dama, kuma sanin Allah, ba ya nufin Allah ya yi masa tilas ba ne. Don ba daidai ba ne, mutum ya kafa hujja da ƙaddara wajen saɓon Allah, kamar yadda wasu mutane suke yi.

Ibni Taimiyya ya ce, «Wannan maganar banza ce. Wato mutum ya kafa hujja da ƙaddara a kan saɓa wa Allah, saboda imma dai ƙaddara ta zama hujja ga kowa da kowa, ko kuma ba hujja ba ce ga kowa da kowa. To idan ƙaddara hujja ce ga kowa da kowa, to babu wanda yake da dama ya yi musu ko inkari ga wanda ya cuce shi, ya zage shi, kuma ya ƙwace masa dukiyarsa, ya ɓata masa matansa, ya sare da takobi a wuya, kuma ya lalata masa gonarsa da ‘ya’yansa. domin ba zai

cuce shi ba, sai da ƙaddara. Babu wanda zai yarda a cuce shi, a kafa masa hujja da ƙaddara. Abu na biyu, idan ƙaddara hujja ce, to da Iblis, da Fir'auna da mutane Annabi Nuhu da Adawa da sauran masu saɓon Allah, waɗanda Allah ya halakar da su, da sun sami hujja. Haka kuwa abu ne da babu wani mai bin wani addini da zai yarda da shi. Abu na uku, da ƙaddara hujja ce, to da babu bambanci tsakanin bayin Allah na ƙwarai da fajirai. Wanda ya saɓa ga tunani na ƙwarai, ya kuma saɓa da fadin Allah cewa,

﴿وَمَا يَسۡتَوِي ٱلۡأَعۡمَىٰ وَٱلۡبَصِيرُ ١٩ وَلَا ٱلظُّلُمَٰتُ وَلَا ٱلنُّورُ ٢٠ وَلَا ٱلظِّلُّ وَلَا ٱلۡحَرُورُ ٢١ وَمَا يَسۡتَوِي ٱلۡأَحۡيَآءُ وَلَا ٱلۡأَمۡوَٰتُۚ﴾ [فاطر: ١٩ – ٢٢].

"Makaho ba zai daidaitu da mai gani ba, haka duhu ba zai yi daidai da haske ba, haka inuwa ba za ta yi daidai da zafi ba, haka matattu ba za su yi daidai da masu rai ba."

Kuma yana cewa,

﴿أَمۡ نَجۡعَلُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ كَٱلۡمُفۡسِدِينَ فِي ٱلۡأَرۡضِ أَمۡ نَجۡعَلُ ٱلۡمُتَّقِينَ كَٱلۡفُجَّارِ ٢٨﴾ [ص: ٢٨].

(Ko za mu sanya waɗanda suka yi imani kuma suka yi ayyuka na ƙwarai kamar masu ɓarna a doron ƙasa, ko kuma za mu sanya masu taƙawa su zama daidai da fajirai).

Abu na huɗu: Ita ƙaddar imani aka ce mu yi da ita, ba kafa hujja ba. Duk wanda ya kafa hujja da ƙaddara to hujjarsa ta banza ce. Duk kuma wanda ya ba da hanzari da ƙaddara to hanzarinsa ba abin karɓa ba ne. Da ana karɓar hujja da ƙaddara to da an karɓi ta Iblis da sauran masu saɓo. Da ƙaddara hujja ce ga bayi da babu wani da za a yi masa azaba a nan duniya ko a lahira. Da ana hujja da ƙaddara da ba yanke hannun ɓarawo ba, ba a kashe wanda ya yi kisan kai ba, da ba wanda za a yi wa haddi don ya yi wani laifi. Kai da ma ba wanda za a yaƙa, ko a yi umarni da wani abu na shari'a ko hana wani mummunan abu.

Abu na biyar, an tambayi Manzon Allah (ﷺ), "Idan dai Allah ya rubuta komai, to meye amfanin aikin da bayi za su yi?" Sai ya ce, "A'a! Ku yi aiki. Kowa abin horewa ne ga abin da aka halicce shi don shi." Abu na shida, idan dai rubutu da Allah ya yi, zai zamo hujja ga masu saɓo, to me ya sa ba zai zama hujja ba wajen ci da sha, da makamantan haka? Ai Allah ya ƙaddara masa ci da sha, da sauransu, amma ba zai ƙoshi ba, ko ya daina ci, sai ya ci, ya sha. Me ya sa ba zai ce, tunda Allah ya rubuta, ba sai na ci, ko na sha ba, idan na zauna haka ma, ƙaddara za ta biyamin buƙatata? Ko kuwa haihuwa: Ai ita ma ƙaddara ce, me ya sa mutum ba ya zama, ya ƙi yin aure, ya ce, idan dai Allah ya rubuta mini ɗa, zan same shi, ko ban kusanci mace ba. Babu mai fadin haka, sai wawa. To haka ma abin da yake wajen bin Allah, ko saɓa masa.

Godiya ta tabbata ga Allah, Ubangijin talikai, kuma tsira da aminci su tabbata ga mafi ɗaukakar Annabawa da Manzanni, Annabinmu, Muhammad, da iyalensa da sahabbansa gabaɗaya. Bayan haka:

Akwai matakan ƙaddara guda huɗu:

Mataki na farko: Allah ya san komai, samamme da ma wanda ba samamme ba. Ya san abin a faru da abin yake faruwa, da wanda zai faru nan gaba idan zai faru ya ya zai faru. Hujja a kan wannan shi ne faɗin Allah:

﴿ لِتَعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ وَأَنَّ ٱللَّهَ قَدۡ أَحَاطَ بِكُلِّ شَيۡءٍ عِلۡمَۢا ١٢ ﴾ [الطلاق: ١٢].

(Don ku san cewa, lalle Allah mai iko ne a kan dukkan komai, kuma iliminsa ya kewaye komai).

Mataki na biyu: Allah ya rubuta komai da zai faru har zuwa tashin ƙiyama. Allah yana cewa:

﴿ أَلَمۡ تَعۡلَمۡ أَنَّ ٱللَّهَ يَعۡلَمُ مَا فِي ٱلسَّمَآءِ وَٱلۡأَرۡضِۗ إِنَّ ذَٰلِكَ فِي كِتَٰبٍۚ إِنَّ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٞ ٧٠ ﴾ [الحج: ٧٠].

(Shin ba ka sani ba ne, cewa Allah yana sane da abin da yake cikin sama da ƙasa. Lalle wannan yana cikin littafi. Lalle wannan wani abu ne mai sauki a gurin Allah).

Yana cewa,

﴿ وَكُلَّ شَيۡءٍ أَحۡصَيۡنَٰهُ فِيٓ إِمَامٖ مُّبِينٖ ١٢ ﴾ [يس: ١٢].

(Kowane abu mun lissfe shi a cikin wani littafi mai bayyanawa).

Ya zo a sunna cikin hadisin Abdullah ɗan Amr bn Ass, Manzo Allah ya ce, (Allah ya rubuta abubuwan day a ƙaddarawa halitta kafin ya halitta sammai da ƙasa da shekara dubu hamsin.

Mataki na uku: Sai Allah ya so faruwar abu, domin duk abin da Allah ya so wakanarsa zai wakana, abin da bai ga damar wakanarsa ba zai wakana ba. Allah yana cewa,

﴿ إِنَّمَآ أَمۡرُهُۥٓ إِذَآ أَرَادَ شَيۡـًٔا أَن يَقُولَ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ ٨٢ ﴾ [يس: ٨٢].

(Kawai al'amarinsa, idan ya yi nufin wani abu sai ya ce da shi, kasance, sai ya kasance).

Kuma Allah yana cewa:

﴿ وَمَا تَشَآءُونَ إِلَّآ أَن يَشَآءَ ٱللَّهُ رَبُّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٢٩ ﴾ [التكوير: ٢٩].

(Kuma ba abin da kuka so ne yake kasancewa ba, sai abin da Allah Ubangijin talikai ya so wakanarsa).

Bukhari da Muslim sun ruwaito daga Abu Hurairah (R.A.) y ace, Manzon Allah (ﷺ) y ace, "Ka da ɗayanku ya ce, Ya Allah ka gafarta mani in ka ga dama. Ya Allah ka ji ƙaina in ka ga dama. Ya sa gaske cikin addu'arsa, domin shi Allah yana aikata abin da ya ga dama ne, babu mai tilasta shi).

Mataki na huɗu: Halittar Allah ga abubuwa da samara da su da ƙudurarsa cikakkiya. Allah shi ne ya halicci kowane mai aiki da aikinsa, da duk mai motsi da motsinsa, dad k mai sukuni da sukuninsa. Allah ta'ala ya ce:

﴿ خَٰلِقُ كُلِّ شَيۡءٖ فَٱعۡبُدُوهُۚ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ وَكِيلٞ ١٠٢ ﴾ [الأنعام: ١٠٢].

Ma'ana: (Allah ne mahallicin komai, kuma shi wakili ne ga dukkan komai).

Kuma Allah yana cewa,

﴿ وَٱللَّهُ خَلَقَكُمۡ وَمَا تَعۡمَلُونَ ٩٦ ﴾ [الصافات: ٩٦].

(Kuma Allah ne ya halicce ku da abin da suka kasance suna aikaitawa).

Bukhari ya ruwaito daga Imaran bn Husaini, daga Annabi (ﷺ) ya ce: "Allah yana nan, lokacin da babu wani abu tare da shi. Kuma al'arshinsa ya kasance a kan ruwa. Kuma ya rubuta komai acikn lauhul mahfuz. Kuma ya halicci sammai da ƙasa).

Don haka dole ne musulmi ya yi imani da waɗannan matakai na ƙaddara guda huɗu. Duk wanda ya musunta ɗaya daga cikinsu to bai yi imani da ƙaddara ba.

Ya ku bayin Allah! Ku sani cewa, Imani da ƙaddara yana fa'idoji, waɗanda su ne kamar haka:

1. Dogaro ga Allah, lokacin da bawa ya bi matakan da ya kamata ya bi. Domin Allah shi ne wanda yake halittar sababi, da abin da sababin yake haifarwa.
2. Samun nutsuwar zuciya. Saboda bawa ya san cewa, duk abin ya faru ƙaddara ce daga Ubangiji.
3. Rashin jiji-da-kai lokacin da bawa zai samu muradinsa. Domin haka ƙaddara ce daga Allah, domin shi ne ya hore masa hanyoyin samin alheri. Don haka sai ya godewa Allah, ya gujewa jiji-da-kai.
4. Rabuwa da damuwa da ɓacin rai lokacin da bawa ya rasa samun abin da ya yi muradi. Domin hakan ya faru ne da ƙaddarar Allah da hukuncinsa. Don haka sai ya yi haƙuri Allah ya ba shi lada a kan hakan.

Ya ‘yan uwa! Haƙiƙa Allah yana cewa,

﴿ مَآ أَصَابَ مِن مُّصِيبَةٍ إِلَّا بِإِذۡنِ ٱللَّهِۗ وَمَن يُؤۡمِنۢ بِٱللَّهِ يَهۡدِ قَلۡبَهُۥۚ وَٱللَّهُ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمٞ ١١ ﴾ [التغابن: ١١].

(Babu wata masifa da za ta faru, sai da izinin Allah. Duk wanda ya bayar da gaskiya da Allah, to Allah zai shiryar da zuciyarsa. Allah masani ne da komai.) Allah yana cewa,

﴿ مَآ أَصَابَ مِن مُّصِيبَةٖ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَلَا فِيٓ أَنفُسِكُمۡ إِلَّا فِي كِتَٰبٖ مِّن قَبۡلِ أَن نَّبۡرَأَهَآۚ إِنَّ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٞ ٢٢ ﴾ [الحديد: ٢٢].

(Babu wata masifa da za ta faru, face sai tana cikin littafi, tun gabanin mu halicce ta. Lallai hakan, mai sauƙi ne a wajen Allah).

Kuma Manzon Allah (ﷺ) yana cewa, “Ya kai ɗan Adam! Ka sani, da al’umma baki ɗaya za su taru, don su cuce ka da wani abu, to ba za su iya ba, sai da abin da Allah ya rubuta maka. Haka ma, da za su taru don su amfane ka da wani abu, ba za su iya mafanarka ba, sai da abin da Allah ya rubuta.” Kuma Manzon Allah (ﷺ) yana cewa, “Idan wani abu ya same ka, kada ka ce ina ma na yi kaza, ko kaza, a’a, ka ce, ƙaddara ce ta Allah, kuma abin da ya ga dama, ya aikata. Domin ‘da’ tana buɗe ƙofar shaiɗan.” Haka kuma, ya tabbata a cikin hadisi, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Abin mamaki ga lamarin mumini: Idan abin daɗi ya same shi, sai ya gode wa Allah, hakan sai ya zamo masa alheri; idan cuta ta same shi, sai ya yi haƙuri, hakan sai ya zame masa alheri.” Ali ya rawaito cewa, Manzon Allah (ﷺ) wata rana ya ke wajen jana’iza, sai ya ɗauki wani abu, yana tona ƙasa da shi. Sai ya ce, “Babu wani mutum, face an rubuta mazauninsa na wuta ko aljanna.” Sai suka ce, “Ya Ma’aikin Allah! Ba ma dogara da abin da aka rubuta mana ba, mu daina aiki?” Sai ya ce, “A’a! Ku yi aiki. Kowa za a saukaƙe shi ga abin da aka halicce shi don shi.

Wanda ya zamo mai rabo, sai a sawwaƙe shi ga aikin masu rabi, haka wanda yake cikin taɓɓaɓu, sai a sawwaƙe masa aikin taɓaɓɓu.”

Ku sani, ya ‘yan uwa! Kungiyoyi biyu ne suka ɓata a babin ƙaddara: Kadariyya, waɗanda suka ce abubuwa na faruwa ne ba tare da sanin Allah ba, da Jabariyya, waɗanda suka ce ɗan Adam tilas ake yi masa kan abin da yake aikatawa. Dukkaninsu ɓatattu ne. Allah ya ƙaddara komai da komai, ya kuma bai wa ɗan Adam iko na ya zaɓi abin da ya ga dama. Kamar yadda Allah ya ce, “Lallai mun shiryar da ɗan Adam tafarki, ko dai ya zama mai godiya, ko ya zama mai butulci.” Yahaya bin Ya’amur ya ce, farkon wanda ya fara magana kan ƙaddara a Basrah, shi ne Ma’abad Aljuhani. Ya ce, “Sai muka yunƙura, ni da Humaid bin Abdurrahman, muka tafi hajji ko umarah, sai muka ce, ina ma mu haɗu da wani cikin sahabbai, mu tambaye shi kan abin da su Ma’abad suke faɗi kan ƙaddara. Sai muka yi katari da Abdullahi ɗan Umar, zai shiga masallaci. Sai muka tare shi, ni da abokina, ɗaya yana damansa, ɗaya yana hagunsa. Sai na fahimci abokina zai bar ni, na yi magana. Sai na ce, “Abu Abdurrahman, wasu mutane sun bayyana a wajenmu, suna karatun Alƙur’ani, suna bibiyar ilimi.” Ya faɗi labarinsu, kuma ya ce, “Kuma suna cewa, sai abu ya faru, sannan Allah yake sani. Suka ce babu ƙaddara.” Sai ya ce, “Idan ka haɗu da su, ka gaya musu cewa, bari ba su suma ba su sani. Na rantse da wanda Abdullahi bin Umar yake rantsuwa da shi, da ɗayansu zai ciyar da misalin dutsen Uhud na zinare, Allah ba zai karɓa ba, har sai ya ba da gaskiya da ƙaddara.” Sannan ya karanto dogon hadisin nan na zuwan Jibirilu, da tambayoyi da ya yi wan Manzon Allah (ﷺ).

MA’ANAR IBADA A MUSULUNCI

Manufofin huɗubar

- Bayanin manufar samar da halittu.
- Bayanin gamammiyar ma’anar ibada a musulmi.
- Bayanin cewa, ibada kala-kala ce a musulunci.
- Bayyanin cewe, kyautata niyya game da abubuwan da suke halal ne yana mayar da su ibada.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma mua neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan aiyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar dashi, wanda kuma ya atar babu mai shiryar da shi, kuma ina shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai allah, shi kaɗai ne bashi da abokin taraiya, kuma ina shaidawa cewa Annabi Muhammad bawansane manzonsane, (Yaku waɗanda kuka bada gaskiya kuji tsoron Allah yadda ya cancanta aji tsoronsa, kada ku mutu face kuna Musulmi). (Yaku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicce ku daga rai guda ɗaya kuma ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga gare su (su biyu) kuji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya dashi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku waɗanda suka yi imani kuji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku aiyukanku, kuma ya gafarta muku zunubanku. Wanda ya bi Allah da manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawun shiriya shiriyar Annabi Muhammadu (ﷺ) kuma mafi sharrin al’amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wata bidi’a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Ya ku bayin Allah! Haƙiƙa Allah mai girma da buwaya bai halicci halittu dan wasa ba, kuma bai bar su sasakai ba. Allah ya halicce su ne don wata hikima mai girma. Allah mabuwayi da ɗaukaka, yana cewa:

﴿ وَمَا خَلَقۡنَا ٱلسَّمَآءَ وَٱلۡأَرۡضَ وَمَا بَيۡنَهُمَا بَٰطِلٗاۚ ذَٰلِكَ ظَنُّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْۚ فَوَيۡلٞ لِّلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنَ ٱلنَّارِ ٢٧ ﴾ [ص: ٢٧].

(Kuma ba mu halicci sama da ƙasa da abin da ke cikinsu a banza ba, wannan shi ne zaton waɗanda suka kafirce, to bone ya tabbata ga waɗanda suka kafice na azabar wuta).

Allah mabuwayi ya ce:

﴿ وَمَا خَلَقۡنَا ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ وَمَا بَيۡنَهُمَا لَٰعِبِينَ ٣٨ مَا خَلَقۡنَٰهُمَآ إِلَّا بِٱلۡحَقِّ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَهُمۡ لَا يَعۡلَمُونَ ٣٩ ﴾ [الدخان: ٣٨ – ٣٩].

(Kuma ba mu halicci sammai da ƙasa da abin da yake cikinsu muna masu wasa ba, ba mu halicce ba sai da gaskiya, sai dai yawancinsu ba su sani ba).

Allah Ta’ala ya bayyana wannan haƙƙin wanda don shi ne ya halicci halitta sai ya ce:

﴿ وَمَا خَلَقۡتُ ٱلۡجِنَّ وَٱلۡإِنسَ إِلَّا لِيَعۡبُدُونِ ٥٦ مَآ أُرِيدُ مِنۡهُم مِّن رِّزۡقٖ وَمَآ أُرِيدُ أَن يُطۡعِمُونِ ٥٧ ﴾ [الذاريات: ٥٦ – ٥٧].

(Kuma ban halicci aljanu da mutane ba, sai don su bauta min. Ba na neman wani arzuƙi a wajensu, kuma ba neman su ciyar da ni).

Don haka hikimar da ta sa ya halicci halittarsa, shi ne, ya umarce su da bauta masa, kuma su tsaya a kan aiki da abin da ya wajabta musu. Ya aiko manzanni masu bshara da gargaɗi don su sanar da halittu Ubangijinsu, su bayyana musu manufar da aka halicce su don ita, daga cikinsu akwai wanda ya karɓi shiriya, da kuma wanda ya mayar, hujjar Allah mai tsayuwa ce a kan bayi.

Ya kai musulmi, ka lura da faɗin Allah Ta’ala;

﴿ وَمَا خَلَقۡتُ ٱلۡجِنَّ وَٱلۡإِنسَ إِلَّا لِيَعۡبُدُونِ ٥٦ ﴾ [الذاريات: ٥٦]

(Kuma ban halicci aljanu da mutane ba sai don su bauta min).

Da faɗinSa:

﴿ وَٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ وَلَا تُشۡرِكُواْ بِهِۦ شَيۡـٔٗا ﴾[النساء: ٣٦].

(Ku bautawa Allah, kuma kada ku tara bautarsa da wani abu).

Ya ku bayin Allah! Ibada tana da ma’ana gamammiya, asalin wannan ibadar shi ne tsarkake addni ga Allah. Ka kaɗaita Allah da dukkan nau’in bauta, ka fuskanta zuwa ga Allah da zuciyarka da so da tsoro da fata. Hakan nan kowace ibada ka yi ta ga Allah. Sallarka ga Allah, addu’arka ga Allah, matsuwarka ga Allah, tsoronka na gaskiya ga Allah, cikar fata da amincewa ga Allah, babu girmama wanin Allah a zuciyarka. Girmamawa ta gaskiya ga Allah shi kaɗai take.

﴿ ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلۡحَقُّ وَأَنَّ مَا يَدۡعُونَ مِن دُونِهِۦ هُوَ ٱلۡبَٰطِلُ وَأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلۡعَلِيُّ ٱلۡكَبِيرُ ٦٢ ﴾ [الحج: ٦].

(Wannan saboda cewa Allah shi ne gaskiya, kuma abin da suke kira ba shi ba ƙarya ne).

Ya kai musulmi, haƙiƙa ma’anar ibada a shar’ar musulunci ma’ana ce ta gabaɗaya, gamammiya ga duk wani alheri daga lamarin addini a duniya da lahira. Haƙiƙa ibada, suna ne da ya tattare dukkanin maganganu da ayyukan da Allah yake so, kuma ya yarda da su. Musulmi a wannan duniyar ya san cewa shi bawa ne na Allah da bauta ta haƙiƙa, don haka shi yana aiki ne tuƙuru don tabbatar da wannan bautar, ba don komai ba sai don ya zama bawan Ubangijinsa na gaskiya. Domin duk wata darajarsa da falalarsa shi ne kasancewarsa bawan Allah na gaskiya. Yana aiwatar da umarce-umarcensa, yana nisantar hane-hanensa, yana tsaye wajen iyakokinsa, yana zartar da farillansa.

Ya kai musulmi, yana daga rahamar Allah da falalarsa a gare mu cewa, ya sanya ibadu nau’i-nau’i. Akwai ibadu na zuciya, su ne, wanda bawa yake yin su da zuciya, kamar ikhlasi da nufatar Allah da dukkan nau’in ibada. Akwai kuma ibada ta jiki, kamar waɗannan salloli guda biyar da musulmi yake yinsu a kowace rana da yini. Haka kuma akwai ibadar da ta shafi kuɗi, kamar zakka da musulmi yake

fitarwa don imani da neman yardar Allah, yana kuma mai ƙara neman kusanci ga Ubangijinsa. Akwai ibadar da bawa yake hana zuciyar bin sonye-soyenta, don biyayya ga Allah kamar yadda yake a a zumi. Akwai ibada da jiki da dukiya gabaɗaya kamar Hajji, domin shi ya haɗa da dukiya da jiki da jihadi a tafarkin Allah shi ne mafi falala da girma.

Sannan Allah Ta'ala ya yi mana falala ya shar'anta mana nafiloli a cikin sallah da nafiloli a sadaka da nifiloli a azumin da nafiloli a hajji da umara, duk wannan don ƙarfafa imaninmu da ɗaukaka darajarmu da ƙarin kyawawan ayyukanmu. Don haka yana da falala da baiwa a gare mu ba ma ƙididdige yabo a gare shi kamar yadda shi ya yabi kansa.

Ya 'yan'uwana a musulunci! Haƙiƙa shari'ar musulunci ta zo cikakkiya, gamammiya, ba ta ɗaukar ƙari ko ragi, Allah Ta'ala ya ce:

﴿ٱلۡيَوۡمَ أَكۡمَلۡتُ لَكُمۡ دِينَكُمۡ﴾ [المائدة: ٣].

(A yau ne na cika muku addininku...)

Allah ya sanya sharuɗa guda biyu, masu girma don karɓar aiki, idan an rasa ɗaya daga cikinsu to aiki ya ɓaci, ya zama rusasshe, abin watsarwa.

Na farko: Shi ne aikin ya zamo tsarkakakke don zatin Allah shi kaɗai, babu riya ba yi don a ji.

Na biyu: Shi ne ya zama daidai ne, ya dace da shari'ar Allah, da sunnar manzon Allah (ﷺ), ba ƙari ko bidi'a, domin Annabinmu Muhammad (ﷺ), ya isar da bayyanannen saƙo, bai bar wani abu na addin ba face sai da ya bayyana su, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Gaskiya ita ce abin da ya zo da shi.

Ya kai musulmi, ba ya ga haka, ka sani cewa; gaskiya ne duk kai-kawonka a cikin rayuwarka idan ka nufi zatin Allah da shi, duk maganganunka da ayyukanka idan nufi kusantar Allah da su, za su zama ibada ce ga Allah.

Musulmi yana bautawa Allah ta hanyar biyayya ga iyayensa da kyautata musu, domin an karɓo daga Abdullahi ɗan Amru ɗan Ass (R.A), ya ce, wani mutum ya zo wajen Annabi (ﷺ), sai ya nemi izininsa don yin jihadi, sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Shin mahaifanka suna da rai?" Sai mutumin ya ce, E. Sai ya ce, "Je ka ka yi jihadi ta hanyar yin biyayya a gare su". Bukhari da Muslim da Nasa'i da Abu Dawud da Tirmizi ne suka rawaito.

Ya kai musulmi, sada zumuncinka, ibada ce ga Allah, domin kana sauke wani wajibi ne da Allah ya wajabta maka, domin yana cewa:

﴿وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ ٱلَّذِي تَسَآءَلُونَ بِهِۦ وَٱلۡأَرۡحَامَ﴾[النساء: ١].

(Kuma ku ji tsoron Allah wanda kuke magiya da shi kuma ku ji tsoron (yanke) zumunta).

Ya kai musulmi! Ciyarwarka ga 'ya'yanka ibada ce ga Allah. Annabi (ﷺ) yana cewa Sa'ad ɗan Abu Waƙƙas: "Haƙiƙa ba za ka ciyar da wata ciyarwa ba kana nufin zatin Allah da ita, face an ba ka lada a kanta, har abin da kake sanyawa a bakin matarka". Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

'Ya'yanka maza da mata tarbiyyarsu da saita su bisa kan tafarki madaidaici da tsayuwa da haka bauta ne ga Allah. Domin Allah yana cewa,

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ قُوٓاْ أَنفُسَكُمۡ وَأَهۡلِيكُمۡ نَارٗا ﴾ [التحريم: ٦].

(Ya ku waɗanda suka yi imani, ku kare kanku da iyalanku daga shiga wuta).

Ya kai musulmi! Cinikinka, da kai-kawonka wajen saye da sayarwa, da gwagwarmayarka wajen kasuwanci, idan ka nufi bauta ga Allah da amfanar da al'umma da shi, za a ba ka ladan kyakkyawar niyyarka.

Aurenka kana mai nufin kame kanka, da katange farjinka, da runtse ganinka, ibada ce ga Allah, kuma ɗa'ar da kake neman kusancin Allah da ita.

Bautarmu ga Allah ba ta taƙaita a kan rukunai kaɗai ba. A'a ta ƙunshi ɗaukacin aikata wajibai da nisantar abubuwan da aka haramta.

Ya ɗan'uwana musulmi, yayin da ka kaucewa ƙasƙantattun halaye da ayyukan haram, domin biyayya ga Allah, ka sani cewa wannan ibada ce ga Allah kake yi. Don haka Ɗalƙ bn Habib ya fassara haƙiƙanin tsoron Allah da cewa, "Ka yi aiki da biyayyar Allah, a bisa haske daga Allah, kana mai neman lada a gurin Allah, kuma ka bar saɓon Allah, a bisa haske daga Allah, kana tsoron uƙubar Allah.

Ibn Mubarak ne ya ruwaito shi a cikin littafin az-Zuhud.

Musulmi mai gaskiya a cikin sayensa da sayarwarsa, ba ya ƙarya ba ya ha'inci ba ya yaudara, wannan ma ibada ce ga Allah. Sulhunta tsakanin masu husuma biyu ibada ce ga Allah. Yaye baƙin cikin masu baƙin ciki da damuwar masu damuwa da ƙuncin masu ƙunci duka ibada ne ga Allah maɗaukakin sarki.

Don haka maganganunsa da ayyukansa, idan niyyarsa ta kyautatu ta tsarkaka ga Allah a cikin duk halayensa, ya zama mai bauta da biyyaya ga Ubangijinsa.

Haka shari'ar musulunci, ke kiran musulmi zuwa alheri. Allah mai buwaya da ɗaukaka ya yawaita hanyoyin alheri, duk wannan domin ƙarin lada da ɗaukaka darajoji da kankare zunubai.

Ya kai ɗau'uwana musulmi, ka ƙarfafa amincewarka da Ubangijinka, ka yi aiki don lahirarka, ka tsaya ƙyam kan biyayya, ka halarto da niyyarka, ka tsaya kan gaskiya a cikin duk wata kyakkyawar magana, ko kyakkyawan aiki, domin ka zama mai bauta ga Ubangijika mai ba da haƘƘin bautar.

Ya kai musulmi! Haƙiƙa faɗi-tashin musulmi don wata maslaha ta al'umma ibada ce ga Allah. Musulmi idan ya yi ƙoƙari wajen amfanar da jama'a, ya zama mai bautar Allah. Bukhari da Muslim sun ruwaito hadisi daga Anas ɗan Malik, ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Babu wani musulmi da zai shuka wata shuka, wani mutum ko tsuntsu ya ci daga gare ta, face ya sami lada". Wannan duk domin kwaɗaitar da musulmi wajen rungumar ayyukan al'umma.

Kawar da abin da zai cutar daga kan hanya sadaka ne, kuma ibada ne. Kai duk wani ilimi da bawa zai koye shi, idan ya nufi amfanar al'umma da shi tare da maslaharsa ta duniya, kuma ya nufi zatin Allah da shi, to Allah zai ba shi ladan niyyarsa, domin kowane mutum zai sami sakamakon niyyarsa ne. Wannan kuwa yana cikin falalar Allah da karamcinsa da kyautatawarsa gare mu.

Ya kai musulmi! Don haka ka tsaya kan biyayya, ka dage a kan ibada, kuma ka kiyayi ƙosawa da sarewa. Allah yana cewa,

﴿ وَٱعۡبُدۡ رَبَّكَ حَتَّىٰ يَأۡتِيَكَ ٱلۡيَقِينُ ٩٩ ﴾ [الحجر: ٩٩].

(Kuma ka bautawa Allah Ubangiji har mutuwa ta riske ka).

Kada ya zama himmarka ka gama ibada, ko ibada ta ƙare, ka damu da kyautatata da tsayawa da haƙƙoƙinta, ka aiwatar da ibada da daɗin zuciya, da yalwar ƙirji, da farin ciki.

Ya kai musulmi! Haƙiƙa Annabinmu yana cewa Bilal “Ka kwantar mana da hankali da sallah”. Ahmad ne ya rawaito shi. Kuma yana cewa: “Kuma an sanya farin cikina a cikin sallah”. Nasa’i ne ya rawaito daga Anas (R.A).

Ya kai musulmi! Don haka ne Annabi ya hana musulmi, tsaurarawa da wuce iyaka a cikin addinisu, ya kuma hana su bautar da za su ƙosa su gaji da ita. Yayin da labari ya iske shi (ﷺ), game da Abdullahi ɗan Amru ɗan Ass (R.A), dangane da ibadarsa mai yawa, da daddare sallah, da rana tilawa, da azumi da ibada, matarsa ta kai ƙara wajen Manzon Allah, kan cewa mijinta ga irin abin da yake yi wanda yake damunta; ta ce shi bai taɓa yaye mana lulluɓi ba. Idan dare ya yi, sai ya ƙare shi a salla da karatun Alƙur’ani. Idan rana ce kuwa sai ya zarce da azumi, ya ci gaba yana azumtar kwanaki dukkansu. Yana ƙiyamullaili a dukkanin darare. Sai Annabi (ﷺ), ya kira shi ya ce da shi: “Ba an ba ni labarin cewar kana tsayuwar dare (dukkansa) ba, kuma kana azumtar yini ba?” Sai ya ce; Haka ne. Sai manzo (ﷺ), ya ce masa “Ya Abdullahi ɗan Amr, haƙiƙa Ubangijinka yana da haƙƙi a kanka, jikinka ma yana da haƙƙi a kanka, iyalinka ma na da haƙƙi a kanka. Ya Abdullahi ka azumci kwana uku daga kowane wata”, Sai ya ce; Ni zan iya fiye da haka. Annabi bai gushe da shi ba, har sai da ya sanya azuminsa kwana ɗaya, shan sa kwana ɗaya. Ya ce; “Wannan shi ne azumin Annabi Dawud, babu fiye da azumin Annabi Dawud". Ya Abdullahi ka yi bacci rabin dare, ka yi sallah sulusinsa, asannan ka yi barci (a karo na biyu), sudusinsa”. Sannan ya ce da shi: “Ka sauke Alƙur’ani a kowane wata sau ɗaya” Bai gushe da shi ba, har ya sanya shi yana sauke shi a kowanne kwana uku.

Abdullahi ɗan Amr ya bi wannan hanya, kuma ya lazimci wannan ladabi. Annabi ya ba shi labarin cewa yana kusa da ya wahala, shekaru kuwa ba su shuɗe ba, har sai da Abdullahi ya kasa yin wannan aiki. Sai ya kasance yana haɗa kwanaki yana azumtarsu, sannan sai ya sha azumi a kwanaki kwatankwacinsu. Yana cewa; ina ma na karɓi rangwamen Annabinku (ﷺ). Bukhari ne ya fitar da shi a cikin azumi da muslim ma a babin azumi.

A’isha (R.A) tana cewa: “Annabi (ﷺ) ya kasance yana azumi har mu ce ba zai sha ba, kuma yana sha, har mu ce ba zai yi azumi ba". Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.

Wasu malamai suka ce, wannan ya yi ne don shi yana lura da maslahohi, yana gabarat da waɗanda suka fi falala, a bisa koma bayansu. Idan akwai wasu al'amuran a cikin al’umma, sai ya jinkirta azumin don biyan buƙatar musumi, idan kuwa ba lokacin wannan ba ne, sai ya yi.

Kuma ya ce, “Wanda ya yi azumin shekara ba shi da ladan azumi”.

Ya kai musulmi! Don haka bidi'o'i da ƙari a cikin lamura ba tare da umarnin shari'a ba dukkninsu babu alheri a cikinsu. A lazimci hanya miƙaƙƙiya, wadda babu shisshigi da sakaci a cikinta.

Kuma Annbi (ﷺ) yana cewa, "Haƙiƙa mafi soyuwar ayyuka a wajen Allah shi ne wanda mai yinsa ya dauwama a kansa, koda kaɗan ne". Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi, daga A'isha (R.A).

Don haka aiki kaɗan da za ka lazimce shi, ka aiwatar da shi da kyau shi ya fi alheri fiye da aiki da yawa da za ka yi shi yau, sannan ka watsar da shi kwanaki. Kasancewar musulmi yana da ibadu kala-kala, an ba shi damar ya ɗauki abin da zai iya a kowanne nau'i. Wannan shi ake nema daga musulmi don ya kasance a cikin azumisa mai ƙaƙƙarfar alaƙa ne da Ubangijinsa, da kuma addininsa, sannan da Annabinsa.

Ina roƙon Allah dacewa da shiriya zuwa kowane alheri, ga kaina da ku, shi mai iko ne a bisa kowane abu.

Allah ya yi min albarka tare da ku, a cikin alƙur'ani mai gima, kuma ya amfanar da ni da ku da abin da ke cikinsa, na ayoyi da wa'azi mai hikima. Abin da zan iya faɗa ke nan, kuma ina nemman gafarar Allah mai girma ga kaina da ku, da sauran musulmi daga kowane zunubi, ku nemi gafararsa, ku tuba zuwa gare shi, lallai shi mai gafara ne mai jinƙai.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga mafi darajar halitta wanda aka aiko shi don ya zama jinƙai ga talikai, da alayensa da sahabbansa da waɗanda suka tafi a bisa tafarkinsa har zuwa ranar sakamako, bayan haka:

Ya ku bayin Allah! Ibada ni'ima ce da ba mai jin (ɗanɗanonta), sai wanda ya rasa ta. Ku tambayin 'yan duniya, ku tambayin waɗanda suka ɗanɗani abubuwar more rayuwa ta duniya, suka hau abin da suke so, su sa tufafin da suka ga dama. Suka more da duk wani abu na rayuwa, kamar yadda Allah Ta'ala Ya ce:

﴿ وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ يَتَمَتَّعُونَ وَيَأۡكُلُونَ كَمَا تَأۡكُلُ ٱلۡأَنۡعَٰمُ وَٱلنَّارُ مَثۡوٗى لَّهُمۡ ١٢ ﴾ [محمد: ١٢].

(Su kuwa waɗanda suka kafirce, suna morewa, kuma suna ci kamar yadda dabbobi suke ci, kuma wuta ce makomarsu).

Sai kuma me? Idan imani bai zauna a ƙoƙoan zuciyar su ba? Idan kuma ba su san darajar imani da bauta ga Allah sarki ɗaya ba? Idan ba su sami alaƙa tsakaninsu da Allah mabuwayi mai ɗaukaka ba? Ba su sami ganawa da shi ba a kowane yini da dare sau biyar. Haƙiƙa abin da wannan yake nufi shi ne rushewar rayuwa ta haƙiƙa, rushewar rayuwar ruhi, rayuwar tunani da imani, da rayuwar aƙida.

Wai shin menene mutum, idan ba tare da imani ba? Su wanene mutane ba tare da aƙida ba? Su wanene mutane ba tare da bautawa Allah ba? Dabbobin daji ne a daji, ko dabbobin gida ne a garke. Amma idan suka zamo muminai masu tauhidi

na gaskiya suka ado da imani, suna lazimtar koyarwa ta musulunci, suna ɗabbaƙa mafi girman tsari da ‘yan’adam suka taɓa sani a tarihinsu, kuma ba za su san kamar sa ba har zuwa tashin alƙiyama.

Ya ku bayin Allah! Haƙiƙa da yawan mutane yau sun munana fahimmta ma’anar ibada, sun taƙaice ta - don jahilcinsu da ɓatansu - a kan wani adadi na ayukan bauta. Suka jahilci manufofinata da abubuwan da ta ƙunsa., Ta hanyar bayanin gamammiyar ma’anarta za mu fahimci yadda wasu suka kauce hanya wajen fahimtar haƙiƙanin abin da ake nufi da ibada. A nan za mu iya kasa su gida uku:

Nau’i na farko: Wanda ya yi wa ibada ƙuntatacciyar fahimta, ya zaci cewa ita ibada ba ta wuce wasu ayyuka na ibada da aka sani ba, kamar sallah da azumi da zakka da umara da hajji. Idan yana masallaci to shi mai bauta ne ga Ubangijinsa, idan ya fita daga masallaci sai ya yi mu’amala da riba, ya rungumi zina, ya sha giya, ya saɓawa iyaye, ya munana zama da abokansa a wajen aiki, da ɗungushe a gurin aiki, za ka ga matarsa da ‘ya’yayensa mata suna shiga ta fitsara. A masallaci yana tare da Allah, da wata fuska, a wajen masallaci kuma yana tare da Allah da mutane da wata fuskar ta daban. Yana bin umarnin Allah a suratul Baƙara:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ كُتِبَ عَلَيۡكُمُ ٱلصِّيَامُ ﴾ [البقرة: ١٨٣].

(Ya ku waɗana suka imani, an wajabta muku azumi).

Amma ba ya bin umarnin Allah, da ya zo a cikin ita dai wannan surar, inda Allah yake cewa:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ كُتِبَ عَلَيۡكُمُ ٱلۡقِصَاصُ فِي ٱلۡقَتۡلَى ﴾ [البقرة: ١٧٨].

(Ya ku waɗanda suka yi imani an wajabta muku ƙisasi game da waɗanda aka kashe).

Yana bin umarnin Allah a cikin Suratul Ma’idah:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِذَا قُمۡتُمۡ إِلَى ٱلصَّلَوٰةِ فَٱغۡسِلُواْ وُجُوهَكُمۡ وَأَيۡدِيَكُمۡ إِلَى ٱلۡمَرَافِقِ وَٱمۡسَحُواْ بِرُءُوسِكُمۡ وَأَرۡجُلَكُمۡ إِلَى ٱلۡكَعۡبَيۡنِ ﴾[المائدة: ٦].

(Ya ku waɗana kuka ba da gaskiya idan kun tashi zuwa sallah to ku wanke fuskokinku, da hannayenku zuwa gwiwoyin hannu, ku shafi kawunanku da (wanke) ƙafarku zuwa idanun sawu biyu).

Amma ya tozarta umarnin Allah na cikin Suratul Ma’idah, ɗin kanta:

﴿ وَمَن لَّمۡ يَحۡكُم بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡكَٰفِرُونَ ٤٤ ﴾ [المائدة: ٤٤].

(Duk wanda bai yi hukunci da abin da Allah ya saukar ba, to waɗannan su ne kafirai).

Wannan gurguwar fahimta ce tauyayyiya. Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa:

﴿ أَفَتُؤۡمِنُونَ بِبَعۡضِ ٱلۡكِتَٰبِ وَتَكۡفُرُونَ بِبَعۡضٖۚ فَمَا جَزَآءُ مَن يَفۡعَلُ ذَٰلِكَ مِنكُمۡ إِلَّا خِزۡيٞ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَاۖ وَيَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ يُرَدُّونَ إِلَىٰٓ أَشَدِّ ٱلۡعَذَابٖۗ وَمَا ٱللَّهُ بِغَٰفِلٍ عَمَّا تَعۡمَلُونَ ٨٥ ﴾ [البقرة: ٨٥].

(Yanzu kuna imani da sashin littafi kuma ku kafirce da sashi, to ba komai ne sakamakon wanda yake aikata haka daga cikinku ba, face tozarata cikin rayuwar duniya, kuma a ranar alƙiyama za a mai da su zuwa mafi tsananin azaba, kuma

Allah ba mai gafala ba ne a bisa abin da kuke aikatawa).

Lallai wannan tawaye ce a cikin fahimtar ma'anar ibada.

Nau'i na biyu: Ya karkatar da ibada ga wanin Allah Mai buwaya da ɗaukaka. Ya miƙa wuya ga wata shari'a ba ta Allah. Yana yanka ga wanin Allah, yana rantsuwa da wanin Allah, yana ɗawafi ba a ɗakin Allah, don girmama wanin Allah, yana gabatar da bakance ga wanin Allah, yana neman taimakkon wanin Allah. Yana neman agajin wanin Allah, yana fakewa ga wanin Allah, yana fawwala lamarinsa zuwa wanin Allah, yana dogara ga wanin Allah, yana amincewa da wasu ƙasashen duniya da al'ummar ƙasar fiye da amincewarsa da mahaliccin sama da ƙasa. Daga cikinsu akwai wanda ya ce: Idan lamurra suka wuyata a gare ku, to ku bazama zuwa mutanen cikin ƙabari! Daga cikinsu akwai wanda yake cewa: Shi ya ƙudurce cewa duniya tana da waliyyai ƙuɗubai da waliyyai watadai, da abdalu, da suke sarrafa tsarin duniya, suke tafiyar da lamurranta!! Alhali Allah mai buwaya da ɗaukaka yana cewa:

﴿ قُلۡ إِنَّ ٱلۡأَمۡرَ كُلَّهُۥ لِلَّهِ ﴾[آل عمران: ١٥٤].

(Ka ce, lalle al'amari dukkaninsa na Allah ne).

Daga cikisu akwai wanda yake cewa: Lallai mu muna bikin tuna ranar haihuwar Sayyid Badawi abin tsoro, wanda in an kira shi zai amsa a kan tudu ne ko a cikin kogi. Allah mai buwaya da ɗaukaka yana cewa:

﴿ أَمَّن يُجِيبُ ٱلۡمُضۡطَرَّ إِذَا دَعَاهُ وَيَكۡشِفُ ٱلسُّوٓءَ وَيَجۡعَلُكُمۡ خُلَفَآءَ ٱلۡأَرۡضِۗ أَءِلَٰهٞ مَّعَ ٱللَّهِۚ قَلِيلٗا مَّا تَذَكَّرُونَ ٦٢ ﴾ [النمل: ٦٢].

(Wane ne wanda yake amsawa mai tsananin buƙata idan ya kira shi? Kuma yake yaye masifa, kuma yake sanya ku masu mayewa a bayan ƙasa? A yanzu akwai wani Ubangiji ba Allah ba? Kaɗan ne ƙwarai kuke wa'azantuwa).

Kuma Allah mabuwayi da ɗaukaka yana cewa:

﴿ وَإِن يَمۡسَسۡكَ ٱللَّهُ بِضُرّٖ فَلَا كَاشِفَ لَهُۥٓ إِلَّا هُوَۖ وَإِن يَمۡسَسۡكَ بِخَيۡرٖ فَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ١٧ ﴾ [الأنعام: ١٧].

(Idan Allah ya same ka da cuta babu mai yaye ta sai shi, idan ya same ka da alheri shi mai iko ne a bisa kowane abu).

Nau'i na uku: Wanda ya sarrafar da ibada ga Allah, yana neman yardarsa da ita, ba ma kokwnato a cikin ikhlasinsa. Sai dai shi ya yi ibada ba a bisa shiriyar Al-mustafa ba, kuma ba a kan sunna ba. Ibadarsa a bar mayar masa ce. Ba za ta karɓu ba wajen Allah mai buwaya da ɗaukaka, Allah Ta'ala ya ce:

﴿ فَمَن كَانَ يَرۡجُواْ لِقَآءَ رَبِّهِۦ فَلۡيَعۡمَلۡ عَمَلٗا صَٰلِحٗا وَلَا يُشۡرِكۡ بِعِبَادَةِ رَبِّهِۦٓ أَحَدَۢا ١١٠ ﴾ [الكهف: ١١٠].

(To wanda ya kasance yana fatan gamuwa da Ubangijinsa, to ya aikata aiki na gari, kuma kada ya tara bautar Ubangijinsa da wani).

Bukhari da Muslim sun ruwaito hadisi daga A'isha tana cewa, lallai Annabi (ﷺ) ya ce: "Wanda ya farar da wani abu a cikin lamarinmu wannan (addininmu), abin da ba ya cikinsa to shi abin mayarwa ne gare shi."

Za a mayar da shi, Allah ba zai karɓe shi ba. Shin wanda ya ƙara wani abu a cikin addinin Allah, ya farar da wani sabon abu da Allah bai yi izini da shi ba a

cikin shari'ar Allah, shin wannan ya bautawa Allah haƙiƙatan?

Ya ku musulmi! Matuƙa a cikin bautar bawa ga Ubangijinsa shi ne har zuwa mutuwa, faɗin Allah Ta'ala ya bayyana haka ƙarara inda ya ce,

﴿ وَٱعۡبُدۡ رَبَّكَ حَتَّىٰ يَأۡتِيَكَ ٱلۡيَقِينُ ٩٩ ﴾ [الحجر: ٩٩].

(Ka bautawa Ubangijinka har mutuwa ta zo maka).

Wannan yana bayyana cewa bautar mutum ga Allah da tsayawara da wajibansa, ba a iyakance shi da wata iyaka, ba ya da ƙarshe sai mutuwa, sai lokacin barin wannan rayuwa. Ita kuwa mutuwa ita ce, wannan abu na gaske, mai ɗaci mai wahala wanda ita bisa haƙiƙa, take da nauyi a zukatan mutane ba su sonta a bisa ɗabi'arsu, Allah Ta'ala Yana cewa:

﴿ كُلُّ نَفۡسٖ ذَآئِقَةُ ٱلۡمَوۡتِ ﴾[آل عمران: ١٨٥].

"Kowace rai mai ɗanɗan mutuwa ce"

A'uzu billahi minasshaiɗanir-rajim:

﴿ إِنَّ ٱلَّذِينَ قَالُواْ رَبُّنَا ٱللَّهُ ثُمَّ ٱسۡتَقَٰمُواْ تَتَنَزَّلُ عَلَيۡهِمُ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ أَلَّا تَخَافُواْ وَلَا تَحۡزَنُواْ وَأَبۡشِرُواْ بِٱلۡجَنَّةِ ٱلَّتِي كُنتُمۡ تُوعَدُونَ ٣٠ نَحۡنُ أَوۡلِيَآؤُكُمۡ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا وَفِي ٱلۡأٓخِرَةِۖ وَلَكُمۡ فِيهَا مَا تَشۡتَهِيٓ أَنفُسُكُمۡ وَلَكُمۡ فِيهَا مَا تَدَّعُونَ ٣١ نُزُلٗا مِّنۡ غَفُورٖ رَّحِيمٖ ٣٢ ﴾ [فصلت: ٣٠ – ٣٢].

"Haƙiƙa waɗanda suka ce, Ubangijinmu shi ne Allah. Sannan suka tsaya a kan tafarki, mala'iku suna sauka a gare su (yayin mutuwa suna cewa); kada ku ji tsoro, kuma kada ku yi baƙin ciki kuma ku yi bushara da aljannan nan da ake muku bushara da ita. Haƙiƙa mu ne majiɓintarku a cikin rayuwar duniya da lahira, kuma ku kuna da abin da zukatanku suke sha'awa a cikinta, kuma kuna da abin da kuke kira. Saukar baƙi ne daga Allah mai gafara mai jin ƙai."

TSAWATARWA DAGA LAIFUFFUKAN HARSHE

Manufofin huɗubar

- Sabawa kai da faɗar kyakkyawar magana da take yardar da Allah.
- Rabauta da yardar Allah.
- Nisantar miyagun maganganu.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammadu bawansa ne manzonsa ne. (Yaku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron Allah yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Yaku waɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammadu (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (a addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta".

Ya bayin Allah: harshe ni’ima ce daga ni’imomin da Allah ya yi wa ɗan adam, an halittawa ɗan adam shi domin ɗandanar abubuwa da kuma yin bayani. Allah yana cewa,

﴿ أَلَمۡ نَجۡعَل لَّهُۥ عَيۡنَيۡنِ ٨ وَلِسَانٗا وَشَفَتَيۡنِ ٩ وَهَدَيۡنَٰهُ ٱلنَّجۡدَيۡنِ ١٠ ﴾ [البلد: ٨ - ١٠]

Ma’ana: “Shin ba mu sanya masa idanuwa biyu ba ne? da harshe da kuma laɓɓa biyu, muka kuma shiryar da shi hanyoyi biyu, (ta alheri da ta sharri)..)

Shi harshe dai shi ake gane mai azancin magana, kuma mai nuna hankali da shiriyar mai iya sarrafa shi ne. Amma duk da haka wasu da dama harshen su ne ya kai su ga ƙabari. Gwaraza ma suna tsoron haɗuwa da illar harshe. Lallai kam babu abin da ke kifa fuskokin mutane a wuta sai abubuwan da harasansu suka girba musu.

Ya ‘yan uwa! Ku sani cewa mumini, bawan da yake tsoron Ubangijinsa, ba ya sakin harshensa yadda ya ga dama, saboda Allah ya wajabta masa kame harshensa a kowane hali kuma ya hana shi yin dukkan abin da yake kishiyantar hakan, kamar

yadda Allah ya hana shi yi da wani inda yake cewa:

﴿ وَلَا يَغۡتَب بَّعۡضُكُم بَعۡضًاۚ أَيُحِبُّ أَحَدُكُمۡ أَن يَأۡكُلَ لَحۡمَ أَخِيهِ مَيۡتٗا فَكَرِهۡتُمُوهُۚ ﴾ [الحجرات: ١٢].

(Kuma kada shashinku ya riƙa yin gibar shashi. Yanzu ɗayanku ya so ya ci naman ɗan uwansa yana matacce? Kun ƙyamaci hakan).

An karɓo daga Abu Barzatal Aslami, Allah ya yarda da shi ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Ya ku taron waɗanda suka yi imani da baki amma imani bai shiga zukatansu ba, kada ku yi da musulmai, kuma kada ku bibiyi tsiraicinsu, haƙiƙa duk wanda yake bibiyar tsiraicinsu, to shi ma Allah zai bibiyi tsiraicisa, duk kuwa wanda Allah ya bibiyi tsiraicinsa, to zai kunyatar da shi har a cikin gidansa”. Abu Dawud ne ya rawaito shi.

Kuma Allah Ya hana mumini yin gulma, kamar yadda ya zo a hadisin Abdullahi ɗan Abbas, cewa haƙiƙa Annabin (ﷺ) ya gifta wasu ƙaburbura biyu sai ya ce: “Tabbas ana azabtar da waɗanda suke cikisu kuma ba a kan wani abu mai wuyar bari ake azabtar da su ba. Laifin ɗayansu ba ya kaffa-kaffa da fitsari, ɗayan kuma yana yaɗa gulma ne”. Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

Bayan haka, yawan tsinuwa na daga cikin abubuwan da ke afka mata a cikin wuta, donn haka suka fi kowa yawa a wuta, kamar yadda yatabbata a cikin hadisin da aka karɓo daga Abu Sa’idil Khudri cewa manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Ya ku jama’ar mata ku yi ta yin sadaka, haƙiƙa na ga ku ne mafi yawan ‘yan wuta, sai suka ce: "Menene ya jawo hakan ya manzon Allah?" Sai ya ce: "Saboda kuna yawan tsinuwa da kuma butulcewa zama da miji”. Bukhari ne ya rawito shi.

Ita kuwa kyakkyawar kalmar da take yardar da Allah, tana ɗaukaka darajar bawa ne. Ya tabbata a hadisin Abu Huraira da ke cikin Sahihil Bukhari, daga Annabi (ﷺ) ya ce, “Haƙiƙa bawa kan furta kalamar da take jawo fushin Allah, ba tare da bwan ya ɗauki kalmar a bakin komai ba, amma kuma sai ta jawo masa shiga wutar jahannama”.

Ya bayin Allah! Haƙiƙa Annabin (ﷺ) ya bai wa wannan ɓangare matuƙar muhimmanci inda ya ɗauki tsare harshe a matsayin mallakar alkhairi gaba ɗaya, kamar yadda ya zo a cikin hadisin Mu’az ɗan Jabal, Allah ya yarda da shi, wand Imamu Ahmada ya ruwaito ta hanya ingantacciya da lafazin kamar haka: “Ba na sanar da kai mamallakin dukkan alheri ba! Ka kame wannan"- Sai ya yi nuna harshensa-. Mu’az ya ce, "Ya Annabin Allah yanzu mu ababan kamawa ne da abin da muke yin magana da shi?" Annabi ya ce: A aha! Ya Mu’az ba ka sani babu abin da ke sa a kifa fuskoki mutane ko hancinsu a wuta ba, sai abubuwan da harasansu suka girba musu".

Manzo ya kasance yana sa ido a kan iyalan gidansa a game da haka, yana tsaftace su da kare su daga afkawa maganganun da Allah ba ya so. An karɓo daga A’isha Allah ya yarda da ita ta ce: "Na ce da Annabi ko ba komai Hafsa ‘yar duƙurƙusa ce". Sai manzon Allah ya ce: “Haƙiƙa kin faɗi kalmar da inda za a cakuɗa ta da ruwan kogi da ta jirkita shi”. Kuma na labarta masa labarin wani mutum sai ya ce “Ni ba zan yi gulmar wani ba, ko mai za a ba ni”. Tirmizi ne ya rawaito shi, kuma ya ce hadisi ne mai kyau ingantacce.

Kuma Imamul Bukhari ya rawaito hadisi a cikin littafinsa na Al Adabul Mufrad ta ingantacciyar hanya, daga Anas Allah ya yarda da shi ya ce, Wani mutum ya yi jawabi a wajen Umar, sai ya yawaita magana, sai Umar ya ce: “Haƙiƙa yawan magana na daga ratatar shaiɗan". (wato surutunsa).

Ya ɗan uwa, yi ƙoƙari ka shagaltar da harshenka da ambaton Allah, da umarni da kyakkyawan aiki, da hani ga mummuna, da kuma daddaɗan zance mai albarka wanda zai sama maka lada mai girma.

Barin sa baki a cikin abin da ba zai amfane ka ba alama ce da ke nuna cikar musuluncinka. Kamar yadda yake cikin hadisin Abi huraira da yake cewa, “Yana daga kyauwn Musuluncin mutum ya bar abin da ba ruwansa”. Tirmzi ne ya rawaito shi.

Kutsawa cikin taɓa mutuncin musulmai sifa ce daga sifofin munafukai, don haka ka nisanci shi iya iyawarka saboda hadisin Wasila Ɗan Asƙa’i, daga Annabi (ﷺ) ya ce: “Haramun ne ga musulmi a kan musulmi zubar da jininsa, da cin mutuncinsa, da cin dukiyarsa. Musulmi ɗan uwan musulmi ne, don haka ba ya zaluntarsa, ba ya taɓar da shi. Tsoron Allah a nan yake". Sai ya nuna zuciya, da hannunsa. Ahmad ne ya rawaito shi.

Miyagun maganganu na daga cikin abubuwan da suka yaɗu a cikin al’ummar musulmi a wannan zamani. Ina ganin babban abin da ya jawo hakan shi ne yaƙar mu da Yahudawa suke yi ta kafofin yaɗa labarai wanda a kodayaushe suke kai hari ga musulmai ta inda ba sa zato. An karɓo daga Abud Darda’ daga Annabi (ﷺ), ya ce : “Babu abin da ya fi nauyi a ma’aunin ladan mumini a ranar alƙiyama irin kyawawan ɗabi’u. Kuma haƙiƙa Allah na fushi da mai yin miyagun maganganu mai kaifin harshe". Tirmizi ne ya rawaito shi, kuma ya ce, hadisi ne kyakkyawa ingantacce.

Yin raki kuwa a lokacin afkuwar musibu maguzanci ne, wanda musulmi aka hana mu yinsa, don haka ne ma aka umarce mu da yin haƙuri tun a karon farko a yayin arangama da musiba. Kuma aka sanya lada gwaggwaɓa a kan hakan. An karɓo daga Sabit ya ce: “Na ji Anas yana cewa da wata daga cikin iyalinsa, ko kin san wance? Haƙiƙa manzon Allah (ﷺ) ya wuce ta tana kuka a kan wani ƙabari, sai ya ce da ita, “Ki ji tsoron Allah ki yi haƙuri”, sai ta ce da shi, "Tafi ka ban wuri! kai ba ka ma damu da musibar da ta dame ni ba". Anas ya ce ba ta san Manzon Allah ne ba, sai aka ce da ita, ai manzon Allah (ﷺ) ne, sai tai ajiyar zuciya. Sai ta je ƙofar gidansa ta tarar babu mai gadi, sai ta ce, "Ya Manzon Allah ai ban san kai ba ne".Sai ya ce: “Ai haƙuri yana amfani ne a lokacin karon battar farko da masifa”. Ahmad da Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

Ya bayin Allah! Haƙiƙa ƙarya da yaɗa ta a tsakanin al’umma haramun ne, kuma laifi ne babba daga cikin manya-manyan laifuka. An karɓo daga abdullahi ɗan Mas’ud daga Annabin (ﷺ) ya ce: “Na hana ku yin ƙarya, haƙiƙa ƙarya na kai bawa ga ayyukan kangara, kangara kuma na kai bawa ga wuta, haƙiƙa mutum yakan dinga yin ƙarya, kuma yana kirdadon ƙarya, har a kai ga rubuta shi maƙaryaci a gurin Allah”. Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.

Kuma dai an karɓo daga Ɗan Mas'ud ya ce: "Karya ba ta halatta ba da gaske ko da gangan, kuma bai halatta ɗayanku ya yi wa ɗansa alƙawari ba, sannan ya ƙi cika masa".

Kuma Allah Maɗaukaki ya umartar bayinsa muminai da tantance gaskiyar labari idan sun ji shi, ya ce::

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِن جَآءَكُمۡ فَاسِقُۢ بِنَبَإٖ فَتَبَيَّنُوٓاْ أَن تُصِيبُواْ قَوۡمَۢا بِجَهَٰلَةٖ فَتُصۡبِحُواْ عَلَىٰ مَا فَعَلۡتُمۡ نَٰدِمِينَ ٦ ﴾ [الحجرات: ٦].

"Ya ku waɗanda suka imani, idan fasiƙi ya zo muku da labari to ku tabbatar da (gaskiyarsa) don kada ku farma wasu jama'a bisa rashin sani sannan ku wayi gari kuna masu nadama bisa abin da kuka aikata".

Babban malami, sheikh Assa'idi ya ce a tafsirin wannan aya: "Wannan na daga cikin ladubban da suka zama lallai masu hankali su ladabtu da su, da yin aiki da su, wato idan wani fasiƙi ya ba su labari su tabbatar da gaskiyar labarin, kada su kama shi daga jinsa haƙiƙa, kama labari daga jinsa haɗari ne mai girman gaske, kuma faɗawa ne cikin saɓo. Haƙiƙa idan aka ɗauki labarin fasiƙi irin ɗaukar da ake yi wa labarin mai gaskiya da adalci za a kai ga yin hukunci da abin da labarin ya ƙunsa, ta dalilin haka sai a yi asarar rayuka da ta dukiya ba tare da dacewar hakan ba, a saboda wancan labari da ke jawo da-na-sani. Abin da yake wajibi yayin jin labarin fasiƙi, shi ne tantance gaskiyarsa, idan dalilai da alamomi sun yi nuni gaskiyarsa sai a yi aiki da shi kuma gaskiya ya faɗa. Idan kuwa dalidai suka yi nuni ƙaryarsa to ba a yin aiki da shi, kuma ƙarya ya faɗa. Kuma hakan na ɗauke da cewa, labarin mai gaskiya abin karɓa ne, na maƙaryaci kuwa abin watsi da shi ne, na fasiƙi kuma abin a tsaya a yi bincike game da shi ne, kamar yadda muka ambata. Kuma don haka ne magabata suke karɓar ruwayoyi da dama daga wajen Khawarijawa da aka san su da gaskiya ko da kuwa fasiƙai ne».

Allah ya yi mana gamon katar, ya ba mu dacewa cikin maganganunmu da ayyukanmu. Amin.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah, Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata a mafi ɗaukakar annabawa, kuma cikamakin annabawa da iyalansa da sahabbansa da wanda ya bi turbarsa har zuwa ranar sakamako.

Bayan haka: Ya bayin Allah! Dalilai sun yin nuni a kan cewa Allah yana da mala'iku masu tsaron mutane, kamar yadda yake a cikin faɗin Allah maɗaukaki:

﴿ وَيُرۡسِلُ عَلَيۡكُمۡ حَفَظَةً ﴾ [الأنعام: ٦١].

(Kuma yana aiko muku da masu tsaro (daga mala'iku))

Kuma Allah ya ambata a cikin abubuwan da suke tsarewa ɗan adam sun haɗa da dukkanin ayyukan mutum na alheri da na sharri da kuma maganganunsa, Allah ya ce:

﴿ وَإِنَّ عَلَيۡكُمۡ لَحَٰفِظِينَ ١٠ ﴾ [الانفطار: ١٠]

Ma’ana: (Babu shakka akwai masu tsaronku).

Kuma ya ce:

﴿ إِذۡ يَتَلَقَّى ٱلۡمُتَلَقِّيَانِ عَنِ ٱلۡيَمِينِ وَعَنِ ٱلشِّمَالِ قَعِيدٞ ١٧ مَّا يَلۡفِظُ مِن قَوۡلٍ إِلَّا لَدَيۡهِ رَقِيبٌ عَتِيدٞ ١٨ ﴾ [ق: ١٧ – ١٨].

“Yayin da masu hadƙuwa biyu suke hadƙuwa ta hagu da kuma ta dama a zaune, ba wata magana da zai furta face tare da shi akwai mai tsaro halartacce”.

Kuma dai Allah ya ce:

﴿ أَمۡ يَحۡسَبُونَ أَنَّا لَا نَسۡمَعُ سِرَّهُمۡ وَنَجۡوَىٰهُمۚ بَلَىٰ وَرُسُلُنَا لَدَيۡهِمۡ يَكۡتُبُونَ ٨٠ ﴾ [الزخرف: ٨٠].

(Ko suna tsammanin cewa mu ba ma jin asirinsu da ganawarsu ne? Ba haka ba ne, manzanninmu ma sun tare da su suna rubutawa).

A cikin Sahihul Bukhari da Muslim an karƃo daga Abu Huraira ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Akwai mala’ikun da suke maye wasunsu a cikinku da daddare, da kuma mala’ikun da suke maye wasunsu a cikinku da rana, suna tattaruwa a lokacin sallar asuba da lokacin sallar la’asar, sannan sai waƌanda suka kwana a cikinku su hau sama, sai Ubangijinsu ya tambaye su, duk da ya fi su masaniya game da ku, ya ce: "Yaya kuka baro bayina?" Sai su ce,"Mun baro su suna yin salla, kuma da muka je ma mun tarar da su suna yin salla”.

Mai littafin Kasshaf, ya ce: “In da za ka ce: Ai Allah wadatacce ne da iliminsa game da rubutun mala’iku, wane amfani rubutn nasu yake da shi? Sai ince, amfanisa yin luƌufi ga bayi, domin kuwa idan suka san Allah na sa ido da bibiya a kansu, kuma mala’ikunsa da su ne mafi ƌaukakar halitttarsa za a wakilta su a kan rubuce ayyukansu da kiyaye su don bijiro da su gaban shaidu a yinin ƙiyama zai fi sa su tsawatuwa da nisantar miyagun ayyuka".

Ya bayin Allah! Bibiyar daidai a dukkanin maganganu shi ne kaƌai mafita daga matsalokin da muka ambata, kuma da haka ne ayyuka za su kyutatu, kuma bawa ya dace da gafarar zunubansa, ya kuma dace da rabauta da samun yardar Allah. Allah yana cewa:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَقُولُواْ قَوۡلٗا سَدِيدٗا ٧٠ يُصۡلِحۡ لَكُمۡ أَعۡمَٰلَكُمۡ وَيَغۡفِرۡ لَكُمۡ ذُنُوبَكُمۡۗ وَمَن يُطِعِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ فَقَدۡ فَازَ فَوۡزًا عَظِيمًا ٧١ ﴾ [الأحزاب: ٧٠ – ٧١].

(Ya ku waƌanda suka yi imani, ku ji tsoron Allah, kuma ku faƌi maganar da take daidai ce, zai kyautata muku ayyukanku, ya kuma gafarta muku zunubanku, duk kuwa wanda ya bi Allah da manzonsa, to haƙiƙa ya rabauta tabauta mai girma).

Kuma kamar yadda magana kan zamo mabuƌin alheri, to haka kuma takan zamo mabuƌin sarri. Kamar yadda Manzon Allah ya faƌa a cikin hadisin Mu’azu wanda ya gabata, “Shin akwai abin da yake kifa mutane a cikin wutar jahannama a kan fuskokinsu, in ba abubuwan da harasansu suka girba ba).

Ya zo cikin hadisi: “Wanda ya yi imani da Allah ranar lahira to ya faƌi alheri ko ya yi shiru”.

Don haka, karantar da mutane Alƙur’ani madaidaiciyar magana ce, haka rawaito hadisan Manzon Allah, da karantar da shi, madaidaiciyar magana ce, haka kuma yaƌa maganganun sahabbai, da na shugabannin malaman Fiƙihu da hikimomin malamai, madaidaciyar magana ce, kamar yadda girmama Allah da tsarkake shi

da yi masa kirari, wannan ma madaidaiciyar magana ce. Haka ma dai, kiran salla da iƙama, Allah maɗaukaki yana cewa:

﴿إِلَيۡهِ يَصۡعَدُ ٱلۡكَلِمُ ٱلطَّيِّبُ وَٱلۡعَمَلُ ٱلصَّٰلِحُ يَرۡفَعُهُۥۚ﴾ [فاطر: ١٠].

(Zuwa gare shi daɗaɗan maganganu suke hawa).

Kuma da yaɗa madaidaiciyar magana ne darajoji da tabbatattun al'amura ke yaɗuwa a tsakanin mutane, sai ya zama su ma suna kwaɗayin ɗabi'antuwa da su. Ta hanyar yaɗuwar mummunar magana ne ɓata da gurɓatattun abubuwa suke yaɗuwa. Daga nan sai ka mutane su canja, sun riƙa aikin ɓarna, suna kuma zaton su masu kyutata aiki ne.

Ya bayin Allah mu riƙa tuna faɗar Allah:

﴿لَا يَعۡزُبُ عَنۡهُ مِثۡقَالُ ذَرَّةٖ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَلَا فِي ٱلۡأَرۡضِ وَلَآ أَصۡغَرُ مِن ذَٰلِكَ وَلَآ أَكۡبَرُ إِلَّا فِي كِتَٰبٖ مُّبِينٖ ٣﴾ [سبأ: ٣].

Ma'ana: (Babu wani abu koda kamar ƙwayar komayya yake ko mafi ƙanƙanta ko mafi girma a sama yake ko a ƙasa da zai ɓuya ga Allah, face yana cikin littafin mai bayyanawa).

RAYUWAR LAHIRA ITA CE RAYUWA TA HAKIKA

Manufofin huɗubar

- Dasa imani da ranar lahira a zukata.
- Kwaɗaitarwa a kan yin guzuri domin lahira.
- Jan-kunne game da raja'a a kan duniya.
- Bayanin banbancin tsakanin gidan duniya da na lahira.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammadu bawansa ne manzonsa ne. (Yaku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron Allah yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Yaku waɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammadu (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (a addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta".

Bayan haka:

Ya ku mutane, wane ne daga cikimu ba ya fatan ya rayu rayuwa mai kyau a duniya da lahira? Wanene zai yarda ya raya duniya mai ƙariya, ya rusha lahira wacce ita ce rayuwa ta haƙiƙa? Ko kuma wanene bay a son ya zama ɗan aljannah?!

Ya ku 'yan uwa! Lallai kowane mai rai ya san ƙarshensa mutuwa ne, kamar yadda Allah yake cewa,

﴿ كُلُّ مَنۡ عَلَيۡهَا فَانٖ ٢٦ وَيَبۡقَىٰ وَجۡهُ رَبِّكَ ذُو ٱلۡجَلَٰلِ وَٱلۡإِكۡرَامِ ٢٧ ﴾ [الرحمن: ٢٦ – ٢٧].

(Duk wanda yake kan doron ƙasa mai ƙarewa ne. Fuskar Ubangijinka ce za ta wanzu, Ma'abocin girma da ɗaukaka).

Don haka, ɗan Adam yana da gidaje biyu: Gidan duniya, wanda ba na tabbata ba ne, da gidan lahira, wanda shi ne dahir. Duniya, komai tsawon da ta yi, mai

ƙarewa ce, ita da duk abin da yake cikinta, don haka, mai hankali shi ne wanda yake kallon duniya a matsayin tasha-tasha, da zai yi guzuri don lahira. Allah yana cewa,

﴿ ٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّمَا ٱلۡحَيَوٰةُ ٱلدُّنۡيَا لَعِبٞ وَلَهۡوٞ وَزِينَةٞ وَتَفَاخُرُۢ بَيۡنَكُمۡ وَتَكَاثُرٞ فِي ٱلۡأَمۡوَٰلِ وَٱلۡأَوۡلَٰدِۖ كَمَثَلِ غَيۡثٍ أَعۡجَبَ ٱلۡكُفَّارَ نَبَاتُهُۥ ثُمَّ يَهِيجُ فَتَرَىٰهُ مُصۡفَرّٗا ثُمَّ يَكُونُ حُطَٰمٗاۖ وَفِي ٱلۡأٓخِرَةِ عَذَابٞ شَدِيدٞ وَمَغۡفِرَةٞ مِّنَ ٱللَّهِ وَرِضۡوَٰنٞۚ وَمَا ٱلۡحَيَوٰةُ ٱلدُّنۡيَآ إِلَّا مَتَٰعُ ٱلۡغُرُورِ ٢٠ ﴾ [الحديد: ٢٠].

(Ku sani cewa, rayuwar duniya wasa ce da wargi da ƙawa da alfahari a tsakanin ku, da tinƙaho a cikin dukiya da ‘ya’ya, kamar misalin girgijen da tsiransa suka ba wa manoma mamaki, sannan sai ya girgiza ka gan shi yalo, sai ya zamo karmami. A lahira akwai azaba mai tsanani, da kuma gafara daga Allah, da yarda. Rayuwar duniya ba komai ba ce, face kayan ruɗi).

Kuma Allah yana cewa,

﴿ إِنَّمَا مَثَلُ ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا كَمَآءٍ أَنزَلۡنَٰهُ مِنَ ٱلسَّمَآءِ فَٱخۡتَلَطَ بِهِۦ نَبَاتُ ٱلۡأَرۡضِ مِمَّا يَأۡكُلُ ٱلنَّاسُ وَٱلۡأَنۡعَٰمُ حَتَّىٰٓ إِذَآ أَخَذَتِ ٱلۡأَرۡضُ زُخۡرُفَهَا وَٱزَّيَّنَتۡ وَظَنَّ أَهۡلُهَآ أَنَّهُمۡ قَٰدِرُونَ عَلَيۡهَآ أَتَىٰهَآ أَمۡرُنَا لَيۡلًا أَوۡ نَهَارٗا فَجَعَلۡنَٰهَا حَصِيدٗا كَأَن لَّمۡ تَغۡنَ بِٱلۡأَمۡسِۚ كَذَٰلِكَ نُفَصِّلُ ٱلۡأٓيَٰتِ لِقَوۡمٖ يَتَفَكَّرُونَ ٢٤ ﴾ [يونس: ٢٤].

(Kaɗai dai, misalin rayuwar duniya, kamar ruwa ne da ya sauko daga sama, sai tsirran ƙasa suka cakuɗe da shi cikin abin da mutane suke ci, da dabbobi, har sai ƙasa ta riƙe adonta, ta ƙawatu, ma’abotanta sun yi tsammanin suna da iko a kanta, sai al’amarinmu ya zo mata da daddare, ko da rana, sai ya mayar da ita girbabbiya, kamar ba ita jiya. Kamar haka ne muke bayyana ayoyi ga mutanen da suke tunani).

Kuma Allah ya ce,

﴿ وَمَا هَٰذِهِ ٱلۡحَيَوٰةُ ٱلدُّنۡيَآ إِلَّا لَهۡوٞ وَلَعِبٞۚ وَإِنَّ ٱلدَّارَ ٱلۡأٓخِرَةَ لَهِيَ ٱلۡحَيَوَانُۚ لَوۡ كَانُواْ يَعۡلَمُونَ ٦٤ ﴾ [العنكبوت: ٦٤].

(Rayuwar wannan duniya, ba komai ba ce, face wasa da wargi. Lallai gidan lahira shi ne rayuwa, da mutane suna da ilimi).

Aliyu bin Abi Ɗalib ya ce, “Duniya ta tafi, tana mai ba da baya, lahira ta taho tana mai gabatowa: Kowace ɗaya daga cikinsu, tana da ‘ya’ya. Ku zamo ‘ya’yan lahira, kada ku zamo ‘ya’yan duniya, domin yau aiki ne ba hisabi, gobe kuma hisabi ne ba aiki.” [Bukhari ya kawo shi]

Zaid ibn Thabit (RA) ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Wanda duniya ita ce damuwarsa, Allah zai ɗaidaita al’amarinsa, ya kuma sanya talaucinsa a gaban idanunsa, kuma ba zai sami komai ba na duniya, sai abin da aka rubuta masa. Wanda kuwa ya zamo lahira ne damuwarsa, Allah zai tattara al’amarinsa gare shi, kuma ya sanya wadatarsa a cikin zuciyarsa, kuma duniya ta zo masa tilas ɗinta.” [Ibni Majah ya rawaito shi]

Ya ku musulmai! Ku yi rige-rige cikin ayyukan alheri, don ku sami duniya da lahira, kada ku fifita duniya a kan lahira, sai ku yi asarar su duka biyun. Saboda ita duniya gona ce, lahira kuma can ake girbi. Duk wanda bai yi shuka a cikinta ba, babu abin da zai girba a lahira. Ibn Rajab yana cewa, lokacin da yake sharhin Abdullahi ɗan Umar, ka kasance kamar baƙo a duniya. Wannan hadisin ginshiƙe ne wajen taƙaita buri a duniya, saboda mumini bai kamata ba a gare shi, ya ɗauki duniya a matsayin matabbaci, zuciyarsa ta nutsu da ita. Abin da ya kamata, ya ɗauki duniya a matsayin tasha, wadda za ta kai shi zuwa lahira.

Ya ku ‘yan uwa! Lallai rayuwar duniya lahira ita ce haƙiƙanin rayuwa, wanda idan mutum ya gan ta, zai riƙa cewa, ina ma na yi aikin alheri a duniya, saboda rayuwa ce da babu mutuwa a cikinta, kuma duk wani abu da rai yake kwaɗayi, ko idanu, akwaita a cikinta, rayuwa ce ta aminci, wadda ta kuɓuta daga dukkan tawaya, ta kuɓuta daga dukkan bala’i, babu cuta a cikinta, babu matsi a cikinta, babu tsufa a cikinta. Manzon Allah (ﷺ) yana cewa, “Wurin sandar ɗayanku a lahira, ya fi duniya da abin da yake cikinta.” Kuma Allah yana faɗa, yayin da yake siffanta ni’imar ‘ya’yan aljanna, ya ce, “Amma idan ya zamo cikin abubuwan kusantarwa, to ƙanshi da aljannar ni’ima za a ba shi.”

Kuma Allah yana cewa,

﴿ وَجَزَىٰهُم بِمَا صَبَرُوا۟ جَنَّةً وَحَرِيرًا ﴿١٢﴾ مُّتَّكِـِٔينَ فِيهَا عَلَى ٱلْأَرَآئِكِ ۖ لَا يَرَوْنَ فِيهَا شَمْسًا وَلَا زَمْهَرِيرًا ﴿١٣﴾ وَدَانِيَةً عَلَيْهِمْ ظِلَٰلُهَا وَذُلِّلَتْ قُطُوفُهَا تَذْلِيلًا ﴿١٤﴾ وَيُطَافُ عَلَيْهِم بِـَٔانِيَةٍ مِّن فِضَّةٍ وَأَكْوَابٍ كَانَتْ قَوَارِيرَا۠ ﴿١٥﴾ قَوَارِيرَا۠ مِن فِضَّةٍ قَدَّرُوهَا تَقْدِيرًا ﴿١٦﴾ وَيُسْقَوْنَ فِيهَا كَأْسًا كَانَ مِزَاجُهَا زَنجَبِيلًا ﴿١٧﴾ عَيْنًا فِيهَا تُسَمَّىٰ سَلْسَبِيلًا ﴿١٨﴾ وَيَطُوفُ عَلَيْهِمْ وِلْدَٰنٌ مُّخَلَّدُونَ إِذَا رَأَيْتَهُمْ حَسِبْتَهُمْ لُؤْلُؤًا مَّنثُورًا ﴿١٩﴾ وَإِذَا رَأَيْتَ ثَمَّ رَأَيْتَ نَعِيمًا وَمُلْكًا كَبِيرًا ﴿٢٠﴾ عَٰلِيَهُمْ ثِيَابُ سُندُسٍ خُضْرٌ وَإِسْتَبْرَقٌ ۖ وَحُلُّوٓا۟ أَسَاوِرَ مِن فِضَّةٍ وَسَقَىٰهُمْ رَبُّهُمْ شَرَابًا طَهُورًا ﴿٢١﴾ ﴾ [الإنسان: ١٢ – ٢١].

(Kuma muka saka musu da aljanna, da hariri, saboda haƙuri da suka yi. Suna kishingiɗe a cikin gadaje, ba sa ganin rana a cikinta, ballantana tsananin sanyi. Inuwowinta suna kusa, kuma an kusanto da ‘ya’yan itatuwanta zuwa ƙasa, ana kewayawa gare su da ƙorai na azurfa, da kofuna, wanda aka daidaita su daidaitawa. Ana shayar da su a cikinta, giya wadda aka haɗa ta da zanjabil, daga wani ido a cikinta, wanda ake ce masa salsabil. Yara madawwama suna kewaya su, idan ka gan su, ka ce lu’u-lu’u ne, saboda tsananin kyau. Idan ka ga waccan aljanna, za ka ga ni’ima da mulki mai girma, tufafin alhariri kore, ya lulluɓe su da istabraƙ, kuma an sanya musu kambu na azurfa, sannan Ubangijinsu yana shayar da su abin sha tsarkakakke).

An karɓo daga Abu Huraira (RA) ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Farkon zugar da za su shiga aljanna, surarsu kamar wata ranar sha huɗu. Ba sa kaki a cikinta, ba sa kaki a cikinta, ba sa bayan-gida, ƙoransu a cikinta na zinare ne, talgeshansu kuwa na zinare da azurfa ne, kowanne daga cikinsu yana da mata biyu, ana ganin ɓargonsu ta bayan nama, saboda tsananin kyau, babu saɓani a tsakaninsu, babu ƙiyayya, zuciyarsu kamar zuciyar mutum ɗaya take, suna tsarkake Allah, safiya da maraice.” Bukhari da Muslim ne suka ruwaito.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah tsira da aminci su tabbata ga Annabin rahmar, Annabinmu Muhammadu da alayensa da sahabbansa da mabiya tafarkinsa har zuwa tashin ƙiyama.

Ya ku mutane! Tunda rayuwar lahira ita ce rayuwa ta gaskiya, don haka magabata suka mayar da duniya a matsayin gona ga lahira. Umar ibn Abdul-Aziz ya faɗa a cikin huɗubarsa, ya ce, “Lallai duniya ba mazaunanta ba ce. Allah ya rubuta mata ƙarewa, ya rubuta wa mazaunanta zakuɗawa daga cikinta, don haka ku yi guzuri, mafificin guzuri, shi ne tsoron Allah.”

Yahaya ɗan Mu’azu kuwa, cewa ya yi, “Ita duniya, giyar Shaiɗan ce. Duk wanda ya bugu da ita, ba zai farka ba, sai lokacin mutuwa, alhali yana mai nadama, tare da wanda suka yi asara.”

Muhammad ibn Wasi’i, ya kasance idan zai yi barci, sai ya ce da iyalinsa, “Ina muku ban-kwana da Allah, domin ta yiyu mutuwa ta ce ta zo.”

Bakr Almuzani cewa ya yi, “Idan ɗayanku ya sami damar kada ya kwanta, face wasiyyarsa tana rubuce a kusa, to ya aikata haka, domin bai sani ba, a ina zai kwana, a duniya ko lahira?”

Uwaisu kuwa, ya kasance, idan aka ce, yaya yanayi? Sai ya ce, “Ni ban damu da yanayin ba!” saboda bai sani ba, idan ya wayi gari, ko zai kai yamma, idan kuma ya kai yamma, ko zai sake wayar gari.

Ya ku ‘yan uwa! Lallai wannan duniya mai ƙarewa, bai kamata ta ruɗe mu ba. Ya kamata mu yi guzurin ayyukan ƙwarai, kamar sallah da azumi da sadaka da biyayya ga iyaye da ciyarwa don Allah, don rabauta a lahira. Ubangiji yana cewa, ﴿ مَنۡ عَمِلَ صَٰلِحٗا مِّن ذَكَرٍ أَوۡ أُنثَىٰ وَهُوَ مُؤۡمِنٞ فَلَنُحۡيِيَنَّهُۥ حَيَوٰةٗ طَيِّبَةٗۖ وَلَنَجۡزِيَنَّهُمۡ أَجۡرَهُم بِأَحۡسَنِ مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٩٧ ﴾ [النحل: ٩٧].

(Wanda duk ya yi aikin ƙwarai, mace ko namiji, alhali yana mumini, to za mu rayar da shi rayuwa mai daɗi, kuma za mu ba su ladansu, da abin da ya fi kyau daga abin da suka kasance suna aikatawa).

YADDA TSARIN KIRAN ANNABAWA YAKE

Manufofin huɗubar

- Tunatar da mutane ƙoƙarin da Annabawa suka yi wajen isar da saƙon Allah.
- Zaburar da masu wa'azi wajen koyi da Annabawa cikin tsarin kira zuwa ga addinin Allah.
- Bada himma wajen sabuntar da hanyoyin da'awa daidai da halin da ake ciki.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga shirrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammad bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammad (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Yaku 'yan uwana masu sauraro, huɗubarmu a yau tana magana ne akan tsarin da Annabawa suka bi, wajen kira zuwa ga addinin Allah Subhanahu Wa ta'ala.

Haƙiƙa tsarin da Annabawa suka bi wajen kiran mutane zuwa addinin Allah, tsari ne da ya wajaba akan dukkan musulmi da musulma su lazimce shi, su bi shi wajen kiran mutane zuwa ga addinin Allah, saboda shi ne mafi alherin tsari da ɗan adam ya sani a tarihi.

Haƙiƙanin kiran Annabawa shi ne kiran mutane zuwa ga tsarkake ibada ga Allah, da barin shirka da shi a cikin magana ne ko aiki, Allah ya ce :

﴿ وَلَقَدۡ بَعَثۡنَا فِي كُلِّ أُمَّةٖ رَّسُولًا أَنِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ وَٱجۡتَنِبُواْ ٱلطَّٰغُوتَ ﴾ [النحل: ٣٦].

Ma'ana : "Haƙiƙa mun aiko wa kowace al'umma Manzo, a kan su bautawa Allah su nisanci Ɗagutu". (Annahal : 36).

Sannan Allah Mai girma da buwaya ya bayyana tsarin da Annabawa suka bi wajen kiran mutane zuwa ga addini daki – daki a cikin Alƙur'ani. Ya bayyana yadda suka bijirar da musulunci ga ɗaiɗaikun mutane da al'ummu da masu mulki, da ƙarfafa da masu rauni, da mawadata da talakawa, da sauransu.

Ya ambaci labaran Annabawa da mutanensu, ya faɗi irin yadda Allah ya ba su nasara, su da mabiyansu, da kuma yadda ya ruguza waɗanda suka ja da su, suka yi musu girman kai, ɗaiɗaikun mutane ne ko jama'a, irinsu Fir'auna, da lamarudu, da irinsu Karuna, Kai! Har ma da jama'u da ƙabilu, irinsu Adawa da Samudawa da sauransu.

Alƙur'ani littafi ne da ya ƙunshi komai da komai, litatfi ne na tauhidi da imani, haka kuma littafi ne na ilimi da hikima da shari'a , littafi ne na addu'a da ibada, littafi ne na Umarni da kira, kamar yadda yake littafi ne na ambato.

Idan muka ɗauki Annabi Nuhu zamu ga salon da ya bi wajen yi wa mutanensa wa'azi, salo na hikima da haƙuri, da jan – hankali, Allah ya ce,

﴿لَقَدۡ أَرۡسَلۡنَا نُوحًا إِلَىٰ قَوۡمِهِۦ فَقَالَ يَٰقَوۡمِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ مَا لَكُم مِّنۡ إِلَٰهٍ غَيۡرُهُۥٓۖ إِنِّيٓ أَخَافُ عَلَيۡكُمۡ عَذَابَ يَوۡمٍ عَظِيمٖ ٥٩ قَالَ ٱلۡمَلَأٞ مِن قَوۡمِهِۦٓ إِنَّا لَنَرَىٰكَ فِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٖ ٦٠ قَالَ يَٰقَوۡمِ لَيۡسَ بِي ضَلَٰلَةٞ وَلَٰكِنِّي رَسُولٞ مِّن رَّبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٦١ أُبَلِّغُكُمۡ رِسَٰلَٰتِ رَبِّي وَأَنصَحُ لَكُمۡ وَأَعۡلَمُ مِنَ ٱللَّهِ مَا لَا تَعۡلَمُونَ ٦٢ أَوَعَجِبۡتُمۡ أَن جَآءَكُمۡ ذِكۡرٞ مِّن رَّبِّكُمۡ عَلَىٰ رَجُلٖ مِّنكُمۡ لِيُنذِرَكُمۡ وَلِتَتَّقُواْ وَلَعَلَّكُمۡ تُرۡحَمُونَ ٦٣ فَكَذَّبُوهُ فَأَنجَيۡنَٰهُ وَٱلَّذِينَ مَعَهُۥ فِي ٱلۡفُلۡكِ وَأَغۡرَقۡنَا ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَآۖ إِنَّهُمۡ كَانُواْ قَوۡمًا عَمِينَ ٦٤﴾ [الأعراف: ٥٩ - ٦٤].

Ma'ana : "Haƙiƙa mun aika Nuhu zuwa ga mutanensa, ya ce musu yaku mutane na ku bauta wa Allah, ba ku da wani abin bauta wa wanda ba shi ba, haƙiƙa ina ji muku tsoron azabar wani yini mai girma. Sai manyan gari daga cikin mutanensa suka ce, haƙiƙa mu muna ganin kana cikin ɓata mabayyani, sai ya ce musu, ya mutanena babu wani ɓata a tare da ni, Kaɗai ni dai Manzone daga Ubangijin Talikai. Ina isar muku da saƙonnin ubanjina ne, kuma ina muku nasiha, sannan na san wani abu dangane da Allah wanda ba ku sani ba. Yanzu kuna mamaki don tunatarwa ta zo muku daga wani mutum daga cikinku, don ya tunatar da ku, ko kwa ji tsoron Allah, kuma wala - alla a yi muku rahama. Sai suka ƙaryata shi, sai muka tseratar da shi da waɗanda suka imani da shi a cikin jirgin ruwa, muka nutsar da waɗanda suka ƙaryata da ayoyinmu, haƙiƙa sun kasance mutane ne makafi" (Al-a'araf : 59 – 63).

A waɗannan ayoyi zamu ga yadda Annabi Nuhu yake yi wa mutanensa wa'azi, ta hanyar tausasawa da hikima – duk da irin munanan maganganun da suke faɗa masa – . Ya fara musu wa'azi da kira zuwa ga tsarkake bauta ga Allah, sannan ya ɗora da tsoratar da su azabar Ubangiji idan suka kafirce suƙi yin imani. To haka tsarin kiran dukkan Annabawa yake, wa'azi da tausasawa, da hikima, da haƙuri.

Fara wa'azi da tauhidi da barin shirka shi ne tsarin da dukkan Annabawa suka bi wajen da'awarsu, Allah Maɗaukakin Sarki a cikin Alƙur'ni ya hakaito mana cewa kowane Annabi abin da yake fara faɗa wa mutanensa shi ne : "Ku bautawa Allah, ba ku da wani abin bautawa da gaskiya wanda ba shi ba".

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon

Allah (S.A.W) ya ce wa Mu'azu ɗan Jabal - Allah ya yarda da shi – yayin da ya aika shi zuwa Yemen, "Haƙiƙa zaka isa wajen wasu mutane ma'abota littafi, idan ka isa wajensu ya zama abin da zaka fara kiransu gare shi, shi ne su shaida babu abin bautawa da cancanta sai Allah, kuma Muhammad Manzon Allah ne, idan sun yi maka ɗa'a akan haka, sai ka sanar da su cewa Allah ya wajabta musu salloli biyar a kowane dare da yini, idan sun yi maka ɗa'a to ka faɗa musu cewa Allah ya wajabta musu zakka, za a karɓa daga masu wadatarsu a mayar da ita ga talakawansu, idan sun yi maka ɗa'a akan haka, to ka kiyaye manya – manyan dukiyoyinsu, ka kuma ji tsoron addu'ar wanda aka zalunta, domin babu shamaki tsakaninta da Allah" Bukhari ne ya rawaito.

Yaku 'yan uwana musulmi : Tausasawa a wajen wa'azi da faɗin zance mai daɗi ga wanda ake wa wa'azi wani abu ne da Allah ya yi umarni da shi, ya cewa Annabi Musa da Haruna yayin da za su je wajen Fir'auna :

﴿ فَقُولَا لَهُۥ قَوۡلٗا لَّيِّنٗا لَّعَلَّهُۥ يَتَذَكَّرُ أَوۡ يَخۡشَىٰ ٤٤ ﴾ [طه: ٤٤]

Ma'ana : "Ku faɗa masa magana mai taushi, wataƙila ya wa'azantu ko ya ji tsoron Allah". (Ɗaha :44). Haka ma amfani da hikima wajen wa'azi wani tsari ne da Allah ya girmama Annabawa da shi, mu lura da Annabi Yusuf (AS) (yadda ya yi amfani da hikima wajen kiran abokansa na kurkuku) ya ce musu :

﴿ يَٰصَٰحِبَيِ ٱلسِّجۡنِ ءَأَرۡبَابٞ مُّتَفَرِّقُونَ خَيۡرٌ أَمِ ٱللَّهُ ٱلۡوَٰحِدُ ٱلۡقَهَّارُ ٣٩ مَا تَعۡبُدُونَ مِن دُونِهِۦٓ إِلَّآ أَسۡمَآءٗ سَمَّيۡتُمُوهَآ أَنتُمۡ وَءَابَآؤُكُم مَّآ أَنزَلَ ٱللَّهُ بِهَا مِن سُلۡطَٰنٍۚ إِنِ ٱلۡحُكۡمُ إِلَّا لِلَّهِۚ أَمَرَ أَلَّا تَعۡبُدُوٓاْ إِلَّآ إِيَّاهُۚ ذَٰلِكَ ٱلدِّينُ ٱلۡقَيِّمُ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعۡلَمُونَ ٤٠ ﴾ [يوسف: ٣٩ - ٤٠].

Ma'ana : "Ya ku abokaina na kurkuku, yanzu abin bautawa daban – daban su ne suka fi alheri ko kuwa Allah wanda yake shi ɗaya mai rinjaye. Ba komai kuke bauta wa ba, wanda ba Allah ba sai sunayen da kuka ƙirƙire su, ku da iyayenku, wanda Allah bai saukar da wani dalili a kansu ba, hukunci gaba ɗaya na Allah ne, ya yi umarni kada a bautawa kowa sai shi kaɗai, wannan shi ne addinin miƙaƙƙe, amma ba fi yawan mutane ba su sani ba". (Yusuf : 39 - 40).

(Haka lamarin yake idan muka duba labarin ƙissar Annabi Luɗu da mutanensa, lokacin da yayi baƙi, su kuma suka zo don yin lalata da waɗannan baƙi), sai Annabi Luɗu ya ce da su – cikin hikima da tausasawa – :

﴿ قَالَ يَٰقَوۡمِ هَٰٓؤُلَآءِ بَنَاتِي هُنَّ أَطۡهَرُ لَكُمۡۖ فَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَلَا تُخۡزُونِ فِي ضَيۡفِيٓۖ أَلَيۡسَ مِنكُمۡ رَجُلٞ رَّشِيدٞ ٧٨ ﴾ [هود: ٧٨].

Ma'ana : "Ya mutanena ga 'ya 'yana mata nan, tsarkakakku ne gareku, ku ji tsoron Allah kada ku kunyata ni a cikin baƙina, Yanzu babu wani shiryayye a cikinku". (Hud : 78).

A wani wajen kwaɗaitarwa da tsoratarwa nan ma Annabi Nuhu ya ce da mutanensa:

﴿ فَقُلۡتُ ٱسۡتَغۡفِرُواْ رَبَّكُمۡ إِنَّهُۥ كَانَ غَفَّارٗا ١٠ يُرۡسِلِ ٱلسَّمَآءَ عَلَيۡكُم مِّدۡرَارٗا ١١ وَيُمۡدِدۡكُم بِأَمۡوَٰلٖ وَبَنِينَ وَيَجۡعَل لَّكُمۡ جَنَّٰتٖ وَيَجۡعَل لَّكُمۡ أَنۡهَٰرٗا ١٢ مَّا لَكُمۡ لَا تَرۡجُونَ لِلَّهِ وَقَارٗا ١٣ وَقَدۡ خَلَقَكُمۡ أَطۡوَارًا ١٤ ﴾ [نوح: ١٠ - ١٤].

Ma'ana : "Na ce ku nemi gafarar ubangijinku haƙiƙa shi mai yawan gafara ne.

zai ƙare ku da dukiya da ‘ya ‘ya, ya kuma sanya muku gonaki, ya sanya muku ƙoramu. Me ya same ku ba kwa neman nutsuwa a wurin Allah. Alhali ya halicceku mataki bayan mataki”. (Nuh : 10 – 14).

Yana cikin tsarin kiran Annabawa, yin wa’azin da duk lokacin da ya dace, da daddare ne ko da rana, (suna ribatar yanayin da ya dace). Allah Maɗaukakin Sarki ya hakaito mana irin yadda Annabi Nuh ya yi amfani da dukkan lokutan da suka dace wajen kiran mutanensa zuwa ga Addinin Allah.

﴿ قَالَ رَبِّ إِنِّي دَعَوْتُ قَوْمِي لَيْلًا وَنَهَارًا ۝٥ ﴾ [نوح: ٥].

Ma’ana : “”Nuhu ya ce, ya Ubangijina na kira mutanena dare da rana)

(Nuh : 5) Ya sake cewa:

﴿ ثُمَّ إِنِّي أَعْلَنتُ لَهُمْ وَأَسْرَرْتُ لَهُمْ إِسْرَارًا ۝٩ ﴾ [نوح: ٩].

“Sannan na bayyana musu (wa’azi) a bayyane, na yi musu (Wa’azi) a ɓoye”. (Nuh : 9).

Hakanan Manzon Allah (S.A.W) ya kasance yana bin mutane a wurin aikin hajj a garin Makkah yana kiransu zuwa ga bauta wa Allah shi kaɗai, ba tare da abokin tarayya ba.

‘Yan uwana musulmi wannan kaɗan kenan daga cikin irin tsari da salo da Annabawa suke bi wajen wa’azi da ilmantarwa da kiran mutane zuwa ga addinin Allah. Zamu ga akwai ilimi da hikima da tausasawa da hankali a cikinsa, don haka wajibi ne a kanku ya ku masu kira zuwa ga Allah da masu tarbiyya ku yi koyi da su, don wa’azi ya yi amfani ya shiga cikin kunnuwa.

Allah ya yi mana Albarka cikin abin da muka ji, na Alƙur’ani da Hadisi, Shi Allah Mai iko ne akan dukkan komai.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah, Kyakkyawan ƙarshe ya tabbata ga masu tsoron Allah, Tsira da Aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, Manzon Allah (S.A.W) da iyalansa da Sahabbansa da waɗanda suka bi su, har zuwa ranar sakamako gaba ɗaya. Bayan haka :

Yaku masu sauraro, yana cikin abin da tsarin kiran Annabawa ya bambanta da shi kawo dalilai gamsassu na hankali akan abin da suke kira a kai, Dalilan da duk mai hankali ba zai iya kawar da su ba, sai dai ya yi girman kai, ya ƙi gaskiya. Hakanan wajen kawo dalilan na shari’a, Idan muka duba ƙissar Annabi Ibrahim (A.S) zamu ga irin waɗannan dalilai na hankali da ya yi amfani da su, wajen jawo hankalin mutanensa zuwa ga bautawa Allah shi kaɗai, ba tare da shirka ba, Allah ya ce :

﴿ وَإِذْ قَالَ إِبْرَٰهِيمُ لِأَبِيهِ ءَازَرَ أَتَتَّخِذُ أَصْنَامًا ءَالِهَةً ۖ إِنِّىٓ أَرَىٰكَ وَقَوْمَكَ فِى ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿٧٤﴾ وَكَذَٰلِكَ
نُرِىٓ إِبْرَٰهِيمَ مَلَكُوتَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَلِيَكُونَ مِنَ ٱلْمُوقِنِينَ ﴿٧٥﴾ فَلَمَّا جَنَّ عَلَيْهِ ٱلَّيْلُ رَءَا كَوْكَبًا ۖ قَالَ هَٰذَا
رَبِّى ۖ فَلَمَّآ أَفَلَ قَالَ لَآ أُحِبُّ ٱلْءَافِلِينَ ﴿٧٦﴾ فَلَمَّا رَءَا ٱلْقَمَرَ بَازِغًا قَالَ هَٰذَا رَبِّى ۖ فَلَمَّآ أَفَلَ قَالَ لَئِن لَّمْ يَهْدِنِى
رَبِّى لَأَكُونَنَّ مِنَ ٱلْقَوْمِ ٱلضَّآلِّينَ ﴿٧٧﴾ فَلَمَّا رَءَا ٱلشَّمْسَ بَازِغَةً قَالَ هَٰذَا رَبِّى هَٰذَآ أَكْبَرُ ۖ فَلَمَّآ أَفَلَتْ قَالَ
يَٰقَوْمِ إِنِّى بَرِىٓءٌ مِّمَّا تُشْرِكُونَ ﴿٧٨﴾ إِنِّى وَجَّهْتُ وَجْهِىَ لِلَّذِى فَطَرَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ حَنِيفًا ۖ وَمَآ أَنَا۠ مِنَ
ٱلْمُشْرِكِينَ ﴿٧٩﴾ وَحَآجَّهُۥ قَوْمُهُۥ ۚ قَالَ أَتُحَٰٓجُّوٓنِّى فِى ٱللَّهِ وَقَدْ هَدَىٰنِ ۚ وَلَآ أَخَافُ مَا تُشْرِكُونَ بِهِۦٓ إِلَّآ أَن يَشَآءَ رَبِّى
شَيْـًٔا ۗ وَسِعَ رَبِّى كُلَّ شَىْءٍ عِلْمًا ۗ أَفَلَا تَتَذَكَّرُونَ ﴿٨٠﴾ وَكَيْفَ أَخَافُ مَآ أَشْرَكْتُمْ وَلَا تَخَافُونَ
أَنَّكُمْ أَشْرَكْتُم بِٱللَّهِ مَا لَمْ يُنَزِّلْ بِهِۦ عَلَيْكُمْ سُلْطَٰنًا ۚ فَأَىُّ ٱلْفَرِيقَيْنِ أَحَقُّ بِٱلْأَمْنِ ۖ إِن كُنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿٨١﴾ ٱلَّذِينَ
ءَامَنُوا۟ وَلَمْ يَلْبِسُوٓا۟ إِيمَٰنَهُم بِظُلْمٍ أُو۟لَٰٓئِكَ لَهُمُ ٱلْأَمْنُ وَهُم مُّهْتَدُونَ ﴿٨٢﴾ وَتِلْكَ حُجَّتُنَآ ءَاتَيْنَٰهَآ إِبْرَٰهِيمَ عَلَىٰ
قَوْمِهِۦ ۚ نَرْفَعُ دَرَجَٰتٍ مَّن نَّشَآءُ ۗ إِنَّ رَبَّكَ حَكِيمٌ عَلِيمٌ ﴿٨٣﴾ ﴾ [الأنعام: ٧٤ – ٨٣]

Ma’ana : “Ka tuna yayin da Ibrahim ya ce wa babansa Azara, yanzu zaka riƙi gumaka ababen bauta, lallai ni ina ganinka kai da mutanenka kuna cikin ɓata mabayyani. Hakanan muke nuna wa Ibrahim mulkin sammai da ƙassai don ya zama cikin masu yaƙini. Yayin da dare ya yi, ya ga tauraro sai ya ce, “wannan ne Ubangijina” yayin da ya faɗi (ya ɓace) sai (Annabi Ibrahim) ya ce bana son wanda yake faɗu wa. Yayin da ya ga wata ya fito fili, sai ya ce wannan ne Ubangijina, yayin da ya ɓace, sai ya ce, in Ubangijina bai shirye ni ba zan kasance cikin mutane ɓatattu. Yayin da ya ga rana ta bayyana sai ya ce, wannan ne Ubangijina, wannan ma ya fi girma, yayin da ta faɗi (ta ɓace), sai ya ce, ya mutanena ni na barranta daga abin da kuke shirka da shi. Na fuskantar da fuskata zuwa ga wanda ya halicci sammai da ƙassai, sannan ina mai karkata zuwa ga gaskiya, ba na cikin masu shirka. Sai mutanensa suka yi jayayya da shi, sai ya ce musu yanzu kuna jayayya da ni dangane da Allah, alhali ya shirye ni, ba na tsoron abin da kuke shirka da shi, sai dai abin da Allah ya so, Ubangijina ya yawalci komai da ilimi, ashe ba zaku wa’azantu ba. Kuma ta yaya zan ji tsoron abin da kuke shirka da shi, alhali ku ba kwa tsoron kun yi shirka da Allah a cikin abin da bai saukar muka da wani dalili a kansa ba. To wane jama’a ne (tsakanin ni da ku) ya fi cancanta da aminci in dai kun sani?. waɗanda suka yi imani ba su haɗa imaninsu da shirka ba, waɗannan suna da cikakken aminci kuma su ne shiryayyu. Waɗannan hujjojinmu ne muka baiwa Ibrahim a kan mutanensa, muna ɗaga darajar wanda muka so, haƙiƙa Ubangijinka mai hikima ne kuma masani”. (Al – An’am : 74 – 83).

A cikin waɗanan ayoyi zamu ga hujjoji na hankali da Annabi Ibrahim ya buga wa mutanensa hujja da su, na bayyana cewa duk abin da baya amfanarwa ba ya cutarwa, ba ya dauwama, bai cancanta a bauta masa ba, Allah Maɗaukakin Sarki Mahaliccin kowa da komai shi ne kaɗai ya cancanta a bauta masa.

Idan mun duba ƙissar Annabi Musa da Fir’auna (zamu ga yadda Annabi Musa ya kafawa Fir’auna hujja ta hankali wadda ya gaza ture ta, yayin da Fir’auna ya tambayi Annabi Musa da Haruna ya ce, waye Ubangijinku, sai Annabi Musa ya ce masa ,

﴿ قَالَ رَبُّنَا ٱلَّذِيٓ أَعۡطَىٰ كُلَّ شَيۡءٍ خَلۡقَهُۥ ثُمَّ هَدَىٰ ٥٠ ﴾ [طه: ٥٠]

Ma’ana : “Ya ce Ubangijinmu shi ne wanda ya halicci dukkan komai kuma ya shiryar (da shi)”. (Ɗaha : 50). Irin waɗannan misalai a ƙissar Annabi (S.A.W) suna da yawa.

Yaku Musulmi, ku nisanci saɓawa tsarin Annabawa wajen kira zuwa ga Allah, kada ku bi hanyoyin ɓatattu, irinsu khawajijawa, da ‘yan shi’a, da sauransu, wajen kira zuwa ga Allah.

Sannan wajibi akan masu wa’azi – malamai da ɗalibai – su amfanu da hanyoyin zamani da aka samu wajen kira zuwa ga addinin Allah, irinsu Internet, da kwamfuta, da salula da sauransu, ku duba ku ga yadda abokan gabarmu suka ribaci waɗannan abubuwa don yaɗa ɓarnarsu.

Ku ji tsoron Allah – bayin Allah – Ku sani fiyayyar shiriya ita ce shiryar Manzon Allah (S.A.W), mu yi koyi da Manzon Allah wajen kiran mutane zuwa ga addini, mafi sharrin al’amura abubuwan da aka ƙaga, duk abin aka ƙaga kuwa bidi’a ce, dukkan bidi’a ɓata ce, dukkan ɓata kuwa yana cikin wuta.

HAKKIN MUSULMI AKAN MUSULMI

Manufofin huɗubar

- Bayanin haƙiƙanin ‘yan uwantaka a musulunci.
- Bayanin wajabcin taimakon juna a musulunci.
- Bayanin falalar ‘yan uwantaka a musulunci da nuna cewa ta fi ‘yanuwantakar Jini.
- Tsoratarwa daga rarrabuwa da ɗaiɗaicewa a tsakanin musulmi.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga shirrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammad bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammad (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Ya ‘yan uwana musulmi : Haƙiƙa addinin musulunci addini ne mai girma, kuma addinine mai tsari, ya tsara wa mabiyansa kyakkyawan tsari, tsarin da ya haɗa kiyaye haƙƙoƙin da wajibai, kuma babu wani aiki na ƙwarai da yake tafiya a banza a cikin wannan tsari, tsari ne da ya ba duk wani mai haƙƙi haƙƙinsa, daga cikin irin waɗannan haƙƙoƙi da wannan tsari ya zo da shi akwai haƙƙin musulmi a kan ɗan uwansa musulmi.

Yaku yan uwa Musulmi : Haƙiƙa Manzon Allah (ﷺ) ya tabbatar da cewa Musulmi yana da haƙƙi a kan ɗan uwansa musulmi, in da yake cewa, “Haƙƙin musulmi a kan musulmi shida ne. Aka ce mene ne su ya Manzon Allah?” Sai Manzon Allah ya ce, su ne, “idan ya gamu da shi ya yi masa sallama, idan ya gayyace shi ya amsa, idan ya neme shi ya yi masa nasiha, ya yi masa, idan ya yi atishawa ya gode wa Allah ya gaishe shi, idan baya da lafiya ya je ya duba shi,

idan ya mutu ya raka shi" Muslim ne ya rawaito shi.

A cikin wannan hadisi mai girma zamu ga Manzon Allah (ﷺ) ya faɗi wasu haƙƙoƙi da musulmi yake da shi akan ɗan uwansa musulmi. Aiki da waɗannan haƙƙoƙi - babu ko shakka – zai kawo soyayya da ƙauna da zaman lafiya a tsakanin musulmi, wanda hakan ya kan zama sababin mutum ya shiga Aljannah. Saboda ya zo a cikin hadisin da Imam Muslim ya rawaito, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Na rantse da wanda raina yake hannunsa, ba zaku shiga Aljannah ba, har sai kun yi imani, kuma ba zaku yi imani ba, har sai kun so junanku. Ashe bana nuna muku abin da idan kuka aikata shi zaku so junanku ba? Ku yaɗa sallama a tsakaninku".

Yana cikin haƙƙin musulmi a kan musulmi kada ya yi masa hassada, kada ya ƙullace shi, saboda shi mumini ƙirjinsa a wanke yake, zuciyarsa mai tsarki ce, yana kwana ba tare da ƙullin wani ko hassada a zuciyarsa ba, Manzon Allah (ﷺ) yana cewa a cikin hadisin da Bukhari da Muslim suka rawaito daga Anas ɗan Malik – Allah ya yarda da shi – ya ce, : "Kada ku yi gaba da juna, kada ku ba juna baya, kada ku yi gasa da juna, ku zama bayin Allah 'yan uwan juna". Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

Yana daga cikin haƙƙin musulmi a kan ɗan uwansa musulmi ya taimaka masa daidai gwargwadon ikonsa wajen biyan buƙatunsa na duniya, ya sauwaƙa masa idan ya shiga tsanani, ya suturta shi yayin da yake buƙatar sutura. An karɓo daga Abu Hurairata – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Wanda ya yaye wa wani mumini baƙin ciki daga cikin baƙin cikin duniya, Allah zai yaye masa wani baƙin ciki daga cikin baƙin cikin lahira. Wanda duk ya sauwaƙa wa wanda yake cikin matsi, Allah zai sauwaƙa masa duniya da lahira, wanda duk ya suturta musulmi, Allah zai suturta shi duniya da lahira. Allah yana cikin taimakon bawa matuƙar bawa yana taimakon ɗan uwansa" Muslim ne ya rawaito.

Hakanan yana cikin haƙƙin musulmi akan musulmi taimakonsa a cikin kowane hali da yanayi, ya taimake shi idan yana zalunci, kamar yadda zai taimake shi idan ana zaluntar shi. An karɓo daga Anas ɗan Malik – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Ka taimaki ɗan uwanka, ana zaluntarsa ko shi yana zalunci. Sai wani mutum ya ce, "Ya Manzon Allah, zan taimake shi idan ana zaluntarshi, amma yaya zan taimake shi idan yana zalunci?" Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Ka riƙe hannunsa" (ka hana shi zalunci).

Yana cikin haƙƙin musulmi ne akan ɗan uwansa musulmi ya ɓoye aibinsa, ya yi masa afuwa da rangwame yayin da ya yi masa wani abu maras daɗi, yin haka yana daga cikin manya – manyan haƙƙin musulmi akan ɗan uwansa musulmi, saboda ɗan uwanka ba mala'ika ba ne, ba Annabi ba ne, mutum ne don haka ka suturta shi.

Malamai suna cewa : Mutane kala biyu ne. Kala na farko su ne waɗanda suka shahara a cikin mutane da nagarta da nisantar saɓo, to irin waɗannan idan suka faɗa cikin kuskure ana son musulmi su yi musu afuwa, su suturta su, kada su bibiyi al'aurarsu, Manzon Allah (ﷺ) yana cewa a cikin hadisin da Imam Ahmad ya rawaito daga Abi Barzatal Assalami ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, : " Yaku taron

waɗanda suka yi imani da harshensu, amma imanin bai shiga zuciyarsu ba. Kada ku yi gulmar musulmi, kada ku bibiyi alurarsu, duk wanda ya bi al'aurar musulmi, shi ma Allah zai bi al'aurarshi, duk kuwa wanda Allah ya bibiyi al'aurarsa to zai kunyata shi a cikin gidanshi" .

Kala na biya daga cikin mutane, su ne, waɗanda suke bayyana saɓonsu a fili, ba sa jin kunyar Allah, ba sa jin kunyar mutane, to irin waɗannan fasiƙai ne, ba a suturta su.

'Yan uwana masu sauraro : Son juna saboda Allah ba ƙarami abu ne a musulunci, yana daga cikin abubuwan da suke nuna cikar imanin mutum, kuma yana iya zama sababi daga cikin sababan da suke kai mutum Aljannah.

Ya tabbata a cikin Bukhari da Muslim daga Anas ɗan Malik – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Abubuwa guda uku, wanda yake da su ya ɗanɗani zaƙin imani, ya zama ya fi son Allah da Manzonsa akan waɗanda ba su ba, sannan ya so mutum don Allah, ba don wani abu ba, sannan ya ƙi komawa kafirci kamar yadda yake ƙin a sanya shi a wuta". Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

An karɓo daga Abu Hurairata – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Wani mutum ya tafi wani gari don ya ziyarci wani ɗan uwansa, sai Allah ya sanya masa Mala'ika a kan hanyarsa yana jiransa. Lokacin da wannan mutumin ya iso wajen Mala'ikan, sai ya ce da shi, "ina zaka je?" Sai ya ce, "Zan ziyarci wani ɗan uwana ne a wannan gari". Sai Mala'ikan ya ce, "Shin akwai wata ni'ima ce wadda kake renonta a wajensa?" sai ya ce, "A'a, ni dai kawai ina son shi ne saboda Allah". Sai Mala'ikan nan ya ce da shi, "Ni Allah ne ya aiko ni wajenka, ya ce, yana sonka kamar yadda kake son shi".

Wannan ita ce haƙiƙanin 'yan uwantaka ta gaskiya, kuma wannan ita ce haƙiƙaninta, haƙiƙa 'yan uwantaka saboda Allah ba ta ginuwa akan komai sai akan igiyar aƙida da igiyar imani da igiyar soyayya saboda Allah, waɗannan igiyoyi ba sa tsinkewa har abada.

An karɓo daga Abu Hurairata – Allah ya yarda da shi – Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Mutane bakwai Allah zai musu inuwa a cikin inuwarsa, ranar da babu wata inuwa sai inuwarsa, shugaba mai adalci, da matashin da ya tashi a cikin ibadar Allah, da mutumin da zuciyarsa take rataye da masallaci, da mutane biyun da suka yi soyayya saboda Allah, sun haɗu saboda shi, sun rabu a kanshi (wato har rabuwa ta zo suna kan soyayyarsu saboda Allah) da mutumin da mace mai matsayi da kyau ta neme shi, sai ya ce mata, ni ina jin tsoron Allah, da mutumin da ya yi sadaka, ya ɓoye ta har hannun dama bai san me hannun hagu ya bayar ba, da mutumin da ya ambari Allah shi kaɗai, idanuwansa suka zubar da hawaye". Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

Da wannan hadisi zamu gane cewa 'yan uwantaka saboda Allah ni'ima ce babba daga wajen Allah, wani marmaron ruwa ne da Allah yake kwarara shi ga muminai masu gaskiya, kamar yadda 'yan uwantaka take wani ruwa ne mai tsarki da Allah yake shayar da bayinsa tsarkaka muminai. Allah Maɗaukakin Sarki ya ce,

﴿ إِنَّمَا ٱلۡمُؤۡمِنُونَ إِخۡوَةٞ فَأَصۡلِحُواْ بَيۡنَ أَخَوَيۡكُمۡۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ لَعَلَّكُمۡ تُرۡحَمُونَ ١٠ ﴾ [الحجرات: ١٠]

“Kaɗai muminai ‘yan uwan junane, ku daidaita tsakanin ‘yan uwanku. Ku ji tsoron Allah don ku samu rahama” (Al – hujrat : 10).

Allah ya yi mana Albarka cikin abin da muka ji na Alƙur’ani mai girma, ya amfanar da mu da abin da yake cikinsa na ayoyi da zikiri mai girma, haƙiƙa Allah mai iko ne akan komai.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah, Kyakkyawan ƙarshe yana ga masu tsoron Allah, Tsira da Aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, Manzon Allah (ﷺ) da iyalansa da Sahabbansa da waɗanda suka bi su gaba ɗayansu, har zuwa ranar sakamako. Bayan haka:

Ya ‘yan uwa masu girma : Haƙiƙanin 'yan uwantakar musulunci ita ce take haɗa abin da yake rabe, take haɗe abin da ya saɓa, ita ce igiyar da take sanya taron al'ummar musulmi su zama kamar jiki ɗaya, ta mayar da su kamar gini, sashensa yana ƙarfafa shashe, irin wannan ‘yan uwantaka ita ce irin wadda take tsakanin Sahabban Manzon Allah (ﷺ), tsakanin mutanen Makka da Madina, har ya kasance mutum yana raba dukiyarsa ya ba ɗan uwansa rabi, ya saki matarsa don ɗan uwansa ya aura.

An karɓo daga Anas – Allah ya yarda da shi – ya ce, Abdur-Rahman ɗan Auf ya zo wajenmu (a Madina) sai Annabi (ﷺ) ya haɗa 'yan uwantaka tsakaninsa da Sa'ad ɗan Rabe'u, wanda yake yana da dukiya mai yawa. Sai ya ce wa Abdur-Rahman "Mutanen Madina sun san cewa ni ina cikin masu dukiya mai yawa, don haka sai raba dukiyata rabi, na baka, kuma ina da mata biyu, ka kalli wanda ta fi ƙayatar da kai, sai in sake ta, idan ta yi idda ka aura. Sai Abdur-Rahman ya ce, "Allah ya yi maka albarka a cikin dukiyarka da iyalanka, ku nuna min kasuwa". Ba a yi wasu kwanaki ba, sai ga Abdur-Rahman ya zo wajen Manzon Allah (ﷺ) da alamar turare a jikinsa, sai Manzon Allah ya ce masa, "Me ya faru ne?" sai ya ce, "Na auri wata mata daga cikin mutanen Madina". Sai Manzon Allah ya ce, "Me ka bata sadaki?" sai ya ce, "Mauni na zinare ko azurfa" sai Manzon Allah ya ce, "Yi walima, koda da akuya ne".

Allahu Akbar! Wannan ita ce 'yan uwantakar musulunci, ku duba ku ga yadda ta mayar da waɗannan mazaje, dukiyarsu da iyalansu sun zama masu sauƙi a wajensu don neman yardar Allah. Ko akwai wanda zai wa'azantu!?.

Ya 'yan uwa musulmi : Haƙiƙa hassada da ƙulli a zuciya suna cikin mafi haɗarin cututtukan zuciya, waɗanda suke rusa 'yan uwantaka, saboda hasada ita ce ɗan uwa ya ga ɗan uwansa a cikin ni'ima, sai ya ƙullace shi, ya yi masa hassada ya yi burin wannan ni'ima ta gushe daga ɗan uwanshi, ya manta da cewa Allah Maɗaukakin Sarki shi ne wanda ya bashi wannan arziƙin, don haka wanke zuciya daga hassada da ƙulli babbar lamari ne, kuma dalili ne daga cikin dalilan da shigar da mutum Aljanna.

Hadisi ya tabbata a cikin littafin (Al – Musnad) na Imam Ahmad daga Anas ya ce, Muna zaune a wajen Annabi (ﷺ) sai ya ce, "Yanzu wani mutum ɗan Aljannah zai ɓullo muku" sai wani mutum daga cikin mutanen Madina ya ɓullo, gemunsa yana ɗigar da ruwan alwalarsa, ya rataye takalmansa a hannun hagun ɗin sa. Da aka wayi gari, sai Annabi (ﷺ) ya sake faɗin abin da ya faɗa, sai wannan mutumin ya ɓullo kamar yadda ya ɓullo a karo na farko. A rana ta uku sai Manzon Allah ya sake faɗin maganarsa ta farko, sai wannan mutumin ya ɓullo kamar yadda ya ɓullo a karo na farko. Da Manzon Allah (ﷺ) ya tashi, sai Abdullahi ɗan Amru ɗan Asi ya bi wannan mutumin, ya ce masa, na ɗan nisanci babana ne, na yi rantsuwa ba zai shiga inda yake ba har tsawon kwana uku, don haka idan ka ga da dama ka bani wuri har zuwa kwana ukun to ka ba ni, sai mutumin nan ya ce, to. Anas (mai riwaya) ya ce, Sai Abdullahi ya bamu labari ya ce "ya kwana tare da wannan mutum kwana uku, bai ga yana tsayuwar dare ba, sai dai idan ya farka da daddare ya juya akan shinfiɗarsa, ya yi kabbara, ya juya har zuwa lokacin sallar asuba. Abdullahi ya ci gaba da cewa "sai dai ban ji yana faɗin komai ba sai alheri" da kwana uku suka wuce, sai na kusa in raina ayyukansa, sai na ce masa "Bawan Allah, babu wani abu na fushi ƙaura tsakanina da mahaifina, kurum na ji Manzon Allah (ﷺ) har sau uku yana cewa "wani mutum ɗan aljannah sai ɓullo muku yanzu" sai in ga ka ɓullo, har sai uku, don haka na so in zo inda kake don in ga aikin da kake, in yi koyi da kai, amma sai ban ga kana wani aiki mai yawa ba, meye ya kaika abin da Manzon Allah ya faɗa?. Sai mutumin nan ya ce, "wannan abin da ka gani shi ne kawai" da na juya sai ya kira ni, ya ce da ni, "wannan abin ka gani shi ne kawai, amma fa bana ɗauke da alush ga wani daga cikin musulmi, kuma bana yi wa wani hassada akan alherin da Allah ya bashi" Sai Abdullahi ya ce, "Wannan shi ne ya kai ka wannan matsayi, kuma shi ne abin bama iyawa".

Yaku al'ummar Musulmi : Irin wannan ‘yan uwantaka ita ce take gadar da ƙarfi ga musulmi, su rinjayi duk wani kafiri maƙiyin wannan addini mai girma. Sai dai abin baƙin ciki a yau musulmi sun zama kamar sharar da ruwa ya ɗauko, sun warwatse, sun rarrabe, maƙiya sun dira a kansu, su wawashe dukiyoyinsu, sun ci mutuncinsu, duk wannan ba don komai ba, sai dai watsar da ‘yan uwantaka da juna, da rashin kiyaye haƙƙin juna. Babu ko shakka ba yadda za a yi al’umma ta dawo da ƙarfinta da kwarjininta sai ta raya ‘yan uwantaka a tsakaninta, musulmi ya kiyaye haƙƙin ɗan uwansa musulmi. Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa :

﴿ وَأَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَلَا تَنَٰزَعُواْ فَتَفۡشَلُواْ وَتَذۡهَبَ رِيحُكُمۡۖ وَٱصۡبِرُوٓاْۚ إِنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلصَّٰبِرِينَ ٤٦ ﴾

[الأنفال: ٤٦].

Ma’ana : “ Ku bi Allah da Manzonsa, Kada ku yi jayayya da juna, sai ku ɓalɓalce, ƙarfinku ya tafi, ku yi haƙuri, haƙiƙa Allah yana tare da masu haƙuri” (Al-anfal : 46).

Saboda haka wajibi ne mu taimaki junanmu, mu zama bayin Allah ‘yan uwan juna, kamar yadda Allah da Manzonsa suka umarce mu, haƙiƙa Allah yana tare da jama’a. kuma ƙarfi yana cikin haɗuwa, rauni kuwa yana cikin rarrabewa da tarwatsewa. Allah ya tsare mu daga rabewa da saɓawa.

KAFAFEN YAƊA LABARI DA TASIRINSU A CIKIN AL'UMMA

Manufofin huɗubar

- Jan hankalin mutane zuwa ga mahimmanci kafafen yaɗa labarai.
- Haɗa kafafen yaɗa labarai da yi wa addinin musulunci hidima.
- Karfafa wa wajen kyawawan halayen cikin aikin yaɗa labarai.
- Fito da matsalolin da kafafen yaɗa labarai na musulunci suke fuskanta don neman mafita.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga shirrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammad bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammad (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Ya ku 'yan uwana musulmi a yau zamu tattauna ne akan wani abu mai girma, mai girma saboda girman amfaninsa idan an yi amfani da shi wajen aikin alheri, mai girma saboda girman haɗarinsa idan an yi amfani da shi a wajen sharri da ɓarna. Abu ne da yake da iko mai ƙarfi a cikin rayuwar mutane, har ma babu wanda zai iya fita ko gujewa ikonsa da tasirinsa. Wannan abu ba komai ba ne face kafafen yaɗa labarai.

Haƙiƙa kafafen yaɗa labarai irinsu Jaridu da Mujallu kafafe ne masu matuƙar tasiri a cikin al'umma, wajen yaɗa aƙida da ɗabi'u, idan an ribace su wajen alheri da fahimtar da mutane addini, da abin da zai amfane su a duniyarsu, haƙiƙa sun zama kafofi mafi girma da amfani, idan kuwa aka yi amfani da su wajen kishiyar haka to sun zama mafi cutarwar kafofi.

Kafar yaɗa labarai a wannan zamani wata tasha ce mai mahimmanci, tana da tasiri mai ƙarfi wajen sharri ko alheri a cikin sha'anin mutane, don haka wajibi ne a yi ƙoƙari a ribaci waɗannan kafafe waɗanda ake sauraro ko ake kallo ko ake karantawa wajen kiran mutane zuwa ga addinin Allah, da yaɗa kyawawan halaye, da yaƙar munanan ɗabi'u.

Saboda haka ina faɗakar da masu hali kan dole ne samar da irin waɗannan kafafe, waɗanda suke magana da yarenmu (hausa), ta yadda zai zama babban aikinsu shi ne yaɗa musulunci da Sunnah a cikin al'umma, abin da muke gani na cutuwa da ɓarna da sharri da rushe addini daga wasu kafafen yaɗa labarai marasa manufa ya ishe mu.

Yaku al'ummar musulmi : Wajibi ne a kan waɗanda suke kula da waɗannan kafafen yaɗa labarai su ji tsoron Allah, su sani cewa dukkanmu masu kiwo ne, kuma dukkanmu za a tambaye mu akan abin aka bamu kiwo, don haka kada a kuskura a gabatarwa da al'umma sai abin da yake kira ne zuwa ga alheri, da kafa kyawawan ɗabi'u na musulunci, a siffofi nagari, hakanan wajibi ne a kansu su tsamo al'umma daga dukkan wani abin da zai ruɗa mata tunani, ya ɓata masa aƙida, ya gurɓata mata halaye, da ayyukansu na yau da kullum.

Yaku 'yan jarida, aikin jarida matsayin numfashi ne ga al'umma, madubi ne ga mutane, don haka ku kiyaye amanar kalma da harafi, da gaskiyar zance, ku sani cewa da imani da tsoron Allah da kyakkyawar manufa kafafen yaɗa labaran musulmi suka fita daban da na arna da kafirai. Ku nisanci ƙarya da jirkita zance, ku kirdadi gaskiya, ku guji yaɗa jita – jita, kada ku faɗi duk abin kuka ji ko kuka gani, ya tabbata Manzon Allah (S.A.W) ya ce : "Mutum ya isa maƙaryaci ya faɗi duk abin da ya ji". Don haka Kada ku bada labari sai wanda ya tabbata, kada ku yaɗa komai sai idan a cikin yaɗa shi akwai gyaruwar al'umma a ciki, da yawa daga cikin 'yan jaridar suna yaɗa labaran da baya halatta a yaɗa su a cikin mutane, saboda yaɗa su yaɗa alfasha ne da mummunan abu cikin muminai, Allah Maɗaukakin Sarki kuwa ya hana haka, don haka ku ji tsoron Allah a cikin ayyukanku.

Yaku 'Yan uwana yan jarida : Abin da ya wajaba ku mayar da hankalinku a kai shi ne yaɗa aƙida ingantacciya, wadda babu shirka da ɓarna a cikinta, saboda Manzon Allah (S.A.W) lokacin ya aiki Mu'azu ɗan Jabal zuwa Yemen abin da ya yi masa wasiyya da shi kenan da farko, ya ce masa ya kira mutane zuwa ga shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah, kuma Annabi Muhammad bawan Allah ne Manzonsa, idan sun amsa masa, sai ya koya musu cewa Allah ya wajabta musu salloli biyar cikin dare da yini… to hakanan ya wajaba akan 'yan jarida su aikata.

Hakanan wajibi ne akan 'yan jarida su kira mutane zuwa ga kyawawan halaye da ɗabi'u, Manzon Allah (S.A.W) ya ce : "Kaɗai an aiko ni don in cika kyawawan halaye".

Hakanan wajibi ne akan kafar yaɗa labarai ta zama mai gaskiya da adalci cikin duk abin da zata faɗa, domin gaskiya da adalci ana son su a cikin dukkan komai. Hakanan kada kafar yaɗa labarai ta nutse cikin yaɗa ɓarna da munanan abubuwa cikin al'umma, kuma wajibi ne kafofin yaɗa labarai su lura da ladubban tattaunawa,

da shiryar da mutane da hikima da kyakkyawan wa'azi. Allah Maɗaukakin sarki ya ce, :

﴿ مَّا يَلۡفِظُ مِن قَوۡلٍ إِلَّا لَدَيۡهِ رَقِيبٌ عَتِيدٞ ١٨ ﴾ [ق: ١٨].

Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa : "Babu wani lafazi da zai faɗa face a wurinsa akwai Raƙibu da Atidu".

Allah ya yi mana albarka cikin abin da muka ji, ya amfane mu da abin da yake cikin Alƙur'ni da Hadisai. Haƙiƙa Allah mai iko ne a kan dukkan komai

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah Maɗaukakin Sarki, Kyakkyawan ƙarshe yana ga masu tsoron Allah, Tsira da Aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, Manzon Allah (S.A.W) da iyalansa da Sahabbansa da waɗanda suka bi su gaba ɗaya, har zuwa ranar sakamako. Bayan haka :

Yaku bayin Allah, : Muna fama da matsaloli da yawa a cikin ƙafafen yaɗa labaranmu, kuma wajibi ne mu canza su, don ƙafafen yaɗa labarai su taka rawar da ta dace.

Daga cikin irin waɗannan matsaloli akwai ƙ arancin samun masu kishin addinin musulunci a fagen yaɗa labarai, da yawa daga cikin masu aiki a ƙafafen yaɗa labarai su kan manta da saƙon addininsu na musulunci yayin da suke gabatar da aikinsu, kurum abin da ya dame su shi ne me zasu samu na abin duniya daga wannan aiki, don haka zaka ga irin waɗannan suna yaɗa abin da yake munana wa ne ga addininsu da aƙidarsu da al'ummarsu.

Hakanan yana cikin matsalolin da muke fama da su ƙarancin masu bada gudummawar ƙudî ga wasu daga cikin ƙafafen yaɗa labarai masu kyakkyawar manufa, don haka sai ka ji irin waɗannan ƙafafe suna fama da rashin kudî, abin da yake kaiwa da rushewarsu wani lokaci.

Kamar yadda yana cikin abin da yake damun da yawa daga cikin masu yaɗa labarai a yau shi ne jahilci da son zuciya, sai ka samu mutum jahili a addini, yana gabatar da wani shirin addini, wanda alal – haƙiƙa ɓarnar da zai yi ta fi gyaran da zai kawo yawa, don haka wajibi ne akan 'yan jarida su san waye zai gabatar da kowane shiri, shirin na addini ne ko ba na addini ba. Ya zama ya san abin da zai gabatar, saboda Allah yana cewa :

﴿ وَلَا تَقۡفُ مَا لَيۡسَ لَكَ بِهِۦ عِلۡمٌۚ إِنَّ ٱلسَّمۡعَ وَٱلۡبَصَرَ وَٱلۡفُؤَادَ كُلُّ أُوْلَٰٓئِكَ كَانَ عَنۡهُ مَسۡـُٔولٗا ٣٦ ﴾ [الإسراء: ٣٦]

Ma'ana : "Kada ka shiga abin da baka da ilimi a kansa, haƙiƙa ji da gani da zuciya dukkan waɗannan ababen tambaya ne a kansu". (Isra'i : 36)

Yana cikin abin da ya wajaba a kan 'yan jarida su lura da shi, waɗannan wasannin kwaikwayon, da ake yaɗa wa, da yawa da cikinsu suna ɗauke da guba da cutar wa mai yawa ga al'umma, musamman ma yara da mata, don haka wajibi ne kafin a yaɗa wasa a tabbatar da meye manufarsa, me zai biyo bayan yaɗa shi.

Daga cikin munanan abubuwan da waɗannan wasannin kwaikwayon suka ƙunsa akwai cire kunya daga zukatan yara, duk da cewa Manzon Allah (S.A.W) yana cewa : "Kunya alheri ce gaba ɗayanta" a wata riwayar "Kunya ba ta kawo

komai sai alheri” Bukhari ne ya rawaito.

Daga cikin abin da waɗannan wasanni suka ƙunsa: cakuɗuwar maza da mata, da rungume – rungume, da sumba a fili, ba tare da tsoron Allah ba, wanda hakan ya kan sanya yara su ɗauka cewa irin waɗannan al’amura babu laifi a aikata su, sai suma su riƙa yi, su tashi a kai.

Daga cikin abubuwar da suke haifarwa : akwai yaɗa ayyuka da maganganun alfasha a cikin al’umma, saboda haka ya zama wajibi a kan ‘yan jarida su san abin da za su riƙa yaɗawa mutane.

Yaku masu sauraro : Muna cikin wani zamani da ɓarna ta yi yawa, don haka ‘yan jarida ku ji tsoron Allah, ku taimaka wajen gyara al’umma daidai gwargwadon ikonku.

Bayin Allah : Wajibi ne akan hukuma da samar da kafafen yaɗa labarai masu nagarta, masu tsarki, waɗanda za su tsaya wajen yaɗa wannan addini ingantacce ga al’umma. Wajibin shugaba ne ya koya wa mutane addininsu, ya tsaftace su daidai iyawarsa, kamar yadda yake wajibi a kan hukuma da tsarkake kafafen yaɗa labaranta, ta gyara su, da shiryar da su zuwa ga abin da yake gyaruwar al’umma ne da ƙasa gaba ɗaya.

Hakanan wajibi ne a kan ɗaiɗaikun mutane su samar da kafafen yaɗa labarai masu kyakkyawar manufa, waɗanda za su kare mummunan farmakin da ake wa musulunci da musulmi, domin muna sane da cewa a cikin dokokin ƙasa akwai damar da samar da kafafen yaɗa labarai, don haka yana kan mawadata su aikata wannan, wataƙila hakan ya zama wani tanadi garesu ranar alƙiyama.

Haka ma wajibi ne a kan mutane su yi inkarin duk wani mummunan aiki ko ɓarna da take fitowa daga kafafen yaɗa labarai, ta hanya mai kyau da shari’a ta yarda da ita, ko dai da hannu, ko da baki, ko kuma da zuciya, kamar yadda ya zo a hadisin Annabi (S.A.W).

Yaku ‘yan jarida ku ji tsoron Allah, ku sani cewa za a tambayeku a wata rana, gaban masanin gaibu, ranar da babu wani wanda zai ɓoye wa Allah, ranar da ake fayyace sirri, ku yaɗa alheri a cikin mutane, a ko yaushe ku riƙa tuna duk wanda ya yi nuni ga aikin alheri to kamar ya aikata ne.

Hakanan yaku mutane ku amfanu da kafafen yaɗa labarai a cikin abin da bai saɓawa shari’a ba, ku tuna ba duk abin da aka faɗa ko ake yaɗa wa ba ne gaskiya, kuma ingantance, wanda Allah yake so, don haka kada ku ɗauki duk abin kuka ji, kowa ana ɗaukar maganarsa ana bari, sai Annabi (S.A.W). Ku sani Allah yana cewa :

﴿ وَقُلِ ٱعۡمَلُواْ فَسَيَرَى ٱللَّهُ عَمَلَكُمۡ وَرَسُولُهُۥ وَٱلۡمُؤۡمِنُونَۖ ﴾ [التوبة: ١٠٥]

Ma’ana : “Ka ce (musu) Ku yi aiki da sannu Allah da Manzonsa da Muminai za su ga aikinku). (Attauba : 105).

JAN-KUNNE A KAN BOKAYE DA MATSAFA

Manufofin huɗubar

- Haɗa zukatan Muslumai da Ubangijinsu.
- Bayanin hukuncin tsafi da bokanci a musulunci.
- Jan-kunne game da zuwa wajen bokaye da matsafa da ‘yan duba.
- Bayan irin haɗarinsu a cikin al’umma.
- Umarni da ruƙo da sababai na shari’a.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammadu bawansa ne manzonsa ne. (Yaku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron Allah yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Yaku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammadu (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (a addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta".

Bayan haka:

Ya ku bayin Allah! Yana daga cikin abin da aka jarrabi mutane da yawa da shi a yau, maza da mata, manya da ƙanana, sai wanda Allah ya kuɓutar da su, ko, zuwa wajen matsafa da bokaye da ‘yan duba da ‘yan tsibbu, don neman taimako a wajensu, don sanin abin da zai zo nan gaba. Su kuwa waɗannan bokaye da ‘yan tsibbu, sai su riƙa yin ƙarya ga mutane, suna cin dukiyoyinsu a banza, kuma suna kare su daga bin tafarkin Allah. Allah ya kiyashe mu! Za ka ga wani gwamna ko basarake, zuciyarsa tana rataye da wani boka ko ɗan tsibbu, ba abin da zai iya aikatawa, sai abin da ya nuna masa ya aikata, ko da wannan abin ya saɓa wa addinin Allah. Yana ji a cikin zuciyarsa cewa ya samu mulki ne ta hanyar wannan bokan, kuma bokan zai iya ƙwace mulkin sanda ya so. Ya manta da faɗin Allah cewa,

﴿ قُلِ ٱللَّهُمَّ مَٰلِكَ ٱلۡمُلۡكِ تُؤۡتِي ٱلۡمُلۡكَ مَن تَشَآءُ وَتَنزِعُ ٱلۡمُلۡكَ مِمَّن تَشَآءُ وَتُعِزُّ مَن تَشَآءُ وَتُذِلُّ مَن تَشَآءُۖ بِيَدِكَ ٱلۡخَيۡرُۖ إِنَّكَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ٢٦ ﴾ [آل عمران: ٢٦].

(Ka ce, «Ya Ubangiji! Kai ne mamallakin mulki, kana bayar da mulki ga wanda ka so, kuma kana kwace mulki daga hannun wanda ka so, ka ɗaukaka wanda ka so, kuma kana ƙasƙantar da wanda ka so, alheri gabaɗaya yana hannunka. Lallai kai mai iko ne a kan komai).

Ka ga wani kuma ɗan kasuwa ne, ba zai saya, ko ya sayar ba, sai da shawarar bokansa, ko ɗan tsibbunsa, wanda zuciyarsa take rataye da shi. Ka ga yana aikata abin da bokansa ya gaya masa, komai muni da ƙazantar da take cikin haka. Ko kuma, a'a, mace ce da take so ta mallake mijinta, ya zamo ba shi da kataɓus, ballantana ya yi wani abu bisa zaɓinsa, sai ta je wajen lalatacce, ƙazamin ɗan tsibbu, tana neman ya taimake ta bisa muradinta. Wannan fa shi ne halinmu, sai wanda Allah ya kare.

Haƙiƙa Allah ya bayyana cewa, koyan tsafi da tsibbu, kafirci ne. Allah ya ce,

﴿ وَمَا يُعَلِّمَانِ مِنۡ أَحَدٍ حَتَّىٰ يَقُولَآ إِنَّمَا نَحۡنُ فِتۡنَةٞ فَلَا تَكۡفُرۡۖ ﴾ [البقرة: ١٠٢].

(Ba sa koya wa kowa, har sai sun ce da shi, "Mu fa fitina ne, kada ka kafirta).

Kuma Allah ya ce,

﴿ وَلَا يُفۡلِحُ ٱلسَّاحِرُ حَيۡثُ أَتَىٰ ٦٩ ﴾ [طه: ٦٩].

(Kuma mai sihiri ba zai rabauta ba, ko ta ina ya zo).

Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Ku nisanci abubuwa bakwai masu halakarwa." Sai aka ce, "Waɗanne ne, ya Ma'aikin Allah?" Sai ya ce, "Haɗa Allah da wani, da tsafi, da kisan kan da Allah ya haramta, sai da gaskiya, da cin dukiyar maraya, da cin riba, da tserewa daga fagen yaƙi, da yin ƙazafi ga tsararrun mata, gafalallu, muminai." [Bukhari da Muslim].

An karɓo daga A'isha (RA) ta ce, wasu mutane sun tambayi Manzon Allah (ﷺ) a kan bokaye. Sai ya ce, "Su ba komai ba ne." Sai suka ce, "Ya Ma'aikin Allah! Suna ba mu labari wani lokaci, na wani abu, sai ya zamo gaskiya." Sai ya ce, "Wannan kalma ce ta gaskiya, wadda aljani yake wabto ta, sai ya raɗa wa mai jiɓintarsa, sai su kuma bokaye su gauraya ƙarya guda ɗari da ita." [Bukhari ya rawaito shi].

Kuma Manzon Allah (ﷺ) ya yi bara'a daga wanda ya yi camfi, ko aka yi masa camfi, ko ya yi bokanci, ko aka yi masa bokanci, kamar yadda Imran ibn Husain ya rawaito. Ya ce, "Wanda ya yi camfi, ko aka yi masa camfi, ba ya tare da mu; ko ya yi bokanci, ko aka yi masa bokanci, ko ya yi tsafi, ko aka yi masa tsafi. Duk wanda ya je wajen boka, ya gaskata shi da abin da yake faɗa, haƙiƙa ya kafirta daga abin da aka saukar wa Muhammad." [Bazzar ya rawaito shi, da salsala ingantacciyya].

Hukuncin mai tsafi da ɗan tsibbu, shi ne a fille musu kai da takobi, kamar yadda wasu daga cikin sahabban Manzon Allah (ﷺ) suka yi.

Ya ku musulmai! Ku sani, illar da waɗannan fasiƙai, bokaye da 'yan tsibbu suke yi a cikin al'umma, tana da yawa. Daga ciki akwai abubuwa kamar haka:

Na farko, zare imani ga waɗanda suke zuwa wajensu, waɗanda suke gaskata su cikin abin da suka faɗa, kamar yadda hadisi ya gabata a kan haka.

Na biyu, yawaita kisa da yaɗa shi a cikin al'umma. Duk abin da muke gani, ko muke ji na ɓatan wane ko wance, ko ganin ƙaburbura a tone, ko ganin wasu sassan ɗan Adam, ana sayar da su, duk wannan sakamakon aikin 'matsafa ne da bokaye, waɗanda suke umartar mabiyansu da waɗannan abubuwa.

Na uku, yaɗa neman mata da fajirci a tsakanin mutane. Sau da yawa boka yakan sadu da mace, kafin ya yi mata aikin da ta zo nema. Ta sanadiyyar haka, ya lalata wa mijinta ita, kuma ya buɗe mata ƙofar ɓarna da fasadi a bayan ƙasa.

Na huɗu, cin dukiyar mutane a banza. Saboda duk wani abu da boka ko ɗan tsibbu yake karɓa, a maimakon aikinsa da tsafinsa, ɓarna ne, kuma datti ne. Abdullahi ibn Mas'ud ya rawaito cewa, Manzon Allah (ﷺ) ya haramta kuɗin kare da sadakin karuwa da ladan boka. [Bukhari ya fitar da shi].

Na biyar, ɓatar da mutane, da ɗora su a kan tafarkin fasiƙanci, ta hanyar hana su bautar Allah: Wasu a hana su sallah, ko gabaɗaya, ko wani yanki nata; wasu wankan janaba; wasu a hana su alheri, a umarce su da suk wani munkari.

Na shida, suna jawo azabar Allah da fushinsa ga al'ummah. Zainab bint Jahsh, Allah ya yarda da ita, ta ce, "Ya Ma'aikin Allah! Yanzu za a halakar da mu, a cikinmu akwai mutanen ƙwarai?" Ya ce, "Idan datti ya yi yawa!"[Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi]. Shin akwai dattin da ya fi na matsafa?

Na bakwai, asarar duniya da lahira. Allah ya ce,

﴿وَلَا يُفۡلِحُ ٱلسَّاحِرُ حَيۡثُ أَتَىٰ ٦٩﴾ [طه: ٦٩].

Ma'ana: "Matsafi ba zai taɓa rabauta ba, ta ko ina ya ɓullo.".

Sheikhul Islam Ibn Taimiyya ya ce, "Zuzzurfan nazari ya tabbatar da cewa, 'yan duba ba sa rabauta, duniya da lahira". [Majmu'ul Fatawa].

Wannan kaɗan kenan daga cikin illolin bokaye da 'yan tsibbu a cikin al'umma. Saboda haka, ya zama wajibi a kan malamai da ɗalibai, su tsaya wajen bayanin illarsu a cikin al'umma, kuma ya zama wajibi a kan shugabanni, su tsayar musu da haddi, kamar yadda shari'a ta tanada, tun kafin ranar nadama ta zo.

Allah ya yi albarka gare ku, tare da ni, cikin Alƙur'ani mai girma, ya kuma amfanar da ni, da ku, da abin da yake cikinsa na ayoyi da wa'azi, mai azanci. Lallai shi majiɓincin haka ne, kuma mai iko a kansa.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah, Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga Annabi (ﷺ).

Ya ku bayin Allah! Ya zama wajibi a kanmu gabaɗaya, mu dogara ga Allah Ta'ala, shi ne mamallakin komai da komai. Duk abin da Allah ya bayar, ba mai hanawa, kuma duk abin da Allah ya hana, babu mai bayar da shi. Allah Ta'ala ya shar'anta mana roƙon sa, da neman biyan buƙatunmu a wajensa, kuma ya huwace mana hanyoyi da shari'a ta yarda da su, wanda za mu riƙe su, don mu cimma

burinmu. Daga cikinsu, akwai roƙonsa, da neman biyan buƙata a wajensa. Duk wanda ya roƙi Allah da gaskiya da ikhlasi, lallai Allah ba zai tozarta aikinsa ba, Allah Ta'ala kusa yake, kuma mai amsa addu'a ne. Shi ne ya arzuta tsuntsu a sama, da kifi a cikin teku, kuma shi ne ya hore duk wani abu da muke gani a sararin duniya. Allah ya ce,

﴿ ٱللَّهُ ٱلَّذِى خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ وَأَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً فَأَخْرَجَ بِهِۦ مِنَ ٱلثَّمَرَٰتِ رِزْقًا لَّكُمْ ۖ وَسَخَّرَ لَكُمُ ٱلْفُلْكَ لِتَجْرِىَ فِى ٱلْبَحْرِ بِأَمْرِهِۦ ۖ وَسَخَّرَ لَكُمُ ٱلْأَنْهَٰرَ ﴿٣٢﴾ وَسَخَّرَ لَكُمُ ٱلشَّمْسَ وَٱلْقَمَرَ دَآئِبَيْنِ ۖ وَسَخَّرَ لَكُمُ ٱلَّيْلَ وَٱلنَّهَارَ ﴿٣٣﴾ وَءَاتَىٰكُم مِّن كُلِّ مَا سَأَلْتُمُوهُ ۚ وَإِن تَعُدُّوا۟ نِعْمَتَ ٱللَّهِ لَا تُحْصُوهَآ ۗ إِنَّ ٱلْإِنسَٰنَ لَظَلُومٌ كَفَّارٌ ﴿٣٤﴾ ﴾ [إبراهيم: ٣٢ – ٣٤].

(Allah wanda ya halicci sama da ƙasa, kuma ya saukar da ruwa daga sama, sannan ya fitar da 'ya'yan itatuwa da shi, don arziki gare ku, kuma ya hore jiragen ruwa, don su gudana a cikin teku, da izininsa, ya kuma hore muku ƙoramu. Kuma ya hore muku rana da wata masu gudu ba ƙaƙƙautawa, kuma ya hore muku dare da yini. Kuma ya ba ku daga duk abin da kuka roƙe shi. Kuma idan za ku lissafa na'imar Allah to ba za ku iya ƙididdige ta ba. Lallai ɗan Adam mai yawan zaluntar kansa ne, mai yawan butulci).

Saboda haka, ya kai mai neman arziki, neme shi a wajen Allah, shi ne mai arzutawa, ma'abocin ƙarfi. Allah ya ce,

﴿ فَٱبْتَغُوا۟ عِندَ ٱللَّهِ ٱلرِّزْقَ وَٱعْبُدُوهُ وَٱشْكُرُوا۟ لَهُۥٓ ۖ إِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿١٧﴾ ﴾ [العنكبوت: ١٧].

(Ku nemi arziki a wajen Allah, kuma ku bauta masa, kuma ku gode masa, zuwa gare shi za ku koma).

Ya ke mai neman haihuwa! Kin manta da adu'ar Annabi Zakariyya, yayin da ya roƙi Ubangijinsa? Ya ce,

﴿ هُنَالِكَ دَعَا زَكَرِيَّا رَبَّهُۥ ۖ قَالَ رَبِّ هَبْ لِى مِن لَّدُنكَ ذُرِّيَّةً طَيِّبَةً ۖ إِنَّكَ سَمِيعُ ٱلدُّعَآءِ ﴿٣٨﴾ ﴾ [آل عمران: ٣٨].

(Ya Ubangiji! Ka ba ni zurriya ta gari daga gare ka, lallai kai mai jin adu'a ne).

Ya kai mai neman mulki, ko ɗaukaka, ko wani abu daban, neme shi wajen Allah, domin shi kusa yake, kuma yana amsa adu'ar bayi. Allah ya ce,

﴿ وَإِذَا سَأَلَكَ عِبَادِى عَنِّى فَإِنِّى قَرِيبٌ ۖ أُجِيبُ دَعْوَةَ ٱلدَّاعِ إِذَا دَعَانِ ۖ فَلْيَسْتَجِيبُوا۟ لِى وَلْيُؤْمِنُوا۟ بِى لَعَلَّهُمْ يَرْشُدُونَ ﴿١٨٦﴾ ﴾ [البقرة: ١٨٦].

(Idan bayina suka tambaye ka game da ni, ka ce ni kusa nake, ina amsa adu'ar mai roƙo, idan ya roƙe ni. Su amsa kira na, kuma su yi imani da ni, ko sa shiriya).

Ya zama wajibi a kanmu, taron 'yan uwa, mu yi taimakekeniya a tsakaninmu, don ceto al'umma daga sharrin waɗannan fasiƙai, fajirai. Kada mu ba su hayar gida ko ɗaki ko shago. Kuma kada mu taimake su cikin abin da suke yi na tsafi da tsibbu, kada mu rufa musu asiri. A'a, mu yi abin da yake wajibi a kanmu, na umarni da kyakkyawa, da hani daga mummuna. Allah yana cewa,

﴿ وَتَعَاوَنُوا۟ عَلَى ٱلْبِرِّ وَٱلتَّقْوَىٰ ۖ وَلَا تَعَاوَنُوا۟ عَلَى ٱلْإِثْمِ وَٱلْعُدْوَٰنِ ﴾[المائدة: ٢].

"Ku yi taimakekeniya a kan aikin nagarta da tsoron Allah, kada ku yi taimakekeniya a kan laifi da ƙetare iyaka".

Sheikhul Islam Ibn Taimiyya yana cewa, "Haƙiƙa mun yi bayani da abin da muka ambata cewa, ladan da aka karɓa a kan haka - wato bokanci - da kyauta da

sadaka, haram ne a kan mai bayarwa, da mai karɓa, kuma haramun ne ga masu gidaje da wakilai, su ba da hayar shaguna ko waninsu ga waɗannan kafirai, don su yi irin wannan amfani da su, idan zatonsu ya yi rinjaye kan cewa, abin da za su yi da su kenan. Kuma wajibi ne a kan shugabanni, da duk wanda yake da iko, su yi aiki don kawar da haka, da kuma hana su zama shaguna, ko kan hanya, ko kuma shiga gidajen mutane. Idan kuwa shugaba bai aikata haka ba, to faɗin Allah ya hau kansu, inda yake cewa,

Ma'ana» "Su, su kasance ba sa hana junasu kan mummunan aiki da suka aikata».

Da kuma faɗarsa,

﴿ لَوۡلَا يَنۡهَىٰهُمُ ٱلرَّبَّٰنِيُّونَ وَٱلۡأَحۡبَارُ عَن قَوۡلِهِمُ ٱلۡإِثۡمَ وَأَكۡلِهِمُ ٱلسُّحۡتَۚ لَبِئۡسَ مَا كَانُواْ يَصۡنَعُونَ ٦٣ ﴾

[المائدة: ١٣].

(Menene ya hana mutane na Allah da malamai ba za su hana su faɗar laifi ba da cin rashawa. Tir da abin da suke aikatawa).

Kowa ya yadda da cewa, su waɗannan tsinannun, suna faɗar laifi, kuma suna abin da bai halatta ba. Kuma ya tabbata daga Manzon Allah (ﷺ), ya ce, "Idan mutane suka ga mummuna, ba su sauya shi ba, to Allah ya kusa ya game su da uƙuba daga gare shi." Wane munkari ne ya fi aikin waɗannan gurɓatattu, sarin masu mulki, maƙiya Manzanni, 'ya'yan sabi'awa, masu bautar taurari.

Ku ji tsoron Allah, ya bayin Allah, kuma ku tuba gabaɗaya, ku nemi gafararsa, ku dogara gare shi, shi kaɗai cikin dukkan abubuwa, ku ƙyale waɗannan abubuwa, ku nesance su, ku lazimci ɗa'ar Allah da Manzonsa, ku kare addininku da aƙidarku, domin a yau, aiki ne babu hisabi, gobe kuma, hisabi ne babu aiki.

ZAKKA: HIKIMOMINTA DA HUKUNCE-HUKUNCENTA

Manufofin huɗubar

- Bayanin hukuncin zakka da matsayinta a Musulunci.
- Bayanin abin da wannan shari'a ta ƙunsa na hikimomi masu ƙayatarwa.
- Bayanin hukunce-hukuncen da suka rataya da nau'o'in dukiyoyin da ake fitar da zakka.
- Bayanin guraren da ake sarrafar da zakka, da kirdado wajen karɓar ta da rabar da ita.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma mua neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan aiyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar dashi, wanda kuma ya atar babu mai shiryar da shi, kuma ina shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai allah, shi kaɗai ne bashi da abokin taraiya, kuma ina shaidawa cewa Annabi Muhammad bawansane manzonsane, (Yaku waɗanda kuka bada gaskiya kuji tsoron Allah yadda ya cancanta aji tsoronsa, kada ku mutu face kuna Musulmi). (Yaku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicce ku daga rai guda ɗaya kuma ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga gare su (su biyu) kuji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya dashi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku waɗanda suka yi imani kuji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku aiyukanku, kuma ya gafarta muku zunubanku. Wanda ya bi Allah da manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawun shiriya shiriyar Annabi Muhammadu (ﷺ) kuma mafi sharrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Bayan haka:

Ya ku bayin Allah, haƙiƙa yana daga hikimar Ubangiji mai girma, cewa ya sassaɓa tsakanin bayinsa a cikin halayensu da arziƙinsu, haƙiƙa Ubangijinku Mai hikima ne Masani. Sai ya yalwatawa sashinsu arziƙi, ya sanya sashi koma bayan haka. Kuma shi ne mai hikima Masani.

﴿ قُلۡ إِنَّ رَبِّي يَبۡسُطُ ٱلرِّزۡقَ لِمَن يَشَآءُ وَيَقۡدِرُ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعۡلَمُونَ ٣٦ ﴾ [سبأ: ٣٦].

"Ka ce, haƙiƙa Ubangiji yana yalwata arziƙi, ga wanda ya so, kuma yana ƙuntatawa (ga wanda ya so), sai dai da yawan mutane ba su sani ba."

Ya jarrabi wasu da dukiya, sai ya yalwata musu ita, Ya ba su dangogin dukiya. Ya jarrabi wasu da talauci. Allah ya ce,

﴿ فَأَمَّا ٱلۡإِنسَٰنُ إِذَا مَا ٱبۡتَلَىٰهُ رَبُّهُۥ فَأَكۡرَمَهُۥ وَنَعَّمَهُۥ فَيَقُولُ رَبِّيٓ أَكۡرَمَنِ ١٥ وَأَمَّآ إِذَا مَا ٱبۡتَلَىٰهُ فَقَدَرَ عَلَيۡهِ رِزۡقَهُۥ فَيَقُولُ رَبِّيٓ أَهَٰنَنِ ١٦ كَلَّا ﴾[الفجر: ١٥ – ١٧].

“Amma mutum idan Ubangijinsa ya jarrabe shi, sai ya girmama shi, ya yi masa ni’ima, sai ya ce, Ubangijina ya girmama ni. Amma idan ya jarrabe shi sai ya ƙuntata masa arziƙinsa sai ya ce, Ubangijina ya tozarta ni. A’a, ba haka lamarin yake ba…).

Ai ba duk wanda Allah ya yalwatawa ba hakan yake nuna ya fi sonsa. Kuma ba duk wanda aka ƙuntatawa ba, hakan yana nufin ba ya son sa, sai dai ita duniya ce, Allah yana ba da ita ga wanda ya ga dama, kuma ya hana wasu daga cikin bayinsa, kuma Yana da ilimi da hikima a cikin hakan.

Ya jarrabi talakawa da mawadata, ya jarrabi mawadaci da dukiya, domin ya ga shin wannan dukiyar za ta zama dalilin godewarsa, ga ni’imomin Ubangiji, da tsayuwa da haƙƙinsa? Kuma ya jarrabi talaka don ya ga shin zai zama daga masu haƙuri masu yarda, ko kuwa zai kasance daga cikin masu fushi?

ya dasa son dukiya a cikin zukata, Allah ya ce,

﴿ وَتُحِبُّونَ ٱلۡمَالَ حُبّٗا جَمّٗا ٢٠ ﴾ [الفجر: ٢٠].

(Kuma kuna son dukiya so mai yawa).

Ita wannan dukiya ni’ima ce ga wasu mutane, kuma musiba ce ga wasu. Ni’ima ce ga wanda ya karɓe ta da haƙƙinta, kuma kashe ta inda ya kamata, ya san cewa Allah yana da haƙƙi a cikin wannan dukiyar, ya ba da wannan haƙƙin cikakkiyar. Wannan, dukiya ta zama ita ce dalilin nagarta da daidaituwar halisa, da rigegeniyarsa a cikin aiki na gari. Wasu kuwa dukiya ta zamo musu dalilin tsaurin kai, da taƙama da fankama, da ruɗuwa da kawunansu. Sai suka hana haƙƙoƙin Allah da ya wajaba a cikin dukiyarsu. Sai ba su ba da haƙƙin dukiyar ba, sai ma dukiyar ta zamo sababin azabtar da su.

﴿ وَلَا تُعۡجِبۡكَ أَمۡوَٰلُهُمۡ وَأَوۡلَٰدُهُمۡۚ إِنَّمَا يُرِيدُ ٱللَّهُ أَن يُعَذِّبَهُم بِهَا فِي ٱلدُّنۡيَا وَتَزۡهَقَ أَنفُسُهُمۡ وَهُمۡ كَٰفِرُونَ ٨٥ ﴾ [التوبة: ٨٥].

(Kada dukiyarsu ta ƙayatar da kai, ko ‘ya’yansu, kaɗai Allah yana nufin ya azabtar da su da ita a rayuwr duniya, kuma rayukansu su fita alhali suna kafirai).

Saɓanin wanda ya ruɗu da kansa, ya ce:

﴿ قَالَ إِنَّمَآ أُوتِيتُهُۥ عَلَىٰ عِلۡمٍ عِندِيٓۚ ﴾[القصص: ٧٨].

(Ya ce, kawai an ba ni ita ne saboda wani sani da nake da shi).

Ya kai musulmi, haƙiƙa Allah Mabuwayi, ya wajabta wa mawadaci haƙƙi da zai ba wa talakawa, sanna haƙƙi ga roƙo da ma wanda ba ya roƙo. Allah ya wajabta wani haƙƙi a dukiyar mawadata, da za su ba wa ‘yan’uwansu talakawa, don su tallafe su da shi, kuma ya sanya wannan rukuni ne daga rukunan musulunci, domin zakka ita ce rukuni na uku daga rukuna musulunci da aka gina shi a kansu. “An gina musulunci a kan abubuwan biyar: Shaidawa babu abin bautawa da gaskiya bisa cancanta sai Allah, kuma cewa, Annabi Muhammadu Manzon Allah ne,

da tsayar da salla, da ba da zakka, da azumin watan Ramadana, da Hajjin ɗakin Allah.” Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi, daga Abdullah ɗan Umar, Allah Ya ƙara yarda a gare shi.

A cikin littattafai Bukhari da Muslim, daga ɗan Abbas, Allah ya yarda da su, faɗin Manzon Allah (ﷺ), ga Mu’azu ɗan Jabal, “Ka sanar da su cewa Allah ya wajabta musu sadaka da za a karɓa daga mawadatansu a ba wa talakawansu.

Nassoshin Alƙur’ani da sunna sun tabbatar da kasancewar zakka rukuni ce na Musulunci, da kuma bayanin muhimmancinta. Allah Ta’ala ya ce:

﴿ وَمَآ أُمِرُوٓاْ إِلَّا لِيَعۡبُدُواْ ٱللَّهَ مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ حُنَفَآءَ وَيُقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَيُؤۡتُواْ ٱلزَّكَوٰةَۚ وَذَٰلِكَ دِينُ ٱلۡقَيِّمَةِ ٥ ﴾ [البينة: ٥].

“Ba a umarce su ba face su bautawa Allah, suna masu tsarkake addini a gare shi, suna masu bin miƙaƙƙen addini, kuma su tsai da sallah su ba da zakka. Wannan shi ne addinin hanya miƙaƙƙiya.”

Ya kai musulmi, haƙiƙa, zakka jarraba ce da gwaji wadda Allah kan jarrabi mawadata da ita. Mai gaskiya a imaninsa zai kuɓuta daga wannan jarrabawa, ta hanyar fitar da zakka a cikin daɗin rai. Yana mai sakankancewa da wajabcinta, yana mai ƙudurce haka, yana ba da ita domin biyayya ga Allah da godewa falalarsa da ni’imominsa. Allah Ta’ala ya ce:

﴿ خُذۡ مِنۡ أَمۡوَٰلِهِمۡ صَدَقَةٗ تُطَهِّرُهُمۡ وَتُزَكِّيهِم بِهَا وَصَلِّ عَلَيۡهِمۡۖ إِنَّ صَلَوٰتَكَ سَكَنٞ لَّهُمۡۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ١٠٣ ﴾ [التوبة: ١٠٣].

(Ka karɓi zakka daga dukiyoyinsu wadda za ka tsarkake su, ka tsaftace su da ita, kuma ka yi addu’a a gare su, haƙiƙa addu’arka nutsuwa ce a gare su, kuma Allah Mai ji ne, Masani).

Allah yana umartar Annabinsa Muhammadu da karɓar zakka daga dukiyoyin mawadata, “Ka karɓi zakka daga dukiyoyinsu.” Allah Ta’ala Ya bayyana hikimarsa ta wajabatata, da faɗinSa: “Da za ka tsarkake su, ka tsaftace su da ita.”

Don haka ke nan zakka tsarki ne ga mai yinta. Tana tsarkake zuciyarsa daga cutar ƙwauro da rowa, tana sanya shi ya yi kyauta ya yi alheri. Kuma tana tsaftace dukiya daga daudarta da ƙazantarta. Domin dukiyar da ba a fitar da zakkarta ba, takan kwashi daudɗa da ƙazanta, kuma babu abin da zai tsaftace ta sai zakka. Kuma ita zakka tsarki ce ga zuciya, domin tana ƙarfafa iman. Domin mai fitr da ita yana rinjayar fizge-fizgen son rai da sha’awoyin zuciya da wasi-wasin shaiɗan. Ya fitar da ita ne don biyayya ga Allah yana mai turmusa hancin maƙiyin Allah. Allah ya ce,

﴿ ٱلشَّيۡطَٰنُ يَعِدُكُمُ ٱلۡفَقۡرَ وَيَأۡمُرُكُم بِٱلۡفَحۡشَآءِۖ وَٱللَّهُ يَعِدُكُم مَّغۡفِرَةٗ مِّنۡهُ وَفَضۡلٗاۗ وَٱللَّهُ وَٰسِعٌ عَلِيمٞ ٢٦٨ ﴾ [البقرة: ٢٦٨].

(Shaiɗan yana yi muku alƙawarin talauci, kuma yana umartar ku da alfasha, Allah kuwa yana yi muku alƙawarin gafara daga gare shi, da falala, kuma Allah Mai yalwar falala ne, Masani).

Kuma zakka tana haɓaka dukiya, domin dukiyar da aka fitarwa zakka tana haɓaka, kuma Allah yana saukar da albarka a cikinta. Ya zo a cikin Sahihu Muslim daga Abu Huraira, Annabi (ﷺ) ya ce, “Babu wata dukiya da za ta tawaya saboda fita da zakka.”

Ya kai ɗan’uwana musulmi, ka ba da zakkar dukiyarka kana mai sakin zuciyarka. Ka ba da zakkar dukiyarka, kana mai ƙudurce wajabcinta a musulunci. Ka ba da zakkar dukiyarka domin biyayya ga Allah da Manzonsa. Ka ba da zakkar dukiyarka don dukiyarka ta wanzu a gare ka, albarkarta ta ƙaru, alherinta ya yawaita, bala’i ya yaye daga gare ka.

Ya ɗan’uwana Musulmi! Ka dubi ni’imar da Allah ya yi maka na wannan dukiya ba ka same ta ba don ƙarfin jikinka, ko basirar ra’ayinka. Tsantsar falala ce, kawai ta Allah da karamcinsa, da baiwarsa da kyautatawarsa a gare ka. Dubi wannan dukiya, sanna ka dubi zakkarta, za ka ga zakkar rubu’in ushurinta ne (Rabin rabin ɗaya bisa goma ne) ko a ce, biyu da rabi a cikin ɗari (2.5%). Ya ba ka da yawa, amma ya gamsu da kaɗan daga wajenka. Sannan wannan ɗan kaɗan ɗin ma amfaninsa kanka zai dawo duniya da lahira.

Ya kai Musulmi! Ka yi kwaɗayi a bisa fitar da zakka, ka yi kwaɗayi a bisa ƙididdige dukiya, ka tantance wajen lissafin, ka lissafe ta a duniya kafin a lissafa maka ita a lahira.

﴿ يَوۡمَ لَا يَنفَعُ مَالٞ وَلَا بَنُونَ ٨٨ إِلَّا مَنۡ أَتَى ٱللَّهَ بِقَلۡبٖ سَلِيمٖ ٨٩ ﴾ [الشعراء: ٨٨ – ٨٩].

“Ranar da dukiya da ‘ya’ya ba za su yi amfani ba, sai wanda ya zo wa Allah da zuciya lafiyayyiya.”

Ya kai ɗan’uwana Musulmi, ka fitar da zakka da niyya da nufi mai kyau, domin Allah, don ayyukanka sun ta’allaƙa ne a bisa niyya. Dole ne sai an yi niyya a yayin fitarwar. Niyyar ba da wannan wajibi mai girma. Idan ka fitar da ita to ka yi bushara da alheri da albarka daga Allah, da lada mai girma a ranar gamuwa da Ubangijinka.

Ya kai Musulmi, haƙiƙa Allah Mai girma da ɗaukaka ya wajabta zakka a dangogin dukiyoyi. Ya wajabta zakka da farko a dangogin abubuwan da kan fito daga ƙasa, na hatsi da kayan marmari, Allah ya ce,

﴿ وَءَاتُواْ حَقَّهُۥ يَوۡمَ حَصَادِهِۦ ﴾[الأنعام: ١٤١].

(Kuma ku ba da haƙƙinsa a ranar girbinsa).

Da faɗinsa:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَنفِقُواْ مِن طَيِّبَٰتِ مَا كَسَبۡتُمۡ وَمِمَّآ أَخۡرَجۡنَا لَكُم مِّنَ ٱلۡأَرۡضِۖ وَلَا تَيَمَّمُواْ ٱلۡخَبِيثَ مِنۡهُ تُنفِقُونَ ﴾ [البقرة: ٢٦٧].

(Ya ku waɗanda suka yi imani ku ciyar daga daɗaɗan abin da kuka tsururuta, daga kuma abin da muka fitar muku daga ƙasa. Kada ku nufi lalatacce a cikinsa kuna ciyarwa).

Ya sanya sharaɗin wannan hatsi ya kai wusuƙi biyar, wato abin da ya yi daidai da kilo ɗari tara. (900kg). ya wajabta usuhuri a cikinsa (Ɗaya bisa goma) na hatsi da kayan marmari, idan ba a wahala a wajen shayar da ita shukar ba, (wato kamar

shukar damina). Kuma ya sanya rabin Ushurinta (ɗaya bisa ashirin), idan an shayar da ita da wahala (kamar ta hanyar amfani da ban-ruwa). Kuma shi Maɗaukakin Sarki bai wajabta zakka a kayan lambu da kayan marmari ba. Saboda su ba a ajiyar su, su abincin lokacinsu ne, saɓanin hatsi da ‘ya’yan itatuwa wanda ake aunawa kuma ake ajiyarsu domin su sukan daɗe tsawon shekara.

Ya kai musulmi, haka nan Allah Ya wajabta ta a dabbobin ni’ima kamar raƙuma da shanu, da awaki, idan su masu fita kiwo ne. Suna kiwo a mafi yawancin lokacin shekara ta hanyar cin ciyayi, ba a kawo musu ciyawa da ruwa, an tandar masu komai. To idan haka dabba take, zakka ta wajaba a cikinta. Mafi ƙarancin nisabin raƙuma, shi ne biyar. Nisabin awaki da tumaki arba’in. Nisabin shanu, kuwa talatin.

Ita kuwa dabbar da ake kawo mata ciyawa da ruwa a mafi yawan lokutan shekara babu zakka a cikinta. Sai dai idan mai ita yana tanadinta ne don kasuwanci. Ma’ana, ta zama wata haja ce ta kasuwanci, wannan ana yi mata ƙima duk shekara, a fitar da zakkarta rubu’in Ushurinta. Su kuwa dabbobin gonaki waɗanda ba kasuwanci aka yi da su ba, kuma ba fita kiwo suke yi ba, sai dai masu su ne suke ci da su. Don su riƙa cin namansu, su riƙa shan nononsu, to babu zakka a cikinsu.

Allah Ya wajaba zakka a cikin kadarorin kasuwanci. Kadarorin kasuwanci kuwa su ne duk abin da musulmi ya tanada don saye da sayarwa na hajoji daban daban. Kamar abinci, ko tufafi, ko abin hawa da makamantansu, to za mu yi masa ƙima a wata fitar da zakka, mu fitar da rubu’in Ushurinsa, na farashinsa, abinci ne ko tufafi ko kayan kwanuka ko motoci, ko safaya fat, ko filaye duk waɗannan suna shiga cikin kadarori. Za mu yi masa farashi a ƙarshen shekara, sai a duba farashin abu a yanzu, farashin ya ƙaru ko ya ragu. Da musulmi zai sai filotin ƙasa don kasuwanci, sai filotin ya shekara, za a yi masa farashi a ƙarshen kowace shekara, a kalli, farashinsa na yanzu, ya biya rubu’in Ushurin farashin da aka yi masa. Da a ce farashin sayen wajen, zai zama, filoti ɗaya dubu ɗari, amma a ƙarshen shekara, ya zama naira dubu ɗari biyar, to za mu ce, zakkarsa za ta kama a kan dubu ɗari biyar. Za a fitar da rubu’in Ushurin farashinsa. Da kuma a ce, farashin, zai faɗi zuwa dubu hamsin, to za mu ce zakkar tana kan naira dubu hamsin ɗin, in hakan ya kai nisabi, haka Allah ya shar’anta.

Zinare da azurfa, Allah ya wajabta zakka a cikinsu, domin su ne ma’aunin dukiya. Allah Ta’ala ya ce:

﴿ وَٱلَّذِينَ يَكۡنِزُونَ ٱلذَّهَبَ وَٱلۡفِضَّةَ وَلَا يُنفِقُونَهَا فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ فَبَشِّرۡهُم بِعَذَابٍ أَلِيمٖ ٣٤ يَوۡمَ يُحۡمَىٰ عَلَيۡهَا فِي نَارِ جَهَنَّمَ فَتُكۡوَىٰ بِهَا جِبَاهُهُمۡ وَجُنُوبُهُمۡ وَظُهُورُهُمۡۖ هَٰذَا مَا كَنَزۡتُمۡ لِأَنفُسِكُمۡ فَذُوقُواْ مَا كُنتُمۡ تَكۡنِزُونَ ٣٥ ﴾ [التوبة: ٣٤ – ٣٥].

(Waɗannan da suke taskance zinare da azurfa, kuma ba sa ciyar da ita a cikin tafarkin Allah, ka yi musu bushara da azaba mai raɗaɗi. Ranar da za a yi msu lalas da ita a wutar Jahannama, sai a ƙona goshinansu da gefunansu da bayansu da ita, a ce, wannan shi ne abin da kuka taskake ga kawunanku, to ɗanɗani abin da kuka kasance kuna taskakewa).

Don haka dai ana fitar da zakkar kuɗaɗe guda biyu, zinare da azurfa, da takardun kuɗi da suke matsayinsu, kuma suka ɗau hukuncinsu wajen ciniki da ma'amala. Ana fitar da rubu'in Ushurinta.

Ya kai musulmi, hannayen jari, a kamfanoni mabambanta sun kasu kashi biyu. Akwai hannayen jari da ake kasuwancinsu, wanda musulmi yake neman riba da su. Yake fitar da su, don sayarwa a lokacin da ake nemansu, ya ɓoye yayin da ba a buƙata. Wannan ana zakkarsu a ƙarshen kowace shekara, za a fitar da ƙimarsu ta lokacin, domin suna matsayin kuɗin da ke hannunka ne.

Su kuwa hannayen jari da aka sanya su kamar ajiya ce, ba a sai da su, ko a saya, sai dai a amfana daga ribarsu, to idan aka karɓi ribarsu ta shekara sai ka fitar da zakkarsu, idan kuwa ki cinye ribar to babu zakka su a cikinsu.

Su kuwa gidaje da filaye wanda ake hayarsu zakka tana wajaba ne a cikinsu, kawai daga sanda ake ƙulla yarjejeniyar hayar idan ka karɓi kuɗin haya a ƙarshen shekara to ka ba da zakkar ta. In kuwa kana karɓa duk wata shida ne, ka kashe b ka ajiyewa, to babu zakka a cikinta. Amma idan kana karɓar ta a ƙarshen shekara ne, ko kana karɓa ka ajiye, to za ka ba da zakkarta. In kuwa kaɗan-kaɗan kake karɓa ka cinye to babu zakka a kai.

Gidanka da kake zaune a cikinsa, da motarka da kake shiga, duk wannan ba zakka a cikinsu. Domin Annabi (ﷺ) yana cewa: "Babu zakka a kan Musulmi a cikin bawansa da dokinsa." Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi daga Abu Huraira.

'Yan uwa musulmi, wannan shi ne abin da za faɗa, ina nemawa kaina da ku da sauran musulmi gafarar Allah, ku nemi gafararsa, lalle shi mai yawan gafara ne mai jin ƙai.

Huɗuba Ta Biyu

Yabo daddaɗa mai albarka ya tabbata ga Allah, kamar yadda Ubangijinmu yake so, kuma ya yarda da shi. Ina shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Yabo na shi ne a duniya da lahira. Kuma ina shaidawa cewa Annabi Muhammadu, bawansa ne, kuma Manzonsa ne, ya aiko shi da rahama da shiriya. Allah ya yi tsira da aminci da albarka a gare shi, da alayensa zaɓaɓɓu da sahabbansa masu girma da tabi'ai, da waɗanda suka bi su da kyautatawa, har zuwa ranar sakamako.

Bayan haka: Ya ku musulmai, haƙiƙa zakka farilla ce, kamar yadda Allah Ya ambata a cikin littafinsa ya ce:

﴿ إِنَّمَا ٱلصَّدَقَٰتُ لِلۡفُقَرَآءِ وَٱلۡمَسَٰكِينِ وَٱلۡعَٰمِلِينَ عَلَيۡهَا وَٱلۡمُؤَلَّفَةِ قُلُوبُهُمۡ وَفِي ٱلرِّقَابِ وَٱلۡغَٰرِمِينَ وَفِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱبۡنِ ٱلسَّبِيلِۖ فَرِيضَةٗ مِّنَ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٞ ٦٠ ﴾ [التوبة: ١٠].

(Haƙiƙa zakka haƙƙi ne na mabuƙata, da miskinai, da masu aiki a kanta, da waɗanda ake son karkato da zuciyarsu (ga musulunci) da wajen fansar bayi, da waɗanda ake bi bashi, da wajen ɗaukaka kalmar Allah, da ɗan tafarki. Farilla ce daga Allah, kuma Allah ya tabbata masani, Mai hikima).

Allah bai ɗora rabon zakka a kan wani Annabi ko mala'ika ba, a'a, Shi ya jiɓinci raba ta da kansa.

Ya ku musulmai! Ku ji tsoron Allah a cikin zakkarku. Ya kai musulmi! Ka sani kai abin amincewa ne a kanta. Don haka ka isar da amana zuwa ga waɗanda suka cancanta:

﴿ إِنَّ ٱللَّهَ يَأۡمُرُكُمۡ أَن تُؤَدُّواْ ٱلۡأَمَٰنَٰتِ إِلَىٰٓ أَهۡلِهَا ﴾ [النساء: ٥٨].

(Haƙiƙa Allah yana umartar ku da ku mayar da amana zuwa ga masu ita)."

Faƙirai da miskinai waɗanda ba su da komai, ko suke da abin da ya gaza wadatar da su buƙatunsu na lalura. Ba su da wani tsayayyen albashi ko wata kadara mai kawo musu abin masarufi ko tsayayyar sana'a, ko wani ya ɗauki nauyin ciyar da su. Sai a ba su abin da zai ishe su shekar guda daga zakka. A ba faƙiri da miskini gwargwadon abin da zai ishe shi. A taimakawa mai neman aure game da aurensa. Domin wannan yana cikin muhimman buƙatu. A ba wa faƙiri da miskini abin da zai ishe su, wannan idan zatonka ya rinjaya a kan shi ya fi cancantarta. Idan kuwa ka ga alamomin wadata a jikinsa, ko alamomin ƙarfi da karsashi, to ka yi masa nasiha, ka yi masa gargaɗi, domin wasu mutane sun zo wa Annabi (ﷺ) suna tambayarsa, ya ba su zakka, sai ya dube su, sai ya gan su ƙarfafa. Sai ya ce, "In kuna so in ba ku, amma ku sani babu haƙƙi a cikin zakka ga mawadaci, ko ƙaƙƙarfa da zai iya nema." Ahmad da Abu Dawud da Nasa'i ne suka rawaito daga Ubaidullah ɗan Addiy.

Ya kai Musulmi! Ka ba wanda ake bi bashi zakka. Wato wanda ya ci bashi don maslahar kansa, ko don maslahar wani, wato ya ɗau bashi, amma ya gaza biya, da sharaɗin ba zai ci gaba da irin wannan sakacin ba. Ka ba wa wanda ya ci bashi don maslahar al'umma ko da mawadaci ne, ka 'yanta wuyan fursunoni na musulmi, ka taimaki mai jihadi, da wanda guzurinsa ya ƙare, wannan ita ce shari'ar Ubangijin talikai.

Ya kai musulmi! Idan ka zama mawadaci, to kar ka karɓi zakka. Idan kuwa ka karɓa, bayan Allah ya wadata ka ga barin karɓar, to ka sani kana cin mafi munin haramun ne. Ya zo a Bukhari da Muslim daga Ibn Umar, Annabi (ﷺ) ya ce, "Roƙo ba zai ƙyale ɗayansu ba, har sai ya gamu da Allah babu ko tsokar nama a fuskarsa." A cikin Sahihi Muslim kuma daga hadisin Abu Huraira, Manzo Allah (ﷺ) ya ce, "Wanda ya roƙi mutane don tara dukiya, to yana roƙar garwashin wuta ne, in ya so ya roƙa kaɗan, ko ya roƙa da yawa." A cikin Musnad na Imam Ahmad, daga Abi Huraira, Manzo Allah (ﷺ) ya ce, "Bawa ba zai buɗe wa kansa ƙofar roƙo ba, sai Allah ya buɗe masa ƙofar talauci". Haka kuma a cikin Bukhari da Muslim daga hadisin Abu Huraira, ya ce, Manzo Allah (ﷺ) ya ce, "Ita wadata ba wai yawan kadarori ba ce, wadata ita ce wadatar zuci."

Ya kai Musulmi! Bukhar da Muslim sun ruwaito hadisi daga Abu Huraira, ya ce, Manzo Allah (ﷺ) ya ce, "Miskini ba shi ne wanda yake yawo cikin mutane, loma ɗaya ko biyu take dakatar da shi ba, ko dabino ɗa ko biyu. Sai dai cikakken miskini, shi ne wanda, ba shi da abin da zai wadatar da shi, kuma ba a faɗakuwa da shi ballantana a ba shi sadaka, kuma ba ya tashi ya roƙi mutane"

Ya kai ɗan'uwana Musulmi! Da yawa waɗanda ba su cancanci zakka ba suna roƙo a ba su. Kuma su nace wajen nema, alhali Allah ya ba su ƙarfin jiki, da lafiyarsa, da ikon yin aiki. Sai dai su sun saba da hakan ne. Suka ga cewa al'ada duk shekara sai an ba su. Da yawa wasu mutane suna roƙon zakka waɗanda da farko su talakawa ne, sai Allah ya wadata su, ya ba su yaran da za su tallafa musu, a bisa lamuransu. Sai dai mutuwar zuciya da cutar kwaɗayi, sun sanya su suna roƙonta alhali su mawadata ne ga barinta.

Ya ɗan'uwa, ka kirdadi, waɗada ba sa roƙo, ka bibiyi masu iyali (masu kamewa), waɗanda ba sa nacewa da roƙon mutane. Wanda bai sani ba zai ɗauka su mawadata ne. Saboda kame kai. Ka yi kirdadon wanda yake bayyana matsayin mawadaci, alhali kuwa Allah ya san halin da yake ciki. Ka kirdadi wanda basussuka suka yi masa yawa.

Lalle abu ne muhimmi, mu san cewa, Allah ya sanya zakka hanya ce, ta haɗin kan al'umma da dunƙulewarta, da jinƙan sashi ga sashi. "Ku jiƙan wanda ke ƙasa, wanda ke sama sai ya jiƙan ku", "Masu jinƙai, Mai rahama zai jinƙan su." Ahmad da Abu Dawud da Tirmizi ne suka rawaito.

Da mawadata za su ba da zakkar dukiyoyinsu, da matalauta sun wadatu. Sun kare mutuncinsu, kuma an samu sauƙin aikata.

Ya ku bayin Allah! Ku yi kwaɗayi a bisa zakkar dukiyarku, ku sadar da ita ga waɗanda suka cancanceta. Ku boye ta, idan kuka san cewa wanda zai karɓe ta mai kame kai ne ba ya so lamarinsa ya bayyana. Ku yi kwaɗai Allah ya jiƙan ku! Ku yi taimakekeniya a bisa biyayya da tsoron Allah. Ku keɓanci talakawa daga makusantanku da zakkarku, domin zakkarka gare su ninki biyu ce. Sadaka da sa da zumunci. Ka bincika maƙotanka, ku yi taimakon juna a wjen binciken talakawa da waɗanda suka cancanta don biyayya ga Allah, da neman kusanci da shi zuwa ga Allah.

Ina roƙon Allah Ya karɓi kyawawan ayyuka daga gare mu da ku, shi Mai iko ne a bisa kowane abu. Ku sani Allah Ya jiƙan ku, mafi kyawun zanci shi ne littafin Allah, kuma mafi alherin shiriya, shiriyar Annabi Muhammadu (ﷺ).

TUBA DAGA BARIN SAƁO

Manufofin huɗubar

- Komawa ga Allah (S.W.T)
- Shiryar da mutane abisa kyautata alaƙarsu da Ubangiji
- Barin ɗebe tsammani da samun rahamar Ubangiji

Huɗuba Ta Farko

Haƙiƙa dukkan yabo ya tabbata ga Allah muna godemasa muna neman taimakonsa muna neman gafararsa, muna neman tsarin Allah daga sharrin kawukanmu da kuma munanan ayyukanmu. Duk wanda Allah ya shirye shi babu mai ɓatar da shi, wanda kuma duk ya ɓatar da shi babu mai shiriyarsa. Ina shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah shi kaɗai ba shi da abokin tarayya kuma ina shaidawa haƙiƙa Annabi Muhammadu bawansane kuma manzonsane.

"Yaku waɗanda sukayi imani kuji tsoron Allah haƙiƙanin jin tsoronsa kada ku kuskura ku mutu face sai kuna musulmai" (Al-Imran 102).

"Yaku mutane kuji tsoron Allah wannan da ya halicce ku daga rai guda ɗaya ya halitta daga jikin matarsa sannan ya yaɗa daga su biyun mazaje da yawa da kuma mataye kuji tsoron Allah wannan da kuke yin tambaya (roƙo) da shi da kuma zumunci haƙiƙa Allah ya kasance akanku mai tsaro" (Nisa'i 1).

"Yaku waɗanda sukayi imani kuji tsoron Allah ku faɗi magana ta daidai, sai Allah ya gyara muku ayyukanku kuma ya gafarta muku zunubanku duk wanda yabi Allah da manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabo mai girma" (Al-ahzab 70 – 71).

Bayan haka;

Yaku bayin Allah ku sani, haƙiƙa kowa ne mutum aikin da aka halicce shi dominsa shi ne ibada. Don haka duk abin da ya aikata na alkhairi to sakamakonsa nasa ne, yana jiransa, kamar yadda duk abin da ya aikata na aikin saɓo to wannan tawaya ce a cikin aikinsa. Kuma cutarwarsa tana komawa akansa kuma zunubi duk inda ya kai da yawa baya cutar da allah da komai, kamar yadda aikin ɗa'a baya amfanar da shi da komai.

Shin ko mun sani – Ya ku musulmi - cewa zunubai ƙazantace Manzon Allah (ﷺ) shi ne ya ambace ta da sunan ƙazanta ya zo a cikin littafin Muwaɗɗa ta Imam Malik (R.A) cewa Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Duk wanda ya aikata wani abu na irin wannan ƙazantar, to ya suturce da suturar Allah...". Koda kuwa mu ba ma ganin wannan ƙazantar afili, koda kuwa ba ma shaƙar warin ta, sai dai ai muna ganin alamun zunuban abisa zukata. Zunubi yana bin bayan zunubi har sai ya lulluɓe zuciya. Allah (ﷺ) yana cewa:

﴿ كَلَّا ۖ بَلْ ۜ رَانَ عَلَىٰ قُلُوبِهِم مَّا كَانُوا۟ يَكْسِبُونَ ﴿١٤﴾ ﴾ [المطففين: ١٤].

(A’aha ba haka ne ba! abin da suka kasance suna aikatawa dai ya yi tsatsa a kan zukatansu).

Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: “Haƙiƙa bawa idan ya yi wani zunubi sai wani baƙin ɗigo ya ya samu akan zuciyarsa, idan kuma ya tuba daga wannan zunubin sai zuciyarsa ta yi haske. Idan kuma ya kama ya ƙara aikatawa sai baƙin ya ƙaru)”. (Tirmizi).

Waɗannan zunuban suna taruwa a cikin zuciyar bawa idan dai har ba’a samu tuba ko istigfari ya biyo bayansu ba har sai zunubin ya cunkushe ta ya lulluɓe ta gaba ɗayanta.

Ya ku musulmi idan ƙazanta ta yi yawa bisa tufafi. kuma aka samu ƙarancin wanke ta to mai kuke tsammani zai faru? To ita zuciya kwatankwacin haka take duk zuciyar da zunubai suka yi yawa a cikinta tuba yayi ƙaranci a gareta menene zai faru da ita?

Ya ku musulmi haƙiƙa mu muna yin zunubi dare da rana, sau da yawa ma wani sai kwanaki da yawa su shuɗe bai ɗaga hannayensa ba, ya tuba ga Allah. Bai roƙe shi gafara abisa irin abin da yake aikatawa na zunubai ba. To me kuke tsammani da irin zuciyar wannan?

Tsabtata ta haƙiƙa ita ce tsabtar zuciya. Tsabtar tufafi ba ta da wani amfani, in har dai zuciya tana gurɓace da ƙazantar zunubi da saɓon Allah (S.W.T).

Sau da yawa mutum yana iya kasancewa tufafinsa masu tsabta, amma zuciyarsa daga ciki tana cike da dattin ƙazantar zunubai mai wari, saboda ko wacce rana yana ƙara mata datti ta hanyar aikata zunubai da kuma rashin tuba da rashin istigfari. Ba shi da wata daraja a karan kansa. Kuma ba shi da daraja a wajen mutane da a ce za su gane haƙiƙaninsa. Kuma ba shi da wata ƙima a wajen mahaliccinsa a ranar Alƙiyama, ranar da za a tona asirai, ranar da za a fitar da dukkanin abin da zuciya ta ɓoye alhalin babu abin da yake ɓuya ga Allah komai ƙanƙantarsa.

Ya ku musulmi dukkan mutane suna yin zunubi sai dai bambanci a tsakaninsu akwai wanda yake gaggawa ya tuba gabarin zunubansa ya kawar dasu ya tsarkake zuciyarsa da tuba da istigfari, sannan kuma akwai wanda yake gafala ya rafkana ga barin zunubansa har su ruɓanya a cikin zuciyarsa.

Ya ku bayin Allah! ƙofar neman gafara a buɗe take domin mu tsabtace zuƙakanmu daga waɗancan zunubai waɗanda muke aikatawa a kullum. Ya ku bayin Allah mu masu roƙon Allah ne mai girma bisa ya karɓi tubanmu, domin mu yayewa wannan zuciyar irin nauyaye-nauyayenta, waɗanda suka shiga tsakanin mu da samun nutsuwa a cikin rayuwanmu. Ubangiji yana cewa:

﴿ قُلۡ يَٰعِبَادِيَ ٱلَّذِينَ أَسۡرَفُواْ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمۡ لَا تَقۡنَطُواْ مِن رَّحۡمَةِ ٱللَّهِۚ إِنَّ ٱللَّهَ يَغۡفِرُ ٱلذُّنُوبَ جَمِيعًاۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلۡغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ٥٣ ﴾ [الزمر: ٥٣].

“Ce da su, (Allah yana cewa) «Ya ku bayina waɗannan da suka yi ɓarna ga kawunansu kada ku ɗebe tsammanin samun rahmar Allah, domin Allah yana gafarta zunubai ne gaba ɗaya, kuma haƙiƙa shi mai gafara ne mai jin ƙai ne”.

Bayin Allah, haƙiƙa yana daga cikin sunayen Allah maɗaukaki akwai «mai gafara, mai karɓar tuba», kuma su waɗannan sunayen guda biyu masu girma sun ƙunshi siffar Gafara da kuma karɓar tuba, domin shi Allah (S.W.T) yana karɓar tuba daga bayinsa, kuma yana yin rangwame dangane da zamiya da sukayi. Allah (S.W.T) ya ce dangane da Annabi Musa sanda ya kashe wani mutum ba tare da niyya ba

﴿ قَالَ رَبِّ إِنِّي ظَلَمْتُ نَفْسِي فَاغْفِرْ لِي فَغَفَرَ لَهُ ۚ إِنَّهُ هُوَ الْغَفُورُ الرَّحِيمُ ﴿١٦﴾ ﴾ [القصص: ١٦].

(Ya ce, ya Ubangijina haƙiƙa ni na zalunci kaina, ka gafarta min. Sai (Allah) ya gafarta masa, domin shi mai gafara ne mai jin ƙai).

Ubangiji (S.W.T) ya ce dangane da Annabi Adam:

﴿ وَعَصَىٰ آدَمُ رَبَّهُ فَغَوَىٰ ﴿١٢١﴾ ثُمَّ اجْتَبَاهُ رَبُّهُ فَتَابَ عَلَيْهِ وَهَدَىٰ ﴿١٢٢﴾ ﴾ [طه: ١٢١ – ١٢٢].

"Adam ya saɓawa Ubangijinsa sai ya ɓace. Sannan Ubangijinsa ya zaɓe shi, ya karɓi tubansa, ya shiryar da shi".

Ubangiji maɗaukaki ya ce:

﴿ وَهُوَ الَّذِي يَقْبَلُ التَّوْبَةَ عَنْ عِبَادِهِ وَيَعْفُو عَنِ السَّيِّئَاتِ وَيَعْلَمُ مَا تَفْعَلُونَ ﴿٢٥﴾ ﴾ [الشورى: ٢٥].

(Shi ne wanda yake karɓar tuba daga wajen bayinsa, kuma yake yin afuwa game da munanan aiyuka).

A cikin wannan aya mai girma, Allah maɗaukakin sarki ya bayyana cewa, shi kaɗai shi yake karɓar tuban bawa idan ya tuba ya bar zunubai da laifuffuka. Ya ƙara bayyana hakan a wasu wure daban, kamar inda yake cewa:

﴿ أَلَمْ يَعْلَمُوا أَنَّ اللَّهَ هُوَ يَقْبَلُ التَّوْبَةَ عَنْ عِبَادِهِ وَيَأْخُذُ الصَّدَقَاتِ وَأَنَّ اللَّهَ هُوَ التَّوَّابُ الرَّحِيمُ ﴿١٠٤﴾ ﴾ [التوبة: ١٠٤].

"Shin basu sani ba cewa haƙiƙa Allah shi yake karɓar tuba daga bayinsa kuma shi yake karɓar sadaka. Kuma haƙiƙa shi Allah shi ne mai karɓar tuba, kuma shi ne mai yin rahama". Da faɗinsa maɗaukaki:

﴿ يَا أَيُّهَا الَّذِينَ آمَنُوا تُوبُوا إِلَى اللَّهِ تَوْبَةً نَصُوحًا عَسَىٰ رَبُّكُمْ أَنْ يُكَفِّرَ عَنْكُمْ سَيِّئَاتِكُمْ ﴾ [التحريم: ٨].

"Ya ku waɗanda suka yi imani ku tuba zuwa ga Allah tuba na gaskiya, tabbas Ubangijinku zai gafarta muku laifuffukan ku". Da kuma faɗinsa (S.W.T):

﴿ وَمَنْ يَغْفِرُ الذُّنُوبَ إِلَّا اللَّهُ ﴾ [آل عمران: ١٣٥].

"Waye yake gafarta zunubai idan ba Allah ba".

Da sauran ayoyi masu kama da waɗannan.

An karɓo hadisi daga Abu Musa, Abdullahi bn Kais al-Ash'ari (R.A) ya ce, Annabi (ﷺ) ya ce, "Haƙiƙa Allah maɗaukaki yana shimfiɗa hannunsa da daddare domin ya karɓi tuban mai yin saɓo da rana, kuma yana shimfiɗa hannunsa da rana domin ya karɓi tuban wanda yayi zunubi da daddare, har sai lokacin da rana ta hudo daga mafaɗarta". (Muslim)

Haƙiƙa sakamakon imani da sunayen Allah "Mai gafara" da kuma "Mai karɓar tuba" suna bayyana ne ga bawa idan ya zama mai komawa ga Allah ta hanyor ƙanƙan da kai a gare shi, da kuma neman gafara dangane da zunuban da ya gabatar a baya, da kuma rashin ɗebe tsammani ga samun rahamar Ubangiji maɗaukakin sarki.

Ya ku bayin Allah! Lalle ita tuba ga barin dukkan zunubai wajibi ne, wanda kuma ana so ya zama an aiwatar da shi da gaggawa, domin yin jinkirta tuba alamace ta tsiyatar lahira ga bawa, da taɓewa, da ma shafewar basira. Allah ya tsare mu.

Ubangiji maɗaukaki yana cewa:

﴿ وَتُوبُوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ جَمِيعًا أَيُّهَ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ لَعَلَّكُمۡ تُفۡلِحُونَ ٣١ ﴾ [النور: ٣١].

"Ku tuba zuwa ga Allah baki ɗaya ya ku muminai ko kwa rabauta".

Kuma yana cewa,

﴿ ٱسۡتَغۡفِرُواْ رَبَّكُمۡ ثُمَّ تُوبُوٓاْ إِلَيۡهِ ﴾ [هود: ٥٢].

"Ku nemi gafarar Ubangijinku sannan ku tuba zuwa gare shi".

Yana cewa:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ تُوبُوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ تَوۡبَةٗ نَّصُوحًا ﴾ [التحريم: ٨].

(Ya ku waɗanda suka yi imani ku tuba zuwa ga Ubangijinku tuba nagari).

Don haka waɗannan ayoyin dama waɗanda suke ɗauke da ma'anoni irin nasu duka suna nuni abisa wajibcin tuba daga dukkanin aikin saɓo, domin a cikin su waɗannan ayoyin akwai umarni da yin tuba gaba ɗaya. Malaman Usulul fiƙhi suna cewa: Dukkan umarni yana fa'idantar da wajabci ne, sai dai idan wani dalili ya nuna rashin wajibcin.

An karɓo daga Abu Huraira (R.A) ya ce: "Na ji Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: "Na rantse da Allah ina neman gafarar Allah da kuma tuba a gare shi a kowanne yini sama da sau saba'in. (Bukhari).

A cikin hadisin da aka karɓo daga wani sahabi mai suna Al'agarru ɗan Yasar Al-muzniy (R.A) ya ce: "Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ya ku mutane ku tuba ga Allah ku nemi gafararsa haƙiƙa ni ina tuba a kowanne wuni sau ɗari" (Muslim).

Malamai suka ce, idan bawa ya tuba ya bar wasu daga cikin zunubansa to zance mafi inganci tubansa ya inganta abisa zunubin da ya tuba gabarin yinsa. Amma sauran sunan awuyansa ba za su gushe ba har sai sanda ya tuba.

Kuma ita tuba bata zama ta gari har sai idan ta cika sharuɗɗa guda uku:

1. Ya ƙauracewa zunubin idan yana yinsa.
2. Sannan ya yi takaicin abin da ya gabata na saɓawa Ubangijinsa.
3. Ya yi niyya da gaske ba zai sake komawa ba kan wannan zunubin har abada.

Abin da ya fi fitowa fili ta hanyar dalilai masu ƙwari a cikin maganganun malamai shi ne, idan bawa ya tuba daga aikata wani zunubi sannan daga baya ya sake komawa ya aikata to wancan tuban nasa na farko ya inganta, sai dai ya sake tuba a karo na biyu. Ba kamar yadda wasu suke cewa; komawarsa ta rushe wancan tuban na farko ba.

Na biyu: Malamai ba su yi saɓani ba akan cewa tuba ba ta inganta, sai idan an haɗata da yin nadama bisa zunubin da aka aikata. Sannan da barinsa idan ya kasance shi mai aikatawa yanayin zunubin.

Yana aga cikin sharuɗɗan tuba biyan abin da ya kamata a biya, wanda aka yi sakaci a kansa. Misali: Mayar da abin da aka zalunci wani akansa.

An karɓo daga Aliyu ɗan Abi Ɗalib (R.A) cewa: Tuba ta ƙunshi abubuwa guda shida:

1. Yin nadama abisa abin da ya gabata na zunubai
2. Biyan farillan da aka bari ba a yi su ba.
3. Da mayarwa wanda aka zalunta abin da aka zalunce da shi.
4. Kuma ya nemi abokin husumarsa da ya yafe masa.
5. Yayi takai da kawowa wajen yin ɗa'a ga Allah kamar yadda ya narke cikin saɓa masa.
6. Kuma ya ɗandana mata ɗacin biyayya ga Allah, kamar yadda ya ɗandana mata zaƙin aikin saɓo.

Lallai ana son ayi alwala da yin sallah raka'a biyu a yayin tuba, tare da cika sharuɗɗan da aka ambata a baya, saboda hadisin da Imam Ahmad ya ruwaito daga Aliyu ɗan Abi Ɗalib (R.A) ya ce: Na kasance idan na ji hadisi daga Manzon Allah (ﷺ) Allah yakan amfanar da ni shi da abin da ya so. Idan kuma wani ne ya faɗa mini hadisi daga gare shi, ina neman ya rantse, idan ya rantse min sai in gaskata shi. Abubakar ya faɗa mini wani hadisi, kuma shi Abubakar gaskiya ya faɗamin, cewa, ya ji Ma'aikin Allah (ﷺ) ya ce: "Babu wani mutum da zai aikata wani zunubi sannan ya yi alwala kuma ya kyautata alwalarsa, sannan kuma ya yi sallah raka'a biyu, sannan ya nemi gafarar Allah mai girma da ɗaukaka face Allah ya gafarta masa".

Abin da yake ƙara tabbatar da ingancin wannan hadisin shi ne hadisin da Imam Muslim ya ruwaito a cikin ingantaccen littafinsa daga Sarkin Muminai Umar ɗan Khaɗɗabi (R.A) daga Annabi (ﷺ) cewa: "Babu wani a cikinku da zai yi alwala ya cika alwalarsa sannan ya ce, "Na shaida babu abin bautawa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Sannan kuma na shaida Annabi Muhammad bawansa ne kuma manzonsa ne, face sai ambuɗe masa ƙofofin aljanna guda takwas ya shiga ta wacce yake so".

Huɗuba Ta Biyu

Dukkan yabo da godiya sun tabbata ga Allah Ubangijin halittu, tsira da aminci su ƙara tabbata ga shugaban Manzanni, Annabin mu Muhammad da iyalan gidansa da sahabbansa baki ɗaya.

Bayan haka;

Haƙiƙa nassoshi na shari'a sun nuna ba za karɓi tuban bawa ba yayin da rai ya kai maƙoshi, wato ya kai hali na gargara. Da kuma yayin da rana za ta hudo daga mafaɗarta. Allah maɗaukakin sarki ya ce:

﴿ هَلۡ يَنظُرُونَ إِلَّآ أَن تَأۡتِيَهُمُ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ أَوۡ يَأۡتِيَ رَبُّكَ أَوۡ يَأۡتِيَ بَعۡضُ ءَايَٰتِ رَبِّكَۗ يَوۡمَ يَأۡتِي بَعۡضُ ءَايَٰتِ رَبِّكَ لَا يَنفَعُ نَفۡسًا إِيمَٰنُهَا لَمۡ تَكُنۡ ءَامَنَتۡ مِن قَبۡلُ أَوۡ كَسَبَتۡ فِيٓ إِيمَٰنِهَا خَيۡرٗاۗ قُلِ ٱنتَظِرُوٓاْ إِنَّا مُنتَظِرُونَ ١٥٨ ﴾ [الأنعام: ١٥٨].

(Ba komai suke jira face sai mala'iku sun zo musu, ko kuma Ubangijinka ya

zo, kuma sai wani sashin ayoyin Ubangijinka sun zo, to lokacin da wani sashi na ayoyin Ubangijinka zai zo, to a wannan lokacin rai wadda ta kasance ba ta yi imani ba, kafin haka, ko kuma ba ta tsuwurwuci wani aikin alkhairi a cikin imaninta ba, imaninta ba zai amfane ta ba. Ka ce, «Ku saurara haƙiƙa mu masu saurarawa ne").

Sashen ayoyin Ubangijinka za su zo musu ne kafin ranar Alƙiyama. Kuma yana daga cikin alamomin tashin Alƙiyama, kamar yadda al-Imam al-Bukhari ya faɗa a cikin tafsirin wannan ayar.

An karɓo daga Abu Huraira (R.A) ya ce Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Alƙiyama ba za ta tashi ba har sai yayin da rana ta ɓullo ta mafaɗarta, idan mutane suka ganta ayayin sai waɗanda suke akan ƙasa duk su yi imani a sannan to wannan shi ne imanin da wata rai ba zai amfaneta ba matuƙar ba ta yi imani ba kafin sannan". (Bukhari)

An karɓo daga Abu Huraira (R.A) ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Alƙiyama ba za ta tashi ba har sai rana ta ɓullo daga mafaɗarta, idan ta ɓullo mutane suka ganta a sannan sai su yi imani gaba ɗaya to a wannan lokacin shi ne: (Rai imaninta ba zai yi mata amfani ba, idan dai ba ta riga ta yi imani ba kafin wannan lokacin" Sannan sai ya karanto wannan ayar data gabata.

An karɓo daga Abu Musa, Abdullahi ɗan Kais, Al-Ash'ariy (R.A) daga Annabi (ﷺ) ya ce: "Haƙiƙa Allah (S.W.T) yana shimfiɗa hannunsa da daddare domin ya karɓi tuban bawan da yayi saɓo da rana sannan yana shimfiɗa hannunsa da rana domin ya karɓi tuban bawan da yayi saɓo da daddare har sai rana ta ɓullo daga mafaɗarta" [Muslim ya ruwaito shi].

An karɓo daga Abu Huraira (R.A) ya ce, Ma'aikin Allah (ﷺ) ya ce: "Dukkan wanda ya tuba kafin rana ta ɓullo ta mafaɗarta to Allah zai karɓi tubansa" [Muslim ya ruwaito shi].

Haka kuma Allah ba ya karɓar tuban bawa yayin da ya kai lokacin gargara kamar yadda ya zo a cikin hadisin Abdullahi ɗan Umar (R.A) daga Annabi (ﷺ) cewa: "Haƙiƙa Allah yana karɓar tuban bawa matuƙar bai kai lokacin gargara ba". Imam Attirmizi ya ce: "Wannan hadisin Hasan ne".

Kuma ma'anarsa idan dai har rai bai kai ga maƙogwaro ba. Ma'ana idan dai mutuwa bata halarto shi ba. Domin ba a la'akari da tuba idan mutuwa ta halarto. Saboda faɗin Allah (S.W.T) cewa:

﴿ وَلَيۡسَتِ ٱلتَّوۡبَةُ لِلَّذِينَ يَعۡمَلُونَ ٱلسَّيِّـَٔاتِ حَتَّىٰٓ إِذَا حَضَرَ أَحَدَهُمُ ٱلۡمَوۡتُ قَالَ إِنِّي تُبۡتُ ٱلۡـَٰٔنَ وَلَا ٱلَّذِينَ يَمُوتُونَ وَهُمۡ كُفَّارٌۚ أُوْلَٰٓئِكَ أَعۡتَدۡنَا لَهُمۡ عَذَابًا أَلِيمًا ١٨ ﴾ [النساء: ١٨].

(Ita tuba ba ta kasance abar karɓa ga waɗannan da suka yi mummunan aiki alhalin basu tuba ba tuntuni, har sai da mutuwa ta halarto ma ɗaya daga cikinsu, sai ka ji shi yana cewa, "Ni na tuba a yanzu". Da kuma waɗannan da suke mutuwa alhalin suna kafirai).

Ya ku bayin Allah! Haƙiƙa tuba zuwa ga Allah tana tabbatarwa da bawa samun arziki na har abada, da kuma rayuwa mai daɗi a nan duniya da kuma lahira. Allah maɗaukakin sarki ya ce:

﴿ مَنْ عَمِلَ صَٰلِحًا مِّن ذَكَرٍ أَوْ أُنثَىٰ وَهُوَ مُؤْمِنٌ فَلَنُحْيِيَنَّهُۥ حَيَوٰةً طَيِّبَةً ۖ وَلَنَجْزِيَنَّهُمْ أَجْرَهُم بِأَحْسَنِ مَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿٩٧﴾ ﴾ [النحل: ٩٧].

(Duk wanda ya aikata wani aiki na-gari, namiji ne ko mace, alhalin yana mumini to za mu rayar da shi rayuwa mai daɗi, sannan kuma za mu saka masu da ladansu, ma fi kyau daga abin da suka kasance suna aikatawa).

Sakamakon tuban muminai ga Ubangijinsu hakan yana sawa su sami zaman lafiya, da shiriyar Allah maɗaukakin sarki ya ce:

﴿ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَلَمْ يَلْبِسُوٓا۟ إِيمَٰنَهُم بِظُلْمٍ أُو۟لَٰٓئِكَ لَهُمُ ٱلْأَمْنُ وَهُم مُّهْتَدُونَ ﴿٨٢﴾ ﴾ [الأنعام: ٨٢].

(Waɗannan da suka yi imani, kuma ba su jirkita imaninsu ba da zalunci to irin waɗannan suna da amintuwa, kuma su ne shiryayyu).

Ma'ana: Waɗanda suka gaskata Ubangiji da Manzonsa suka yi aiki da shari'arsa, kuma basu cakuɗa imaninsu ba da shirka, irin waɗannan suke da nutsuwa da aminci, kuma su ne waɗanda suka dace da bin tafarki na gaskiya, to idan tuba ya samu karɓuwa, to aminci da shiriya sun samu.

Daga cikin amfanin tuba, akwai canza munanan aiyuka da kyawawa, da kuma shafe guraban munanan aiyuka. Kamar yadda ya zo a cikin faɗin Ubangiji maɗaukakin sarki:

﴿ إِلَّا مَن تَابَ وَءَامَنَ وَعَمِلَ عَمَلًا صَٰلِحًا فَأُو۟لَٰٓئِكَ يُبَدِّلُ ٱللَّهُ سَيِّـَٔاتِهِمْ حَسَنَٰتٍ ۗ وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُورًا رَّحِيمًا ﴿٧٠﴾ ﴾ [الفرقان: ٧٠].

"Sai dai fa wanda ya tuba, ya yi imani, ya kuma aikata aiki nagari, to irin waɗannan su ne Allah yake canza munanan aiyukansu su zama kyawawa. Kuma Allah ya kasance mai gafara ne mai jin ƙai".

Haƙiƙa Allah (S.W.T) ya bayyana ƙarara a cikin wannan ayar cewa, waɗannan da suke yi zina da wanda aka ambata a tare da su, idan suka tuba, suka yi imani, suka aikata aiki nagar, to Allah zai canza munanan aiyukansu su zama kyawawa. Wannan yana nuna cewa, tuba daga aikata zina tana tafiyar da gurbinta. waɗannan da suke cewa: Wanda duk ya yi zina da wata mace, wai ba ta halatta a gare shi ya aure ta ba, ko da sun tuba su biyun sun kyautata aikinsu, to wannan magana ta su ba daidai ce ba. Domin an samu daga wajen sahabbai cewa ya halatta ya auri matar da ya yi zina da ita matuƙar sun tuba.

Yana daga cikin amfanin tuba, rabauta da samun yardar Allah, da kuma kubuta daga wuta, kamar yadda Allah (S.W.T) ya faɗa:

﴿ وَٱلَّذِينَ إِذَا فَعَلُوا۟ فَٰحِشَةً أَوْ ظَلَمُوٓا۟ أَنفُسَهُمْ ذَكَرُوا۟ ٱللَّهَ فَٱسْتَغْفَرُوا۟ لِذُنُوبِهِمْ وَمَن يَغْفِرُ ٱلذُّنُوبَ إِلَّا ٱللَّهُ وَلَمْ يُصِرُّوا۟ عَلَىٰ مَا فَعَلُوا۟ وَهُمْ يَعْلَمُونَ ﴿١٣٥﴾ ﴾ [آل عمران: ١٣٥].

(Waɗannan da idan sun aikata wata alfasha ko kuma suka zalunci kawunansu, sai su tuna Allah, su nemi gafarar zunubansu, waye ya ke gafarta zunubai idan ba Allah ba. Sannan ba su dogewa akan abin da suka aikata alhalin suna sane. To irin waɗannan sakamakonsu wata gafara ce daga wajen Ubangijinsu, da kuma aljannatai wanda ƙoramu suke gudana a ƙarƙashinsu, suna masu dauwama a ciki. Madallah da ladan masu aiki).

Ma'ana: Idan sun aikata wani zunubi sai su biyo bayansa da tuba, da neman gafarar Ubangijinsu.

Yaku bayin Allah! Imam Ahmad da Imamul Bukhari sun ruwaito wani hadisi daga Abu Huraira shi kuma daga Annabi (ﷺ) ya ce: Haƙiƙa wani mutum ya aikata wani zunubi sai ya ce, "Ya Ubangiji ni na aikata wani zunubi ka gafarta min". Sai Ubangiji ya ce, "Bawana ya aikata wani zunubi, sai ya san cewa shi yana da Ubangiji wanda yake yafe zunubi, kuma yake kamu da shi zunubin, to haƙiƙa na yafewa bawana". Sannan kuma ya aikata wani zunubin sannan ya ce, "Ya Ubangiji haƙiƙa na aikata zunubi ka yafe min". Sai Ubangiji mai girma da buwaya ya ce. "Bawana ya san cewa yana da Ubangiji, wanda yake yafe zunubi, kuma yake kamu da shi, to haƙiƙa na gafartawa bawana". Sannan dai kuma ya ƙara aikata wani zunubi, sai ya ce, "Ya Ubangji na aikata zunubi ka gafarta min". Sai Allah ya ce, "Bawana ya aikata zunubi sannan ya san cewa yana da Ubangiji yana gafarta zunubai, kuma yana iya kamu akansa”.

TARBAR WATAN RAMADAN

Manufofin huɗubar

- Kwaɗaitar da mutane a kan su yi shirya zukatansu don tarbar watan Ramadan.
- Kwaɗaitarwa a bisa ribatar kwanakinsa masu falala.
- Bayani a kan wasu daga falalolin azumi da hukunce-hukuncensa da fa'idojinsa.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma mua neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan aiyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar dashi, wanda kuma ya atar babu mai shiryar da shi, kuma ina shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai allah, shi kaɗai ne bashi da abokin taraiya, kuma ina shaidawa cewa Annabi Muhammad bawansane manzonsane, (Yaku waɗanda kuka bada gaskiya kuji tsoron Allah yadda ya cancanta aji tsoronsa, kada ku mutu face kuna Musulmi). (Yaku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicce ku daga rai guda ɗaya kuma ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga gare su (su biyu) kuji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya dashi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku waɗanda suka yi imani kuji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku aiyukanku, kuma ya gafarta muku zunubanku. Wanda ya bi Allah da manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawun shiriya shiriyar Annabi Muhammadu (ﷺ) kuma mafi sharrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma

Bayan haka:

Allah Ta'ala Yana cewa:

﴿ شَهۡرُ رَمَضَانَ ٱلَّذِيٓ أُنزِلَ فِيهِ ٱلۡقُرۡءَانُ هُدٗى لِّلنَّاسِ وَبَيِّنَٰتٖ مِّنَ ٱلۡهُدَىٰ وَٱلۡفُرۡقَانِۚ فَمَن شَهِدَ مِنكُمُ ٱلشَّهۡرَ فَلۡيَصُمۡهُۖ وَمَن كَانَ مَرِيضًا أَوۡ عَلَىٰ سَفَرٖ فَعِدَّةٞ مِّنۡ أَيَّامٍ أُخَرَۗ يُرِيدُ ٱللَّهُ بِكُمُ ٱلۡيُسۡرَ وَلَا يُرِيدُ بِكُمُ ٱلۡعُسۡرَ وَلِتُكۡمِلُواْ ٱلۡعِدَّةَ وَلِتُكَبِّرُواْ ٱللَّهَ عَلَىٰ مَا هَدَىٰكُمۡ وَلَعَلَّكُمۡ تَشۡكُرُونَ ١٨٥ ﴾ [البقرة: ١٨٥].

(Watan Ramadan wanda aka saukar da Alƙur'ani a cikinsa a matsayin shiriya ga mutane da bayyanannun ayoyi daga shiriya, da mai rarrabewa tsakanin gaskiya da ƙarya, duk wanda azumi ya riske shi a halin zaman gida to ya azumce shi, wnda kuwa ya kasance mara lafiya ko a bisa tafiya, to ya rama a wasu kwanakin na daban, Allah yana nufin sauƙi ne da ku ba ya nufin ƙunci da ku ba, sannan kuma domin ku cika adadin (kwanakin azumin), kuma ku girmama Allah a bisa shiriyar ku da ya yi, kuma tsammaninku za ku gode).

Ya wanda fakuwarsa ta tsawaita ga barin mu! Kwanakin sulhu sun gabato. Ya wanda asararsa ta dawwama! Haƙiƙa kwanakin kasuwanci mai riba sun gabato. Ya wanda bai ci riba ba a cikin wannan wata! To a cikin wane wata ne zai ci riba? Duk wanda bai kusanci Ubangijinsa a cikin wannan watan ba, to har abada ma ba zai kusance shi ba.

Ya ku mutane! Ku ji tsoron Allah Ta'ala, kuma ku gode masa a bisa ni'imomin da ya yi muku na lokutan alheir, da abin da ya ba ku na falaloli da karamomi. Ku girmama waɗannan lokuta, ku ba su matsayinsu da aikta biyayya da ayyuka masu kusantarwa zuwa ga Allah, da nisantar saɓo da abubuwa masu jefa mutun a cikin hallaka. Domin ba a samar da waɗannan lokuta ba sai domin kankare munanan ayyukanku, da ƙara inganta kyawawan ayyukanku, gami kuma da ɗaukaka darajojinku.

Ya ku bayin Allah! Haƙiƙa kun fuskanci wani wata mai girma, da yanayi mai cike da riba mai girma ga wanda Allah Ya datar da shi ga aikata aiki na ƙwarai. Kun fuskanci wtan Ramadana, wanda aka saukar da Alƙur'ani a cikinsa. Wata ne da ake ninka kyawawan ayyuka a cikinsa. Kuma ake girmama munanan ayyuka a cikinsa. Allah Ya sanya azumtar yininsa farilla ce daga rukunan musulunci, kuma tsayawa a dararensa nafila ce don kammala farillanku. Duk wanda ya azumce shi don ba da gaskiya da neman ladan Allah, Allah zai gafarta abin da ya gabata daga zunubansa. Wanda kuma ya tsaya darensa, yana mai imani da neman lada, Allah zai gafarta masa abin da ya gabata daga zunubansa. Wanda ya yi Umara a cikinsa, kamar wanda ya yi hajji ne. A ciki ne ake buɗe ƙofofin aljanna, ayyukan biyayya kan yawaita daga ma'abota imani. Ana kulle ƙofofin wuta, sai saɓo ya yi ƙaranci daga ma'abota imani. Ana ɗaure shaiɗanu, ba za su sami damar isowa zuwa ga masu imani ba, irin yadda suke isa zuwa gare su a wasu lokutan.

Bukhari ya rawaito hadisi daga Abu Huraira, ya ce, Manzon Allah tsira da amincin Allah ya ce, Allah ya ce, "Duk wani aikin ɗan-adam na shi ne, ban da azumi, domin shi nawa ne, kuma ni ne nake sakawa a kansa. Kuma azumi garkuwa ne, idan ranar azumin ɗayanku ta kasance, kada ya yi batsa, kada ya yi hayaniya, idan wani ya zage shi ko ya neme shi da faɗa, to ya ce, ni ina azumi. Na rantse da wanda ran Muhammadu ke hannunsa, haƙiƙa rihin bakin mai azumi ya fi ƙamshi a wajen Allah fiye da ƙamshin almiski. Mai azumi yana da farin ciki biyu, da yake yinsu. Idan ya yi buɗa-baki zai yi farin ciki da shan ruwansa, idan kuma ya gamu da Ubangijinsa, zai yi farin ciki da azuminsa".

Ya ku mutane! Ku yi azumi domin ganin jinjirin watan azumi, kuma kada ku gabace shi da azumin rana ɗaya ko biyu. Domin Annabi (ﷺ) ya yi hani a kan haka, sai dai fa wanda ake bin sa azumin Ramadan da ya shuɗe to ya rama shi. Ko kuma ya kasance bisa wata al'ada ta azumi, to kamar wanda yake azumin Litinin ko Alhamis, ko azumin fararen kwanaki (Ranakun 13, 14, 15 na kowa ne wata) sai suka kuɓuce masa, to wannan babu laifi idan ya azumce su kafin Ramadan da kwana ɗaya ko biyu.

Kada ku azumci ranar da ake kokwanton ta. Wato ran ashirin da ga Sha'aban, idan a wannan daren an sami abin da zai hana ganin jinjirin wata na hadari ko duhu ko makamantansu. Ya zo a cikin Sahihil Bukhari, daga hadisin Abdullahi ɗan Amru (R.A), cewa Annabi (ﷺ) ya ce, "Kada ku yi azumi har sai kun gan shi, idan an muku lullumi, to ku cika lissafin talatin."

Hakanan ya ruwaito daga Abu Huraira daga Annabi S.A.W, ya ce "Idan ya ɓuya a gare ku, to ku cika lissafin Sha'aban talatin." Kuma Ammar bin Yasir ya ce: " Duk wanda ya azumci ranar da ake kokwanto a cikinta to, haƙiƙa ya saɓi Baban Kasim (ﷺ)"

Duk wanda ya ga jinjirin wata to, ya sanar da shugaba, kada ya ɓoye. Idan aka sanar a rediyo cewa an ga wata, to ku yi azumi. Idan kuma aka sanar cewa an ga watan Shawwal to ku sauke. Domin sanarwar shuwagabanni kamar hukunci ne a kan hakan.

Ya ku bayin Allah! Abu ne sananne ga kowane musulmi cewa, azumin Ramadan ɗaya ne daga cikin rukunan musulunci da Allah ya wajabta shi a bisa bayinsa. Saboda haka duk wanda ya musa wajabcinsa to shi kafiri ne. Domin ya ƙaryata Allah da Manzonsa da haɗuwar Musulmi. Allah Ta'ala ya ce:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ كُتِبَ عَلَيۡكُمُ ٱلصِّيَامُ كَمَا كُتِبَ عَلَى ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِكُمۡ لَعَلَّكُمۡ تَتَّقُونَ ١٨٣ ﴾ [البقرة: ١٨٣].

(Ya ku waɗanda suka yi imani, an wajabta muku azumi kamar yadda aka wajabatawa waɗanda suka gabace ku, lalle za ku samu taƙawa).

Kuma ya ce:

﴿ شَهۡرُ رَمَضَانَ ٱلَّذِيٓ أُنزِلَ فِيهِ ٱلۡقُرۡءَانُ هُدٗى لِّلنَّاسِ وَبَيِّنَٰتٖ مِّنَ ٱلۡهُدَىٰ وَٱلۡفُرۡقَانِۚ فَمَن شَهِدَ مِنكُمُ ٱلشَّهۡرَ فَلۡيَصُمۡهُۖ وَمَن كَانَ مَرِيضًا أَوۡ عَلَىٰ سَفَرٖ فَعِدَّةٞ مِّنۡ أَيَّامٍ أُخَرَۚ ﴾ [البقرة: ١٨٥].

(Watan Ramadana wanda a cikinsa aka saukar da Alƙur'ani domin shiriya ga mutane da bayyanannun ayoyi daga shiriya, kuma mai rarrabewa tsakanin ƙarya da gaskiya, duk wanda ya zama mazaunin gida a kwanakin watan to ya azumce shi…).

Don haka azumi wajibi ne a kan kowane musulmi, baligi, mai hankali, mai iko, mazaunin gida, namiji ne ko macen da ba ta jinin haila, ko na biƙi (a lokacin) azumin. Ba ya wajaba a kan kafiri, amma da zarar ya musulunta a tsakiyar rana to ya kame bakinsa a ragowar yininsa, amma ba zai rama wannan ranar ba.

Azumi ba ya wajaba a kan yaron da bai balaga ba, sai dai idan azumin ba ya ba shi wahala, za a iya umartarsa da ya yi, don ya saba domin sahabbai (R.A) suna horar da yaransu a kan yin azumi, har ya kasance yaro yana kuka saboda yunwa sai su ba shi abin wasa ya shagala da shi har sai lokacin faɗuwar rana ya yi.

Azumi ba ya wajaba a kan wanda ba shi da hankali, kamar mahaukaci, ko wawa, ko makamantansu, ko babba wanda yake sambatu, to wannan azumi bai hau kansa ba. Haka nan ba ciyarwa ko tsarki ko salla a kansa, domin ba shi da cikakken hankali, kamar yaro yake kafin ya fara tantance abubuwa. Azumi ba ya wajaba a kan wanda ya kasa kamar mai shekaru da yawa, wato tsoho, ko kuma marar lafiyar

da ba a tsammanin warkewarsa, sai dai zai ciyar da miskinai a madadin azumin. Ga kowane miskini rubu'in Sa'i (mudu ɗaya). Amma an fi so idan ya haɗa da mahadĩn abincin, kamar nama da mai (ko kayan miyarsa).

Ya ku Musulmai, shi ko mara lafiya da ake sa-ran warkewarsa, idan azumin ba ya wahalar da shi, kuma ba ya cutar da shi, to ya wajaba ya yi azumin, domin ba shi da uzuri. Idan kuwa azumin yana wahalar da shi amma ba ya cutar da shi, to zai sha, kuma an karhanta masa azumin. Idan kuma azumin yana cutar da shi to haramun ne ya yi azumin. Duk kuma sanda ya warke daga cutarsa to ya rama abin da ya sha. Idan ya mutu kafin ya warke babu komai a kansa.

Mace mai ciki wadda azumi yake yi mata wahala saboda rauninta ko nauyin cikinta, ya halatta ta sha, sannan ta rama idan ta samu sarari kafin ta haihu ko bayan ta samu tsarki daga jinin nifasi. Mai shayarwa ko nononta kan yi ƙaranci saboda yin azumin, kuma wannan ƙarancin zai cutar da shayarwar, to ya halatta ta sha sannan ta rama a lokutan da babu wahala ko tawaya (a nonon nata) a cikinsu. Amma matafiyi idan ya yi nufin dabara ne kawai don ya sha azumi, to shan azuminsa haramun ne a kansa, ya wajaba ya yi azumi.

Idan kuwa ba nufi ko dabarar shan azumi ba ne ya sa shi yin tafiyar, to yana da zaɓi, ko dai ya yi azumi ko kuma ya sha, sai ya rama adadin kwanakin da ya sha, amma an fi son ya aikata abin da ya fi yi masa sauƙi.

Idan yin azumin ya yi daidai da rashin yin (a wajen wahala ko sauƙi) to an fi son ya yi azumin domin shi ne aikin Annabi (ﷺ), kuma domin kuwa shi ya fi gaggawa a wajen sauke nauyin da ke kansa. Kuma galibi ya fi ramuwar sauƙi. Idan kuwa azumin zai yi masa wahala saboda tafiyarsa, to an karhanta masa yin azumin. Idan kuwa wahalar ta tsananta, to haramun ne ya yi azumi, domin Annabi (ﷺ) ya fita a shekara buɗe Makka, zuwa Makka a cikin Ramadana, sai ya yi azumi, sai aka ce masa haƙiƙa azumi ya wahalar da mutane, suna jiran abin da ka aikata. Take kawai sai ya yi umarni aka kawo masa kofin ruwa, bayan La'asar, sai ya ɗaga shi har sai da mutane suka gani, sannan ya sha, sai aka ce masa bayan haka, ai wasu mutane sun ci gaba da azumi, sai ya ce, "waɗannan su ne masu saɓo".

Babu bambanci a tsakanin matafiyin da tafiyar ta bijiro masa don wata buƙata, ko kuma matafiyin da tafiyar tasa mai maimaituwa ce a yawan lokuta. Irin waɗannan sun haɗar da 'yan tasi, ko kuma direbobin manyan motoci, domin su duk sanda suka fita daga garinsu sun zama matafiya. Abin da ya halatta ga sauran matafiya ya halatta a gare su na daga Ramadana, da ƙasarun salla mai raka'a huɗu, da haɗawa a tsakanin sallar Azahar da La'asar, da tsakanin Magariba da Isha'i, a yayin buƙatar hakan. Shan azumi shi ne mafifice a gare su, fiye da yin azumi. Idan shan shi ya fi sauƙi a gare su, sai su rama shi a kwanakin sanyi. Domin masu mota suna da garin da suke zaune, da iyalin da suke komawa gare shi. Duk sanda suke a garinsu to suna zaman gida, duk kuwa sanda suka fita daga cikinsa, to matafiya ne, abin da matafiya suke da shi to su ma suna da shi, abin da ke kan matafiya yana kansu. Duk wanda ya yi tafiya a cikin yinin Ramadana yana azumi, mafifici ya cika azuminsa, idan ya wahala to ya sha sai ya rama. Tafiyar ba ta taƙaita da

wani lokaci ba. Duk wanda ya fita daga garinsa to shi matafiyi ne, har sai ya dawo garinsa, ko da ya zauna a lokaci mai tsawo a garin da ya je ɗin. Sai dai idan ya yi nufin ya samu damar shan azumi ta hanyar daɗewar tasa. To a nan ya haramta ya sha azumi, kuma azumi ya wajaba a gare shi, domin farillolin Allah ba sa saraya domin dabarar mutum. Azumi ba ya wajaba a kan mace mai haila ko jinin biƙi, kuma idan sun yi, to azumin nasu bai inganta ba. Sai dai idan sun yi tsarki kafin ketowar alfijir ko da da minti ɗaya ne, to a nan azumi ya wajaba a kansu kuma ya inganta in sun yi ko da ba su yi wanka ba sai bayan hudowar alfijir. Kuma ya lazimce su su rama kwanakin da suka sha.

Ya ku musulmai! Haƙiƙa Annabi (ﷺ) ya kwaɗaitar a bisa tsayuwar dare a wannan wata ya ce: "Duk wanda ya tsaya a Ramadana yana mai imani, da kuma neman lada, to za a gafarta masa abin da ya gabata na zunubinsa." Haka nan sallar Asham ko Tarawihi, tana daga ƙiyamu Ramadana. Ya kamata ku tsai da waɗannan salloli ku kyautata su, ku tsaya tare da limaminku har sai ya idar, domin duk wanda ya tsaya tare da limaminsa har ya ƙare, to za a rubuta masa ladan tsayuwar dare cikakke, ko da kuwa ya yi barci.

Ya wajaba, limamai su ji tsoron Allah a wannan Asham ɗin. Su kula da waɗanda suke binsu sallah, su kyautata sallar gare su, su tsai da ita, da nutsuwa. Kada su yi sauri a cikinta sai su haramtawa kansu da waɗanda suke binsu alheri, kuma kada su yi caccaken kurciya, ba sa nutsuwa a cikin ruku'inta, da sujjadarta, da zamanta da tsayuwa bayan ruku'i. Ya wajaba ga limamai, kada ɗayansu ya fita daga masallaci kafin mutane ko ya yawaita sallamomi ba tare da kyautata salla ba. Domin Allah Ta'ala yana cewa:

﴿لِيَبْلُوَكُمْ أَيُّكُمْ أَحْسَنُ عَمَلًا﴾[الملك: ٢].

"Domin ya jarraba ku wane ne ya fi kyautata aiki a cikinku."

Bai ce, wane ne ya fi sarin gamawa, ko yawan aiki ba.

Haƙiƙa Annabinku wanda shi ne mafi kwaɗayin mutane a bisa alheri, kuma abin koyi kyakkyawa ga wanda ya kasance yana ƙaunar rahamar Allah da ladan ranar lahira, ya kasance ba ya ƙari a bisa raka'a goma sha ɗaya, ba a Ramadana ba, ba kuma a wanisa ba. A cikin sahihi Muslim daga Ibn Abbas R.A, ya ce, Annbi (ﷺ) ya yi sallar asham da sahabbansa a Ramadana, sannan ya bar hakan, don tsoron kada a wajabta wa mutane, sai kuma su kasa.

Hadisi ya inganta daga Amirul Muminina Umar ɗan Khaɗɗab, cewa, shi ya umarci Ubayyu ɗan Ka'ab da Tamimud Dari, su yi salla da mutane raka'a goma sha biyu. wannan shi ne adadin da Annabi (ﷺ) yake sallata. kuma Khalifa shiryayye Umar ɗan Khaɗɗabi, ya bi shi a cikinsa. Shi ne mafifincin adadin da ake sallar Asham da shi. Idan wani zai ƙara a kan haka don kwaɗayin lada ba wai don gujewa sunna ba, bayan ta bayyana a gare shi, ba za a yi masa inkari ba. Don an rawaito haka daga sashin magabata. Abin da kawai za a masa inkari akai shi ne, saurin da ya wuce iyaka, irin wanda wasu limamai suke yi, su jawo wa kansu da na bayansu asarar alheri.

Allah Ya datar da ni da ku zuwa cin moriyar waɗannan lokuta ta hanyar ayyukan biyayya kuma ya kare mu daga aikata munkarin ayyukan da munana. Ya shiryar da mu tafarkinsa madaidaici, ya nisantar da mu tafarkin Jahimu, ya sanya mu dage masu azumtar Ramadana, kuma mu kasance daga waɗanda suke tsayuwa dararensa, suna masu imani da neman lada, lallai Shi Mai yawan kyauta ne, Mai baiwa.

Abin da zan faɗa ke nan, ina neman gafarar Allah ga kaina da ku da ragowar Musulmai daga dukkan zunubai.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah, majiɓincin wanda ya ji tsoronsa. Duk wanda ya dogara a gare shi, to haƙiƙa zai isar masa. Wanda ya fake da shi, zai isar masa. Ina gode masa, ina shaidawa babu abin bautawa a gaskiya bisa cancanta sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa Annabi Muhammadu, bawansa ne, kuma Manzonsa ne, kuma masoyinsa ne, kuma badaɗayinsa ne. Allah Ya yi daɗin tsira da albarka a gare shi, da alayensa, da sahabbansa da wanda ya yi kira da kiransa, ya shiryu da shiriyarsa.

Bayan haka: Ya ku bayin Allah! Akwai fa'idoji masu ɗinmbin yawa a cikin azumi. Daga cikinsu akwai:

1. Durƙusar da zuciya. Domin yawan ƙoshi da abinci da biyan buƙata na shawa'a yakan gadarwa zuciya girman kai da taƙama da gafala.
2. killace zuciya don tunani da zikiri, domin biyan buƙata ta sha'awa kan sanya zuciya ta ƙeƙashe ta makance. Amma zama da yunwa na wani lokaci kan haskaka zuciya, ta zama mai taushi, gami da gusar da ƙeƙashewarta, ta zama killatacciya da tunani da zikirin Ubangiji.
3. Mawadaci yakan tuna irin ni'imar da Allah ya yi masa, ta hanyar da haka, zai tuna wanda shi kwata-kwata ma ba ya da komai. Wannan zai janyo masa godewa ni'imar Allah da wadatar da ya yi masa. Kuma zai sanya shi ya jiƙan ɗan uwansa mabuƙaci, ya taimaka masa da abin da ya sauwaƙa.
4. Azumi kan ƙuntata magudanar jini, waɗanda su ne magudanar shaiɗan a jikin ɗan'adam, domin shaiɗan yana gudana a jikin ɗan'adam a magudanar jini, sai azumi ya kwantar da wasi-wasin shaiɗan da karya tunzurin sha'awa da fushi.

Kusanci zuwa ga Allah ba ya cika ta hanyar barin abin da aka halatta, Sai bayan mutum ya bar abin da Allah ya haramta a kowane lokaci, kamar ƙarya da azalunci da ta'addanci a kan mutane da cin dukiyoyinsu da mutuncinsu. Don haka Annabi (ﷺ) ya ce, "Duk wanda bai bar faɗin zur, da aiki da shi ba, to Allah ba ya buƙatarr ya bar abincinsa da abin shansa.

Wani daga cikin magabata yana cewa: "idan ka yi azumi to jinka da ganinka da harshenka duk su yi azumi daga ƙarya da haram, ka bar cutar maƙoci. Ya zama kana da nutsuwa a yinin azumin naka. Kada ka sanya ranar azuminka, da ranar da

baka azumi, daidai wa daida, ta wajen rashin kamewa".

Magabata sun kasance idan suna azumi, sai su zauna a masallatai su ce; “Muna kare azuminmu ne ba za ma cin naman wani ba.”

Bayin Allah masu azumi suna kasu zuwa nau’i biyu.

Na Farko: Wanda ya bar abincinsa da abin shasa da sha’awarsa saboda Allah Ta’ala, yana fatan aljanna. To wannan yana ciniki ne da Allah, kuma ma’aikacinsa ne. Shi kuwa Allah, ba ya taɓar da ladan wanda ya kyautata aiki. Wannan mai azumi za a ba shi abin da ya so a cikin aljanna na abinci da abin sha, da mata. Allah Ta’ala ya ce:

﴿ كُلُواْ وَٱشۡرَبُواْ هَنِيٓـَٔۢا بِمَآ أَسۡلَفۡتُمۡ فِي ٱلۡأَيَّامِ ٱلۡخَالِيَةِ ٢٤ ﴾ [الحاقة: ٢٤].

(Ku ci ku sha, kuna masu farin ciki, saboda abin da abin da kuka gabatar a kwanakin da suka wuce).

Mujahid da waninsa sun ce, wannan aya a kan masu azumi ta sauka.

Bukhari da Muslim sun ruwaito daga Annabi (ﷺ), ya ce: “Lallai a cikin aljanna akwai wata ƙofa da ake ce mata Rayyan. Masu azumi ne kawai za su shiga ta cikinta, babu mai shiga cikinta banda su.” A wata ruwayar kuma, “Wanda ya shiga zai sha abin shan da ba zai yi ƙishi ba har abada.”

Nau’i na biyu daga masu azumi, waɗanda suke azumin gabarin duk wanda ba Allah. Sai ɗayansu ya kiyaye kansa da abin da kan ya ƙunsa, ya kiyaye cikinsa da abin da cikin ya tattara, ya riƙa tuna mutuwa da ruɓewa a ƙabari, ya nufi lahira da aikinsa, ya bar duk wani ƙale-ƙale na duniya. To wannan idin shi ne ranar gamuwa da Ubangijinsa, kuma farin cikinsa da gamuwa ne da shi:

﴿ مَن كَانَ يَرۡجُواْ لِقَآءَ ٱللَّهِ فَإِنَّ أَجَلَ ٱللَّهِ لَأٓتٖۚ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ ٥ ﴾ [العنكبوت: ٥].

(Wanda ya kasance yana burin gamuwa da Allah to haƙiƙi ajalinsa (da Allah Ya sanya) mai zuwa ne, kuma shi mai ji ne mai gani).

Ya ku bayin Allah! Haƙiƙa wata azumi yana da keɓance-keɓancensa saboda Alƙur’ani, kamar yadda Allah Ta’ala Ya faɗa:

﴿ شَهۡرُ رَمَضَانَ ٱلَّذِيٓ أُنزِلَ فِيهِ ٱلۡقُرۡءَانُ ﴾ [البقرة: ١٨٥]

“Watan Ramadana wanda aka saukar da Alƙur’ani a cikinsa.”

Haka nan ɗan Abbas ya ce: “Haƙiƙa an saukar da shi jimilla guda daga Lauhil Mahfuz zuwa Baitul Izzah a daren Lailatul Kadari, shaidar haka, faɗin Allah Ta’ala:

﴿ إِنَّآ أَنزَلۡنَٰهُ فِي لَيۡلَةِ ٱلۡقَدۡرِ ١ ﴾ [القدر: ١].

“Haƙiƙa mun saukar da shi a daren Lailatul Kadri”.

Zuhri ya kasance idan Ramadana ya shigo sai ya ce, “Ramadan wata ne kawai na karanta Alƙur’ani da ciyar da abinci.”

Ibnul Hakam ya ce: “Maliku y kasance idan Ramadana ya shiga yana ƙauracewa karantun hadisi, da zama da ɗaliban ilimi. Ya mai da hankalinsa a kan karantun Alƙur’ani daga Mus’hafi.”

Hakan nan ya ku bayin Allah, wannan watan horarwa ne a kan ciyarwa da yawan kyauta, domin ya zo a cikin Bukhari da Muslim daga ɗan Abbas Allah

ya yarda da shi ya ce: Annabi (ﷺ), ya kasance mafi kyautar mutane da alheri. Kuma lokacin da ya fi kyauta shi ne da Ramadana, yayin da Jibrilu ya gamu da shi. Jibrilu ya kasance yana gamuwa da shi a kowane Ramadana. Sai ya yi karatun Alƙur'ani tare da shi. Lallai Manzon Allah (ﷺ) ya fi sakakkiyar iska kyauta, yayin da Jibrilu yake gamuwa da shi.

Hikimar yawan kyautarsa a watan Ramadan ta haɗa da:

1. Darajar lokacin da ninka ladan aiki a cikinsa, domin aiki yana ƙara daraja da darajar lokaci, ko guri ,ko don darajar ma'aikin da taƙawarsa.
2. Haka nan akwai taimakawa masu azumi masu asham a cikinsu da maus zikiri a bisa ɗa'arsa. Sai mai taimaka musu ya cancanci ladansu, kamar yadda wanda ya shirya mayaƙi yake da ladan yin yaƙi, kuma wanda ya tsaya da kulawa da iyalinsa bayan tafiyarsa, yake da ladan yaƙi.
3. Sannan haɗa azumi da yana daga abin da ke wajabta aljanna. Ya zo a cikin Sahihi Muslim daga Abu Huraira, daga Annabi (ﷺ) cewa, "Waye a cikinku ya wayi gari yana azumi?" Sai Sayyidina Abubakar ya ce "Ni ne". Ya ce waye a cikinku ya raka jana'iza? Abubakar ya ce, "Ni ne". Waye a cikinku ya yi sadaka? Ya ce, "Ni ne". Ya ƙara cewa wanene a cikinku ya gaida mara lafiya? Sai Abubakar ya ce, "Ni ne". Sai Manzon ya ce, "Waɗannan abubuwan ba su taɓa haɗuwa ga mutum ɗaya ba face ya shiga aljanna."

Daga ciki azumi ba makawa a samu wani tasgaro ko tawaya a cikinsa, ita ko sadaka tana ɗora abin da ya shiga cikinsa na tawaya da tasgaro don haka, zakkar Fid-da-kai, ta wajaba a ƙarshen Ramadana domin tsarkake mai azumi daga yasasshiyar magana da batsa.

Allah Ka karɓi azuminmu da tsayuwar darenmu.

Allah ka gafartawa rayayyunmu da matattunmu, da ƙaraminmu da babbanmu, da namijinmu da macenmu, da mahalarcinmu da mafakinmu. Allah Ka yi salati da sallama a bisa Annabi Muhammadu, da alayensa da sahabbansa, ka yi sallama, sallama mai yawa.

SALLAH ITA CE MAFIFICIN BATU

Manufofin huɗubar

- Bayanin wajabcin kiyaye sallah da yadda ake yin hakan
- Bayanin Muhimmancin Sallah da Matsayinta a Musulunci
- Bayani a kan cewa Sallah alaƙa ce mai maimaituwa tsakanin bawa da Ubangijinsa
- Bayani kan tasirin Sallah bisa zuciya da gaɓɓai

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga shirrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammad bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammad (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Bayan haka:

Ya ku 'yan uwa musulmi, haƙiƙa ɗan adam rarrauna ne ba ya da ƙarfi sai lokacin da yake tare da Ubangijinsa, rundunoni na sharri suna fuskantar mutum, fito-na-fito tsakanin ingije sha'awa da kuma ruɗi na kwaɗayi, yaƙar tsaurin kai kan yi masa wahala. kuma daidaitacciyar hanya kan yi masa tsawo, kuma zango kan yi masa nisa, kuma ba shi da wata mafaka daga waɗannan igiyoyin ruwa masu awon ƙoƙarin awon gaba da shi face riƙo da Allah, da fakewa da shi.

Ya ku musulmi, haƙiƙa dacewa da wannan lokaci mai daraja da Musulmi suke ciki a wannan kwanaki ya sanya buƙatar yin bayani game da mafi muhimmancun ibada a musulunci, kuma mafi girmanta wajan kusanci da Allah mai maɗaukakin sarki. wannan kuwa ita ce ibadar da Annabinmu Muhammadu kan fake zuwa gare ta yayin da wani lamari ya tsananta gare shi. Maganarmu a yau za ta kasance ne

game da rukuni na biyu daga rukunan musulunci, kuma jigonsa wanda wannan addinin ya ginu a kansa, kuma ita ce farkon abin da Allah ya wajabta a ibadodi, kuma ita ce farkon abin da za a yi wa bawa hisabi a kansa ranar alƙiyama, kuma ita ce ƙarshen wasiyar da Ma'aikin Allah (ﷺ) ya yi wa al'ummarsa wasiyya da shi yayin rabuwarsa da duniya. Inda ya ce a lokacin da zai cika: "Ina jaddada muku lamarin sallah! Ina jaddada muku lamarin sallah da kuma lamarin bayinku". Ahmad Da Abu Dawud da Ibn Majah suka ruwaito shi. Kuma ita ce ƙarshen abin da za a rasa daga addini; idan ta tozarta to addini gaba ɗayansa ya tozarta.

Sallah (ita ce ibadar) nan da falalarta ta cika kunnuwan halittu, saboda abin da aka tanadarwa masu kiyayeta. An rawaito daga Abu Umamata Allah ya ƙara yarda a gare shi, cewa Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Duk wanda ya fita daga gidansa yana mai tsarki zuwa sallar farilla, to zai sami ladan wanda ya yi harama da hajji,wanda kuma yafita zuwa nafilar walha babu abin da ya tashe shi sai ita, to zai sami ladan wanda ya yi umara, kuma salar da aka yi bayan wata sallar, alhali babu yasasshiyar magana tsakaninsu, za a rubuta ta a cikin illiyyuna". Abu Dawud ne ya rawaito shi da isnadi kyakkyawa.

Haka nan Annabi mai (ﷺ) ya ce "Sallah ita ce mafificin abu, don haka duk mai mai son yawaita ta, to sai ya yawaita". Ɗabarani ne ya rawaito a cikin Al-Ausat, kuma hadisi ne kyakkyawa .

Muhimmancin sallah na ƙara bayyana ne cikin kasancewarta an saukar da ita daga birbishin sammai bakwai, ba tare da an aiko ta hanyar saƙo ba, da kuma kasancewarta mai sadarwa tsakanin bawa da Ubangijinsa. Sallah ta kasance ita ce abin faranta ran masana Allah, kuma hutun zukatansu, ga ta kuma tana hani ga barin alfasha da mummunan aiki. Allah Ta'ala Ya ce:

﴿إِنَّ ٱلصَّلَوٰةَ تَنۡهَىٰ عَنِ ٱلۡفَحۡشَآءِ وَٱلۡمُنكَرِۗ﴾ [العنكبوت: ٤٥].

"Haƙiƙa sallah tana hana alfasha da mummunan aiki".

Allah mai tsarki da ɗaukaka Ya yi kira zuwa kiyayeta ya ce:

﴿حَٰفِظُواْ عَلَى ٱلصَّلَوَٰتِ وَٱلصَّلَوٰةِ ٱلۡوُسۡطَىٰ وَقُومُواْ لِلَّهِ قَٰنِتِينَ ٢٣٨﴾ [البقرة: ٢٣٨].

(Ku kiyaye salloli, da kuma sallah ta tsakiya, kuma ku tsaya kuna masu biyayya ga Allah).

Kuma an sanya farin cikin al-Musɗafa (ﷺ) a cikinta, domin Anas (R.A.) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "An sanya mini ƙaunar mata da turare, kuma an sanya farin cikina a cikin sallah". Bukhari da waninsa suka rawaito shi.

Kai nutsuwarsa ma (ﷺ) ba ta kasance ba face a cikinta, don haka ita ce matsera idan wani lamari ya tsananta a gare shi, kuma ita ce mafaka idan gajiya ta samu, sai mai tsira da amincin Allah yakan ce: "Ya Bilali tashi ka yi iƙamar sallah, ka sama mana hutu da ita)) .

Sasannin mai sallah sun cika da kwarjini, kuyaɓunsa sun haskaka da hasken imani, annashuwar imani ta cika zuciyarsa, yana tadabburin Alƙur'ani a cikin sallarsa, kuma yana ɗaukaka addu'arsa, kuma yana ƙaskantar da kai ga Ubangijinsa a cikin ganawarsa, damuwarsa ta tattara ne a kan lamarin Allah, kuma ya samu

farincikinsa da (yardar) Ubangijinsa gare shi, dan haka ya kusantar da shi.

Wannan kaɗan ne daga cikin girman sallah a cikin wannan addini, kuma wannan ɗan tsakure ne daga cikin ma'anoninta a zukantan muminai. Sai dai duk da haka za ka ga da yawa daga cikin musulmi suna sakaci cikin ba da wannan farilla ma girma. Suna sallah amma basa kyautata sallarsu; suna caccakata caccakar hankaka, ba sa nutsuwa, kuma ba sa tuna Allah a cikinta sai kaɗan.

Daga cikin alamomin sakaci da sallah akwai yawan waiwaye a cikin sallah, da soshe-soshen jiki. Ko kuma ɗan kasuwa yana sallah amma idonsa yana a kan kayansa, to waɗannan, ko da a zahiri suna sallah da jikkunansu, to amma a haƙiƙa ba sallah suke ba. Domin Annabi (ﷺ) ya ce wa mutumin da ba ya nutsuwa a cikin sallarsa: “Ka koma ka sake sallah domin kai ba ka yi sallah ba”.

Ya ku bayin Allah; haƙiƙa akwai wasu abubuwa da sukan janyo halartowar zuciya ga mai yin sallah, daga cikin su akwai: halarto da ma'anar abin da (shi mai sallar) yake faɗa kuma yake aikatawa a cikin sallarsa: misali: idan ya yi kabbara ya ɗaga hannayansa, ya tuna cewa wannan girmamawa yake ga Allah, kuma idan ya sanya hannun dama a kan na hagu ya tuna cewa wannan ƙasƙantar da kai yake a gabansa. Kuma idan ya yi ruku'u to yana girmama Allah ne, kuma idan ya yi sujjuda to wannan ƙasƙantar da kai ne gaba ga ɗaukakar Allah.

An karɓo daga Abu Hurairata (R.A.) daga Annabi)ﷺ(ya ce: "Allah Ta'ala Ya ce, "Na raba sallah tsakanina da bawana gida biyu, kuma bawana zai sami abin da ya roƙa (a cikinta)". Yayin da bawa ya ce, ﴿ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ۝٢﴾. Sai Allah Ta’ala ya ce, «Bawa na ya gode mini». Idan bawa ya ce, ﴿ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ ۝٣﴾, sai Allah Ta’ala ya ce, «Bawana ya yabe ni». Idan kuma ya ce,
﴿مَٰلِكِ يَوۡمِ ٱلدِّينِ ۝٤﴾, sai Ya ce, «Bawana ya girmama ni», wani karan kuma ya ce, «Bawana ya fawwala lamarinsa zuwa gare ni». Idan ya ce:
﴿إِيَّاكَ نَعۡبُدُ وَإِيَّاكَ نَسۡتَعِينُ ۝٥﴾, sai ya ce: «Wannan tsakanina ne da bawana, kuma bawana zai sami abin da ya tambaya». Idan ya ce,
﴿ٱهۡدِنَا ٱلصِّرَٰطَ ٱلۡمُسۡتَقِيمَ ۝٦ صِرَٰطَ ٱلَّذِينَ أَنۡعَمۡتَ عَلَيۡهِمۡ غَيۡرِ ٱلۡمَغۡضُوبِ عَلَيۡهِمۡ وَلَا ٱلضَّآلِّينَ ۝٧﴾, sai ya ce wannan na bawana ne kuma bawana zai sami abin da ya roƙa». Muslim ne ya ruwaito shi.

Yayin da ka ce: (سبحان ربي العظيم وبحمده) ko ka ce, (سبحان ربي الأعلى وبحمده), ko da kuwa ka faɗe su ne da murya ƙasa-ƙasa to haƙiƙa Allah yana jin duk wata magana da kake faɗa, kuma yana ganin duk wani aiki da kake aikata wa, komai ƙankantarsa. Kuma ya san duk abin da kake tunani a cikinsa ko da kaɗan ne. Kuma yayin da ka kalli gurbin sujjadarka to, Allah yana ganinka. Kuma yayin da ka yi nuni da yatsanka lokacin ambaton Allah a cikin tahiya; to Allah yana ganin nuninka, domin shi Maɗaukakin Sarki, Shi ne Mai kewayewa ga bawansa, da sani da iko da gudanarwa, da ji da gani, da wanin wannan na daga ma’anonin Rububiyyarsa.

Kuma yana daga abin da zai taimaka masa wajan tsoron Allah a cikin sallah da nutsuwa a cikinsa, da ba da ita a bisa mafi cikar kama shi ne, ya roƙi Allah ya

taimake shi a bisa kyautata ibadar, domin Imamu Ahmad da Abu Dawud sun fitar da hadisi daga Mu’azu ɗan Jabal: cewa Manzon Allah (ﷺ) ya riƙi hannunsa kuma ya ce, "Ya Mu'azu wallahi ni ina sonka, wallahi ni ina sonka". Sai ya ce, "Ina maka wasici kada ka bari bayan kowacce sallah ka ce, Ya Ubangiji ka taimake ni bisa ambatonka, da gode maka, da kyautata bautarka)) .

Kuma yan daga abin da yake taimakawa bisa tsoron Allah (a cikin sallah), imanin bawa cewa tsoron Allah shi ne ruhin sallah, Allah Ta'ala ya ce,

﴿ ٱلَّذِينَ هُمۡ فِي صَلَاتِهِمۡ خَٰشِعُونَ ٢ ﴾ [المؤمنون: ٢]

Ma’ana: (Waɗanda suke masu tsoron Allah a cikin sallarsu).

Ina faɗin abin da kuke ji, kuma ina neman gafarar Allah ga kaina da ku, da kuma sauran musulmi daga kowane zunubi, kuma ku nemi gafararsa lallai shi ne mai yawan gafara mai yawan rahama.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, majiɓincin nagartattu, mai gafarta zunubin masu neman gafara, mai ɗora karayar karyayy. Kuma Allah ya yi tsira da aminci a bisa shugaban masu tsoron Allah, kunma shugaban masu neman gafara, da kuma alayensa da sahabbansa gaba ɗaya, da kuma waɗanda suka bi tafarkinsu har zuwa ranar sakamako, bayan haka.

Ya ku bayin Allah! Haƙiƙa sallah ita ce maraba tsakanin kafirci da imani, domin Jabir ya ruwaito cewa, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Haƙiƙa abin da ke tsakanin mutum da kafirci ba wani abu ba ne face barin sallah”. Muslim ne ya rawaito shi .

An karɓo daga Buraida ya ce: Na ji Ma'aikin Allah (ﷺ) yana cewa: “Alƙawarin da ke tsakaninmu (mu musulmi) da su (kafirai) shi ne sallah, duk wanda ya bar ta haƙiƙa ya kafirta”. Ahmad da Abu Dawud da Nasa'i da Tirmizi da Ibn Majah ne suka rawaito shi, kuma Tirmizi ya ce: Hadisi ne kyakkyawa ingantacce.

An karɓo daga Abdullahi dan Shaƙiƙ al-Uƙaili (R.A.) ya ce: "Sahabban Muhammadu (ﷺ) sun kasance ba sa ganin cewa akwai wani aiki da barinsa yake zama kafirci ban da sallah". Tirmizi ne ya rawaito shi .

Ya ku bayin Allah! Haƙiƙa yana daga shiriyar Annabi (ﷺ) zaburarwa a kan yin sallah a cikin jama'a, da ƙarfafa wajabcinta, da bayanin falalarta; Muslim ya rawaito Daga Abi Huraira ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Sallah a cikin jama'a ta ɗara sallar mutum a cikin gidansa, da sallar sa a kasuwarsa da daraja ashirin da ɗoriya, dalilin haka shi ne idan ɗayansu ya yi alwala, ya kyautata alwalar, sannan ya zo masallaci, babu wani abu da ya zaburar da shi sai sallah, kuma ba ya nufin komai face sallah, ba zai yi taku ɗaya ba face an ɗaukaka masa daraja ɗaya da shi, kuma an sarayar masa da laifi ɗaya da shi, har sai ya shiga masallaci. Kuma idan ya shiga masallaci zai zamo cikin (ladan) sallah matuƙar sallah ce ta tsare shi, kuma mala'iku suna yin addu'a a bisa ɗayanku matuƙar ya kasance a mazauninsa da ya yi sallah a cikinsa, suna cewa: “Allah ka gafarta masa, Allah ka karɓi tubansa, matuƙar bai cuci wani ba a cikinsa, matuƙar alwalarsa ba ta karye ba”.

Kuma mai tsira da amincin Allah ya yi gargaɗi a kan ƙin amsawa mai kiran sallah ba tare da wani uzuri ba. Domin an karɓo daga Ibn Abbas (R.A.) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Wanda ya ji kiran sallah sannan bai amsa ba, to ba shi da sallah, sai dai idan yana da wani uzuri”. Ibn majah ne ya rawaito shi, da Ibn Hibban a cikin Sahihinsa, da Hakim kuma ya ingantan shi.

Duk sanda aka samu mutane uku zuwa sama, to sallar jam'i wajibi ce a kansu, a birni suke ko a ƙauye, in ko ba haka ba shaiɗan zai mallake su, ya ɓatar da su ga barin tafarki madaidaici, domin an karɓo daga Abud Darda'i ya ce: Nia ji Ma'aiki (ﷺ) yana cewa: "Babu wasu mutum uku a cikin birni ko ƙauye da ba a tsaida sallah a cikinsu face shaiɗan ya mallake su, don haka na hore ku da lizimtar jama'a, domin ita kura tana cin dabbar da ta yi nisa ne". Ahmad da Abu Dawud da Nasa'i suka rawaito shi.

An karɓo daga Abu Huraira Allah ya ƙara yarda a gare shi ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Haƙiƙa na yi nufin na umarci matasa na su tattaro min kawuna na itatuwa, sannan in zo wa mutanan da suke sallah a gidaddajinsu ba tare da suna da wata larlura ba, na ƙone musu gidajen".

Sai aka cewa Yazid wato ibn al-A'asam-: Juma'a yake nufi ko wata sallar? Ya ce: kunne na ya kurumce in ba na ji Aba Hurairah yana rawaito shi daga Manzon Allah (ﷺ) ba, bai ambaci Juma'a ko wata salla ba. Muslim da Abu Dawud suka rawaito shi, da kuma ibn majah da Tirmizi, amma shi a taƙaice.

Kuma an rawaito daga ɗan Mas'ud ya ce: "Da za a ce ku yi sallah a cikin gidajanku kamar yadda wannan mai noƙewar yake yi a gidansa, da kun bar sunnar Annabinku, da kuma za ku bar sunnar Annabinku da kun ɓata". Muslim da Abu Dawud suka rawaito shi.

Ya ku bayin Allah! Ku kiyaye sallah ta hanyar ba da rukunanta, da sharaɗanta da wajibanta, sannan ku cika ta ta hanyar aikata mustahabbanta, domin sallah ita ce jigon addini, kuma babu addini ga wanda babu sallah a gare shi; Allah Ta'ala Ya ce

﴿ حَٰفِظُواْ عَلَى ٱلصَّلَوَٰتِ وَٱلصَّلَوٰةِ ٱلۡوُسۡطَىٰ ﴾ [البقرة: ٢٣٨].

Ma’ana: (Ku kiyaye salloli da kuma sallar tsakiya).

Ina neman tsari da Allah daga shaiɗani abin la’anta, da sunan Allah mai rahama mai jinƙai:

﴿ قَدۡ أَفۡلَحَ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ١ ٱلَّذِينَ هُمۡ فِي صَلَاتِهِمۡ خَٰشِعُونَ ٢ وَٱلَّذِينَ هُمۡ عَنِ ٱللَّغۡوِ مُعۡرِضُونَ ٣ وَٱلَّذِينَ هُمۡ لِلزَّكَوٰةِ فَٰعِلُونَ ٤ وَٱلَّذِينَ هُمۡ لِفُرُوجِهِمۡ حَٰفِظُونَ ٥ إِلَّا عَلَىٰٓ أَزۡوَٰجِهِمۡ أَوۡ مَا مَلَكَتۡ أَيۡمَٰنُهُمۡ فَإِنَّهُمۡ غَيۡرُ مَلُومِينَ ٦ فَمَنِ ٱبۡتَغَىٰ وَرَآءَ ذَٰلِكَ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡعَادُونَ ٧ وَٱلَّذِينَ هُمۡ لِأَمَٰنَٰتِهِمۡ وَعَهۡدِهِمۡ رَٰعُونَ ٨ وَٱلَّذِينَ هُمۡ عَلَىٰ صَلَوَٰتِهِمۡ يُحَافِظُونَ ٩ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡوَٰرِثُونَ ١٠ ٱلَّذِينَ يَرِثُونَ ٱلۡفِرۡدَوۡسَ هُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ ١١ ﴾ [المؤمنون: ١ – ١١].

(Haƙiƙa muminai sun rabauta, wannan da suke tsoron Allah a cikin sallarsu) har zuwa faɗinsa maɗaukakin sarki: (da kuma waɗanda suke kiyaye sallarsu. waɗannan su ne masu gado. Waɗanda suke gadar aljannar Firdausi, su masu dauwama ne a cikinta).

AMBATON ALLAH TA'ALA

Manufofin hudubar

- Bayanin girman sha'anin zikiri a rayuwar musulmi.
- Kwadaitarwa a kan ambaton Allah a kowane hali.
- Karfafa alakar bawa da Ubangijinsa.
- Gargadi kan gujewa ma'abota gafala da mantuwa

Huduba Ta Farko

Dukkan Yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma mua neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan aiyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar dashi, wanda kuma ya atar babu mai shiryar da shi, kuma ina shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai allah, shi kadai ne bashi da abokin taraiya, kuma ina shaidawa cewa Annabi Muhammad bawansane manzonsane, (Yaku wadanda kuka bada gaskiya kuji tsoron Allah yadda ya cancanta aji tsoronsa, kada ku mutu face kuna Musulmi). (Yaku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicce ku daga rai guda daya kuma ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yada maza da mata daga gare su (su biyu) kuji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya dashi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku wadanda suka yi imani kuji tsoron Allah kuma ku fadi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku aiyukanku, kuma ya gafarta muku zunubanku. Wanda ya bi Allah da manzonsa hakika ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawun shiriya shiriyar Annabi Muhammadu (ﷺ) kuma mafi sharrin al'amura (a addini) kagaggunsu, kuma duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Bayan haka, ina yi muku wasiyya ya ku mutane, da kaina da tsoron Allah Mai buwaya da daukaka, ku ji tsoronsa a ɓoye da sarari, ku ji tsoronsa, ku bauta masa, ku yi sujadda a gare shi, ku aikata alheri, tabbas za ku rabauta.

Ya ku mutane! Hakika zukatan 'yan Adam kamar sauran abubuwa ne masu rai, suna da bukatar abubuwan da duk mai rai yake da bukatar don ya rayu, ya haɓaka. Kuma duk masu hakali sun hadu a kan cewa zukata kan yi tsatsa kamar yadda karfe kan yi tsatsa, kuma suna jin kishirwa kamar yadda tsiro kan ji kishirwa. Kuma suna bushewa kamar yadda hantsa kan bushe. Don haka, su ma suna bukatar a rika goge masu tsatsarsu. A shayar da su a gusar musu da kishi. Mutum a wannan rayuwa, kewaye yake da makiya ta kowane gefe, ga zuciyarsa mai yawan umartarsa da mummuna aiki, tana tura shi ramin hallaka. Hakan nan son zuciyarsa da shaidaninsa suma suna nasu kokar. Don haka yake cikin matukar bukatar abin da zai kare shi ya amintar da shi, ya kwantar masa da tsoro, ya sanya

nutsuwa a zuciyarsa. Kuma mafificin abin da yake yaye irin waɗannan cututtuka, yake karewa daga maƙiya, shi ne ambaton Allah, da yawaita wannan ambaton ga mahaliccinta abin bautawarta. Domin Shi ne, mai goge zukata, mai darje su, kuma maganinsu idan cututtuka su sun lulluɓe su.

Ibnulk Kayyim Allah ya jiƙansa ya ce "Na ji shakhul islam Ibn Taimiyyah Allah ya tsarkake sirrinsa, yana cewa: "Zikiri ga zuciya kamar ruwane ga kifi, yaya kifi zai kasance idan ya rasa ruwa?"

Ya ku bayin Allah! Alƙa tsakanin bawa da Ubangijinsa ba ta taƙaita a kan lokacin ganawa da shi da safe ba ko da yamma kawai. Sannan daga nan kuma mutum ya tafi harkarsa ta duniya yana abin da ya ga dama ba tare da wani ƙaidi ko takunkumi ba. Sam a'a, yin haka addini ne na boge ba na gaskiya ba. Alaƙa ta gaskiya tsakanin bawa da Ubangijinsa ita ce, mutum ya ambaci Ubangijinsa ako ina yake, kuma wannan zikirin ya kasance yana sa masa takunkumi na bin umarnin Allah da haninsa, kuma yana wa ɗan adam bushara da rauninsa, kuma yana taimaka masa a wajen fakewa zuwa Ubangijinsa cikin duk abin da zai biyo masa.

Ya ku bayin Allah!

Haƙiƙa addini maiƙaƙƙe ya zaburar a kan musulmi ya kasance ƙulla alaƙa da Ubangijinsa, don ruhinsa ya rayu, zuciyarsa ta tsarkaka, ya sami taimako da dace daga gare shi. Don haka, nassosi da suke kira zuwa ga ya waita zikiri suka zo a cikin Alƙur'ani da sunnar Annabi (ﷺ). Allah Ta'ala Ya ce

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱذۡكُرُواْ ٱللَّهَ ذِكۡرٗا كَثِيرٗا ٤١ وَسَبِّحُوهُ بُكۡرَةٗ وَأَصِيلٗا ٤٢ ﴾ [الأحزاب: ٤١ – ٤٢].

(Ya ku waɗanda suka yi imani, ku ambaci Allah ambato mai yawa. Kuma ku tsarkake shi da safiya da maraice).

Hakanan Allah ya ce,

﴿ وَٱلذَّٰكِرِينَ ٱللَّهَ كَثِيرٗا وَٱلذَّٰكِرَٰتِ أَعَدَّ ٱللَّهُ لَهُم مَّغۡفِرَةٗ وَأَجۡرًا عَظِيمًا ٣٥ ﴾ [الأحزاب: ٣٥].

(Da masu ambaton Allah maza, da masu ambato Allah mata, Allah ya tanadar musu da gafara da lada mai girma). Kuma Allah Ya ce,

﴿ وَلَذِكۡرُ ٱللَّهِ أَكۡبَرُ ﴾[العنكبوت: ٤٥].

(Kuma lalle ambaton Allah shi ne mafi girma).

Ya ce, (kalmomi biyu ababen so ne ga Allah mai rahama, sauƙaƙa ne a kan harshe, masu nauyi ne a kan ma'auni: subhanallahi wabihamdihi, subhanallahil azim). Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.

Kuma ya ce "Yanzu ba na ba ku labarin mafi alherin ayyukanku ba, kuma mafi tsarkakarsu a wajen Mamallakinku ba, kuma mafi ɗaukaka ga darajarku, kuma mafi alheri a gare ku fiye da zinare da azurfa, kuma mafi alheri fiye da ku gamu da abokan gabarku ku doki wuyayensu, su ma su doki wuyayenku! Suka ce, "Wannan mene ne kuwa, ya Ma'aikin Allah?". Sai ya ce, "Ambaton Allah Mai buwaya da ɗaukaka". Ahmad ne ya raiwato shi.

Kuma Annabi (ﷺ) ya ce, "Wanda ya ce, Subhanallahi wa bi hamdihi za a dasa masa dabinai a Aljanna". Tirmizi ne ya rawaito shi.

Ya bayin Allah! Da zikiri ne ake ije cututtuka, ake yaye baƙƙan ciki, kuma masifu kan zama masu sauƙi a kan wanda suka aukawa. Allah ya ƙawata harasan masu zikir da shi, kamar yadda ya ƙawata ganin masu gani da haske. Gafalallen harshe, kamar makahon ido ne, ko kurman kunne, ko shanyayyen hannu.

Ambaton Allah mai buwaya da ɗaukaka buɗaɗɗiyar kofa ce tsakanin bawa da Ubanagijinsa, matuƙar bawa bai rufe ta da gafalarsa ba.

Hasannul Basari Allah ya jiƙansa ya ce, "Ku nemi daɗin ɗanɗano cikin abubuwan uku: cikin Sallah, da zikiri da karatun alƙur'ani, idan kun samu to, in ba haka ba to ku sani cewa ƙofar a rufe take".

Ya ku musulmi! Haƙiƙa zunubai manyansu da ƙananansu ba zai yiwu 'yan'adam su aikata su ba face sai cikin hali na gafala da manta ambaton Allah; domin ambaton Allah Ta'ala, tsani ne na cikakkiyar rayuwa wanda zai yi wuya, mutum yana tare da ita, kuma ya jefa kansa cikin tanderun jahimu, ko fushi da uƙubar Ubangiji mai girma. A ɗaya gefen, mai barin zikiri, da mai manta shi, shi matacce ne, shaiɗan bai damu a wane juji zai jefa shi ba.

Allah Ta'ala ya ce:

﴿ وَمَن يَعۡشُ عَن ذِكۡرِ ٱلرَّحۡمَٰنِ نُقَيِّضۡ لَهُۥ شَيۡطَٰنٗا فَهُوَ لَهُۥ قَرِينٞ ٣٦ ﴾ [الزخرف: ٣٦].

(Kuma duk wanda ya makance ga barin ambaton mai rahama za mu hore masa shaiɗani sai ya zama abokinsa).

Kuma Allah Ta'ala ya ce,

﴿ وَمَنۡ أَعۡرَضَ عَن ذِكۡرِي فَإِنَّ لَهُۥ مَعِيشَةٗ ضَنكٗا وَنَحۡشُرُهُۥ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ أَعۡمَىٰ ١٢٤ ﴾ [طه: ١٢٤].

(Duk wanda ya kau da kai ga barin ambaton Allah mai rahama, to yana da rayuwa mai ƙunci, kuma za mu tashe shi ranar alƙiyama a makaho).

Ibn Abbas (R.A) ya ce "Shaiɗan a gurfane yake da a kan zuciyar ɗan adam. Idan ya gafala ya yi rafkanarwa sai ya yi masa wasi-wasi, idan kuwa ya mabaci Allah sai ya noƙe"

Wani mutum ya kasance a bayan Manzon Allah (ﷺ) a kan wata dabba, sai dabbar ta yi tuntuɓe da su, sai mutumin ya ce "Shaiɗan ya tabe". Sai Annabi (ﷺ) ya ce masa, "Kada ka ce, Shaiɗan ya tabe, domin alokacin zai ciko har ya zama kamar girman gidan nan. Ka dai ce, Bismillahi, to alokacin sai ya ƙanƙance har ya koma tamkar ƙuda" Ahmad ne ya rawaito da Abu Dawud kuma ingatancce ne.

Ibnul Kayyum Allah ya jiƙansa ya rawaito daga sashin magabata; cewa, idan zikiri ya kankama a zuciya, to idan shaiɗan ya kusanto mutum, sai mutumin ya kada shi, kamar yadda shaiɗan yake kada mutum. Sai shaiɗanu su taru a kansa, suna cewa, me kuma ya sami wannan? Sai a ce, ai mutum ne ya shafe shi"

Yawaita ambatun Allah maganin munafunci ne, kuma 'yantuwa ne daga ribatar son zuciya, kuma dama ce da ke sadar da bawa zuwa yardar Ubangijinsa, da abin da ya tanadar masa na ni'ima madauwamiyya. Zikiri makami ne da ake ba wa mutum, daga makamai na yaƙi waɗanda ba sa dakushewa. Domin hadisi ya tabbata daga Annabi (ﷺ) game da buɗe Kusɗandiniyya, ya ce, "Yayin da suka zo ganuwarta, sai su sauka, ba za su yi yaƙi da makami ba, ba za su yi jifa da kibiya ba. Za su ce, la'ilaha illaha wallahu akbar: sai ɗaya daga ɓangarorinta biyu na ganuwa ya faɗi.

Sannan su ƙara cewa, La’ilaha illallah, wallau akbar, sai ɗaya ɓangaren kuma shi ma ya faɗi. Sannan su faɗa a karo na uku: la’ilaha illallah wallahu akabar, sai a buɗe musu, sai su shige ta, su sami ganima…” Muslim ne ya rawaito shi.

Ya ku mutane! Ambaton Allah Ta’ala shi ne mafi darajarar abin da zai ɗarsu a zuciya, kuma mafi tsarkin abin da baki zai furta, kuma mafi ɗaukakar abin da hankalin wayayyan musulmi zai haskaka da shi. Mutane gabaɗaya sukan sami damuwa a rayuwarsu, ko su sami kasawa, saboda damuwa da za ta kewayesu ta ko’ina, alhali su raunana ne ba za su iya ɗauke wa kansu wannan wahalhalun ba idan sun sauko musu, ko su ije su idan sun kusa afko musu. Duk da haka ambaton Allah yana raya jin girman Allah a zukatansu, da jin cewa shi mai iko ne a bisa kowane abu, kuma babu wani abu da zai kuɓuce daga ƙarfinsa, kuma shi ne yake yaye abin da ya sami mutum na wahala. A yayin nan ne mai zikiri zai ji farin ciki da nutsuwwa sun lulluɓe zuciyarsa da gaɓɓansa. Allah yana cewa,

﴿ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَتَطۡمَئِنُّ قُلُوبُهُم بِذِكۡرِ ٱللَّهِۗ أَلَا بِذِكۡرِ ٱللَّهِ تَطۡمَئِنُّ ٱلۡقُلُوبُ ٢٨ ﴾ [الرعد: ٢٨].

(Waɗanda suka yi imani kuma zukatansu ke nutsuwa da ambaton Allah. A saurara lallai da ambaton Allah ne zukata kan nutsu).

Ya kai musulmi! Ba za ka ji tsoron wani ɓacin rai ba ko damuwa, matuƙar kana tare da ambaton Allah. Allah mai girma da ɗaukaka yana faɗa a ɗikin hadisi ƙudusi; “Ni ina nan wajan zaton bawa ne, kuma ina tare da shi idan ya ambace ni, idan ya ambace ni a ransa zan ambace shi a raina. Idan ya ambace ni a cikin taro, zan ambace shi a ciki taro mafi alheri daga wannan taron nasa”. Bukhatari da Muslim ne suka rawaito shi.

Sayyadina Ali da Nana Faɗima (R.A) sun kai kuka wajen Manzon Allah na abin da take fuskenta na niƙa da aiki mai wahala, sai ta roke shi ɗan aiki, sai Manzon Allah ya ce, “Yanzu ba na shiryar da ku zuwa abin da ya fi ɗan aiki alheri ba, idan za ku kwanta, ku yi Tasbihi talatin da uku, ku yi Tahmidi talatin da uku, ku yi Takbiri talatin da huɗu, wannan ɗari kenan a harshe amma dubu a ma’auini. Aliyu ya ce “Ban taɓa barin su ba tun da na ji su daga Annabi (ﷺ), wani mutum ya ce “Har a daren yaƙin Siffin?" Ali ya ce, "Har a daren yaƙin Siffin". Ahmad ya rawaito shi. Daren Siffin: shi ne daren yaƙi mai tsanani da ya afku tsakaninsa da abokan faɗansa, mutanen Sham. Allah ya yarda da su baki ɗaya.

Ya ku bayin Allah! Da ɗayanmu zai kallafawa kansa ganin wani abu da kan faru akai-akai, wato irin mutane da gafala da ƙarancin zikiri kan halakar da su. Yanzu dubi irin duhun gidajen da suka wafinta daga ambaton Allah! yanzu dubi marasa lafiya galaɓai tattu, Allah ya sallamasu ga kaeukansu, yayin da suka manta shi. Sai ba suka kasa ɗora ƙashin da Allah ya karya. Suka ƙara cuta a kan cutarsu, yanzu dubi waɗanda ake yi wa sihiri maza da mata, hannayensu masu sihiri da dabo da maƙaryata 'yan damfara sun kai ga cimma su. Sun raba su da jin daɗin rayuwa. sun raba su da kwanciyar hankali, sun rushe musu gidan rayuwa na sa'ada gabaɗaya.

Me ya hana ɗayanaku ya yi tunani a game da waɗannan da aka jarrabe su da shafar maridan aljanu ba shaiɗanun suna jin raɗaɗi suna birgima kamar masu birgima a kan ƙonannanan rairayi. Shaiɗanu suna makarsu. Sun kasa zama guri guda, kuma sun kasa samun kwanciyar hankali. Ku faɗa min gaskiya – Ya ku bayin Allah - ɗayanku ba zai tambayi kansa cewa, mai hana waɗannan wahalallu ambaton Allah ne? Me hana su fakewa a cikin ƙarfafan ganuwoyi na Ubangiji, waɗanda su ne za su magance musu duk wata cuta mai karya garkuwar jiki?! Shin waɗannan ba su sani ba, cewa shiga gida da fita daga cikinsa yana da zikiri? Shin ba su sani ba cewa, bacci yana da zikiri, hakanan tashi daga barci yana da nashi? Shin ba su sani ba cewa, safiyar kowace rana tana da zikiri, hakanana ma maraice, kai hatta tarawa da iyalinsa akwai zikiri, kai har shiga ban ɗaki da fitowa daga cikinsa? Kowanne abu yana da zikiri, yadda ya zo mana daga ma'aiki (ﷺ) wanda ya sani ya sani, wanda ya jahilta ya jahilta.

Ya ku musulmi ku ji tsoron Allah "Ku ambaci Allah ambato mai yawa, tabbas za ku rabauta.

Ina faɗar abin da kuke ji, kuma ina neman gafarar Allah ga kaina da sauran musulmi daga duk zunbai. Ku nemi gafararsa. Lallai shi mai gafara nema mai yawan rahama.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah, yabo daddaɗa mai albarka kamar yadda Ubangijinmu yake so kuma Ya yarda. Kuma ina shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah Shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Yabo da kirari nasa ne a duniya da lahira. Kuma ina shaidawa cewa Muhammadu bawansa ne kuma Manzonsa ne, ya aiko shi da rahama da shiriya, Allah ya yi tsira da aminci a gare shi, da iyalinsa tsarkaka, da sahabbansa masu girma, da mabiyansu, da waɗanda suka biyo bayansu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

Ya ku bayin Allah!

A cikin mutane akwai waɗanda suke ambaton Allah, sai dai su ba su fahimtar ma'anar zikirin, sai zukatansu suka kasa sanin girman Allah da haƙiƙanin matsayinsa, alhali shi ambaton Allah zance ne da tsigar masu tsoron Allah ke tashi da shi, sannan fatar jikinsu da zukatansu su tausasa zuwa ga ambaton Allah. Sai dai mutane saboda abin da suka saba da shi, da abin da suka jahilta na ma'anarsa, suna nanata ambaton Allah abakinsu kamar yadda suke nanata kowace irin magana ta yau-da-gobe. In ba haka ba shin wani ya taɓa tunanin ma'anar (Allahu Akbar) wadda take ita ce jigon Takbiri, kuma ita ce farkon abin da aka ɗorawa Manzo (ﷺ), yayin da aka umarce shi da gargaɗi, Allah ya ce,

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلۡمُدَّثِّرُ ١ قُمۡ فَأَنذِرۡ ٢ وَرَبَّكَ فَكَبِّرۡ ٣ ﴾ [المدثر: ١ – ٣].

(Ya kai wannan na lulluɓe. Ka tashi ka yi gargaɗi. Kuma ka girmama Ubangijinka).

Lallai ita kalma ce mai girma, tana raya matacciyar ƙasa. Sautinta yana ɗa rugugi kamar rugugin kogi mai tumbatsa, ko ma ta fi haka. Lallai ita kalma ce da ya wajaba ta yi rugugi a kunnen duk wani ɓarawo, don hannunsa ya raurawa, jikinsa ya girgiza. Hakanan ta yi rugugi a kunnen duk wani azzalumi ɗan ta'adda mai girman kai, don ya wa'azantu in yana cikin masu wa'zantuwa, ya san cewa akwai wani Ubangijin da ya fi shi ƙarfi, kuma wanda ya fi girma sama da dabararsa da izgilinsa da makircinsa. Shi ne wanda kamunsa ya kire kamun duk wani ɗan-adam da makircinsa da yaudararsa. Allah Shi ne mafi girma ga duk wani mai girma.

Ku ji tsoron Allah ya ku Musulmi, ku ambaci Allah da yawa, lallai za ku rabauta. Ka ji tsoron Allah ya kai musulmi gafallale, idan kai bayan jin wannan huɗuba, ka ji cewa kana daga cikin wanda ya rasa zuciyarsa, saboda gafalarsa, to kada ka yanke ƙaunar dawo da ita da ambaton Allah, domin Allah Yakan haɗa waɗanda suka rabu bayan sun yi dukkan zaton cewa ba za su sake haɗuwa ba.

Mai tambaya yana iya tambaya: Me ya sa ambaton Allah (S.W.T) tare da sauƙinsa a kan harshe da ƙarancin wahalarsa, ya zamo mafi amfani da falala, a cikin jimillar ibadu tare da wahalhalu masu maimaituwa a cikinsu.

Amsa: Allah ya sanyawa ragowar ibadu gwargwado, ya sanya musu lokuta iyakantatu, amma shi zikiri bai sanya masa gwargwado ko lokaci ba, kuma ya yi umarni da a yawaita shi dmin gijon zikiri shi ne albaƙiyatus salihat, saboda abin da ya tabbata daga Annabi (ﷺ) ya ce, "Ku riƙi garkuwarku". Muka ce, "Ya Manzon Allah, daga wani abokin gaba ne da ya zo? Ya ce, "A'a, garkuwarku daga wuta, ku ce, Hasbunallahu, walhamdulillahi, wala'ilaha illallah, wallahu akbar, domin su za su zo ranar alƙiyama suna masu kuɓutarwa, kuma ababen gabatarwa, kuma su ne wanzazzun ayyukan alheri (Albaƙiyat Assaliha)". Hakim ya rawaito shi, kuma ya inganta shi.

Sannan kowane musulmi na gari ya sani cewa, mai tasiri mai amfani shi ne, zikiri a kan harshe tare da halartowar zuciya, domin harshe shi ne mai bayanin abin da ke cikin zuciya, ita kuwa zuciya ita ce taskar da ake aje sirruka a cikinta. Sha'anin ƙirji kuwa shi ne ya yalwata da ambaton abin da ke cikinsa, kuma jefa shi a kan harshe yakan yi daɗi, kuma ba zai tsaya da ambatonsa a zuciya kwawai ba har sai harshensa ya amayar da shi, yana mai aiki da faɗar Allah ta'ala, inda yake cewa,

﴿ وَٱذۡكُر رَّبَّكَ فِي نَفۡسِكَ تَضَرُّعًا وَخِيفَةً وَدُونَ ٱلۡجَهۡرِ مِنَ ٱلۡقَوۡلِ بِٱلۡغُدُوِّ وَٱلۡأٓصَالِ وَلَا تَكُن مِّنَ ٱلۡغَٰفِلِينَ ﴿٢٠٥﴾ ﴾ [الأعراف: ٢٠٥].

(Kuma ka ambaci Ubangijinka a cikin zuciyarka kana mai ƙasƙantar da kai da tsoro, ba tare da ɗaga murya ba, safe da marece. Kuma kada ka zama daga cikin gafallalu).

Amma yin zikiri da harshe, alhali zuciya tana wasa, amfaninsa kaɗan ne, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Ku sani cewa, Allah ba ya amsa addu'a daga zuciya mai wasa." Hakim da Tirmizi ne suka rawaito shi, kuma Tirmizi ya kyautata shi.

Hakanan halartowar zuciya a wani lokacin yayin zikiri, tare da gafalarta a mafi yawan lokaci, shi ma amfaninsa kaɗan ne, domin zuciya za ta yi ta waiwaye ne zuwa da sha'awa-saha'awan duniya, kuma abu ne sananne cewa mai waiwaye ba ya isa da wuri ba. Don haka halartar zuciya a kowane lokaci ko mafi yawan lokaci shi ne abin gabatarwa a kan dukkan ibadu, kai! Da shi ne ma ragowar ibadu kan yi daraja. Kuma shi ne moriyar ibadu na aikace.

Saboda haka ne ma Annabi (ﷺ) ya yi gargaɗi a game da fashewar majalisai ba tare da an ambaci Allah a cikinsu ba. Ya ce; "Babu wasu mutane da za su tashi daga wani majalisin da ba su ambaci Allah a cikinsa ba, face sun tashi kamar daga kan mushen jaki ne, kuma wannan majalisin zai zame musu asara a gare su." Abu Dawud da Hakim ne suka rawaito shi.

To don haka ka ga Manzon Allah (ﷺ) yana nuna ƙinsa ga majalisin gafalallu, kuma yana yin hani a bisa duk wani taro da ya wofinta daga ambaton Allah, kuma duk wani majalisin da ake manta ambaton Allah a cikinsa. Sannan kuma majalisin ya tarwatse bayan hayaniya mai tsawo, a kan neman abinci da sha'awar rayuwa, cikin kacaniya da hayaniya, da zunɗe da yafice. Irin waɗannan majalisai masu wari ne. Don haka mai tsira da amincin Allah ya ce, "Duk wanda ya zauna a wani mazauni da hayaniya ta yawaita a cikinsa, sai ya ce kafin ya tashi! Tsarki ya tabbata a gare Ka ya Ubangijinmu, da yabonka, na shaida babu abin bautawa da gaskiya sai kai, ina neman gafararka, ina tuba zuwa gare ka. Sai Allah Ya kankare masa abin da ya kasance a wannan majalisin nasa." Tirmizi da Ibn Majah ne suka rawaito shi.

Ina neman tsarin Allah daga shaiɗan tsinanne:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تُلۡهِكُمۡ أَمۡوَٰلُكُمۡ وَلَآ أَوۡلَٰدُكُمۡ عَن ذِكۡرِ ٱللَّهِۚ وَمَن يَفۡعَلۡ ذَٰلِكَ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡخَٰسِرُونَ ٩ ﴾ [المنافقون: ٩].

"Ya ku waɗanda suka yi imani kada dukiyoyinku da 'ya'yanku su shagaltar da ku daga ambation Allah, duk wanda ya aikata haka to waɗannan su ne asararru).

Ku yi salati! Allah Ya yi muku rahama! A bisa mafificin halitta mafi alherin 'yan adam.

AMFANIN TSORON ALLAH A RAYUWAR MUSULMI

Manufofin huɗubar

- Amfanin tsoron Allah da muhimmancinsa.
- Haƙiƙanin ma'anar tsoron Allah.
- Ɗaukakar masu tsoron Allah da abin da Allah ya yi musu tanadi.
- Siffofin masu tsoron Allah.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammadu bawansa ne manzonsa ne. (Yaku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron Allah yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Yaku waɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammadu (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (a addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta".

Bayan haka, ina yi muku wasiyya da ni kaina, a kan jin tsoron Allah. Domin tsoron Allah shi ne matattarar dukkanin alkhairi bakiɗaya. Babu wani alkhairi na kusa, ko na nesa, face tsoron Allah yana zaburarwa a kansa. Haka nan, babu wani sharri na kusa ko na nesa, a fili ko a ɓoye, face tsoron Allah yana ba da katanga don kariya daga gare shi.

Kuma haƙiƙa tsoron Allah shi ne abu na farko da Allah ya yi wa mutanen farko da na ƙarshe wasiyya da shi. Allah Yana cewa:

﴿ وَلَقَدۡ وَصَّيۡنَا ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ مِن قَبۡلِكُمۡ وَإِيَّاكُمۡ أَنِ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَۚ ﴾ [النساء: ١٣١]

(Haƙiƙa Mun yi wasici ga waɗanda a ka ba wa littafi a gabaninku da kuma ku, a kan ku ji tsoron Allah).

Taƙawa dai, ita ce da'awar dukkanin annabawa da kuma salihan bayi. Ko wane

Annabi yakan cewa, mutanensa :

﴿ أَلَا تَتَّقُونَ ﴿١٠٦﴾ ﴾ [الشعراء: ١٠٦].

(Yanzu ba kwa ji tsoron Allah ba).

Kuma Waliyyan Allah su ne waɗanda suka yi imani, kuma suka kasance masu tsoron Allah.

Asalin ma'anar kalmar taƙawa, shi ne mutum ya sanya kariya da shamaki tsakaninsa da duk abin da yake tsoron sharrinsa. Allah Shi ne mafi cancantar a ji tsoronsa, tare da girmamawa.

Imam Ali (R.A), yana bayin ma'anar Tsoron Allah da cewa, (shi ne ka ji tsoron Mai girma (Allah), kuma ka yi aiki da Alƙur'ani, kuma ka wadatu da kaɗan, kuma ka yi tanadin ranar lahira».

Ya ku bayin Allah! Ya kamata mu san siffofin masu tsoron Allah, domin mu yi ƙoƙari mu yi koyi da su. Kaɗan daga cikin siffofin, sun haɗar da:

Imani da abin da gaibi, da tsayar da sallah, da ciyarwa domin Allah, yarda da abin da Allah ya saukar, da sakankancewa da ranar lahira. Allah Yana cewa:

﴿ ذَٰلِكَ ٱلۡكِتَٰبُ لَا رَيۡبَۛ فِيهِۛ هُدٗى لِّلۡمُتَّقِينَ ﴿٢﴾ ٱلَّذِينَ يُؤۡمِنُونَ بِٱلۡغَيۡبِ وَيُقِيمُونَ ٱلصَّلَوٰةَ وَمِمَّا رَزَقۡنَٰهُمۡ يُنفِقُونَ ﴿٣﴾ وَٱلَّذِينَ يُؤۡمِنُونَ بِمَآ أُنزِلَ إِلَيۡكَ وَمَآ أُنزِلَ مِن قَبۡلِكَ وَبِٱلۡأٓخِرَةِ هُمۡ يُوقِنُونَ ﴿٤﴾ أُوْلَٰٓئِكَ عَلَىٰ هُدٗى مِّن رَّبِّهِمۡۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُفۡلِحُونَ ﴿٥﴾ ﴾ [البقرة: ٢ – ٥].

(Wannan Alƙur'ani babu kokwanto a cikinsa, shiriya ne ga masu tsoron Allah. Waɗanda suke imani da abin da ya ɓoyu, kuma suke tsaida sallah, kuma suke ciyarwa daga abin da Allah ya azurta su da. Waɗanda suke imani da abin da muka saukar maka, da abin da muka saukar gabaninka, kuma suke sakankancewa da ranar lahira. To waɗannan suna bisa shiriya daga Ubangijinsu, kuma waɗannan su ne masu samun babban rabo).

Daga cikin siffarsu, akwai cika alƙawari, da kuma haƙuri a kan abin da ya same su na bala'i a rayuwa. Allah Ta'ala yana cewa:

﴿ لَّيۡسَ ٱلۡبِرَّ أَن تُوَلُّواْ وُجُوهَكُمۡ قِبَلَ ٱلۡمَشۡرِقِ وَٱلۡمَغۡرِبِ وَلَٰكِنَّ ٱلۡبِرَّ مَنۡ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةِ وَٱلۡكِتَٰبِ وَٱلنَّبِيِّـۧنَ وَءَاتَى ٱلۡمَالَ عَلَىٰ حُبِّهِۦ ذَوِي ٱلۡقُرۡبَىٰ وَٱلۡيَتَٰمَىٰ وَٱلۡمَسَٰكِينَ وَٱبۡنَ ٱلسَّبِيلِ وَٱلسَّآئِلِينَ وَفِي ٱلرِّقَابِ وَأَقَامَ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتَى ٱلزَّكَوٰةَ وَٱلۡمُوفُونَ بِعَهۡدِهِمۡ إِذَا عَٰهَدُواْۖ وَٱلصَّٰبِرِينَ فِي ٱلۡبَأۡسَآءِ وَٱلضَّرَّآءِ وَحِينَ ٱلۡبَأۡسِۗ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ صَدَقُواْۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُتَّقُونَ ﴿١٧٧﴾ ﴾ [البقرة: ١٧٧].

"Albirru shi ne wanda ya yi imani da Allah, da ranar lahira, da mala'iku, da littattafai da annabawa, kuma ya ba da dukiya ga makusanta, da marayu, da talakawa, da matafiyi, da masu roƙo, da wajen fansar bayi. Kuma ya tsayar da sallah ya ba da zakka. Da masu cika alkawari idan su ɗauka, kuma da masu haƙuri lokacin yunwa da cuta da lokacin yaƙi. Waɗannan su ne waɗanda suka yi gaskiya, kuma su ne masu tsoron Allah).

Yana daga siffarsu, yawaita istigfari game da zunubansu. Allah yana cewa:

﴿ وَسَارِعُوٓاْ إِلَىٰ مَغۡفِرَةٖ مِّن رَّبِّكُمۡ وَجَنَّةٍ عَرۡضُهَا ٱلسَّمَٰوَٰتُ وَٱلۡأَرۡضُ أُعِدَّتۡ لِلۡمُتَّقِينَ ﴿١٣٣﴾ ٱلَّذِينَ يُنفِقُونَ فِي ٱلسَّرَّآءِ وَٱلضَّرَّآءِ وَٱلۡكَٰظِمِينَ ٱلۡغَيۡظَ وَٱلۡعَافِينَ عَنِ ٱلنَّاسِۗ وَٱللَّهُ يُحِبُّ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ﴿١٣٤﴾ وَٱلَّذِينَ إِذَا فَعَلُواْ فَٰحِشَةً أَوۡ ظَلَمُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ ذَكَرُواْ ٱللَّهَ فَٱسۡتَغۡفَرُواْ لِذُنُوبِهِمۡ وَمَن يَغۡفِرُ ٱلذُّنُوبَ إِلَّا ٱللَّهُ وَلَمۡ يُصِرُّواْ عَلَىٰ مَا فَعَلُواْ وَهُمۡ يَعۡلَمُونَ ﴿١٣٥﴾ ﴾ [آل عمران: ١٣٣ – ١٣٥].

)Kuma ku yi gaggawa zuwa neman gafara daga Ubangijinku, da wata aljannah wacce fadinta kamar fadin sama da ƙasa ne, an tande ta ga masu tsoron Allah. Waɗanda suke ciyarwa a lokacin da dadi da lokacin wahala, kuma masu hadiye fushi, kuma masu afuwa ga mutane. Kuma Allah yana son masu kyautatawa. Su ne waɗanda idan suka aikata wata alfahasha, ko suka zalinci kawunansu sai su ambaci Allah, kuma su nemi gafarar zubbansu, kuma wanene yake gafarta zunubi ba Allah ba. Ba sa doge wa a kan abin da suka aikata na laifi alhalin suna sane).

Tsoron Allah yana cikie da alfano ga bawa duniya da lahira. Kaɗan daga cikin alfanonsa:

- Ubangiji zai sanya bawa mai tsoron Allah abin da zai banbance tsakanin ƙarya da gaskiya, Allah yana cewa,

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِن تَتَّقُواْ ٱللَّهَ يَجۡعَل لَّكُمۡ فُرۡقَانٗا وَيُكَفِّرۡ عَنكُمۡ سَيِّـَٔاتِكُمۡ وَيَغۡفِرۡ لَكُمۡۗ وَٱللَّهُ ذُو ٱلۡفَضۡلِ ٱلۡعَظِيمِ ٢٩ ﴾ [الأنفال: ٢٩].

(Ya ku waɗanda suka yi imani, in kun ji tsoron Allah, to zai sanya muku mafita ya kankare muku laifukanku, ya gafarta muku. Kuma lalle Allah ma'abocin falala ne mai girma).

- Yana da cikin alafanon tsoron Allah: Allah yana karɓar aikin mai taƙawa ne, kamar yadda ya ce,

﴿ إِنَّمَا يَتَقَبَّلُ ٱللَّهُ مِنَ ٱلۡمُتَّقِينَ ٢٧ ﴾ [المائدة: ٢٧].

(Kaɗai Allah Yana karɓa ne daga masu jin tsoronsa).

- Daga cikin alfanon akwai samon karramawa ta Allah ta'ala, Allah yana cewa,

(Haƙiƙa mafi girman daraja da matsayi a cikinku shi ne mafi tsoron Allah daga cikinku).

- Yana daga cikin amafanin tsoron Allah, Ubangiji zai ba wa mai shi kaso biyu na rahamarsa, kuma ya sanya masa haske da zai riƙa tafiya a cikinsa, kuma ya gafarta masa zunubbansa, kamar yadda Allah ya ce,

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَءَامِنُواْ بِرَسُولِهِۦ يُؤۡتِكُمۡ كِفۡلَيۡنِ مِن رَّحۡمَتِهِۦ وَيَجۡعَل لَّكُمۡ نُورٗا تَمۡشُونَ بِهِۦ وَيَغۡفِرۡ لَكُمۡۚ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٢٨ ﴾ [الحديد: ٢٨].

(Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron Allah, ku yi imani da manzansa, zai ba ku kaso biyu daga cikin rahamarsa, ya sanya muku haske a cikin rayuwarku, ya gafarta muku, haƙiƙa Allah mai yawan gafara ne mai jinƙai).

- Yana daga cikin amfanin taƙawa ga bawa, shi ne za ta zama dalilin kuɓutarsa yayin da bayi za su ƙetare wuta, Allah yana cewa,

﴿ وَإِن مِّنكُمۡ إِلَّا وَارِدُهَاۚ كَانَ عَلَىٰ رَبِّكَ حَتۡمٗا مَّقۡضِيّٗا ٧١ ثُمَّ نُنَجِّي ٱلَّذِينَ ٱتَّقَواْ وَّنَذَرُ ٱلظَّٰلِمِينَ فِيهَا جِثِيّٗا ٧٢ ﴾ [مريم: ٧١ – ٧٢].

"Babu wani daga cikinku, face sai ya shige ta kanta. Wannan wani abu ne na dole da Ubangijinka ya hukunta shi. Sannan sai mu tseratar da masu tsoron Allah, kuma mu bar azzalimai a gurfane a cikinta"

Sannan Allah ya sake faɗa:

﴿ وَيُنَجِّي ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ٱتَّقَواْ بِمَفَازَتِهِمۡ لَا يَمَسُّهُمُ ٱلسُّوٓءُ وَلَا هُمۡ يَحۡزَنُونَ ٦١ ﴾ [الزمر: ٦١].

(Kuma Allah zai tseratar da waɗanda suka ji tsoron Allah ta hanyar ba su

babban rabonsu, babu wani mummunan abu da zai same su, kuma ba za su yi baƙin ciki ba).

- Kuma yana daga cikin amfanin tsoron Allah, Ubangiji zai gadar musu da gidan Aljanna ranar ƙiyama, Allah ya ce,

﴿ تِلۡكَ ٱلۡجَنَّةُ ٱلَّتِي نُورِثُ مِنۡ عِبَادِنَا مَن كَانَ تَقِيّٗا ٦٣ ﴾ [مريم: ٦٣].

(Wannan ita ce Aljannar da za mu gadawa wanda yake mai tsoron Allah daga bayinmu).

Daga cikin irin wannan amfanin, Allah yana tare da masu tsoron Allah da goyon bayansu, da ba su nasara, Allah yana cewa,

﴿ إِنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلَّذِينَ ٱتَّقَواْ وَّٱلَّذِينَ هُم مُّحۡسِنُونَ ١٢٨ ﴾ [النحل: ١٢٨].

(Allah yana tare da masu jin tsoronsa, kuma mau kyautatawa a cikin ayyukansu).

- Hakanan Allah yana buɗewa masu tsoron Allah albarkatunsa daga sama da ƙasa, kamar yadda ya ce,

﴿ وَلَوۡ أَنَّ أَهۡلَ ٱلۡقُرَىٰٓ ءَامَنُواْ وَٱتَّقَواْ لَفَتَحۡنَا عَلَيۡهِم بَرَكَٰتٖ مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلۡأَرۡضِ ﴾ [الأعراف: ٩٦].

(Da a ce ma'abota alƙaryu za su yi imani, da mun buɗe musu taskokin albarkatunmu daga sama da ƙasa."

- Sannan Allah yana sanya wa mai tsoron Allah mafita daga duk wani ƙunci da damuwa, kamar yadda ya ce,

﴿ وَمَن يَتَّقِ ٱللَّهَ يَجۡعَل لَّهُۥ مَخۡرَجٗا ٢ ﴾ [الطلاق: ٢].

(Duk wani wanda ya ji tsoron Allah zai sanya masa mafita).

Ya ku bayin Allah, ku yi guziri da tsoron Allah da ku rabauta a rayuwarku ta duniya da lahira, domin tsoron Allah shi ne mafi alfanon abin da bawa ya yi guziri da shi. Allah yana cewa,

﴿ وَتَزَوَّدُواْ فَإِنَّ خَيۡرَ ٱلزَّادِ ٱلتَّقۡوَىٰۚ وَٱتَّقُونِ يَٰٓأُوْلِي ٱلۡأَلۡبَٰبِ ١٩٧ ﴾ [البقرة: ١٩٧].

(Ku yi guzuri, haƙiƙa mafi amfanin guzuri shi ne tsoron Allah. Kuma ku ji tsorona yaku masu hankula).

Allah Ya ƙara da cewa:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَلۡتَنظُرۡ نَفۡسٞ مَّا قَدَّمَتۡ لِغَدٖۖ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَۚ إِنَّ ٱللَّهَ خَبِيرُۢ بِمَا تَعۡمَلُونَ ١٨ وَلَا تَكُونُواْ كَٱلَّذِينَ نَسُواْ ٱللَّهَ فَأَنسَىٰهُمۡ أَنفُسَهُمۡۚ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡفَٰسِقُونَ ١٩ ﴾ [الحشر: ١٨ – ١٩].

(Ya ku waɗanda suka yi imani, ku ji tsoron Allah, kuma kowace rai ta yi duba ga abin da ta gabatar domin gobe (Kiyama). Ku ji tsoron Allah, haƙiƙa Allah Masani ne game da duk abin da kuke aikatawa. Kada ku zama kamar waɗanda suka manta da Allah, sai ya mantar da su kawunansu. Waɗannan su ne fasiƙai).

Allah ya albarkace ni tare da ku da abin da muka ji na Alƙur'ani ya gafarta mana zunubbanmu, lalle shi mai yawan gafara ne mai jin ƙai.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin halittu. Tsira da amincin Allah ya tabbata ga Annabin rahama, Muhammadu bn Abdullahi da alayensa da sahabbansa, da waɗanda suka bi tafarkinsa har zuwa ƙiyama.

Bayan haka,

Ku sani – Allah ya muku rahama – Wanda Allah ya azurta ta shi da taƙawa, har ta mamye zuciyarsa, to babu shakka ya ɗanɗani ni'ima ta sa'adar duniya kafin ta lahira. Kuma ya kasance mafi karamci a gurin Allah. An karɓo daga Abu Hurairata, ya ce, na ce, Ya ma'aikin Allah(ﷺ), wanene ya fi karamci cikin mutane? Sai ya ce, "Wanda ya fi su tsoron Allah". Sai suka ce, Ba a kan haka muke maka tambaya ba. Sai ya ce, "Annabin Allah Yusuf, ɗan Annabin Allah, ɗan badaɗayin Allah". Sai suka ce, Ba a kan haka muke maka tambaya ba. Sai ya ce, "Kuna tambaya ta ne game da labawan asali, to masu kirkinsu a jahiliyya, su ne masu kirkinsu a musulunci idan sun yi ilimi".

Ya bayin Allah! Ku sani tsoron Allah yana hana hannu taɓa riƙe haram, yana hana ƙafa ta tafi gurin abin da zai fusata Allah. Yana hana harshe faɗar duk wata magana da Allah zai yiwa mutum hisabi a kansa. Yana hana ido kallon haram. Tsoron Allah yana sanya mutum ya riƙa tafiya a gwadaben rayuwa yana mai taka-tsantsan cikin duk abin da zai yi ko ya bari. Sayyidina Umar Alfaruƙ yana cewa Ubayyi bn Ka'ab: Menene taƙawa? Sai ya ce, "Shin ka taɓa bin hanya mai ƙaya? Sai Umar ya ce, "Na'am". Sai Ubayyu ya ce, "To ya riƙa yi?" Sai ya ce, "Na yi dage na kula? Sai Ubayyu ya ce, "To wannan shi ne tsoron Allah, ya dage, ya kuma yi taka-tsantsan kada ya jawo kansa hushin Allah ta'ala".

Tsoron Allah shi ne zai sanya mutane a kan tafarkin gaskiya koda yaushe, Allah Ta'ala yana cewa,

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِن تَتَّقُواْ ٱللَّهَ يَجۡعَل لَّكُمۡ فُرۡقَانٗا وَيُكَفِّرۡ عَنكُمۡ سَيِّـَٔاتِكُمۡ وَيَغۡفِرۡ لَكُمۡۗ وَٱللَّهُ ذُو ٱلۡفَضۡلِ ٱلۡعَظِيمِ ٢٩ ﴾ [الأنفال: ٢٩].

(Ya ku waɗanda suka yi imani, idan kuka ji tsoron Allah, zai sanya muku mafita, kuma ya kankare muku laifuffukanku, kuma ya gafarta muku. Allah ma'abocin falala ne mai girma).

Babu abin da yake riƙe tsoron Allah, ya kafe shika-shikansa a zuciyar muminin sai yawan ambaton Allah a kowane lokaci, a kowane hali. Idan mumini ya gafala daga ambaton Allah wanda shi ne yake shayar da jijiyoyin taƙawa to sai ta bushe, ganyayyakinta su zube, ta zama kamar bushasshen karmami rididdigagge, iskar waswasi tana sheƙe shi, wadda shaiɗan ke tayar wa da ɗan-adam, hakanan zuciyarsa mai masa umarni da mummunan umarni. Don haka babu makawa a dawwama a kan zikirin Allah, da tasbihi tare da godiya ga Allah, don mutum ya samu ya murƙushe waɗannan abokan gabar tasa guda biyu (Sheɗan da son zuciya).

Muslim ya ruwaito hadisi daga Sauban, ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Na umarce ka da yawan sujjada ga Allah, domin babu sujjada ɗaya da za ka yi don Allah, face Allah ya ɗaukaka darajarka da ita, ya kuma share maka laifi da ita".

Allah yana cewa,

﴿ لَّقَدۡ كَانَ لَكُمۡ فِي رَسُولِ ٱللَّهِ أُسۡوَةٌ حَسَنَةٞ لِّمَن كَانَ يَرۡجُواْ ٱللَّهَ وَٱلۡيَوۡمَ ٱلۡأٓخِرَ وَذَكَرَ ٱللَّهَ كَثِيرٗا ٢١ ﴾ [الأحزاب: ٢١].

(Haƙiƙa kuna da abin koyi mai kyau game da Manzon Allah, ga wanda yake fatan haɗuwa da Allah, da kuma ranar lahira, kuma ya ambci Allah dayawa).

Mumini shi ne wanda yake yin koyi da Manzon Allah, domin shi ne yake kyakkyawan fatan haɗuwa da Allah, sannan ya yi imani da sakamakon lahira. Wannan kuwa ba zai samu ba sai da yawan tuna Allah, yawan tuna Allah shi ne zai yiwa bawa jagora zuwa ga samun mafi ɗaukakar masauki a gurin Allah. Sannan shi ma zikirin ba zai zama ya samu ba sai da koyi da Manzon Allah. To wannan koyin idan mumini ya lazimce shi, to shi ne zai zama daga cikin masu tsoron Allah.

Muna roƙon Allah Ta'ala ya sanya mu cikin masu tsoronsa. Muna roƙonsa ya azurta mu da taƙawarsa, kuma ya sanya mu cikin bayinsa masu tsoronsa, kuma ya saukar da mu a masaukansu wanda ya yi musu alkawari da faɗarsa:

﴿ إِنَّ ٱلۡمُتَّقِينَ فِي جَنَّٰتٖ وَنَهَرٖ ٥٤ فِي مَقۡعَدِ صِدۡقٍ عِندَ مَلِيكٖ مُّقۡتَدِرِۢ ٥٥ ﴾ [القمر: ٥٤ – ٥٥].

(Lalle masu tsoron Allah suna cikin aljannatai da ƙoramu, cikin mazauni na gaskiya, a gurin sarki mai cikakken iko).

GOMAN ƘARSHE NA RAMADAN

Manufofin huɗubar

- Tunatar da mutane falalar wannana goman ƙarshen.
- Bayanin ayyukan sunnah da ake so a aikata a wannan goman.
- Ƙarfafa alaƙar bawa da Ubangijinsa da ƙoƙari wajen neman kusanci gare shi

Huɗuba Ta Farko

Yabo da godiya da kirari sun tabbatar da Allah, taimakonsa da gafararasa muke nema, muna neman tsarinsa daga sharrin kawunanamu da munannan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar to babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatara to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai ne ba Shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa Annabi Muhammadu bawaƙn sa ne manzon sa ne (ya ku waɗabda suka yi imani kuji tsoron Allah yadda ya cancanci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmai) (ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanad ya halicce ku daga rai guda ɗaya, kuma ya halicci matarsa daga gare su (Su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junaku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci, lalle allah mai akula ne da ku). (ya ku waɗanda suka yi imani ku tsi tsoron Allah kuma ku faɗi Magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafatar muku zunubanku. Wanda yabi da manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawun shiriya shiriyar Annami Muhammad (ﷺ) kumamafi sharin al'amura (a addini) ƙagaggunsu. Kuma duk wani ƙagaggen abu (a addini) bidi'a ce, kuma duk warta bidi'a ɓata ce, kuma duk wani bata yana wuta.

Bayan haka, ya ku mutane ina muku wasiyya da ni kaina da tsoron Allah mai buwaya da ɗaukaka, domin tsoron Allah, shi ne mafi girman abin da kuka ɓoye, kuma mafi kyawun abin da kuka baiyana, kuma mafificin abin da kuka taskance. Allah ya taimake mu a bisa lazimtartasa, kuma ya wajabta mana ladanta.

Ya ku musulmi, waɗannan su ne kwanankin watanku na Ramadan ga su suna raguwa, ga dararensa masu daraja suna ƙarewa, suna raguwa suna ƙarewa, alhalin yi musu shaida a bisa ayyukanku, masu kiyayewa ga abin da kuka ba su ajiya, kuma sito-sito ne ababen kiyayewa, za a kirawo ku ranar alƙiyama (Ranar da kowace rai za ta sami abin da ta aikata). Ubangijiku zai yi kira, (Ya ku bayina kaɗai waɗannan ayyukanku ne nake ƙididdige su a gare ku, sannan na biya ku a kansu. Duk wanda ya sami alheri to ya gode wa Allah, wanda kuwa ya sami saɓanin haka to kada ya zargi kowa sai kansa).

Wannan shi ne watanku, kuma ga ƙarshensu ya zo, Mutane diyawa sun fara zumi, amma sun rasu kafin gama shi. Wasu kuma sun fatan ganin na gaba. Amma

Allah bai nuna musu ba. Shin kuna lura kuwa da ajali da wucewarsa?! Kuma shin kuna kula da yadda guri yake yaudara masu shi?!

Ya ku ‘yan uwa! In dai akwai mai tsawatarwa cikin rayuka, kuma da mai wa’azi cikin zukata, to ‘yan kwanaki sun rage daga kwanankinsa, kuma ragowa masu tarin girma, su ne kwanakin goma raguwar da Annabinku Muhammadu (ﷺ) yake kulawa da su dukkanin kulawa, a cikin ashirin da suke sallah da barci amma yayin da goman (ƙarshe) suka shiga sai ya himmatu, ya ƙoƙarta ya ɗaura ɗamara, ya ƙauracewa shimfiɗarsa, ya tashi iyalinsa yana ƙwanƙwasa ƙofar Fadῑma da Ali Allah ya ƙara yarda a gare su yana mai cewa “Yanzu ba kwa tashi ku yi sallah ba?” Yana kwankwansa ƙofar yana mai karanta faɗar Allah:

﴿ وَأۡمُرۡ أَهۡلَكَ بِٱلصَّلَوٰةِ وَٱصۡطَبِرۡ عَلَيۡهَاۖ لَا نَسۡـَٔلُكَ رِزۡقٗاۖ نَّحۡنُ نَرۡزُقُكَۗ وَٱلۡعَٰقِبَةُ لِلتَّقۡوَىٰ ١٣٢ ﴾ [طه: ١٣٢].

(Kuma ka umarci iyalinka da sallah, kuma ka yi haƙuri a kanta, ba ma tambaye ka arziƙi ba, mu ne masu azurtaku. Kuma kyakkyawan ƙarshe ya tabbata ga masu tsoron Allah).

Kuma yana zuwa ɗaukuna na matanyensa yana umarni da cewa, “Ku tashi ma’abota ɗakuna, da yawa rai mai sutura a duniya amma matsaraiciya ranar alƙiyawa”. Bukhari ya ruwaito shi.

Annabi kasance idan kwanan goma ya rage daga Ramadan, ba ya barin wani da yake da ikon tashi daga iyalinsa face ya tashe shi.

Yana daga sunnonin waɗanda kwanaki, ƙoƙari wajen tashi da daddare da abin da ke cikin haka na cikasa abin da ya kuɓucewa mutum na cikon farilla.

Game da ƙiyamullalli wani na iya cewa “Wannan tsayuwar daren nafilace. Ni in na kiyaye farillai ya ishe ni. Amsar da za a ba shi ita ce, haƙiƙa a cikin kiyaye farillai akwai alheri mai yawa, kuma shi kaɗai za a tambayi musulmi, amma wa ya sanar da kai cewa ka ba da farillan yadda ya kamata?!. Haƙiƙa kai kana buƙatar nafilfili don cike tawayar da ke cikin farillan. Kuma game da ranar alƙiyama. Adu Dawud da waninsa sun rawaito cewa, “Allah Ta’ala zai ce “Duba sallar bawana, shin ya cikata ko ya tauyeta? To idan ta kasance cikakkiya ce sai a rubuta ma sa ita cikakkiya, idan kuma wani abu ya tawaya daga cikinta sai ya ce: “Ku duba bawana shin yana da nafilla?” Idan ya kasance yana da ita, sai ya ce: “Ku cikawa bawana farillarsa”. Sannan a a ƙarɓi ayyuka a wannan yanayi.

Allah (S.W.T) ya wajabta farilla, kuma ya san cewa daga cikin bayins akwai waɗanda za su taƙaita wajen cikata, sai ya shar’anta musu nafiloli don ya ɗora wannan karaya, don jinƙan da ya ke musu. Mu ɗauka ma ka cika farillai, ka ba su haƙƙinsu, to ai an umarce ka da koyi da Annabinka (ﷺ). Allah Ta’ala Ya ce,

﴿ لَّقَدۡ كَانَ لَكُمۡ فِي رَسُولِ ٱللَّهِ أُسۡوَةٌ حَسَنَةٞ لِّمَن كَانَ يَرۡجُواْ ٱللَّهَ وَٱلۡيَوۡمَ ٱلۡأٓخِرَ وَذَكَرَ ٱللَّهَ كَثِيرٗا ٢١ ﴾ [الأحزاب: ٢١].

(Lallai abin koyi kyakkyawa ya tabbata gare ku, game da Manzon Allah, ga wanda ya kasance yana ƙaunar (samun yardar) Allah, da ranar lahira).

Ya ku bayin Allah! Kuma yana daga falalolin wannan goman cewa, ana fatan dacewa da daren lailatul kadari a cikinta, daren da Allah Ta’ala Ya ce game da shi:

﴿ لَيۡلَةُ ٱلۡقَدۡرِ خَيۡرٞ مِّنۡ أَلۡفِ شَهۡرٖ ٣ ﴾ [القدر: ٣].

(Daren lailatul ƙadari ya fi wata dubu alheri).

Malam Annakha'i yana cewa, "Aiki a cikinsa ya fi wata dubu alheri, banda shi daern" Wata dubu kuwa - ya ku bayin Allah - shekara tamanin da uku da wata huɗu ne. Don haka aiki a wannan dare ga wanda Allah ya datar da shi ya fi aikin cikin shekara Tamanin da uku da wata huɗu. Hadisi ya zo a cikin Bukhari da Muslim, daga Abu Huraira (R.A) Annabi (ﷺ) ya ce, "Duk wanda ya sallaci daren lailatul ƙadari yana mai ba da gaskiya da neman lada, to za a gafartamasa abin da ya gabata na zunubansa". Fadinsa "yana mai ba da gaskiya" yana nufin "yana mai ba da gaskiya da abin da Allah ya yi alƙawari game da shin a ladan masu ƙiyamullaili a cikinsa, da neman lada, da biɗar sakamako". Wannan dare ɗaya ne daga dararen goman ƙarshe na Ramadan a bisa zance mafi rinjaye. Haƙiƙa Allah (S.W.T) ya ɓoye wa bayi saninsa don jin ƙai a gare su; domin su yi ƙwazo wajen nemansa, a cikin waɗannan darare masu girma, ta hanyar sallah da zikiri da addu'a, sai su ƙara kusanci ga Allah. Kuma ya ɓoye wannan dare ga bayi, don gane wanda yake mai ƙoƙari wajen nemanta, mai ƙwaɗayi a kanta, da wanda yake mai kasala ko mai sakaci. Duk kuwa wanda ya yi ƙoƙari a bisa wani abu to zai same shi.

Ya ku bayin Allah! Lailatul ƙadari tana da alamomi da ake gane ta da su, sai dai mafi ingancin abin da ya zo dangane da alamointa su ne, rana za ta fito a safiyar wannan rana mai haske sosai, babu dallarin haske a gare ta, domin ya zo cikin sahihu Muslim daga Ubayyi bin Ka'ab (R.A) ya ce "Manzon Allah (ﷺ) ya ce "Kuma alamarta rana za ta fito a safiyar yininta fara babu dallarin haske gare ta."

Wannan alama tana kasancewa bayan wucewar daren. Hikimar hakan, don mutane su yi ƙoƙari wajen nemanta, kuma masu ƙoƙari su yi farin ciki da ƙwazonsu da aikinsu. Kuma haƙiƙa sunna ta nuna cewa daren Lailatul Kadari a kan iya sanin sa ta hanyar mafarki na gari. Domin ya zo a cikin Bukhari da Muslim daga Ibn Umar cewa wasu mazaje daga Sahabban Annabi (ﷺ) an nuna musu daren Lailatul Kadari cewa, shi a cikin bakwan ƙarshe yake, sai mai tsira da amincin Allah ya ce "Ai ga mafarkinku ya haɗu a cikin bakwai ta ƙarshe, to duk wanda zai lalube ta, to ya lalube ta a cikin bakwai na ƙarshe".

Kai kacokan ma an nunawa Annabi (ﷺ) yaushe ne daren Lailatul Kadari, domin ya zo a cikin Bukhari daga Abi Sa'id Alkhudri, ya ce "Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Haƙiƙa ni, an nuna min daren Lailatul Kadari, sannan aka mantar da ni shi, don haka, ku neme shi a goman ƙarshe, kuma ni na gan ni ina sujjada cikin ruwa da taɓo" Abu Sa'id ya ce" Sai na ga Annabi (ﷺ) yana sujjada a cikin ruwa da taɓo, har sai da na ga a alamun taɓo a goshinsa".

Ya ku 'yan'uwa masu girma! Haƙiƙa yana daga sunnonin waɗannan kwanaki goma: Shiga I'itikafi, wanda shi ne zama cikin masallaci na tsawon wani lokaci na waɗannan kwanaki masu albarka, don keɓanta, domin bauta ga Allah mai buwaya da ɗaukaka, Allah Ta'ala Ya ce:

﴿ وَأَنتُمۡ عَٰكِفُونَ فِي ٱلۡمَسَٰجِدِ ﴾[البقرة: ١٨٧].

(Kuma alhali ku kuna masu I'itikafi a cikin masallatai).

Kuma Bukhari ya ruwaito daga Abu Sa'id Alkhudri cewa, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Duk wanda zai yi I'itikafi tare da ni, to ya yi I'itikafi a goma na ƙarshe, domin ni. an nuna min wannan daren sannan aka mantar da ni shi". Don haka ya kamata ga wanda ya sami ikon haka, sai ya yi saboda lada mai girma da horar da kai a kan bin Allah da ke cikin yin hakan.

Shi mai itikafi ya tsare kansa ne don biyyaya ga Allah da ambatonsa, ya yanke kansa daga duk wani abu mai shagalarwa da zai shagaltar da shi game da Allah. Ya duƙufa da zuciyarsa da jikinsa da aikata abin da zai kusanta ga Allah. Babu abin da ya rage masa face Allah da abin da zai janyo masa yardarsa.

Ma'anar I'itikafi da haƙiƙaninsa, shi ne, yanke alaƙoƙi da halittu, don saduwa da hidimar mahalicci, kuma duik lokacin da sanin Allah ya ƙarfafa da sonsa, da matsawa gare shi sai su gadarwa da mai su yankewa zuwa ga Allah, a kowane lokaci.

Kuma yana da sunnonin goman ƙarshe na Ramadan: Koƙari wajen sauke Alƙur'ani mai girma don koyi da Annabi (ﷺ), da yawaita sadaka, wadda ita ce sunnar mala'ika Jibrilu tare da Annabi (ﷺ) domin Jibrilu ya kasance yana bitar alƙur'ani a kowace shekara a watan Ramadan tare da Manzon Allah (ﷺ), har yayin da shekrar ƙarshe ta raytuwarsa (ﷺ) ta zo sai Mala'ika Jibrilu ya yi bitar Alƙur'ani tare da shi a cikinta sau biyu. Bukhari da Muslim ne suka rawaito daga Ibn Abbas (R.A).

Kuma Bukhari ya ruwaito hadisi daga Ibn Abbas (R.A) ya ce "Annabi (ﷺ) ya kasance mafi kyautar mutan. Kuma lokacin da ya fi kyauta shi ne a Ramadan lokacin da Mala'ika JIbrilu yake haɗuwa da shi, yana bitar alƙur'ani tare da shi. Lallai Manzon Allah ya fi sakakkiyar iska kyauta yayin da Jibrilu ya gamu da shi".

Da dai waɗanda suka imani da girman ladan sadakar da Annabi ya faɗa, suna kwaɗayin ba da sadakar su, da zakkar fidda kansu ga mabuƙata da faƙirai da sun kasance sun gabatar da alheri ga kawukansu, kuma sun nuna mihammancin koyarwar Manzo (ﷺ) Sun zama rayayyar al'umma, wacce take yin ilimi. Kuma tana aiki da iliminta, tana samun ribar ta fuskar gyaruwar halayenta da ɗabi'unta.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah, Ubanjigin talikai. Tsira da amincin su tabbata a bisa mafi darajar manzanni, Annabinmu Muhammadu da alayensa da sahabbansa gaba ɗaya, bayan haka:

Ya ku bayin Allah! Haƙiƙa I'itikafi yana da falala mai girma, daga cikinta:

Akwai cewa a cikin waɗannana dararen goma waɗanda suka fi watanni dubu alheri. Annabi (ﷺ) ya kasance yana I'itikafi a goman farko, sannan ta tsakiya. Sannan wata rana ya leƙo da kansa ya yi wa mutane magana, mutane suka matso, ya ce "Haƙiƙa ni na yi I'itikafin goman farko, ina neman wannan dare, sannan na yi I'itikafin goman tsakiya, sannan aka ce min, daren yana cikin goman ƙarshe, don haka wanda a cikinku yake so ya yi I'itikafi to ya yi". Muslim ne ya rawaito

shi.

Daga ciki falalar i'itikkafi, akwai cewa, Annabi (ﷺ) bai taɓa barin I'itikafi ba. Ya kasance yana I'itikafi a kwana goma kowace shekara. Yayin da shekarar da ya rasu ta zo, sai ya yi I'itikafin kwana ashirin. Yayin da matansa suka yi gasa a kan I'itikafi, sai ya bar shi, ya rama shi a goman farko na shawwal. Bukhari ne ya rawaito shi.

Daga ciki falalar, akwai cewa Annabi (ﷺ) ya kasance yana barin abin da yake halaliyarsa ne, wato bacci da mata. Da wannan ne aka fassara faɗin A'isha (R.A) "Sai ya ƙara ɗaura ɗamara". Ma'ana yana barin bacci shi da kusantar matarsa.

Daga ciki falalar, akwai cewa, Annabi (ﷺ) yana aikata abin da ya yi hani a kansa. Domin ya yi hani a bisa saɓi-zarcen azumi. Wato jinkirta sahur har zuwa lokacin sahur (ma'ana mutum ya ƙi cin komai bayan azumi har lokaci ɗaukar wani azumin). Amma ya kasance yana aikata haka musamman ma a cikin goman ƙarshe.

Kuma yana daga cikin falalar: cewa, matayen Annabi (ﷺ) sun yi I'itikafi bayansa, har Nana A'isha (R.A) tana cewa "Wata mata mai jinin Istihadha daga matayen Annabi (ﷺ) ta yi I'itikafi tare da shi, sai ta kasance tana ganin jaja-jaja da fatsi-fatsi, har wani sa'in muka kasance muna sanya tasa a ƙarƙashinta yayin da take Sallah. Bukhari ne ya rawaito shi.

Ya ku Musulmi! Haƙiƙa Allah ya sanyawa I'itikafi wasu dokoki da hukunce-hukunce daga cikinsu;

1. Ya wajaba mai I'itikafi ya tabbatar da manufar yin I'itikafi ya ta hanyar bin shiriyarsa.
2. Idan mai I'itikafi ya yi niyyar I'itikafi, wajabi ne sai ya kai karshe, ya hallata ya katse shi, musamman idan ya ji tsoron yin riya da aikinsa.
3. Babu wani hadisi da ya zo cikin iyakance mafi ƙaranci lokacin yin I'itikafi.

Shuwagannin huɗu, da jamhurum malamai na da, da na yanzu sun tafi a kan cewa, mai I'itikafi zai shiga I'itikafi ne kafin faɗuwar rana a daren da yake son ya shiga I'itikafi a cikinsa.

1. An so ga mai I'itikafi ya riƙi waje na musamman ga kansa, domin ya keɓance da Ubangijinsa, kuwa ya huta a gurin, kuma don kada wani ya faɗo masa, yayin da yake canja tufafi, ko tarbar wanda yake son ya ziyarce shi daga iyalinsa.
2. Ya halarta mai I'itikafi ya yi kai-kawo a masallaci. sai dai an fi so kada ya yawaita kai-kawon saboda dalilai guda biyu.
   - Cewa, Annabi (ﷺ) ya an yi masa wata lema a cikin masallaci, baya fitowa daga cikinta sai don sallah, kuma mafificiyar shiriya ita ce shiriyarsa.
   - Cewa, Annabi (ﷺ) ya ce "Mala'iku suna yi wa ɗayanku addu'a matuƙar yana zaune a gurin da ya yi sallarsa. Bukhari ne ya rawaito shi.
3. Amma matsalar fita daga masallaci, ta ya kasu kashi uku:
   - Na farko: Wanda ya halatta, shi ne fita saboda lamari da ya zama babu makawa a shari'a ko a ɗabi'a, kamar fita don sallar juma'a, ko ci da sha,

idan bai sami wanda zai zo masa da shi ba.

- Na biyu: Fita domin aikin biyaiya wanda bai wajaba a gare shi ba, kamar duba mara lafiya, da halarta jana'iza, idan ya sharɗanta shi tun farko to ya halarta. In ba haka ba bai halarta ba.
- Na uku: Fita domin abin da ya saɓawa I'itikafi; wato kamar fita domin saye da sayarwa, da tarawa da iyalinsa, da makamancinsa, wannan bai halatarba.

Bayin Allah! Ya wanda ya yi nishaɗi tun farkon wata har yayin da lamari ya girmama kaka ta yi sai ya bar tsaiwar dare, ya kasha dararensa cikin wasa da wargi da saɓon Allah, ya kaucewa taren kyaututtukan Ubangijinsa mai yawan kyauta. Ina gargaɗinka ka bar kasala a kan abin da ka fara watanka da shi na tsaiwar dare da azumi.

Ya ma'abotan gafala, ku faɗaka, ya ahlussunna ku farka, wallahi asara ce da rashin dace a ce an ba ka labarin wani dare da bauta a cikinsa ta fi bautar shekara tamanin da uku, sannan ba za ka tashi kana mai bauta ga Ubangijinka ba, kana mai sujjada.

Kashedinka daga ruɗuwa da abin da ka aikata. Ka kasance kamar waɗanda Allah ya bayyana halayensa da cewa,

﴿ كَانُواْ قَلِيلٗا مِّنَ ٱلَّيۡلِ مَا يَهۡجَعُونَ ١٧ وَبِٱلۡأَسۡحَارِ هُمۡ يَسۡتَغۡفِرُونَ ١٨ ﴾ [الذاريات: ١٧ – ١٨].

(Sun kasance ɗan barci kaɗan suke yi da daddare. Kuma suna neman gafara a lokacin sahur).

Ba su nemi gafara ba sai domin suna ji a jikinsu cewa, sun tauye wani abu na haƙƙin Allah, duk da tsayawarsu a mafi yawan dare. Ka zamo kamar wanda Allah mai buwaya da ɗaukaka, Ya ce a game da su,

﴿ وَٱلَّذِينَ يُؤۡتُونَ مَآ ءَاتَواْ وَّقُلُوبُهُمۡ وَجِلَةٌ أَنَّهُمۡ إِلَىٰ رَبِّهِمۡ رَٰجِعُونَ ٦٠ ﴾ [المؤمنون: ٦٠].

(Da kuma waɗanda suke aikata abin da suke aikatawa (na ɗa'a ga Allah) alhali zukatansu suna masu jin tsoron cewa su masu komawa ne zuwa Ubangijin su).

Ka tuna cewa abin da kake cikinsa da falalar Allah da datarwarsa. Wanda ya ba ka, kuma ya datar da kai, shi ne ya haramtawa waninka, kuma ya hana shi. Don haka, ka faɗi kamar yadda salihai suka ce,

﴿ وَقَالُواْ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ ٱلَّذِي هَدَىٰنَا لِهَٰذَا وَمَا كُنَّا لِنَهۡتَدِيَ لَوۡلَآ أَنۡ هَدَىٰنَا ٱللَّهُۖ ﴾ [الأعراف: ٤٣].

"Godiya ta tabbata ga Allah wanda ya shiryar da mu ga wannan, kuma ba mu kasance za mu shiriya ba ba don Allah ya shiryar da mu ba".

Ka lura da abin da Allah ya faɗa ga bawansa kuma Annabinmu (ﷺ):

﴿ وَلَئِن شِئۡنَا لَنَذۡهَبَنَّ بِٱلَّذِيٓ أَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡكَ ثُمَّ لَا تَجِدُ لَكَ بِهِۦ عَلَيۡنَا وَكِيلًا ٨٦ إِلَّا رَحۡمَةٗ مِّن رَّبِّكَۚ إِنَّ فَضۡلَهُۥ كَانَ عَلَيۡكَ كَبِيرٗا ٨٧ ﴾ [الإسراء: ٨٦ - ٨٧].

(Da dai mun so da mun tafi da abin da muka yi wahayi gare ka, sannan ba za ka sami wani mai yi maka wakilci a kanmu ba. Sai domin rahama daga Ubangijinka lallai falalarsa ta kasance mai girma a gare ka).

Har wasu daga magabata suka ɗauki wannan ayar a matsayin gargaɗi mafi girma a littafin Allah. Kasance mai ƙasƙan da kai, mai ƙokari a cikin biyayya, mai tsoron kada a ƙi karɓar aikinsa, domin babu mai amincewa makircin Allah sai

mutane asararru. Kaɗai Allah yana karɓa ne daga masu taƙawa. Kuma kai ba ka sani ba ko kana cikinsu.

Sannan ku sani ya bayin Allah cewa, A'isha matar Annabi (ﷺ) ta tambaye shi idan na riski daren Lailatul Kadari me zance a cikinsa, sai ya ce ki ce, "Ya Ubangiji haƙiƙa Kai mai afuwa ne, kana son afuwa, ka yi afuwa a gare ni."

Ya Allah ka datar da mu a cikin waɗannan kwanaki masu albarka, Allah kai ne mai afuwa ka yi mana afuwa, ka gafarta mana da waɗanda suka gabace mu da imani, kada ka sanya ƙullata a cuciyarmu ga waɗanda suka yi imani, ya Ubanginmu kai ne mai gafar mai tausayi.

ZAKKAR FID-DA-KAI DA SALLAR IDI

Manufofin hudubar

- Bayani a kan abin da ya wajaba musulmi ya aikata bayan ƙarewar Ramadan.
- Bayanin tallafar juna da ke cikin musulunci.
- Bayanin hukunce-hukucen sallar idi da abin da ke cikinta na hikimomi.

Hudubа Ta Farko

Yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma mua neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan aiyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar dashi, wanda kuma ya atar babu mai shiryar da shi, kuma ina shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai allah, shi kaɗai ne bashi da abokin taraiya, kuma ina shaidawa cewa Annabi Muhammad bawansane manzonsane, (Yaku waɗanda kuka bada gaskiya kuji tsoron Allah yadda ya cancanta aji tsoronsa, kada ku mutu face kuna Musulmi). (Yaku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicce ku daga rai guda ɗaya kuma ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga gare su (su biyu) kuji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya dashi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku waɗanda suka yi imani kuji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku aiyukanku, kuma ya gafarta muku zunubanku. Wanda ya bi Allah da manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawun shiriya shiriyar Annabi Muhammadu (ﷺ) kuma mafi sharrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Ya ku bayin Allah! Ku ji tsoron Ubanjiginku, ku yi wa kanku hisabi, me kuke aiwatarwa a cikin watanku mai girma, domin shi baƙo ne mai gaggawar tafiya, ya kusa ya tafi ya bar ku, kuma zai zamo mai shaida a gare ku, ko a kanku, da abin da kuka ɓoye a cikinsa na ayyuka, to ku yi gaggawa – Allah ya jikan ku – ku ribaci abin da ya rage da cikinsa da tuba da neman gafara, da yawaita kyawawan maganganu, da ayyuka, da aiki zuwa ga ma'abocin girman da buwaya, da fatan wannan zai tohe muku giɓin da ya faru daga gareku.

Ya ku bayin Allah! Haƙiƙa Ubangijinku Mai girma ya shar'anta muku ibada masu girma a ƙarshen wannan wata, wanɗanda za su ƙara muku imani da cikar ibada da ni'imar Allah gare ku..

Zakkar Fid-da-kai; wata sadaka ce da take wajaba yayin gama azumin watan Ramadan. An san zakkar Fid-da-kai da suna na sadaka wajiba, saboda sauke azumin watan Ramadan. Domin sadaka wajiba daidai take da ma'anar zakka, don

haka ake kiranta zakkar fidda kai.

Ya ku bayina Allah! Malaman fiƙihu sun haɗu a kan cewa zakkar fid da kai wajibi ce a kan kowane Musulmi mai iko. Hadisin da aka rawaito daga Ibn Umar (R.A) yana nuna shar'anta ta, ya ce, "Manzon Allah (ﷺ) ya wajabta zakkar fid da kai a watan Ramadan a bisa mutane, sa'i guda na dabino, ko sa'i na sha'ir, a kan kowane ɗa, ko bawa, namiji ko mace, daga cikin musulmai" Bukhari ne ya rawaito. Umarni a nan yana nuna wajabci.

Musulunci ya shar'anta zakkar fid da kai saboda hikimomi guda biyu. Su ne;

Hikima ta farko: Tsarkake azumin mai azumi. An shar'anta zakkar fid da kai don toshe giɓin da yakan faru a cikin azumin mai azumi, saboda ba makawa a tsarkake shi daga ya sasshiyar magana, da batsa, da manyan lamura, da ƙananansu. Haƙiƙa Annabi (ﷺ) ya yi nuni zuwa haka a cikin hadisi inda Ibn Abbas ya ce, "Manzon Allah (ﷺ) ya farlanta zakkar fid da kai, don ta zam tsarki ga mai azumi, daga yasasshiyar magana, da sakin baki, don kuma ciyarwa ga musulmai" Ahmed ne ya rawaito shi.

Hikima ta biyu: Tallafwa faƙirai da miskinai. An shar'anta zakkar fid da kai don tausasawa miskinai da wadatar da su ga barin roƙo a ranar Idi, da shigar da farin ciki a zukatansu a ranar da mutane suke farin ciki, da annushuwa, domin ta hanyar ba su zakka ne za a sauƙaƙa musu damuwa da raɗaɗin talauci da wahala.

Ya ku bayin Allah! Akwai sharaɗai da suke wajabta zakkar Fid-da-kai sun:

Musulunci: Don haka bata wajaba a kan kafiri ba, koda yana da makusanta musulmai waɗanda ciyar da su ya wajaba akansa, domin zakka idaba ce ta Musulunci, ba ta wajaba a kan wanda ba Musulmi ba.

'Yanci: Ba ta wajaba a kan bawa a asali, domin ba ya mallakar dukiya, amma idan bawan ya zama mabiyi ne ga shugabansa, to a nan zakka ta wajaba a kan Ubangidansa, saboda wajabcin ciyarwarsa a kansa take, faɗin Annabi (ﷺ) "Ku ba da (zakkar Fid-da-kai) a madadin duk wani ɗa, ko bawa da kuke ciyar da shi".

Iko na dukiya: Akan fitar da ita, wannan iko kuwa yana tabbata ne, da mallakar dukiyar da ta ƙaru a kan buƙatarsa a daren idi da yininsa, don haka zakkar tana wajaba idan mutum ya mallaki wannan gwargwado na dukiya, ko da ya cancanci a ba shi zakka.

Shigar lokaci: Zakkar Fid-da-kai tana wajaba bayan gama azumin watan Ramadana, wannan kuwa na kasancewa ne da faɗuwar ranar yinin ƙarshe na azumi, domin babu azumi a bayansa. Kuma lokacinta yana ƙarewa ne dazarar a gama sallar idi. Kuma ba ya halatta a jinkirta ta, daga ranar idi. Idan ba a fitar da ita a ranar Idi ba, ya fitar daga baya to ta zama sadaka ba zakka ba.

Idan mutum ya zama mai gida, zai fitar da ita ga kansa, da wanda yake ciyar da su, kamar mata da ɗa, ko da ƙarami ne, da uwa da bawa da mai hidima. Hadisin "Ka fara da wanda kake ɗaukar nauyinsa". Yana ƙarfafa haka. Kuma Annabi (ﷺ) ya ce, "Ku ba da (zakkar fid da kai) a madadin kowane ɗa da bawa, daga waɗanda kuke ciyarwa".

Shi kuwa jinjirin da ba a haifa ba kafin Idin zakkar Fid-da-kai, a madadinsa ba ta wajaba a kan mahaifinsa ba, amma babu laifi idan ya fitar da ita, kuma zai sami ladan nafila.

Amma gwargwadon abin da za a fitar sa'i ne na alkama, ko sha'ir ko zabibi, ko wanin haka daga mafi rinjayen abincin mutanen garin. Sa'i kuwa a ma'aunanmu na zamani yana daidai da kilogram (2.176). An rawaito daga Ibn Umar cewa, Annabi (ﷺ) ya wajabta sadaƙar Fid-da-kai a sa'in na alkama.

Haƙiƙa malaman fiƙihu na Hanafiyya sun halarta fitar da ƙimarta daga kuɗi, ko kadarori, domin manufa dai ita ce, toshe buƙatar mabuƙata a ranar Idi, wannan kuwa yakan samu ta hanyar ba da kuɗi, kamar yadda yakan samu da ragowar jinsunan da suka zo a cikin hadisin. Sai dai jamhurun malaman fikihu sun tafi a kana rashin halarcin fitar da ƙima a cikin zakkar fid da kai, domin hadisai sun bayyana wasu jinsin na musamman daga alkama da sha'ir da zabibib.

Ibnu Taimiyya ya ce, "Amma fitar da kuɗi domin buƙata da maslaha da aadalci, babu laifi a yin hakan".

Ana rabata ga talakawa da misikinai a ranar Idi, domin shigar da farin ciki a garesu da samar musu da abin da suke buƙata.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah, kuma kyakkyawan ƙarshe yana ga masu tsoron Allah. Kuma babu sakamakon ta'addanci sai a kan bisa azzalumai. Allah ya yi tsira a bisa mafi darajar manzanni, Annabinmu Muhamamdu da alayensa da sahabbansa ya yi tsira.

Bayah haka: Ya ku bayin Allah! Haƙiƙa Allah ya shar'antawa musulmi idi guda biyu masu albarka, kowane daga cikinsu yana zuwa ne bayan wata idaba mai girma, kuma bayan aiwatar da wani rukuni daga rukunnan addnin musulunci. kuma akwai wadatuwa a cikin waɗannan idodi guda biyu ga musulmai da alheri da albarkatu da amfani mai yawa. Kuma sun zama a madadin iduka na jahilyya.

An karɓo daga Anas ya ce, "Manzon Allah (ﷺ) ya zo Madina ya iske suna da kwanaki biyu da suke wasanni a cikinsu, sai ya ce, "Waɗanne kwanaki ne waɗannan?" suka ce. "Mun kasance muna wasa a cikinsu a jahiliyya" sai ya ce, "Haƙiƙa Allah ya musanya muku da mafi alheri daga gare su: idin ƙaramar Sallah, da idin Babbar Sallah" Abu Dawud da Nasa'i ne suka rawaito shi.

Domin kowace al'umma tana da iduka da suka ƙunshi ma'anonin wannan addinin, da manufofinsa, da burace-buracen mabiyansa da kuma irin ibadojinsa.

Allah Ta'ala ya ce,

﴿لِّكُلِّ أُمَّةٍ جَعَلْنَا مَنسَكًا هُمْ نَاسِكُوهُ﴾[الحج: ٦٧].

(Kowace al'umma mun sanya mata idin da suke yi).

Ibn Abbas (R.A) ya fassara ma'anar (mansak): da idi. Ibn Jarir ne ya rawaito.

Al'ummomin da suke da addinin da aka saukar Allah ya sanya musu kwanakin idi don samun lada. Waɗanda kuma ba su da wani saukakken addini Allah ya

ƙaddar musu riƙar wasu kwanaki a matsayin kwanakin idi, don su ƙara tsunduma cikin ɓata.

Idi a shari'ar Annabi su ne idin layya, da idin ƙaramar sallah, da idin juma'a. Saɓanin haka kuwa to bukukuwa ne na jahiliyya, da suke ƙara wa mutum nisanta daga Allah. Kamar dai bikin ranar haihuwa.

Ya ku bayin Allah: Idi ya ƙunshi wasu ma'anoni na musulunci manya-manya, da amfani mai yawa. Idi ya ƙunshi aƙidar Musulunci tsarkakakkiyya tataciyya, wadda take ita ce mafi girman ni'ima da Allah ya yi wa ɗan Adam. Haka kuwa na tabbatar ta hanyar girmama Allah da kabbar gare shi, da kuma yabo da kirari a gare shi. Tare da shaidawa cewa, shi ne Ubangijin gaskiya wanda Musulmi yake neman kusanci zuwa gare shi, ta hanyar roƙo da fata, da neman taimako da dukkan nau'o'in ibada, ba tare da tara bautarsa da wani abu ba, kamar yadda Allah Ta'ala ya ce:

﴿ وَأَنَّ ٱلۡمَسَٰجِدَ لِلَّهِ فَلَا تَدۡعُواْ مَعَ ٱللَّهِ أَحَدٗا ١٨ ﴾ [الجن: ١٨].

(Kuma masallatai na Allah ne, don haka kada ku kira wani tare da Allah).

Shaidawa da gaskiya cewa Annabi Muhammadu bawansa ne kuma Mazonsa ne, ta hanyar bin umarninsa, da barin haninsa, da gaskanta labarinsa, da bautawa Allah da abin da ya shar;anta. Idi ya ƙunshi bayanin shari'ar musulunci, ta hanyar bayyana alamomi na idi, da gabatar da sallarsa, da bayyana hukunce-hukuncen musulunci a huɗubarsa.

Idi ya ƙunshi tsarkake ɗabi'u, da kyautata halaye, ta hanyar kwaɗaitarwa a kan haƙuri da juriya, da sa da zumunci a cikin wannan ranar, da afuwa, da tsarkake zukata daga ƙullata da hassada da gaba. Domin Idi yini ne na farin ciki da 'yan'uwantaka ta Musulunci.

Idi ya ƙunshi alaƙa ta 'yan uwantaka tsakanin Musulmi, da tallafawa ta zamantakewa ta hanyar ba da zakkar Fid-da-kai kafin sallah, saboda faɗinsa: "Ku wadatar da su ga barin yawon ruƙo a wannan yini". Yana nufin faƙirai. Daru Kuɗni ne ya rawaito shi daga Ibn Umar.

Idi ya ƙunshi sauƙin musulunci da rangwamensa, domin a wannan ranar Allah ya wajabta aje azumi, ya halarta daɗaɗan abubuwa, kamar yadda yake gabanin azumi wajen halatta su. Sai dai musulunci ya ƙulla wannan da babban tushe, wato imani da miƙa wuya ga Ubangijin talilkai, ya buɗe farin cikin idi da murnarsa ta hanyar buɗe shi da salla raka'a biyu da Allah Ta'ala. Don kada musulmi ya shantake wajen holewa ya manta da Ubangijinsa, wanda ya raine shi da ni'imomisa, ya ije masa bala'i, Allah Ta'ala ya ce;

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تُحَرِّمُواْ طَيِّبَٰتِ مَآ أَحَلَّ ٱللَّهُ لَكُمۡ وَلَا تَعۡتَدُوٓاْۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ ٱلۡمُعۡتَدِينَ ٨٧ وَكُلُواْ مِمَّا رَزَقَكُمُ ٱللَّهُ حَلَٰلٗا طَيِّبٗاۖ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ ٱلَّذِيٓ أَنتُم بِهِۦ مُؤۡمِنُونَ ٨٨ ﴾ [المائدة: ٨٧ – ٨٨].

(Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku haramta daɗaɗan abubuwa da Allah ya halatta muku, kuma kada ku wuce iyaka, haƙiƙa Allah ba ya son masu wuce iyaka. Kuma ku ci daga abin da Allah Ya azurta ku da shi, halak mai daɗi, kuma ku ji tsoron Allah wanda kuka yi imani da shi).

Ya ku bayin Allah, akwai hukunce-hukunce a waɗannan kwanaki, daga cikin

su akwai cewa, Allah ya shar'anta mana kabarbari bayan kammala azumin watan ramadan, sai ya ce,

﴿ وَلِتُكۡمِلُواْ ٱلۡعِدَّةَ وَلِتُكَبِّرُواْ ٱللَّهَ عَلَىٰ مَا هَدَىٰكُمۡ وَلَعَلَّكُمۡ تَشۡكُرُونَ ١٨٥ ﴾ [البقرة: ١٨٥].

(Kuma domin ku cika adadi, kuma ku girmama Allah saboda shiriyar ku da ya yi, ko kwa godewa Allah).

Annabi (ﷺ) ya yi umarni da sallar Idi ga maza da mata har da kullallun mata waɗanda ba al'adarsu ba ce su fita, da masu haila, domin su halarci addu'ar alheri, da addu'ar musulmi, su ƙauracewa wajan Sallah, kada su zauna cikin filin idin, domin filin idi masallaci ne, yana da duk hukunce-hukuncen masallaci.

Bukhari da Muslim sun ruwaito hadisi daga Ummu Aɗiyya (R.A) ta ce, "Manzon Allah (ﷺ) ya umarce mu da fitar da masu haila da kullallun mata, su masu haila su nisanci salla.- wani lafazin-: Su nisanci wajen Sallah, su halarci alheri da addu'ar musulmi, sai na ce, "Ya Ma'aikin Allah idan ɗayarmu ba ta da riga" sai ya ce, "'Yar uwarta ta tufatar da ita da rigarta."

Ku fito ya ku Musulmi zuwa sallar Idi, mazanku da matanku, yara da manya, don bauta ga Allah, da aiwatar da umarnin Manzon Allah, da neman alheri, da addu'ar Musulmi. Da yawa alheri da kyaututtuka kan sauka a filin idi daga Ubangiji mai girma, addu'o'i tsarkaka da ake karɓar su suna gudana a wannan guri. Mazaje su fita suna masu tsabta, suna masu sanya turare, suna masu sanya mafi kyawun tufafinsu. Sai dai bai halatta su sa alharini ba, da kowane abu na zinare, domin su haramun ne ga maza. Mata su fita cikin kamun kai, ba tare da sun sa turare ko bayyana ado ba.

Sunna ce mutum ya ci dabino kafin ya fita sallar idi, ya ci wuturi, uku ko biyar ko sama da haka in ya so, ya dai tsaya a kan mara. Anas ɗan Malik (R.A) ya ce, "Annabi (ﷺ) ya kasance ba ya fita da safe ranar idi har sai ya ci dabinai, kuma yana cin su mara"

Haƙiƙa Allah mabuwayi mai ɗaukaka ya ce,

﴿ لَّقَدۡ كَانَ لَكُمۡ فِي رَسُولِ ٱللَّهِ أُسۡوَةٌ حَسَنَةٞ لِّمَن كَانَ يَرۡجُواْ ٱللَّهَ وَٱلۡيَوۡمَ ٱلۡأٓخِرَ وَذَكَرَ ٱللَّهَ كَثِيرٗا ٢١ ﴾ [الأحزاب: ٢١].

(Haƙiƙa kuna da abin koyi kyakkyawa cikin lamarin Manzon Allah, ga wanda ya ke ƙaunar rahamar Allah da ladan ranar lahira, kuma ya ambaci Allah da yawa).

Ku ji tsoron Allah - ya ku bayin Allah - ku sadar da zumunci, domin ma'abata 'yan uwantakar jini, sashinsu shi ne mafi cancanta da sashi. Ku sadar da zamuncinsu, ko da sun yanke muku naku zumuncin. Allah ya dauwamar muku da albarkatunsa, ya yalawata muku arzikinku, ya albarkaci rayuwarku.

Ina neman tsari da Allah daga shaiɗani abin la'anta:

﴿ إِنَّ ٱللَّهَ يَأۡمُرُ بِٱلۡعَدۡلِ وَٱلۡإِحۡسَٰنِ وَإِيتَآيِٕ ذِي ٱلۡقُرۡبَىٰ وَيَنۡهَىٰ عَنِ ٱلۡفَحۡشَآءِ وَٱلۡمُنكَرِ وَٱلۡبَغۡيِۚ يَعِظُكُمۡ لَعَلَّكُمۡ تَذَكَّرُونَ ٩٠ ﴾ [النحل: ٩٠].

(Haƙiƙa Allah yana umarni da adalci da kyautatawa, da ba wa makusanta, kuma yana hani a kan alfasha da mummunan aiki, da zalunci. Yana yi muku wa'azi, tsammaninku za ku wa'azantu).

TSAWATARWA GAME DA FITINAR MATA

Manufofin hudubar

- Riga kafin fitinar mata.
- Tarbiyyantar da mata a kan kamun kai.
- Tunatar da musulmai nauyin da ke kansu.

Hudùba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammadu bawansa ne manzonsa ne. (Yaku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron Allah yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Yaku waɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammadu (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (a addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta".

Bayan haka: Haƙiƙa Allah ya umarci mutanen farko da na ƙarshe da jin tsoronsa, domin kuwa da dalilinta ne ake samun tsira da kuma rabautar duniya da ta lahira kamar yadda Allah maɗaukakin sarki yake cewa:

﴿ وَلِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۚ وَلَقَدۡ وَصَّيۡنَا ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ مِن قَبۡلِكُمۡ وَإِيَّاكُمۡ أَنِ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَۚ وَإِن تَكۡفُرُواْ فَإِنَّ لِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۚ وَكَانَ ٱللَّهُ غَنِيًّا حَمِيدٗا ١٣١ ﴾ [النساء: ١٣١].

“Kuma abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙassai duk na Allah ne. Kuma haƙiƙa mun yi wa waɗanda aka bai wa littafi gabaninku, da ku kanku wasiyya ku ji tsoron Allah. Idan kuwa kuka kafirce, to ku sani cewa (duk) abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙassai na Allah ne. Allah kuwa ya kasance mawadaci ne sha-yabo”.

Sai Allah ya yi umarni da jin tsoronsa, wanda shi ne kariyar afkawa zuwa kowace irin fitina, abin nufi da cewa a ji tsoronsa shi ne, a aikata umaninsa, kuma nisanci haninsa, a fili fa ɓoye. Kuma wannan umarni da Allah ya yi ya shafi gabaɗayan bayinsa; mazansu da matansu, sai dai maza su ne waɗanda suke

tsaye a kan al’amuran mata, don haka ya zama dole a kansu su ɗora mata a kan jin tsoron Allah mai girma da buwaya ta kowace hanyar tarbiyya wadda shari’a ta yarda da ita. Allah ya fifita maza a kan mata saboda abin da suke ciyarwa daga dukiyoyinsu, da kuma cikar hankalisu da hangen nesansu a cikin al’amura, da ma wasun waɗannan abubuwan. Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿ ٱلرِّجَالُ قَوَّٰمُونَ عَلَى ٱلنِّسَآءِ بِمَا فَضَّلَ ٱللَّهُ بَعۡضَهُمۡ عَلَىٰ بَعۡضٖ وَبِمَآ أَنفَقُواْ مِنۡ أَمۡوَٰلِهِمۡ ﴾ [النساء: ٣٤].

“Maza sama suke da mata saboda abin da Allah ya fifita sashinsu (da shi) bisa sashi, da kuma abin da suke ciyarwa daga dukiyoyinsu”.

Malam Shanƙiɗi Allah ya rahamshe shi, ya ce a ƙarƙashin tafsirin wannan aya: “Allah ya yi nuni da cewa namiji ya fi mace, saboda kasancewa namiji ɗaukaka ce da cika, matanci kuwa a asali, ɗabi’a ce ta tawaya. Kuma duk halittu sun haɗu a kan haka, domin kuwa za ka ga gabaɗayan mutane suna sanyawa mace dukkan nau’o’in kayan ado da kwalliya, wannan kuwa yana nuna ƙoƙarinsu ne na cike tawayar matanci. Saɓanin namiji, wanda kasancewarsa namiji kaɗai ya wadatar da shi daga ƙaye-ƙayen kwalliya da makamantan haka. Umarni da tsoron Allah ya shafi umartar kai da kuma iyalai, kuma maza su aka ɗorawa tsayuwa a kan mata saboda fifikon matsayinsu a kansu.

Sannan kuma abu ne a fili gare mu gabaɗaya cewa, halin da mata muslmai ke ciki a yau ya saɓa da irin halin da matan musulmai suke kai a lokacin Manzon Allah, (ﷺ). Matanmu a yau sun zaɓi hanyar ‘yan ba ruwanmu da addini, don haka da su suke koyi sau da ƙafa kamar dai yadda hadisi ya ambata, yanzu mafi yawancin matanmu sun fice daga bin shiriyar addini miƙaƙƙe da hanya madaidaiciya, sun koma bin bayyananniyar hanyar ɓata wadda za ta jefa su a cikin wutar hawiya! Allah ka tsare mu, amin.

Kuma wannan saɓawa da mata suka yi hotonsa na fitowa fili ne ta salo daba-daban, manya daga cikinsu su ne:

Cakuɗuwarsu da maza a ma’aikatun hukuma, da ƙananan makarantu da manya. Da kuma cakuɗeɗeniyar maza da mata a kasuwanni da motocin haya da makamantan haka, alhaku kuwa duk wannan haramun ne, Allah maɗaukaki ya ce:

﴿ وَلَمَّا وَرَدَ مَآءَ مَدۡيَنَ وَجَدَ عَلَيۡهِ أُمَّةٗ مِّنَ ٱلنَّاسِ يَسۡقُونَ وَوَجَدَ مِن دُونِهِمُ ٱمۡرَأَتَيۡنِ تَذُودَانِۖ قَالَ مَا خَطۡبُكُمَاۖ قَالَتَا لَا نَسۡقِي حَتَّىٰ يُصۡدِرَ ٱلرِّعَآءُۖ وَأَبُونَا شَيۡخٞ كَبِيرٞ ٢٣ فَسَقَىٰ لَهُمَا ثُمَّ تَوَلَّىٰٓ إِلَى ٱلظِّلِّ فَقَالَ رَبِّ إِنِّي لِمَآ أَنزَلۡتَ إِلَيَّ مِنۡ خَيۡرٖ فَقِيرٞ ٢٤ فَجَآءَتۡهُ إِحۡدَىٰهُمَا تَمۡشِي عَلَى ٱسۡتِحۡيَآءٖ قَالَتۡ إِنَّ أَبِي يَدۡعُوكَ لِيَجۡزِيَكَ أَجۡرَ مَا سَقَيۡتَ لَنَاۚ فَلَمَّا جَآءَهُۥ وَقَصَّ عَلَيۡهِ ٱلۡقَصَصَ قَالَ لَا تَخَفۡۖ نَجَوۡتَ مِنَ ٱلۡقَوۡمِ ٱلظَّٰلِمِينَ ٢٥ ﴾ [القصص: ٢٣ – ٢٥].

(Lokacin kuma da (Annabi Musa) ya gangara wajen ruwan Madyana sai ya sami wasu mutane masu yawa suna shayar (da dabbobinsu), kuma ya sami wasu mata su biyu a gefensu suna tsare dabbobinsu, sai ya ce (da su) “Me ya same ku ne”? Sai suka ce: “Mu ai ba ma shayarwa har sai duk makiyayan sun juya, kuma mahaifinmu tsoho ne tukuf”. To sai ya shayar musu (da dabbobin nasu) sannan ya koma wurin wata inuwa ya ce, “Ya Ubangijina haƙiƙa ni maɓuƙace ne ga abin da

ka saukar zuwa gare ni na alheri”. Sai ɗayarsu ta zo masa tana tafiya cikin kunya ta ce: “Babana yana kiran ka don ya saka maka ladan shayarwar da ka yi mana”. To lokacin da ya zo wurinsa ya kuma ba shi labarin (abubuwan da suka faru da shi) sai ya ce da shi, “Kada ka ji tsoro, ka tsira daga azzaluman mutane”).

Ya ‘yan uwa! Ku yi tunani a kan irin wannan matsayin da waɗannan ‘yan mata suka ɗauka. Sannan kuma a auna shi da abubuwa da suke faruwa a yau.

Bayan haka: An karɓo daga Abdullahi bn Amr, daga Manzon Allah, (ﷺ) ya ce: “Ku umarci ‘ya’yanku da salla suna ‘yan shekara bakwai, ku kuma ɗake su a kan sakaci da ita idan suna ‘yan shekara goma, sannan kuma ku raba tsakaninsu a wajen kwanciya”. Abu Dawud da Hakim ne suka rawaito shi.

Wannan hadisi yana nuni a kan cewa haƙiƙa musulunci ya haramta cakuɗar maza da mata, kuma yana ba da tarbiyya a kan kame kai tun a lokacin yarinta.

Halin kuwa da mafi yawan mata suke kai a yau na saɓawa dokokin shari’a, irin su cakuɗuwa da maza a kasuwanni, da ɗaga murya da wasun haka, gyransu haƙƙi ne da yake wuyan kowa, don haka ya zama dole kowa ya tsayu da sauke nasa nauyin ko da yake hukuma ita ta fi kowa kaso mafi yawa.

Bayyanar da ado ma, da fitar da sassan jiki, da suke motsa sha’awa su kuma haifar da ɓarna su ma na daga cikin gagga-gaggan saɓo. Domin kuwa su ne hanyar da ke sadarwa zuwa ga zina. Ga shi kuwa Allah ya yi umarni da sa hijabi kuma ya ce, a rintse idanuwa, kuma yana hana fitar maguzanci. Allah maɗaukakin sarki yana cewa:

﴿ قُل لِّلۡمُؤۡمِنِينَ يَغُضُّواْ مِنۡ أَبۡصَٰرِهِمۡ وَيَحۡفَظُواْ فُرُوجَهُمۡۚ ذَٰلِكَ أَزۡكَىٰ لَهُمۡۗ إِنَّ ٱللَّهَ خَبِيرُۢ بِمَا يَصۡنَعُونَ ٣٠ وَقُل لِّلۡمُؤۡمِنَٰتِ يَغۡضُضۡنَ مِنۡ أَبۡصَٰرِهِنَّ وَيَحۡفَظۡنَ فُرُوجَهُنَّ وَلَا يُبۡدِينَ زِينَتَهُنَّ إِلَّا مَا ظَهَرَ مِنۡهَاۖ وَلۡيَضۡرِبۡنَ بِخُمُرِهِنَّ عَلَىٰ جُيُوبِهِنَّۖ وَلَا يُبۡدِينَ زِينَتَهُنَّ إِلَّا لِبُعُولَتِهِنَّ أَوۡ ءَابَآئِهِنَّ أَوۡ ءَابَآءِ بُعُولَتِهِنَّ أَوۡ أَبۡنَآئِهِنَّ أَوۡ أَبۡنَآءِ بُعُولَتِهِنَّ أَوۡ إِخۡوَٰنِهِنَّ أَوۡ بَنِيٓ إِخۡوَٰنِهِنَّ أَوۡ بَنِيٓ أَخَوَٰتِهِنَّ أَوۡ نِسَآئِهِنَّ أَوۡ مَا مَلَكَتۡ أَيۡمَٰنُهُنَّ أَوِ ٱلتَّٰبِعِينَ غَيۡرِ أُوْلِي ٱلۡإِرۡبَةِ مِنَ ٱلرِّجَالِ أَوِ ٱلطِّفۡلِ ٱلَّذِينَ لَمۡ يَظۡهَرُواْ عَلَىٰ عَوۡرَٰتِ ٱلنِّسَآءِۖ وَلَا يَضۡرِبۡنَ بِأَرۡجُلِهِنَّ لِيُعۡلَمَ مَا يُخۡفِينَ مِن زِينَتِهِنَّۚ وَتُوبُوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ جَمِيعًا أَيُّهَ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ لَعَلَّكُمۡ تُفۡلِحُونَ ٣١ ﴾ [النور: ٣٠ – ٣١].

(Ka ce wa muminai maza, su runtse daga ganinsu, kuma su tsare farjojinsu. Wannan shi ne mafi tsarki a gare su. Lallai ne Allah, Masani ne ga abin da suke aikatawa. Kuma ka ce wa muminai mata, su runtse daga gannansu, kuma su tsare farjojinsu, kuma kada su bayyana adonsu, face abin da ya bayyana daga gare ta, kuma su doka da mayafansu a kan wuyan rigunansu, kuma kada su nuna adonsu face ga mazansu ko ubanninsu, ko ubannin mazansu, ko ‘ya’yansu ko ɗiyan mazansu, ko ‘yan’uwansu ko ‘yan’yan ‘yan’uwansu, ko ‘yan uwansu maza, ko ‘ya’yan ‘yan’uwansu mata, ko matansu, ko ƙwaraƙwaransu, ko mabiya, ba masu buƙatar mata ba daga maza, ko ƙananan yara waɗanda ba su tsinkaya a kan al’aurar mata. Kuma kada su yi duka da ƙafafunsu, domin a san abin da suke ɓoyewa daga adonsu. Kuma ku tuba zuwa ga Allah gabaɗaya, ya ku muminai. Tsammaninku, ku sami babban rabo).

Kiyaye farji, yana iya nufin rufe tsiraici, da kuma nisantar zina.

Imamu Ahmad da Muslim sun ruwaito hadisi daga Abu Huraira ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: “Sanfirin mutane biyu ‘yan wuta ne, har yanzu ban gan su ba. (Na farkonsu) wasu jama’a ɗauke da bulalu kamar jelar shanu suna dukan mutane da su, da kuma wasu mata sanye da sutura amma kuma suna tsirara, masu karkataccen hali, masu kwarkwasa, kawunansu kamar karkataccen tozon raƙumi, ba za su shiga aljanna ba kuma ba za su ji ƙamshinta ba, ga shi kuwa ana jiyo ƙamshinta tun daga nisan kaza da kaza.

Ɗan Abdulbarri ya ce: “Manzo Allah (ﷺ) yana nufin matan da suke sa shara-sharan kayan da suke siffata jiki kuma ba sa suturce shi, a suna sun sa sutura, amma kuma a haƙiƙance kuma tsirara suke. Karkatattu daga bin gaskiya, kuma masu karkatar da mazajensu daga gaskiya. ‘Yan uwa a yi hattara.

Malamai sun yi bayanin abin da ake nufin da (Sanye da kaya, kuma tsirara) cewa, ita ce macen da take sa shara-sharan kayan da ba za su rufe mata tsiraici ba, ko matsattsun kayan da suke bayyana sassan halittarta. Alhali kuwa suturar mace a shari’ance ita ce wadda take suturce ta, ba tare da ta bayyanar da jikinta ba, ko wata gaɓa daga cikin gaɓɓanta ba, saboda kaurin kayan da kuma yalwarsu.

Wannan shi ne abin da ya sauƙaƙa. Allah ya yi mana gafara ni da ku da sauran musulmi bakiɗaya. Lalle shi mai karɓar gafara ne mai jin ƙai.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga fiyayyen halitta baki ɗaya, da iyalansa da sahabbansa, da wanda ya bi shiriyarsa, kuma ya yi riƙo da sunnarsa har zuwa ranar sakamako.

Bayan haka: Haƙiƙa matan magabata Allah ya rahamshe su, masu kamun kai ne, masu sanya hijabi ne, masu kuma biyayya ga Ubangijin talikai ne, a duk abin da aka umarce su. Mu kalli labarin ƙagen da aka yi wa Nana A’isha. Labarin ya bayyana cewa A’isha ba ta yi wa wannan sahabi magana ba, (wato Safwan Ibn Mu’aɗɗil), kuma shi ma ko kalma bai ce mata ba, sai dai ji ta yi yana cewa, inna lillahi wa inna ilaihi raji’un, a yayin da ya gan ta haka dai har suka iso Madina.

A yayin da aka yi umarni da hijabi nan take suka rungume shi da gaggawa.

Ya zo a cikin ingantaccen hadisi daga Ummu Salama ta ce: Yayin da wannan ayar ta sauka:

﴿يُدۡنِينَ عَلَيۡهِنَّ مِن جَلَٰبِيبِهِنَّۚ﴾ [الأحزاب: ٥٩].

(Su yafa mayafansu).

Matan Madina sai suka rinƙa fita kamar masu ɗauke da hankaki a kansu, saboda nutsuwa, suna sanye da baƙaƙen tufafi. Allahu Akbar, ka ji gaggawar amsa umarnin Allah da na Manzonsa.

An karɓo daga Ummu Salama ta ce, wata mace ta ce da ita: “Ni mace ce da nake tsawaita leɓatun suturata, kuma nakan wuce ta gurin da yake da ƙazanta. Sai ta ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Abin da yake biye da shi yana tsarkake shi”. Malik da Ahmad da Tirmizi da Abu Dawud da kuma Darimi ne suka rawaito shi.

Malam Baji, ya ce: “yayin da suka bi umarnnin da aka yi musu, kuma suka hanu daga hanin da aka yi musu sai Allah ya tsare su daga fitintinu da bala’ai na duniya da lahira kuma ya tanadar musu da lada mai girma.

Matan magabata sun sami tarbiyyar kamun kai, da kunya da aiwatar da umarni tare da nisantar hani, don haka muna da kyakkyawan abin koyi game da su, amma fa ga wanda yake fatan haɗuwa da Allah da manzo da ranar lahira sumul ƙalau.

Ya bayin Allah! Idan fa muka bar matanmu da ‘ya’yanmu ba nusarwar ƙwarai zuwa ga Ubangiji, ba shakka za su faɗa cikin halaka.

Allah dai ya sanya maza su zama tsayayyu a kan mata. Su kuma mata ya yi su masu raunin hankali da addini don haka ne ma manzo ya yi wasiyyar alheri game da su. Kamar yadda yake a cikin hadisin Amr ɗan Ahwas al-Jushami, Allah ya yarda da shi ya ce, Haƙiƙa ya ji Annabi (ﷺ) a hajjin ban kwana yana cewa, bayan ya godewa Allah ya yi masa kirari kuma ya tunatarwa, ya yi gargaɗi sannan sai ya ce: “Ku saurara ku yi wasiyyar alheri ga mata, haƙiƙa su mataimaka ne gare ku". A wani lafazin hadisin. “……..Haƙiƙa an halicci mace ne daga ƙashin haƙarƙari, kuma mafi kantarar ƙashin haƙarƙarin mafi ɗaukakarsa, in ka tafi miƙar da shi ka karya shi in ka bar shi kuma ba zai daina karkata ba, don haka ku yi wa mata wasiyya. Manzo Allah ﷺ) ya keɓe mata da cewa, a yi musu wasiyya ne saboda rauninsu da kuma buƙatuwasu ga wanda zai tsayu a kan tafiyar da al’amuransu. Shi ya sa ya ce, ku karɓi wasicina game da su, kuma ku yi aiki da ita, ku kuma yi haƙuri da su ku tausasa musu kuma ku kyautata musu. Babu shakka idan mace ta rasa nusarwa za ta iya zama shaiɗaniyar kanta, kuma ɓatacciya mai ɓatar da mutane daga hanya maidaidaiciya. Hatta karuwan da ake da su a yau, sun isa shaida kan yadda macen da ta rasa saiti da nusarwa take zama. Ya ‘yan’uwa! Wannan bai isa ya sa mu faɗaka ba?

Don haka ya ke 'yar uwata musulma, ki ji tsoron Allah, ki ƙanƙame addininki, ki yi riƙo da musuluncinki, kuma ki yi alfahari da riƙo da addininki. Ki ɗaga kanki sama a ko ina. Kuma ki guji kuraye masu fuskokin mutane, rundunar Iblis, waɗanda suke nemanki ruwa a jallo su faruto ki cikin ruwan sanyi, sannan su halaka ki a tsanake. Ko da yaushe kasance tare da littafin Allah da sunnar Annabi (ﷺ). Ki yi koyi da raywar matan farko na ƙwarai daga matan sahabbai da tabi'ai. Idan kin yi haka za ki samu rabauta da gidan aljanna, da yardar Allah.

HIKIMOMI DA SIRRIKAN HAJJI

Manufofin huɗubar

- Tunatar da mutane sirrikan Hajji da hikimominsa
- Tunatar da su da ni'imar musulunci
- Bayanin zamantowar addini tilas ne da muhimmancin ibada ga mutum ɗaya da al'umma
- Bayanin cewa gyara ba ya yiwa sai da addinin gaskiya

Huɗuba Ta Farko

Yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarin sa daga sharrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar da shi babu mai shiryar da shi; kuma ina shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin taraiya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammadu bawansa ne Manzonsa ne (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron Allah yadda ya cancanci a ji tsoronsa ne. Kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicce ku daga rai guda ɗaya, kuma ya halicci matarsa daga gare shi, kum aya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron Allah kuma ku faɗimagana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawun shiriya shiriyar Annabi Muhammadu (ﷺ). kuma mafi sharrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (a addini) bidi'a ne, duk wata bidi'a ɓata ce, duk wani ɓata yana wuata.

Bayan haka:

Ya ku mutane, shin kun ga aikin hajji da irin girmansa, shin kun ga imani da haskakawarsa, kun ga cincirindon jama'a yadda suka zo suna girmama Allah suna kambama shi suna yabonsa? Lallai kallon taron hajji abu ne mai ban mamaki, abin kallo ne mai ɗimauta hankali. Muminai suna farin ciki da shi, masu tauhidi sun ɗaukaka da shi. Masu laifi sun shaƙe da shi. Gafalallu sun razana da shi. To menene manufar aikin hajji ne ya ku musulmi? Ba na tsammani waɗannan tarurruka manya suna wucewa ba tare da izini ba, ko wannan adadi mai girma yana shuɗewa ba tare da la'akari ba. Haƙiƙa waɗannan cincirindo na mutane sun zo ne don su amsa kiran da Allah ya yi musu, sun zo suna girmama Allah, Allah yana cewa,

﴿ وَلِلَّهِ عَلَى ٱلنَّاسِ حِجُّ ٱلۡبَيۡتِ مَنِ ٱسۡتَطَاعَ إِلَيۡهِ سَبِيلٗاۚ وَمَن كَفَرَ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَنِيٌّ عَنِ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٩٧ ﴾ [آل عمران: ٩٧].

(Kuma Allah ya wajabtawa mutane ziyartar ɗaki ga wanda ya sami iko zuwa gare shi).

Taro ne babba da duniya kan girgiza saboda shi, maƙiya su tsorata da shi, yahudu da nasara su razana, shin kun kiyaye haka? Shin kun ji girman wannan addini, da girman wannan al'umma?

Ya ku 'yan uwa, haƙiƙa hajji ya zamo fage ne na haɗin kan Al'umma bayan rabuwanta, kuma wata matashiya ta girman wannan al'umma bayan wulaƙantuwarta, kuma alamar rayuwarta da samuwarta. Bai kamata al'umma ta gafala daga hikimomin aikin hajji ba da sirrinkansa, domin shi ne maɗaurin alaƙoƙi. Fage na sanin juna da jaddada imani, da zurfafa alaƙoƙi da zumunci; domin a cikinsa ne musulmi yake sanin ɗan uwansa daya zo daga guri mai nisa, sai ya ji daga gare shi; ya amayar masa da damuwarsa, ya taimaka masa wajan biyan buƙatunsa. Ya ku bayin Allah, haƙiƙa tsayawa kaɗan tare da ayoyin aikin hajji cikin littafin Allah ta'ala ya isa ya baiyyana mana wani abu na sirrikan hajji da hikimominsa, da abin da ya ƙunsa na ma'anoni tare da tsaftace halaiya, da hanyoyin rabuwa da munanan halaye da ke bayuwa zuwa ado da kyawawa.

Wannan tsokaci yakan baiyana ne cikin mafi girman hikimomi da manufofi na wannan ibada mai girma. Haƙiƙa tsayuwa ce tare da kaɗaita Allah mai girma da ɗaukaka, wanda aka gina ɗaki dadaɗɗe saboda shi, kuma aka sanya nufatarsa daga sassan duniya dan haɓaka ibdar tauhidi da tsarkake ta ga Allah (S.W.T) wanda ba shi da abokin taraiya. Allah yana cewa,

﴿ وَإِذۡ بَوَّأۡنَا لِإِبۡرَٰهِيمَ مَكَانَ ٱلۡبَيۡتِ أَن لَّا تُشۡرِكۡ بِي شَيۡـٔٗا وَطَهِّرۡ بَيۡتِيَ لِلطَّآئِفِينَ وَٱلۡقَآئِمِينَ وَٱلرُّكَّعِ ٱلسُّجُودِ ٢٦ ﴾ [الحج: ٢٦].

(Kuma yayin da muka ajiye Ibrhaimu a wajan ɗaki, muka ce, kada ka haɗa bauta ta da wani abu, kuma ka tsarkake ɗaki na ga masu ɗawafi da masu tsayuwa da masu yin ruku'u, masu yin sujjada).

Haƙiƙa tataccen tauhidi shi ne ƙashin bayan halifancin mutum a bayan ƙasa, kuma mafificin abin da ake nema, mafi girman abin da ake kwaɗayi, mafi darajar abin da ake dangantuwa gare shi. Ba a kafa mulki mai ƙwari sai a kan turaku na tauhidi, kuma ba ya gushewa ya tafi sai don ɓacewar tauhidin. Daular musulunci ba ta ɗaukaka ba sai da yaɗuwarsa, kuma ba ta ƙaskanta ba, ba ta tozartaba sai da barbajewarsa.

Shi ne tataccen tauhidi wanda yake tattara mutane zuwa tudun kwanciyan hankali da kariya daga guguwar shirka ga Allah cikin bautarsa, da ayyukansa, da shisshigi cikin sunayensa. Tauhidi ne da ya tattaro kyakkyawan fata wajen Allah, da tsoronsa, da neman taimako da agaji wajensa, kuma kada a yi hukunci aban ƙasa sai da abin da ya shar'anta (S.W.T). Tauhidi ne da yake mamaye zukatan musulmi da yaƙini, wanda aka shar'anta hajji saboda shi, Allah Subhanahu yana cewa,

﴿ حُنَفَآءَ لِلَّهِ غَيۡرَ مُشۡرِكِينَ بِهِۦۚ وَمَن يُشۡرِكۡ بِٱللَّهِ فَكَأَنَّمَا خَرَّ مِنَ ٱلسَّمَآءِ فَتَخۡطَفُهُ ٱلطَّيۡرُ أَوۡ تَهۡوِي بِهِ ٱلرِّيحُ فِي مَكَانٖ سَحِيقٖ ٣١ ﴾ [الحج: ٣١].

(Suna masu bin miƙaƙƙen addini, ba masu tara bautarsa da wani ba, kuma duk wanda ya yi shirka da Allah, to kamar ya rikito ne daga sama, sai tsuntsaye su fyauce shi, ko iska ta sulmiya da shi cikin wani guri mai zurfi).

Don haka Allah ya sanya Ka'aba ɗakin Allah mai alfarma don tsayuwar maslahar mutane. Shi kuwa hajarul Aswadu alama ce ta gane mafara da aka sanya a cikin wannan gini mai albarka. Ba wai guri ne na neman albarka a wjan duwatsu ba, in ban da koyi da Annabi wajan sumbantarsa, da kewaya ɗaki. Haƙiƙa Umar Alfaruk (R.A) ya bayyana wannan kyakkyawar fahimtar da faɗinsa: (haƙiƙa ni nasan cewa kai dutse ne da ba ka cutarwa ba ka amfanarwa, kuma ba don ina ganin Manzon Allah yana sumbantar ka ba, da ban sumbace ka ba).

Ya wajaba musulmi ya sani sani na sakankancewa yayin da yake yin ɗawafi a ɗaki, ya ke sumbatar Hajarul Aswadi, yake shafar Rukunul Yamani cewa mai amfanarwa da cutarwa shi ne Allah ta'ala shi kaɗai. Kuma duk wani tasgaro ga wannan ma'ana yana jefa mutum ne cikin farautar shirka da Allah wanda ba a kafa daɗaɗɗen ɗaki ba sai don kore shi da gusar da shi. Don haka ne Annabi (ﷺ) ya aiki Abubakar (R.A) a shekara ta tara bayan hijira don ya yi kira cikin mutane, ranar layya cewa kada wani mushriki ya yi hajji daga bana, kuma kada wani mutum ya sake ɗawafi tsirara. Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

﴿ ذَٰلِكَ وَمَن يُعَظِّمۡ حُرُمَٰتِ ٱللَّهِ فَهُوَ خَيۡرٞ لَّهُۥ عِندَ رَبِّهِۦۗ وَأُحِلَّتۡ لَكُمُ ٱلۡأَنۡعَٰمُ إِلَّا مَا يُتۡلَىٰ عَلَيۡكُمۡۖ فَٱجۡتَنِبُواْ ٱلرِّجۡسَ مِنَ ٱلۡأَوۡثَٰنِ وَٱجۡتَنِبُواْ قَوۡلَ ٱلزُّورِ ٣٠ ﴾ [الحج: ٣٠].

(wannan kenan, kuma wanda ya girmama alfarmomin Allah to shi ne mafi alheri gare shi. Kuma an halatta muku dabbobin ni'ima, sai fa idan abubuwan da ake karantawa a gare ku, don haka ku nisanci ƙazanta daga gumaka, kuma ku nisanci maganar ƙarya).

Wani la'akarin - Ya bayin Allah - tare da ayoyin hajji; shi ne inda Allah mai buwaya da ɗaukaka ya sanya hukunce-hukuncensa da ladabansa, don mutane su san abin da ya wajaba a gare su a waɗancan farfajiyoyi, da abin da ya wajaba na girmama umarnin Allah da barin wasa da shi, ko kasala da sakaci, domin ibada ba guri ne na wasa, ko tasgaro ba ta kowace fuska ba, don haka faɗin Allah subhanahu wata'ala ya zo yana mai gargaɗi ga mai tauyewa a cikinta, yana sakaci da ita, inda yake cewa bayan jero wasu abubuwa na daga hukunce-hukuncen aikin hajji. Kamar inda Allah yake cewa,

﴿ ذَٰلِكَ لِمَن لَّمۡ يَكُنۡ أَهۡلُهُۥ حَاضِرِي ٱلۡمَسۡجِدِ ٱلۡحَرَامِۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ ١٩٦ ﴾ [البقرة: ١٩٦].

(Wannan ga wanda iyalinsa ba su kasance mahalartan masallaci mai lafarma ba. Kuma ku ji tsoron Allah, kuma ku sani cewa, Allah mai tsananin uƙuba ne), Bai ce: Ku sani cewa Allah mai gafara ne mai rahama ba. Wannan kuwa don ƙarfafa alfarmar hajji ne da kyautata aiwatar da shi yadda ya kamata; domin yana aukuwa ne cikin iyakokin Allah ta'ala da ya shar'anta. Shi ne kuwa yake cewa:

﴿ وَمَن يَتَعَدَّ حُدُودَ ٱللَّهِ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ٢٢٩ ﴾ [البقرة: ٢٢٩].

(Wanda ya tsallake iyakokin Allah to waɗannan su ne azzalumai). Kuma don muminai su lura da gaske cewa, uƙuba tana tare da sakaci.

Wani la'akari tare da ayoyin hajji, shi ne, su na bayyana aikin hajji a matsayin wani bigire ne na taimakekeniya, da kyauta, da jin abin da wasu ke ji, da toshe buƙatunsu, har a guraren ibada. Aya ta zo a jerin bayanin hajji tana nuna girman taimakekeniya, da buƙatuwa zuwa tausayawa ga talakawa, da mayunwata da toshe yunwarsu, Allah ta'ala yana cewa,

﴿ لِّيَشۡهَدُواْ مَنَٰفِعَ لَهُمۡ وَيَذۡكُرُواْ ٱسۡمَ ٱللَّهِ فِيٓ أَيَّامٖ مَّعۡلُومَٰتٍ عَلَىٰ مَا رَزَقَهُم مِّنۢ بَهِيمَةِ ٱلۡأَنۡعَٰمِۖ فَكُلُواْ مِنۡهَا وَأَطۡعِمُواْ ٱلۡبَآئِسَ ٱلۡفَقِيرَ ٢٨ ﴾ [الحج: ٢٨].

(domin su halarci anfani gare su, kuma su ambaci sunan Allah a cikin kwanaki sanannu, a bisa abin da ya azurtasu na daga dabbobin ni'ima. Ku ci daga gare su, kuma ciyar da matalauci faƙiri). A cikin wata ayar kuma yana cewa:

﴿ فَإِذَا وَجَبَتۡ جُنُوبُهَا فَكُلُواْ مِنۡهَا وَأَطۡعِمُواْ ٱلۡقَانِعَ وَٱلۡمُعۡتَرَّۚ كَذَٰلِكَ سَخَّرۡنَٰهَا لَكُمۡ لَعَلَّكُمۡ تَشۡكُرُونَ ٣٦ ﴾ [الحج: ٣٦].

(Idan gefensu ya faɗi to ku ci daga gare su, kuma ku ciyar da wanda yake mai kamewa (daga tambaya) da mai bijirowa (da yinta). Hakane muka yassare muku su tsammaninku za ku gode). Shi alƙani'i: shi ne wanda baya roƙon mutane don jin nauyi tare da jin yunwarsa da talaucinsa, shi kuwa almu'utar shi ne talakan da yake roƙon mutane.

La'akari na huɗu: Shi ne, martabar taƙawa da girman tasirinta, da cewa ita ce ma'auni wanda ake auna ayyuka da shi, ake auna mutane da shi, don haka wasiyya da taƙawa ta yawaita a cikin ayoyin hajji, domin haƙiƙa Allah ta'ala ya ce,

﴿ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ ١٩٦ ﴾ [البقرة: ١٩٦].

(Kuma ku ji tsoron Allah, kuma ku sani Allah mai tsananin uƙuba ne).

Kuma ya ce,

﴿ وَتَزَوَّدُواْ فَإِنَّ خَيۡرَ ٱلزَّادِ ٱلتَّقۡوَىٰۚ وَٱتَّقُونِ يَٰٓأُوْلِي ٱلۡأَلۡبَٰبِ ١٩٧ ﴾ [البقرة: ١٩٧].

(Kuma ku yi guzuri, domin mafi alherin guzuri shi ne tsoron Allah. Kuma ku ji tsorona ya ma'abota hankali).

Kuma Allah Subhanatu wata'ala ya ce,

﴿ فَمَن تَعَجَّلَ فِي يَوۡمَيۡنِ فَلَآ إِثۡمَ عَلَيۡهِۚ وَمَن تَأَخَّرَ فَلَآ إِثۡمَ عَلَيۡهِۚ لِمَنِ ٱتَّقَىٰۗ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّكُمۡ إِلَيۡهِ تُحۡشَرُونَ ٢٠٣ ﴾ [البقرة: ٢٠٣].

(Wanda ya yi gagagwa a kwana biyu babu laifi a kansa, wanda ya jinkirta shi ma babu laifi a kansa, ga wanda ya ji tsoron Allah). Kuma ya ce,

﴿ ذَٰلِكَ وَمَن يُعَظِّمۡ شَعَٰٓئِرَ ٱللَّهِ فَإِنَّهَا مِن تَقۡوَى ٱلۡقُلُوبِ ٣٢ ﴾ [الحج: ٣٢].

(Kuma wanda ya girmama alamomin bautar Ubangiji to yana cikin jin tsoron Allah na zukata). Kuma subhanahu ya ce,

﴿ لَن يَنَالَ ٱللَّهَ لُحُومُهَا وَلَا دِمَآؤُهَا وَلَٰكِن يَنَالُهُ ٱلتَّقۡوَىٰ مِنكُمۡ ﴾[الحج: ٣٧].

(Namansu da jinayansu ba sa samin Allah, sai dai tsoron Allah ne daga gare ku zai riske shi).

Tsoron Allah - ya bayin Allah - shi ne matattarar alheri gaba ɗaya.

Haƙiƙa kai msulmi, idan ka bautawa Allah a kan haske, kana fatan ladan Alah,

ka bar haramtattun abubuwan da Allah ya haramta, a bisa haske daga Allah, kana tsoron ukubarsa, hakika ka tabbatar da tsoron Allah dungurungum dinsa a rayuwar ka, wanda karkashinsa za ka tabbatar da hakkokin da aka rataya maka game da mahaliccin ka, da 'yan uwanka a addini.

Dukkan kujuba-kujuba ta ayyukan hajji - Ya bayin Allah –suna nuna wannan manufa, domin musulmi kamar jiki daya ne, kamar gini ne da sashinsa kan karfafar sashi. musulmai a farfajiyoyin hajji mai albarka suna rayuwa a lokutan da ma'anar takawa da take fitar da tushen yan uwantaka mai karkarfan madauri ke tabbata. Wadda take hada kan musulmi tare da sabanin garuruwansu da harasansu, a yayin da alhazai ke canja tufafinsu na yau da kullum, su sa tufafin hajji iri daya, su fito cikin kama daya, su fuskanci Ubangiji daya, da talbiya daya, su jefar da duk wani kirari a kasa, da wani take na bangaranci, su rungumi wannan talbiyya, suna kewaya daki daya, suna aiwatar da ibada daya. Lallai wanna hoto mai rai na amafanin takawa, da kuma yake nunawa mutane cewa babu wasu dalilai na hankali da za su sa su su rika rayuwa cikin kiyayya da kyamar juna, da rarrabuwa dama da hauni. Babu wasu dalilai da za su sa masu girmankai za su yi girman kai, masu dagawa su yi dagawa. Babu wasu dalilai da za su ba da damar yin alfahari da dangi ko lakabila. Kai idan takawa ta ginu a zuciyar bawa za ta sanya shi yana halarto da cewa Allah ta'ala ya sanya nasabar mutane da jinsunansu duk ga iyaye biyu, don ya sanya mahaifar Nana Hauwa'u wata mahada ce mai fadi wadda zumunce-zumunce kan sassarke a jikinta, kuma alakoki kan karfafu da ita. Allah ya ce,

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِنَّا خَلَقۡنَٰكُم مِّن ذَكَرٖ وَأُنثَىٰ وَجَعَلۡنَٰكُمۡ شُعُوبٗا وَقَبَآئِلَ لِتَعَارَفُوٓاْۚ إِنَّ أَكۡرَمَكُمۡ عِندَ ٱللَّهِ أَتۡقَىٰكُمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌ خَبِيرٞ ١٣ ﴾ [الحجرات: ١٣].

(Ya ku mutane hakika mun halicce ku daga namiji, da mace, kuma mun sanya ku al'ummai da kabilu don ku san juna).

Ya ku bayin Allah! Lalle akwai hikimomi a cikin aikin hajji da bai kamata su buya ga ma'abota hankali ba.

Daga ciki akwai cewa, shi aikin hajji gagarumin taro ne na musulunci da yake kira zuwa hadin kan al'umma da hunkulewarta. Alhazai sukan taru a guri daya, a fili daya, suna bautar Allah, bayan sun hadu gabanin haka a sallah daya, sun yi azumin wata daya, suna yin sahu suna daura da juna. Duk wadannan abubuwa ne da suke nuna haduwar kan al'umma, kuma cewa ita wannan al'umma ba za ta rabauta ba sai da haduwa da curewa. Sannan kuma tsawatarwa ce a kan jayayya da rarrabuwa, kuma cewa musulmi ba a rinjayesu ba sai saboda rarrabuwarsu da daidaituwarsu, kuma makiya suna samin nasara yayin da musulmi suka kasa magana da kalma daya, suka yi garuruwansu a yaga, kowa ya yanki kasarsa mai zaman kanta. Allah ta'ala ya ce,

﴿ وَأَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَلَا تَنَٰزَعُواْ فَتَفۡشَلُواْ وَتَذۡهَبَ رِيحُكُمۡ ﴾[الأنفال: ٤٦].

(Kuma kada ku yi jayayya sai ku yi asara, kuma karfinku ya tafi).

Daga cikin hikimomin aikin hajji akwai jaddada imani da gyara zuciya.

Cututtukan fitinu da sha'awoyi kan bijirowa mutane, shi ko hajji yana tumbatsa da alamomi na tauhidi, dake goge kurakuri, ya cika kyawawan ayyuka. Ya zo a cikin hadisi cewa, (wanda ya yi hajji, sannan bai yi batsa ba, bai yi fasiƙanci ba, zai komo daga zunubansa kamar ranar da mahafiyarsa ta haife shi). Bukhari da Muslimu ne suka rawaito.

Yana daga cikin hikimomin hajji cewa, shi jajircewa ne a lokacin ƙasƙanci, kuma tsayawa ne kyam a lokacin rauni. Domin an kewaye wannan al'ummar ta ko ina, ana tuhumarta a cikin addininta, su kuwa mabiyansa kan ɗauki wannan da rauni da karɓar kaye. To a wannan hali ne alhazai ke zuwa da wannan taro don su raya ma'anonin dagewa da sadaukantaka. Musulmi suna ɗaukaka bayan rauninsu, su yi ƙarfi bayan kayan da aka yi musu, su haɗa kai bayan rarrabuwarsu. Allah ya ce,

﴿ وَٱعۡتَصِمُواْ بِحَبۡلِ ٱللَّهِ جَمِيعٗا وَلَا تَفَرَّقُواْ ﴾[آل عمران: ١٠٣].

(Kuma ku yi riƙo da igiyar Allah kada ku rarraba).

Yana daga cikin hikimomin hajji cewa, shi saƙone zuwa duniyar kafirai cewa wannan al'ummar ba za ta taɓa saurarawa ba game da addininta, ba za ta yi ciniki a bisa akidunta ba. Mai ƙarfice tare da Ubangijinta, mai buwayiya ce da addininta. Kafirai sau dadama sukan firginta su tsorata saboda ganin irin wannan dandazo na jama'a. Sau tari mai niyar cin zarafin wannan al'umma yakan yi shiru ya fasa ganin irin wannan haɗuwa ta musulmi. Lallai al'ummar mu tana shelanta riƙonta da addininta da ƙanƙamewarta ga Alƙur'aninta ta hanyar wannan aikin hajjin. Wannan addini shi ne rayuwarta, kuma alamar wanzuwarta, maɓuɓɓugar girmanta da bayyanarta. Allah yana cewa,

﴿ لَقَدۡ أَنزَلۡنَآ إِلَيۡكُمۡ كِتَٰبٗا فِيهِ ذِكۡرُكُمۡۖ أَفَلَا تَعۡقِلُونَ ١٠ ﴾ [الأنبياء: ١٠].

(Haƙiƙa mun saukar muku da wani littafi wanda ɗaukakar ku ke ciki yanzu ba kwa hankalta ba).

Su ma'abota imani duk da abin da ke shigarsu na rauni da ƙasƙanci sai dai suna riƙo da addininsu, kuma suna da abin da zai farkar da su ya raya zukatansa cikin ibadunsu. Kamar hajji da abin da ke cikinsa na yawan talbiya da yankan hadaya da layya, da tauhidi da sakankancewa, da addu'a, da tsoron Allah da ƙanƙan da kai.

Ina faɗan abin da kuke ji, kuma ina neman gafarar Allah ga kaina da ku, ku nemi gafararsa daga kowane zunubi, lallai shi mai gafara ne mai jin ƙai.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, kyakkyawan ƙarshe yana ga masu tsoron Allah, kuma babu sakamakon wuce gona da iri sai a kan azzalumai. Ina shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, shi kaɗai, ba shi da abokan taraiya, majiɓincin salihai, kuma ina shaidawa cewa Annabi Muhammadu bawansa ne kuma manzonsa ne, kuma cikamakin Annabawa.

Bayan haka, Ya ku mutane! Lallai yana daga cikin hikimomin aikin Hajji cewa shi, tunatarwa ne zuwa ga lahira da faɗakarwa zuwa wannan ranar mai tsanani. Allah yana cewa,

﴿ رَبَّنَآ إِنَّكَ جَامِعُ ٱلنَّاسِ لِيَوۡمٖ لَّا رَيۡبَ فِيهِۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُخۡلِفُ ٱلۡمِيعَادَ ٩ ﴾ [آل عمران: ٩]

(Ubangijinmu lalai kai mai tattara mutane ne ga yinin da babu kokonto a cikinsa, lalle Allah ba ya saɓa alkawari).

Ranar Arfa ƙaramin hoto ne filin tashi ranar Alƙiyama. A cikinsa akwai tunatarwa ga taruwar mutane a gaba ga Ubangijinsu, da ƙasƙantar da kansu gare shi, alhali wahala da gajiya ta sa me su.

Yana daga cikin hikimomin hajji cewa, aikin hajji wata alama ce ta zahiri kuma ta musamman dake nuna riƙo da addini da ibada. Babu wata al'umma daga al'ummomi da aka bawa irinta, wannan kuwa yana nuna darajar wannan al'ummar, da kuma cewa, ita ce al'umma madauwamiya, domin duk abin da zai same ta na masifofa ba zai kawar da ita ba matuƙar ta fuskanci Ubangijinta, ta nufi ɗakinsa da alfarmarsa. To don menene za mu ɗebe ƙauna alhalin ga hajji kuwa yana jaddada haɗinkai da mahabba tsakaninmu? Don me muke baƙin ciki ga hajji kuwa yana ɗaure dangantaka, yana ƙara mana dunƙulewa da soyaiya.

Ya ku Musulmi, lallai wanda duk zai nufi wannan ɗaki zai ji ƙarin alfahari da jin girma, kuma imanisa kan haskak a yayin da zai ga wannan ɗaki, da zai ga turmutsetseniyar mutane a wajansa, yana ganin irin kwaɗayinsu ga bin koyarwar Annabi, alhali sun zo daga gurare masu nisa. Wanda zai lura da wannan hajji, zai riski kasancewar wannan al'umma mafificiyar al'umma ce, kuma za ta iya kamuwa da cuta, amma ba za ta mutu ba, tana iya yin rauni amma ba za ta ɓalɓalce ba. Tana dai buƙatar wanda zai farkar da ita, ya shiryar da ita, ya nuna mata abin da zai amfane ta, ya gyara mata halinta.

Yana daga cikin hikimomin hajji, cewa shi taro ne da sunan musulunci, Allah ya tattara su a kan addininsa, ya tattaro su a kan shari'arsa, ba kishin ƙabila ko launi ko jinsi ne ya tara su ba. Wannnan addinin ne ya tattara su, imani ne ya haɗa kansu. A cikin wannan akwai ƙarfafa cewa wannan al'umma ba abin da zai iya haɗa kanta sai musulunci, ba mai tattara ɗaiɗaicewar ta sai imani, domin shi ne addinin haɗinkai, da taimakekeniya da rungumar juna.

Haƙiƙa a cikin ayoyin hajji Allah yana tuna wa musulmi cewa, wannan addini abu ne da ba makawa sai sun riƙe shi, kuma yana tuna musu cewa, duk wata al'umma da take watsi da lalmarin addinin, ta take wofintar da shari'ar Ubangijinsa, ko ta riƙe shi tana jin kunya, ko tana ganin addini ne da ya riƙe mata wuya, to fa ta yi watsi ne da mafi girman ƙarfinta, da tushen ɗaukakarta, da sakin hanyar samun babban rabo a duniya da lahira. Kuma kowace al'umma da ta rasa addininta a cikin zamantakewarta, ko ta rungumi tutar ci-baya, to za ta kasance cikin ruɗani ba makawa, za ta yi ta bankaura, Allah ya musanya ɗaukakarta da ƙasƙanci, ya musanya kwanciyar hankalinta da tsoro, idan ta juya baya sai Allah ya canza ta da wasu mutanen da ban, sannan ba za su zamo kwantankwacinsu ba.

Al’ummar da ba ta jin ɓuƙatuwarta zuwa lazimtar addini, wannan al’umamce da ba ta da imani, sannan ta yi nisa daga rahamar mai rahama; domin Annabi yana cewa: (Abu uku duk wanda ya same su to ya sami zaƙin imani; wanda Allah da Manzonsa suka zamo mafi soyuwa gare shi daga waninsu. Kuma ya so mutum, ba don komai ba sai don Allah. Kuma ya ƙyamaci komawa kafirci bayan Allah ya tserar da shi daga gare shi kamar yadda yake ƙyamar a jefa shi cikin wuta). Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi. Lallai babu mafi ƙasƙanci gurin Allah daga al’ummar da yin addini bai shiga lokon zuciyarta ba, ba ratsa jininta da tsokarta ba, sannan za ta yi ta raguwa ne tana wulaƙanta, ta faɗa rauni bayan ƙarfi. Haƙiƙa ba kowa ne yake samun shiriyar Allah ba, sai dai ita wata baiwa ce daga Allah ta rahamarsa. Ya wajaba ga wanda aka ba shi ita ya riƙe ta gam-gam. Kuma kada burace-buracen zukata da farfagandar maƙiya su sami hanyar raunana shika-shikan addinin a cikin zukata, ko muryoyin masu kira da ajuyawa addini baya da sunan ‘yanci da kawo gyara, su sami tasiri. Haƙiƙa ƙira ta haƙiƙa itace ƙirar Allah),

﴿ صِبۡغَةَ ٱللَّهِۖ وَمَنۡ أَحۡسَنُ مِنَ ٱللَّهِ صِبۡغَةٗۖ وَنَحۡنُ لَهُۥ عَٰبِدُونَ ١٣٨ ﴾ [البقرة: ١٣٨].

(Wanene ya fi Allah iya ƙira, kyautata ƙirara, kuma mu masu bauta ne gare shi). Allah yana cewa,

﴿ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَا نُكَلِّفُ نَفۡسًا إِلَّا وُسۡعَهَآ أُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلۡجَنَّةِۖ هُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ ٤٢ وَنَزَعۡنَا مَا فِي صُدُورِهِم مِّنۡ غِلّٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهِمُ ٱلۡأَنۡهَٰرُۖ وَقَالُواْ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ ٱلَّذِي هَدَىٰنَا لِهَٰذَا وَمَا كُنَّا لِنَهۡتَدِيَ لَوۡلَآ أَنۡ هَدَىٰنَا ٱللَّهُۖ لَقَدۡ جَآءَتۡ رُسُلُ رَبِّنَا بِٱلۡحَقِّۖ وَنُودُوٓاْ أَن تِلۡكُمُ ٱلۡجَنَّةُ أُورِثۡتُمُوهَا بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ٤٣ ﴾ [الأعراف: ٤٢ – ٤٣].

(Kuma waɗanda suka yi imani suka ba da gaskiya ba ma ɗora wa rai sai abin da za ta iya, waɗannan su ne ma’abota aljanna. Su masu dauwamane a cikinta, kuma muka cire musu abin da yake zukatansu na ƙullata, suka ce, godiya ta tabbata ga Allah wanda ya shiryar da mu ga wannan, kuma mu ba mu kasance za mu shiriya ba ba don Allah ya shiryar da mu ba. Haƙiƙa manzannin Ubangijinmu sun zo da gaskiya. Kuma aka kiraye su da cewa, waccan aljanna an gadar muku da ita ne saboda abin da kuka kasance kuna aikatawa).

TASIRIN LAIFUKA A RAYUWAR ƊAN ADAM

Manufofin huɗubar

- Bayanin haɗarin da ke tattare da soƃon Allah.
- Jan-kunne game da saƃon Allah.
- Dasa tsoron Allah a zukata.
- Kwaɗaitarwa a kan tuba.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ƃatar da shi, wanda kuma ya ƃatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammadu bawansa ne manzonsa ne. (Yaku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron Allah yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Yaku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammadu (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (a addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ƃata ce, duka wani ƃata kuma yana wuta".

Bayan haka:

Ya ku bayin Allah! Ku sani, laifuka da ɗan Amda yake yi, da saƃon Allah, dare da rana, suna rugurguza rayuwar ɗan Adam, saboda tsayuwar rayuwa da ingancinta, ya dogara ne kacokam a kan biyayya ga Allah da daidaito a kan al'amarinsa, da kuma lazimtar shari'arsa. Duk wanda ya karkace wa addinin Allah, duk wanda ya bi Shaiɗan, to yana bin abin da ba shi da tabbas ne, yana bin abin da zai jawo masa takaici, musamman yayin da zai haɗu da Ubangijinsa. Allah yana cewa,

﴿ فَبِمَا نَقْضِهِم مِّيثَٰقَهُمْ لَعَنَّٰهُمْ وَجَعَلْنَا قُلُوبَهُمْ قَٰسِيَةً ۖ يُحَرِّفُونَ ٱلْكَلِمَ عَن مَّوَاضِعِهِۦ وَنَسُوا۟ حَظًّا مِّمَّا ذُكِّرُوا۟ بِهِۦ ۚ وَلَا تَزَالُ تَطَّلِعُ عَلَىٰ خَآئِنَةٍ مِّنْهُمْ إِلَّا قَلِيلًا مِّنْهُمْ ۖ فَٱعْفُ عَنْهُمْ وَٱصْفَحْ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿١٣﴾ ﴾ [المائدة: ١٣].

(Saboda warware alƙawarinsu da suka yi, sai muka tsine musu, muka sanya zukatansu suke ƙeƙashe, suna sauya kalmomi daga gurabensu, kuma sun manta wani rabo daga cikin abin da aka yi musu wa'azi da shi. Ba za ka gushe ba kana tsinkaye a kan wani ha'inci daga gare su, sai kaɗan daga cikinsu. Ka yafe musu, ka kuma kawar da kai, Allah yana son masu kyautatawa).

Kuma Allah ya ce,

﴿ كَلَّا بَلْ رَانَ عَلَىٰ قُلُوبِهِم مَّا كَانُوا يَكْسِبُونَ ﴿١٤﴾ ﴾ [المطففين: ١٤].

"Bari dai, abin da suka kasance suna aikatawa, ya yi tsatsa a cikin zuciyarsu."

Kuma Allah yana cewa,

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ إِن تَتَّقُوا۟ ٱللَّهَ يَجْعَل لَّكُمْ فُرْقَانًا وَيُكَفِّرْ عَنكُمْ سَيِّـَٔاتِكُمْ وَيَغْفِرْ لَكُمْ ۗ وَٱللَّهُ ذُو ٱلْفَضْلِ ٱلْعَظِيمِ ﴿٢٩﴾ ﴾ [الأنفال: ٢٩]

(Ya ku waɗanda suka yi imani, idan kuka ji tsoron Allah, zai sanya muku mararraba, kuma ya kankare muku daga zunubanku, kuma ya gafarta muku. Lalle Allah ma'abocin falala ne mai girma).

Lallai saɓon Allah yana gadar wa ɗan Adam ƙunci da rashin jin daɗin rayuwa, kamar yadda Allah yake cewa,

﴿ وَمَنْ أَعْرَضَ عَن ذِكْرِى فَإِنَّ لَهُۥ مَعِيشَةً ضَنكًا وَنَحْشُرُهُۥ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ أَعْمَىٰ ﴿١٢٤﴾ قَالَ رَبِّ لِمَ حَشَرْتَنِىٓ أَعْمَىٰ وَقَدْ كُنتُ بَصِيرًا ﴿١٢٥﴾ قَالَ كَذَٰلِكَ أَتَتْكَ ءَايَٰتُنَا فَنَسِيتَهَا ۖ وَكَذَٰلِكَ ٱلْيَوْمَ تُنسَىٰ ﴿١٢٦﴾ وَكَذَٰلِكَ نَجْزِى مَنْ أَسْرَفَ وَلَمْ يُؤْمِنۢ بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِۦ ۚ وَلَعَذَابُ ٱلْءَاخِرَةِ أَشَدُّ وَأَبْقَىٰٓ ﴿١٢٧﴾ ﴾ [طه: ١٢٤ – ١٢٧].

(Duk wanda ya bijirewa ambato na, to rayuwar ƙunci ta tabbata gare shi, kuma za mu tashe shi ranar alƙiyama, makaho. Sai ya ce, "Ya Ubangiji! Mai ya sa ka tashe ni makaho, alhali na kasance mai idanu" Sai ya ce, "Haka nan ne ayoyinmu suka zo maka, sai ka ƙyale su, kai ma yau haka za a ƙyale ka. Kamar haka ne muke saka wa wanda ya wuce gona da iri, bai ba da gaskiya ga ayoyin Ubangijinsa ba. Azabar lahira ta fi tsanani da wanzuwa).

Lallai 'yan uwa, mu sani, yana daga cikin illar laifuka mafi haɗari, kewa da suke sawa tsakanin bawa da Ubangijinsa. Sai ka ga, ɗa'a da biyayyar Allah suna yi masa nauyi, amma kuma yana jin daɗin saɓon Allah, kuma ya saba da saɓon Allah, saɓo ba ya yi masa wahala. Wannan wace irin makanta ce? Allah ya kiyashe mu!

Ya ku 'yan uwa musulmi! Ku sani, rayuwa ingantacciya, ita ce rayuwar da ake yi wa Allah biyayya a cikinta, rayuwar da za ta mayar da mutum bawa ga Allah shi kaɗai, ta kuma mayar da shi ɗa 'yantacce ga duk wani abu da ba Allah ba. Huzaifa ya ce, na ji Manzon Allah (ﷺ) yana cewa, "Za a bijiro da fitinu a kan zukata, kamar tabarma. Duk zuciyar da fitina ta ratsa cikinta, sai a yi ɗigo baƙi a cikinta, duk zuciyar da ta yi inkarin sa, sai a yi ɗigo fari a cikinta, har sai sun koma zuciya iri biyu: Ɗaya fari fat, kamar wani falalen dutse, fitina ba za ta cutar da ita ba har abada. Ɗayar kuwa ta zamo baƙa ƙirin, ba ta san ma'arufi ba, ba ta inkarin munkari ba, sai abin da son zuciya ya gaya mata."

An karɓo daga Abdullahi bn Umar ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Ya ku gungun muhajirai! Abubuwa guda biyar, idan aka jarrabe ku da su, suka sauka a cikinku, ina neman tsari da Allah, ku riske su: Alfasha ba ta taɓa bayyana a

cikin wasu mutane ba, suna aikata ta, face sai annoba ta bayyana a cikinsu, da cututtuka irin waɗanda magabatansu ba su san su ba; kuma mutane ba su taɓa tauye mudu da sikeli ba, face sai an jarrabe su da fari, da tsananin rayuwa, da zaluncin shugabanni; babu mutanen da za su hana zakka, face sai an hana su ruwa daga sama, ba don saboda dabbobi ba, da ba za a yi musu ruwa ba; ba wanda za su warware alƙawarin Allah, da alƙawarin Manzonsa, face sai Allah ya ɗora abokin gabansu a kansu, su karɓe wani abu daga cikin abin da yake hannunsu; matuƙar kuma shugabanninsu ba su amfani da littafin Allah ba, sai Allah ya jefa tsanani a tsakaninsu." [Hakim ne ya rawaito shi]

Don wannan ita ce ƙa'idar Allah, kamar yadda yake cewa,

﴿ وَٱتَّقُواْ فِتۡنَةٗ لَّا تُصِيبَنَّ ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ مِنكُمۡ خَآصَّةٗۖ وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ ٢٥ ﴾

[الأنفال: ٢٥].

(Ku ji tsoron fitina, wadda ba za ta shafi waɗanda suka yi zalunci ba daga cikinku kawai. Ku sani, Allah mai tsananin uƙuba ne).

Haka ya zo a cikin hadisi, Zainab bint Jahsh ta ce, "Shin za a halaka mu, alhali akwai mutanen ƙwarai?" Sai ya ce, "Idan ɓata-gari suka yi yawa!" Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.

An karɓo daga Huzaifa ibn Yaman, ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Na rantse da wanda raina yake hannunsa, lallai ko ku yi umarni da kyakkyawa, ku yi hani kan mummuna, ko kuma lallai Allah ya kusa ya aiko muku da uƙuba daga gare shi, sannan ku yi ta roƙon sa, ba zai amsa muku ba." Tirmizi ne ya ruwaito shi.

Ya ku musulmai! Me ya nutsar da Fir'auna? Me ya halakar da adawa da samudawa da mutanen Annabi Luɗu, da Karuna da Hamana, da ma jama'a masu yawa? Abin da ya halakar da su shi ne saɓon Allah. Allah yana cewa,

﴿ وَعَادٗا وَثَمُودَاْ وَقَد تَّبَيَّنَ لَكُم مِّن مَّسَٰكِنِهِمۡۖ وَزَيَّنَ لَهُمُ ٱلشَّيۡطَٰنُ أَعۡمَٰلَهُمۡ فَصَدَّهُمۡ عَنِ ٱلسَّبِيلِ وَكَانُواْ مُسۡتَبۡصِرِينَ ٣٨ وَقَٰرُونَ وَفِرۡعَوۡنَ وَهَٰمَٰنَۖ وَلَقَدۡ جَآءَهُم مُّوسَىٰ بِٱلۡبَيِّنَٰتِ فَٱسۡتَكۡبَرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَمَا كَانُواْ سَٰبِقِينَ ٣٩ فَكُلًّا أَخَذۡنَا بِذَنۢبِهِۦۖ فَمِنۡهُم مَّنۡ أَرۡسَلۡنَا عَلَيۡهِ حَاصِبٗا وَمِنۡهُم مَّنۡ أَخَذَتۡهُ ٱلصَّيۡحَةُ وَمِنۡهُم مَّنۡ خَسَفۡنَا بِهِ ٱلۡأَرۡضَ وَمِنۡهُم مَّنۡ أَغۡرَقۡنَاۚ وَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيَظۡلِمَهُمۡ وَلَٰكِن كَانُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ يَظۡلِمُونَ ٤٠ ﴾ [العنكبوت: ٣٨ - ٤٠].

(Da adawa da samudawa, wani abu daga cikin matsugunansu ya bayyana gare ku. Shaiɗan ya ƙawata musu ayyukansu, sai ya kare su daga bin tafarkin Allah, alhali suna gani, da Karuna da Fir'auna da Hamana, haƙiƙa Annabi Musa ya zo musu da ayoyi bayyanannu, sai suka yi girman kai a doron ƙasa, kuma ba su zamo masu tsere mana ba. Kowanne mun damƙe shi saboda laifinsa: Daga cikinsu akwai waɗanda muka aika wa mahaukaciyar iska wadda take ƙunshe da tsakuwowi; daga cikinsu akwai wanda tsawa ta kama su; daga cikinsu akwai wanda muka shafe ƙasa da su; daga cikinsu akwai waɗanda muka nutsar. Bai cancanta Allah ya zalunce su ba, sai dai kansu suka kasance suna zalunta).

Dukkan godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin Talikai, mai kowa mai komai, mai iko a kan dukkan komai. Tsira da amincin Allah su tabbata ga Annabin tsira Annabin rahma Muhammad ɗan Abdullah da alyensa masu tsarki, da sahabbansa yardaddu a gurin Allah. Da duk wanda suka bi tafarkinsu na gaskiya har zuwa ranar sakamako.

Bayan haka:

Ya ku ‘yan uwa Musulmi! Duk wanda yake son tsira a duniya da lahira, to ya lazimci yin biyayya ga Allah da Manzonsa. Allah yana cewa,

﴿ وَمَن يُطِعِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ فَقَدۡ فَازَ فَوۡزًا عَظِيمًا ﴿٧١﴾ ﴾ [الأحزاب: ٧١].

(Duk wanda ya yi biyayya ga Allah da Manzonsa, haƙiƙa ya rabauta, rabauta mai girma).

Ku sani ya ‘yan uwa, yana daga cikin abin da zai tseratar da ku daga azabar Allah, umarni da kyakkyawa da hani ga mummuna, kamar yadda hadisi ya nuna a baya.

Kuma wajibi ne a kan shugabanni su tsayar da haddi a kan duk wani wanda ya keta haddi, domin da yin haka ne za su sami yardar Allah.

Kuma ku yawaita tuba zuwa ga Allah. Allah yana cewa,

﴿ وَتُوبُوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ جَمِيعًا أَيُّهَ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ لَعَلَّكُمۡ تُفۡلِحُونَ ﴿٣١﴾ ﴾ [النور: ٣١].

(Ku tuba zuwa ga Allah gabaɗayanku ya ku muminai. Lalle za ku samu rabuta).

Yana kuma cewa,

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ تُوبُوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ تَوۡبَةٗ نَّصُوحًا ﴾ [التحريم: ٨].

(ya ku waɗanda suka yi imani, ku yi tuba ta gaskiya zuwa ga Allah).

Anas ya rawaito cewa, Manzon Allah (ﷺ) yana tuba sau saba’in a yini guda. [Bukhari].

Tuba ta gaskiya it ace wadda ta cika sharuɗan da malamai suka faɗa guda huɗu. Sharuɗan su ne: Yin nadama a kan abin da ya wuce, da ƙuduri kan ba zai sake aikata laifin ba a sauran rayuwarsa, kuma ya daina saɓon, idan a lokacin yana yin sa. Idan kuwa laifin ya shafi bayi ne cikin haƙƙoƙinsu, to sai ya biya su, ko ya nemi yafiyarsu. Sharaɗi na ƙarshe, ya tuba a lokacin da lokacin tuba ne, kafin ya sharafa, ko kuwa rana ta fito daga yamma. Allah ya datar da mu!

Ya Allah kai ne mai jujjuya zukata, ka tabbatar da zuciyarmu a kan addininka. Allah ka shiryar da mu ga mafi kyan halaye, babu wanda yake shiryar wa ga ma fi kyan halaye sai kai. Kuma ka raba mu da miyagun halaye, babu mai raba mutum da miyagun halaye sai kai. Ya Allah ka taimaka mana bisa ga ambatonka, da gode maka da kyautata bauta gareka. Ya Ubangijinmu kada ka karkatar da zukatanmu bayan ka shiryar da mu, kuma ka ba mu wata rahama daga wajenka. Lalle kai mai yawan kyauta ne.

HAKKIN SHUWAGABANNI DA TALAKAWA

Manufofin huɗubar

- Bayyana cewa shari'ar musulunci cikakkiya ce a cikin tsarinta.
- Bayyana cewa shari'ar musulunci ta wajabta samun shugaba a cikin al'umma.
- Sanar da shugabanni haƙƙoƙin talakawa da suke kansu.
- Sanar da talakawa haƙƙoƙin shugabanni a kansu.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga shirrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammad bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammad (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

'Yan uwana Musulmi, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa a cikin littafinsa mai tsarki :

﴿ٱلۡيَوۡمَ أَكۡمَلۡتُ لَكُمۡ دِينَكُمۡ وَأَتۡمَمۡتُ عَلَيۡكُمۡ نِعۡمَتِي وَرَضِيتُ لَكُمُ ٱلۡإِسۡلَٰمَ دِينٗاۚ﴾ [المائدة: ٣]

Ma'ana : "A yau na cika muku addininku, kuma na cika muku ni'imata gareku, na yardar muku musulunci ya zama addini gareku". (Al-Ima'ida : 3)

Haƙiƙa addinin musulunci addini ne cikakke ta kowanne ɓangare, don haka musulmi ba sa buƙatar wani addini wanda ba shi ba, basu buƙatar wata shari'a wadda ba ita ba, saboda cikar shari'ar musulunci, ta ƙunshi dukkan abin da yake maslaha ne ga al'umma, ta bawa dukkan mutane haƙƙoƙinsu, talakawa da masu arziƙi, masu mulki da waɗanda ake mulka, namiji da mace, kai har ma da dabbobi, Allah Maɗaukakin Sarki ya ba duk wani mai haƙƙi haƙƙinsa.

To daga cikin abin da musulunci ya ba shi kulawa, al'amarin shugabanci da jagoranci, musulunci bai bar mutane su zauna kara zube ba, a'a ya yi umarni da naɗa shugaba koda a halin tafiya ne, saboda amfanin samun shugaba a cikin al'umma amfani ne bayananne baya buƙatar wani dogon bayani, don rayuwar mutane ba za ta tsayu ta gyaru ba sai idan akwai shugabanci a cikinsu, don haka Allah maɗaukakin sarki da Manzon Allah (ﷺ) suka nuna mahimmancin bin shugaba da samun shugabancin a cikin mutane, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce :

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُواْ ٱلرَّسُولَ وَأُوْلِي ٱلۡأَمۡرِ مِنكُمۡۖ ﴾ [النساء: ٥٩]

Ma'ana : "Yaku waɗanda kuka yi imani ku bi Allah, ku bi Manzon Allah, (sannan ku bi) ma'abota al'amari daga cikinku" (Al – Nisa'i 59).

Kuma Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Duk wanda ya yi min ɗa'a to ya yi wa Allah, wanda kuma ya saɓa min to ya saɓa wa Allah. Haka duk wanda ya bi shugaba to ya bi ni, wanda kuma ya saɓa wa shugaba to ya saɓa min. shugaba garkuwa ce da ake yaƙi a bayanta, ake kariya da ita, don haka idan shugaba ya yi umarni da tsoron Allah, ya yi adalci, to yana da lada, in kuwa ya aikata saɓanin haka to wannan laifi yana kansa" Bukhari ne ya rawaito.

An karɓo daga Ummu Salama, matar Annabi (ﷺ), daga Annabi (ﷺ) ya ce, : "Haƙiƙa za a naɗa muku shugabanni a bayana, waɗanda zaku ga abu mai kyau a tare da su, kuma ku ga marasa kyau, wanda ya ƙi maras kyau ɗin ya kuɓuta, haka ma wanda ya yi inkari, sai dai wanda ya yarda ya bi (to wannan mai laifi ne). Sai sahabbai suka ce "ba za mu yaƙe su ya Manzon Allah? Sai ya ce, "a'a, matuƙar dai suna yin sallah". Muslim ne ya rawaito shi.

Ya 'yan uwa : Waɗannan kaɗan kenan daga cikin dalilan da suke nuna mahimmancin samar da shugabanci a musulunci, saboda haka ma musulunci ya tsara haƙƙoƙin shugaba akan talakawansa, ya kuma tsara haƙƙin talaka a kan shugabansa.

Yana cikin haƙƙin talakawa akan shugabansu ya samar musu da kotunan da za su riƙa yanke hukunci tsakanin mutane da sasanta su, ya samar da kwamitocin da za su riƙa sasanta mutane, suna umarni da kyakkyawan aiki suna hana mummuna. Kamar yadda yake wajibi ne akan shugaba ya tsaida haddi akan duk wanda ya ƙetare iyaka, ya zalunci bayin Allah, ya taɓa rayukansu ko jininsu ko dukiyoyinsu, Manzon Allah (ﷺ) yana cewa : "Haddi ɗaya da za a yi aiki da shi a bayan ƙasa, ya fi a yi wa mutanen ƙasa ruwa na kwana arba'in". Ibnu Majah ne ya rawaito shi, Sheikh Albani ya ce Hadisi ne mai kyau.

Hakanan haƙƙi ne akan shugaba ya sadar da haƙƙoƙi ga masu su, ya samar da 'yan sanda, waɗanda za su ba da tsaro ga mutane da dukiyoyinsu, saboda rayuwa ba ta yiwu wa sai da tsaro, kamar yadda wajibi ne akan shugaba ya gina makarantu da wuraren ibada, ya samar da ƙwararrun malamai waɗanda za su koyar da al'umma addini kamar yadda Manzon Allah ya zo da shi. Ya taimaka wa masu bincike, ya taimaka a wajen buga littattafan addini da sauran irin waɗannan ayyuka.

Hakanan wajibi ne akan shugaba ya zama mai adalci tsakaninsa da talakawansa, saboda adalci shi ne tushen rayuwa, kuma da adalci ne al'amura suke daidaita duniya da lahira.

Shaikhul Islam Ibnu Taimiyya yana cewa : "Al'amurar mutane na duniya suna daidaita ne da adalcin da yake haɗe da nau'uka na zalunci fiye da yadda al'amura za su miƙe da zalunci a cikin haƙƙoƙi, ko da kuwa ba su tarayya a zunubi ba, don haka aka ce, Allah yana tsayar da daula mai adalci ko da kuwa kafira ce, ba ya kuma tsayar da daular azzaluma ko da kuwa musulma ce, hakanan ana cewa : Duniya tana dauwama da adalci da kafirci, amma bata dauwama da zalunci da musulunci. Manzon Allah (ﷺ) yana cewa : "Babu wani zunubi da ya fi sanya azaba da wuri fiye da zalunci da yanke zumunci" Azzalumi ana buge shi a duniya koda kuwa an masa gafara da rahama a lahira, saboda adalci tsari ne a cikin komai da komai, idan aka tsayar da al'amarin duniya akan adalci sai komai ya tsaya, koda kuwa ma'abocin duniyar nan ba shi da rabo a lahira, idan kuwa ba tsayar da al'amurar duniya akan adalci ba, to lamarin ba zai tsaya ba, ko da kuwa ma'abocinsa yana da imanin da zai ishe shi a lahira" (Duba : Maj'mu'ul Fatawa 28/ 146).

Haka nan shugaba ya zama ƙarfi wajen zartar da abin da yake gaskiya ne a cikin talakawansa, ya nisanci zalunci, da ƙarya da cin amana, da ha'inci, da sauran munanan halaye.

Waɗannan su ne kaɗan daga cikin haƙƙoƙin talakawa a kan shugabaninsu, don haka wajibi ne akan shugabanni su kiyaye waɗannan haƙƙoƙi, saboda al'amuran talakawansu amana ce a wuyansu, Allah zai tambaye su abin da ya basu kiwo na daga bayinsa. Ku ji tsoron Allah yaku shuwagabanni, ku kamanta, ku nemi taimakon Allah ta hanyar sallah da haƙuri, Allah yana tare da masu haƙuri, kuma kyakkyawan karshe yana ga masu tsoron Allah.

Allah Maɗaukakin Sarki ya yi mana albarka cikin abin da muka ji na Alƙur'ani da Hadisi, haƙiƙa shi mai iko ne akan komai.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah, Kyakkyawan ƙarshe yana ga masu tsoron Allah, Tsira da Aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, Manzon Allah (ﷺ) da iyalansa da Sahabbansa da waɗanda suka bi su gaba ɗayansu, har zuwa ranar sakamako. Bayan haka:

Yaku 'yan uwana musulmi : Babu ko shakka shugabanni suna da haƙƙoƙi masu girma a kanmu, wanda da samuwar su ne al'amura za su miƙe, su daidaita, komai ya tafi yadda ake so, daga cikin irin waɗannan haƙƙoƙi akwai ji da biyayya a cikin abin ba saɓon Allah da Manzonsa ba ne.

Ji da biyayya ga shuwagabanni – ya 'yan uwa – wajibi ne ko da kuwa waɗannan shuwagabannin suna zalunci da son kai, yin tawaye da fito – na – fito da su baya halatta, saboda Manzon Allah (ﷺ) ya hana. Manzon Allah (ﷺ) yana cewa : "Za a samu son kai, da wasu abubuwan da kuke ƙi". Sai sahabbai suka ce, "To me kake

umartar mu da shi ya Rasulallahi?" sai Manzon Allah ya ce, "Ku sauƙe nauyin da yake kanku, ku kuma ku roƙi Allah haƙƙinku". Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

Imam Annawawiy – Allah ya yi masa rahama – ya ce, "Wannan hadisi yana daga cikin mu'ujizar Annabta, wannan hadisi ya maimaitu da yawa, kuma abin da hadisin ya bada labari shi ma an same shi da yawa. Sannan a cikin hadisin akwai kwaɗaitarwa a kan ji da biyayya (ga shugaba) koda kuwa wanda yake kai azzalumi ne mai shirme, sai a bashi haƙƙinsa na biyayya, ba za a yi masa tawaye ba, baza a jire shi ba, za a koma a ƙasƙantar da kai ga Allah a kan ya yaye cutarsa, ya ije sharrinsa, ya gyara shi". Duba littafin (Sharhin Sahihi Muslim J 12 sh 543, Bugun Darul Khari.

An karɓo daga Abu Zarri – Allah ya yarda da shi – ya ce, Badaɗayina (wato Manzon Allah) ya yi min wasiyya in ji kuma in yi biyayya, koda wanda aka shugabantar min bawa ne mai yankakken gaɓɓai. Muslim ne ya rawaito shi.

An karɓo daga Ummul Husaini – Allah ya yarda da ita -, ta ji Manzon Allah (ﷺ) yana huɗuba a hajjin ban – kwana yana cewa : "Koda an ɗora muku bawa, yana jagorantarku da Littafin Allah to ku saurare shi kuma ku yi masa ɗa'a". Muslim ne ya rawaito.

Shaikhul Islam Ibnu Taimiyya – Allah ya ji ƙansa da rahama – yana cewa, "Wannan ya sa mashahurin mazhabar Ahlil – sunnah rashin yarda da fito – na – fito da shuwagabanni, da yaƙarsu da takobi, ko da kuwa waɗannan shuwagabannin suna da zalunci, kamar yadda hadisai ingantattu masu yawa daga Annabi (ﷺ) suka nuna, saboda ɓarna da fitinar da zata samu wajen yaƙarsu tafi wadda ake samu a dalilin zalincinsu, wanda ba bu yaƙi a cikinsa, babu fitina. Sannan ba a kawar da fitina ƙarama da babba, don haka a tarihi ba a taɓa samun waɗanda suka yi fito – na – fito da mai mulki ba face sai ya zama ɓarnar da suka haifar ta fi wadda suka kawar. Haka kuma Allah Maɗaukakin Sarki bai yi umarni a yaƙi duk wani azzalumi ba, kamar yadda bai ce a fara yaƙar duk wani wanda ƙetare iyaka ba, abin da ya ce, shi ne :

﴿ وَإِن طَآئِفَتَانِ مِنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٱقۡتَتَلُواْ فَأَصۡلِحُواْ بَيۡنَهُمَاۖ فَإِنۢ بَغَتۡ إِحۡدَىٰهُمَا عَلَى ٱلۡأُخۡرَىٰ فَقَٰتِلُواْ ٱلَّتِي تَبۡغِي حَتَّىٰ تَفِيٓءَ إِلَىٰٓ أَمۡرِ ٱللَّهِۚ فَإِن فَآءَتۡ فَأَصۡلِحُواْ بَيۡنَهُمَا بِٱلۡعَدۡلِ وَأَقۡسِطُوٓاْۖ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلۡمُقۡسِطِينَ ٩ ﴾ [الحجرات: ٩].

"Idan jama'u biyu daga cikin muminai suka yi faɗa da junansu to ku yi musu sulhu, idan ɗayansu ta ƙetare iyaka akan ɗayar, to ku yaƙi wadda ta ƙetare iyakar har sai ta koma zuwa ga umarnin Allah (na yarda da sukhu) idan ta dawo zuwa ga umarnin Allah, to ku yi musu sulhu da adalci". Anan zamu ga Allah bai yi umarni da fara yaƙar jama'ar da suka ƙetare iyaka ba har sai bayan da suka ƙi yarda da umarnin Allah, to yaya kuma Allah zai yi umarni a fara yaƙar shuwagabanni!?" (Duba : Minhajus sunnah J 3 sh 391).

Don haka – yaku 'yan uwa – abin da wasu matasa suke yi na fito – na – fito da shuwagabanni da yaƙarsu abu ne da ya ci karo da dalilai na shari'a masu yawa, waɗanda suka yi umarni da rashin yin haka, da haƙuri da kawar da kai daga abin

irin waɗannan shugabanni suke yi, matuƙar dai suna sallah.

Yana daga cikin haƙƙin shugaba a kan talakawansa su yi masa addu'a, saboda hakan yana daga cikin manya – manyan abubuwan da suke kusantar wa ga Allah, mafi girman ɗa'a gare shi, sannan yana cikin nasiha ga Allah da bayinsa. Kuma aƙida ce daga cikin aƙidun Ahlis-sunnah wal Jama'a, kamar yadda Imam Sabuni da Isma'iliy da Ɗahawiu suka faɗa. Duba (Alma'alum min wajibil alaƙa bainal Hakim Wal Mahkum Na ibnu Baz Sh 21).

Hakanan yana cikin haƙƙin shugabanni yi musu nasiha da daidaita su, wannan haƙƙi ne da yake kan wuyan malamai da masu da'awa, sannan ya dace a wajen yi wa shugabanni nasiha a lura da lokutan da suka dace, da maganganun da suka dace, a tunatar da su kyakkyawan aiki, a hana su mummunan aiki, cikin ladabi da sauƙaƙawa, da rangwantawa. A kiyaye da matsayinsu da darajarsu, hakan zai sa a karɓa a kuma samu abin da ake nema".

Ibnul Jauziy – Allah ya yi masa rahama – yana cewa : "Abin da yake halatacce ne wajen umarni da kyakkyawan aiki da hani ga mummuna ga masu mulki shi ne wa'azi da tausasa wa, amma kausasa magana kamar cewa, "Yakai azzalumi, ya wanda ba ya tsoron Allah. Idan irin wannan zai kawo fitinar da sharrinta zai kai zuwa ga wani to baya halatta, in kuwa abin ba zai shafi wani ba sai shi kansa mai wa'azin to ya hallata a wurin jumhurun malamai". Duba (Al-adabush shar'iyya 1/196).

Yana daga cikin haƙƙoƙinsu taimakonsa da basu goyon baya, saboda wajibi ne a kan musulmi su taimaka wa masu mulkinsu cikin duk abin da zai kawo ci gaba da alheri a dukkan ɓangarori na cikin gida da waje, da zartar da dokoki da hukunce – hukuncen shari'a, da umarni da aiki mai kyau da hana mummuna, abin da ya shafi kowa – da kowa da abin da ya shafi masu mulkin.

Wannan kaɗan kenan daga cikin haƙƙoƙin shugabanni a kan talakawansu, don haka ku ji tsoron Allah – 'Yaku bayin Allah – ku bi Allah da Manzonsa ba. Zaku rabauta duniya da lahira.

HUƊUBA AKAN DAIDAITO AKAN KOYARWAR ALKUR'ANI DA SUNNAH

Manufofin huƊubar

- Bayanin cewa daidaito wani abu ne da ake so a musulunci.
- Bayyana cewa Musulunci addini ne da ya dace da Ɗabiʼar Ɗan adam.
- Jan – kunne da tsoratarwa daga wuce gona da iri a addinin musulunci.
- Bayanin cutarwar da wuce gona da iri yake haifarwa ga musulunci da musulmai.

HuƊuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga shirrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaƊai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammad bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waƊanda suka yi imani ku ji tsoron yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda Ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaƊa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku wanƊanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faƊi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammad (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Yaku Jamaʼa, A yau zamu taɓa wani maudu'i mai girma, wanda dukkan alʼummar musulmi suke buƙatarsa fiye da buƙatarta ga abincinta da abin shanta, saboda mahimmancinsa a rayuwar musulmi, wannan abu shi ne daidaito akan koyarwar alƙurni da hadisi, da barin wuce gona da iri.

ku sani – ya ku bayin Allah – daidaito shi ne tsayawa a tsakiya, ba tare da an koma gefe ba, kuma ba a wuce inda ya kamata a tsaya ba. Allah MaƊaukakin Sarki yana cewa :

﴿ وَكَذَٰلِكَ جَعَلۡنَٰكُمۡ أُمَّةٗ وَسَطٗا لِّتَكُونُواْ شُهَدَآءَ عَلَى ٱلنَّاسِ وَيَكُونَ ٱلرَّسُولُ عَلَيۡكُمۡ شَهِيدٗاۗ ﴾

[البقرة: ١٤٣].

Maʼana : "Hakanan muka sanyaku tsaka – tsakin alʼumma (wato zaɓaɓɓu masu adalci) don ku zamo shaida a kan mutane, ku kuma Manzo ya zama shaida a

kanku". (Albaƙara : 143). Ya sake cewa :

﴿يَٰٓأَهۡلَ ٱلۡكِتَٰبِ لَا تَغۡلُواْ فِي دِينِكُمۡ وَلَا تَقُولُواْ عَلَى ٱللَّهِ إِلَّا ٱلۡحَقَّۚ﴾ [النساء: ١٧١]

Ma'ana : "Ya ku ma'abota littafi – Yahudu da Nasara – ka da ku wuce gona da iri a cikin addininku, kada ku faɗi komai akan Allah sai gaskiya". (Annisa'i : 171).

Manzon Allah (S.A.W) yana cewa, "Haƙiƙa wannan addini mai sauƙi ne, babu wani wanda zai tsananta a cikin wannan addini face sai addinin ya rinjaye shi, don haka ku daidaita, ku kusanto, ku yi bushara, ku nemi taimako ta hanyar sammako da yammaci, da wani yanki na dare" Bukhari ne ya rawaito.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (S.A.W) ya ce min "Je ka tsinto min tsakuwowi, sai na tsinto masa 'yan ƙananan tsakuwoyi, kamar irin waɗanda ake iya harba wa da ɗan yatsa, lokacin da Manzon Allah (S.A.W) ya ɗora su akan hannunsa, sai ya ce, "Da kamar waɗannan zaku yi jifa, ku nisanci wuce da gona da iri a addini, domin abin da ya halaka waɗanda suke gabaninku shi ne wuce da gona da iri" Ahmad ne ya rawaito shi.

Imam Ibnu Jarir – Allah ya yi masa rahama – ya ce, "Ina ganin cewa Allah Maɗaukakin Sarki ya siffata (wannan al'umma) da cewa tana kan daidaito da tsaka – tsaki, saboda daidaitonta a cikin addini, ba su wuce gona da iri ba, irin yadda Kirista suka yi wajen bauta, da abin da suka faɗa akan Annabi Isa, haka kuma wannan al'umma ba ta zama mai gazawa akan abin da aka umarce ta da shi ba, irin gazawar Yahudu waɗanda suka canza littafin Allah, suka kashe Annabawa, suka yi wa Ubangijinsu Allah ƙarya, suka kafirce masa. Amma ita wannan al'umma ma'abociyar daidaito ce, don haka Allah ya saiffata su da hakan, domin al'amarin da Allah ya fi so shi ne tsaka – tsaki (ba gazawa ba wuce gona da iri)".

Yaku 'yan uwana : Daidaiton wannan addini da tsaka – tsakinsa yana bayanna ne a dukkan sasannin wannan addini, a ɓangaren aƙida, musulunci ya zama tsaka – tsaki a cikin addinai, babu karkacewa, ko maguzanci a cikinsa, kaɗai bautar Allah ce tsantsa. Ta kaɗaita Allah a cikin ayyukansa da wajen bauta masa, da sunayensa da siffofinsa, babu kamanta Allah da wani abin halitta, babu korewa Allah siffofinsa. Babu lalata ma'anar nassi.

A ɓangaren ƙaddara ma musulunci a tsakiya yake, tsakanin waɗanda suke kore ƙaddara, da wanda yake cewa kuma bawa tilasta shi a ke yi a cikin aikinsa.

A wajen imani, nan ma musulunci tsakiya yake tsakanin waɗanda suka yi jafa'i, suka cire ayyukan ibada daga abin da ake kira imani, da waɗanda suka wuce gona da iri suka fitar da duk wanda ya yi saɓo daga da'irar imani, da waɗanda suka yi hukunci da kafircinsa. Waɗanda suke kan gaskiya ba sa kafirta mutum don ya yi zunubi, matuƙar bai halatta yin sa ba, kamar yadda wanda yake saɓo ba ya zama mai cikakken imani, mumini gwargwadon imaninsa, fasiƙi ne da manya – manyan zunubansa.

A babin Annabta da walittaka da sahabbai akwai tsaka – tsaki a cikinsu : ba wuce gona da iri, da ɗaukan (Annabawa da waliyyai da sahabbai) Alloli koma bayan Allah, babu kuma jafa'I irin jafa'in Yahudawa, waɗanda suka ƙaryata wasu Annabawan, suka kashe wasu.

Hakanan Musulmai suna tsakiya wajen imani da Annabawa, sun yi imani da dukkan Annabawa, da dukkan littattafan Allah, kuma suna son waliyyan Allah, sannan suna nema wa Sahabban Manzon Allah (S.A.W) yardar Allah gaba ɗayansu.

Ya ‘yan uwana musulmi : daidaito da tsayawa a tsakiya ba tare da wuce gona da iri ba a cikin wannan addini yana shiga ɓangaren ibada, saboda a musulunci ba a watsar da ɓangaren jiki, a kula da ɓangaren zuciya kaɗai ba, a’a ana haɗawa ne gaba ɗaya, a ba jiki haƙƙinsa, kamar yadda za a ba wa zuciya haƙƙinta. Allah yana cewa :

﴿ وَٱبۡتَغِ فِيمَآ ءَاتَىٰكَ ٱللَّهُ ٱلدَّارَ ٱلۡأٓخِرَةَۖ وَلَا تَنسَ نَصِيبَكَ مِنَ ٱلدُّنۡيَاۖ ﴾ [القصص: ٧٧].

Ma’ana : “Ka nemi gidan lahira da abin da Allah ya baka, amma kada ka manta da rabonka na duniya” (Alƙasas : 77).

Saboda tsayawa akan daidaito Manzon Allah (S.A.W) ya hana Usman Bin Maz’un ya yi wa kansa fiɗiya, ya haramta wa kansa jin daɗin duniya, ya ce masa, “Ni na fi ku tsoron Allah da kiyaye dokokinsa, amma duk da haka ina azumi ina hutawa, ina yin sallar (dare) kuma ina barci, ina auren mata, duk wanda ba ya son sunnata to ba ya tare da ni”. Bukhari da Muslim ne suka rawaito. A riwayar Muslim Manzon Allah (S.A.W) cewa ya yi : “Masu wuce gona da iri sun halaka” a wata riwayar dai ta Muslim cewa ya yi : “Wannan addini mai sauƙi ne, ku shige shi da sauƙi, kuma ku yi a hankali, babu wanda zai tsananta a wannan addini face sai addinin ya rinjaye shi”. Don haka musulunci ya nisantar da mabiyansa daga dukkan wani abun da yake tauye haƙƙin ɗan adam ne, da duk abin da yake sakaci ne wajen daidaita tsakanin rai da jiki.

Yaku Musulmi : Daga cikin ɓangarorin da daidaiton wannan addini yake fitowa fili a cikinsu shi ne, abin da ya shafi halal da haram, shari’ar musulunci ta zama tsakiya tsakanin Yahudawa waɗanda aka haramta musu da yawa daga cikin daɗaɗan abubuwa, da mutanen da suka halatta komai har da abin da aka haramta. amma musulmi sun tsaya inda Allah da Manzonsa suka tsayar da su.

A tsarin tattalin arziki, musulunci ya daidaita tsakanin ‘yancin ɗaiɗaiku da kuma al’umma, ya girmama mallakar mutum ɗaya , ya tabbatar da ita, ya tsarkaketa, ta yadda ba zata cutar da al’umma ba, sai musulunci ya zama a tsakiya, saɓanin tsarin ‘yan jari hujja, tsarin da ya damu da mutum ɗaya akan sauran al’aumma (ya ba si dama ya wawure dukiyar al’umma, ya yi duk abin ya ga dama ko da al’umma zata cutu) hakanan saɓanin tsarin ‘yan gurguzu da yake hana mutum mallakar ɗaiɗaiku, da hujjar maslahar al’umma.

A wajen ciyarwa nan ma ana samun daidaito, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce,

﴿ وَٱلَّذِينَ إِذَآ أَنفَقُواْ لَمۡ يُسۡرِفُواْ وَلَمۡ يَقۡتُرُواْ وَكَانَ بَيۡنَ ذَٰلِكَ قَوَامٗا ٦٧ ﴾ [الفرقان: ٦٧].

Ma’ana : “Waɗanda idan za su ciyar ba sa ɓarna, ba sa kuma yin ƙwafro, sun kasance a tsaka – tsakin haka”. (Alfur’ƙan : 67).

Wannan kaɗan kenan daga cikin wuraren da addinin musulunci yake a tsaka – tsaki, wanda hakan yana nuna wannan addini yana da girma, kuma addini ne na

Allah. Godiya ta tabbata ga Allah wanda ya shiryar da mu, ba don ya shiryar da mu ba da bamu shiryu ba. Ku ji tsoron Allah – Yaku bayin Allah – ku siffatu da abin da Allah ya umarce ku da shi, na daidaito da tsayawa a tsakiya, zaku rabauta.

Allah ya yi mana Albarka cikin abinda muka ji, na Alƙur 'ani da Hadisi, Shi Allah Mai iko ne akan dukkan komai.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah, Kyakyawan ƙarshe yana ga masu tsoron Allah, Tsira da Aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, Manzon Allah (S.A.W) da iyalansa da Sahabbansa da waɗanda suka bi su, har zuwa ranar sakamako gaba ɗaya. Bayan haka :

Ya 'yan uwana musulmi, Akwai wasu abubuwa da yin su yake kore daidaito a cikin addini, wajibi akan mutane su nisance su, daga cikin su :

Akwai wuce gona da iri a bidi'a, mai wuce gona da iri shi ne mai yin ƙari a kan abin da shari'a ta yi umarni da shi, kodai wajen adadi ko wajen kamar da za a yi aikin, ko kuma yawansa, kamar wanda zai yi tasbihi ɗari bayan ya gama sallah, maimakon ya yi talatin da uku, kmar yadda Annabi (S.A.W) ya umarta a yi, ko kuma wanda zai ɗora wa kansa sanya waɗansu tufafi na daban yayin da zai yi sallah ko zai shiga masallaci, da makamancin haka.

Ita ko bidi'a tana sanya mai yin ta ya yi wa Allah gyara, ya zo da sabon abu wanda Allah da Manzonsa ba su yi umarni da shi ba.

Shaikhul – Islam Ibnu Taimiyya – Allah ya yi masa rahama - ya ce, "Ya riga ya gabata cewa addinin Allah tsaka – tsaki ne, tsakanin mai wuce goda da iri da wanda yake gaza yin abin ake so. Duk abin da Allah Maɗaukakin Sarki ya umarci bayinsa da shi, sai Shaiɗan ya fito wa (masu ƙoƙarin yi) ta hanya biyu, don ya ɓatar da su, ko dai ya sanya su, su wuce gona da iri, ko kuma ya sanya su su yi sakaci da abin". (Al-wasiyyatul Kubra)

Yaku musulmi, ku sani cewa wuce gona da iri a addini yana kawo munanan al'amura, daga cikinsu, akwai halaka, kamar yadda Manzon Allah (S.A.W) ya ce : "Masu wuce gona da iri sun halaka, masu wuce gona da iri sun halaka". A wata riwayar ya ce, "Abin da ya halaka waɗanda suke gabaninku shi ne wuce gona da iri" don haka duk mai wuce gona da iri ƙarshensa shi ne halaka a nan duniya tun gabanin lahira. Halaka a nan ta haɗa halaka ta zahiri da kuma halaka ta ɓoye, zai iya halaka ya daina yin biyayya da ibada, ya gaza yin ta gaba ɗaya, zai iya kuma halaka ta hanyar karkacewarsa a aƙida, da saɓawa umarnin Allah da shiriyar Manzon Allah (S.AW).

Daga cikin munanan abubuwan da wuce gona da iri yake haifarwa akwai ta'adanci da yawan kafirta mutane ba kai ba gindi.

Daga cikin irin waɗannan abubuwa akwai ɓata surar musulunci da musulmi a idon duniya, wuce gona da iri yana ɓata hoton musulunci a yau a duniya, yana sanya mutane su guje wa addinin, kuma buɗe ƙofa ne ga sukan addinin.

Daga ciki akwai faɗawa cikin saɓo, ka duba ka ga yadda khawarijawa wuce gona da iri ya kai su zuwa ga kashe musulmi, da barin masu bautawa gumaka.

Daga cikin tasirin wuce gona da iri akwai barin ibada. Imamul Bukhari – Allah ya ji ƙansa da rahama – ya yi babi a cikin littafinsa ya ce, "Babin da yake bayanin abin da aka hana na tsanantawa wajen ibada". Al – Hafiz Ibnu Hajar – Allah ya yi masa rahama – ya fassara wannan babi da cewa "a cikin wannan babi akwai kwaɗaitarwa wajen daidaito a cikin ibada, da hana zurfafa wa a cikinta, da umarnin a fukanci ibada cikin nishaɗi". (Duba Fathul – Bari J 3 sh 36).

Ku ji tsoron Allah – yaku bayin Allah – ku tsaya kan abin Allah da Manzonsa (S.A.W) suka umarta, kada ku wuce gona da iri a cikin ayyukanku, wuce gona da iri sharri ne, kada kuma ku yi sakaci, a cikin sakaci ma akwai halaka, ku sani Allah ba zai daina baku lada ba, har sai kun daina bauta masa, ku ɗauki ayyukan da zaku iya, ku nemi taimakon Allah, Shi ne mafi alherin masu taimako.

WANI ƁANGARE NA NI’IMAR ALJANNA DA AZABAR WUTA

Manufofin huɗubar

- Kwaɗaitar da mutane aljanna, da tsoratarwa daga azabar wuta.
- Zaburarwa a kan kyawawan ayyuka.
- Siffofin ‘yan aljanna.
- Siffofin ‘yan wuta.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammadu bawansa ne manzonsa ne. (Yaku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron Allah yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Yaku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammadu (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (a addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta".

Bayan haka: Ya ku musulmi!

Babban jigon maganarmu ta yau shi ne, magana a kan aljanna, wacce babu mai samunta sai waɗanda Allah ya jiƙansu daga cikin bayinsa. Ita ce babbar abar nema a wajen dukkanin musulumi baki ɗaya. Haƙiƙa ita ce babbar abar bege a wajen dukkanin muminai.

Haka kuma Allah ya yi tanadin wuta, ga dukkanin kafirai da munafukai. Allah ya halicci aljanna da ni’imominta, ya kuma halicci wuta da azabarta, kuma kowacce ya yi mata tanadin mutanenta. Allah yana cewa:

﴿ وَسَارِعُوٓاْ إِلَىٰ مَغۡفِرَةٖ مِّن رَّبِّكُمۡ وَجَنَّةٍ عَرۡضُهَا ٱلسَّمَٰوَٰتُ وَٱلۡأَرۡضُ أُعِدَّتۡ لِلۡمُتَّقِينَ ١٣٣ ﴾[آل عمران: ١٣٣].

(Ku yi gaggawa zuwa neman gafara daga Ubangijinku da aljanna wacce faɗinta ya kai faɗin sama da ƙasa, kuma Allah ya yi tanadinta ne ga masu tsoronsa).

A wata ayar kuma, Allah Maɗaukakin sarki ya ƙara da cewa"

﴿ فَإِن لَّمۡ تَفۡعَلُواْ وَلَن تَفۡعَلُواْ فَٱتَّقُواْ ٱلنَّارَ ٱلَّتِي وَقُودُهَا ٱلنَّاسُ وَٱلۡحِجَارَةُۖ أُعِدَّتۡ لِلۡكَٰفِرِينَ ٢٤ ﴾ [البقرة: ٢٤].

(Idan kun kasa a baya, to a nan gaba ma ba za ku iya ba, ku tsoron shiga wuta wacce makamashinta mutane ne da duwatsu, an tanade ta don kafirai).

Ya ku jamar muminai, ku sani Aljanna ita ce makomar muminai waɗanda Allah ya yi musu ni'ima daga cikin annabawa da siddiƙai da salihan bayi, wadda ƙoramunta suke gudana. Gidajenta an yi su ne da tubali na zinare da azurfa. Turɓayarta daga Za'afaran ne, runfunanta an yi su ne daga lu'ulu'u. Ga mata nan zaɓaɓɓu masu tarin alheri. Muminan da suka sami shiga cikinta za su ci su sha, babu bayangida, babu fitsari, babu kaki, babu zubar da yawu, ko majina. Gatsarsu ƙamshin almiski take..

Kullum suna cikin farin ciki da dariya, za su kasance a haka har abada. babu mutuwa, suna masu fararen fuskoki ga kyau mai matuƙar burgewa, ga matan Hurun'ini. Suna cikin dangogin ni'ima waɗanda ba sa yankewa. Ga kuma ƙari a lokacin da Ubangiji zai ɗauke hijabi su gan Shi, Allah Yana cewa:

﴿ فَلَا تَعۡلَمُ نَفۡسٞ مَّآ أُخۡفِيَ لَهُم مِّن قُرَّةِ أَعۡيُنٖ جَزَآءَۢ بِمَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ١٧ ﴾ [السجدة: ١٧].

(Wata rai ba ta san abin da aka ɓoye musu na abin da yake faranta rai, sakamakon abin da suka kasance suna aikatawa).

An karɓo hadisi, daga Abu Huraira, daga manzon Allah (ﷺ) ya ce, Allah maɗaukakin sarki Yana cewa: "Na yi wa bayina na ƙwarai alkawarin abin da ido bai taɓa gani ba, kunne bai taɓa ji ba, zuciya ba ta taɓa saƙa shi ba", Gaskiyar wannan shi ne faɗar Allah:

﴿ فَلَا تَعۡلَمُ نَفۡسٞ مَّآ أُخۡفِيَ لَهُم مِّن قُرَّةِ أَعۡيُنٖ جَزَآءَۢ بِمَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ١٧ ﴾ [السجدة: ١٧].

(Wata rai ba ta san abin da aka ɓoye musu na abin da yake faranta rai, sakamakon abin da suka kasance suna aikatawa).

Hakanan an karɓo daga Abu Huraira, daga manzon Allah yana cewa: "Haƙiƙa farkon waɗanda za su fara shiga aljanna suna farare tas kamar farin wata a ranakun hasken shi. Sannan masu biye musu, kamar tauraruwa mafi haske a sama. Ba sa fitsari, ba sa bayangida, ba sa kaki, ba sa zubar da yawu. Matajin kansu na zinariya ne. Guminsu yana ƙamshin almiski, turarensu na wuta na lu'ulu'u ne. Matansu kuwa Hurun'inu. Halayensu kamar halayen mutum ɗaya. Tsawonsu kuwa kamar tsawon babansu Annabi Adam, zira'i sittin".

An karɓo daga Jabir ya ce: Na ji manzon Allah yana cewa: "Haƙiƙa 'yan aljanna suna ci, suna sha, ba sa zubar da yawu, ba sa fitsari, ba sa bayan-gida, ba sa kaki". Sai sahabbai suka ce: to ya matsayin abincin da suke ci? Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: " Gyatsa ce za su kawai, da kuma gumi, kuma gumi mai ƙanshin almiski. Suna tasbihi da tahmidi, kamar yadda suke numfashi. [Muslim].

An karɓo daga Abi Huraira daga manzon Allah ya ce: "Duk wanda aka shigar da shi aljanna ba zai taɓa shiga wahala ba. Tufarsa ma ba za ta taɓa tsufa ba, kuma

yana cikin ƙuruciya har abada. [Muslim].

An karɓo daga Abu Sa'idul Khudri da Abu Huraira, daga Manzon Allah ya ce, "Mai kira zai yi kira a ranar alƙiyama, ya ce, "Ya ku 'yan aljanna, haka za ku dawwama cikin ƙoshin lafiya, babu cuta har abada, kuma zaku dawwama a cikin rayuwa babu mutuwa ha abada. Za ku dawwama a cikin ƙuruciya babu tsufa har abada. Kuma za ku dawwama a cikin ni'ima babu talauci har abada". Wannan ya yi daidai da faɗin Allah maɗaukakin sarki cewa:

﴿ وَنُودُوٓاْ أَن تِلۡكُمُ ٱلۡجَنَّةُ أُورِثۡتُمُوهَا بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ﴿٤٣﴾ ﴾ [الأعراف: ٤٣].

(Kuma aka kira 'yan aljanna aka ce dasu « Wannan gidan aljanna ne, an gadar muku da ita sakamakon abin da kuka kasance kuna aikatawa).[Muslim].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Kais, daga Manzon Allah ya ce: "Haƙiƙa mumini yana da wata rumfa a gidan aljanna wacce aka yi ta daga gudan lu'ulu'u mai kwarmi. tsawonta ya kai Mil sittin. Kowane mumini an tanadar masa iyalansa. Yana ziyartarsu, kuma ba sa ganin junansu. [Muslim].

Haka nan an karɓo daga Abu Huraira ya ce: Manzon Allah ya faɗa cewa: "Saihanu da Juhainu da Furat da Nil, duksuna daga cikin ƙoramun aljanna suke." [Muslim].

Amma ita kuwa wuta, gida ne na bala'i da azaba. Ana shayar da 'yan cikinta daga tafasasshen ruwan zafi. Allah ya ce:

﴿ لَهُمۡ شَرَابٞ مِّنۡ حَمِيمٖ وَعَذَابٌ أَلِيمُۢ بِمَا كَانُواْ يَكۡفُرُونَ ﴿٤﴾ ﴾ [يونس: ٤].

(Suna wani abin sha na tafasasshen ruwa , da wata azaba mai raɗaɗi saboda abin da suka kasance suna aikatawa na kafirci).

Wuta makoma ce mai munin gaske ga duk bayi masu saɓo. Allah ta'ala ya ce:

﴿ وَإِنَّ لِلطَّٰغِينَ لَشَرَّ مَـَٔابٖ ﴿٥٥﴾ جَهَنَّمَ يَصۡلَوۡنَهَا فَبِئۡسَ ٱلۡمِهَادُ ﴿٥٦﴾ ﴾ [ص: ٥٥ – ٥٦].

(Lalle waɗanda suka wuce iyaka suna da mafi mummunar makoma. Jahannama ce da za su shege ta. To tir da wannan abin shimfiɗar).

Allah zai sanya musu wando na dalmar wuta, sannan wutar za ta lulluɓe fuskokinsu baki ɗaya. Allah yana cewa:

﴿ سَرَابِيلُهُم مِّن قَطِرَانٖ وَتَغۡشَىٰ وُجُوهَهُمُ ٱلنَّارُ ﴿٥٠﴾ ﴾ [إبراهيم: ٥٠].

(Wandunansu na dalmar wuta ne, sannan wutar za ta lulluɓe fuskokinsu).

An karɓo daga Shaƙiƙ ɗan Abdullahi, ya ce, Manzon Allah ya faɗa cewa: "Za a zo da jahannama a ranar alƙiyama, tana da linzami dubu saba'in, tare da kowane linzami akwai mala'ika dubu saba'in suna janta" [Muslim].

An karɓo daga Abu Huraira, ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Wutar da mutane suke amfani da ita ɓangare ɗaya ne daga cikin ɓangarori saba'in na zafin wutar jahannama".Sai sahabbai suka ce: "Ai ya manzon Allah ko da kamar haka take ai ta isa ta zama azaba". Sai ya ce, "To an fifita ta lahira da kaso sittin da tara sama da ta duniya kowane kaso zafinsa ya kai zafin ta duniya". [Muslim].

An karɓo daga Abu Huraira yana cewa: wani lokaci muna tare da Manzon Allah, sai ya ji wata ƙara, sai Manzon Allah ya ce, "Kun san ko ƙarar mene ne wannan? Sai muka ce, "Allah da manzonsa ne suka fi kowa sani". Sai ya ce, "Wani

dutse ne da aka jefa shi a wuta tsawon shekara saba'in sai yanzu ya iske ƙarshenta. [Muslim ne ya rawaito shi].

An karɓo daga Samurah. Ya ji Manzon Allah ﷺ yana cewa: "Daga cikin mutane akwai wanda wuta za ta kama shi har zuwa idon sawusa. Wani kuma zuwa ƙug. Wani kuma zuwa wuyansa". [Muslim ne ya rawaito shi].

Allah ka samu cikin masu rabauta da gidan aljannah. Ka haɗa da annabawa da siddiƙar, da shu'hada'u da salihan bayinka a cikita. Ka sauƙaƙe mana aikin da za kusantar da mu zuwa gareta. Ka tsare daga azabar wuta. Abin da ya sauwaƙa ku ji shi ke nan daga bakina. Ina neman gafarar Allah ga ni kaina da ku baki-ɗaya. Don haka kuma ku nemi gafarsa, donmin shi mai gafara ne mai jin-ƙai.

Huɗuba Ta Biyu

Yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah. Tsira da amincin Allah su tabbata ga annabin rahama, annabinmu Muhammadu da alayensa da sahabbansa da waɗanda suka bi tafarkinsa har zuwa tashin ƙiyama. Bayan haka:

Ya ku bayin Allah. Ubangiji mai girma da buwaya ya horewa bayin hanyoyi daban daban don samin gidan aljannah domin tsananin tausayinsa ga bayinsa.

Allah yana faɗa a cikin littafin mai tsarki cewa:

﴿إِنَّ ٱللَّهَ ٱشۡتَرَىٰ مِنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ أَنفُسَهُمۡ وَأَمۡوَٰلَهُم بِأَنَّ لَهُمُ ٱلۡجَنَّةَۚ يُقَٰتِلُونَ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ فَيَقۡتُلُونَ وَيُقۡتَلُونَۖ وَعۡدًا عَلَيۡهِ حَقّٗا فِي ٱلتَّوۡرَىٰةِ وَٱلۡإِنجِيلِ وَٱلۡقُرۡءَانِۚ وَمَنۡ أَوۡفَىٰ بِعَهۡدِهِۦ مِنَ ٱللَّهِۚ فَٱسۡتَبۡشِرُواْ بِبَيۡعِكُمُ ٱلَّذِي بَايَعۡتُم بِهِۦۚ وَذَٰلِكَ هُوَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡعَظِيمُ ١١١﴾ [التوبة: ١١١].

(Lalle Allah ya sayi rayukan muminai da farashin aljanna. Su yi yaƙi don ɗaukaka kalmar Allah, sai su kashe kuma a kashe su. Wannan alkawari ne na gaskiya da ya ɗaukarwa kansa a cikin Attaurah da Linjila da Alƙur'ani. Wanene wanda ya fi Allah cika alkawarinsa?! Don hka ku yi murna da wannan ciniki da kuka yi da Allah. Wannan kuma shi ne babban rabo

An karɓo daga Jarir ɗan Abdullahi ya ce: Mun kasance a wani lokaci a wajen Manzon Allah da daddare, wata yana tsakiyar haskensa, sai Manzon Allah ya ce: "Haƙiƙa za ku ga Ubangijinku, a fili kamar yadda kuke ganin wannan watan a wannan lokaci, ta bare da turereniya ba. Saboda haka duk kada ɗayanku ya yarda a fi ƙarfinsa akan sallar Asuba da ta Magariba". [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi].

Manzon Allah ya ce: "Duk wanda ya yi sallar nafila raka'a goma sha biyu a yini da dare, Allah zai gina masa gida a aljanna. Raka'a biyu kafin asubahi. Raka'a huɗu kafin azahar da raka'a biyu a bayanta, da raka'a biyu bayan sallar magariba da raka'a biyu bayan sallar isha'i". Muslim ne ya ruwaito shi.

A game da ƙiyamullaili, Allah yana cewa;

﴿تَتَجَافَىٰ جُنُوبُهُمۡ عَنِ ٱلۡمَضَاجِعِ يَدۡعُونَ رَبَّهُمۡ خَوۡفٗا وَطَمَعٗا وَمِمَّا رَزَقۡنَٰهُمۡ يُنفِقُونَ ١٦﴾

[السجدة: ١٦].

(Jukkunansu suna nisa da shimfiɗinsu. Suna bautawa Ubangijinsu suna masu

tsoron azabarsa, masu kwaɗayin ladansa. Kuma suna ciyarwa daga abin da muka azurta su). Shi ya sa Manzon Allah yake cewa: “Ku yaɗa sallama a tsakaninku. ku ciyar da abinci, ku sada zumunci, ku yi sallah da daddare lokacin da mutane suke barci, sai ku shiga aljanna da aminci”. [Tirmizi ne ya ruwaito].

Sannan ka lizimci ambaton Allah. Kamar yadda Annabi (ﷺ) yake cewa: (Wanda duk ya ce, Subhanallahi, wal-Hamdu lillahi, to za a dasa masa dabino a aljannah). (Tirmizi ne ya ruwaito).

Hakanan Manzon Allah yana cewa: “Na ga Annabi Ibrahim a daren da aka yi Isra’i da ni. Ya ce ya Muhammad ka isar wa da al’ummarka gaisuwata. Ka ba su labari da cewa, aljanna turɓayarta mai ƙanshi ce. Ruwanta mai daɗi ne. ƙasarta ƙeƙuwa ce. Dashenta kuwa shi ne, Subhanallahi, wal-Hamdu lillahi Walaa-ilaaha Illal-Lahu. Wal-Lahu Akbar”. [Tirmizi ne ya ruwaito].

Yana daga cikin hanyoyin samin gidan aljannah, bawa ya kyautata halayensa. Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: "Ba na ba ku labari ‘yan aljanna daga cikin mazajenku ba? Annabi yana aljanna, Siddiƙi yana aljanna, Shahidi yana aljanna, da wanda yake ziyarar ɗan’uwansa a can wani gari don Allah. Matanku 'yan aljannah su ne: Da dukkanin mace mai yawan nuna ƙauna ga mijinta, mai yawan haihuwa, wacce take ɗora hannunta a kan hannun mijinta in ta ɓata masa rai, ta riƙa cewa, "Ba zan iya barci ba idan ba ka huce ba". Nisa'i ne ya ruwaito shi.

Allah maɗaukakin sarki yana cewa:

﴿ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ أُوْلَٰٓئِكَ هُمۡ خَيۡرُ ٱلۡبَرِيَّةِ ٧ جَزَآؤُهُمۡ عِندَ رَبِّهِمۡ جَنَّٰتُ عَدۡنٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدٗاۖ رَّضِيَ ٱللَّهُ عَنۡهُمۡ وَرَضُواْ عَنۡهُۚ ذَٰلِكَ لِمَنۡ خَشِيَ رَبَّهُۥ ٨ ﴾ [البينة: ٧ - ٨].

(Haƙiƙa waɗanda suka yi imani, kuma suka yi ayyuka na gari, to waɗannan su ne mafi alkhairin halitta. Sakamakonsu a wajen Ubangijinsu aljannatai ne waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu. Suna dawwama a cikinsu har abada. Allah ya yarda da su. Suma sun yarda da shi. Wannan sakamakon ne na wanda duk ya ji tsoron Ubangijinsa).

Ya Allah ka ba mu da cewa da gidan Aljannarka ta Firdausi. Ka sanya mu cikin masu aiki tuƙuru don gina lahirarsu da sa mun yardarka, da ganin fuskarka ranar gobe ƙiyama. Allah ka nisatar da fuskokinmu daga wuta. Ka nesatar da ayyukanmu daga ayyukan ‘yan wuta. Ka sa aljannarka madawwamarmu. Amin.

HANYOYIN DA AKE BI DON KAMA ZUKATAN MASU SAURARO

Manufofin huɗubar

- Haɗa Zukata da Allah Maɗaukakin Sarki.
- Fito da wasu daga cikin hanyoyin da mai wa'azi zai kama zukatan masu sauraro da su.
- Bayanin yadda ake shiryar da mutane ta hanyar hikima da kyakkyawan wa'azi da tausasawa.
- Bayanin wasu daga cikin hanyoyin da Manzon Allah (S.A.W) yake bi wajen kira zuwa ga Allah.
- Tsoratarwa daga korar mutane daga fahimtar addini.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga shirrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammad bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammad (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Ya ku 'yan uwana musulmi masu sauraro : a yau zamu yi magana ne akan tsokar da ta fi mahimmanci a jikin ɗan adam, tsokar da idan ta gyaru dukkan jiki ya gyaru, idan kuwa ta ɓace to dukkan jiki ya ɓace.

Kasancewar zuciya tana da mahimmanci a babba a wajen gyaruwar ɗan adam, sai ta zama kamar sarki a jikin jiki, sauran gaɓoɓi talakawanta, don haka wajibi ne akan mai wa'azi da kira zuwa ga addinin Allah ya damu da sanin hanyoyin da zai isar da kiransa da saƙonsa gareka, don wa'azinsa ya isa ga mutane, su amfani da

shi. Ga wasu daga cikin waɗannan hanyoyin :

Abu na farko : Wajibi ne akan mai da'awa ya haɗa zukatan mutane da Allah, ya koya musu tsarkake Allah, da dogaro gare shi, da son shi, da fata, da tsoro duk ga Allah Maɗaukakin Sarki, saboda idan zuciya ta tsarkaka, ta koma zuwa ga Allah, to zai mata sauƙi ta kamanta umarnin Allah, ta hanu daga abin da ya hana.

Hakanan wajibi ne akan mai da'awa ya zama yana ƙara wa kansa ilimi, ya karanta Al'ƙur'ani ya hardace da abin da zai iya daga cikinsa, ya karanci Sunnah ya fahimce ta daidai gwargwado.

Kamar yadda yake kan da'awa ya zama mai sauƙi da haƙuri da mutane, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa Annabinsa :

﴿ فَبِمَا رَحۡمَةٖ مِّنَ ٱللَّهِ لِنتَ لَهُمۡۖ وَلَوۡ كُنتَ فَظًّا غَلِيظَ ٱلۡقَلۡبِ لَٱنفَضُّواْ مِنۡ حَوۡلِكَۖ فَٱعۡفُ عَنۡهُمۡ وَٱسۡتَغۡفِرۡ لَهُمۡ وَشَاوِرۡهُمۡ فِي ٱلۡأَمۡرِۖ ﴾ [آل عمران: ١٥٩]

Ma'ana : "Saboda Rahamar Allah ka tausasa musu, domin da ka zama mai tsanani da kaushin zuciya da sun watse daga wajenka, ka yi musu afuwa ka shawarce su a cikin al'amarin…". (Ali Imran : 159)

Sannan An karɓo daga A'isha – Allah ya yarda da ita – ta ce, Manzon Allah (S.A.W) ya ce, "Sauƙi da tausasawa ba sa shiga cikin komai face sai sun ƙawata wannan abun, haka nan ba a rasa tausasawa a cikin komai face sai ya yi muni" Muslim da Ahmad da Abu Dawud suka rawaito shi. Yana daga cikin sauƙaƙawa yin abubuwan da za su zo :

1. Kada ya matsanta wa mutane da tsawaita wa a wajen sallah ko huɗuba.
2. Kada ya matsanta wa mutane da yawan karatu, da tsawaita shi, da yin karatun da bai dace da buƙatunsu ba.
3. Mai wa'azi ya zama tare da mutane a koda yaushe, kada ya zama mai girman kai a garesu, kada ya nisance su, kada ya zama idan sun neme shi basa samunsa, idan suna buƙatarsa sai su rasa shi, saboda kusantarsu da ƙaunarsu shi ne zai jawo masa matsayi a zukata, da soyayya a cikin zuciya, idan ya yi magana su ji, su yi aiki da ita, idan ya nemi su yi wani abu su aikata, idan ya fuskantar da su zuwa ga wani abu, su yarda su yi abin da ya ce. Saboda haka mai wa'azi ya zama yana tare da mutane yana cikin muhimman abubuwa.

Daga cikin abin da mai da'awa yake kama zukatan mutane da shi, ya zama abin koyi a wurinsu, kada ya aikata abin da ya hana su, ya yi kuma abin da ya umarce su da shi , Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa :

﴿ أَتَأۡمُرُونَ ٱلنَّاسَ بِٱلۡبِرِّ وَتَنسَوۡنَ أَنفُسَكُمۡ وَأَنتُمۡ تَتۡلُونَ ٱلۡكِتَٰبَۚ أَفَلَا تَعۡقِلُونَ ٤٤ ﴾ [البقرة: ٤٤]

Ma'ana : "Kuna umartan mutane da alheri amma kuna manta wa da kawunanku, alhali kuna karanta littafi, ashe ba za ku zama masu hankali ba". (Baƙara : 44)

Haka kuma ana son mai wa'azi da da'awa ya zama mai kyauta da bayarwa gwargwadon ikonsa, Saboda Manzon Allah (S.A.W) ya kasance mutum ne mai yawan kyauta, ya kasance lokacin da ya fi kyauta shi ne cikin watan Ramadan, lokacin da Mala'ika Jibrilu yake haɗuwa da shi ya yi masa karatun Alƙur'ani, kamar yadda Imamul Bukhari ya rawaito

Yaku ‘yan uwa musulmi : Yana cikin babban muhimmin abin da ake kama zukata da shi, hikima wajen wa’azi da karantarwa. Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa Annabinsa :

﴿ ٱدۡعُ إِلَىٰ سَبِيلِ رَبِّكَ بِٱلۡحِكۡمَةِ وَٱلۡمَوۡعِظَةِ ٱلۡحَسَنَةِۖ وَجَٰدِلۡهُم بِٱلَّتِي هِيَ أَحۡسَنُۚ إِنَّ رَبَّكَ هُوَ أَعۡلَمُ بِمَن ضَلَّ عَن سَبِيلِهِۦ وَهُوَ أَعۡلَمُ بِٱلۡمُهۡتَدِينَ ١٢٥ ﴾ [النحل: ١٢٥].

Ma’ana : “Ka yi kira zuwa ga hanyar Ubangijinka da hikima da wa’azi mai kyau, ka yi jayayya da su ta (hanyar) da ta fi kyau, haƙiƙa Ubangijinka ya san wanda ya ɓace ga barin hanyarsa, kuma shi ne ya san shiryayyu”. (Annahal : 125)

Ibnu Kasir – Allah ya jiƙansa da rahama - ya ce : “Allah Maɗaukakin Sarki yana mai umartar Annabinsa Muhammad (S.A.W) da cewa ya kira mutane zuwa ga Allah da hikima. Ibnu Jarir ya ce, (Hikima) ita ce abin da Allah ya saukar masa na Alƙur’ani da Sunnah, wa’azi kyakkyawa kuwa shi ne abin da yake cikin (Alƙur’ani) na tsawatarwa da (faɗin) abubuwan da suka sami mutanen da (suka saɓawa Allah), ka tunatar da su don su kiyayi azabar Allah Maɗaukakin Sarki. Faɗin Allah “Ka yi jayayya da su ta (hanyar) da ta fi kyau) tana nufin wanda ya buƙaci jayayya da tattaunawa da kai a cikinsu to ka yi jayayyar da tattaunawar da shi ta fuskar da ta fi kyau, da tausasawa, da kyakkyawar magana, kamar faɗin Allah “Kada ku yi jayayya da ma’abota littafi sai ta (hanyar) da ta fi kyau, sai dai idan waɗanda suka yi zalunci ne daga cikinsu” (Anan zamu ga Allah ya umarci Annabinsa) da tausasawa, kamar yadda ya umarci Musa da Haruna – Amincin Allah ya tabbata a gare su – da tausasawa lokacin da ya aike su zuwa ga Fir’auna, Allah ya ce, “Ku faɗa masa magana mai taushi ko ya wa’azantu ko kuma ya ji tsoron Allah”. Faɗin Allah “haƙiƙa Ubangijinka ya san wanda ya ɓace ga barin hanyarsa” ma’ana ya san wanda yake ɗan wuta a cikinsu, ya san ɗan Aljannah, ya kuma rubuta hakan a wajensa, ya gama da shi, don haka ka kira su zuwa ga Allah, kada ka damu da wanda ya ɓace daga cikinsu, shiriyarsu ba a wajenka take ba, kaɗai kai mai isarwa ne, hisabi kuwa yana wajenmu “Kai ba ka shiryar da wanda ka so” “Shiriyarsu ba a kanka ta ke ba, sai dai Allah yana shiryar da wanda ya so”.

Yana cikin hikima wajen yin wa’azi ɓoye sunan wanda ya yi aikin da ba daidai ba yayin yi masa wa’azi a cikin jama’a, kamar yadda Manzon Allah (S.A.W) yake yi, yana cewa “Me yasa wasu mutane suke kaza da kaza”.

Don haka wajibi ne a kanka – mai wa’azi – ka lura da waɗannan hanyoyi masu kyau, har wa’azinka ya kai zuwa ga wanda kake kira, ya yi amfani duniya da lahira.

Allah Maɗaukakin Sarki ya yi mana albarka cikin abin da muka ji, na Alƙur’ani da Hadisi, Haƙiƙa shi Allah mai iko ne akan dukkan komai.

Godiya ta tabbata ga Allah, Kyakkyawan ƙarshe yana ga masu tsoron Allah, Tsira da Aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, Manzon Allah (S.A.W) da iyalansa da Sahabbansa da waɗanda suka bi su gaba ɗayansu, har zuwa ranar sakamako. Bayan haka:

Ya kai ɗan uwana mai da'awa : Saurara ka ji wasu daga cikin hanyoyin da Manzon Allah (S.A.W) yake bi wajen da'awarsa don ka yi koyi da shi

An karɓo daga Anas ɗan Malik – Allah ya yarda da shi – ya ce, wasu mutane guda uku sun je gidajen matan Annabi (S.A.W) suna tambayar yaya ibadan Annabi (S.A.W) take, da aka faɗa musu, kai ka ce sun ganta kaɗan, don haka sai suka ce, ina mu ina ibadar Annabi (S.A.W) alhali an gafarta masa abin da ya gabata na zunubi da abin da zai zo, saboda haka sai ɗayansu ya ce, Ni dai zan yi ta sallah da daddare har abada. Ɗayan kuma ya ce, "Ni kuma zan yi ta yin azumi ba zan huta ba" Ɗayan kuma ya ce, "Ni kuma zan nisanci mata, ba zan yi aure ba har abada". Sai Manzon Allah (S.A.W) ya je wajensu ya ce, "Ku ne kuka ce kaza da kaza, To Wallahi ni na fi ku tsoron Allah, na fi ku kiyaye dokokinsa, amma duk da haka ina azumi kuma ina hutawa, ina yin sallar (dare) kuma ina yin barci, ina kuma tarawa da mata, duk wanda ba ya son sunnata to ba ya tare da ni".(Bukhari)

Misali na biyu : An karɓo daga Aisha – Allah ya yarda da ita – ta ce, Manzon Allah (S.A.W) ya yi wani abu, ya kuma ya yi rangwame a kan yin sa, amma sai wasu mutane suka ƙyamaci wannan abun, sai labari ya zo wa Annabi (S.A.W) sai ya yi huɗuba ya godewa Allah ya ce, "Me ya samu wasu mutane suke ƙyamatar abin da na yi!?, to na rantse da Allah ni na fi su sanin Allah, na fi su tsananin tsoronsa". Bukhari ya rawaito shi.

Na Uku :An karɓo daga Anas ɗan Malik – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (S.A.W) ya ce, "Me yasa mu waɗansu mutane suke ɗaga idanuwansu sama a cikin sallarsu!?" Sai Manzon Allah (S.A.W) ya tsananta ya ce, "Ko dai su hanu daga hakan, ko kuma a fizge ganin nasu". Abu Dawud ne ya rawaito.

Na huɗu : An karɓo daga Mu'awiyya ɗan Hakam Assulamiy – Allah ya yarda da shi – ya ce, Ina cikin sallah tare da Manzon Allah (S.A.W) sai wani mutum ya yi atishawa, sai na ce masa "Yarhamukal Lahu" nan da nan sai mutane suka zare min idanuwa suna kallona, sai na ce, "Wayyo Kaicona!, meye ya same ku, kuke kallona" sai mutanen suka riƙa dukan cinyoyinsu, da dai na ga suna nuna min in yi shiru, sai na yi shiru. Lokacin da Manzon Allah (S.A.W) ya gama sallah – kai! na fanshe shi da babana da babata – ban taɓa ganin malami da ya iya koyarwa kamarsa ba, Wallahi bai yi min tsawa ba, ko ya doke ni, ko ya zage ni, kaɗai ya ce min "Wannan sallah ba dace a yi maganganu da mutane a cikinta ba, ita dai sallah tasbihi ce, da kabbara da karatun Alƙur'ani". Muslim da Ahmad da Abu Dawud suka rawaito shi.

Misali na biyar : shi ne hadisin da Anas ɗan Malik ya rawaito ya ce, Wani mutumin ƙauye ya yi fitsari a wani wuri a cikin masallaci, sai mutane suka yi masa tsawa, amma sai Manzon Allah (S.A.W) ya hana su. Da ya gama fitsarinsa, sai Manzon Allah (S.A.W) ya yi umarni da guga cike da ruwa aka zuba a kai" Bukhari

ne ya rawaito.

Waɗannan kaɗan kenan daga cikin hanyoyin da Manzon Allah (S.A.W) yake bi wajen wa'azi da kiran mutane zuwa addinin Allah. Idan muka lura zamu ga a cikin waɗancan hadisai irin yadda Manzon Allah (S.A.W) yake tausayawa mai kuskure, yake kuma fahimtar da shi, ba tare da tozartawa, ko zagi ko cin mutunci ba.

Yaku 'yan uwa masu da'awa : Ku sani cewa akwai wasu kura – kurai da masu wa'azi da da'awa suke faɗa wa cikinsu, waɗanda suke sa mutane suna guje wa addini da gaskiya, ga wasu daga cikin irin waɗannan kura – kurai don mu nisance su :

Daga cikinsu : akwai tsananta wa mutane da kausasa musu, mu duba mu ga yadda Manzon Allah (S.A.W) yake cewa wakilansa yayin da ya aika su zuwa kiran mutane, yakan ce musu, "Ku yi bushara, ku sauwaƙa, ku koyar, kada ku kori mutane" Muslim ne ya rawaito.

Daga cikin irin waɗannan kura – kuran akwai fatawa ba da ilimi ba, wanda wannan babbar musiba ce a addini. An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi – Allah ya yarda da shi – ya ce, mun fita wata tafiya, sai dutse ya sami wani mutum daga cikinmu ya ji masa ciwo a ka, sai kuma ya yi mafarki (janaba ta same shi), ya tambayi abokan tafiyarsa, shin akwai wani rangwame na yin taimama (ma'ana ba sai na yi wanka ba, saboda ciwon da yake kaina), sai suka ce, "babu wani sauƙi tun da dai zaka iya amfani da ruwa", sai ya je ya yi wanka, ya mutu. Jabir ya ce, da muka dawo wajen Annabi (S.A.W)aka ba shi labarin abin da ya faru, sai Manzon Allah (S.A.W) ya ce, "Sun kashe shi, Allah ya kashe su, ba za su tambaya yayin da ba su sani ba, ku sani maganin jahilci tambaya, kaɗai ya ishe shi ya yi taimama, ya ɗaure ciwonsa, ya yi shafa a kan sauran jikinsa" Abu Dawud da Ibnu Majah suka rawaito shi.

Ku duba yaku 'yan uwana irin yadda fatawa ba da ilimi ba ta jawo kisan rai, Allah Maɗaukakin Sarki ya kare mu.

A ƙarshe ku sani yaku 'yan uwana masu wa'azi, cewa wajibi ne ku kama zukatan mutane da hanyar kyakkyawan wa'azi, da shiryarwa tare da hikima, ku bi hanyar Manzon Allah (S.A.W) da Sahabbansa da waɗanda suka bi yo bayansu, ku yi koyi da su iya iyawarku, ku nisanci korar mutane daga wannan addini mai girma, ko yaushe ku riƙa tuna faɗin Manzon Allah (S.A.W) cewa "Allah ya shiryi mutum ɗaya ta hanyarka, ya fi maka jajayen raƙuma". Allah yana tare da ku, ba kuma sai tozarta ayyukanku ba.

FALALAR GOMAN FARKO NA ZUL HIJJAH

Manufofin huɗubar

- Bayanin cewa Allah yana halittar abin da ya so kuma yana zaɓa
- Tunatar da mutane da lokuta na alheri, da cin moriyarsu cikin aiyuka na kwarai
- Bayanin falalar waɗannan kwanaki goma
- Bayanin yalwar rahamar Allah, da falalarsa a kan bayinsa

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma mua neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan aiyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar dashi, wanda kuma ya atar babu mai shiryar da shi, kuma ina shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai allah, shi kaɗai ne bashi da abokin taraiya, kuma ina shaidawa cewa Annabi Muhammad bawansane manzonsane, (Yaku waɗanda kuka bada gaskiya kuji tsoron Allah yadda ya cancanta aji tsoronsa, kada ku mutu face kuna Musulmi). (Yaku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicce ku daga rai guda ɗaya kuma ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga gare su (su biyu) kuji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya dashi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku waɗanda suka yi imani kuji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku aiyukanku, kuma ya gafarta muku zunubanku. Wanda ya bi Allah da manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawun shiriya shiriyar Annabi Muhammadu (ﷺ) kuma mafi sharrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Bayan haka: Ya ku musulmi, ku ji tsoron Allah wanda yake halittar abin da ya so kuma yake zaɓi, ya halicci sammai kuma ya zaɓi ta bakwai daga ciki. Ya halicci aljannatai ya zaɓi firdausi daga cikinsu. Ya halicci mala'iku kuma ya zaɓi mala'ika Jibrilu da Mika'ilu da Israfilu daga cikinsu. Ya halicci mutane ya zaɓi muminai daga cikinsu. Ya zaɓi Annabawa aga cikin muminai. Ya zaɓi Manzanni daga cikin Annabawa. Ya zabi Ulul azmi daga cikin Manzanni. Ya zaɓi badaɗai biyu daga cikin ulul azmi. Ya zaɓi Annabi Muhammadu (ﷺ) daga cikin bada ɗai guda biyu. Ya halicci garuruwa, ya zaɓi Makka daga cikinsu. Ya halicci kwanaki ya zaɓi watan Ramadan daga cikin watanninsu. Daga kwanakinsu kuma ya zaɓi yinin juma'a. Daga sa'o'insu kuma ya zaɓi wata wata sa'a a ranar juma'a. Daga gomin kwanakinsu ya zaɓi goman farko na watan zul-Hijjah.

Yaku bayin Allah! Haƙiƙa kwanaki goma na zul Hijjah, suna da cikin kwanaki masu matuƙar albarka, saboda suna da matsayi mai girma a wajan Allah ta'ala da suke nuna ƙaunarsa gare su, da girmamawarsa gare su. Su goma ne masu albarka, masu ƙarancin munanan ayyuka, masu maɗaukakan darajoji, masu mabanbantan

ayyukan biyayya.

Waɗannan kwanaki goma suna falala mai yawa, kaɗan daga ciki, su ne:

1. Allah ta'ala ya rantse da su sai ya ce,

﴿ وَلَيَالٍ عَشۡرٖ ۝٢ ﴾ [الفجر: ٢].

(Kuma ina rantsuwa da darare goma).

kuma Allah ta'ala ba ya rantsuwa sai da abu mai girma.

2. Sannan kuma Allah ta'ala ya gwamata da mafificin lokuta. Allah ya haɗa su da alfijir, da adadi cika, da mara, da dare wajen rantsuwa.
3. A cikinsu Allah ta'ala ya cika addini, da cikar wannan addini ne Musulmi sukan samu kamala suma, kuma ladansu ya cika, su rayu cikakiyar rayuwa wadda za su samu kariya acikinta daga munanan aiyuka, kuma su ji daɗin ayyukan biyayya. Da kuma cikar addini ne sunna ke yin nasara, a rinjayi bidi'a. Imani ya yi ƙarfi, munafunci ya mutu. Da cikar addini ne mutum ke cin nasara a kan zuciyarsa mai yawan umarni da mummunan aiki, don ta zama rai mai nutsuwa, tana bautawa Allah kamar yadda ya yi umarni, tana ko yi da Annabawa, tana abokantakar mutane na-gari, tana ɗabi'antuwa da kyawawan halaye. Da cikar addini ne mutum kanci nasara a kan shiɗaninsa wanda yake kautar da shi daga tafarki madaidaici. Ya ci nasara a kan san zuciya da sha'awoyi. Haƙiƙa addini ya cika. Kuma Manzo (ﷺ) ya bar mu a kan farin tafarki, daransa kamar ranarsa ne, babu mai karkacewa daga kansa sai halakakke taɓaɓɓe. Haƙiƙa yahudawa sun mana hassada a bisa wannan kamala. Wani malami daga malaman yahudawa ya cewa Umar (R.A), wata aya ɗaya a cikin littafinku, da mu a ka saukarwa ita, da mun riƙi ranar a matsayin idi: Ayar tana cewa, (A yau na cika muku addiniku, kuma na cika mukku ni'imata, kuma na yardar muku musulunci a matsayin addini), Umar ya ce: "Ni na san yaushe ta sauka, da inda ta sauka, ta sauka ranar arfa, ranar juma". Bukhari ne ya ruwaito shi. Cikar addini na nuna cikar al'umma da kasancewarta mafificyar al'umma.
4. Kuma yana daga fallarsu cewa, Allah ya cika ni'imarsa. Kuma yana daga falalarsu cewa, Zukata za su sami ni'ima kala-kala, ta hanyar ayyuka na ƙwarai, na magana da na aikin gaɓɓai. Kuma yana daga cikar ni'imar cewa, Allah ya buɗe zukatan bayi ga musulunci, mutane suka riƙa shiga addinin Allah jama'u-jama'u, sai ga shi sun haura dubu ɗari. Kuma yana daga cikar ni'imar cewa, Allah ya rinjayar da musulunci a kan sauran addinai, a lokacin da ake da dangogin addinai a tsibirin larabawa, daga ciki akwai yahudanci da nasaranci, da bautar wuta, da bautar gumaka da munafinci, sai duk musulunci ya rinjayesu, Allah ta'ala ya ce:

﴿ هُوَ ٱلَّذِيٓ أَرۡسَلَ رَسُولَهُۥ بِٱلۡهُدَىٰ وَدِينِ ٱلۡحَقِّ لِيُظۡهِرَهُۥ عَلَى ٱلدِّينِ كُلِّهِۦۚ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ شَهِيدٗا ۝٢٨ ﴾ [الفتح: ٢٨].

(Shi ne wanda ya aiko manzonsa da shiriya da addinin gaskiya, don ya rinjayar da shi a kan dukkanin addinai, kuma Allah ya isa mai shaida).

Kuma yana daga cikar ni'ima, hana kafirai shiga harami, da keɓantar musulmai daga haka. Sai kan musulmai ya haɗu har suka zama kamar jiki ɗaya, suka ɗayanta abin bautarsu, kalmarsu ta haɗu, hanyarsu ta haɗu. Lallai wannan ni'ima ce mai

girma ka ga cewa ma’abota imani sun yi rinjaye, ma’abota kafirci sun tarwatse.

5. Kuma yana daga cikin falalar waɗannan kwanaki, cewa, ibadu kan tattaru a cikinsu, a cikinsu akwai salloli kamar yadda suke a wasunsu, a cikinsu akwai zakka ga wanda shekara ta kewayo masa, a ciki akwai azumi ga wanda ya yi nufin nafila, ko bai samu hadaya ba. A cikinsu akwai hajji zuwa ɗaki mai alfarma, wanda ba ya kasancewa a wasunsu, akwai zikiri, da talbiya da addu’ar dake nuna tauhidi. Tattaruwa ibadu a cikinsu ɗaukaka ce da ba ta da makamanci a wasu kwanakin.
6. Yana daga falalolinsu cewa, su ne mafifincin yininnika na duniya duka. Su ne mafi soyuwar kwanki zuwa Allah ta’ala. Kuma Allah ya fi son ayyukan kirki a cikinsu. Lokac ne na riba, kuma tafarkin tsira, kuma fagen gasa na aikin lherai. An karɓo daga Ibn Abbas (R.A) ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, (babu wasu kwanaki da aikin alheri ya fi soyuwa zuwa ga Allah a cikinsu kamar waɗannan kwanaki). Sahabbai suka ce, ya Manzon Allah ko da jihadi a tafarkin Allah? Ya ce, (Koda jihadi a tafarkin Allah, sai mutumin da ya fita da ransa da dukiyarsa sannan bai dawo da ko ɗaya ba) Bukhari ne ya ruwaito shi. Wannan yana nuna cewa aiki a cikin kwanaki goma shi ya fi jihadi da rai kawai, ko da dukiya kaɗai, kuma ya fi yin jihadi da su, a dawo da su, ko ɗaya daga cikin su. Domi ba abin da ya fi aiki a cikin waɗannan kwanaki sai wanda ya fita da ransa da dukiyarsa amma bai dawo da ko ɗaya ba.
7. Sannan Ranar Arfa a cikinsu take, wato ranar tara ga Zul-Hijjah. Ranar Arfa yini ne da aka san shi da falala da yawan lada, da gafarta zunubai. Shi yini ne mai girma, ana sanin ma’abotansa da tauhidi, dominsu suna faɗan: La’ilaha Illallahu, ga shi Manzon Allah (ﷺ) ya ce, (kuma mafificin abin da na faɗa ni da Annabawa gabanina: La’ilaha illallahu). Malik da Tirmizi ne suka ruwaito shi. Kuma Tirmizi ya inganta shi. Kuma mutum yana sanin raunin kansa yayin da yake yawaita addu’a, yake naci ga Allah wajen addu’a, ya zo a cikin hadisi: (Mafificiyar addu’a ita ce addu’ar ranar Arfa), kuma yana sanin ‘yan uwansa musulmi wanda suka taru daga ko ina a fili ɗaya, yana sanin maƙiyinsa wanda ba’a taɓa ganin shi cikin wulaƙanci da ƙasƙanci ba kamar a ranar Arfa. Mutum yana sanin yawan gafarar Allah a wannan rana saboda yawancin hanyoyin gafara na kaɗaita Allah da kiransa, da kiyaye gaɓɓansa da azuminsa idan ba mai aikin hajji ba ne. Kuma shi ne ranar hajji babba, Annabi (ﷺ) (Hajji ita ce tsayuwar Arfa). Abu Dawud da Nasa'i da Tirmizi da Ibn Majah ne suka ruwaito shi, daga Abdurrahman ɗan Ya’amur Addili (R.A). A zumtar wannan yini na nafila kan kankare zunuban shekara biyu: wadda ta wuce, da mai zuwa. Ban kuwasan wata rana mai wannan falalar ba.
8. Yana daga falalarsu cewa, ranar laiya a cikinsu take, wato ranar goma ga Zul Hijja, wadda ita ce goma ga zul hijja, kuma mafificin ranaku kamar yadda yazo a hadisi, (mafificin kwanaki ranar laiya). Mafi girman aiyukan hajji irin su jifa, da aski kai, da yanka hadaya, da ɗawafi, da sa’ayi, da sallar idi, da yanka laiya, da haɗuwar musulmi a sallar idi, da yiwa junansu barka, duka a cikin waɗannan kwanaki goma suke.

Bayin Allah, haƙiƙa falalar kwanaki goma suna da yawa, bai kamata Musulmi ya tozartar da su ba. Ya wajaba ya ci moriyarsu, ya yi gasa na aikin alheran da ke cikinsu, ya tafiyar da su cikin aiki nagari. Ina faɗan abin da kuke ji, kuma ina neman gafar allah ga kaina da ku daga kowane zunubi, ku nemi gafarsa, lallai shi mai gafara ne mai jinƙai.

Huɗuba Ta Biyu

Yabo ya tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Tsira da aminci su tabbata ga cikamakin Annabawa, da alyensa da sahabbansa da waɗanda suka tafi a kan tafarkinsa har ya zuwa ranar sakamako. Bayan haka:

Ya ku bayin Allah, yana daga ayyukan da aka shar'anta cikin waɗannan kwnaki zikiri. Allah ta'ala yana cewa:

﴿ لِّيَشۡهَدُواْ مَنَٰفِعَ لَهُمۡ وَيَذۡكُرُواْ ٱسۡمَ ٱللَّهِ فِيٓ أَيَّامٖ مَّعۡلُومَٰتٍ عَلَىٰ مَا رَزَقَهُم مِّنۢ بَهِيمَةِ ٱلۡأَنۡعَٰمِۖ ﴾[الحج: ٢٨].

(Domin su halarci amfanuunka gare su, kuma su ambaci sunan Allah cikin sanannun kwanaki, saboda abin da ya azurtasu da shi na daga dabbobin ni'ima).

Kuma Imamu Ahmad ya rawaito daga ibn Umar cewa, Annabi (ﷺ) ya ce, (babu wasu kwanaki mafiya girma, da kuma aikin da ya fi soyuwa zuwa ga Allah a cikinsu kamar waɗannan kwanaki guda goma, don haka ku yawaita hailala da kabbara da hamdala a cikinsu).

Abu Huraira da Ibn Umar sun kasance idan goma ga Zulhijjah suka shigo suna fita kasuwa, suna kabbara, kowa shi kaɗai, yayin da mutane suka ji su sai su tuna kabbara, sai kowa shi kaɗai ya yi kabbara. Wannan kabbara ce zalla, kuma ana so mutum ya yawaita tasbihi da hailala da hamdala da zikiri tare da kabbara. Ya yawaita karanta Alƙur'ani domin shi ne mafificin zikiri, kuma acikinsa shiriya da rahama da albarka mai girma da tasiri, da warraka suke. Kuma musulmi ya san cewa zikiri shi ne mafi soyuwar zance zuwa Allah ta'ala, kuma shi ne dalilin tsira a duniya da lahira kuma dalilin rabauta, kuma mai kiyaye ma'abocinsa daga kafrici da shaiɗan da wuta. Da shi ake ambaton bawa a wajan Ubangijinsa, kuma Allah da Mala'ikunsa suna yin sallati ga mai zikiri kuma shi ne mafi ƙarfin makami. Shi ne mafificin ayyuka, mafi tsarkakarsu, mafi ɗaukakarsu a daraja, mafifici a kan ciyarwa, da shi ne Allah yake nununka lada, ya yafe laifi, ya nauyaya ma'auni.

Kuma ya gwama shi da sallar juma'a, Allah ya ce,

﴿ فَإِذَا قُضِيَتِ ٱلصَّلَوٰةُ فَٱنتَشِرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَٱبۡتَغُواْ مِن فَضۡلِ ٱللَّهِ وَٱذۡكُرُواْ ٱللَّهَ كَثِيرٗا ﴾ [الجمعة: ١٠]

(To idan an gama sallah, to ku watsu cikin ƙasa, kuma ku nemi falalar Allah, kuma ku ambaci Allah diyawa).

Kuma ya gwama shi da azumi Allah ya ce,

﴿ وَلِتُكۡمِلُواْ ٱلۡعِدَّةَ وَلِتُكَبِّرُواْ ٱللَّهَ عَلَىٰ مَا هَدَىٰكُمۡ وَلَعَلَّكُمۡ تَشۡكُرُونَ ١٨٥ ﴾ [البقرة: ١٨٥].

(Kuma ku cika adadin azumi, kuma ku girmama Allah saboda shiryar da ku da suka yi).

Kuma aya ta gwama shi da hajji sai ya ce,

﴿ فَإِذَا قَضَيۡتُم مَّنَاسِكَكُمۡ فَٱذۡكُرُواْ ٱللَّهَ كَذِكۡرِكُمۡ ءَابَآءَكُمۡ أَوۡ أَشَدَّ ذِكۡرٗا ﴾[البقرة: ٢٠٠]

(Kuma idan kun idar da ayyukan hajjinku ku ambaci Allah kamar yadda kuke ambaton iyayanku, ko fiye da haka).

Kuma yana daga mafifitan ayyukan a waɗannan kwanaki - ya bayin Allah - yin talbiyya da hajji da neman kusanci zuwa Allah da azumin Arfa ga wanda bai ya aikin hajji, an karɓo daga Abi ƙatadata (R.A) ya ce, an tambayi Annabi (ﷺ) game da azumin ranar Arfa, ya ce, "Yana kankare shekarar da ta wuce da shekara mai zuwa". Muslim ne ya rawaito.

Ya ku bayin Allah! Ana so Musulmi ya yawaita azumi akwanaki gomɗa, da zai azumci kwana tara, to babu ya laifi a shari'a, domin azumi yana daga aiki na gari. Abin da ya zo daga Nana Aisha cewa, ba ta taɓa ganin Manzon Allah (ﷺ) ya yi azumin kwanaki goma na zulhijja ba, to ita ta na ba labarin abin da ta sani ne, domin kwananta a cikin kwanaki tara ɗaya ne tak. Da yawa kuma yakan bar abu don tsoron kada a wajabtawa al'ummarsa, yakan bar shi don uzurin rashin lafiya ko tafiya ko jihadi ko makamantansu.

Ya wajaba ga musulmi, idan goman zulhijja ta shigo yana da nufin laiya kada ya ciri wani abu daga gashinsa, ko fatarsa, ko farcansa. Haka ya zo daga Manzon Allah. Amma waɗanda za a yi musu layya ne, to babu laifi su, su ciri wani abu daga waɗancan abubuwa, domin Annabi ya yi hani ne ga wanda zai yi laiya, su kuwa mutanen gida za a yi musu laiya ne, basu suke yi ba. Don haka ba mu san cewa Annabi yana hana iyalinsa su ciri wani abu daga haka ba, tare da cewa yana yin laiya a madadinsu. Saboda Allah ya yana yin layya kashi biyu ne; ɗaya ga kansa, da iyalansa, ɗaya ga al'ummarsa gaba ɗaya, Allah ya saka masa da alheri a madadinmu, ya san ya mu daga mabiyansa, sarari da ɓoye, ya tashe mu cikin tawagarsa, ya shayar da mu daga tafkinsa, ya haɗa mu da shi a aljanna, lallai shi mai karamci ne mai kyauta ne.

Ku yawaita salati da sallama ga Annabin ku Muhammadu, ku yawaita yi masa salati a kowane lokaci, domin haƙƙinsa a kanku yana girma sosai. Ku yawaita salati a gare shi domin shi ya umarce ku da haka; ku yawaita salati a gare shi domin ku sami lada mai girma dayin haka; domin duk wanda ya yi salati sau ɗaya a gare shi, Allah zai masa salati goma.

Ya kamata musulmi ya yi rigegeniya da kowane aiki na ƙwarai a waɗannan kwanaki goma, ya yawaita addu'a da istigfari, ya nemi kusanci zuwa ga Allah da duk wani aiki mai kusantarwa ga falalar Allah, ku ribace su, kada ku yi nawa ko kasala. Mu sani cewa, Allah ta'ala yana da kyaututtuka a cikin kwanakinsa, to mu ribaci dama, mu yawaita kyawawan aiyuka, ko Allah ya yi mana afuwa game da kura-kuranmu da munanan aiyukanmu.

Allah ka shiryar da mu zuwa ga mafi shiryuwar zantuttuka da aiyuka, babu mai shiryarwa gare su sai kai. Allah ka nesanta mu daga munanan maganganu da ayyuka da soye-soyen zukata da cututtuka, babu mai nesanta mu daga munanansu sai kai, Allah ka shiryar da mu ka daidaita mu.

Allah ya yi min albarka da ku, da Alƙur'ani mai girma, kuma ya amfane ni, da ku da abin da ke cikinsa na daga ayoyi da wa'azi mai hikima, ya amfane mu da shiriyar Shugabannin Manzanni, da miƙaƙƙiyar maganarsa.

SON ALLAH DA MANZONSA(ﷺ)

Manufofin huɗubar

- Bayanin wajabcin son Allah da Manzonsa. Da fifita su a kan komai
- Dasa son Allah da Manozonsa a cikin zukata.
- Bayanin alamomin son Allah da Manzonsa.
- Abubuwan da suke haifar da son Allah da Manzonsa.
- Jan-Kunne a kan gabatar da son mata ko dukiya ko ‘ya’ya a kan son Allah da Manzonsa.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammadu bawansa ne manzonsa ne. (Yaku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron Allah yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Yaku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammadu (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (a addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta".

Bayan haka:

Ya ‘yan uwa musulmai! Maganarmu a yau, magana ce mai girma, kowane ɗaya daga cikinmu yana buƙatar ta. Imaninmu ba zai cika ba, sai mun tabbatar da ita: Abin nufi, son Allah da Manzonsa, da kuma gabatar da su a kan duk wani abu da ba su ba. Lallai imani ba zai cika ba, ba tare da ƙaunar Allah, da son Manzon Allah (ﷺ) ba. Babu yadda za a yi mutum ya zama cikakken mai imani, ba tare da ya gabatar da son Allah da Manzonsa a kan duk wani abu da ya mallaka na dukiya, ko ɗa, ko mahaifa, ko ma sauran mutane baki ɗaya ba, kamar yadda Manzon Allah (ﷺ) ya yi bayanin haka cikin ingantaccen hadisi.

Ya ‘yan uwa musulmi! Haƙiƙa Allah ya umarci muminai, da su ƙaunaci Manzon Allah (ﷺ) a wuri daban-daban a cikin littafinsa. Kaɗan daga ciki, Allah yana cewa,

﴿ قُلۡ إِن كَانَ ءَابَآؤُكُمۡ وَأَبۡنَآؤُكُمۡ وَإِخۡوَٰنُكُمۡ وَأَزۡوَٰجُكُمۡ وَعَشِيرَتُكُمۡ وَأَمۡوَٰلٌ ٱقۡتَرَفۡتُمُوهَا وَتِجَٰرَةٞ تَخۡشَوۡنَ كَسَادَهَا وَمَسَٰكِنُ تَرۡضَوۡنَهَآ أَحَبَّ إِلَيۡكُم مِّنَ ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَجِهَادٖ فِي سَبِيلِهِۦ فَتَرَبَّصُواْ حَتَّىٰ يَأۡتِيَ ٱللَّهُ بِأَمۡرِهِۦۗ وَٱللَّهُ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلۡفَٰسِقِينَ ٢٤ ﴾ [التوبة: ٢٤].

(Idan dai iyayenku, da ‘ya’yanku, da ‘yan uwanku, da matanku, da danginku, da dukiyoyinku da kuka tara, da kasuwancin da kuke tsoron durƙushewarsa, da gidajen da kuke son su, sun fi soyuwa gare ku, sama da Allah da Manzonsa da jihadi a cikin tafarkinsa, to ku dakata har Allah ya zo da al’amarinsa. Allah ba ya shiryar da mutanen da suke fasiƙai ne).

Alƙadhi Iyad, mai littafin Ashafa, yana cewa, a cikin littafinsa: «Wannan aya ta isa wajen tabbatar da wajabcin ƙaunar Manzon Allah (ﷺ), da tabbatar da cancantarsa da soyayyar muminai, don Allah ya ƙwanƙwanshi wanda ya zama dukiyarsa da matansa da ‘ya’yansa sun fi soyuwa zuwa gare shi, sama da Allah da Manzonsa. Sannan ya yi narko da faɗinsa, “….ku dakata har Allah ya zo da al’amarinsa.” Sannan ya rataya musu fasiƙanci a ƙarshen ayar, ya kuma sanar da su cewa suna daga cikin waɗanda suka ɓata, kuma Allah ba zai shiryar da su ba.

Allah yana cewa,

﴿ قُلۡ إِن كُنتُمۡ تُحِبُّونَ ٱللَّهَ فَٱتَّبِعُونِي يُحۡبِبۡكُمُ ٱللَّهُ وَيَغۡفِرۡ لَكُمۡ ذُنُوبَكُمۡۗ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٣١ ﴾ [آل عمران: ٣١].

(In kun kasance kuna son Allah, to ku yi mini biyayya, sai Allah ya so ku, kuma ya gafarta muku laifukanku. Kuma Allah mai yawan gafara ne mai jin ƙai).

Kuma Allah ya ce,

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تُقَدِّمُواْ بَيۡنَ يَدَيِ ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦۖ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَۚ إِنَّ ٱللَّهَ سَمِيعٌ عَلِيمٞ ١ ﴾ [الحجرات: ١].

(Ya ku waɗanda suka yi imani! Kada ku sha gaban Allah da Manzonsa. Ku ji tsoron Allah, lallai Allah mai ji ne, kuma masani).

Ya zo a cikin sunnar, Manzon Allah (ﷺ), kamar yadda Anas ibn Malik ya rawaito cewa, “Dayanku ba zai yi imani ba, har sai na kasance mafi soyuwa a gare shi, sama da mahaifansa da ɗansa da sauran mutane baki ɗaya.” Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.

Haka nan, Anas ibn Malik ya rawaito cewa, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Abubuwa guda uku, duk wanda ya same su, ya sami zaƙin imani: Allah da Manzonsa su zamo su ne mafi soyuwa gare shi daga abin da ba su ba; kuma ya so mutum, ba don komai ba, sai don Allah; kum ya dinga ƙyamar ya koma cikin kafirci, kamar yadda yake ƙyamar a jefa shi a cikin wuta.”. Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.

Lallai ƙaunar Allah da Manzonsa, tana da alamomi, wanda malamai suka yi bayaninta dalla-dalla, suka tsamo daga cikin littafin Allah, da sunnar Manzon Allah (ﷺ). Alƙali Iyadh yana cewa, "Mai gaskiya a cikin da’awar ƙaunar Manzon Allah (ﷺ), shi ne wanda aka ga alamomin ƙauna tare da shi. Abu na farko, koyi da shi, da aiki da sunnarsa, bin maganganunsa da ayyukansa, kwatanta umarninsa da nesantar abin da ya hana, da kamanta ladabi irin nasa, a cikin kowane irin yanayi

mai dadi ko marar dadi. Duk wannan yana ƙunshe a cikin fadin Allah cewa,

﴿ قُلۡ إِن كُنتُمۡ تُحِبُّونَ ٱللَّهَ فَٱتَّبِعُونِي يُحۡبِبۡكُمُ ٱللَّهُ وَيَغۡفِرۡ لَكُمۡ ذُنُوبَكُمۡۗ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٣١ ﴾ [آل عمران: ٣١].

(In kun kasance kuna son Allah, to ku yi mini biyayya, sai Allah ya so ku…).

Haka da fifita abin da ya shar'anta, kuma ya kwadaitar a kai, a kan bin son zuciya, da bin sha'awa. Allah yana cewa,

﴿ وَٱلَّذِينَ تَبَوَّءُو ٱلدَّارَ وَٱلۡإِيمَٰنَ مِن قَبۡلِهِمۡ يُحِبُّونَ مَنۡ هَاجَرَ إِلَيۡهِمۡ وَلَا يَجِدُونَ فِي صُدُورِهِمۡ حَاجَةٗ مِّمَّآ أُوتُواْ وَيُؤۡثِرُونَ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمۡ وَلَوۡ كَانَ بِهِمۡ خَصَاصَةٞۚ وَمَن يُوقَ شُحَّ نَفۡسِهِۦ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُفۡلِحُونَ ٩ ﴾ [الحشر: ٩].

(Wadanda suka zauni gida, suka yi imani tun ganinsu, suna son wadanda suka yi hijira zuwa gare su. Ba sa jin takuruwa a zuciyarsa daga a ka ba su. Su na fifita 'yan uwansu akansu ko da kuwa sun kasance suna da buƙata. Wadannan su ne masu samun babbar nasara).

Yana daga ciki, taimakon addininsa, ta hanyar magana ko aiki, da kare sunnarsa; yana daga ciki, yawan begen haduwa da shi; yana daga ciki, son karatun Alƙur'ani, da ƙin duk wanda ba ya son Allah da Manzonsa.

Amma abubuwan da suke jawo soyayyar Allah da Manzonsa ga bayi, su ne; yin imani da Allah Ta'ala, ayyuka na ƙwarai, haƙuri, kyautata wa bayi, tsarki, tuba. Allah yana cewa,

﴿ وَٱللَّهُ يُحِبُّ ٱلصَّٰبِرِينَ ١٤٦ ﴾ [آل عمران: ١٤٦].

(Allah yana son masu haƙuri).

Haka kuma, Allah yana cewa,

﴿ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ١٩٥ ﴾ [البقرة: ١٩٥].

(Lalle Allah yana son masu kyautayi).

Haka kuma, Allah yana cewa,

﴿ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ سَيَجۡعَلُ لَهُمُ ٱلرَّحۡمَٰنُ وُدّٗا ٩٦ ﴾ [مريم: ٩٦].

(Lallai wadanda suka ba da gaskiya, kuma suka yi ayyuka na ƙwarai, da sannu Allah zai sanya musu ƙauna).

Kuma Allah yana cewa,

﴿ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلتَّوَّٰبِينَ وَيُحِبُّ ٱلۡمُتَطَهِّرِينَ ٢٢٢ ﴾ [البقرة: ٢٢٢].

(Lallai Allah yana son masu tuba, kuma yana son masu tsarki).

Haka kuma, Allah yana cewa,

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مَن يَرۡتَدَّ مِنكُمۡ عَن دِينِهِۦ فَسَوۡفَ يَأۡتِي ٱللَّهُ بِقَوۡمٖ يُحِبُّهُمۡ وَيُحِبُّونَهُۥٓ أَذِلَّةٍ عَلَى ٱلۡمُؤۡمِنِينَ أَعِزَّةٍ عَلَى ٱلۡكَٰفِرِينَ يُجَٰهِدُونَ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَلَا يَخَافُونَ لَوۡمَةَ لَآئِمٖۚ ذَٰلِكَ فَضۡلُ ٱللَّهِ يُؤۡتِيهِ مَن يَشَآءُۚ وَٱللَّهُ وَٰسِعٌ عَلِيمٌ ٥٤ ﴾ [المائدة: ٥٤].

(Ya ku wadanda suka yi imani! Duk wanda ya ba da baya ga barin addininsa daga cikinsu, da sannu Allah zai zo da wasu mutane, wadanda yake son su, kuma su ma suke son sa, masu ƙanƙan da kai a kan muminai, masu nuna ɗaukaka a kan kafirai, suna yin jihadi a cikin tafarkin Allah, ba sa tsoron zargin mai zargi. Wannan wata falala ce daga Allah yana bayar da ita ga wanda ya so. Kuma lalle Allah mai yalwatawa ne, masani).

Yabo da godiya da kira sun tabbata ga Allah, Ubangijin talikai. Tsira da amincin Allah su tabbata ga Annabin rahma, Annabinmu Muhammad da alayensa da sahaabban da sauran masu ƙaunarsa har zuwa ranar ƙiyama. Bayan haka:

Ya ku ‘yan uwa! Ku sani, sahabban Manzon Allah (ﷺ) sun nuna rayuwa abar misali, wajen ƙaunar Manzon Allah (ﷺ), da girmama shi. Ba a taɓa samu wasu mutane a doron ƙasa ba waɗanda suka so win bil-adama kamar yadda sahabban Manzon Allah (ﷺ) suka so shi. Daga wajensu ne za mu koyi yadda haƙiƙanin son Manzon Allah ya ke.

An karɓo daga Amr bin Aas (RA) ya ce, “Babu wani da ya fi soyuwa zuwa zuciyata, sama da Manzon Allah (ﷺ); babu wanda ya fi ƙima a idanuna, sama da shi; amma duk da haka ba na iya cika idanuna wajen kallon sa, saboda girmamashi. Da za a tambaye ni, in siffanta shi, da ba zan iya ba, saboda ba na iya cika idanuna wajen kallon sa.” Muslim ne ya ruwaito shi.

Urwatu ɗan Mas'ud (R.A.) kafin ya shiga musulunci, ya ga irin yadda sahabban Manzon Allah (ﷺ) su ke girmama shi, suke nuna masa soyayya ta haƙiƙa, suke tabarraki da wasu abubuwa masu alaƙa da shi. Ya kuma ga irin yadda suke gaggawar zartar da umarninsa. Lokacin da ya je sulhul Hudaibiyya, ya gane wa idonsa hakan. Ga yadda ruwayar ta zo:

"Sannan Urwa ya zurawa sahabban Annabi (ﷺ) ido yana kallon su. Ya ce: "Wallahi babu wani kaki da Manzon Allah (ﷺ) ya tofar face ya faɗa a hannun ɗaya daga cikinsu, kuma ya shafe fuskarsa da jikinsa da shi. Idan ya umarce da wani abu, nan da nan sai su zartar da wannan abin. Idan kuma ya rage ruwan alwala, to fa kamar sa yi faɗa a kan sauran wannan ruwan. Idan kuwa yana magana to kowa sai ya yi tsit yana sauraron shi. Ba sa iya ƙura masa ido, domin irin yadda suke ganin girmansa. Daga nan Urwatu ya koma ga kafirai 'yan uwansa ya ce musu: "Ya jama'ata! Wallahi na yi yawo na ga sarakuna daban-daban. Na ga sarki ƙaisara na rumawa, naga sarkin Farisawa Kisra, naga na Habasha Najashi, to amma wallahi ban ga sarkin da mutanensa suke girmama shi ba kamar yadda sahabban Manzon Allah (ﷺ) suke girmama shi. Wallahi bai yi kaki ya tofar ba face ya faɗa a hannun ɗaya daga cikinsu, kuma ya shafe fuskarsa da jikinsa da shi. Idan ya umarce da wani abu, nan da nan sai su zartar da wannan abin. Idan kuma ya rage ruwan alwala, to fa kamar sa yi faɗa a kan sauran wannan ruwan. Idan kuwa yana magana to kowa sai ya yi tsit yana sauraron shi. Ba sa iya ƙura masa ido, domin irin yadda suke ganin girmansa". Bukhari ne ya ruwaito shi.

An tambayi Aliyu bin Abi Talib, “Yaya ƙaunarku ta kasance ga Manzon Allah (ﷺ)?” Sai ya ce, “Na rantse da Allah, ya kasance, ya fi soyuwa ga zukatanmu, sama da dukiyoyinmu, da ‘ya’yanmu, da iyayenmu. Kai sama ma da ruwan sanyi ga mai jin ƙishi”.

Kuma Alƙali iyad ya rawaito cewa, Bilal da Huzaifatubn Yaman da Ammar bn Yasir, sun kasance lokacin da mutuwa ta zo musu, suna cewa, “Gobe za mu haɗu

da masoya, Muhammadu da rundunarsa.”

Ya ku 'yan uwana musulmi! Ku sani Allah yana cewa,

﴿ قُلۡ إِن كُنتُمۡ تُحِبُّونَ ٱللَّهَ فَٱتَّبِعُونِي يُحۡبِبۡكُمُ ٱللَّهُ وَيَغۡفِرۡ لَكُمۡ ذُنُوبَكُمۡۗ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٣١ ﴾ [آل عمران: ٣١].

(Ka ce, idan har kuna son Allah, to ku bi ni Allah zai so ku ya gafarta muku zunubbanku. Kuma Allah mai yawan gafara ne, mai yawan jin ƙai).

Malam Ibni Kasir yana cewa, «Wannan aya mai girma, ta yanke hukunci a kan dukkan wanda ya yi da’awar ƙaunar Allah, amma kuma ba ya kan tafarkin Manzon Allah (ﷺ), da cewa lallai shi maƙaryaci ne, har sai ya bi shari’ar Manzon Allah (ﷺ), da addinin da Annabi ya zo da shi, cikin gabaɗayan maganganunsa da ayyukansa da yanayinsa, kamar yadda ya tabbata cikin hadisi, Manzo Allah (ﷺ) yana cewa, “Duk wanda ya aikata wani aiki, ba tare da umarninmu ba, za a mayar masa da aikinsa.” Wani daga cikin masu hikima yana cewa, Batun inda yake, shi ne a so ka, ba wai kai ka ce, kana so ba". Hasanul Basari yana cewa, "Wasu daga cikin mutane sun yi da'awar ƙaunar Allah, sai Allah ya jarrabe su da wannan aya". Kuma Manzon Allah yana cewa, "Na hore ku da bin sunnata da sunnar halifofi na shiryayyu. Ku cije su da fiƙoƙinku. Kuma ina jan-kunnenku game da fararrun al'amurra. Domin duk wani fararren abu bid'a ne, duk wata bid'a kuwa ɓata ce".

Ya ku ‘yan uwa! Ku sani, yana daga cikin haƙƙoƙin Manzon Allah (ﷺ) a kan bayi, su dinga yin salati gare shi, kamar yadda Allah yake cewa,

﴿ إِنَّ ٱللَّهَ وَمَلَٰٓئِكَتَهُۥ يُصَلُّونَ عَلَى ٱلنَّبِيِّۚ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ صَلُّواْ عَلَيۡهِ وَسَلِّمُواْ تَسۡلِيمًا ٥٦ ﴾ [الأحزاب: ٥٦].

“Lallai Allah da mala’ikunsa suna salati ga Annabi. Ya ku waɗanda suka yi imani! Ku yi salati gare shi, kuma ku yi masa taslimi.”

Haka yana daga cikin haƙƙoƙinsa a kan wannan al’umma, girmamashi da kambama shi. Allah yana cewa,

﴿ لَّا تَجۡعَلُواْ دُعَآءَ ٱلرَّسُولِ بَيۡنَكُمۡ كَدُعَآءِ بَعۡضِكُم بَعۡضٗا ﴾[النور: ٦٣].

(Kada ku sanya kiran Manzon Allah a tsakaninku, kamar kiran junanku).

Haka nana, yana daga cikin haƙƙoƙinsa, kare martabarsa da martabar sahabbansa masu girma.

Ya Allah ka sanya cikin masu ƙaunar Annabinka ƙauna ta haƙiƙa. Ka tabbatar da digadiganmu akan sunnarsa, mu rayu akai mu mutu a kai, kuma a tashe mu tare da tawagar ƙwarai, ta Annabawa da siddiƙai da salihai da shahidai.

KIYAYE HAKKIN MAKOTAKA DA MAKOCI

Manufofin huɗubar

- Bayanin haƙƙin Maƙotaka a musulunci.
- Bayyana haƙƙin maƙoci a kan maƙocinsa.
- Fito da Falalar kyautatawa maƙoci.
- Jan – kunne da razanarwa akan cutar da maƙoci.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga shirrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammad bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammad (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

'Yan uwa musulmi : Huɗubarmu a yau tana magana ne akan wani maudu'i babba da kowa yake buƙatarsa, abu ne mai girma wanda Mala'ika Jibrilu (A.S) ya yi ta yi wa Manzon Allah (ﷺ) wasici da shi, har sai da ya yi zaton za a bashi gado, wannan abu ba komai ba ne face haƙƙin maƙotaka.

Haƙiƙa – yaku 'yan uwa – maƙoci yana da haƙƙoƙi masu girma a addinin musulunci, waɗanda ya wajaba a kiyaye su, a lazimce su, kada a yi sakaci da su.

Maƙoci a shari'a shi ne wanda ya maƙotace ka, musulmi ne shi ko kafiri, mutum ne nagari ko kuma fajiri, abokin ka ne ko kuwa maƙiyinka ne, ɗan uwanka ne ko ba ɗan uwanka ba, kai koma waye, in dai ya zauna kusa da kai to ya zama maƙocinka yana da haƙƙi a kanka.

Al – Hafiz Ibnu Hajar – Allah ya yi masa rahama – yana cewa : "sunan maƙoci ya haɗa musulmi da kafiri, mai bauta wa Allah da fasiƙi, aboki da maƙiyi, ɗan gari da baƙo, mai amfanarwa da maras amfanarwa, makusanci ne ko wanda yake

nesa, gidansa a kusa yake ko a nesa. Maƙotaka tana da matakai, wasu sun fi wasu, mafi girman matsayi a maƙota shi ne wanda ya haɗa siffofin farko gaba ɗaya (ma'ana ya zama musulmi, mai bauta wa Allah, aboki, ɗan gari, mai amfanarwa, makusanci, kuma wanda gidansa yake kusa) sannan sai wanda yake bi ye masa a cikin waɗannan siffofi har zuwa wanda yake da siffa ɗaya" (Duba Fathul Bari J 10 Sh 441).

Don haka, Maƙocin da gidansa yake jikin naka, ba daidai yake da maƙocin da gidansa yake nesa da kai ba, maƙocin da yake ɗan uwanka ne, ba daidai yake da maƙocin da yake ba ɗan uwanka ba, kamar yadda nagarin maƙoci ba daidai yake da fasiƙin maƙoci ba.

Musulunci ya yi wasiyya da maƙoci, ya ɗaukaka darajarsa, maƙoci a musulunci yana alfarma da haƙƙoƙi masu yawa. Allah ya yi umarni da kyautata wa maƙoci a ayoyi da yawa : Allah ya ce:

﴿ وَٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ وَلَا تُشۡرِكُواْ بِهِۦ شَيۡـٔٗاۖ وَبِٱلۡوَٰلِدَيۡنِ إِحۡسَٰنٗا وَبِذِي ٱلۡقُرۡبَىٰ وَٱلۡيَتَٰمَىٰ وَٱلۡمَسَٰكِينِ وَٱلۡجَارِ ذِي ٱلۡقُرۡبَىٰ وَٱلۡجَارِ ٱلۡجُنُبِ وَٱلصَّاحِبِ بِٱلۡجَنۢبِ وَٱبۡنِ ٱلسَّبِيلِ وَمَا مَلَكَتۡ أَيۡمَٰنُكُمۡۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ مَن كَانَ مُخۡتَالٗا فَخُورًا ٣٦ ﴾ [النساء : ٣٦].

Ma'ana : "Ku bauta wa Allah kada ku yi shirka da shi da wani abu, ku kyautata wa iyaye, da makusanta, da marayu, da miskinai, da maƙocin da yake makusanci, da maƙocin da yake nesa, da wanda yake kusa da kai, da wanda yake matafiyi, da abin da hannun damanku suka mallaka, haƙiƙa Allah ba ya son wanda yake mai yawan girman kai mai yawan alfahari" (Annisa'i 36).

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Jibrilu mai gushe ba, yana ta yi min wasiyya aka maƙoci, har sai da na yi zaton zai ce a bashi gadona" Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

An karɓo daga Abu Hurairata – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Wanda duk ya yi imani da Allah da ranar ƙarshe to ya faɗi alheri ko ya yi shiru. Wanda duk ya yi imani da Allah da ranar ƙarshe to ya gimama maƙocinsa. Duk wanda ya yi imani da Allah da ranar ƙarshe to ya girmama baƙonsa". Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

Imam Alƙali Iyad – Allah ya yi masa rahama – ya ce, "Ma'anar hadisin shi ne duk wanda ya lazimci ayyukan musulunci to ya zama wajibi a kansa ya girmama maƙocinsa da baƙonsa, ya kyautata musu, saboda bayanin haƙƙin maƙoci, da kwaɗaitarwa akan kiyaye shi". (Sharhin Sahih Muslim).

An karɓo daga Abu Shuraih – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Wallahi bai yi imani ba, Wallahi bai yi imani ba, Wallahi bai yi imani ba!!. Aka ce, "Waye shi ya Manzon Allah (ﷺ)?" Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "shi ne wanda maƙocinsa bai aminta daga sharrinsa ba". Bukhari ne ya rawaito.

Imam Abu Muhammad Ibnu Abi Jamra – Allah ya yi masa rahama – ya ce, "Kiyaye haƙƙin maƙota yana cikin cikar imani, mutanen jahiliyya sun kasance suna kiyaye wannan haƙƙi, kamanta wannan umarni zai yi wu ta hanyar sadar da ayyukan alheri gare shi gwargwadon iko, kamar yi masa kyauta, da sallama, da

sakin fuska yayin da aka haɗu, da bibiyar halin da ake ciki, da taimakonsa cikin abin da yake buƙata, da sauransu, da kare shi daga cutarwa ta kowace hanya" (Fathul Bari J10 sh 442).

An karɓo daga Abu Hurairata - – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Haƙƙin musulmi a kan musulmi shida ne" Aka ce "Meye su ya Rasulallahi? Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "idan ka gamu da shi ka yi masa sallama, idan ya gayyaceka ka amsa masa, idan ya nemi nasiha ka yi masa, idan ya yi atishawa ya godewa Allah ka gaishe shi, idan ya yi rashin lafiya ka je ka duba shi, idan ya mutu ka raka shi". Muslim ne ya rawaito shi.

Ya 'yan uwa : Babu ko shakka cutar da maƙoci haramun mai tsanani. An karɓo daga Abu Shuraih – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Wallahi bai yi imani ba, Wallahi bai yi imani ba, Wallahi bai yi imani ba!!. Aka ce, "Waye shi ya Manzon Allah (ﷺ)?" Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "shi ne wanda maƙocinsa bai aminta daga sharrinsa ba". Bukhari ne ya rawaito.

Hadisi ya inganta daga Abu Hurairata – Allah ya yarda da shi – ya ce, An bawa Manzon Allah (ﷺ) labarin wata mace aka ce, "Ya Manzon Allah, wance tana sallar dare, tana yi azumin Ramadana, amma tana da kaifin harshe, tana cutar da maƙotanta" sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Babu alheri a tare da ita, 'yar wuta ce". Aka sake ce masa : "Wance kuma tana sallar farilla ne kaɗai, tana azumin watan Ramadan, tana sadaka da ɗan abin da take da shi na cukwi, amma ba ta cutar da kowa. A riwayar Imam Ahmad "Ba ta cutar da kowa da harshenta" Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Yar Aljannace". Bukhari ne ya rawaito shi a cikin (Al'adabul Mufrad).

Kai! hadisi ya zo da tsinewa wanda yake cutar da maƙocinsa, An karɓo daga Abu Juhaifa – Allah ya yarda da shi – ya ce, wani mutum ya kawo wa Manzon Allah (ﷺ) ƙarar cewa Maƙocinsa yana cutar da shi, sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Je ka, ka fitar da kayanka, ka zuba su akan hanya". Da ya je ya zuba, sai mutane suka riƙa wuce wa, suna tsine wa wannan maƙoci. Sai wannan maƙocin ya ruga wajen Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Ya Manzon Allah mutane suna tsine min" sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Ai Allah ya tsine maka tun gabanin mutane su tsine maka". Sai ya ce, "Ya Manzon Allah ba zan ƙara ba". Bukhari ne ya rawaito shi a cikin littafin "Al – Adab".

Yanzu – yan uwa – bayan waɗannan hadisai da wannan razanarwar akan cutar da maƙoci ake samun masu yin sakaci da wannan haƙƙi, suna cutar da maƙotansu!.

A yau abin baƙin ciki da takaici an wayi gari muna ganin cututtuka kala – kala na wasa da sakaci da wannan haƙƙi mai girma, haƙƙin maƙotaka, kamar takurawa maƙoci ta hanyar ajiye mota a gaban ƙofar gidansa don takura masa wajen shiga da fita, da barin ruwa yana kwarara a gaban gidansa, da cutar da maƙoci da mummunan wari da ɗoyi wanda yake fitowa daga wannan magudanar ruwan da sauransu. Hakanan da cutar da maƙoci ta hanyar barin shara a ƙofar gida, ko ƙetare iyaka cikin haƙƙinsa, ko shiga iyakarsa, ko yi masa sata, da ɗauke masa kaya, a wurin aiki ko makaranta ko kasuwa, da sauransu.

Ya tabbata daga Miƙdad ɗan Aswad – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce wa sahabbansa : "Me zaku ce akan sata?" sai sahabbai suka ce "Ai Allah da Manzosa sun haramta ta, don haka haramun ce". Sai Manzon Allah ya ce, "To mutum ya yi sata a gida goma, ya fi sauƙi a kan ya yi sata a gidan maƙocinsa".

Yana daga cikin cutar da maƙoci yi masa ta'adda, da cutar da 'ya'yansa, ko yin wasa da abin hawansa, ko damunsa da ƙara mai tsanani, kamar sautin waƙa, ko hon ɗin mota, musammam ma a lokacin barci da hutawa, duk waɗannan cutarwa ce da aka haramta a tsakanin mutane, don haka haramcinta ga maƙoci ya fi fitowa fili.

Yana daga cikin mafi girman cutar da maƙoci ha'intar shi da yaudarar shi, kamar bibiyar al'amurarsa don gano laifinsa, ko kai maganarsa wurin maƙiyansa, ko leƙa masa wuraren alfarmarsa daga saman gida ko da taga, da sauransu, don haka ma narkon azaba mai tsanani ya zo daga Manzon Allah (ﷺ) ga wanda zai riƙa yaudara da leƙa al'aurar maƙotansa. Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Mutum ya yi zina da mata goma ya fi masa sauƙi da ya yi zina da matar maƙocinsa".

Saboda haka waɗanda suke yaudara da ha'intar maƙotansa, waɗanda suke jiran samun wata dama don su ha'inci maƙotansu, su cutar da su, ta hanyar tare matansu, ko yi musu aike, ko kallonsu, su ji tsoron Allah, su sani yin haka laifi ne mai girma, kuma haɗari babba.

Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa :

﴿ وَٱلَّذِينَ يُؤْذُونَ ٱلْمُؤْمِنِينَ وَٱلْمُؤْمِنَٰتِ بِغَيْرِ مَا ٱكْتَسَبُوا۟ فَقَدِ ٱحْتَمَلُوا۟ بُهْتَٰنًا وَإِثْمًا مُّبِينًا ﴿٥٨﴾ ﴾ [الأحزاب: ٥٨].

Ma’ana : “Waɗanda suke cutar da muminai maza da mata ba ta wani abin da suka yi ba, haƙiƙa waɗannan sun ɗauki ƙire da zunubi bayananne” (Al – Ahzab : 58).

Allah ya yi mana Albarka cikin abin da muka ji na Alƙur’ani mai girma, Allah ya amfanar da mu da abin da yake cikinsa na ayoyi da zikiri mai girma, haƙiƙa Allah mai iko ne akan komai.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah, Kyakkyawan ƙarshe yana ga masu tsoron Allah, Tsira da Aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, Manzon Allah (ﷺ) da iyalansa da Sahabbansa da waɗanda suka bi su gaba ɗayansu, har zuwa ranar sakamako. Bayan haka:

Yaku bayin Allah: Hanyoyin cutar da maƙoci suna da yawa, amma waɗanda suka fi afkuwa su ne : Maƙoci ya yi abin da zai cutar da maƙocinsa a wajensa, kamar mutum ya shuka bishiya a ƙofar gidansa amma reshenta ya kai kan kwanon maƙocinsa, yana cutar da shi, ko ya gina rijiya da riƙa tsotse wa maƙocinsa ruwa, ko maƙoci ya yi wani wurin sana’a a wajensa, amma yana cutar da maƙota da hayaƙi ko ƙura, ko wani sauti maras daɗi, ko ya yi window yana leƙen gidan

maƙotansa. Ko ya yi ƙatuwar katangar da za ta kare musu rana da iska, da sauran iri waɗannan ayyuka. Duk waɗannan cutarwa ne ya wajaba a kawar da su.

Yana daga cikin babbar cutar da maƙoci mutum ya ba da hayar gidansa ga mutanen da ba sa sallah, ba sa tsoron Allah, haƙiƙa irin waɗannan mutane suna takura wa maƙota, suna iya yin tasiri akan 'ya'yansu da duk wanda ya cakuɗa da su, don haka waɗanda suke bawa kafirai da fasiƙai haya kusa da gidajen musulmi su ji tsoron Allah, kuma su sani hayar da suke karɓa haramun ne, sannan musulmi suna yi muku addu'a mummuna, kuna samun alhaki da zunubi.

Yana daga cikin cutar da maƙoci, mutum ya hana maƙocinsa amfanuwa da kayansa a yanayin da ba zai cutar da shi ba, kamar maƙoci ya buƙaci zai sanya katako a jikin katangar maƙocinsa, katangar da zata iya ɗaukar wannan katakon, to wajibi ne ya bashi dama, saboda hadisin da Bukhari da Muslim suka rawaito daga Abu Hurairata – Allah ya yarda da shi – Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Kada ɗayanku ya hana maƙocinsa ya kafa katakonsa a jikin katangarsa".

Yana daga cikin cutar wa ga maƙota hana su amfanuwa da abin da aka yi don jama’a, kamar hana su ɗibar ruwa daga ƙoramu da wuraren da ruwa yake taruwa, ko ya hana su kiwo a jeji, ko yin ciyawa da itace a wuraren da bana kowa ba ne, ko hana su amfanuwa da ma'adinan da suke ƙasa wanda na kowa – da – kowa ne, kamar gishiri da waninsa. Hadisi ya tabbata a cikin Bukhari da Muslim daga Abu Hurairata – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Kada ku hana yin amfani da ruwan da ya rage muku, don ku hana fitowar ciyawa da shi".

‘Yan uwa musulmi : Magabanta na ƙwarai sun buga kyakkyawan misali wajen kyautatawa maƙoci, daga cikin su, akwai wanda Imam Az – Zahbi – Allah ya yi masa rahama – ya ambata a cikin litattafinsa (Siyari A’alamin Nubala’i J 13 sh 433). Ya ce, Wani Maƙocin Abu Hamzatas Sukkari ya yi niyyar sayar da gidansa, da aka tambaye shi, “Nawa zai sayar?” sai ya ce, “Dubu biyu kuɗin gida, dubu biyu kuma kuɗin maƙotaka da Abu Hamza”. (ya faɗi haka ne saboda irin yadda yasan dadin zama da Abu Hamza). A lokacin da Abu Hamzata ya ji labari, sai ya aiko wa da wannan maƙocin nashi dubu huɗun da ya nema kyauta, ya ce, kada ka sayar da gidanka”.

Allahu Akbar!, waɗannan su ne magabatanmu na ƙwarai, masu taimaka wa maƙotansu a lokacin da suke da buƙata, ba irin maƙotan da suke jiran wata dama ba, da maƙoci zai ɗaga gidansa, su kuma su saye su ƙara da nasu, shi kuma ya san inda ya yi!.

Hakanan an rawaito cewa Ibrahim ɗan Huzaifa ya sayar da gidansa, a lokacin da mai sayen ya so ya kafa shaida cewa ya saya, sai Ibrahim ya ce, “ba zaka kafa shaida ba har sai in zaka sayi maƙotakar Sa’id ɗan Asi daga gareni (ma’ana har sai ya ƙara masa kuɗi saboda wannan gida da ya sayar masa yana kusa da Sa’id ɗan Asi, shi kuma Sa’id mutum ne mai kyautata wa maƙota) sai mutane suka cewa Ibrahim “Yanzu ka taɓa ganin wanda ya saya ko ya saida maƙotaka?” Sai ibrahim ya basu amsa da cewa : “Ba zaku sayi maƙotakar wanda idan ka munana masa, shi sai ya kyautata maka, idan ka yi masa wauta, shi sai ya yi haƙuri da kai,

idan ka shiga tsanani, sai ya baka kyauta. Kai! Ba na buƙatar cinikinku, ku bani gidana". Da labari ya je wa maƙocin nasa Sa'id sai ya aika masa da dirmahi dubu ɗari kyauta!.

An tambayi Imam Ahmad ɗan Hanbal – Allah ya yi masa rahama – dangane da Walid ɗan Kasim ɗan Walid, sai Imamu Ahmad ya ce, "Amintacce ne, na rubuta hadisi daga wajensa, kuma maƙocin Ya'ala ɗan Ubaid ne, kuma ni na tambayi Ya'ala ɗan Ubaid akan maƙocinsa Walid ɗan Kasim ɗan Walid Al-hamdaniy sai ya ce min "Madallah da wannan mutumin, maƙocina ne tsawon shekara hamsin, amma ban taɓa ganin komai a tare da shi ba sai alheri". (Duba Siyar).

Wannan kaɗan kenan daga cikin iri yadda magabatanmu suke zama da maƙotansu, don haka ina kira ga 'yan uwa musulmi da mu ji tsoron Allah, ku kyautatawa maƙotanmu, mu tuna cewa Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa :

﴿ وَتَعَاوَنُواْ عَلَى ٱلۡبِرِّ وَٱلتَّقۡوَىٰۖ وَلَا تَعَاوَنُواْ عَلَى ٱلۡإِثۡمِ وَٱلۡعُدۡوَٰنِۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَۖ إِنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ ٢ ﴾

[المائدة: ٢].

Ma'ana : "Ku taimakekkiniya da junanku akan ayyukan alheri da tsoron Allah, kada ku taimaki juna akan laifi da ƙetare iyaka (zalunci) ku ji tsoron Allah, Haƙiƙa Allah mai matsananciyar uƙuba ne" (Al – Ma'ida : 2). Allah Maɗaukakin Sarki ya sa mu dace.

ALAMOMIN TASHIN KIYAMA

Manufofin huɗubar

- Cusa imani da Allah da ranar lahira a zukata.
- Umarni a kan ayyukan ƙwarai da ribatar lokaci
- Faɗakar da mutane dangane da kusantowar alƙiyama.
- Jan-kunne game da fitintinu da kuma hanyoyin kauce musu.
- Bayanin wasu daga cikin alamomin tashin ƙiyama.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammadu bawansa ne manzonsa ne. (Yaku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron Allah yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Yaku waɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammadu (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (a addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta".

Bayan haka:

Ya ku musulmai! Matashiyar maganarmu a yau, tana da girma, magana ce da ta shafi gaibu, wato maganna a kan alamomin tashin ƙiyama. Allah yana cewa,

﴿ فَهَلۡ يَنظُرُونَ إِلَّا ٱلسَّاعَةَ أَن تَأۡتِيَهُم بَغۡتَةٗۖ فَقَدۡ جَآءَ أَشۡرَاطُهَاۚ فَأَنَّىٰ لَهُمۡ إِذَا جَآءَتۡهُمۡ ذِكۡرَىٰهُمۡ ١٨ ﴾ [محمد: ١٨].

(Ba komai suke suke jira ba, face sa'a ta zo musu babu zato, babu tsammani. Haƙiƙa alamominta sun riga sun zo, to yaya za su yi idan wa'azinta ya zo musu?).

A cikin hadisin Jibril, sananne, wanda Imam Muslim ya rawaito, yana cewa, "Ka ba ni labari a kan imani." Sai ya ce, "Imani shi ne, ka bayar da gaskiya ga Allah da mala'ikunsa da littattafansa da manzanninsa da ranar ƙarshe, kuma ka ba da gaskiya da ƙaddara, mai daɗi da mara daɗi."

An karɓo daga Huzaifa bin Usaid, ya ce, “Wata rana mun kasance muna zaune, muna hira a inuwar wani ɗaki na Manzon Allah (ﷺ), sai muka ambaci sa’a, sai muryoyinmu suka ɗaukaka, sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Alƙiyama ba za ta kasance ba, ko ba za ta tsaya ba, har sai alamomi guda goma sun kasance gabaninta….” har zuwa ƙarshen hadisin. [Abu Dawud ya ruwaito].

Sanin lokacin tashin ƙiyama na daga cikin abin da Allah ya bar wa kansa sani. Allah yana cewa,

﴿ يَسۡـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلسَّاعَةِ أَيَّانَ مُرۡسَىٰهَاۖ قُلۡ إِنَّمَا عِلۡمُهَا عِندَ رَبِّيۖ لَا يُجَلِّيهَا لِوَقۡتِهَآ إِلَّا هُوَۚ ثَقُلَتۡ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ لَا تَأۡتِيكُمۡ إِلَّا بَغۡتَةٗۗ يَسۡـَٔلُونَكَ كَأَنَّكَ حَفِيٌّ عَنۡهَاۖ قُلۡ إِنَّمَا عِلۡمُهَا عِندَ ٱللَّهِ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعۡلَمُونَ ١٨٧ ﴾ [الأعراف: ١٨٧].

(Suna tambayar ka game game lokacin tashin ƙiyama. Yaushe ne za ta tsaya? Ka ce, “Iliminta na wurin Ubangijina, babu wanda yake bayyana da lokacinta, sai shi. Ta nauyaya a sama da ƙasa, ba za ta zo muku ba, face babu zato, babu tsammani. Suna tambayar ka, kamar kai masani ne gare ta. Ka ce, “Kaɗai dai, saninta na wurin Allah, sai dai da yawa mutane ba su sani ba).

Kuma ya ce,

﴿ يَسۡـَٔلُكَ ٱلنَّاسُ عَنِ ٱلسَّاعَةِۖ قُلۡ إِنَّمَا عِلۡمُهَا عِندَ ٱللَّهِۚ وَمَا يُدۡرِيكَ لَعَلَّ ٱلسَّاعَةَ تَكُونُ قَرِيبًا ٦٣ ﴾ [الأحزاب: ٦٣].

(Mutane suna tambayar ka game da alƙiyama. Ka ce, “Saninta na wajen Allah. Me ya sanar da kai, wata ƙila sa’a za ta zama kusa?) .

Kuma ya ce,

﴿ يَسۡـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلسَّاعَةِ أَيَّانَ مُرۡسَىٰهَا ٤٢ فِيمَ أَنتَ مِن ذِكۡرَىٰهَآ ٤٣ إِلَىٰ رَبِّكَ مُنتَهَىٰهَآ ٤٤ ﴾ [النازعات: ٤٢ – ٤٤].

(Suna tambayar ka game da sa’a, yaushe ne za ta tsaya? Me ya haɗa ka da zmbaton ta? Zuwa ga Ubangijinka matuƙarta take).

Kuma yayin da mala’ika Jibrilu ya tambayi Manzon Allah (ﷺ) lokacin tashin ƙiyama, sai ya ce, “Wanda ake tambaya a kanta, bai fi mai tambayar sani ba.” [Muslim ya rawaito shi].

Ibni Rajab, Allah ya ji ƙan sa yana cewa, "Abin da yake nufi, ilimin halitta baki ɗaya kan lokacin sa’a ɗaya yake, abin da yake nuna Allah ne ya keɓanta da sanin lokacinta".

Imamu Ahmad ya rawaito hadisi daga Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Ranar da aka yi isra’i da ni, na haɗu da Ibrahim da Musa da Isa, sai suka ambaci tashin ƙiyama, sai suka mayar da lamarinsu ga Ibrahim. Sai ya ce, “Ba ni da masaniya a kanta.” Sai suka mayar da lamari ga Musa. Sai ya ce, “Ba ni da sani a kanta.” Sai suka mayar da lamari ga Isa. Sai ya ce, “Amma lokacin aukuwarta, babu wanda ya san haka, sai Allah. Kuma yana cikin abin da Allah ya yi mini alƙawari, cewa Dujal zai fito tare da ni, akwai sanduna guda biyu, idan ya gani, sai ya narke, kamar yadda dalma take narkewa.” Ya ce, “Sai Allah ya halakar da shi.”

Haƙiƙa ayoyin Alƙur’ani da hadisan Ma’aiki sun yi nuni a kan ƙarantuwar sa’a da kusancinta. Allah yana cewa,

﴿ ٱقۡتَرَبَ لِلنَّاسِ حِسَابُهُمۡ وَهُمۡ فِي غَفۡلَةٖ مُّعۡرِضُونَ ١ ﴾ [الأنبياء: ١].

(Hisabin mutane ya kusa, su suna cikin gafala, suna ba da baya).

Kuma Ubangiji ya ce,

﴿وَمَا يُدۡرِيكَ لَعَلَّ ٱلسَّاعَةَ تَكُونُ قَرِيبًا ٦٣﴾ [الأحزاب: ٦٣].

(Me ya sanar da kai cewa wata ƙila sa'a ta kasance kusa?).

Kuma Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "An aiko ni, alhali ni da sa'a muna kamar haka." Ya yi nuni da yatsunsa, yana miƙe su. [Bukhari da Muslim suka rawaito shi]

Haƙiƙa alamomin tashin ƙiyama sun rabu guda biyu: Kanana da manya. Kanana su ne wanda za su zo tsawon lokaci, kafin tashin ƙiyama, kuma za su zamo cikin abin da aka saba da shi a rayuwa, yau da kullum. Wasu daga cikin ƙananan, za su iya bayyana tare da manyan alamomin, ko bayan bayyanarsu. Su kuwa manyan, su ne alamu, wanda za su bayyana dab da sa'a, kuma abubuwa ne da ba a saba da su ba a rayuwa: Kamar bayyanar Dujal, da makamancin haka. Amma ta fuskar bayyanarsu, iri uku ne: Na ɗaya, wanda sun bayyana, sun wuce; na biyu, sun bayyana, kuma suna ta haɓaka; na uku, wanda har yanzu ba su bayyana ba. Daga cikin ƙananan alamomin, akwai aiko Manzon Allah (ﷺ), saboda hadisin Sahl (RA) ya ce, "An aiko ni, ni da sa'a, muna kamar haka." yana nuni da yatsunsa, yana miƙe su. [Bukari da Muslim suka ruwaito].

Kuma haka mutuwarsa, saboda hadisin Auf bin Malik (RA), ya ce, "Ka lissafa abubuwa guda shida a gabanin sa'a: Na farko, mutuwata." Sannan ya ambaci sauran. [Bukhari ya rawaito shi]. Da mutuwarsa ne wahayi ya yanke. Kamar yadda Ummu Aiman ta faɗawa Abubakar da Umar cikin amsar da ta ba su lokacin da suka ziyarce ta a gidanta bayan mutuwar Annabi. (ﷺ) [Muslim ne ya ruwaito].

Daga ciki alamomin alƙiyama, akwai bayyanar fitintinu masu girma, wanda ƙarya za ta cuɗanya da gaskiya, imani ya riƙa reto a cikin zukata, mutum ya wayi gari yana musulmi, kafin rana ta faɗi, ya kafirta. Abu Musa ya rawaito cewa, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Gabanin sa'a, akwai fitintinu, kamar yankin dare mai duhu. Mutum zai wayi gari a cikinsu, yana mumini, amma yamma ta yi, ya zama kafiri, ko kuma da yamma yana mumini, ya wayi gari ya zama kafiri.". [Ahmad da Abu Dawud da Ibn Majah ne suka ruwaito].

Yana daga cikin alamomin, bayyanar wata wuta a yankin Hijaz (Makka da Madina). Abu Huraira ya rawaito, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Sa'a ba za ta tsaya ba, har sai wuta ta fito a yankin Hijaz wacce za ta haskaka wuyayukan raƙuma a Busra." [Muslim ya rawaito shi]. Kuma wannan wuta ta bayyana a tsakiyar ƙarni na bakwai, a shekara ta 654. Wuta ce gagaruma, malamai da suka ga zamaninta, sun kawo labarinta, kamar yadda Ibn Kasir ya yi a cikin littafinsa Al-Bidaayah Wan-Nihaayah.

Yana daga cikin alamomin, tozarta amana. An karɓo daga Abu Huraira, ya ce Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Idan aka tozarta amana, ka jira sa'a." [Bukhari ya rawaito shi]

Allah ya albarkance mu, ni da ku, cikin Alƙur'ani mai girma, kuma ya amfane mu, ni da ku, da abin da yake cikinsa na ayoyi da wa'azi mai azanci. Shi majiɓincin haka ne, kuma mai iko a kan haka.

Godiya ta tabbata ga Allah, Ubangiji talikai. Tsira da aminci su tabbata ga Manzon Allah (ﷺ).

Bayan haka, ya ‘yan uwa! Yana daga cikin alamomin sa’a ƙanana, yaɗuwar neman mata da fitsara. Manzon Allah (ﷺ) yana cewa, “Na rantse da wanda raina yake hannunsa (Allah), wannan al’umma ba za ta ƙare ba, har sai mutum ya shimfiɗe mace a kan hanya (zai yi lalata da ita), zaɓaɓɓun cikinsu a wannan lokaci, shi ne wanda zai ce, “Ina ma ka sa ta a bayan katanga.” [Abu Ya’ala ya rawaito shi].

Yana daga cikin alamominta, kisfe ƙasa da rikiɗa halitta da jifa. Kuma yana daga ciki, baiwa ta haifi uwar gijiyarta; ka ga mutane marasa takalmi, talakawa, suna gasar gina gidaje masu tsawo. An karɓo daga Sahl ibn Sa’ad cewa, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “A ƙarshen zamani, za a samu kisfe ƙasa, da jifa, da rikiɗa halitta.” Sai aka ce, “Yaushe hakan zai faru, ya Ma’aikin Allah?” Sai ya ce, “Idan dai kaɗa-kaɗe suka bayyana, da 'yan mata masu waƙe-waƙe”. [Tabarani ya rawaito shi].

A cikin hadisin Jibril shahararren nan, ya ce, “Ka ba ni labarin alamominta.” Sai ya ce, “Baiwa ta haifi uwargidanta, ka ga marasa takalmi, masu tafiya tsirara, talakawa, masu kiwon awaki, suna gasar gina dogayen benaye” [Muslim ne ya rawaito shi].

Yana daga cikin alamomin, bayyanar ƙarya, da kusancin kasuwanni. An karɓo daga Abu Huraira (RA) ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Sa’a ba za ta tsaya ba, har sai fitintinu sun bayyana, ƙarya ta yawaita, kuma kasuwanni su yi kusanci da juna.” [Imam Ahmad ya rawaito shi]

Ya ku ‘yan uwa musulmai! Waɗannan kaɗan kenan daga alamomin tashin ƙiyama ƙanana. Amma manyan su ne, wanda bayansu za a yi tashin ƙiyama. Daga ciki, akwai fitowar Yajuju da Majuju. Allah yana cewa,

﴿ حَتَّىٰٓ إِذَا فُتِحَتۡ يَأۡجُوجُ وَمَأۡجُوجُ وَهُم مِّن كُلِّ حَدَبٖ يَنسِلُونَ ٩٦ ﴾ [الأنبياء: ٩٦].

(Har sai sanda aka buɗe Yajuju da Majuju, alhali suna ta gangarowa daga kowane tudu(.

Daga ciki kuma, akwai fitowar dabba daga ƙasa, wadda za ta riƙa yi wa mutane magana. Allah ya ce,

﴿ وَإِذَا وَقَعَ ٱلۡقَوۡلُ عَلَيۡهِمۡ أَخۡرَجۡنَا لَهُمۡ دَآبَّةٗ مِّنَ ٱلۡأَرۡضِ تُكَلِّمُهُمۡ أَنَّ ٱلنَّاسَ كَانُواْ بِـَٔايَٰتِنَا لَا يُوقِنُونَ ٨٢ ﴾ [النمل: ٨٢].

(Idan zance ya tabbata a kansu, sai mu fito musu da wata dabba daga ƙasa, tana yi musu magana, “Lallai mutane sun kasance ba sa sakankancewa da ayoyinmu.”).

An karɓo daga Huzaifa bn Usaid, ya ce, Manzon Allah (ﷺ) wata rana, ya leƙo daga ɗaki, alhali muna tattaunawa a kan tashin alƙiyama. Sai ya ce, “Alƙiyama ba za ta tsaya ba, har sai kun ga alamomi guda goma: Hudowar rana daga yamma, da Dujjal, da hayaƙi, da dabba, da yajuju da majuju, da fitowar Annabi Isa (AS), da kifar da ƙasa guda uku: kifarwa ta gabas, kifarwa ta yamma, da kifarwa ta tsibirin larabawa. Da wuta da za ta fito daga tsakiyar birnin Adn, za ta kora mutane zuwa

matattara, ta kwana da su, idan sun kwana, kuma ta yi ƙailula da su, idan sun yi ƙailula.” [Ibni Majah ya rawaito shi]

Ya ku bayin Allah! Waɗannan wasu kenan daga cikin alamomin tashin alƙiyama, ƙanana da manya. Shin mun shirya wa tashin alƙiyama? Me muka aikata, don tunkarar wannan rana mai tsoratarwa? Shin yanzu, ba ma koma zuwa ga Allah ba, mu nemi gafararsa?

﴿ أَلَمۡ يَأۡنِ لِلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَن تَخۡشَعَ قُلُوبُهُمۡ لِذِكۡرِ ٱللَّهِ وَمَا نَزَلَ مِنَ ٱلۡحَقِّ ﴾ [الحديد: ١٦].

(Har yanzu lokaci bai yi ba ga wanda suka ba da gaskiya, zukatansu su risina ga ambaton Allah, da abin da ya saukar na gaskiya?).

Ku sani, ya bayin Allah! Lallai aukuwar mafi yawan alamomin tashin ƙiyama ƙanana, yana nuna kusancin aukuwar manya, wanda idan suka auku, tashin alƙiyama ya zo. Don haka, ku ji tsoron Allah, ya bayin Allah, ku inganta ayyukanku, ku yi tanadi da ranar tashin alƙiyama, ku sani lallai sa’a tana nan tafe, babu kokwanto a cikinta.

Ya Ubangiji! Ka ɗaukaka musulunci da musulmai, ka ƙasƙantar da kafirci da kafirai, ka kuma rushe maƙiya addininka.

KAYAN MAYE DA TASIRINSU WAJEN LALATA SAMARI

Manufofin huɗubar

- Sanin cewa, hankali ni'ima ce, wajibi ne a gode wa Allah a kanta.
- Gargaɗin samari da su guji shan kayan maye waɗanda za su lalata musu rayuwarsu.
- Yaƙi da al'adar shan kayan maye tsakanin samari

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga shirrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammad bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammad (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Bayan haka:

Ya ku bayin Allah! Lalle Allah ya fifita ɗan-adam a kan dadama daga halittarsa, kamar yadda yake cewa,

﴿ وَلَقَدۡ كَرَّمۡنَا بَنِيٓ ءَادَمَ وَحَمَلۡنَٰهُمۡ فِي ٱلۡبَرِّ وَٱلۡبَحۡرِ وَرَزَقۡنَٰهُم مِّنَ ٱلطَّيِّبَٰتِ وَفَضَّلۡنَٰهُمۡ عَلَىٰ كَثِيرٖ مِّمَّنۡ خَلَقۡنَا تَفۡضِيلٗا ٧٠ ﴾ [الإسراء: ٧٠].

(Haƙiƙa mun karrama ɗan-adam, kuma mun ɗauke shi a kan tudu da cikin teku, kuma mmu azirta shi da kayan daɗi, kuma muka fifita shi a kan yawayawanci abin da muka halitta fifitawa ta sosai).

Allah ya fifita ɗan adam da abubuwa masu yawa, wadda ya ɗara halittu dadama da su. Allah ya fifita shi da hankali, da fahimta da tunani. Hankali ne mafi girman ni'ima da Allah ya yi wa ɗan-adam. Da hankali ne yake iya banbance tsakanin

alheri da sharri, da abu mai cutarwa da mai amfanarwa. Da hanakali ɗan adam zai yi rayuwa mai kyau, ya iya tafiyar da al'amuransa. Da shi ne yake shaƙatawa ya more rayuwarsa. Da hankali ne duk al'ummomi kan ci gaba a rayuwa.

Da zarar mutum ya rasa hankalinsa, to shi da dabbobi duk ɗaya babu bambanci. Ba ya da wani amfani, kuma ba zai amfana da komai ba. Zai ma zama kaya a kan danginsa da al'ummarsa.

To duk da tsadar da hankali yake da ita, za ka ga wani wanda shi bai damu da hankalinsa, ballanta ma ya yi ƙoƙarin ganin ya ba shi wata kariya ta musamman.

Kai har ma za ka ga da wanda zai sa ƙafarsa ya take hankalinsa, ya kama bin son zuciyarsa, kuma basirarsa ta makance.

Da zarar mutum mai hankali ya kwankwaɗi kofin giya, ko wani abu mai sa maye, ko ya shaƙi wata tabar mai bugarwa, to fa nan take zai lalubi hankalinsa ya rasa. To shi ke nan daga sannan ya zama dabba sanye da mutane. Sai kuma ya shiga duniyar laifuffuka da alfasha. Rayuwa kuma ta sakwarkwace, ya manta da Ubangijinsa, ya zalinci kansa, ya keta rigar mutuncinsa da hannunsa. Da zarar hankali ya ɓace to 'ya'yansa sun zama marayu, matarsa ta yi rashin miji. Da hake ne ya watsar da wani abu na lalurar rayuwa wanda duk wata sharɓi'a da Allah ya saukar da ita ta zo da wajabcin kiyaye shi, wanda shi ne hankali. Wanda duk ya sha abin maye har ya rasa hankalinsa, wannan ya cuci kansa, ya kuma cuci al'ummarsa, ya jefa su, ya kuma jefa addininsa cikin wulaƙanci. Zai kuma zama barazana ga zaman lafiyar al'umma.

Ya ku bayin Allah! Kayan maye sun gama rusa mutanen da suke da alaƙa da su. Sun jefa su cikin kurkuku shekaru aru-aru, sakamakon abin da suka jawo kansu na laifuffuka. 'yan'yansu da matansu suka zauna tamkar marayu. Ya lalata yarintasa da rayuwarsa ta hanyar amfani da makamin da maƙiyansa suka ba shi. Har aka wayi gari gidajen yari sun cika maƙil da irin waɗannan asararru.

Ya ku bayin Allah! Wasu wawaye marasa hankali sun ɗauko abin da maƙiya suka kawo musu, maɓarnata suke dillancinsa. Wallahi musifa ce kawai ta faɗa wa musulmi ba tare da sun ankara ba. Domin maƙiya sun gane ta ina za su shiga musulmi su yi musu illa. Allah ya yi gaskiya da ya ce,

﴿وَلَا يَزَالُونَ يُقَٰتِلُونَكُمۡ حَتَّىٰ يَرُدُّوكُمۡ عَن دِينِكُمۡ إِنِ ٱسۡتَطَٰعُواْۚ﴾ [البقرة: ٢١٧].

(Ba za su gushe ba suna yaƙar ku, har sai sun raba ku da addininku idan sun samu iko).

Babban abin mamaki shi ne, mutumin da zai sayi abin za raba shi da hankalinsa da kuɗinsa. Me ya sa wanda zai sha giya, ba zai wa'azuntu da wani wanda ya sha ta ta rusa masa rayuwarsa ba? Me ya sa wanda yake shan abin maye, ya yarda ya fitar da kansa daga tawagar masu hankali zuwa ƙungiyar mahaukata?!

Hasanul Basari yana cewa, «Da a ce ana sayar da hankali, da mutane sun sayar da shi da tsada».

Ayoyi da hadisai masu yawa sun zo don tabbatar da haramcin shan giya, kamar faɗar Allah da yake cewa,

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِنَّمَا ٱلۡخَمۡرُ وَٱلۡمَيۡسِرُ وَٱلۡأَنصَابُ وَٱلۡأَزۡلَٰمُ رِجۡسٞ مِّنۡ عَمَلِ ٱلشَّيۡطَٰنِ فَٱجۡتَنِبُوهُ لَعَلَّكُمۡ تُفۡلِحُونَ ٩٠ ﴾ [المائدة: ٩٠].

(Lalle kaɗai giya da caca da gumaka, da kibau na rantsuwa, duk daga aiki ne na sheɗan, don haka ku nisance shi, lalle za ku rabauta).

Kai su sahabbai ma ba wai kawai haramcinta suka fahimta ba kaɗai, a'a sun fahimci cewa an haɗa ta da shirka, wadda ita ce zunubin da ya fi kowa ne zunubi da ɗan adam zai saɓa wa Allah da shi.

An karɓo daga Ibn Abbas Allah ya yarda da shi, ya ce, «Yayin da haramcin giya ya sauko, sai sahabban Annabi (S.A.W.) suka tafi wajen junansu, suka ce, an haramta giya, kuma na sanya ta daidai da shirka). Ɗabrani ne ya ruwaito shi, da salsala ingantacciya.

Saboda Allah cewa ya yi, «ƙazanta ce daga aikin shaiɗan». Kuma dangane da shirka ya ce, «To ku nisanci ƙazanta ta gumaka».

Muslim ya ruwaito hadisi daga Abdurrahman bn Wa'ala ya ce, na tambayi Ibn Abbas game da sayar da giya? Sai ya ce, Manzon Allah (S.A.W.) ya kasance yana da wani aboki na ƙabilar Saƙif, ko kuma Daus. Sai ya gamu da Annabi (S.A.W.) a ranar buɗe Makka, yana ɗauko wata gora ta giya don bawa Annabi kyauta. Sai Manzon Allah (S.A.W.) ya ce, «Wane, ba ka san Allah ya haramta giya ba?» Sai mutumin nan ya cewa yaronsa: Tafi ka sayar da ita. Sai Manzon Allah (S.A.W.) ya ce, «Da me ka umarce shi?» Sai ya ce, Na umarce shi ne ya sayar da ita ne. sai Manzon Allah ya ce, «Wanda ya haramta shanta shi ne kuma ya haramta sayar da ita». Sai ya sa aka je aka zubar da ita a bayan gari.

Daga cikin hadisan da suka bayyana haramcin giya, akwai hadisin da Manzon Allah (S.A.W.) yake cewa, «Babuwani da zai sha giya, kuma a karɓi sallarsa har tsawon kwana arba'in. Idan kuma ya mutu da ita a cikinsa, za a haramta masa Aljannah. Idan ya mutu a cikin kwana arba'in da shanta to ya mutu irin mutuwar jahiliyyah». Ɗabrani ne ya ruwaito shi da salsala mai kyau daga Abdullah bn Amr.

Wand duk ya sha giya a duniya, to Allah zai haramta ta masa shan ta lahira. Kamar yadda ya zo a hadisi na Abdullahi ɗan Umar, ya ce, Manzon Allah (S.A.W.) ya ce, «Wanda ya sha giya a duniya to ba zai sha ta lahira ba». Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.

An karɓo daga Ibn Umar (R.A.) ya ce, Manzon Allah (S.A.W.) «Allah ya la'anci giya, da mai shanta, da shayar da ita, da mai sayar da ita, da mai sayanta, da mai tace ta, da wanda yake sa wa a tace masa, da mai dakonta, da wanda ake masa dakonta». Abu Dawud ne da Ibn Majah suka ruwaito shi.

A musulunci an harmata duk wani abu mai sanya maye, kaɗan ɗinsa da mai yawa. Domin shan kaɗan shi yake jawo shan mai yawan. Sannan shan abin maye ya zame masa jiki. An karɓo daga Jabir, (R.A.) ya ce, Manzon Allah (S.A.W.) ya ce, «Duk abin mai yawansa zai sa maye, to kaɗan ɗinsa haramun ne». Abu Dawud ne da Nasa'i suka ruwaito shi.

Ya ku bayin Allah! Yana daga abin da ya kamata a ja kunne a kansa, tabar wiwi, da sauran abubuwan da suke raba mutum da hankalinsa, su raunana mutum su raunana masa duk wani kuzari. Shan irin waɗannan ƙazantattun abubuwa suna makantar da gani, su tushe basira, kuma ana ɗaukar duk wani mai shansu mutumin da ba adali ba, wanda bai san yadda zai tafiyar da lamuransa ba. Yana dariya barkatai babu dalili. Yana kuka ba tare da wani dalili ba. Za ka ga idanunsa suna walƙatawa kamar wanda ya ga mutuwa.

Kamar yadda maƙiya musulunci suke kawo kayan maye kala-kala, suka mayar da tamkar ƙawar haɗiya ta magani, alhalin suna ɗauke da sinadiri mai cutarwa kamar herawin. Duk wannan aiki ne na shaiɗan. Don haka ku nisance shi don ku samu rabauta.

Wannan shi ne abin da zan iya faɗa. Ina neman gafarar Allah ga kaina da ku bakiɗaya. Ku nemi gafararsa. Lalle shi mai yawan gafara ne mai jin-ƙai.

Huɗuba Ta Biyu

Yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah. Tsira da amincin Allah su tabbata ga mafi ɗaukakar Annabawa, annabinmu Muhammad da iyalan gidansa, da sahabbansa, da tabi'ai, da duk wani wanda ya bi hanyarsa da kyautatawa har zuwa ranar sakamako. Bayan haka:

Ya bayin Allah! Lalle kayan maye sun cutarwa ƙwarai a addini, kamar yadda Allah yake cewa,

﴿ إِنَّمَا يُرِيدُ ٱلشَّيۡطَٰنُ أَن يُوقِعَ بَيۡنَكُمُ ٱلۡعَدَٰوَةَ وَٱلۡبَغۡضَآءَ فِي ٱلۡخَمۡرِ وَٱلۡمَيۡسِرِ وَيَصُدَّكُمۡ عَن ذِكۡرِ ٱللَّهِ وَعَنِ ٱلصَّلَوٰةِۖ فَهَلۡ أَنتُم مُّنتَهُونَ ٩١ ﴾ [المائدة: ١٩].

(Kaɗai shedanne yake son ya jefa adawa da ƙiyayya tsakaninku ta hanyar giya da caca, kuma ya hana ku ambaton Allah. To ko za ku hanu).

Kayan maye suna hana sallah, ga shi kuwa ita ce ginshiƙin addini, kuma suna hana ambaton Allah. Kuma mai shan su yana tare da shaiɗanu. Duk wani wanda ya saba shan giya sai ka gan shi ba ya iya ayyukan ɗa'a. Yana ganin wahalarsu a kansa. Zuciyarsa ba ta tare da alheri sam-sam. Sannan kuma ka same shi mai son aikata haramun ne, koda yaushe, domin zuciyarsa ta riga ta runu da waɗannan kayan ƙazamtar. Don haka koda yaushe addinin a cikin raguwa yake, al'amarunsa ƙara taɓarɓarewa suke.

Ya ku bayin Allah! Yana daga cikin cututtukan kayan maye cewa, su suna dakusar da ƙwaƙwalwa. Tana mayar da mutum su-su-su, kuma ya zamana ba ya zama ba ya gani sosai. Sannan ya riƙa tangaɗi idan yana tafiya. Zuciyarsa ta daina bugawa yadda ya kamata, sukan sa jijiyoyinsa su ɗaɗɗaure, yakan iya samun shanyewar wani ɓangaren jikinsa, jininsa ya daina gudana yadda ya kamata. Kamar yadda zai zama kullum cikin tsoro da damuwa. Duk sanda ya ji wani motsi sai ya firgita. Ta ko ina tsoro ne kewaye da shi, yana jin tsoran ƙarshen lamarinsa, da cututtukan da za su iya auka masa.

Babu ruwansa da duk wani halin ƙwarai. Yana aikata duk wani laifi. Sau nawa ne ake aukawa manya-manyan laifuffuka saboda kayen maye da aka sha. Sau tari an aukawa ayyukan alfasha da saɓon Allah saboda shan abin da ya bige hankali. A lokuta dadama an ketawa wasu rigar mutuncinsu, an sace dukiyoyin wasu, an samu miyagun haɗurra a kan hanyoyi, duk saboda shaye-shayen kayen maye.

Ya ku bayin Allah!Maƙiya Allah ba za su taɓa saurarawa wani mumini ba, za su yi ta yin fafutukar ganin sun rushe al'ummar muslmi, sun rushe halayyar samari. Don haka suka mai da ƙoƙarinsu da himmarsu wajen su ga sun sauwaƙe samun kayan maye, ta yadda yara ma za su iya samusu. Wannan ya taimaka wajen yaɗuwarsu cikin samarin musulmi, har ta kai wasu an shigar da su asibitin mahaukata, wasu kuma an kai su gidajen yari.

Ya ku iyaye, akwai nauyi babba a kanku dangane da wannan lamari. Don haka ku sanya wa 'ya'yanku idanu, ku riƙa yi musu addua'a ta gari da ikhlasi da kykkyawar niyya, domin Allah ya tsare mu gabaɗaya daga wannan gubar mai rushe rayuwa. Don haka, sai mun taimakawa juna domin yaƙar wannan annoba.

Allah yana cewa,

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ قُوٓاْ أَنفُسَكُمۡ وَأَهۡلِيكُمۡ نَارٗا وَقُودُهَا ٱلنَّاسُ وَٱلۡحِجَارَةُ عَلَيۡهَا مَلَٰٓئِكَةٌ غِلَاظٞ شِدَادٞ لَّا يَعۡصُونَ ٱللَّهَ مَآ أَمَرَهُمۡ وَيَفۡعَلُونَ مَا يُؤۡمَرُونَ ٦ ﴾ [التحريم: ١].

(Ya ku waɗanda suka imani, ku tsare kawukanku da iyalanku daga wuta, mutane da duwatsu ne makamashinta. Masu gadinta mala'iku ne masu kausasan zukata, masu ƙarfi, ba sa saɓawa Allah abin da ya umarce su, suna aikata abin da aka umarce su da shi).

HUƊUBAR SABUWAR SHEKARA

Manufofin huɗubar

- Bayanin saurin sheɗuwar shekaru da lokaci.
- Bayanin abin da yake wajaba a kan bawa game da hakan.
- Wajabcin yi wa kai hisabi, da kuma gaggauta tuba.
- Kwaɗaitarwa a kan ga amfani dd lokaci ta hanyar ayyukan ɗa'a

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga shirrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammad bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammad (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Bayan haka:

Ya ku bayin Allah! A wannan rana muna bankwana da wata shekara, wadda ta riga ta tattara komatsenta. Ba wani abu ne ya rage ba, sai 'yan awanni kaɗan ne suka rage mana mu shiga sabuwar shekara, wadda za ta buɗe sabon shafinta. To, me muka shuka wa kanmu kwanakin shekarar da ta wuce, kuma da wane abu ne muka cika shekarar, kuma da me za mu tunkari ita wannan sabuwar shekarar? Wadda ga ta nan dai, ba mu sani ba, shin za mu cikashe, ko kuma za mu kasance daga waɗanda suke tafiya zuwa lahira. Dole mu yi wa kawunanmu hisabi. Idan har mun yi ayyuka na ƙwarai a kwanakin shekararmu da ta wuce, to sai mu godewa Allah. Idan kuma wasa da shirme muka yi, da rashin biyayya ga Allah, to sai mu sauya tunaninmu kuma mu tuba zuwa ga Allah, tuba wadda take ta gaskiya. Domin mafi alherin abin da za mu dinga cika shekarunmu da shi, shi ne mu dinga tuba zuwa ga Allah Ta'ala, a kan abubuwan da muka yi sakaci a kansu na rashin ɗa'a ga Allah, ko kuma zunuban da muka aikata. Kuma mu godewa Allah da Ya

ba mu damar gyara kurakuranmu.

Daga Abi Huraira (R.A), lallai Manzon Allah (ﷺ), ya ce: “Kada ɗayanku ya yi burin mutuwa, ko dai mai ayyukan kyautatawa ne, watakila zai ƙara, ko kuma mai ayyukan munanawa ne, watakila zai tuba. Bukhari ne ya rawaito shi, kuma wannan lafizin nasa ne, da Muslim.

Ya ku musulmai! Lallai darare da ranaku wasu taskoki ne na adana ayyuka. Sukan tsufar da sabon abu, kuma su matso da na nesa kusa. Kwanaki suna shuɗewa, kuma shekaru suna maimaituwa, kuma mutane suna ta ƙara komawa zuwa ga Allah. Wani ya yi gaba wani ya yi baya. Wancan mara lafiya. Kuma kowanne yana komawa ne zuwa ga Allah. Haƙiƙa, Maɗaukakin Sarki, ya ratse da wannan zamanin, wanda ya ara mana da cewa, lallai mutum yana cikin asara, sai fa wanda ya siffatu da abubuwa huɗu: waɗanda suka yi imani, suka yi ayyukan ƙwarai, suka yi wasiyya da gaskiya, kuma suka yi wasiyya da haƙuri. Ubangiji Mai ɗaukaka Yana cewa:

﴿ وَٱلۡعَصۡرِ ۝١ إِنَّ ٱلۡإِنسَٰنَ لَفِي خُسۡرٍ ۝٢ إِلَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَتَوَاصَوۡاْ بِٱلۡحَقِّ وَتَوَاصَوۡاْ بِٱلصَّبۡرِ ۝٣ ﴾ [العصر: ١ – ٣].

Ma’ana: (Ina rantsuwa da zamani! Lallai ɗan’adam yana cikin asara. Sai dai waɗanda suka yi imani, suka aikata ayyukan ƙwarai, suka yi (wa juna) wasiyya da gaskiya, suka yi wasiyya da haƙuri).

Wannan sura mai girma, Imam Shafi’i yana faɗa dangane da ita cewa, “Da ba a saukar da wata sura ba sai wannan, da ta ishi mutane.”

Ya kai masoyi, ka yi duba zuwa ga shafukan rayuwarka da ta shuɗe, mai ka aje a cikinsu domin lahirarka? Ka yi tunani a ranka,: me wannan harshe naka ya faɗa? Me kuma idanunka suka kalla? Kunnen nan nak me ya ji? Kuma waɗannan ƙafafuwan naka ina suka je? Ya hannu! Me kika taɓa? Abin da ake buƙata a gurinka shi ne ka riƙe linzamin rayuwarka da kanka. Ka yi wa kanka hisabi. Maimun ɗan Mihran yana cewa: “Bawa ba zai zama haƙiƙanin mai tsoron Allah ba, har sai ya zama mai bibiyar kansa ƙeƙe-da-ƙeƙe sama da yadda ɗan kasuwa yake bin ƙwaƙƙwafin abokin kasuwancinsa”

Don haka dole mu yi wa kanmu hisabi a kan farillai. Kuma mu yi wa kanmu hisabi a kan abubuwan da aka hana. Gamu a kan dokin dare-da-rana yana famar tiƙar gudu damu zuwa lahira. Abud Darda’i ya ji wani mutum yana tambaya game da wata jana’iza da ta wuce: mutumin ya ce wanene wannan? Sai Abud Darda, ya ce, «Ai kai ne».

A yayin da aka tambayi Abu Hazim: Yaya zuwa wajen Allah yake? Sai ya ce, «Amma shi mai ɗa’a, kamar matafiyi ne ya dawo ga iyalansa. Shi kuwa mai saɓo, kamar a dawo da gujajjen bawa ne ga ubangidansa».

Ku dage da ƙoƙari ya ku masoya, tun daga yanzu. Domin su ayyuka ƙwarai, suna amfani ne idan mutum ya cika da su. Kada ya zo yana cewa:

﴿ قَالَ رَبِّ ٱرۡجِعُونِ ۝٩٩ لَعَلِّيٓ أَعۡمَلُ صَٰلِحٗا فِيمَا تَرَكۡتُ كَلَّآۚ إِنَّهَا كَلِمَةٌ هُوَ قَآئِلُهَاۖ وَمِن وَرَآئِهِم بَرۡزَخٌ إِلَىٰ يَوۡمِ يُبۡعَثُونَ ۝١٠٠ ﴾ [المؤمنون: ٩٩ – ١٠٠].

“Ya ce, “Ya Ubangijina ka mayar da ni (duniya). Ko na aikata aiki na ƙwarai a cikin abin da na bari. Kayya! Lallai ne ita kalma ce, shi ne mai faɗinta, alhali kuwa

a baya gare su akwai wani shamaki har ranar da za a tayar da su.”

Ya ku masoya! Ku ribaci shekarunku, kar ku ɓata su da aikata abubuwan da ba su da amfani, da gafala. Ku ribaci kwanaki ƙarfi, ku ƙara ƙaimi wajen ayyuka na ƙwarai. Domin dare da rana suna aiki a kanku, to kuma ku yi aiki akansu kamar yadda suke yi. Haka Umar ɗan Abdul’aziz ya faɗa.

Haka nan, ku nutsu ku duba kimar lokaci, kar ku ɓata lokacinku akan abin da ba ɗa’ar Allah ba. Domin faufau, ba gami tsakanin wanda ya zauna a wani guri yana ambaton Allah, da wanda ya zauna a wani wuri yana ɓata lokacinsa da zantukan shirme waɗanda ba za su amfanar da shi ba. Ko kuma mai saɓon da zai dulmiyar da shi a cikin Jahannama. Malam Ibn Kasir yana cewa a wajen faɗin Allah Ta’ala:

﴿ وَهُوَ ٱلَّذِى جَعَلَ ٱلَّيۡلَ وَٱلنَّهَارَ خِلۡفَةً لِّمَنۡ أَرَادَ أَن يَذَّكَّرَ أَوۡ أَرَادَ شُكُورٗا ٦٢ ﴾ [الفرقان: ٦٢].

Ma’ana: (Kuma shi ne wanda ya sanya dare da yini masu maye gurbin juna, ga wanda yake son ya yi tunani, ko kuwa ya yi nufin ya gode).

Malam Ibn Kasir ya ce,: “Kowane ɗaya daga cikinsu yana maye gurbin abokinsa, suna tare ba sa gajiya, idan wannan ya tafi, sai wancan ya zo. An sanya su suna bibiyar juna domin su zama lokacin bautar bayi ga Ubangiji. Duk wanda wani aiki ya kuɓuce masa da daddare, sai ya yi shi da rana. Wanda kuma ya kuɓuce masa da rana, sai ya yi shi da daddare” .

Ya ku bayin Allah ku sani cewa, dare da yini wasu ababan hawa ne, da suke nisanta ka da duniya kuma suke kusantar da kai zuwa lahira. Farin ciki ya tabbata ga bawan da ya amfani shekarunsa.

﴿ يُقَلِّبُ ٱللَّهُ ٱلَّيۡلَ وَٱلنَّهَارَۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَعِبۡرَةٗ لِّأُوْلِي ٱلۡأَبۡصَٰرِ ٤٤ ﴾ [النور: ٤٤].

(Allah yana juyar da dare da yini. Lallai a cikin wannan akwai abin kula ga ma’abota gannai).

Kullum muna ganin shekaru suna zuwa su shuɗe. Idan wannan shekara ta zo ta wuce, sannan muka shiga sabuwa, sai mu riƙa ganinta da tsawo, nan da nan sai ta zo ita ma ta wuce. Abdullahi ɗan Umar ya ce: “Manzon Allah (ﷺ) ya riƙe kafaɗata, sai ya ce: “Ka zama a duniya kamar kai baƙo ne, ko matafiyi.”

Don haka kada mumini ya saki jiki da duniya, kuma kada ya nutsu da ita, domin shi mutum a kan hanya yake, dole ne ya shirya kansa domin wannan tafiyar.

Ya kai ɗan’uwana Musulmi! Farkon shekara nan dole kowa ya tsaya tsayin daka ya bin ciki kansa ya kuma gyara hanyar gudanar da rayuwarsa, da kuma gusar da kurakurai, da komawa zuwa ga hanyar daidai. Domin komawa kan gaskiya ya fi dagewa akan ƙarya. Kada ka riƙa kallon yawon laifuffukanka ka ɗauka Allah ba zai gafarta maka ba. Kada tsofaffin kurakuranka su hana ka tuba ta gaskiya ga Allah. Ubangijin Ta'ala yana cewa, a lokacin da yake magana da masu manyan laifuka da kurakurai, waɗanda suka cuci kansu. Yana cewa:

﴿ قُلۡ يَٰعِبَادِيَ ٱلَّذِينَ أَسۡرَفُواْ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمۡ لَا تَقۡنَطُواْ مِن رَّحۡمَةِ ٱللَّهِۚ إِنَّ ٱللَّهَ يَغۡفِرُ ٱلذُّنُوبَ جَمِيعًاۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلۡغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ٥٣ ﴾ [الزمر: ٥٣].

(Ka ce (Allah ya ce) “Ya ku bayina waɗanda suka cutar da kansu da soɓo, kada ku yanke ƙauna daga rahamar Allah. Lallai Allah yana gafarta zunubai gabaɗaya. Lallai shi, shi ne mai gafara, mai jin ƙai). To me za mu yi? Sai Ya ce:

﴿ وَأَنِيبُوٓاْ إِلَىٰ رَبِّكُمۡ وَأَسۡلِمُواْ لَهُۥ مِن قَبۡلِ أَن يَأۡتِيَكُمُ ٱلۡعَذَابُ ثُمَّ لَا تُنصَرُونَ ٥٤ وَٱتَّبِعُوٓاْ

﴿ أَحۡسَنَ مَآ أُنزِلَ إِلَيۡكُم مِّن رَّبِّكُم مِّن قَبۡلِ أَن يَأۡتِيَكُمُ ٱلۡعَذَابُ بَغۡتَةٗ وَأَنتُمۡ لَا تَشۡعُرُونَ ٥٥ ﴾ [الزمر: ٥٤ – ٥٥].

(Kuma ku mayar da al'amari zuwa ga Ubangijinku, kuma sallama masa, tun kafin azaba ta zo muku, sannan kuwa ba za a taimake ku ba. Kuma ku bi mafi kyawun abin da aka saukar muku daga Ubangijinku, tun kafin azaba ta zo muku bagatatan, kuma ku ba ku sani ba).

Wace irin azaba ce za ta zo maka kwatsam, ba tare da ka shirya ba, idan har kana saɓawa Allah? Ita ce mutuwa! Shin mutuwa tana turo da saƙon sanarwa ne kafin zuwanta? A'a! Yanzu mutun zai hau motarsa da ƙafafuns, Amma bayan jima kaɗan sai ka gan shi ana saukar da gawarsa! Kuma mutum zai sa kayansa da kansa, amma ba zai cire su da kansa ba, wataƙil sai an sa almakashi an yanke masa su. Wannan shi ne ma'anar faɗin Allah:

﴿ أَن تَقُولَ نَفۡسٞ يَٰحَسۡرَتَىٰ عَلَىٰ مَا فَرَّطتُ فِي جَنۢبِ ٱللَّهِ وَإِن كُنتُ لَمِنَ ٱلسَّٰخِرِينَ ٥٦ أَوۡ تَقُولَ لَوۡ أَنَّ ٱللَّهَ هَدَىٰنِي لَكُنتُ مِنَ ٱلۡمُتَّقِينَ ٥٧ أَوۡ تَقُولَ حِينَ تَرَى ٱلۡعَذَابَ لَوۡ أَنَّ لِي كَرَّةٗ فَأَكُونَ مِنَ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ٥٨ ﴾ [الزمر: ٥٦ – ٥٨].

(Kada wani rai ya ce: "Ya nadamata a kan abin a na yi sakaci akan sha'anin Allah kuma lallai na kasance haƙiƙa daga masu izgili. Ko kuma (kada) ya ce "Da Allah Ya shiryar da ni, da na kasance daga masu taƙawa. Ko kuma (kada) ya ce a lokacin da yake ganin azaba, "Da lallai a ce ina da wata komawa (zuwa duniya) domin in kasance daga masu kyautatawa).

Allah ya nuna ƙarya yake, don haka ya ce,

﴿ بَلَىٰ قَدۡ جَآءَتۡكَ ءَايَٰتِي فَكَذَّبۡتَ بِهَا وَٱسۡتَكۡبَرۡتَ وَكُنتَ مِنَ ٱلۡكَٰفِرِينَ ٥٩ ﴾ [الزمر: ٥٩].

(Na'am! Lallai ayoyina sun je maka, sai ka ƙaryata su, kuma ka yi girman kai, kuma ka kasance daga kafirai).

Kada saɓon Allah ya hana ka tuba, ka riƙa cewa, wallahi ni mai zunubi ne da yawa! To idan kamai yai mai yawon saɓo ne, to shi kuma Allah Mai yawan gafara ne.

Kana cewa zunubaina manya-manya ne. To gafarar Allah ta fi zunubanka girma. Da a ce zunubanka za su yi tsiri har su taɓo samaniya, sannan ka haɗu da Allah kana mai neman gafararSa, Zai gafarta ma. Da zunubanka za su kasance kamar kumfar kogi, ko kamar yawan yashi, ko kuma kamar yawan ruwan sama, to rahamar Allah ta fi haka faɗi. Allah yana cewa:

﴿ وَرَحۡمَتِي وَسِعَتۡ كُلَّ شَيۡءٖ ﴾ [الأعراف: ١٥٦].

"Kuma rahamata ta yalwaci dukkan komai..."

Kawai ka sauya! Wannan shi ne abin da ake son ka yi. Duk abin da ya wuce, Allah Zai gafarta maka shi, duk yawansa da nauyinsa da girman laifin da ke cikinsa. Duk wannan sai Allah Ya sauya maka shi zuwa kyawawan aiki. Shin ana samun abin da ya fi wannan ya ɗan'uwana? Wace falala ce ta fi wannan girma?

Har ila yau, bayan Allah Ya yafe maka, sai kuma Ya yi farin ciki da kai. Ya zo a cikin hadisi a Sahihil Bukhari, Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: "Lallai Allah ya fi tsananin farin ciki ga tuban bawansa, sama da mutumin da ya kasance a wata dokar daji – yana cikin halin tafiya, yana tare da abin hawansa, kuma guzurinsa da ruwansa yana kanta, sai ta ɓace masa. Ya neme ta ya rasa. A yayin da ya yanke

ƙauna ba zai ganta ba, sai ya sallamawa mutuwa. Sai ya zo ƙarƙashin wata bishiya, ya zauna yana jiran mutuwa a yayin da yake cikin barci yana jiran mutuwa, sai ga taguwarsa nan, tana dawowa, kuma ta tsaya a gabansa. A yayin da ya buɗe idanunsa sai ya same ta, sai farin cikin ya rufe shi, saboda tsabar farin ciki sai ya ce: ya Allah kai ne bawana, ni ne Ubangijinka." Bai ma san me yake faɗa ba, don haka sai ya yi kuskure saboda tsabar farin ciki.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah, Ubangijin talikai. Tsira da amincin Allah su tabbata ga fiyayyen halitta Annabinmu Muhammad da alayensa da sahabbansa da waɗanda suka bi tafarkinsu har zuwa tashin ƙiyama. Bayan haka:

Ya kai ɗan'uwana, Lallai gyara duk wata kantara daga gare ka, bayan yi wa kai hisabi, gyara ne ga rayuwarka. Kuma wata babbar dama ce mai inganci wajen gyara kanka da kanka. Kuma wannan ba yana nufin mutum ya haɗa ayyukan kirki a tsakiyar ayyukan ɓarna ba, wannan abu ne wanda yake bai dace ba.

Lallai komawa zuwa ga Allah, tana buƙatarka da ka ƙara tsarin rayuwarka gabaɗayanta. Kuma ka sake ƙulla alaƙa tsakaninka da Ubangijinka alaƙa cikakkiya mai nagarta, kuma da aiki cikakke. Kuma Maɗaukakin Sarki yana kiranka zuwa ga samun wannan ta hanyar shugaban Istigfari. Ya zo a cikin Sahihil Bukhari da Muslim daga hadisin Bara'u ɗan Azib, Allah ya yarda da shi, ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Bana nuna maka shugaban Istigfari ba? Sai na ce, E, ina so, ya Manzon Allah. Sai ya ce: "Shugaban Istigfari shi ne bawa ya ce "Ya Allah Kai ne Ubangijina babu abin bautawa bisa cancanta sai Kai. Kai ka halicce ni kuma ni bawanKa ne, kuma ina kan alƙawarinKa da wa'adinKa, gwargwadon iyawata. Ina neman tsarinKa daga sharrin abin da na aikata, ina bijiro da ni'imarKa a kaina, kuma ina bijiro da zunubina, Ka gafarta min domin haƙiƙa babu Mai gafarta zunubi sai Kai".

Ya ku 'yan'uwana na addini! Lallai shi wannan wata na Muharram, yana daga cikin mafi ɗaukakar watannin Allah Maɗaukakin Sarki. Matsayinsa mai girma ne, kuma alfarmarsa daɗaɗɗiya ce, shi ne farkon wata a shekara. Kuma yana daga cikin watannin Allah masu alfarma. A cikinsa ne Allah Ya tseratar da Annabi Musa da mutanensa daga Fir'auna da 'yan kanzaginsa. Ayyukan kirki a wannan watan suna da falala mai girma, tun ba ma azumi ba. Imam Muslim ya rawaito a cikin Sahihinsa daga Abu Huraira, Allah Ya yarda da shi, ya ce: "Manzon Allah (ﷺ), ya ce: "Mafificin azumi bayan Ramadan (shi ne azumin) watan Allah mai alfarma. Kuma mafi falalar sallah, bayan sallar farilla, ita ce sallar dare".

Kuma mafi falalar kwanakin wannan watan, ya ku bayin Allah, ita ce ranar Ashura.

Hadisi ya zo a cikin littafin Bukhari da Muslim, daga ɗan Abbas, Allah ya yarda da su, ya ce: "Manzon Allah (ﷺ), ya zo Madinah, sai ya sami Yahudawa suna azumtar ranar Ashura, sai ya ce musu (ﷺ), wace rana ce wannan kuke azumtarta? Sai suka ce: wannan rana ce mai girma. A cikinta ne Allah ya kuɓutar

da annabi Musa da mutanensa, kuma ya dulmiyar da Fir’auna da ‘yan kanzaginsa. Sai Annabi Musa ya azumce ta, domin godiya, don haka mu ma muke azumtarta. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Mu muka fi ku cancanta Annabi Musa. Sai Manzon Allah ya azumci wannan rana, kuma ya yi umarni da azumtar wannan rana.

Haka nan ya zo a cikin ingantaccen littafin Muslim, daga Abu Katada Allah Ya yarda da shi: An tambayi Manzon Allah (ﷺ) game da azumin ranar Ashura? Sai ya ce: "Ina tsammanin Allah zai kankare (zunuban) shekarar da take gabaninsa". Allahu Akbar! Me ya fi wannan falala, wanda ba wanda zai yadda ta kuɓuce masa sai asararre.

Kuma lallai Manzon Allah ya yi azamar azumtar ranar da take kafin wannan rana, domin ya saɓawa yahudawa, sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Idan har na kai zuwa badi, zan azumci rana ta tara” . Muslim ne ya ruwaito shi daga ɗan Abbas, Allah Ya yarda da su.

Don haka ya kamata a kan musulmi ya azumci wannan ranar, domin koyi da annabawan Allah, da kuma neman ladan Allah. Kuma sannan ya kamata mutum ya azumci ranar da take kafin ranar Ashura, domin saɓawa Yahudawa, da kuma aikata abin da sunnar Musɗafa (ﷺ) ta tabbatar. Lallai haƙiƙa, aiki ne ɗan kaɗan da lada mai yawa, daga Allah.

Haƙiƙa wannan - Ya ku masoyana - yana daga cikin godiyar Allah game da ni’imominsa, kuma buɗe farkon shekara ne da aikin mafi falala, wanda ake neman ladan Allah Maɗaukakin Sarki da shi. Cikakken mai hankali shi ne wanda yake gane irin tagomashin da wannan irin aiki ya ƙunsa. Don haka mutanen kirki sai ku zage dantse.

Kuma ku sani – Allah Ya yi muku rahama – lallai Allah ya umarce ku da yawaita salati da sallama ga wanda aka aiko shi rahama ga talikai, Manzo mai shiryarwa, zaɓaɓɓe, amintacce, ma’abocin mu’ujizozi, da ayoyi bayyanannu. Allah Maɗaukakin Sarki Yana cewa:

﴿ إِنَّ ٱللَّهَ وَمَلَٰٓئِكَتَهُۥ يُصَلُّونَ عَلَى ٱلنَّبِيِّۚ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ صَلُّواْ عَلَيۡهِ وَسَلِّمُواْ تَسۡلِيمًا ٥٦ ﴾

[الأحزاب: ٥٦].

(Lallai Allah da mala’ikunsa suna yin salati ga Annabi, ya ku waɗanda suka yi imani ku yi salati a gare shi, kuma ku yi sallama matuƙar sallama).

Kuma Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: “Duk wanda ya yi salati a gare ni, Allah Zai yi masa da wannan salati goma.” Allah ka yi salati ga Annabinka kuma bawanka Muhammad da iyalan ɗakinsa kamar yadda ka yi tsira da amincinka ga Annabi Ibrahim da alayensa lalle kai wanda ake godewa ne, kuma mai girma.

ZAKKA DA GUDUMMAWAR DA TAKE BAYARWA WAJEN TAIMAKON AL'UMMA

Manufofin hudubar

- Bayanin wajabcin bayar da zakka, da irin dukiyoyin da ake bada zakka a cikinsu.
- Bayanin ta'asirin zakka a cikin al'umma.
- Tsoratarwa daga hana zakka.
- Bayanin hikomomin wajabta bayar da zakka.

Huduba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga shirrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammad bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammad (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Bayin Allah : waye a cikinmu baya son a ƙara masa arziƙinsa, dukiyarsa ta ƙaru? Allah ya tsarkake masa ita, ya yi masa albarka a cikinta? To ku taho zuwa ga abin yake sanya haka, wannan abu ba komai ba ne face bayar da zakka. Wannan ibadar ta dukiya da Allah Maɗaukakin Sarki ya wajabta ta akan bayinsa, don haka – Yaku bayin Allah – ku bayar da abin da Allah ya wajabta muku a cikin dukiyoyinku, wadda Allah ya azurta da ita, haƙiƙa ya fitar da ku daga cikin iyayenku baku da komai, baku san komai ba, ba kwa mallakar amfani ko cutarwa ga kawunanku, sannan ya azurta ku, ya baku abin da baku taɓa tunanin samunsa ba, don haka ku gode masa, ku bayar da abin da ya wajabta muku, don ku samu kuɓuta, kuma dukiyoyinku su tsarkaka. Ku nisanci rowa da son kai da abin da Allah ya wajabta muku, saboda hakan halaka ne, kuma zare albarkar dukiyarku ne. Ku saurara mafi

girman abin da Allah ya wajabta muku a cikin dukiyoyinku shi ne bayar da zakka, wadda take rukuni ne na uku a musulunci, kuma abokiyar haɗin sallah ce a cikin Alkur'ani. Sannan ta wajaba akan dukkan musulmi baligi ɗa, mai hankali, wanda ya mallaki abin da ya kai zakka cikakkiyar mallaka.

Allah Maɗaukakin Sarki ya wajabta ta a cikin littafinsa mai girma, inda yake cewa :

﴿ وَأَقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُواْ ٱلزَّكَوٰةَ وَٱرۡكَعُواْ مَعَ ٱلرَّٰكِعِينَ ﴿٤٣﴾ ﴾ [البقرة : ١١٠]

Ma'ana : «Ku tsayar da sallah ku bayar da zakka ku yi ruku'u da masu ruku'u» (Al- Baƙara 43).

Ya sake cewa :

﴿ وَأَقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُواْ ٱلزَّكَوٰةَ ﴾ [البقرة : ١١٠].

Ma'ana : "Ku tsaida sallah ku bayar da zakka" (Al-baƙra : 110). Haka umarni da bayar da zakka da yin sallah ya yi ta maimaituwa a cikin Alƙur'ani har sama da aya (80).

Hakanan Manzon Allah (ﷺ) ya bayyana wa al'ummarsa wajabcinta. An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "An gina musulunci a bisa abubuwa biyar, akan a kaɗaita Allah, da tsaida sallah, da bayar da zakka, da azumin watan Ramadan, da hajji" Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

Lamarin zakka bai tsaya nan ba, sai da Allah Maɗaukakin Sarki ya yi kashedi mai tsanani akan duk wanda yake hana zakka, Allah ya ce:

﴿ وَلَا يَحۡسَبَنَّ ٱلَّذِينَ يَبۡخَلُونَ بِمَآ ءَاتَىٰهُمُ ٱللَّهُ مِن فَضۡلِهِۦ هُوَ خَيۡرٗا لَّهُمۖ بَلۡ هُوَ شَرّٞ لَّهُمۡۖ سَيُطَوَّقُونَ مَا بَخِلُواْ بِهِۦ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۗ وَلِلَّهِ مِيرَٰثُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۗ وَٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ خَبِيرٞ ﴿١٨٠﴾ ﴾ [ل عمران: ١٨٠].

Ma'ana : "kada waɗanda suke rowa da abin da Allah ya basu na falalarshi su yi zaton haka alheri ne garesu, a'a hakan sharri ne a garesu, za a naɗa musu abin da suka yi rowa da shi ranar alƙiyama. Gadon sammai da ƙassai duk mallakar Allah ne. kuma Allah masani ne dangane da abin da kuke aikatawa". (Al –Imran : 180).

Ya sake cewa a wurin :

﴿ وَٱلَّذِينَ يَكۡنِزُونَ ٱلذَّهَبَ وَٱلۡفِضَّةَ وَلَا يُنفِقُونَهَا فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ فَبَشِّرۡهُم بِعَذَابٍ أَلِيمٖ ﴿٣٤﴾ ﴾ [التوبة: ٣٤].

Ma'ana : «Waɗanda suke taskake zinare da azurfa ba sa ciyar da su saboda Allah, ka yi musu bushara da azaba mai tsanani. Ranar da ɗumama musu ita a cikin wutar Jahannama, a naɗe goshinsu da gefensu da bayansu da ita, a ce musu wannan shi ne abin da kuka taskake wa kawunanku, ku ɗanɗani abin da kuke taskakewa». (Attauba)

Manzon Allah (ﷺ) ya fassara ayar farko da faɗinsa : "Duk wanda Allah ya bashi dukiya, amma bai bayar da zakkarta ba, za a mayar masa da wannan dukiya ta zama maciji, wanda baya da gashi a kansa saboda yawan dafinsa, a rataya masa shi, yana cafkar muƙamuƙinsa, yana cewa : "Ni ne dukiyarka, ni ne abin da ka taskake" Bukhari ne ya rawaito.

Yaku musulmi : Ku sani cewa zakka tana da fa'idoji a addinance da ɗabi'ance cikin al'umma masu yawa, ga kaɗan daga cikinsu :

1. Bayar da zakka tsaida ɗaya daga cikin rukunan addinin musulunci ne, wanda a kansu arziƙin bawa yake duniya da lahira.
2. Yin zakka yana kusantar da bawa ga Ubangijinsa, kuma tana ƙara imani, kamar yadda sauran ibadu suke kusantar da bawa ga Allah.
3. Abin da yake biyo bayan bayar da zakka na lada mai yawa, Allah yana cewa : ﴿ يَمۡحَقُ ٱللَّهُ ٱلرِّبَوٰاْ وَيُرۡبِي ٱلصَّدَقَٰتِۗ ﴾ [البقرة: ٢٧٦].

"Allah yana shafe albarkar riba, yana renon sadaka" (Albaƙra : 276). A wani wurin ya ce,

﴿ وَمَآ ءَاتَيۡتُم مِّن رِّبٗا لِّيَرۡبُوَاْ فِيٓ أَمۡوَٰلِ ٱلنَّاسِ فَلَا يَرۡبُواْ عِندَ ٱللَّهِۖ وَمَآ ءَاتَيۡتُم مِّن زَكَوٰةٖ تُرِيدُونَ وَجۡهَ ٱللَّهِ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُضۡعِفُونَ ٣٩ ﴾ [الروم: ٣٩] •

"Duk abin da kuka bayar na haramun don ya ƙaru a dukiyar mutane, to ba zai ƙaru a wurin Allah ba, abin da kuka bayar na sadaka kuna nemar yardar Allah to wannan shi ne mai ninkuwa" (Arrum : 39).

Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Wanda ya yi sadaka da kwatankwacin dabino, daga tsakaken abin ya samu – Allah ba ya karɓa abu sai mai tsarki – to Allah yana karɓar wannan sadakar da hannun damansa, ya reneta kamar yadda ɗayanku yake renon ɗan goɗiyarsa, har ta zama kamar girman dutse". Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

1. Allah yana kankare zunubai da ita, kamar yadda Manzon Allah (ﷺ) yake cewa "Sadaka tana kankare zunubai kamar yadda ruwa yake bice wuta". Anan ana nufin sadakar nafila da ta farilla (zakka).

Daga cikin fa'idojin zakka na gyaran halaye da take kawo wa, akwai :

1. Zakka tana sanya mai yinta ya zama mai karamci da kyauta da rangwame.
2. Zakka ta kan sa mai yin ta, ya zama mai tausayi da jin ƙai ga 'yan uwansa miskinai. Masu jinƙai kuwa Allah mai rahama yana jin ƙansu.
3. Abu ne wanda ake gani bada dukiya da jiki ya kan kawo yalwar ƙirji, da buɗewar zuciya, da nutsuwa, kuma yana sanya mutum ya zama abin ƙauna a wurin 'yan uwansa musulmai saboda irin amfanin da yake yi wa 'yan uwansa.
4. Zakka tana tsarkake mai yin ta daga rowa da son kai, kamar yadda Allah ya ce, ﴿ خُذۡ مِنۡ أَمۡوَٰلِهِمۡ صَدَقَةٗ تُطَهِّرُهُمۡ وَتُزَكِّيهِم بِهَا وَصَلِّ عَلَيۡهِمۡۖ إِنَّ صَلَوٰتَكَ سَكَنٞ لَّهُمۡۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ١٠٣ ﴾ [التوبة: ١٠٣].

«Ka karɓi sadaka daga dukiyoyinsu wadda zaka tsarkake su ka gyara su da ita».

A Bangaren zamantakewa kuwa, Zakka tana bada gudummawa mai yawa daga ciki akwai:

1. A cikinta akwai kawar wa talakawa buƙatunsu, waɗanda su suka fi yawa a cikin mafi yawan garuruwa.

2. A cikin zakka akwai ƙarfafa musulmi, da ɗaukaka su, don haka ya halatta a bada zakka don yin jihadi saboda Allah.
3. Zakka tana kawar da gaba da hassada da ƙyashi da suke cikin zukatan talakawa da miskinai, saboda idan talakawa na ganin masu hali da dukiya suna walwala a cikin dukiyarsu, kuma ba sa amfanarsu da ita, da kaɗan koda da yawa, to wannan zai iya jawo gaba da ƙulli ga mawadata, saboda basu kiyaye haƙƙinsu ba, ba su biya musu buƙatunsu ba. Amma ida mawadata suka bada wani 'yanki na dukiyarsu ga talakawa a farkon shekara, sai waɗannan abubuwa su gushe, a samu soyayya da haɗuwa da juna.
4. A cikin zakka akwai ƙaruwar dukiya da yawaita albarkarta, kamar yadda hadisi ya nuna.
5. A cikin zakka akwai faɗaɗa dukiya da yaɗata, saboda dukiya idan aka sarrafa wani abu daga cikinta, sai ta ƙara buɗewa, mutane da yawa su amfanu da ita, saɓanin idan ta zama tana jujjuyawa tsakanin mawadata kaɗai, talakawa ba sa samun komai.

Waɗannan fa'idoji gaba ɗaya suna cikin zakka, kuma suna nuna zakka wani abu ne da yake lallai a same shi don gyara ɗaiɗaikun mutane da al'umma. Tsarki ya tabbata ga Allah Masani Mai hikima.

'Yan uwa muslmi : ku sani zakka tana wajaba ne a cikin wasu abubuwa keɓantattu kamar haka :

1. Kayan da aka tanda don kasuwanci, gidaje ne ko motoci ko dabbobi ko wasu tufafi da sauran nau'ikan dukiya, abin da za a bayar na wajibi a ciki shi ne za a kasa dukiyar goma, a ɗau kashi ɗaya a kasa shi huɗu sai a bada kashi ɗaya, Mai kayan zai ƙimanta shi a farkon kowace shekara ya bada abin da ya cancanta. Amma abin da ya tanada don buƙatarsa, ko don yin haya da shi, daga gidaje ko motoci da sauran abin da aka tanada, to babu zakka a cikinsa, saboda Manzon Allah (ﷺ) yana cewa : "Babu zakka akan musulmi cikin bayinsa da dokinsa (abin hawansa)". Imam Ahmad ne ya rawaito shi.
2. Abu na biyu da ake fitar wa da zakka shi ne zinare da azurfa ko abin da yake a matsayinsu wajen zama kuɗin abubuwa, idan mutum ya mallaki nisabi, kuma shekara ta zagayo a kansa bai ragu ba, to wajibi ne ya lissafa abin da yake da shi ya kasa arba'in ya bada kaso ɗaya.
3. Abu na uku da ake fitarwa da zakka : kayan gona, duk wanda ya noma abin da ake ci kuma ana iya ajiye shi, sannan ya kai wisƙi sittin, to wajibi ne ya bada zakkarsa anan take.

Waɗannan su ne abubuwan da ake fitar wa da zakka, koma bayansu na abin da mutum ya mallaka, na kayan amfanin yau da kullum, kamar motar da yake hawa, ko tufafin da yake sanyawa, da makamantansu to babu zakka a cikinsu.

Yaku bayin Allah : Musulmi nagari shi ne wanda yake kallon dukiyar da Allah ya bashi a matsayin amana, da Allah ya bashi, ya kuma dace ya bada haƙƙinta, ya yi amfani da ita cikin abin da Allah ya yarda da shi. Ba musulmi nagari ba ne

wanda yake ɗaukar dukiyarsa a matsayin wani abu nashi na dole da ya wajaba Allah ya bashi, kuma yake mata kallon dauwama da rashin ƙarewa, haƙiƙa duk wanda ya zama haka to ya yi hasara duniya da lahira. Muna roƙon Allah ya kare mu.

Allah ya yi mana albarka cikin abin da muka ji, daga Alƙur'ani da Sunnah, ya yi mana gafara, haƙiƙa shi mai iko ne akan komai.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah, Kyakkyawan ƙarshe yana ga masu tsoron Allah, Tsira da Aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, Manzon Allah (ﷺ) da iyalansa da Sahabbansa da waɗanda suka bi su gaba ɗayansu, har zuwa ranar sakamako. Bayan haka:

Ya 'yan uwa : Allah Maɗaukakin Sarki ya jiɓinci bayanin waɗanda za a bawa zakka a cikin Alƙur'ani mai girma, inda yake cewa :

﴿ إِنَّمَا ٱلصَّدَقَٰتُ لِلۡفُقَرَآءِ وَٱلۡمَسَٰكِينِ وَٱلۡعَٰمِلِينَ عَلَيۡهَا وَٱلۡمُؤَلَّفَةِ قُلُوبُهُمۡ وَفِي ٱلرِّقَابِ وَٱلۡغَٰرِمِينَ وَفِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱبۡنِ ٱلسَّبِيلِۖ فَرِيضَةٗ مِّنَ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٞ ٦٠ ﴾ [التوبة: ٦٠].

Ma'ana : «Kaɗai sadaka (wato zakka, haƙƙi ne na) faƙirai da miskinai da masu aiki a kanta, da waɗanda ake janyo zukatansu, da bayi, da waɗanda ake bi bashi, da kuma saboda Allah da matafiya, wajibi ne daga wajen Allah, Allah masani ne mai hikima» (Attauba : 60).

Waɗannan sune sinfi takwas da ake bawa zakka : ga bayaninsu ɗaya bayan ɗaya :

1. Faƙirai, su ne waɗanda ba sa samun abin da zai ishe su, sai ɗan kaɗan wanda bai kai rabi ba, idan ya zama mutum bai mallaki abin da zai iya ciyar da iyalisa ba na wata shida to shi faƙiri ne, ya halatta a bashi abin da zai ishe shi da iyalansa tsawon shekara.
2. Miskinai : su ne waɗanda suke da rabin abin da zai ishe su, ko fiye da rabin, amma ba su da abin da zai ishe su shekara guda, don haka sai a cika musu na shekara guda.
3. Masu aiki a kan zakkar : su ne waɗanda shugaba yake wakilta wa don karɓo zakkar daga mawadata, sannan su raba ta ga waɗanda suka cancanta, su kiyayeta, To waɗannan ya halatta a basu zakka gwargwadon aikinsu koda kuwa suna da watada da hali.
4. Waɗanda ake son a ja zukatansu zuwa ga musulunci : su ne shugabannin ƙabilu, waɗanda imaninsu bai yi ƙarfi ba, ya halatta a basu zakka don ƙarfafa musu imaninsu, su zama masu kira zuwa ga addinin Allah. Idan mutum yana da raunin imani kuma baya cikin shugabannin da ake yi wa biyayya, kawai yana cikin gama – garin mutane, to shin za a bahi zakka don ƙarfafa imaninsa, ko kuwa? malamai sun yi saɓani wajen ba shi zakka!?.

5. Bayi : wannan ya haɗa da sayen bayi da ‘yanta su da kuɗin zakka, da fanso ribatattun musulmi daga wurin kafirai, dak da kuɗin zakka.
6. Waɗanda ake bi bashi : idan ba su abin da zasu biya bashinsu da shi, to irin waɗannan ya halatta a basu abin da zasu biya bashinsu da shi, bashin mai yawa ne ko kaɗan, ko da kuwa suna da wadatar abin za su ci, misali da za a ƙaddara cewa ga wani mutum yana da inda yake samun abincinsa da na iyalansa, amma ana bin shi bashi wanda ba zai iya biya ba, to za a bashi abin zai biya masa bashinsa daga cikin zakka. Ba ya halatta wanda yake bin wani bashi ya sauke masa bashin da abin da ya yi niyya na zakka.
7. Wajen ɗaukaka kalmar Allah : wato jihadi don ɗaukaka kalmar Allah, za baiwa masu jihadi abin da zai ishe su daga zakka don fita zuwa jihadi, a sayi kayan jihadi daga cikin kuɗin zakka. Yana cikin Fisabilillahi neman ilimin addini, za a bawa ɗalibin da yake neman ilimin addini abin da zai iya neman ilimi da shi, daga littattafai da makamantansu, sai dai idan yana dukiyar da zai iya samun abin da yake so.
8. Matafiyi : shi ne wanda guzuri ya yanke masa, sai a bashi abin da zai kai shi gida daga cikin zakka.

Waɗannan su ne waɗanda Allah ya ambata a cikin littafinsa, ya kuma bawa waɗannan wajibi ne da ya fito daga gare shi a kan ilimi da hikima. Allah Masani ne mai hikima.

Ba ya halatta a sarrafa zakka a cikin waɗanda ba waɗannan ba, kamar gina masallaci, ko gyara hanya, saboda Allah ya faɗi waɗanda suka cancanci zakka a keɓe, keɓe abu kuwa yana kore shi daga wanda ba shi ba.

Ku ji tsoron Allah – Yaku bayin Allah – ku yi wa kanku hisabi, ku yi adalci, kada ku zaton zakka tara ce ko hasara ce a kanku, a’a wallahi zakka ganima ce da riba ga wanda ya yi ta, kuma ɗaya ce daga cikin rukunan musulunci, abokiyar sallah ce a cikin littafin Allah. Aiki da ita aiki ne da rukuni mai girma daga rukunan musulunci, sannan tsarki ce daga saɓo da zunubi ga wanda ya bayar da ita, tsarkake wa ce garehi da ayyukansa, kuma albarka ce da ƙaruwa a cikin dukiyarsa.

Allah Maɗaukakin Sarki ya ce :

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَنفِقُواْ مِن طَيِّبَٰتِ مَا كَسَبْتُمْ وَمِمَّآ أَخْرَجْنَا لَكُم مِّنَ ٱلْأَرْضِۖ وَلَا تَيَمَّمُواْ ٱلْخَبِيثَ مِنْهُ تُنفِقُونَ وَلَسْتُم بِـَٔاخِذِيهِ إِلَّآ أَن تُغْمِضُواْ فِيهِۚ وَٱعْلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ غَنِيٌّ حَمِيدٌ ﴿٢٦٧﴾ ٱلشَّيْطَٰنُ يَعِدُكُمُ ٱلْفَقْرَ وَيَأْمُرُكُم بِٱلْفَحْشَآءِۖ وَٱللَّهُ يَعِدُكُم مَّغْفِرَةً مِّنْهُ وَفَضْلًاۗ وَٱللَّهُ وَٰسِعٌ عَلِيمٌ ﴿٢٦٨﴾ ﴾ [البقرة: ٢٧٨ - ٢٦٨].

Ma’ana : “Yaku waɗanda ku ka bada gaskiya ku ciyar daga daɗaɗan abubuwan da kuka tsururuta da abin da muka fitar muku da cikin ƙasa, kada ku nufi mummuna ku ciyar daga cikinsa, alhali ku ba za ku karɓe shi ba idan an baku, sai da rintse idanu, ku sani lallai Allah mawadaci ne abin yabo. (Ku sani) Shaiɗan yana muku alƙawarin talauci da rowa (idan kun bayar da abin da kuke da shi) Allah kuwa yana muku alƙawarin gafara da falala. Allah mai yalwa ne kuma masani”. (Albaƙra : 267).

WASU DAGA CIKIN AYOYIN HALITTUN ALLAH

Manufofin huɗubar

- Tunatar da mutane wasu daga cikin ayoyin halittun Allah.
- Bayanin girman Allah Ta'ala, kuma da cewa shi ne wanda ya cancanci bauta shi kaɗai.
- Kiran Mutane da su godewa Allah ta'ala da ya hore musu waɗannan manya-manyan halittu.
- Kiran mutane a kan su yi amfani da waɗannan halittu wajen bautawa Allah

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammadu bawansa ne manzonsa ne. (Yaku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron Allah yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Yaku waɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammadu (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (a addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta".

Bayan haka:

Ya 'yan uwa! Lallai cikin halittun Allah baki ɗaya, akwai aya da take tabbatar da cewa, Allah shi kaɗai ne, kuma shi ya cancanta a bautawa shi kaɗai. Allah yana cewa,

﴿ أَوَلَمۡ يَنظُرُواْ فِي مَلَكُوتِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا خَلَقَ ٱللَّهُ مِن شَيۡءٖ وَأَنۡ عَسَىٰٓ أَن يَكُونَ قَدِ ٱقۡتَرَبَ أَجَلُهُمۡۖ فَبِأَيِّ حَدِيثٖ بَعۡدَهُۥ يُؤۡمِنُونَ ١٨٥ ﴾ [الأعراف: ١٨٥].

(Shin ba su yi duba ba cikin masarautar sama da ƙasa, da ma duk wani abin da Allah ya halitta. Kuma tabbas ajalinsu ya ƙarato. To da wane zance ne bayansa

suke bayar da gaskiya?) .

Kuma Allah ya ce,

﴿ أَفَلَمۡ يَنظُرُوٓاْ إِلَى ٱلسَّمَآءِ فَوۡقَهُمۡ كَيۡفَ بَنَيۡنَٰهَا وَزَيَّنَّٰهَا وَمَا لَهَا مِن فُرُوجٖ ٦ وَٱلۡأَرۡضَ مَدَدۡنَٰهَا وَأَلۡقَيۡنَا فِيهَا رَوَٰسِيَ وَأَنۢبَتۡنَا فِيهَا مِن كُلِّ زَوۡجِۭ بَهِيجٖ ٧ تَبۡصِرَةٗ وَذِكۡرَىٰ لِكُلِّ عَبۡدٖ مُّنِيبٖ ٨ ﴾ [ق: ٦ - ٨].

(Shin ba su yi duba ba zuwa sama da take kansu, yaya muka gina ta, kuma muka ƙawata ta, babu wata ɓaraka, ko kecewa tare da ita. Kasa kuma muka miƙar da ita, kuma muka jefa duwatsu a cikinta, muka tsirar daga kowane irin nau'in kayan marmari mai ƙayatarwa. Faɗakarwa ce da tunatarwa ga duk wani bawa mai komawa ga Allah).

Kuma Allah ya ce,

﴿ أَفَلَا يَنظُرُونَ إِلَى ٱلۡإِبِلِ كَيۡفَ خُلِقَتۡ ١٧ وَإِلَى ٱلسَّمَآءِ كَيۡفَ رُفِعَتۡ ١٨ وَإِلَى ٱلۡجِبَالِ كَيۡفَ نُصِبَتۡ ١٩ وَإِلَى ٱلۡأَرۡضِ كَيۡفَ سُطِحَتۡ ٢٠ ﴾ [الغاشية: ١٧ – ٢٠].

(Shin ba sa yin nazari kan raƙuma, yaya aka halicce su? Haka nan sama, yaya aka ɗaga ta? Haka nan ƙasa, yaya aka shimfiɗa ta?).

Lallai yana daga cikin ayoyin Allah, halittar sama da ƙasa. Duk wanda ya yi nazari kan halittar sama, da kyawunta da ɗaukakarta, da ƙarfinta, zai gane ikon Allah da cancantarsa da a bauta masa shi kaɗai. Halitta da take nuna iyawa da ƙwarewa; halitta da babu makusa a tare da ita. Allah yana cewa,

﴿ فَٱرۡجِعِ ٱلۡبَصَرَ هَلۡ تَرَىٰ مِن فُطُورٖ ٣ ثُمَّ ٱرۡجِعِ ٱلۡبَصَرَ كَرَّتَيۡنِ يَنقَلِبۡ إِلَيۡكَ ٱلۡبَصَرُ خَاسِئٗا وَهُوَ حَسِيرٞ ٤ ﴾ [الملك: ٣ – ٤].

(Ka mayar da gani zuwa sama. Shin ka ga wata kecewa tare da ita? Sannan ka sake mayar da gani karo na biyu, ganinka zai dawo gare ka, yana taɓaɓɓe, alhali ya gaji).

Haka idan mutum ya yi nazari kan halittar ƙasa, yadda Allah ya shimfiɗa ta, kuma ya keta hanyoyi a cikinta, ya kuma kafa duwatsu a kanta, ya kuma albarkace ta da abubuwa irin daban-daban na buƙatun halitta, kuma ya hore ta ga ɗan Adam yana kai-kawo a kanta daga nan zuwa can ba tare da tangarɗa ba. Kuma a cikinta ɗan Adam yake samun abincinsa, da abin sha. Duk wannan yana nuna ikon Allah da cancantarsa a bauta masa shi kaɗai. Allah yana cewa,

﴿ وَفِي ٱلۡأَرۡضِ ءَايَٰتٞ لِّلۡمُوقِنِينَ ٢٠ ﴾ [الذاريات: ٢٠].

)A cikin ƙasa akwai ayoyi daban-daban ga masu sakankancewa da samuwar Allah).

Hakanan yana daga cikin ayoyinsa, abin da ya watsa a sama da ƙasa na halittu iri daban-daban: Sama akwai mala'iku, wanda ba mai iya ƙididdige su, sai Allah. Allah yana cewa,

﴿ وَمَا يَعۡلَمُ جُنُودَ رَبِّكَ إِلَّا هُوَ ﴾[المدثر: ٣١].

(Babu wanda ya san yawan rundunar Ubangijinka, sai shi).

A ƙasa kuwa, akwai halittu dangi daban-daban, sun saɓa da juna ta fuskar halittarsu. Daga cikinsu akwai waɗanda suke masu amfani ga ɗan Adam, wanda ta hanyarsu yake ƙara sanin cikar ni'imar Allah a kan bayi. Daga cikinsu akwai masu cutarwa ga ɗan Adam, wanda ta hanyarsa ɗan Adam yake ƙara gane matsayinsa

da kuma rauninsa a gaban sauran halittun Allah. Kuma dukkaninsu suna tsarkake Allah, tare da gode masa, kamar yadda ya ce,

﴿ تُسَبِّحُ لَهُ ٱلسَّمَٰوَٰتُ ٱلسَّبۡعُ وَٱلۡأَرۡضُ وَمَن فِيهِنَّۚ وَإِن مِّن شَيۡءٍ إِلَّا يُسَبِّحُ بِحَمۡدِهِۦ وَلَٰكِن لَّا تَفۡقَهُونَ تَسۡبِيحَهُمۡۚ إِنَّهُۥ كَانَ حَلِيمًا غَفُورٗا ٤٤ ﴾ [الإسراء: ٤٤].

(Sama guda bakwai, da ƙasa, da abin da yake cikinsu, suna tsarkake Ubangiji. Kai babu wani abu, face sai yana tsarkake shi. Lallai shi ya kasance mai haƙuri ne, mai gafara).

Kuma duk wannan halittu, Allah yake arzuta su shi kaɗai. Kamar yadda Allah ya ce,

﴿ وَمَا مِن دَآبَّةٖ فِي ٱلۡأَرۡضِ إِلَّا عَلَى ٱللَّهِ رِزۡقُهَا ﴾ [هود: ٦].

(Babu wata dabba da take rarrafawa a ƙasa, face Allah ne yake arzuta ta).

Yana daga cikin ayoyinsa, dare da rana. Allah ya sanya dare, don nutsuwa ga bayi: Su kwanta a cikinsa, su yi barci, su sami hutu. Ya kuma sanya rana, gudanar da harkokin rayuwa, da neman arziki. Kamar yadda Allah ya ce,

﴿ قُلۡ أَرَءَيۡتُمۡ إِن جَعَلَ ٱللَّهُ عَلَيۡكُمُ ٱلَّيۡلَ سَرۡمَدًا إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلۡقِيَٰمَةِ مَنۡ إِلَٰهٌ غَيۡرُ ٱللَّهِ يَأۡتِيكُم بِضِيَآءٍۖ أَفَلَا تَسۡمَعُونَ ٧١ قُلۡ أَرَءَيۡتُمۡ إِن جَعَلَ ٱللَّهُ عَلَيۡكُمُ ٱلنَّهَارَ سَرۡمَدًا إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلۡقِيَٰمَةِ مَنۡ إِلَٰهٌ غَيۡرُ ٱللَّهِ يَأۡتِيكُم بِلَيۡلٖ تَسۡكُنُونَ فِيهِۚ أَفَلَا تُبۡصِرُونَ ٧٢ ﴾ [القصص: ٧١ – ٧٢].

(Ka ce, “Ku ba ni labari, idan Allah ya sanya dare dindindin, har zuwa ranar tashin ƙiyama, wane Ubangiji ne ba Allah ba, zai zo muku da haske. Ba kwa jin abin da ake gaya muku?” Ka ce, “Ku ba ni labari, idan Allah ya sanya rana dindindin, har zuwa ranar tashin ƙiyama, wane Ubangiji ne ba Allah ba, zai zo muku da dare, wanda za ku nutsu a cikinsa? Ba kwa ganin abin da ake gaya muku?).

Ya ku ‘yan uwa! Lallai wannan sararin duniya gabaɗayansa, da abin da yake cikinsa, halitta ce ta Ubangiji, ba wanda ya halicce ta, sai shi, kamar yadda Allah ya ce,

﴿ أَمۡ خُلِقُواْ مِنۡ غَيۡرِ شَيۡءٍ أَمۡ هُمُ ٱلۡخَٰلِقُونَ ٣٥ أَمۡ خَلَقُواْ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَۚ بَل لَّا يُوقِنُونَ ٣٦ ﴾ [الطور: ٣٥ – ٣٦].

)Shin an halicce su ne daga babu, ko kuma su suka yi halitta? Ko kuma sun halicci sama da ƙasa ne? Bari dai, ba sa sakankancewa ne).

Duniya ba ta halicci kanta ba, kuma ba zai yiwu a ce haka kawai ta samu ba, ba tare da wani abu ya halicce ta ba. Wanda ya halicce ta, shi ne Allah, kuma shi yake tsaye da lamarinta, babu wanda ya halicce ta, sai shi, ba kuma wani Ubangiji, sai shi. Albarkacin Allah sun ya waita, shi ne wanda ya fi kowa iya ƙaddarawa».

Da fatan Allah ya albarkace ni da ku bakiɗaya da abin da muka ji na ayoyin ƙur’ani mai hikima, da wa’azi mai amfani. Lalle shi Allah mai ji ne mai gani.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin Talikai. Tsira da amincin Allah su tabbata ga fiyayye halitta, kuma fiyayyen annabawa, Annabinmu Muhammadu da alayensa da sahabbansa da waɗanda suka bi tafarkinsa har zuwa ranar ƙiyama.

Bayan haka, ya ku ‘yan uwa! Ya zama wajibi mu gode wa Allah, bisa waɗannan halittu da ya yi, kuma ya hore su gare mu. Allah ya da sanar da mu abin da ba mu sani ba, ya koya mana abin da zai inganta addininmu da rayuwarmu. Yana daga cikin abin da Allah ya sanar da mu, mafarar halittar wannan duniyar, abin da ba za a iya sanin sa ba, sai ta hanyar Manzanni. Duk wani wanda zai yi magana kan yadda aka halicci sama da ƙasa, to dole ne mu gwada maganarsa da abin da Manzanni suka zo da shi. Idan sun yi daidai, sai mu karɓa, idan kuwa suka saɓa wa juna, to ba za a karɓi maganarsa ba.

Hakanan yana daga cikin abin da Allah ya sanar da mu, ya halicci sama da ƙasa, da abin da yake tsakaninsu: Ya halicci sama a cikin kwana biyu, ya kuma kafa duwatsu a kanta, ya tanadar da albarkatu, wanda bayi za su amfana da su, cikin wasu kwanaki biyu daban. Idan aka haɗa wannan, kwana huɗu kenan. Sannan ya nufi sama, alhali tana hayaƙi, sai ya daidaita ta, ta zama sama, sammai bakwai, cikin kwanaki biyu, ya yi wahayi cikin kowace sama, da abin da ya keɓance ta. Gabaɗaya kwana shida kenan, da Allah ya halicci sama da ƙasa a cikinsu, kuma ya ajiye abubuwa da ɗan Adam yake buƙata a cikinsu: Ya samar da ruwa, ya samar da abinci iri daban-daban, waɗanda za su tabbatar da ɗorewar ɗan Adam a doron ƙasa, kuma ya kimsa wa ɗan Adam yadda zai yi huldɗa da danginsa, da ma sauran halittun Allah. Duk Allah ya yi wannan, ba don komai ba, sai don a bauta masa shi kaɗai, kamar yadda Allah yake cewa,

﴿ وَمَا خَلَقۡتُ ٱلۡجِنَّ وَٱلۡإِنسَ إِلَّا لِيَعۡبُدُونِ ٥٦ ﴾ [الذاريات: ٥٦].

(Ban halicci aljanu da ɗan Adam ba, sai don su bauta mini).

Don haka, ya zama tilas a kan kowane mutum, ya bauta wa Allah shi kaɗai, kamar yadda Allah ya yi umarni, don godiya ga Allah, bisa waɗannan manya-manyan baiwaiwaki da Allah ya yi mana. Kamar yadda Allah ya ce,

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ كُلُواْ مِن طَيِّبَٰتِ مَا رَزَقۡنَٰكُمۡ وَٱشۡكُرُواْ لِلَّهِ إِن كُنتُمۡ إِيَّاهُ تَعۡبُدُونَ ١٧٢ ﴾ [البقرة: ١٧٢].

(Ya ku waɗanda suka yi imani! Ku ci daga abubuwa masu tsarki, da muka arzuta ku da su, kuma ku gode wa Allah, idan kun kasance shi kaɗai kuke bautawa).

Kuma Allah yana cewa,

﴿ فَٱبۡتَغُواْ عِندَ ٱللَّهِ ٱلرِّزۡقَ وَٱعۡبُدُوهُ وَٱشۡكُرُواْ لَهُۥٓ إِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ ١٧ ﴾ [العنكبوت: ١٧].

(Ku nemi arziki a wajen Allah, kuma ku bauta masa, ku kuma gode masa. Zuwa gare shi ne za ku koma).

Ya Ubangiji! Muna gode maka a kan waɗannan kyaututtuka masu girma, kuma muna gode maka a kan aiko mana Manzanni da ka yi. Godiya ta tabbata ga Allah, wanda ya shiryar da mu ga wannan addini, ba mu zamo masu shiriya ba, ba don Allah ya shiryar da mu ba.

TSARKIN MARA LAFIYA DA SALLARSA

Manufofin huɗubar

- Tunatarwa a kan muhimmancin kiyaye sallah
- Bayanin sunnar jarraba, da roƙon Allah lafiya
- Gargaɗi a kan ɗabi'ar sakacin marasa lafiya da sallah
- Wayar dakan likitoci da masu kula da marasa lafiya

Huɗuba Ta Farko

Yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan ayyukanmu, wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin taraiya, kuma ina shaidawa cewa Annabi Muhamamdu bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda suk a yi imani ku ji tsoron Allah yadda ya cancanci a ji tsoronsa kuma kada ku mutu face kuna musulmi). (Yaku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicce ku daga rai guda ɗaya kuma ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga gare su (su biyu) kuji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya dashi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku waɗanda suka yi imani kuji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku aiyukanku, kuma ya gafarta muku zunubanku. Wanda ya bi Allah da manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kumamafi kyawun shiriya shiriyar Annabi (ﷺ), kuma mafi sharrin al'amura (a addini) ƙagagunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (a addini) bidi'a ce, kuma duk wata bidi'a ɓata ce, kuma duk wani ɓata yana wuta.

Bayan haka:

Ya kai musulmi, ka yi sani - Allah ya datar da ni da kai zuwa dukkan alheri – cewa Allah mai buwaya da ɗaukaka, mai hikima ne cikin jarrabarsa ga bayinsa da abin da yake jarrabasu da shi. Shi yakan jarrabesu wani lokacin da abin farin ciki, wani lokacin kuwa da tsanani, duk wannan jarrabawar da gwadawar domin ya bayyana godiyar mai godiya da haƙurin mai haƙuri. Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa,

﴿ وَلَنَبۡلُوَنَّكُمۡ حَتَّىٰ نَعۡلَمَ ٱلۡمُجَٰهِدِينَ مِنكُمۡ وَٱلصَّٰبِرِينَ وَنَبۡلُوَاْ أَخۡبَارَكُمۡ ٣١ ﴾ [محمد: ٣١].

(Kuma wallahi za mu jarrabe ku don mu san masu jihadi daga cikinku, da masu haƙuri, kuma don mu jarraba haƙiƙanin lamarinku).

Yana jarrabasu da farin ciki da tsanani. An karɓo daga Suhaib Ar-Rumi (R.A) ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, Mamakin lamarin mumini, shi lamarinsa dukkaninsa

alheri ne, kuma babu mai wannan sai mumini, idan farin ciki ya same shi sai ya gode, sai ya zama alheri gare shi, idan kuma cuta ta same shi sai ya yi haƙuri sai ya zama alheri gare shi. Muslim ne ya rawaito shi.

Kenan Mumini yayin bala'i yana haƙuri yana yarda yana ƙaunar abin da Allah yayi wa masu haƙuri alƙawari da shi, Allah ya ce,

﴿ إِنَّمَا يُوَفَّى ٱلصَّٰبِرُونَ أَجۡرَهُم بِغَيۡرِ حِسَابٖ ١٠ ﴾ [الزمر: ١٠].

(Kaɗai ana cikawa masu haƙuri ladansu ba tare da lissafi ba).

Kuma ya ce,

﴿ وَبَشِّرِ ٱلصَّٰبِرِينَ ١٥٥ ٱلَّذِينَ إِذَآ أَصَٰبَتۡهُم مُّصِيبَةٞ قَالُوٓاْ إِنَّا لِلَّهِ وَإِنَّآ إِلَيۡهِ رَٰجِعُونَ ١٥٦ أُوْلَٰٓئِكَ عَلَيۡهِمۡ صَلَوَٰتٞ مِّن رَّبِّهِمۡ وَرَحۡمَةٞۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُهۡتَدُونَ ١٥٧ ﴾ [البقرة: ١٥٥ – ١٥٧].

(Kuma ka yi wa masu haƙuri bushara. Waɗanda idan masifa ta same su sai su ce,, mu ga Allah muke, kuma mu zuwa gare shi muke komawa. Waɗannan suna da tsira daga Ubangijinsu da rahama, kuma waɗannan su ne shiryayya).

An karɓo daga Abu Sa'id da Abu Hurairah (R.A) daga Annabi (ﷺ) ya ce, (Babu wani Abu da zai sami mumini na raɗaɗi, ko wahala, ko damuwa, ko ɓaƙin ciki, ko cuta, har ƙaya da zai taka ta, face Allah ya kankare masa zunubinsa da ita). Bukhari ne ya rawaito shi. Ya kai musulmi, muslmi ba ya fatan bala'i, ba ya taro bala'i, domin shi bai sani ba zai iya haƙuri ko zai iya fushi, don haka ne yayin da Al'abbas baffan Annabi (ﷺ) ya yi tambaya cewa, wace addu'a zai yi, sai Annabi (ﷺ) ya ce, "Ya baffana, ka tambayi lafiya, sai ya maimaita masa tambyaar sau dayawa shi kuma yana ce masa, "Ya banfan Manzon Allah ka roƙi Allah lafiya) Ahmad ne ya rawaito shi, da Bukhari cikin Al'adabul Mufrad, da Tirmizi kuma ya inganta shi.

Yakai Musulmi ka kusanci Allah a lokacin lafiyarka da ƙarfinka da abin da za ka iya na biyayya, domin idan ka aikata haka sannan ka gajiya, to Allah zai rubuta maka ladan abin da ka kasance kana aikata shi cikin halin lafiyarka. Kuma an karɓo daga Abu Musa (R.A) ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Idan bawa ya yi rahsin lafiya ko ya yi tafiya za a rubuta masa abin da ya kasance yana aikatawa yana halin zaman gida mai lafiya). Bukhari da Abu Dawud ne suka rawaito shi.

Ya ku bayin Allah, Allah mai girma da buwaya yana cewa,

﴿ إِنَّ ٱلصَّلَوٰةَ كَانَتۡ عَلَى ٱلۡمُؤۡمِنِينَ كِتَٰبٗا مَّوۡقُوتٗا ١٠٣ ﴾ [النساء: ١٠٣].

(Lalle sallah ta kasance ga muminai abin wajabtawa ne bisa lokatai). Ma'ana, abar wajabtawa a lokatai keɓantattu da Allah mai ɓuwaya da ɗaukaka ya ɓayyanasu, kuma Annabi (ﷺ) ya ƙara filla-filla da su. Sai Allah mai girma ya bayyana muhimmancin sallah da girman sha'aninta, kuma cewa ita an wajabtata a kan muminai bisa lokuta a lokuta na musamman.

Ya kai musulmi, haƙiƙa yana daga ɗabi'ar Musulmi kulawa da sallah da lura da ita, da dauwamar aikatar da ita da kiyayeta, ga shi Allah ta'ala yana cewa,

﴿ ٱلَّذِينَ هُمۡ عَلَىٰ صَلَاتِهِمۡ دَآئِمُونَ ٢٣ ﴾ [المعارج: ٢٣].

(Waɗanda suke madauwama a kan sallarsu).

Kuma yake cewa,

﴿ وَٱلَّذِينَ هُم عَلَىٰ صَلَاتِهِمۡ يُحَافِظُونَ ٣٤ أُوْلَٰٓئِكَ فِي جَنَّٰتٖ مُّكۡرَمُونَ ٣٥ ﴾ [المعارج: ٣٤ – ٣٥].

(Wadanda suke kiyaye sallarsu. Wadannan suna cikin aljannatai ababan girmamawa).

Kenan sallah sha'aninta a zuciyar mumini sha'ani ne mai girma, yana kiyaye ta, yana lazimtar ta, ba ya rabuwa da ita matukar hankalinsa yana nan, matukar yana ji, yana hankaltar abin da yake fada, to lallai ana nemansa da ya yi sallah. Allah ta'ala ya ce game da Isah dan Maryama:

﴿ وَأَوۡصَٰنِي بِٱلصَّلَوٰةِ وَٱلزَّكَوٰةِ مَا دُمۡتُ حَيّٗا ٣١ ﴾ [مريم: ٣١].

(Kuma ya yi min wasiyya da sallah da zakka matukar ina raye).

Ya kai Musulmi, lallai wasu daga cikin musulmi sukan yi sakaci cikin sallah, ba don kasala wajen yin ta ba, ba kuma don wulakantata ba, sai dai wasu shubuhohi da kan bijiro musu, da suke sa su su jinkirta yin sallah a lokacinta, musamman wanda aka jarraba da wata cuta, wannan cutar kan iya sanya shi ya jinkirta sallah daga lokacinta, da jinkirta ta zuwa wani lokaci daban, har ya warke daga wananan cuta da ta same shi. Yana ganin cewa wannan cutar za ta hana shi yin wannan sallah, da cika sahradanta da wajibanta, sai ka gan shi yana sakaci da sallah saboda jahilci, ba wai kasala ba, ko wulakanci da ita.

Ya kai musulmi! Abu ne sananne cewa tsarki daga najasa da kari, da najasar tufafi da ta jiki da bagiren da zai yi sallar, sharadi ne na ingancin sallah; domin Allah ta'ala yana cewa:

﴿ وَثِيَابَكَ فَطَهِّرۡ ٤ ﴾ [المدثر: ٤].

(Kuma ka tsarkake tufafinka). Kuma Annabi (ﷺ) yana cewa game da mutum bi yu da ake azabatar da su a cikin kaburburansu: "Shi dai dayansu ya kasance ba ya kaffa-kaffa da bawali) Bukhari ne yarawaito daga hadisin Jabir (R.A).

Kuma an karɓo daga Ibn Abbas (R.A) ya c, "Manzon Allah (ﷺ) ya ce, "Mafi yawancin azabar kabari daga bawali ne, don haka ku tsarkaka daga bawali". Bazzar da Ɗabarani da Hakim da Daru kudduni ne suka ruwaito shi. Kuma Annabi (ﷺ) yana cewa, "Ba a karɓar sallar dayanku idan ya yi kari har sai ya yi alwala". Muslim ne ya rawaito shi daga hadisin Abi Huraira (R.A). Sai ya nuna mana shardanta tsarki ga jiki da tufafi da gurin da mutum ke sallah a kanta, wannan abu ne da ake nema a shari'ah.

Sai dai mara lafiya wani lokaci yakan iya gazawa game da wadannan abubuwa, ya iya kasancewa rashin lafiya ne ya hana shi yin tsarki da ruwa, ko ya hana shi wanke gaɓɓan alwarsa da ruwa. Idan ya sami ikon yin haka ko aka sama masa wanda zai taimaka masa a kan alwala, to wannan ni'ima ce daga Allah. Sai dai idan haka ya yi masa wuya ya kasa yin alwala da ruwa, ko don rashinsa, ko kasa amfani shi, ko idan yin amfani da shi yakan kara masa rashin lafiya, ko ya jinkirta warkewa, domin Allah ta'ala ya sanya masa musayar haka, shi ne taimama, Allah ta'ala ya ce,

﴿ فَلَمۡ تَجِدُواْ مَآءٗ فَتَيَمَّمُواْ صَعِيدٗا طَيِّبٗا فَٱمۡسَحُواْ بِوُجُوهِكُمۡ وَأَيۡدِيكُمۡ ﴾ [النساء: ٤٣].

(Idan ba ku sami ruwa ba, to ku yi taimama a kasa tsarkakkiya, ku shafi

fuskokinku da hannayenku da su).

Idan kuma aka ƙaddara cewa, ba zai iya alwala da ruwa ba, kuma ba shi da abin da zai yi taimama da shi, kuma lamarin ya yi wahala, to zai yi sallah a halin da ya sami kansa. Allah yana cewa,

﴿وَمَا جَعَلَ عَلَيۡكُمۡ فِي ٱلدِّينِ مِنۡ حَرَجٖ﴾[الحج: ٧٨].

(Allah bai sanya muku wahala a cikin addini ba).

Ya kai Musulm! Wani lokacin rashin lafiya ya iya samun musulmi a sashin gaɓɓansa na alwala, ta yadda ba zai iya bi ta kansu da ruwa ba, wannan yana da hali biyu; ko dai wannan gaɓar ta zama a lulluɓe da abin rufewa wanda za a iya shafa akansa ta samansa, wannan za a yi shafa a kan abin da aka lulluɓe shi da shi na maɗauri, sai ya yi shafa akansa yayin alawala, kuma shafar ta wadatar; domin wannan shafar tana daidai da wanki, ko kuma ya zama ba za a iya wanke wannan gaɓar da ruwa ba, kuma samun ruwa komai ƙanƙantar sa zai yi tasiri bisa raunin, to a nan sai ya yi taimama. An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas ya ce: rauni ya sami wani mutum a zamin Manzon Allah (ﷺ), sannan ya yi mafarki, sai aka umarce shi da yin wanka, kuma ya yi wankan ya mutu. Da labari ya zo ga Annabi (ﷺ) sai ya ce, "Sun kashe shi; Allah ya wadan su, ashe ba maganin rashin sani ita ce tambaya ba?" Abu Dawud, da ibn Khuzaimah, da Ibn Hibban ne suka ruwaito shi.

Idan duk haka ya faskara, to sai ya yi shafa a kan makarin da ruwa, in kuma hakan ma ya yi wuya, to sai ya yi taimama ga wannan gaɓar.

Ya ku bayin Allah!

kowane musulmi ana nemansa da ya yi sallolin farilla, matuƙar hankalinsa na nan, matuƙar yana ganewa yana fahimta, to a na nemansa da wannan sallar gwargwadon iyawarsa, kuma sallar farilla ba ta faɗuwa daga gare shi matuƙar yana fahimta; domin wannan farilla rukuni ne daga rukunan musulunci, kuma dalili ne na gaskiya bisa abin da ke cikin zuciya na musulunci da imani; tana nuni a bisa lazimtar musulunci da gaskiya, ita tana daga mafi girman farillan musulunci, kuma mafi darajarta bayan tauhidi domin musulmi ana nemansa da sallah a tafiyarsa da zaman gidansa, ana nemansa da ita a halin tsoronsa da kwanciyar hankalinsa, ana neman sa da ita a rashin lafiyarsa da cikin lafiyarsa, sallah ba ta taɓa saraya daga gare shi har abada, kuma halin magabatanmu na gari haka yake. Muhammadu shugaban na farko dana ƙarshe, jagoranmu Shugabanmu (ﷺ) ya kasance yana aiwatar da sallah a lokacin rashin lafiyarsa, ko da zaune yake, yana salla a zaune yayin da ya gajiya daga tsayuwa. An ba da labari cewa Anas (R.A) ya faɗo daga kan doki sai ya daushe, sai ya kasance yana sallah a zaune. Bukhari da Muslim ne suka ruwaito.

Ya ɗan uwana, idan aka jarrabe ka da cuta, to ka sani cewa, salla dole ce, dole kuma a ba da ita a lokacinta, dole a kula da ita, kuma Ubangijin mu maigirma da ɗaukaka ba ya kallafawa bayi abin da ba za su iya ba, sai dai lamarin mai sauƙi ne, Allah ta'ala yana faɗa game da siffar Annabinsa (ﷺ),

﴿وَيَضَعُ عَنۡهُمۡ إِصۡرَهُمۡ وَٱلۡأَغۡلَٰلَ ٱلَّتِي كَانَتۡ عَلَيۡهِمۡ﴾[الأعراف: ١٥٧].

(Kuma yana sauke musu nauyinsu da takure-takuren da ke kansu).

Ka yi sallah a tsaye domin tsayuwa rukuni ne daga rukunan sallah, kuma ya wajba a bisa mara lafiya ya yi sallar farilla a tsaye, ko a sunkuye, ko a dogare a jikin garu, ko sanda da zai dogara akanta.

Idan ka gajiya game da tsayuwa, ko kana wahala, to ka yi sallah a zaun. Idan ka gaza zaman to, ka yi sallah a kan kwiɓinka. Idan ka kasa, to ka yi sallah a rigingine; Imaranu ɗan Husaini (R.A) ya ce, “Na kasance ina da Basur, sai na tambayi Manzon Allah (ﷺ)? Sai ya ce, "Ka yi sallah a tsaye. Idan ba za ka iya ba, to ka yi a zaune. Idan ba za ka iya ba, to a kan kwiɓinka). Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

Manzon (ﷺ) ya ziyarci wani mara lafiya, sai ya ganshi yana sallah a kan wani matashi, sai ya karɓe shi, ya yi wurgi da shi. Sai ya sake ɗaukar wani itace zai yi sallah akansa; sai ya karɓe shi, ya yi jifa da shi, sannan ya ce, "Ka yi sallah a ƙasa in za ka iya, idan ba haka ba, ka yi nuni, ka sanya sujjadarka ƙasa-ƙasa daga ruku’inka). Baihaƙi ne ya ruwaito shi daga Ibn Abbas, kuma Malam Albani ya ce hasan ne.

Wannan yana nufin dole a yi sallah a lokacin ta, ko da ka kasance a kwiɓinka ne, koda da nuni da kanka? Domin muhimmin lamari shi ne fahimtar zuciya da riskar abin da yake faɗi.

Ya kai Musulmi, ka yi sallah a tsaye, in ka sami ikon ruku’u ka yi ruku’i a tsaye, idan ba za ka iya yin ruku'u a tsaye ba, ka yi nuni da ruku’i, sannan ka yi nuni da sujjada. Wato ka ƙudirianiyar cewa, kai yanzu kana yin ruku’i ne a haka, ko kana yin sujjada ne. Ka sanya kanka a cikin sujjada mafi ƙasa-ƙasa daga ruku’u, don ruku’u ya banbanta da sujjada.

Inko ba zaka iya nuni da kanka ba cikin ruku’i da sujjada, to sai ka yi amfani da idanuwanka, sai ka runtse kaɗan wajen ruku’i, kuma ka runtse da sosai wajen sujjada.

Amma nuni da yatsa, kamar yadda wasu marasa lafiya suke aikatawa. Bai inganta ba, kuma ba shi da asali a Alƙur’ani ko Sunnah, ko a cikin zantuttukan malamai.

Ya kai Musulmi ka sani cewa, Allah ya wajabta wa musulmi sallah yayin rincaɓewar yaƙi da karafkiyar takubba. Ya wajbta musu sallah yayin da suke fuskantar abokin gabarsu, suna fito-na-fito da abokan gabarsu, to ina ga musulmin da ke cikin nutsuwarsa da kwanciyar hankali?

Allah ka ya fe mana ka karɓi ibadunmu na ƙwarai ka sanar da mu addininmu, ka kuma karɓi rayuwarmu muna musulmi. Ku ne mi gafar Ubangijinku shi mai gafara ne mai jin ƙai.

Huɗuba Ta Biyu

Yabo ya tabbata ga Allah. Tsira da aminci su tabbata ga mafi ɗaukakar manzanni, Annabin mu Muhamamdu da alayensa da sahabbansa da wanda ya bi

tafarkinsa har ya zuwa ranar sakamako.

Bayan haka:

Ya ku musulmi, fuskantar Alƙibla sharaɗin ingancin sallah ne, wannan ba wani ruɗani a cikinsa, sai dai idan mara lafiya ya kasa fuskantar alƙibla ko a ƙaddara cewa gadon sa da shimfiɗarsa ba su kalli alƙibla ba, kuma juya su ya faskara, to za ka yi sallah ne yadda ka samu halinka, wannan ba zai hana ka ba.

Ya kai musulmi, wasu marasa lafiyar sukan kasa yin alwala kuma sukan rasa waɗanda za su taimaka su ga hakan, ko kuma tufafinsu da shimfiɗarsu su ɓaci da najasa, su kasa gusar da ita ko canjata, ko kuma wannan rahsin lafiyar ya zama shi ya janyo hakan. Sai lokutan sallah su wuce tufafinsa na cikin najasa, shimfiɗarsa na cikin najasa, gas hi ba zai iya tsarkake su ba, wannan zai yi sallah a halin da ya tsinci kansa a ciki, Allah kuma ya san halinsa da makomarsa.

Idan ciwo ko rauni yana fitar da ruwa ko mugunya, to sai ka yi sallar a haka. An karɓo daga Miswar ɗan Makhramah, cewa shi ya shiga wajen Umar bn Khaɗɗab a daran da aka soke shi, sai ya tashi Umar domin sallar asubahi, sai Umar ya ce, "Na'am babu rabo cikin musulunci ga wanda ya bar sallah". Sai ya yi sallah, alhalin mikinsa yana tsartar da jini). Imamu Maliku ne ya ruwaito shi.

Hakanan faɗakkakun zukata suke, hakanan muminan zukata masu sakankancewa suke, wannan ciwon babba bai zama abu ne da zai hana su tuna sallah da kulawa da himmantuwa da ita ba.

Ya ku bayin Allah; ya wajaba ga musulmin da yake kula da mara lafiya a gidansa ko yake zaune da shi a asibiti ya tsoraci Allah, ya taimaki mara lafiyan wajen aiwatar da waɗannan sallolin, ya tuna masa su idan lokutansu sun zo. Ya taimaka masa wajen yin su. Ya wajaba musulmi su taimaka wajan yin wannan farillar, musamman idan kana da iyaye biyu; uba da uwa, to ya wajaba ka ji tsoron Allah game da su, ka taimake su wajen yin wannan aiki na gari, da kiransu zuwa sallah, da saukaƙe wahalhalu gare su, da hidimta musu da abin da zai taimake su wajan ba da wannan farilla, domin Allah yana cewa,

﴿ وَأۡمُرۡ أَهۡلَكَ بِٱلصَّلَوٰةِ وَٱصۡطَبِرۡ عَلَيۡهَا ﴾[طه: ١٣٢].

(Kuma ka umarci iyalanka da sallah, kuma ka yi haƙuri a kanta).

Ya wajaba ga likitoci musulmi da waɗanda ke lura da marasa lafiya a asibitoci su tsoraci Allah cikin lamarin marasa lafiya musulmi, su tuna musu lokacin sallah, su bayyana musu lokutanta, su himmatu da wannan lamari himmatu wa babba, su bayyana musu alamomin alƙibla, su taimaka musu a bisa abin da zai saukaƙe musu lamarin sallarsu na alwala da taimama, domin wannan abu abin nema ne, kuma yana daga cikin taimakekeniya cikin biyayya da tsoron Allah. Allah kuwa yana cewa,

﴿ وَتَعَاوَنُواْ عَلَى ٱلۡبِرِّ وَٱلتَّقۡوَىٰۖ وَلَا تَعَاوَنُواْ عَلَى ٱلۡإِثۡمِ وَٱلۡعُدۡوَٰنِ ﴾[المائدة: ٢].

(Kuma ku yi taimaki juna a kan biyayya da tsoron Allah, kuma kada ku yi ku taimaka wa juna a kan zunubi da ta'addanci).

Haƙiƙa likita ya kan iya damuwa da kula da lokacin shan magani, da wasu ƙaiyadaddun lokuta na safiya da yammaci, wannan abu ne mai kyau, sai dai kar mu

yi sakaci da sallah, kada mumanta cewa ita tana daga mafi muhimmancin lamurra, mu kula da ita da sha'aninta, domin ita abincin ruhi ce, bai kamata a yi sakaci ko wasa da ita ba. Idan likita yana kulawa da lokacin shan magani, to ya wajaba a kula da mara lafiya game da waɗannan salloli, mu tuna masa idan lokacinta ya yi, mu bayyana masa, mu taimaka masa, mu ba shi duk abin da zai taimaka masa yin wannan sallar, domin wannan lamari ne mai hummanci ƙwarai. Mara lafiya da ba zai iya alwala ba a kowane lokaci, ko yana samun wahala wajen saukowa don yin kowace sallah a lokacinta, to ya halatta ya haɗa tsakanin Azahar da La'asar, da kuma tsakanin magariba da isha'i. Amma zai yi azahar raka'a huɗune, la'asar ma huɗu, magariba uku isha'i huɗu. An halatta masa haɗawa banda ƙasaru; domin a cikin wannan akwai tausasawa gare shi da saukaƙawa, idan cika tsarki da sauka don ba da kowace sallah ita kaɗai ya yi masa wahala ya halatta ya haɗa tsakaninsu saboda uzuri na shari'ah, Abin da dai ake buƙata shi ne a kula da wannan farilla a himmatu da ita da tunata, da kiyaye ta, domin ita ce adireshin musulunci.

Ya kai musulmi, ka kula da wannan sallar, ka kiyaye ta, ka lazimceta, ka sani cewa babu rabuwa tsakaninka da ita har ka gamu da Allah kana mai kiyayeta, kana mai lazimtar ta, kana mai dauwamar aikata ta, domin ka zama daga masu gadan aljannar firdausi maɗaukakiya. Allah yake cewa,

﴿ وَٱلَّذِينَ هُمۡ عَلَىٰ صَلَوَٰتِهِمۡ يُحَافِظُونَ ٩ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡوَٰرِثُونَ ١٠ ٱلَّذِينَ يَرِثُونَ ٱلۡفِرۡدَوۡسَ هُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ ١١ ﴾ [المؤمنون: ٩ - ١١].

(Da kuma waɗanda suke kiyaye sallar su, waɗannan su ne masu gado. Waɗanda suke gadon aljannar firdausi su masu dauwama ne a cikinta).

Kuma Allah maɗaukaki yana cewa,

﴿ فَإِنۡ خِفۡتُمۡ فَرِجَالًا أَوۡ رُكۡبَانٗا ﴾[البقرة: ٢٣٩].

(Idan kun ji tsoro, to (ku yi sallar) kuna tafe ko kuna haye).

Malamai suka ce, wannan dalili ne a kan cewa ga jiyawa game da rukunan sallah kan sarayar da su idan ya ji tsoron abokin gaba, ko yayi ƙoƙarin riskar abokin gabar zai sallah ne a yanayin da yake ciki ko da da nunine, yana kallan alƙibla ne ko baya kallonta. Ina roƙon Allah ya sanyani ni da ku daga masu kiyayeta masu lura da ita, masu lazimtarta, lallai shi mai iko ne a bisa komai, Allah ya sanya ni da ku daga masu kiyayeta har ranar da zamu gamu da shi da falalarsa da karamcin sa.

Kuma ku sani – Allah ya jiƙanku – cewa mafi kyawun zance shi ne littafin Allah,

kuma mafi alherin shiriya ita ce shiryar Muhammadu (ﷺ), kuma mafi sharrin lamurra fararrunsu kuma duk wata bidi'a ɓata ce. kuma ku lazimci jama'a domin hannun Allah na tare da jam'a. Ku yi salati – Allah ya jiƙanku – a bisa Annabinku Muhammadu – don aiwatar da umarnin Ubangijinku wanda yake cewa,

﴿ إِنَّ ٱللَّهَ وَمَلَٰٓئِكَتَهُۥ يُصَلُّونَ عَلَى ٱلنَّبِيِّۚ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ صَلُّواْ عَلَيۡهِ وَسَلِّمُواْ تَسۡلِيمًا ٥٦ ﴾ [الأحزاب: ٥٦].

(Haƙiƙa Allah da mala'ikunsa suna salati ga Annabi ya ku waɗanda suka yi imani ku yi salati da taslimi a gare shi).

Allah ka yi salati da sallama da albarka a bisa shugaban na farko da na karshe Muhammadu ɗan Abdullahi, kuma ka yi yarda bisa halifofinsa shiryaiyu.

MUNANA ZATO

Manufofin huɗubar

- Magance wannan mummunar ɗabi’a
- Koyar da mutane samun nutsuwa a zuciya
- Karfafa ‘yan uwantaka tsakanin musulmi

Huɗuba Ta Farko

Yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga sharrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammadu bawansa ne manzonsa ne. (Yaku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron Allah yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Yaku waɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammadu (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (a addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Bayan haka;

Ya ku musulmi! Haƙƙin da yake kanmu shi ne samar da alaƙarmu ta zama mai ƙarfi tabbatacciya kamar ginin bulo-da-bulo, mu fuskanci mutane da farar aniya, mu fuskance su da so da ƙauna, da sakakkiyar fuska, kuma mu kyautata zato a wajen mu’amalar mu da juna. Mu cire duk wani zargi wajen kallon ayyukan mutane da maganganunsu. Sau tari za ka ga wasu idan wani ya samu wata ni'ima ko wani cigaba na rayuwa sai su shi ga cikin baƙin ciki da ɓacin rai, da samun ƙunci da rashin walwala da kiɗimewa saboda wannan ci gaba da ya samu a raywarsa. Dayawa za ka ji idan musulmi sun zauna a majalisa babu abin da suke cewa sai dai.. Ko wani kaza yake nufi da abin nan da yayi, ko ya aikata. Babu abin da suke yi sai munana zato ga ‘yan uwansu, wanda baya haifar da komai sai kawo gaba da ƙyashi da kawo tarwatsewar hadin kan jama’a, da raba ‘yan uwantaka, da raba zumunci, da kawo shakku a ɗaiɗaikun al’umma.

Dayawa mun gani ko muna jin mutane suna faɗin irin sakamakon munanan zato da mutane suke yiwa juna. Idan kuma mummunan zato ya mamaye zuciya to babu abin da zai haifar sai saurin tuhamar juna, da kuma bin diddigin asiran mutane da zubar musu da mutunci, da binciken makusanci, har ka ji mai munana zato ga al'umma yana cewa "Zan yi ƙoƙarin gano haƙiƙanin abin da ake ciki" wajen bincikensa, sai kuma ya ci zarafin ɗan uwansa, ko ya aibata shi, aƙarshe sai ka ga ya yi laifi kashi-kashi. Lallai munana zato a tsakanin mutane yana kawo lalata alaƙa da gaba da kuma son zuciya da ruɗani, wannan kuma shi ya ke rusa soyayya a tsakanin mu, da kuma ƙeƙashewar zukata, da rashin amincewa juna. Sai su fara gaba da juyawa juna baya da yanke zumunta. Al'amarin da zai magance mana wannan shi ne faɗin Allah ta'al:

﴿ وَأَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَلَا تَنَٰزَعُواْ فَتَفۡشَلُواْ وَتَذۡهَبَ رِيحُكُمۡۖ وَٱصۡبِرُوٓاْۚ إِنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلصَّٰبِرِينَ ٤٦ ﴾

[الأنفال: ٤٦].

Ma'ana: (Kuyiwa Allah ɗa'a da manzonsa kuma kada ku yi saɓani a tsakanin ku, sai kuraraba kuma kwarjininku ya tafi, kuyi haƙuri, lallai Allah yana tare da masu haƙuri).

Al'umma sun kasance masu tarbiyya irinta musulunci, da kuma kyakkyawar zuciya, da 'yan uwantaka, da tausayi, kuma alaƙarmu takasance kamar ginin bulo da bulo.

Ya ku bayin Allah! Ku sani munana zato baya kawo alkhairi, sai dai ya zama ya kawo sharri da gaba da yanke zumunta, da tarwatsa dangi da ɓata 'yan uwantaka ta musulunci. Kaɗan ne daga cikin masu munana zato ba sa aikin saɓo. A lahira kuma za su yi nadama. Allah ya tsare mu. Allah (S.W.T) yana cewa:

﴿ وَقَالُواْ مَا لَنَا لَا نَرَىٰ رِجَالٗا كُنَّا نَعُدُّهُم مِّنَ ٱلۡأَشۡرَارِ ٦٢ أَتَّخَذۡنَٰهُمۡ سِخۡرِيًّا أَمۡ زَاغَتۡ عَنۡهُمُ ٱلۡأَبۡصَٰرُ ٦٣ ﴾

[ص: ٦٢ – ٦٣].

(Kuma suka ce, 'me ya same mu, ba muganin waɗansu mazaje mun kasance muna ƙidaya su daga asharara? Shin mun riƙe su abin izgili ne. ko idanunmu sun karkafta daga gare su ne?).

Masu tafsiri dadama sun fassara «Asharara» a wannan ayar da cewa ana nufin su ne raunanan musulmi, waɗanda ake masu izgili a nan duniya, ake tsammanin Allah ba zai taɓa musu rahma ba a lahira..

Kuma waɗanda mujrimai suka kasance suna yi musu isgilanci a nan duniya, suma za su rama a gobe alƙiyama kamar yadda Allah (S.W.T) ya ce:

﴿ إِنَّ ٱلَّذِينَ أَجۡرَمُواْ كَانُواْ مِنَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ يَضۡحَكُونَ ٢٩ وَإِذَا مَرُّواْ بِهِمۡ يَتَغَامَزُونَ ٣٠ وَإِذَا ٱنقَلَبُوٓاْ إِلَىٰٓ أَهۡلِهِمُ ٱنقَلَبُواْ فَكِهِينَ ٣١ وَإِذَا رَأَوۡهُمۡ قَالُوٓاْ إِنَّ هَٰٓؤُلَآءِ لَضَآلُّونَ ٣٢ وَمَآ أُرۡسِلُواْ عَلَيۡهِمۡ حَٰفِظِينَ ٣٣ فَٱلۡيَوۡمَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مِنَ ٱلۡكُفَّارِ يَضۡحَكُونَ ٣٤ ﴾ [المطففين: ٢٩ – ٣٤].

(Lalle ne waɗanda suka kafirta sun kasance (a duniya) suna yiwa waɗanda suka yi imani dariya. Kuma idan sun shuɗe su, sai su dinga yin zunɗe. Kuma idan suka juya zuwa ga iyalansu, sai su tafi suna kakaci. Kuma idan sun gansu sai su ce "lalle waɗannan ɓatattune". Alhali kuwa ba a aike su ba domin su zama masu tsaro akansu. To yaufa (a lahira) waɗanda suka yi imani, suke yiwa kafirai dariya).

Hakanan Allah ta’ala yana cewa:

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱجۡتَنِبُواْ كَثِيرٗا مِّنَ ٱلظَّنِّ إِنَّ بَعۡضَ ٱلظَّنِّ إِثۡمٞۖ﴾ [الحجرات: ١٢].

Ma’ana: (Yaku waɗanda suka yi imani, ku guji yawancin zato, domin wani ɓangare na zato zunubi ne).

Waɗannan ayoyi suna nuni akan kiyaye mutunci musulmi matuƙar kiyayewa, da rashin munana masa zato, idan kuma an ga wani yanayi to sai ayi masa nasiha.

Wannan kira ne ga muminai da su kiyaye kawunansu daga munana zato ga kowa, da samun hadin kai a tsakaninsu da rashin bibiyar asiran juna, kamar yadda ya zo a cikin littafin (Musannaf) na Abdurrazaƙ daga Abu Huraira yace daga Annabi (ﷺ) ya ce, “Ku guji zato, domin zato, shi ne mafi ƙaryar zance, kada ku riƙa satar maganganun juna, kada ku riƙa leƙan asirin juna, kuma kada ku riƙa yiwa juna hassada, kada ku yi gaba da juna, kada ku juya baya atsakaninku, ku zama bayin Allah ‘yan uwan juna.

Ya bayin Allah,

Wasu malamai sun ce. munana zato ga mutumin da halayensa na kirki suka bayyana da nagartarsa ta amanarsa, to haramun ne. Amma mutumin da halayensa marasa kyau, suka fito fili, ya kuma kasance mai bayyanar da ɓarna to babu laifi idan an munana masa zato.

An karɓo daga Sa’id ɗan Musayyib, yace “wani ɗan'uwana daga cikin sahabban Manzon Allah (S.W.A.) ya rubuto mini cewa, "Kasance mai kallon ɗan'uwan da kyawawan zato, har sai munanan halayensa sun bayyana gare ka. Duk kamlar da ta fito daga bakin ɗan uwanka, to kada ka yi mata mummunar fassara matuƙar kana iya ba ta kyakkyawar fassara".

Don haka, wannan ƙa'ida ce mai mahimmanci, musamman wajen mu'amalantar manyan mutane masu daraja cikin al'umma. Amma duk da haka sai ka ga wasu ba su fahimci hakan ba. Sai ka ga sun yanke wa mutum hukunci ba tare sun yi la'akari da niyyarsa ba. Mutum kuwa zai iya mummunar magana ba tare da ya yi nufi ba, illa iyaka zamiyar harshe ya samu, Kamar yadda Ibn Kayyim yake cewa, “Kalma ɗaya mutane biyu suna iya amfani da ita, ɗaya yana nufin mummunar ma’ana, ɗaya kuma baya nufin haka, saboda lura da halayensa, da abin da yake kira zuwa gare shi yake karewa. Don hakane ba’a kafirta mutumin da yayi kuskure ba saboda tsabar farin ciki ya ce, “Allah kai ne bawana, ni kuma Ubangijinka” kalmace ta kafirci idan muka kalleta da wannan ma’ana, amma shi da ya faɗeta, ba haka yake nufi ba ya faɗeta ne bisa kuskure saboda tsananin farin ciki.

Sheikhul Islam Ibn Taimiyya yake cewa lokacin da yake kallon maganar waɗanda suka saɓa masa, sai yace “Wannan magana dunƙulalliya, mai son gaskiya yana iya ba ta ma’ana mai kyau. Marar gaskiya kuma zai shigar abubuwa diyawa a ƙarƙashinta".

Wannan shi ne tsarin da malamai magabata na ƙwarai suka rayu akansa. saboda kasancewarsu masu tsarkakkiyar zuciya, da kaucewa son zuciya da yiwa al’umma nasiha, sukan kalli maganganun mutane ta fuska mai kyau.

Yaku bayin Allah, yana daga cikin munana zato, fassara maganganun wasu da aikinsu da mummunar fassara, da tuhuma ba tare da bincike ba, ko nema musu mafita, da ƙoƙarin yin mummunar fassara ga kowace magana ko aiki wanda yake ɗaukar fuska biyu, fuskar alkhairi da fuskar sharri. Don me mutane suke yin hukunci akan abin da yake cikin zukata, bayan kuma sanin abin da zuciya ta ɓoye da hisabinta haƙƙine na Allah (S.W.T) wanda shi ne masanin abin da yake ɓoye da bayyane. Amma shi ɗan Adam ba shi da haƙƙin shiga cikin abin da yake ɓoye, sai dai abinda yake bayyane. wannan shi ne abinda magabata na ƙwarai suka kasance akansa, waɗanda zukatansu suke cike da ilimi na musulunci tatacce.

Abdurrazzaƙ ya ruwaito hadisi a cikin littafinsa Al-Musannaf daga Abdullah ɗan Utbah ɗan Abdullah ɗan Mas'ud ya ce: Na ji Umar ɗan Khaɗɗab (R.A) ya ce "Mutane ana gane kurakuransu a zamanin Manzon Allah (ﷺ) ta hanyar wahayi. Amma yanzu wahayi ya daina sauka, don haka mu yanzu muna gane kurakuranku ne da abin da ya bayyana na ayyukanku. Duk wanda ya bayyana mana alherinsa, sai mu zauna da shi lafiya, kuma mu kusanto shi, babu ruwan mu da abin da yake na zuciyarsa, Allah shi ne zai yi masa hukunci akan abin da ya ɓoye a zuciyarsa. Wanda kuma ya bayyanar mana da sharrinsa, to ba zamu amince masa ba, kuma ba zamu gaskata shi ba, koda ya ce, shi da zuciya ɗaya yake zaune da mu".

Ya zama wajibi akan kowa ne musulmi ya binciki kansa game da kowace kalma da zai furta,ko wani hukunci da zai yanke, ya riƙa tuna faɗin Allah ta'ala,

﴿ وَلَا تَقْفُ مَا لَيْسَ لَكَ بِهِۦ عِلْمٌ ۚ إِنَّ ٱلسَّمْعَ وَٱلْبَصَرَ وَٱلْفُؤَادَ كُلُّ أُوْلَٰٓئِكَ كَانَ عَنْهُ مَسْـُٔولًا ﴿٣٦﴾ ﴾

[الإسراء: ٣٦]

"Kuma kada ka bi abin da ba ka da ilimi game da shi. Lalle ne ji da gani da zuciya, dukkan waɗannan, abin da ake tambayar mutum ne akansu) (Suratul Isra'i 35).

Abin da kuke ji shi ne abin da zan faɗa muku. Ina kuma neman gafarar Allah gare ni da kuma sauran musulmi daga kowane zunubi, ku nemi gafarar Ubangiji, domin shi mai gafara ne, mai rahama.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, babu wanda fushin Allah yake sauka akansa sai azzalumai, tsira da aminci su tabbata ga shugaban manzanni, Annabin mu Muhammad kuma masoyinmu, da kuma iyalansa da sahabbansa da kuma waɗanda suka bi tafarkinsu har zuwa ranar sakamako.

Ya ku bayin Allah! Mummuna zato yana da wasu dalilai da suke haddasa shi. Babban abin da yake haddasa ɗabi'a ta mummunan zato shi ne tarbiyyar da mutum ya samu daga gida ko ya abokai. Domin duk sanda mutum ya biye wa son zuciyarsa, sai ka ga ya faɗa cikin ɗabi'ar munana zato. Idan mutum yana son abu sai ya makance ya kurumce. Hakanan idan ya so wani, sai ka ga ya rufe idonsa ba ya ganin kuskurensa ko da kuwa yana da kuskuren. Idan kuma ba ya son mutum, to ba zai taɓa ga farinsa ba. Ko da yaushe zai riƙa bin diddingasa ne don ya samo

kurakuransa.

Waɗansu mutane kuwa suna ruɗawa da cewa a kodayaushe su ne mutanen kirki, sauran mutane kuma akan kuskure suke, yana mai tsarkake kansa, yana raina wasu. Sai wannan ya gadar masa da mummunan zato. Lallai mummunan zato tsakanin musulmi abu ne wanda ya yaɗu a wannan zamani. Aka wayi gari ‘yan uwantaka da take tsakanin al’umma tayi rauni, Wannan kuwa zai jawo musu rauni wajen fuskantar ƙalu-bale na cikin gida da waje.

Yaku bayin Allah! Lalle an cuci mutane dadama ta hanyar munana musu zato da tuhumarsu akan abin da ba ji ba ba su gani ba. Hakanan an ƙauracewa wasu mutanen kiriki dadama a sanadiyyar wannan mummunar ta’ada. Allah (S.W.T) ya ce:

﴿ وَٱلَّذِينَ يُؤْذُونَ ٱلْمُؤْمِنِينَ وَٱلْمُؤْمِنَٰتِ بِغَيْرِ مَا ٱكْتَسَبُوا۟ فَقَدِ ٱحْتَمَلُوا۟ بُهْتَٰنًا وَإِثْمًا مُّبِينًا ﴿٥٨﴾ ﴾ [الأحزاب: ٥٨].

(Lalle waɗanda suke cutar da muminai maza da mata, ba tare da abin da suka aikata ba, haƙiƙa sun ɗaukarwa kansu wani mummunan ƙage da laifi mabayyani).

Idan muka gamsu da cewa mummunan zato abu ne mai halakarwa, to tilas ne mu tashi domin magance wannan matsalar saobda kada ɓarna ta yaɗu ta game ko-ina-da-ina.

Daga cikin hanyoyin magance wannan matsala, akwai kyautata zato ga mutane, da nisantar munana zato, da ƙoƙarin zurfafa tunani mai tsawo kafin ka yanke hukunci ko tuhuma. A koda yaushe kuskure wajen kyautata zato ga mutane, ya fi alheri sama da kuskure wajen munana zato ga mutane. Umar bn Khaɗɗab yake cewa “Kada ka yi wani zato daga duk wata kalma da fito daga ɗan uwanka mumini sai na alheri, matuƙar hakan mai yi wu wa ne”.

Daga cikin hanyoyin magance mummunan zato, akwai bawa mutane uzuri, da rashin bibiyar asiransu, da kallon zamiyarsu. da ƙoƙarin siffantowa da kyawawan ɗabi’u na musulunci wajen hukunci ga mutane, da kuma amfani da abin da yake a bayyane da barin abinda yake a ɓoye ga Allah (S.W.T) masanin abin da yake a bayyane da ɓoye.

Yaku bayin Allah kuji tsoron Allah ku fahimci faɗin Allah ta’ala:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ٱجْتَنِبُوا۟ كَثِيرًا مِّنَ ٱلظَّنِّ إِنَّ بَعْضَ ٱلظَّنِّ إِثْمٌ ۖ وَلَا تَجَسَّسُوا۟ وَلَا يَغْتَب بَّعْضُكُم بَعْضًا ۚ أَيُحِبُّ أَحَدُكُمْ أَن يَأْكُلَ لَحْمَ أَخِيهِ مَيْتًا فَكَرِهْتُمُوهُ ۚ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ تَوَّابٌ رَّحِيمٌ ﴿١٢﴾ ﴾ [الحجرات: ١٢].

(Ya ku waɗanda suka yi imani ku guji yawayawancin zato, lalle wani zaton laifi ne. Kuma kada ku yi leƙen asiri. Kuma kada sashenku yayi gibar sashe, shin ɗayanku na son yaci naman ɗan uwansa yana matacce, to kunƙi hakan. Kuma ku bi Allah da taƙawa, lalle Allah mai karɓar tuba ne mai jin ƙai).

IDIN KARAMAR SALLAH

Manufofin huɗubar

- Bayanin cewa kowace al'umma tana da idi, da banbance idin musulmi.
- Amfanunnukan idi.
- Bayanin dacewar fitar mata zuwa idi a shari'ance.
- Zaburarwa ga ayyukan kirki, da tsoratarwa game da zunubai.
- Bayanin sunnoni da ladubban idi.
- Falalar azumtar shida ga watan Shawwal.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga shirrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammad bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammad (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Bayan haka:

Ku ji tsoron Allah ya ku musulmai haƙiƙanin jin tsoron Allah, ku yi riƙo da igiya ƙaƙƙarfa ta musulunci, ku nemi yardar Ubangijinku ta hanyar yi masa ɗa'a, haka nan ku guji fushinsa ta hanyar barin saɓa masa.

Ya ku musulmai! Lallai ne kowace al'umma tana da biki (idi), wanda yake maimaituwa a gare su a wasu lokuta keɓantattu. Idin yakan ƙunshi aƙidojinsu da al'adunsu da abubuwan da suka gada da abubuwan da suke so, da burace-buracensu. Kowace al'umma tana da matuƙar farin ciki a idinta, takan kuma yi farin ciki da haɗuwar da ake yi, haka nan sukan girmama lokacin, kuma su zaɓi guri mai tsari, sannan su sanya kaya sababbi, sukan yi kwalliya da kaya iri-iri. Haka nan Allah Ya ƙaddarawa kowace al'umma, har al'ummomin jahiliyya,

bukukuwa daban-daban, domin zama fitina a gare su da kuma ƙari a kan ɓatansu, kamar yadda Allah maɗaukaki yake cewa:

﴿ وَلَا يَحۡسَبَنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ أَنَّمَا نُمۡلِي لَهُمۡ خَيۡرٞ لِّأَنفُسِهِمۡۚ إِنَّمَا نُمۡلِي لَهُمۡ لِيَزۡدَادُوٓاْ إِثۡمٗاۚ وَلَهُمۡ عَذَابٞ مُّهِينٞ ١٧٨ ﴾ [آل عمران: ١٧٨].

(Kuma kada waɗanda suka kafirta su yi zaton cewa lallai ne jinkirin da Muke yi musu alheri ne ga rayukansu. Muna yi musu jinkirin ne domin su ƙara laifi kawai, kuma suna da azaba mai wulaƙantarwa).

Hakanan Allah yana faɗa:

﴿ لِّكُلِّ أُمَّةٖ جَعَلۡنَا مَنسَكًا هُمۡ نَاسِكُوهُ ﴾[الحج: ٦٧].

(Ga kowace al'umma Mun sanya wurin yanka, su ne masu yin baiko gare shi…..).

Ɗan Abbas Allah Ya yarda da su ya ce, (Almansak- wurin baiko - yana nufin idi). An karɓo hadisi daga Anas, Allah ya yarda da shi, ya ce: manzon Allah ya iso Madina kuma muna da ranaku biyu da muke wasa a cikinsu sai ya ce: "lallai Allah ya musanya muku da abin da ya fi su alkhairi (su ne) idin ƙaramar sallah da idin babbar sallah».

Bukukuwan sauran al'ummomi waɗanda ba na musulunci ba, bukukuwa ne na jahiliyya da suke cike da ɓata, ba su da wata manufa managarciya da maslaha ta duniya da lahira, babu maganar tausayi ko jin ƙai a ciki, kamar yadda Allah Maɗaukaki yake cewa,

﴿ وَمَن يَبۡتَغِ غَيۡرَ ٱلۡإِسۡلَٰمِ دِينٗا فَلَن يُقۡبَلَ مِنۡهُ وَهُوَ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ مِنَ ٱلۡخَٰسِرِينَ ٨٥ ﴾ [آل عمران: ٨٥].

(Kuma wanda ya nemi wanin Musulunci ya zama addini, to, ba za a karɓa daga gare shi ba. Kuma shi a lahira yana daga cikin masu hasara).

Amma idi a musulunci yana da manufa mai girma, da karamci da cikakken amfani, da maslaha ta duniya da lahira. Musulunci yana da idi guda biyu. Idin ƙaramar sallah da idin babbar sallah. Kuma dukkansu suna zuwa ne bayan wata ibada mai girma, kuma a bayan wani rukuni daga cikin rukunan musulunci, kuma akan yi shi a mafificin lokaci. Idin babbar sallah yakan kasance a ƙarshen tsayuwar Arfa, kuma yakan kasance a ranar Alhajjul Akbar (wato goma ga zulhijja). Idin ƙaramar sallah kuwa yakan kasance bayan an gama azumin watan Ramadan. Haka kuma sukan kasance bayan ƙoƙari da dagewa a ayyukan ibada da yawaita ɗa'a, a cikin ranaku da darare masu ɗaukaka da falala, da kuma wasu sa'o'i masu albarka da ake ninninka lada, kuma musulmi yake tsoron uƙuba a cikinsu. Musulmi sukan yi rigegeniya a wannan lokaci, sukan ribaci waɗannan sa'o'i da ayyuka na gari. Sukan yi iya bakin ƙoƙarinsu wajen bautar Ubangijinsu da yi masa biyayya, har sai yayin da ruhin ɗan adam ya sami abin da take so, ta ƙoshi da abincinta, sanna kuma gajiya ta fara rufe ta; ƙarfi ya fara ƙarewa, sai Allah Ta'ala ya buɗewa bawansa wata ƙofa ta samin hutu, da shaƙatawa, domin a samu kalamar tarbiyyar jiki da ta ruhi, duk domin mutum ya iya shirin tinkarar sauran ibadu.

Ya tabbata a cikin hadisi daga manzon Allah (ﷺ): "Lallai Ubangijinka yana da haƙƙi a kanka, kuma jikinka yana da haƙƙi a kanka, lallai matarka tana da haƙƙi

a kanka, kuma masu ziyararka suna da haƙƙi a kanka, don haka ka ba wa kowane mai haƙƙi haƙƙinsa”

Wani daga cikin magabata yana cewa: “Ku dinga hutar da ƙwaƙwalenku a wasu lokuta domin su ma suna gajiya kamar yadda jiki yake gajiya”

Addinin musulunci yakan bi mutum musulmi a hankali kuma mataki-mataki, daga nan zuwa can, daga wannan yanayi zuwa wani yanayin, daga abu kyakkyawa zuwa wanda ya fi shi kyau, domin ya jadda masa rayuwarssa da karsashinsa, don ya iya cimma abin da zai amfane shi, ya dace da kowane irin alheri.

Haka nan, idi yana daga cikin alamomin musulunci na zahiri, kuma ina cike da hikimomi da amfani iri-iri, ta fuskar aƙida, da ibada da amfaninsa a shari’a, kuma amfaninsa a wurin zamantakewar al’umma, da kuma amfaninsa a duniya da lahira.

Ya bayin Allah!

Dangane da amfanin idi ta fuskar aƙida: lallai hukunce-hukuncen idi suna nanata kaɗaitar Allah ga bayinSa da wajabcin bauta masa shi kaɗai ba tare da abokin tarayya ba. Da abin da ya ƙunsa na addu’o’i da girmamawa da miƙa wuya da sallamawa da soyayya, da makamantan haka na abubuwan da suke kasance haƙƙin Allah ne shi kaɗai. Allah yana cewa:

Ma'ana: (Kuma lallai ne wuraren sujuda na Allah ne, saboda haka kada ku kira kowa tare da Allah (a cikinsu)).

Amfanin Idi kuwa ta ɓangaren ibada: Haƙiƙa koyarwar idi, tana tabbatar da bauta ga Allah ubangijin talikai, ta yadda ƙanƙan da kai da saduda suke tabbata ga Allah gami da soyayya. Haka nan jigon ibada yana komawa ne zuwa ga soyayya don Allah saduda domin Allah da tsoro don Allah. Wani daga cikin magabata yana cewa: (wanda ya bauta wa Allah da tsoro kawai to wannan ɗan Khawarij ne, wanda kuma ya bauta wa Allah da soyayya kawai, wannan zindiƙi ne, wanda kuma ya bauta wa Allah da saduda da tsoro da soyayya, to wannan shi ne cikakken mai bauta), Allah maɗaukakin sarki yana cewa,

﴿إِنَّهُمۡ كَانُواْ يُسَٰرِعُونَ فِي ٱلۡخَيۡرَٰتِ وَيَدۡعُونَنَا رَغَبٗا وَرَهَبٗاۖ وَكَانُواْ لَنَا خَٰشِعِينَ ٩٠﴾

[الأنبياء: ٩٠].

(Lallai ne su sun kasance suna tsereren iya zuwa ga ayyukan alheri. Kuma suna kiranmu a kan kwaɗayi da fargaba. Kuma sun kasance masu ƙin aikata saɓo gare mu).

Dangane da amfanin idi kuwa ta fuskar shari’a, Idi yana ƙunshe da bayyana farillan addinin musulunci da alamomin addini da yayata koyarwar addini, da sanar da shari’o’in imani, domin addinin musulunci ya ci gaba da zama a tsare kuma mai ƙarfi mai kariya ta yadda ba zai rusu ba. Sannan ta yadda masu ƙoƙarin jirkita shi da lalata shi ba za su iya ci nasara ba, domin addinin musulunci ƙaƙƙarfa ne ta hanyar shari’o’insa. Ya dace da halittar ɗan Adam. Haka nan koyarwar hukunce-hukuncen addinin musulunci takan kasance mai sauƙi ga babba da ƙarami da namiji da mace da na kusa da na nesa.

Rukunan addinin musulunci a fili suke, sannan iyakokinsa sanannu ne a fili suke, haka nan koyarwarsa da hukunce-hukuncensa sun watsu ko’ina, kuma addini

ne na duniya baki ɗaya. Allah maɗaukakin sarki yana cewa,

﴿ فَأَقِمۡ وَجۡهَكَ لِلدِّينِ حَنِيفٗاۚ فِطۡرَتَ ٱللَّهِ ٱلَّتِي فَطَرَ ٱلنَّاسَ عَلَيۡهَاۚ لَا تَبۡدِيلَ لِخَلۡقِ ٱللَّهِۚ ذَٰلِكَ ٱلدِّينُ ٱلۡقَيِّمُ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعۡلَمُونَ ٣٠ ﴾ [الروم: ٣٠].

(Saboda haka ka tsayar da fuskarka ga addini, kana mai karkata zuwa ga gaskiya, halittar Allah da Ya halitta mutane a kanta. Babu musanyawa ga halittar Allah. Wannan shi ne addini maidaidaici, kuma amma mafi yawan mutane ba su sani ba).

Kuma saboda wannan ƙarfin da yake da shi, wannan yakan ƙara wa addinin kyau, kuma yakan ƙara faɗaɗa, yakan tabbata ba tare da raurawa ba. Ya , kuma kamar haskenta yake a wajen kusantowarsa. Ya zama kamar rana wajen ɗaukakarsa, wanda ya mame kowa da haskensa Godiya ta tabbata ga Allah da ya sanya mu muka zama musulmai. Shi ne addinin adalci da aminci da nutsuwa da sa'ada, shi ne addinin 'yan uwantaka, addinin alkhairi. Addinin da ke kwaɗaitarwa ga dukkanin wani alheri, yake hani ga barin kowane sharri.

Amma amfanin idi a rayuwar al'umma gaɓa ɗaya, shi ne yakan tabbar da haɗin kai da haɗuwar zuciya tsakanin musulmai, da kawar da duk wani barin gutsuri tsoma da fushi da ƙullata. Akan sami cikar jin ƙai da rahama da ziyarce-ziyarce, yanke zumunci yakan ƙare. Akan yi musayar abubuwa masu amfani. Ya zo a cikin hadisi: (kwatankwacin musulmai a cikin soyayyarsu da jin ƙansu da tausayinsu kamar jiki ne guda, idan wani sashe ya kamu da rashin lafiya, dukkanin sauran jiki ma sai ya karɓa da rashin barci da zazzaɓi). Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.

Daga cikin amfanin idi da hikimominsa da manufofinsa shi ne yaddyyana buƙatarsu wajen ubangijinsu, ba kuma za su iya wadatuwa daga taimakonsa ba daidai da ƙiftawar ido. Sukan yi tawasulli zuwa ga Allah domin ya biya musu buƙatunsu da gyara musu al'amuransu ta hanyar sallar idi a cikin jam'i, da jin ambaton Allah da ni'imomin Allah da falalolinsa. Haka nan da sanin hukunce-hukuncen addinin musulunci a huɗuba. Wannan ya sa su sami alheri mai girma da gamammiyar falala wadda al'ummomin da suka gabace su ba su samu irin wannan ba. Don haka godiya ta tabbata ga Allah a bisa gamewar ni'imarsa da ɗaukakar karamcinsa.

Ya ku bayin Allah, saboda garaɓasar wannan idi, da kuma abin da ya tattara na rahama da albarka, sai Manzon tsira (ﷺ) ya yi umar da a fita zuwa gare shi, hatta mata masu haila da 'yan mata, amma ba tare da sun yi fitar nuna tsiraici da sanya turare da nuna kwalliya ba, duk domin su sami wannan alherin. Daga Umm Aɗiyyah, Allah ya yarda da ita tana cewa: "Manzon Allah (ﷺ) ya umarce mu da mu fito da 'yammata, da masu haila a yayin idin ƙaramar salla da babba, amma su masu haila sai su nisanci wurin sallah, su ma su sami alheri, su kuma saurari addu'o'in musulmai. Sai na ce, "Ya manzon Allah, ɗayarmu ba ta da abin da za ta rufe jikinta". Sai ya ce, "'Yar uwarta ta ara mata nata abin rufe jikin". Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

A wata ruwayar ta Bukhari ta ce: “Mun kasance ana umartarmu da fita a ranakun idi har akan umarci ‘yan mata su fita daga wuraren da suke zaune, har mai haila, sai su dinga yin kabbara idan musulmai sun yi kabbara, kuma su dinga yin addu’a idan sun yi addu’a, suna fatan albarkar wannan rana da tsarkinta.

Allah Akbar Allah Akbar Allah Akbar, La’ilaha illallah, wallahu akbar Allah Akbar, walillahil hamdu.

Ya ku bayin Allah, ku yi riƙo da sallah domin ita ce jigon addini, kuma mai hani ce daga alfasha da zunubai, ku tsayar da ita a cikin gidajen Allah kuma a cikin jam’i, domin ita ce abu na farko da za a tambayi bawa a kansa ranar alƙiyama, idan aka karɓe ta, to sai a karɓe ta da sauran ayyukan, idan kuma aka mayar da ita, to sai a mayar da ita da sauran ayyukan.

Ku fitar da zakkar dukiyoyinku wadda za ta tsarkake zukatanku, dukkan wanda ya fitar da ita yana tare da albarka, kuma akwai busharar lada a gare shi. Haka nan duk wanda ya yi rowa game da zakkarsa to an toshe albarkar dukiyarsa kuma azaba mai raɗaɗi da uƙuba za su tabbata a gare shi.

Ku azumci watan azumi, ku yi aikin hajji ga ɗakin Allah mai tsarki, za ku shiga aljanna tare da aminci. Hakanan ku riƙi yin biyayya ga iyaye da kuma sadar da zumunci. Domin haƙiƙa duk wanda ya yi riƙo da wannan ya tsira. Ku kyautata kula da matanku na aure da ‘ya’yanku da masu yi muku hidima da duk wanda Allah ya damƙa al’amarinsa a hannunku. Ku kula da haƙƙoƙinsu, kuma ku tafi da su a kan abin da zai amfane su, ku guji abin da zai cutar da su. Ubangiji maɗaukakin sarki yana cewa,

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ قُوٓاْ أَنفُسَكُمۡ وَأَهۡلِيكُمۡ نَارٗا وَقُودُهَا ٱلنَّاسُ وَٱلۡحِجَارَةُ عَلَيۡهَا مَلَٰٓئِكَةٌ غِلَاظٞ شِدَادٞ لَّا يَعۡصُونَ ٱللَّهَ مَآ أَمَرَهُمۡ وَيَفۡعَلُونَ مَا يُؤۡمَرُونَ ٦ ﴾ [التحريم: ٦].

(Ya ku waɗanda suka yi imani, ku kare kawunanku da iyalinku daga shiga wuta, makamashinta mutane da duwatsu ne. Masu gadinta waɗansu mala’iku ne kaushi, masu ƙarfi. Ba su saɓawa Allah ga abin da Ya umarce su, kuma suna aikata abinda aka umarninsu).

Hakanan ya zo a cikin hadisi: “Kowannenku mai kiwo ne, kuma kowannenku abin tambaya ne game da abin da aka ba shi kiyo». Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi, daga Ibn Umar.

Allah Akbar Allah! Akbar Allah Akbar! La’ilaha illallah, wallahu akbar Allah Akbar, walillahil hamd.

Ya ku musulmai, ku kiyayi yin tarayya da Allah maɗaukakin sarki a wajen addu’a ko neman taimako ko neman agaji, ko yanka ko bakance ko tawakkali, ko wani abu makamancin wannan daga cikin nau’ikan ibadu waɗanda ake yin su domin Ubangijin talikai kawai. Duk wanda ya yi shirka da Allah a cikin bautarsa, haƙiƙa Allah ya haramta masa aljanna. Ubangiji maɗaukakin sarki yana cewa:

﴿ إِنَّهُۥ مَن يُشۡرِكۡ بِٱللَّهِ فَقَدۡ حَرَّمَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِ ٱلۡجَنَّةَ وَمَأۡوَىٰهُ ٱلنَّارُۖ وَمَا لِلظَّٰلِمِينَ مِنۡ أَنصَارٖ ٧٢ ﴾[المائدة: ٧٢].

(Lalle duk wanda ya yi tarayya da Allah, to haƙiƙa Allah ya haramta masa

aljanna, kuma makomarsa wuta ce, kuma azzalumai ba su da wasu mataimaka.)

Ku guji kashe rai wadda Allah ya haramta, domin ya zo a cikin Sahihil Bukhari daga hadisin Ɗan Umar, Allah ya yarda da su ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Bawa ba zai gushe ba yana zaman lafiya da addininsa matuƙar dai bai zubar da jinin da aka haramta ba”.

Haka nan ku guji riba, domin riba tana gadar da fushin Ubangiji, kuma tana cinye albarkar dukiya da kwanaki, ku guji zina, domin zina bala’i ce mai kai mutum wuta. Ubangiji maɗaukakin sarki yana cewa:

﴿ وَلَا تَقۡرَبُواْ ٱلزِّنَىٰٓۖ إِنَّهُۥ كَانَ فَٰحِشَةٗۖ وَسَآءَ سَبِيلٗا ٣٢ ﴾ [الإسراء: ٣٢].

(Kuma kada ku kusanci zina. Lallai ne ita ta kasance alfasha ce, Kuma hanyarta ta yi muni ƙwarai).

Kuma ku guji irin aikin Mutanen Annabi Luɗ, domin Allah ya la’anci wanda yake aikata wannan, kuma manzon Allah ya la’anci mai aikata hakan. An karɓo daga Ɗan Abbas, Allah ya ƙara musu yarda ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce “Allah ya la’anci wanda yake aikata aikin mutanen Annabi Luɗ, Allah ya la’anci wanda yake aikata aikin mutanen annabi Luɗ, Allah ya la’anci wanda yake aikata aikin mutanen annabin Luɗ”. Imam Ahmad da Hakim ne suka ruwaito shi.

Haka nan ina gargaɗinku ku guji kayan maye masu gusar da hankali, domin su fitina ce mai halakarwa, kuma suna gadar da fushin Ubangiji, kuma sukan nuna mutum a wata irin sifa, wadda zai dinga ganin abu mai kyau a matsayin mummuna, mummuna a matsayin mai kyau.

An karɓo daga Jabir, daga manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Duk wani abu mai sa maye haramun ne, kuma lallai akwai Allah ya yi alƙawari ga duk mai shan abin maye cewa zai shayar da shi daga ruwan gulandon ‘yan wuta”. Imam Muslim da Nasa’i ne suka rawaito shi.

Ku guji dukiyar musulmai da kuma zaluntarsu. Duk wanda ya yanki taƙi ɗaya na ƙasa ba tare da haƙƙi ba, Allah zai yi misa 'yar wuya da ƙassai bakwai.

Ku guji dukiyar marayu da miskinai. Domin wannan yana jawo talauci da lalacewa, da uƙuba ta gaggawa.

Ku guji yin ƙazafi ga mata masu kamun kai, domin wannan yana daga abubuwa masu halakarwa.

Ku guji yin giba da annamimanci, domin wannan zalunci ne ga musulmi, kuma saɓo ne mai tafiyar da ayyukan ƙwarai ga mai yi, kuma Allah ya haramta hakan a cikin Alƙur’ani.

Ku guji jan kaya a ƙasa da alfahari da takama, domin Abu Huraira Allah ya ƙara yarda a gare shi ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Duk abin da ya wuce idon sawu na daga izari to yana cikin wuta”. Bukhari ne ya ruwaito shi.

Ya ku taron mata ku ji tsoron Allah, ku yi ɗa’a ga Allah da manzonSa. Ku kiyaye sallolinku, kuma ku yi ɗa’a ga mazajen aurenku, ku kula da haƙƙoƙinsu, ku kyautata zama da maƙota, kuma ku lura da tarbiyyar ‘ya’yanku ta hanyar tarbiyyar musulunci da riƙo da amana.

Don haka ku guji nuna tsaraici da rashin kamun kai da cakuɗeɗeniya da maza, ku yi riƙo da sutura da kamewa, za ku kasance daga cikin masu rabauta, kuma za ku shiga aljanna tare da mata na ƙwari, kuma Ubangijin sammai da ƙassai zai yarda da ku.

Daga Abdurrahman ɗan Auf, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Idan mace ta sallaci sallolinta guda biyar, kuma ta azumci watanta, kuma ta kiyaye farjinta, kuma ta yi biyayya ga mijinta, za a ce mata: ki shiga aljanna daga kowace ƙofa da kike so". Imam Ahmad da Ɗabarani ne suka rawaito.

Haka nan, an karɓo daga ɗan Abbas Allah ya yarda da su ya ce: "na halarci sallar idin ƙaramar sallah tare da manzon Allah (ﷺ) sai ya je wajen mata tare da Bilal, sai ya karanta masu faɗar Allah:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ إِذَا جَآءَكَ ٱلۡمُؤۡمِنَٰتُ يُبَايِعۡنَكَ عَلَىٰٓ أَن لَّا يُشۡرِكۡنَ بِٱللَّهِ شَيۡـٔٗا وَلَا يَسۡرِقۡنَ وَلَا يَزۡنِينَ وَلَا يَقۡتُلۡنَ أَوۡلَٰدَهُنَّ وَلَا يَأۡتِينَ بِبُهۡتَٰنٖ يَفۡتَرِينَهُۥ بَيۡنَ أَيۡدِيهِنَّ وَأَرۡجُلِهِنَّ وَلَا يَعۡصِينَكَ فِي مَعۡرُوفٖ فَبَايِعۡهُنَّ وَٱسۡتَغۡفِرۡ لَهُنَّ ٱللَّهَۖ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ١٢ ﴾ [الممتحنة: ١٢].

(Ya kai wannan Annabi! Idan mata muminai suka zo maka suna yi maka mubaya'a a kan ba za su yi shirka da Allah ba ga komai, kuma ba za su yi sata ba, kuma ba za su yi zina ba, kuma ba za su kashe 'ya'yansu ba, kuma ba za su zo da ƙarya da suke ƙiƙirarta daga tsakanin hannuwansu da ƙafafunsu, kuma ba za su saɓa maka ga wani abu da aka sani na shari'a ba, to, ka karɓi mubaya'arsu, kuma ka nemi Allah ya gafarta musu. Lallai Allah Mai gafara ne Mai jinƙai). Sai ya ce: (kun yarda da wannan), wata mata ta ce: Na'am ya manzon Allah.

Imam Ahmad ya rawaito cewa, Umamata Bint Ruƙayya ta yi wa manzon Allah mubaya'a a kan wannan ayar. A cikinsa kuma akwai faɗar cewa "Kada ku riƙa rusa kuka don mutuwa, kuma kada ku yi fitar ƙyale-ƙyale, irin fitar ƙyale-ƙyalen jahiliyya".

Ma'anar: " kuma ba za su zo da ƙarya da suke ƙiƙirarta daga tsakanin hannuwansu da ƙafafunsu" shi ne ka da su zo da wasu 'ya'ya da ba na mazajensu ba su ce na su ne.

Allah Akbar Allah Akbar Allah Akbar, La'ilaha illallah, wallahu akbar Allah Akbar, walillahil hamdu.

Bismillahi Rahmanir Rahim. Allah yana cewa:

﴿ وَإِذَا قُرِئَ ٱلۡقُرۡءَانُ فَٱسۡتَمِعُواْ لَهُۥ وَأَنصِتُواْ لَعَلَّكُمۡ تُرۡحَمُونَ ٢٠٤ ﴾ [الأعراف: ٢٠٤].

(Kuma idan an karanta Alƙur'ani sai ku saurare shi, kuma ku yi shiru, La'alla ko kwa samu rahama).

Allah ya yi albarka gare ni da ku a cikin Alƙur'ani mai girma, ya amfane ni da ku daga abin da yake cikinsa na ayoyi da tuntuntuni na hikima, kuma ya amfane mu da koyarwar shugaban mursalai, da maganarsa daidaitacciya. Abin da zan faɗa ke nan. Ina neman gafarar Allah mai girma gare ne da ku da sauran musulmai daga kowane zunubi, ku nemi gafararsa domin Shi Mai yawan gafara ne Mai yawan rahama.

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, kyakkyawan ƙarshe yana ga masu tsoron Allah, babu taɓewa sai ga azzalumai, da tsira da aminci bisa cikamakin annabawa, Annabi Muhammad sallallahu alaihi wasallam. Bayana haka:

Allah Akbar! Allah Akbar!! Allah Akbar!!! La'ilaha illallah, wallahu akbar, Allah Akbar, walillahil hamdu.

Allahu Akbar kwatankwacin adadin abin da ya halitta a sama. Allahu Akbar kwatankwacin adadin abin da ya halitta a ƙasa. Allahu Akbar kwatankwacin adadin abin da ke tsakanin waɗannan. Allahu Akbar kwatankwacin adadin komai, Allahu Akbar kwatankwacin cikar komai, Allahu Akbar kwatankwacin abin da littafi ya ƙididdige.

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin sammai da ƙassai, mai jiɓintar al'amarin komai, mai amsa addu'o'i, yakan karɓi tuba daga bayinsa kuma yakan yi afuwa daga munanan ayyuka. Ba wani abu da ya fi ƙarfin Allah ya yi kauta da shi. afuwarsa ba ta tawaya domin ya yi yafiya ga manyan zunubai. Ina godewa Ubangijina a bisa kyawawan ni'imominsa da ba sa yankewa a wani lokaci daga cikin lokuta. Ina shaidawa babu abin bautawa da gaskiya bisa cancanta sai Allah, Shi kaɗai ba shi da abokin tarayya, yana da sunaye mafiya kyau, da siffofi masu girma. Haka nan ina shaidawa cewa manzonmu, kuma shugabanmu Annabi Muhammad, bawanSa ne kuma manzonSa ne, wanda aka aiko shi da bayyanannun hujjoji. Ya Allah Ka ƙara daɗin tsira da aminci da albarka a kan bawanka kuma manzonka, Annabi Muhammad, da iyalansa da sahabbansa, kyawawan shuwagabanni.

Ku ji tsoron Allah ya ku musulmai, ku yi masa ɗa'a, ku nemi yardarsa kuma kar ku saɓa masa. Ya ku musulmai, lallai wannan idin naku idi ne mai karamci, kuma taro ne mai girma. Allah yakan sanya alheri da dama a cikinsa ga al'ummar muslmai. Haka kuma Ubangijinmu ya shar'anta wasu hukunce-hukunce a wannan Idi. Hakanan Annabi (ﷺ) ya sunnanta sunnoni a cikinsa:

Allah ya shar'anta yin wanka kafin a fita sallar Idi. Kuma babu laifi idan mutum ya yi wanka tun kafin alfijir ya keto Idan har yin hakan ya fi masa sauƙi. Haka nan an sunnanta yin kwalliya da kaya masu kyau. Ya zo a cikin hadisi; "lallai Allah yayin da ya yi wata ni'ima ga bawa, Yana son ya ga ɓurɓushin wannan ni'imar tare da shi". Ibn Sa'ad da Ɗahawi ne suka ruwaito shi.

Kuma sunna ce yin asuwaki da sanya turare, da aske gashin baki da kuma yanke farce. Amma kar mutum ya kuskura ya aske gemunsa, domin yin hakan haramun ne.

Har ila yau, an sunnanta mutum ya fara cin dabino kafin cin komai. Sannan kuma mutum ya sauya hanyar da yi bi a yayin zuwa yayin komawa. Sannan bayan haka, an sunnanta bayyana kabarbari a daren idi, kuma musulmi su bayyana kabarbarinsu a yayin fita zuwa wajen yin salla har sai liman ya fara huɗuba, sai ya ce:

Allah Akbar Allah Akbar Allah Akbar, La'ilaha illallah, wallahu akbar Allah Akbar, walillahil hamdu.

Yana daga cikin hikimar yin kabarbari shi ne girmama Ubangiji da kuma turbuɗe hancin shaiɗan da ƙasƙantar da shi, da wulaƙanta shi. Da kuma bayyana cewa musulmi ya fi ƙarfin zuciyarsa da wani kwaɗayi na duniya, da bayanin cewa lallai Allah shi ne ya fi komai girma da ɗaukaka a zuciyar musulmi.! Allah maɗaukakin sarki yana cewa:

﴿وَلِتُكۡمِلُواْ ٱلۡعِدَّةَ وَلِتُكَبِّرُواْ ٱللَّهَ عَلَىٰ مَا هَدَىٰكُمۡ وَلَعَلَّكُمۡ تَشۡكُرُونَ ١٨٥﴾ [البقرة: ١٨٥].

(… Kuma domin ku cika adadin, kuma domin ku girmama Allah a kan ya shiryar da ku, kuma tsammaninku, za ku gode).

Ya ku musulmai! Abu Dawud da Ibn Majah sun rawaito daga Ɗan Abbas Allah ya ƙara yarda a gare su cewa: "Manzon Allah ya farlanta zakkar fid-da-kai domin tsarkake mai azumi daga yasasshen zance da maganganun batsa, sannan kuma ciyarwa ce ga miskinai».

An karɓo daga Abu Sa'id Alkhudri ya ce: "Mun kasance muna fitar da zakkar fid-da-kai, sa'i ɗaya na alkama ko na sha'iri kuma sa'i na dabino ko zabib, ko kuma sa'i na cukwi. Idan ya fitar daga irin abincin da mutancen garinsu suke amfani da shi ya yi daidai.

Wannan zakka ta fid-da-kai, wajibi ce a kan kowane musulmi, namiji ne ko mace, babba ne ko ƙarami. Kuma an fi son a fitar da ita kafin a tafi sallar idi. Kuma za a yin hakan kafin kwana ɗaya ko biyu ga idi.

Allah Akbar! Allah Akbar!! Allah Akbar!!! La'ilaha illallah, wallahu akbar, Allah Akbar, walillahil hamd.

Ku ji tsoron Allah ya ku musulmai. Kuma ku sani cewa Shi Mai Shar'antawa Mai Hikima, ya sunnanta muku azumi guda shida na Shawwal, kuma ya sanya hakan ya zama tamkar bibiyar ayyukan kirki ne da wasu ayyukan kirki. Domin manzon Allah (ﷺ) yana cewa: "Duk wanda ya azumci Ramadan, sannan ya bi shi da shida ga Shawwal, ya kasance kamar ya yi azumin shekarar ce gaba ɗaya." Muslim ne ya rawaito shi.

Yadda aka yi azumin Ramadan tare da shida na watan shawwal ya zama kamar azumin shekara , shi ne Allah mai girma da ɗaukaka, yakan ninka dukkanin wani kyakkyawan aiki zuwa ninki goma kwatankwacinsa. Kamar yadda yake a faɗar Allah maɗaukaki:

﴿مَن جَآءَ بِٱلۡحَسَنَةِ فَلَهُۥ عَشۡرُ أَمۡثَالِهَا﴾ [الأنعام: ١٦٠].

"Wanda ya zo da kyakkyawa aiki guda, to, yana da goma ɗin misalinsa"

Don haka azumin Ramadan akan ƙirga shi a matsayin an ninka shi kwatankwacin wata goma, shi kuwa azumin shida ga Shawwal akan ƙirga shi a matsayin kwatankwacin kwana sittin. Da wannan sai a sami kwatankwacin ladan shekara cikakkiya.

Abin da ya fi falala dangane da azumtar waɗannan kwana shida na Shawwal shi ne, a yi su da gaggawa bayan ranar idi, kuma yana da kyau a yi su a jere. Amma babu laifi ga wanda ya yi su a rarrabe. Hakan nan ba laif idan mutum ya jinkirta

yin su har zuwa tsakiyar watan ko ƙarshensa. Kuma a sani yin wannan azumi ba wajibi ba ne. Kuma abin da wasu suke zato na cewa duk wanda ya riga ya yi a wata shekara, to wai ya wajaba a kansa duk sauran shekarun, wannan ba haka ba ne, domin yin azumin sunna ne ba wajibi ba. Duk wanda ya yi zai sami lada, wanda kuma ya bari bai yi ba, ba wani abu a kansa. Haka nan duk wanda ya zama yana yin wannan azumin a kowace shekara, sannan sai wata shekarar ya yi rashin lafiya ko kuma tafiya ta kama shi a daidai lokacin yin azumin, to za a rubuta masa ladan azumin, ko da kuwa bai yi ba. Hakan kuma na ƙarfafa ne da faɗin manzon Allah a hadisi ingantacce cewa: "Idan bawa ya yi rashin lafiya ko kuma ya yi tafiya, Allah maɗaukakin sarki zai rubuta masa lada misalin abin da ya kasance yana yi a yayin zaman gida". Bukhari ne ya fitar da shi, da Ahmad, daga Abu Musal Ash'ari, Allah ya yarda da shi.

Haka kuma ba ya halatta a gabatar da azumin shida ga Shawwal alhalin kuma akwai ramuwa a kan mutum, domin yana daga cikin sharaɗin samun ladan azumin shidan shi ne ya kasance mutum ya azumci Ramadan gabaɗayansa. Da haka ne mutum zai kasance kamar ya azumci shekara gabaɗayanta.

Ya bayin Allah, ku godewa Ubangijinku a bisa abin da ya yi muku tagomashi da shi a wannan na zaman lafiya da imani, da kuma lafiyar jiki da yassara arziƙi da yalwar rayuwa, da kuma kashe wutar fitintinu. Kuma ni'imar Allah tana dawwama ne ta hanyar godiya gare shi maɗaukakin sarki da kuma yi masa ɗa'a.

Ya bayin Allah, "Lallai Allah da manzonsa suna yin salati ga manzon Allah, ya ku waɗanda suka imani ku yi salati a gare shi tare da cikakkiya sallama. Haƙiƙa, ya ce (sallal lahu alaihi wasallam) "duk wanda ya yi salati a gare ni guda ɗaya, Allah zai yi masa da guda goma da wannan salatin." Don haka ku nemi daɗin tsira da aminci a bisa ga shugaban na farko da na ƙarshe. Ya Allah ka yi salati ga annabin Muhammad da iyalan Muhammad kamar yadda ka yi salati ga Ibrahim da iyalan Ibrahim, ka yi daɗin albarka ga Muhammad da iyalan Muhammad kamar yadda ka yi albarka ga Ibrahim da iyalan Ibrahim lallai kai ne abin godiya mai yabawa, ka yi daɗin tsira da aminci mai yawa.

HUƊUBAR IDIN BABBAR SALLAH

Manufofin huɗubar

- Bayanin yin layya.
- Bayanin sharaɗan layya da ladubbanta
- Umarni da kaɗaita Allah da tsoratarwa game da wasu saɓon Allah na fili.
- Wasiyyoyi ga ɗaukakin ɓangarorin al'umma

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga shirrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammad bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammad (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Bayan haka:

Ya ku 'yan'uwa a musulunci! Ina yi wa kai na da ku wasiyya da jin tsoron Allah maɗaukakin sarki, domin wannan ita ce wasiyyarsa ga bayinsa na farko da na ƙarshe. Allah maɗaukakin sarki yana cewa:

﴿ وَلَقَدۡ وَصَّيۡنَا ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ مِن قَبۡلِكُمۡ وَإِيَّاكُمۡ أَنِ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ ﴾[النساء: ١٣١].

(Haƙiƙa mun yi wasicci ga waɗanda muka baiwa littafi gabaninku da ku kanku, da ku ji tsoron Allah).

Ya ku bayin Allah, shin kun san kowace rana ce wannan? Ita ce ranar idin babbar sallah mai girma wanda Allah ya ɗaukaka ta kuma ya girmama matsayinta, kuma ya ambace ta da sunan Ranar Babban Hajji. Domin alhazai suna aiwatar da mafi girman ayyukan hajjinsu a cikinsa. Sukan yi jifan sheɗan, su yanka abin yankansu, su aske kawunansu, su yi ɗawafi ga ɗakin Allah, sannan su yi sa'ayi

tsakanin Safa da Marwa. A wannan rana ne, alhazai suke babban shirin dunfarar filin Mina, bayan sun tsaya a waje mai girma, wajen tsayuwar Arfa. Sun ɗaga hannayensu cikin ƙanƙan da kai zuwa ga Allah. Sun zubar da hawaye na tsoron Allah domin neman tuba da komawa ga Allah. Sannan sun nemi taimako a gurin wanda duk wani taimako da datarwa ke hannunsa. Sannan sun hari Muzdalifa, sun kwana a nan, duk domin biyayya ga sunnar Mustafa (ﷺ), wanda yake cewa: “Ku koyi ayyukan hajjinku daga gurina”

Ya ku bayin Allah. Allah ya sanya wannan rana, ranar biki da farin ciki, wanda albarkasa da falalarsa da alherinsa yake komawa ga musulmi gabaɗaya. A wannan rana musulmai sukan ƙara kusantar Ubangijinsu ta hanyar yanka hadayarsu, domin biyayya ga sunnar Manzon Allah (ﷺ). Domin Manzon Allah (ﷺ), ya yi yanka hadayarsa da kansa, da hannunsa mai albarka. Ya soke raƙuma sittin da uku a hajjinsa ta bankwana. Bukhari da Muslim sun rawaito cewa, Manzon Allah (ﷺ) ya yi layya da raguna guda biyu ƙosassu, masu ƙaho. Ya yanka su da hannunsa, ya ambaci sunan Allah sannan ya yi kabbara.

Allahu Akbar! Allahu Akbar!! La’ilaha illal lah, Allahu Akbar, Allahu Akbar walil lahil hamd.

Ya ku musulmai, haƙiƙa akwai falala mai girma da lada gwaggwaɓa ga wanda ya raya sunnar yin layya. An samo hadisi daga manzon Allah ya ce: “ Babu wani aiki da da ɗan’adam zai yi a ranar babbar sallah, wanda Allah ya fi so, sama da zubar da jini (yanka abin yanka), kuma ita (abin yankan) za ta zo ranar alƙiyama da kofatunta da ƙahonninta da gashinta. Kuma jinin da aka zubar yana da wata daraja a wurin Allah tun kafin ya zuba a ƙasa. Kuma wanda ya yi layya ana ba shi lada a kowane gashin na jikin dabbar, da ko wane sufi nata. Don haka, ku jiyar da kanku daɗi da ita). Imam Ahmad da Tirmizi da Ibn Majah ne suka rawaito.

Yana daga cikin abin da ya kamata a sani, Allah ya tsare ku, shi ne akwai sharuɗɗa guda uku game da abin layya.

Na farkon su shi ne: Cikar shekarun da aka ambata a shar’ance. Wanda shi ne shekara biyar ga raƙumi, da kuma shekara biyu ga shanu, da shekara ɗaya ga tumaki da kuma rabin shekara ga awaki.

Sharaɗi na biyu: Ya kasance abin da za a yanka ɗin lafiyye ne marar illa, wanda zai ta hana a yi layyar da shi. Kuma manzon Allah ya bayyana hakan, idan ya bayyana cewa, (Nau’in dabbobi guda huɗu ba sa wadatarwa a layya. Daga ciki akwai gurguwa da gurguntakar ta bayyana sosai, sai kuma mai makantar da makantar ta bayyana, da kuma dabba mara lafiya, wadda rashin lafiyar ta bayyana, da ramamma marar kitse). Imam Ahmad da Abu Dawud da Tirmizi da Nisa'i suka ruwaito shi daga Bara’u ɗan Azib, Allah ya yarda da shi.

Shardi na Uku: A yanka abin layyar a cikin lokacin da shari’a ta ƙayyade. Lokacin shi ne, daga fitowar rana a ranar idi, zuwa faɗuwar rana, a rana ta uku. Amma abin da ya fi falala shi ne a ranar farko. Kuma babu laifi a yanka da daddare. Kuma akuya guda ɗaya za ta ishi mutum ɗaya da iyalan gidansa, kamar yadda ya zo a hadisin Abu Ayyub, Allah ya yarda da shi.

Allah Akbar! Allah Akbar!! Allah Akbar!!! La'ilaha illallah, wallahu akbar Allah Akbar, walillahil hamdu.

Ya ku 'yan'uwa masu yin layya, ya kamata a gare ku kyautata a wurin yankanku, ta hanyar wasa wuƙa, domin hutar da abin da za a yanka, da kuma tausaya masa. Sannan kuma akan kwantar da shi ne daga ɓangaren hagunsa. Kuma abin da ya inganta a sunna game da naman da aka yanka shi ne, mutum ya ci wani abu daga ciki, sannan ya yi sadaka da wani kaso, sannan kuma ya kyauta da wani. Kuma sannan an fi so mutum ya yanka da kansa, ko kuma ya kasance yana wurin a lokacin da za a yi yankan. Kuma ba a ba wa mahauci ladan aikinsa daga cikin naman da aka yanka. Ubangiji maɗaukaki sarki yana cewa,

﴿ فَصَلِّ لِرَبِّكَ وَٱنۡحَرۡ ۝٢ ﴾ [الكوثر: ٢].

(Ka yi sallah domin Ubangijinka, kuma ka yi yanka)

Allah Akbar Allah Akbar Allah Akbar, La'ilaha illallah, wallahu akbar Allah Akbar, walillahil hamdu.

Ya 'yan'uwa a Musulunci, ana lissafa wannan taron, ta ɓangaren ginuwarsa da albarkarsa da hikimar yinsa, a matsayin wani abu da yake bayyana haɗin kan musulunci. Allah yana cewa:

﴿ إِنَّمَا ٱلۡمُؤۡمِنُونَ إِخۡوَةٞ ﴾ [الحجرات: ١٠].

(Lallai muminai 'yan'uwa ne).

Allah ya ƙara da cewa:

﴿ إِنَّ هَٰذِهِۦٓ أُمَّتُكُمۡ أُمَّةٗ وَٰحِدَةٗ ﴾ [الأنبياء: ٩٢].

(Wannan al'umma taku alumma ce guda ɗaya)

Allah yana cewa:

﴿ وَمَن يَبۡتَغِ غَيۡرَ ٱلۡإِسۡلَٰمِ دِينٗا فَلَن يُقۡبَلَ مِنۡهُ وَهُوَ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ مِنَ ٱلۡخَٰسِرِينَ ۝٨٥ ﴾ [آل عمران: ٨٥].

(Kuma wanda ya nemi wini addini ba musulunci, to, ba za a karɓa daga gare shi ba. Kuma shi a lahira yana daga cikin masu hasara).

Sannan Allah yana cewa:

﴿ وَلَقَدۡ بَعَثۡنَا فِي كُلِّ أُمَّةٖ رَّسُولًا أَنِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ وَٱجۡتَنِبُواْ ٱلطَّٰغُوتَ ﴾ [النحل: ٣٦].

(Haƙiƙa mun aika wa kowace al'umma da manzo da cewa, ku bautawa Allah ku ƙauracewa duk wani ɗagutu).

To waye wanda ya halicci bayi, ya azurta su, kuma ya samar musu da ji da gani da hankali da tunani, ba Allah shi kaɗai ba? Kuma ba wani abu kwatankwacinsa, daga cikin mala'iku ko annabawa ko mutane da duwatsu ko waliyyai wanda za a iya daidaita shi da Allah ko wane ne. Ba wanda yake iya samarwa da kansa wani abin amfani, ko abin cutarwa, kuma ba su da ta cewa game da mutuwa ko rayuwa ko tashi a ranar ƙarshe. Yana daga abin mamaki ka ga wasu suna neman kusanci ga wani abin halitta mai rauni, kuma faƙiri, sannan su manta da wanda ya yi halitta mai ƙarfi kuma wanda yake mawadaci.

﴿ ءَٱللَّهُ خَيۡرٌ أَمَّا يُشۡرِكُونَ ۝٥٩ ﴾ [النمل: ٥٩].

(Shin Allah shi ne mafi alheri ko kuma abin da suka shirka da shi).

﴿ ءَأَرۡبَابٞ مُّتَفَرِّقُونَ خَيۡرٌ أَمِ ٱللَّهُ ٱلۡوَٰحِدُ ٱلۡقَهَّارُ ۝٣٩ ﴾ [يوسف: ٣٩].

(Wasu iyayengiji mabanbanta su ne suka fi alheri, ko kuwa Allah kaɗaitacce mai ƙarfi).

Tsarki ya tabbata a gare shi kuma ya ɗaukaka daga abin da suke haɗa shi da shi.

Ya bayin Allah, ya zama wajibi ga bayi su kaɗaita Ubangijinsu a cikin duk abubuwan da suke yi da kuma a duk halin da suke ciki. Ba a yin sallah sai don Allah, ba a yin addu'a sai don shi, ba a yanka, ba a bakance, ba a neman kusanci, sai da Allah, ba a rantsuwa ba a neman taimako sa ga Allah.

﴿ قُلْ إِنَّ صَلَاتِي وَنُسُكِي وَمَحْيَايَ وَمَمَاتِي لِلَّهِ رَبِّ الْعَالَمِينَ ﴿١٦٢﴾ لَا شَرِيكَ لَهُ ۖ وَبِذَٰلِكَ أُمِرْتُ وَأَنَا أَوَّلُ الْمُسْلِمِينَ ﴿١٦٣﴾ ﴾ [الأنعام: ١٦٢ – ١٦٣].

(Ka ce sallata da yankana da rayuwata da mutuwata duk na Allah ne Ubangijin talikai. Ba shi da abokin tarayya, da wannan aka umarce ni, kuma ni ne farkon masu miƙa wuya).

Ya bayin Allah ku ji tsoron zuwa wajen masu sihiri da masu duba da bokaye, da masu da'awar sanin gaibu:

﴿ قُلْ أَفَرَءَيْتُم مَّا تَدْعُونَ مِن دُونِ اللَّهِ إِنْ أَرَادَنِيَ اللَّهُ بِضُرٍّ هَلْ هُنَّ كَٰشِفَاتُ ضُرِّهِۦٓ أَوْ أَرَادَنِي بِرَحْمَةٍ هَلْ هُنَّ مُمْسِكَاتُ رَحْمَتِهِۦ ۚ قُلْ حَسْبِيَ اللَّهُ ۖ عَلَيْهِ يَتَوَكَّلُ الْمُتَوَكِّلُونَ ﴿٣٨﴾ ﴾ [الزمر: ٣٨].

"Ka ce, "Ashe to kun gani abin da kuke kira, waɗanda suke wanin Allah ne, idan Allah ya nufe ni da wata cuta, shin, su abubuwan nan masu yaye min cutarsa ne? Ko kuma ya nufe ni da wata rahama, shin, su abubuwan nan masu hana ni rahamarsa ne?" Ka ce, "Mai isata Allah ne, gare Shi masu tawakkali ke dogara).

Ya ku shugabannin musulmai, ya ku masu riƙe da madafun iko, lallai abin da ke wuyanku a gaban Allah abu ne mai girma. Domin lallai Allah yakan kawar da wani abu ta hanyar shugaba ba tare da ya kawar da shi ta hanyar Alƙur'ani ba. Ku yi jagorancin mutanenku da littafin Allah, ku yi hukunci da sunnar manzon Allah, ku tsayar da addini. Ku riƙe Allah yana cewa:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا الَّذِينَ ءَامَنُوٓا أَطِيعُوا اللَّهَ وَأَطِيعُوا الرَّسُولَ وَأُولِي الْأَمْرِ مِنكُمْ ۖ فَإِن تَنَٰزَعْتُمْ فِي شَيْءٍ فَرُدُّوهُ إِلَى اللَّهِ وَالرَّسُولِ إِن كُنتُمْ تُؤْمِنُونَ بِاللَّهِ وَالْيَوْمِ الْآخِرِ ۚ ذَٰلِكَ خَيْرٌ وَأَحْسَنُ تَأْوِيلًا ﴿٥٩﴾ ﴾ [النساء: ٥٩].

(Ya ku waɗanda suka yi imani! Ku yi ɗa'a ga Allah kuma ku yi ɗa'a ga Manzonsa, da shugabanni daga cikinku. Idan kun yi jayayya a cikin wani abu, to ku mayar da shi zuwa ga Allah da Manzonsa, idan kun kasance kun yi imani da Allah da ranar lahira, wannan shi ne mafi alheri gare ku, kuma shi ne mafi kyan makoma).

Malaman musulunci, matsayinku a wannan addini mai girma ne. Ku ne magada annabaw,a kuma halifofin manzanni, masu bijiro da gyara, kuma amintattu game da isar da kiran Allah da bayani. Ku tashi ku yi tsayuwar daka wajen isar da abin da ya wajaba a kanku. Ku guji karkatar da ilimi don ɗan wani abin ƙashin miya. Ku zama ababan koyi na gari ga jama'a.

Allah yana cewa,

﴿ وَلْتَكُن مِّنكُمْ أُمَّةٌ يَدْعُونَ إِلَى الْخَيْرِ وَيَأْمُرُونَ بِالْمَعْرُوفِ وَيَنْهَوْنَ عَنِ الْمُنكَرِ ۚ وَأُولَٰئِكَ هُمُ الْمُفْلِحُونَ ﴿١٠٤﴾ ﴾ [آل عمران: ١٠٤].

(Lalle a samu wata al'umma daga cikinku da za su riƙa kira zuwa ga alheri, kuma suna umarni da kyakkyawan abu, kuma suna hana mummuna. Waɗannan su ne masu cin babban nasara).

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah, godiya mai yawa tsarkakakkiya mai albarka, kamar yadda Ubangijinmu yake so, kuma ya yarda. Ina shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya, yana da sunaye mafiya kyau, da sifofi maɗaukaka. Kuma ina shaidawa cewa Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma manzonsa ne, masoyinsa ne kuma badaɗayinsa ne, kuma shi ne amintaccensa a kan wahayinsa, kuma shi ne zaɓaɓɓe a cikin halittunsa kuma maɗaukaki, daga manzanninsa, Allah ya turo shi mai shiryarwa, mai bushara mai gargaɗi, kuma mai kira zuwa ga Allah da izininsa kuma fitila ce mai haskakawa. Ubangiji ya ƙara daɗin tsira a gare shi, da iyalansa da sahabbansa da matansa da 'yan'uwansa da mabiyansa, da daɗin tsira da aminci mai yawa.

Allah Akbar Allah Akbar Allah Akbar, La'ilaha illallah, wallahu akbar Allah Akbar, walillahil hamdu.

Ya ku musulmai, ku tuna haɗuwarku irin wannan, ranar da Allah zai haɗa na farko da na ƙarshe, domin rarrabe hukunci a tsakaninsu. A cikinsu akwai wanda zai karɓi littafinsa da hannun dama, akwai kuma wanda zai karɓi littafinsa da hannun hagu. Ku tuna, ya ku bayin Allah, ranar da za a tashe ku zuwa ga Ubangijinku zai tashe ku a cikin tsaraici ba takalma, kuna masu loɓa, kamar yadda iyayenku suka haife ku, idanuwa sun yi muku zuru-zuru. Ku tuna ya ku bayin Allah, ku tuna mutuwa da magaginta, da ƙabari da duhunsa da tashi a ranar lahira da ɗimautarsa. Don haka ku yi shiri don tunkarar wannan ta hanyar tuba na gaskiya da ayyukan kirki waɗanda za su kusantar da ku zuwa ga Allah. Sayyidina Abubakar Allah ya yarda da shi yana cewa: "Kowane mutum mai wayar gari ne a cikin iyalansa, amma kuma mutuwa ta fi kusa da shi sama da hancin takalminsa.

Ya 'yan'uwa na aƙida, gida na musulunci wani tubali ne na ginin al'ummar musulma a addinin musulunci. Ta hanyar gyaruwar zamantakewar iyali ne al'umma duka take gyaruwa, idan kuma suka ɓaci, komai na al'umma yakan ɓaci, kuma rukunan al'ummar sukan sakwarkwace. Saboda haka ya zama wajibi a kan miji da mata da 'ya'ya su tabbatar da gyaruwa gidansu. Kuma su samar da tarbiyya mai kyau. Kuma su toshe duk wata hanya da kan iya kawo ɓaraka. Kuma ya zama tilas a kan mata da miji, kowannensu ya sauke haƙƙin ɗan uwansa da yake kansa. Duk wata matsala ta zamantakewar iyali, da yawan sake-saken aure a cikin al'umma, da sauran abubuwan da suke tarwatsa gidaje, sai kawai don ƙin aiwatar da abin da ya dace daga ɓangaren mata da miji. Kowannensu ya ƙi yin abin da ya kamata ya yi. Sau nawa irin wannan ya zama sababin lalacewar 'ya'ya, har ma suka zama abin farautar mutanen banza. Saboda haka ya zama dole a kanmu mu haɗa kai gaba ɗaya don ganin mun samar da mafita ga wannan matsaloli a cikin

al’umma. Kuma waɗanda suke malamai da shugabanni da marubuta, ya kamata su ba wa wannan matsala haƙƙin da ya kamata. Ya bayin Allah, al’amarin aure, da tsadar sadaki, da lalacewar ‘yan mata, da nuna alfahari, da ɗorawa kai abin da bai kamata ba, da ɓarnatar da dukiya da almubazzaranci, duk abubuwa ne da ya kamata a lura da su.

Ya ku matasa, duk burin wanna al’umma yana kanku, ku ne manyan gobe. Ya kamata ku tashi wajen ganin kun sauke nauyin da yake kanku. Ku ne jikiokin jaruman farko na wannan al’umma waɗanda suka jagoranci buɗe garuruwa da musulunci. Don haka ku tashi tsaye ku yi abin da ya kamata ku yi. Ku san matsayinku, ku yi riƙo da addininku. Kuma ku nemi haɗin kai da malamanku, kuma ku riƙi hanyar da take ita ce madaidaiciya, tsakatsakiya ba tare da shisshigi ko kasawa ba. Haka kuma banda zaƙewa, kuma ban da lalaci. Ku guji aukawa cikin gafala da sha’awar zuciya, da kuma kutsawa cikin shubuhohi.

Ya ‘yan matan musulmai, ku ji tsoron Allah, ku kiyaye kanku ta hanyar kamewa, da kunya da hijabi. Ku kasance mata musulmai, muminai, masu tawali’u. Ku a musulunci wani abu ne mai karamci kuma mai tsada. Don haka ku masu ilimi game abin da maƙiya musulunci suke ƙullawa, waɗanda suke son cutar da ku ta hanyar yaɗa tsaraici da cakuɗuwar maza da mata, da halatta abubuwan da Allah ya haramta. Ku tashi tsaye wajen aikinku na tarbiyya ga ‘yan baya masu tasowa.

Ya ‘yan’uwa musulunci, ku kula da sallah domin ita ce tushen addininku. Ba wani rabo a cikin addinin musulunci ga wanda ya bar sallah. Ku ɗabi’antu da ɗabi’un musulunci masu kyau. Kuma ku guji furta abubuwa ba tare da ɗabbaƙa su ba. Domin shi addinin musulunci ba kawai a faɗa da baki ba ne, abu ne da ya shiga zuciya, kuma ayyuka sukan gaskata shi. Ku godewa Allah maɗaukakin sarki a bisa dukkanin ni’imominsa da falalolinsa, domin addininku na musulunci yana tabbatar da nutsuwa, yana kuma kore kokwanto da kwan-gaba-kwan-baya, da rashin tabbas. Allah ya yi gaskiya da yake cewa:

﴿ وَمَن يَعۡشُ عَن ذِكۡرِ ٱلرَّحۡمَٰنِ نُقَيِّضۡ لَهُۥ شَيۡطَٰنٗا فَهُوَ لَهُۥ قَرِينٞ ٣٦ وَإِنَّهُمۡ لَيَصُدُّونَهُمۡ عَنِ ٱلسَّبِيلِ وَيَحۡسَبُونَ أَنَّهُم مُّهۡتَدُونَ ٣٧ ﴾ [الزخرف: ٣٦ – ٣٧].

(Kuma wanda ya bijirewa ambaton Allah Mai rahama, to, za mu haɗa shi da shaiɗan shi ne abokinsa. Kuma lallai su, haƙiƙa suna kange su daga hanya, kuma suna zaton cewa su shiryayyu ne).

Allah Akbar! Allah Akbar!! Allah Akbar!! La’ilaha illallah, wallahu akbar Allah Akbar, walillahil hamd.

KISFEWAR RANA DA WATA

Manufofin huɗubar

- Wa’azantuwa da ayoyin Allah da halitta a sararin samaniya.
- Tunani a kan halittar sama da ƙasa yana tunatarwa ɗan-adam cewa, ajalinsa ya kusa.
- Izinar da take cikin kusufin rana da wata, da abin ya wajaba yayin da ya faru.
- Kira zuwa ga gaggauta tuba da aiki na ƙwarai.
- Jan-kunne a kan aikata wasu laifuffuka.
- Sanin lokacin kusufi ba ya ciki sanin ilimin gaibi.

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga shirrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammad bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammad (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Bayan haka:

Ku ji tsoron Allah ya ku musulmai haƙiƙanin jin tsoron Allah maɗaukakin sarki, ku yi tunani akan abubuwan da ya halitta a cikin sammai da ƙassai, lallai a cikin wannan akwai aya ga masu hankali. Ku yi tunani a waɗannan samman ƙarfafa da Allah Ya ɗaukaka da ƙarfinsa, kuma Ya riƙe su da ƙudurarsa, da rahamarsa ta yadda ba za su faɗo kan bayi ba. Ku yi tunani a kan yadda Allah ya gina su ba tare da wata ɓaraka ko tsaga ba, da kuma yadda Ya ƙawaita sama da fitilu, waɗanda suka mamayeta da kyawu da haske. Kuma ya halicci rana mai haske wata mai haskawa. Sannan sai ku yi tunani, yaya waɗannan abubuwa masu haskakawa da fitilu suke tafiya da izinin Allah, a kan falakinsu wanda Allah Ya ɗora su a kai

tun lokacin da ya halicce su har zuwa lokacin da za a tarwatsa su, ba sa ƙarawa a kan tafiyarsu kuma ba sa ragewa, kuma ba sa tashi daga kan wurin kuma ba sa kaucewa. Tsarki ya tabbata ga wanda yake tafiyar da su da ƙudurarSa, ya tsururuci wannan tsarin nasu da hikimarsa, kuma shi ne Mai ƙarfi Mabuwayi.

Ya bayin Allah, lallai rana da wata ayoyi ne guda biyu daga cikin ayoyin Allah, waɗanda suke nuni ga cikar ƙudurarsa, da cikar kamalarsa da hikimarsa da rahamarsa. Idan ka yi dubi girmansu, da tsarin tafiyarsu, za ka gane girman ƙudurar Allah. Kuma idan ka yi dubi maslaha da amfanin da ke cikin saɓawa a cikin tafiyarsu, za ka tarar cewa a cikin wannan akwai cikar kamala da rahamar Allah.

Ku saurara! Yana daga cikin hikimar Allah a wajen tafiyarsu abin da yake faruwa na kusufi, wanda shi ne gushewar haskensu gaba ɗaya, ko wani sashensa. Lallai hakan yana faruwa ne da umarnin Ubangiji. Allah yana tsoratar da bayinsa da shi, domin su tuba zuwa gare shi su nemi gafararsa, su bauta masa, su girmama shi.

Ya bayin Allah, lallai Allah Mai girma da ɗaukaka Yana nunawa bayinsa abin da zai tunatarsu a cikin sasannin samaniya, in har sun kasance masu yin imani ne. Allah yana cewa:

﴿ سَنُرِيهِمۡ ءَايَٰتِنَا فِي ٱلۡأٓفَاقِ وَفِيٓ أَنفُسِهِمۡ حَتَّىٰ يَتَبَيَّنَ لَهُمۡ أَنَّهُ ٱلۡحَقُّۗ أَوَلَمۡ يَكۡفِ بِرَبِّكَ أَنَّهُۥ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ شَهِيدٌ ٥٣ ﴾ [فصلت: ٥٣]

(Za Mu nuna musu ayoyinmu a cikin sasannin sama da kuma a cikin kawunansu, har ya bayyana a gare su cewa lallai (Alƙur'ani), shi ne gaskiya. Ashe, kuma Ubangijinka bai isa ba, ga cewa lallai shi Halartacce ne a kan kowane abu?).

Sannan Allah ya same jan hankalinmu da mu duba ayoyinsa a cikin sammai da ƙassai, domin mu dinga tuna cewa duniya ta zo ƙarshe, don mu yi guzurin tafiyar da babu dawowa, mu daina nawa. Kuma dole ne mu san gajartar rayuwar duniya, duk kuwa da yadda ta yi tsawo. Da kuma kusantowar lahira, ta hanyar kusantower ajali. Kuma idan ɗan adam ya rasu to shi alƙiyamarsa ta tsaya, domin a wannan lokaci ba wani aiki, kuma ba riskar wani abu, kawai hisabi ne a Barzahu sannan kuma da gidan lahira. Allah yana cewa:

﴿ أَوَلَمۡ يَنظُرُواْ فِي مَلَكُوتِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا خَلَقَ ٱللَّهُ مِن شَيۡءٖ وَأَنۡ عَسَىٰٓ أَن يَكُونَ قَدِ ٱقۡتَرَبَ أَجَلُهُمۡۖ فَبِأَيِّ حَدِيثِۭ بَعۡدَهُۥ يُؤۡمِنُونَ ١٨٥ ﴾ [الأعراف: ١٨٥].

"Shin, ba su yi duba ba a cikin mulkin sammai da ƙasa, da kuma abin da Allah Ya halitta daga kome, kuma akwai tsammani kasancewar ajalinsu, haƙiƙa ya kusanto? To da wane labari a bayansa suke yin imani".

Sannan wanda ba ya wa'aztuwa da ayoyin da suke watse a cikin sararin samaniya, sai ya yi la'akari da faɗin Allah:

(Wanda Allah ya ɓatar, to, babu mai shiryar da su, kuma yana ƙale su, a cikin ɓatansu suna ɗimuwa).

A wata faɗar kuma Allah Ya ce:

﴿ قُلِ ٱنظُرُواْ مَاذَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ وَمَا تُغۡنِي ٱلۡأٓيَٰتُ وَٱلنُّذُرُ عَن قَوۡمٖ لَّا يُؤۡمِنُونَ ١٠١ ﴾ [يونس: ١٠١].

“Ka ce, “Ku dubi abin da yake cikin ammai da ƙasa Kuma ayayo da gargaɗi ba su wadatar da mutanen da ba su yi imani ba).

Sannan Allah ya tsoratar da mutane mummunan kamunsa, a inda ake faɗa maɗaukakin sarki, bayan wannan ayar:

﴿ فَهَلۡ يَنتَظِرُونَ إِلَّا مِثۡلَ أَيَّامِ ٱلَّذِينَ خَلَوۡاْ مِن قَبۡلِهِمۡۚ قُلۡ فَٱنتَظِرُوٓاْ إِنِّي مَعَكُم مِّنَ ٱلۡمُنتَظِرِينَ ١٠٢ ثُمَّ نُنَجِّي رُسُلَنَا وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ كَذَٰلِكَۚ حَقًّا عَلَيۡنَا نُنجِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ١٠٣ ﴾ [يونس: ١٠٢ - ١٠٣].

“To, shin suna jiran wani abu face kamar misalin kwanukan waɗanda suka shuɗe daga gabaninsu? Ka ce, “Ku yi jira! Lallai ni tare da ku, ina daga masu jira. Sannan sai mu tseratar da manzanninmu da waɗanda suka yi imani, kamar wannan ne tabbatacce ne a gare mu, kuɓutar da masu imani).

Allah yana da hikimomi masu yawa dangane da halittar sammai da ƙasa, kamar yadda Yake cewa:

﴿ حِكۡمَةُۢ بَٰلِغَةٞۖ فَمَا تُغۡنِ ٱلنُّذُرُ ٥ ﴾ [القمر: ٥].

(Hikima cikakkiya! Sai dai abubuwan gargaɗi ba sa amfani.)

Sau nawa Allah Yana turo da gargaɗi a harasan manzanni, kuma sau nawa Allah Yana turo da wani abin gargaɗi a cikin sasannin duniya, sai dai kamar yadda maɗaukakin sarki yake cewa: “Sai dai abubuwan gargaɗi ba sa amfani”.

Ya inganta daga manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Lallai rana da wata ayoyi ne guda biyu daga ayoyin Allah ba sa yin kusufi don mutuwar wani ko don rayuwar wani, sai dai Allah yana tsoratar da bayinsa da su. Idan kun ga wani abu na daga haka, ku yi gaggawa zuwa ga zikirin Allah da kuma zuwa ga Sallah da addu’a da istigfari”. Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

To, shin mun yarda da tsoratarwar da Ubangijinmu yake yi mana, kuma mun tsorata ɗin, sannan muka kama hanyar komawa gare shi tun farkon dare. Ya tabbata daga manzon Allah (ﷺ) ya ce, “Duk wanda ya ji tsoro zai kama hanya tun farkon dare, wanda kuma ya kama hanya tun farkon dare to zai isa masaukinsu. Ku saurara, lallai hajar Allah mai tsada ce, lalle hajar Allah ita ce aljanna”. Tirmizi ne ya ruwaito shi.

Yana daga cikin yarda da tsoratarwar Ubangijinmu a gare mu, shi ne mu ji tsoro mu yi aikin kirki, mu guji mummunan aiki. Mu yi istigfari mu tuba daga sauran zunubai. Haka kuma mu yi addu’a mu yi zikiri, kar mu yi ɗagawa da alfahari. Mu yi sadaka sosai kuma mu guji azabar Sa’ira. Har sai Allah ya tabbatar da mu da tabbataccen zance a duniya da lahira kamar yadda Maɗaukakin sarki yake cewa:

Ma’an: (Allah yana tabbatar da waɗanda suka yi imani da magana tabbatacciya a cikin rayuwar duniya, da kuma Lahira. Kuma Allah Yana ɓatar da azzalumai, kuma Allah Yana aikata abin da Yake so).

Abin nufi da faɗarsa: “ a rayuwar duniya”, shi ne a cikin ƙabari a daidai lokacin da za a dawo da ran mamaci zuwa gangar jikinsa, a lokacin yana jin takun takalman waɗanda suka kawo shi, a yayin da suka juya suna komawa. Sai wasu mala’iku guda biyu su zo masa, su daka mishi tsawa. Sai su tashe shi su zaunar da shi, sai su ce masa: “wanene Ubangijinka? Menene addininka? Wani wannan mutumin

da aka aiko a cikinku? Mene ne iliminka? Shi dai mumini zai ce, “Ubangijina shi ne Allah. Addinina kuma shi ne musuluncil. Annabina shi ne Muhammad tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Na karanta littafin Allah sai na yi imani da shi na kuma gaskata. Wannan ita ce ƙarshen fitinar da za a bijirowa mumini. A wannan shi ne ma’anar faɗar Allah “Allah yana tabbatar da waɗanda suka yi imani da magana tabbatacciya a cikin rayuwar duniya). Amma fajiri sai ya ce: Ha! Ha! Ban sani ba, na ji mutane suna cewa kaza. Sai a ce masa; “Ba ka sani ba. Ba ka karanta ba”. Abu Dawud ne ya ruwaito shi.

Don haka sai mu ɗauki wannan al’amari da matuƙar mahimmanci. Kuma mu yi tanadin neman tsari daga azabar ƙabari, kamar yadda manzon Allah ya umarce mu, yayin da aka yi kusufi, inda yake cewa: “Ku nemi tsarin Allah daga azabar ƙabari”. Sannan ya koyar da mu neman tsari daga wannan azaba a ƙarshen kowace sallah, inda muke cewa: (Ya Allah ina neman tsarinka daga azabar ƙabari da azabar wuta da fitinar rayuwa da mutuwa da kuma sharrin fitinar Dujal mai shafaffiya albarka). Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.

Yana daga cikin abubuwa masu halakarwa da manzon Allah ya tsawatar a kansu, a lokacin da aka yi kusufi, shi ne zina. Inda yake cewa: (Ya ku al’ummar Muhammad, ba wanda ya fi Allah kishin ya ga bawansa ya yi zinam ko baiwarsa ta yi zina. Ya al’ummar Muhammad, da kun san abin da na sani da kun yi dariya kaɗan, da kuma kun yi kuka mai yawa.” Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.

Don haka sai mu gujewa zina da duk sabubbanta ya bayin Allah, kuma mu rufe dukkanin ƙofofinsa. Kuma mu sani ba wanda ya fi Allah kishi, don haka mu guji fushinsa, kuma mu guji duk wani abu da ke kusantarwa zuwa ga zina, domin mu yi aiki da faɗar Allah inda yake cew: “Kada ku kusanci zina, lallai ta kasance alfasha ce, kuma hanyar ta ta yi muni”. Kuma daina zira ga abin Allah ya haramta, kamar yadda Ubangijinmu ya yi mana wannan tarbiyyar, a cikin faɗinsa:

﴿ قُل لِّلۡمُؤۡمِنِينَ يَغُضُّواْ مِنۡ أَبۡصَٰرِهِمۡ وَيَحۡفَظُواْ فُرُوجَهُمۡۚ ذَٰلِكَ أَزۡكَىٰ لَهُمۡۗ إِنَّ ٱللَّهَ خَبِيرُۢ بِمَا يَصۡنَعُونَ ٣٠ وَقُل لِّلۡمُؤۡمِنَٰتِ يَغۡضُضۡنَ مِنۡ أَبۡصَٰرِهِنَّ وَيَحۡفَظۡنَ فُرُوجَهُنَّ ﴾ [النور: ٣٠ – ٣١].

(Ka ce wa muminai maza su kame ganinsu, kuma su tsare farjinsu. Wannan shi ne mafi tsarki a gare su. Lallai ne Allah, Masani ne ga abin da suke sana’antawa. Kuma ka ce wa muminai mata, su runtse daga gannansu, kuma su tsare farjinsu…).

Wanda bai wa’azntu da tsoratarwar Allah ba, yaushe ne kuma zai wa’aztu. Wanda zuciyarsa ta gafala yaushe zai faɗaku ya dawo kan hanya. Shin mai muke jira ne, ko sai mutuwa ta zo mana ba shiri, kamar yadda Allah ya ce:

﴿ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءَ أَحَدَهُمُ ٱلۡمَوۡتُ قَالَ رَبِّ ٱرۡجِعُونِ ٩٩ لَعَلِّيٓ أَعۡمَلُ صَٰلِحٗا فِيمَا تَرَكۡتُۚ كَلَّآۚ إِنَّهَا كَلِمَةٌ هُوَ قَآئِلُهَاۖ وَمِن وَرَآئِهِم بَرۡزَخٌ إِلَىٰ يَوۡمِ يُبۡعَثُونَ ١٠٠ ﴾ [المؤمنون: ٩٩ – ١٠٠].

(Har idan mutuwa ta je wa ɗayansu, sai ya ce, ‘Ya Ubangijina, ku mayar da ni (duniya). Tsammanina in aikta aiki na ƙwarai cikin abin da na bari. Kayya! Lallai ne ita kalma ce, shi ne mafaɗinta, alhali kuwa a baya gare su akwai wani shamaki har ranar da za a tayar da su).

Hadisi ingantance ya zo daga Manozon Allah (ﷺ), a yayin da aka yi kusufi, ya ce: “Lallai haƙiƙa an yi min wahayi cewa, za a fitine ku a cikin ƙabari, kwatankwacin ko kuma kusa da fitinar Dujal. Abu Dawud ne ya ruwaito shi.

Muna neman tsarin Allah daga fitinar ƙabari, muna neman tsarin Allah daga fitinar rayuwa da ta mutuwa, muna neman tsarin Allah daga fitinar Dujal shafaffe. Ba wanda ya fi Allah tausayi, kuma Shi ne yake cewa:

﴿ وَإِذْ تَأَذَّنَ رَبُّكُمْ لَئِن شَكَرْتُمْ لَأَزِيدَنَّكُمْ وَلَئِن كَفَرْتُمْ إِنَّ عَذَابِي لَشَدِيدٌ ﴿٧﴾ ﴾

[إبراهيم: ٧].

(Idan kun gode zan ƙara muku, amma idan kun butulce, lallai haƙiƙa azabata mai tsanani ce).

Ba wanda ya fi Allah haƙuri, Shi ne yake cewa,

﴿ وَمَن يَحْلِلْ عَلَيْهِ غَضَبِي فَقَدْ هَوَىٰ ﴿٨١﴾ ﴾ [طه: ٨١].

(Kuma wanda fushina ya sauka a kansa, to lallai ya halaka).

Duk wanda yake fito-na-fito da Allah ta hanyar saɓa masa to haƙiƙa ya taɓe. Allah yana cewa: “Ya ku bayina, da a ce na farkonku da na ƙarshenku da mutanenku da aljanunku sun kasance da zuciyar mutumin da ya fi kowa tsoron Allah daga cikinku, wannan ba zai ƙari mulkina da komai ba. Ya ku bayina, da a ce na farkonku da na ƙarshenku da mutanenku da aljanunku sun kasance da zuciyar mutumin da ya fi kowa fajirci daga cikinku, wannan ba zai ragi mulkina da komai ba. Ya ku bayina lallai ayyukanku ne nake lissafa muku, sannan nake ƙididdige muku su, sannan in cika muku su. Duk wanda ya sami alheri, sai ya godewa Allah, wanda kuma ya sami saɓanin haka, kar ya zargi kowa sai kansa. Muslim ne ya ruwaito shi, daga Abu Zarr, Allah Ya yarda da shi.

Allay ya amfanar da ni da ku da shiriyar littafinsa. Wannan shi ne abin da zan ce, ina neman gafarar Allah ga kaina da kuma ku, da dukkanin sauran musulmi daga kowane irin zunubi, ku nemi gafararsa, lallai shi mai gafara ne mai jinƙai.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su ƙara tabbata ga Manzon Allah (ﷺ). Bayan haka:

Ya ku bayin Allah! A nan muna son mu faɗakar da ku akan wasu abubuwa waɗada dadama daga cikin mutane ba su sansu ba. Na farko: Bayar da labarin Kusufi kafin ya faru, ba wani abu ba ne daga ilimin gaibu, kawai dai yana daga cikin ilimi na yau da kullum, wanda ɗan adam zai iya sani. Shekhul Islam, Ibn Taimiyya Allah ya yi masa rahama, ya ce: “Al'adar Allah ta gudana akan cewa, Kusufin rana yana aukuwa ne a ƙarshen wata. Shi kuma kusufin wata yana faruwa a tsakiyar wata, wato cikin dararen sha uku ko sha huɗu ko sha biyar. To shi wata ba ya Kusufi sai a waɗanna darare. Sannan kuma har ila yau, watan yakan ɓuya ne a ranakun ashirin da tara da kuma talatin, to ita kuma rana ba ta yin nata Kusufin sai a waɗannan kwanaki da wata yake ɓuya. Sannan da rana da wata, dukkansu suna da wasu kwanaki sanannu a bisa al’ada, wanda ya san su to zai san lokacin

faruwar kusufin rana ko na wata.

Ibn Taimiyya ya ƙara da cewa: “Amma sanin wani abu game da al’adar kisfewar rana da wata, wannan wani abu ne da waɗanda suke da ilimin tafiyar rana da wata suka sani. Ba ilimin gaibi ne ba, kawai kamar ilimi ne na sanin canjin yanayi". Ya ƙara da cewa: “Sai dai duk lokacin da masana lissafi maganarsu ta zo ɗaya akan sha'anin kusufin rana ko na wata, to yana da wuya su yi kuskure. Amma kuma duk da haka ba a gina wani abu na shari'a akan maganarsu, domin ita dai sallar Kusufi, ba za a yi ta ba, har sai mun gani da idanuwanmu". Ya ci gaba da cewa: “Idan mutum ya yi shiri domin ganin wannan lokaci, wato abin masana suka ba da labarinsa, to yin haka ya dace domin yana da cikikin gaggawa ne zuwa ga biyayya ga Ubangiji Maɗaukakin Sarki, tare da yi Masa bauta.”

Abu na biyu: Lallai rana ta taɓa kisfewa a zamanin Manzon Allah (ﷺ), sai ya fito a firgice, har yana jan gwadonsa a ƙasa, har sai da ya iso masallaci, sannan aka jama'a domin sallah. Nan da nan sai mutane suka taru. Sai Manzon Allah ya yi sallah raka’a biyu. A kowace raka’a akwai ruku’u biyu da sujjada biyu. Sai ya yi kabbara ya karanta Fatiha da wata sura mai tsawo, kamar Suratul Baƙara. Har sai da sahabbansa suka dinga faɗuwa saboda tsawon tsayuwar. Sannan ya yi ruku’u, ya tsawaita ruku’un, sannan ya ce: Sami’al Lahu Liman Hamidahu, Rabbana walakal Hamd. Sannan ya ƙara karanta Fatiha da wata sura mai tsawo, ba ta farko ba, sannan ya ƙara yin wani ruku’u mai tsawo ba na farko ba. Sannan ya ce: Sami’al Lahu Liman Hamidahu, Rabbana walakal Hamdu. Sannan ya tsawaita tsayuwar, sannan ya yi sujjada. Daga nan bayan ya ɗago daga sujjada sai ya tsawaita zama a tsakanin sujjada, sannan ya yi sujjada ya tsawaita ta. Daga nan sai ya tashi zuwa raka’a ta biyu. Sai ya tsawaita tsayuwar, amma ba ta kai tsayuwar da ya yi a raka’ar farko ba. Sannan ya yi ruku’u ya tsawaita ruku’un, amma bai kai tsawon ruku’un da ya yi a raka’ar farko ba. Sannan ya ce: Sami’al Lahu Liman Hamidahu, Rabbana walakal Hamdu. Sannan ya ƙara karatu ya tsawaita karatun, amma bai kai na farko ba. Sannan ya yi ruku’u, ruku’u na biyu, ya tsawaita shi, kuma shi ma bai kai na farkon ba. sannan ya yi sujjada guda biyu, sai ya yi sallama. A lokacin har rana ta bayyana. Kuma an ji shi a cikin sujjadarsa (ﷺ), yana cewa: “Ya Ubangiji ba ka yi mini akawarin ba za ka musu azaba ba alhalin ni ina cikinsu? Kuma ba ka yi mini alkwarin ba za ka yi musu azaba ba matuƙar dai suna yin istigfari?

Daga nan sai ya yi wa mutane huɗuba, ya yi musu cikakken wa'azi. Ya yabi Allah, da abubuwan da suka kamace Shi, Maɗaukakin Sarki, sannan ya ce: “Lallai rana da wata ayoyi ne guda biyu, daga ayoyin Allah ba sa kisfewa domin mutuwar wani ko don rayuwarsa. Idan kun ga haka, ku yi gaggawa zuwa ga sallah, ku yi gaggawa zuwa masallaci, ku yi gaggawa zuwa zikirin Allah da roƙonsa da neman gafararsa”. A wata ruwayar “Ku yi addu’a, ku yi sadaka, ku yi Sallah”. Sannan ya ce: “Ya al’ummar Muhammdu, babu wani wanda ya fi Allah kishi, daga bawanSa ya yi zina, ko baiwarSa ta yi zina. Ya al’ummar Muhammadu, wallahi da kun san abin da na sani da kun yi dariya kaɗan, kuma da kun yi kuka da yawa. Ya ce: Ba wani abu da aka yi muku alƙawarisa, face sai na gan shi a cikin sallata wannan.

Kuma an yi min wahayi, cewa lallai za a fitine ku a cikin ƙaburburanku, kusa ko kwatankwacin fitina Dujal". Sannan ya umarce su da su nemi tsari daga azabar ƙabari, sannan ya ce: “Lallai an zo da wuta, sashenta yana makar sashe, wannan shi ne lokacin da kuka gan ni na ja da baya, tsoron kada wani abu ya same ni daga hucinta. Har sai da na ga Amr ɗan Luhaiy a cikinta, yana jan 'yan hanjinsa a cikin wuta. Sannan na ga matan nan da ta ɗaure mage, ita ba ta ba ta abinci ba kuma ba ta ƙale ta ta fita ta nemi abincinta da kanta ba, har sai da yunwa ta kashe ta". Sannan ya ce: "Sai aka zo da aljannah, shi ne a lokacin da kuka gan ni na ɗan yi gaba, har na tsaya a wannan gurin da na tsaye. Kuma na miƙa hannuna, ina ƙoƙarin in tsiko kayan marmarinta domin ku gani da idanuwanku. Sai kuma na ga kada in yi hakan".

Ya al'ummar Annabi Muhammad! Ku sani fa kusufin rana ko wata wani baban al'amari ne mai ban tsoro. Baban dalili kuwa iri yadda Manzo (ﷺ) ya firgita ya yi gaggawa zuwa ga sallah yayin da rana ta yi kusufi. Sannan da irin waccan gamsasshiyar huɗuba da ya yi. Don haka wajibi mu riƙa tsorata duk sa'adda muka ga kusufi na rana ko wata, sannan mu yi gaggawar yin sallah da addu'a a masallatanmu, mu nemi gafarar Allah. Kuma mu yi ta yin sadaka. Kuma Annabi (ﷺ) ya yi umarni da 'yanta baiwa ko bawa lokacin da kusufi ya faru. Domin wanda duk ya 'yanta wani shi ma za a 'yanta shi daga shiga wuta. Don haka waɗannan abubuwa su ne suke taimakawa wajen yaye bala'in da yake tattare da kusufin rana ko wata.

Ya ku musulmi ku sani duk sa'adda aka samu kusufi to ana yin gaggawar fara sallah, a kowane lokaci hakan ta faru, ba a la'akari da cewa ko wannan lokacin yana daga cikin lokuta da aka hana yin sallah a cikinsu. Domin wannan salla ce ta roƙon Allah ya yaye wani bala'ai da ya sauka. Don haka za a iya yinta bayan la'asar, da bayan asuba, da lokacin hodowar rana.

Kuma ku sani ana son a sunna a yi wannan sallar cikin jam'i a masallatai. Kamar yadda Manzon Allah (ﷺ) ya yi. Kuma mata da maza suka halarci wannan sallah tare da shi. Amma koda mutun shi kaɗai ya yi ta yi.

Allah Ta'ala yana cewa:

﴿ وَمِنۡ ءَايَٰتِهِ ٱلَّيۡلُ وَٱلنَّهَارُ وَٱلشَّمۡسُ وَٱلۡقَمَرُۚ لَا تَسۡجُدُواْ لِلشَّمۡسِ وَلَا لِلۡقَمَرِ وَٱسۡجُدُواْ لِلَّهِ ٱلَّذِي خَلَقَهُنَّ إِن كُنتُمۡ إِيَّاهُ تَعۡبُدُونَ ٣٧ ﴾ [فصلت: ٣٧].

(Yana daga cikin ayoyinsa, dare da yini, da rana da wata. Ka da ku yi sujjada ga rana ko wata. Ku yi sujjada ga Allah wanda shi ne ya halicce su, idan har kun kasance shi kaɗai kuke bautawa).

HUƊUBAR ROKON RUWA

Manufofin huɗubar

- Umarni da tuba da neman gafarar Allah.
- Bayanin a kan cewa yaye bala'i da musibu yana haɗe da yawan istigfari .
- Tunatar da mutane yi wa Allah ɗa'a da kuma tsoratar da su game da saɓa masa.
- Yawaita addu'a da ƙanƙan da kai da komawa zuwa ga Allah maɗaukakin sarki.s

Huɗuba Ta Farko

Dukkan yabo da godiya da kirari sun tabbata ga Allah, taimakonsa da gafararsa muke nema, kuma muna neman tsarinsa daga shirrin kawukanmu da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar da shi, wanda kuma ya ɓatar to babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya. Kuma ina shaidawa cewa, Annabi Muhammad bawansa ne manzonsa ne. (Ya ku waɗanda suka yi imani ku ji tsoron yadda ya cancaci a ji tsoronsa, kada ku mutu face kuna musulmi). (Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku wanda ya halicceku daga rai guda ɗaya, kuma ya ya halicci matarsa daga gare shi, kuma ya yaɗa maza da mata daga garesu (su biyu). Ku ji tsoron Allah wanda kuke yiwa junanku magiya da shi, (kuma ku kiyaye) zumunci. Lalle Allah mai kula ne da ku). (Ya ku wanɗanda suka yi imani ku ku ji tsoron Allah kuma ku faɗi magana ta daidai. Sai Allah ya gyara muku ayyukanku, kuma ya gafarta muku zunubbanku. Wanda ya bi Allah da Manzonsa haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma). Bayan haka, lalle mafi gaskiyar magana maganar Allah, kuma mafi kyawon shiriya shiriyar Annab Muhammad (ﷺ). Kuma mafi shirrin al'amura (a addini) ƙagaggunsu, kuma duk wani ƙagaggen abu (addini) bidi'a ce, duk wata bidi'a ɓata ce, duka wani ɓata kuma yana wuta.

Bayan haka:

Ina yi muku wasiyya ya ku mutane, da ni kaina, da mu ji tsoron Allah maɗaukakin sarki. Ku tsoraci Allah. Domin tsoron Allah, hanya ce ta tsira da aminta, kuma hanya ce ta rabauta da karamci. Waɗanda suka kuɓuta daga azabar Allah su ne masu tsira. Allah yana cewa:

Ma'ana: (Sannan kuma, mu tserar da waɗanda suka yi aiki da taƙawa, kuma mu bar azzalumai a cikinta a gurfane).

Kuma su ne masu gadon gidan aljannah. Allah yana cewa:

﴿ تِلۡكَ ٱلۡجَنَّةُ ٱلَّتِي نُورِثُ مِنۡ عِبَادِنَا مَن كَانَ تَقِيّٗا ٦٣ ﴾ [مريم: ٦٣].

Ma'ana: (Wancan aljanna ce wadda muke gadar da ita ga wanda ya kasance mai aiki da taƙawa daga bayina).

kuma za a karɓi ayyuka ne kawai daga waɗanda suke masu taƙawa. Allah yana cewa:

﴿إِنَّمَا يَتَقَبَّلُ ٱللَّهُ مِنَ ٱلۡمُتَّقِينَ ٢٧﴾ [المائدة: ٢٧].

(Lalle, Allah yana karɓa ne kawai daga masu taƙawa ne).

Ya ku musulmai, Allah Ta'ala albarkatunsa sun yawaita, kuma ambatonsa ya ɗaukaka, Shi ne mai yafe zunubai, mai suturce aibi, yana kiran bayinsa:

﴿وَتُوبُوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ جَمِيعًا أَيُّهَ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ لَعَلَّكُمۡ تُفۡلِحُونَ ٣١﴾ [النور: ٣١].

"Kuma ku tuba zuwa ga Allah gabaɗaya ya ku muminai. Ko wala'alla kwa sami babban rabo."

Haka kuma yana kiransu yana cewa: "Ya ku bayina, lallai ku kuna kuskure da rana da dare, ni kuma Ina yafe zunubai gabaɗaya, ku nemi yafewata, Zan yafe muku." Muslim ne ya rawaito shi, daga Abu Zarril Gifari, Allah ya yarda da shi.

Tsarki ya tabbata a gare shi, kuma ya ɗaukaka, shi ya fi kowa sani game da halittarsa. Ya san kasawarsa da rauninsu da gajiyawarsa. Don haka sai ya buɗe musu ƙofar fatan samun afuwarsa da kwaɗayin rahamarsa, samun yardarsa. Allah yana cewa:

﴿وَٱللَّهُ يَدۡعُوٓاْ إِلَىٰ ٱلۡجَنَّةِ وَٱلۡمَغۡفِرَةِ بِإِذۡنِهِۦ﴾[البقرة: ٢٢١].

(Kuma Allah yana kira zuwa ga aljanna da gafara da izininsa).

Rahamar Ubangiji mai kwarara ce babu mai sama ta wegi. Haka nan ni'imominsa ba su da iyaka, wane ne yake rantsuwa cewar Allah ba zai gafarta zunuban bayinsa ba?!

﴿وَمَن يَغۡفِرُ ٱلذُّنُوبَ إِلَّا ٱللَّهُ﴾ [آل عمران: ١٣٥].

"Kuma wanene ke gafara zunubai in ba Allah ba?"

Ya ku 'yan'uwa, idan neman gafara ya yi yawa a cikin al'umma, kuma ya fito daga zukata nitsatssu, sai Allah ya gusar daga gare su gungun cutarwa, sai Allah ya kawar daga gare su nau'i-nau'i na bala'o'i da masifu.

﴿وَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيُعَذِّبَهُمۡ وَأَنتَ فِيهِمۡۚ وَمَا كَانَ ٱللَّهُ مُعَذِّبَهُمۡ وَهُمۡ يَسۡتَغۡفِرُونَ ٣٣﴾ [الأنفال: ٣٣].

"Kuma Allah ba zai musu azaba ba alhali kuwa kai kana cikinsu, kuma Allah ba zai musu azaba ba alhali kuwa suna yin istigfari."

Da istigfari ne rahamomi suke sauka.

﴿لَوۡلَا تَسۡتَغۡفِرُونَ ٱللَّهَ لَعَلَّكُمۡ تُرۡحَمُونَ ٤٦﴾ [النمل: ٤٦].

(Don me ba ku neman Allah gafara ba , ko wala'alla za a yi muku rahama?)

Ya ku masoya, lallai gyaruwar ɗaiɗaikun mutane da al'umma, da barin zunubai da laifuffuka, yana alaƙa mai ƙarfi tsakanin hakan da samun biyan buƙatu, da yalwatar alheri. Akwai ƙaƙƙarfar alaƙa tsakanin samun wadata ta dukiya da kuma ƙarfi da dauwama akan yin istigfari. Ku saurari kiran da Annabi Nuhu ya yi wa mutanensa ind yake cewa:

﴿فَقُلۡتُ ٱسۡتَغۡفِرُواْ رَبَّكُمۡ إِنَّهُۥ كَانَ غَفَّارٗا ١٠ يُرۡسِلِ ٱلسَّمَآءَ عَلَيۡكُم مِّدۡرَارٗا ١١ وَيُمۡدِدۡكُم بِأَمۡوَٰلٖ وَبَنِينَ وَيَجۡعَل لَّكُمۡ جَنَّٰتٖ وَيَجۡعَل لَّكُمۡ أَنۡهَٰرٗا ١٢﴾ [نوح: ١٠ – ١٢].

(Sai na ce, 'Ku nemi gafarar Ubangijinku, lallai ne shi ya kasance Mai yawan gafara ne. Ya sako (girgijen) sama a kanku da ruwa mai kwarara. Kuma ya yalwata

ku da dukiyar da ‘ya’ya, Ya sanya muku (albarka) ga gonaki, kuma Ya sanya muku koguna).

Kuma mafificin istigfari, ya ‘yan’uwa musulmai shi ne, bawa ya fara da yabo ga Ubangijinsa, sannan ya yi iƙrari da ni’imar Allah, sannan ya yarda shi mai laifi ne , sannan daga nan sai ya nemi gafarar Ubangijinsa. Kamar yadda ya zo a hadisin Shaddad ɗan Auws, Allah ya yarda da shi, daga manzon Allah (ﷺ) ya ce, (Shugaban Istigfari shi ne bawa ya ce” ya Allah kai ne Ubangijina babu abin bautawa bisa cancanta sai kai, kai ka halicce ni kuma ni bawanka ne, kuma ina kan alƙawarinka da wa’adinka, gwargwadon iyawata. Ina neman tsarinka daga sharrin abin da na aikata, ina komowa da ni’imarka a kaina, kuma ina dawowa gare ka da zunubina, ka gafarta min domin haƙiƙa babu mai gafarta zunubi sai kai). Bukhari ne ya ruwaito shi.

Allah ya sanya ni da ku mu zan cikin waɗanda suka farka don ƙoƙarin cimma abin ya guje musu, kuma . Haka nan Allah ya tsare ni da ku, kada mu zama kamar wanda shekarunsa suka tafi, amma aikinsa ya yi ƙaranci, kuma ajalinsa ya kusanto, kuma sannan ya munana zatonsa ga Ubangijinsa.

Ku ji tsoron Allah Ubangijinku, kuma ku mayar da zukatanku gare shi, ku kyautata masa zato, ku dage wajen bibiyar ayyukanku, kuma ku yi gaskiya wajen kamun ƙafa da Allah. Duk wanda ya koma ga Allah da gaske, sai ya karɓi tubansa idan ya tuba. Ku guji alfasha da zancen banza, da zama da waɗanda suke da miyagun aiki, da harka da wawaye. Ku kiyaye wa mutane alfarmarsu, kada ku dinga ɓata ayyukanku. Ku sadar da zumunci. Ku taimakawa marayu da iyayensu mata. Ku yi sadaka da dinare da abin da Allah ya hore muku, ku ji tsoron wuta ko da da tsagin dabino ne. Allah yana cewa:

﴿ فَلَا ٱقۡتَحَمَ ٱلۡعَقَبَةَ ١١ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا ٱلۡعَقَبَةُ ١٢ فَكُّ رَقَبَةٍ ١٣ أَوۡ إِطۡعَٰمٌ فِي يَوۡمٍ ذِي مَسۡغَبَةٖ ١٤ يَتِيمٗا ذَا مَقۡرَبَةٍ ١٥ أَوۡ مِسۡكِينٗا ذَا مَتۡرَبَةٖ ١٦ ﴾ [البلد: ١١ – ١٦].

(To don me ne bai kutsawa cikin Aƙaba ba. Kuma mene ne ya sanar da kai abin da ake wa Aƙaba? Ita ce ‘yanta bawa. Ko ciyarwa, a cikin wani yini ma’abocin yunwa. Ga maraya makusanci. Ko kuwa wani miskini matalauci).

Ku yawaita salati da neman tsira a bisa ga zaɓaɓɓe, wanda ya shiryar da al’umma, shugabanmu abin koyinmu, Muhammad ɗan Abdullahi. Ya Allah ka yi daɗin tsira da aminci da albarka a bisa bawanka kuma manzonKa, Muhammad da iyalansa da matansa da sahabbansa.

Huɗuba Ta Biyu

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Tsira da aminci su ƙara tabbata a bisa mafificin manzanni, Annabinmu Muhammad da alayensa da sahabbansa gabaɗaya, bayan haka:

Ya ku ‘yan’uwa! Ku sani, idan zunubai suka yi yawa, sai mutane su cancanci a halakar da su. Kuma idan zunubai suka yi yawa sai arziƙi ya yi ƙaranci, albarka ta gushe, fasadi ya game ko’ina, cututtuka su yawaita, al’amura su cakuɗe.

Wata rana manzon Allah ya fuskanci sahabbansa, sai ya ce: (Abubuwa biyar idan aka jarrabe ku da su, kuma ina neman tsarin Allah kar ku riske su. Alfasha ba za ta bayyana ba a cikin al'umma har su dinga bayyana ta, har sai annoba da cututtuka sun watsu cikinsu , irin waɗanda ba su taɓa samun mutanen da suka gabace su ba. Kuma ba za su tauye mudu da sikeli ba, har sai an kama su da fari da tsadar abinci, da zaluncin shugaba a kansu. Kuma ba za su hana zakka ba, har sai an hana su ruwan sama. Ba don dabbobi ba, da ba za a yi musu ruwa ba. Kuma ba za su warware alƙawarin Allah da manzonsa ba sai Allah ya ɗora abokan gabansu akansu sun wawashe musu arzikinsu. Kuma matuƙar shugabanni ba su hukunci da littafin Allah kuma suka riƙa zami sonka cikin abin da Allah ya saukar, har sai Allah ya sanya yaƙinsu a tsakaninsu". Ibn Majah ne da Hakim suka ruwaito shi kuma suka inganta shi, Albani ya kyautata shi.

Ya bayin Allah, lallai akwai shu'umci a cikin saɓon Allah, kuma zunubai suna da matsalolinsu. Nawa suka halakar daga cikin al'ummomi, kuma nawa suka rugurguza:

﴿ وَكَمْ قَصَمْنَا مِن قَرْيَةٍ كَانَتْ ظَالِمَةً وَأَنشَأْنَا بَعْدَهَا قَوْمًا ءَاخَرِينَ ﴿١١﴾ ﴾ [الأنبياء: ١١].

(Kuma da yawa Muka karya wata alƙarya ta kasance mai zalunci, kuma Muka ƙaga halittar waɗansu mutane na daban a bayanta).

﴿ كَمْ تَرَكُوا۟ مِن جَنَّٰتٍ وَعُيُونٍ ﴿٢٥﴾ وَزُرُوعٍ وَمَقَامٍ كَرِيمٍ ﴿٢٦﴾ وَنَعْمَةٍ كَانُوا۟ فِيهَا فَٰكِهِينَ ﴿٢٧﴾ كَذَٰلِكَ ۖ وَأَوْرَثْنَٰهَا قَوْمًا ءَاخَرِينَ ﴿٢٨﴾ فَمَا بَكَتْ عَلَيْهِمُ ٱلسَّمَآءُ وَٱلْأَرْضُ وَمَا كَانُوا۟ مُنظَرِينَ ﴿٢٩﴾ ﴾ [الدخان: ٢٥ – ٢٩].

(Sun bar gonaki da maremarin idanun ruwa da yawa. Da shuke-shuke da matsayi mai kyau. Da wata ni'ima da suka kasance a cikinta suna masu raha. Kamar haka! Kuma muka gadar da ita ga waɗansu mutane na daban. Sannan sama da ƙasa ba su yi kuma a kansu ba, kuma ba su kasance waɗanda ake yi wa jinkiri ba).

Ta hanyar saɓo ne ni'imomi suke gushewa, azaba take sauka, bala'o'i suke yawaita, fitintinu su yi ta faruwa, Allah yana cewa:

﴿ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُغَيِّرُ مَا بِقَوْمٍ حَتَّىٰ يُغَيِّرُوا۟ مَا بِأَنفُسِهِمْ ﴾ [الرعد: ١١].

(Lallai Allah ba ya sauyi ga al'umma har sai sun sauya abin da ke zukatansu).

Ya 'yan'uwa, lallai hikimar Allah da mashi'arsa ta gudana cewa yana jarrabar bayinsa a cikin wannan gida na duniya. Allah Yakan jarrabe su da alheri ko sharri. Ya kan jarrabe su da kyawawa, ko ya jarrabe su da abin ƙi. A cikin irin waɗanan masifu akwai rahamar Ubangiji da babu mai ɗandanarta sai mai nagartaccen imani. Ta ƙarƙashin irin waɗan masibu ne bawa yakan tabbatar da tauhidi ya samu yaƙini. Idan wahala ta yi yawa abubuwa suka girmama, sai mafita ta samu. Allah yana cewa:

﴿ حَتَّىٰٓ إِذَا ٱسْتَيْـَٔسَ ٱلرُّسُلُ وَظَنُّوٓا۟ أَنَّهُمْ قَدْ كُذِبُوا۟ جَآءَهُمْ نَصْرُنَا ﴾ [يوسف: ١١٠].

(Har lokacin da manzanni suka yanke tsammani, kuma suka yi zaton cewa an musu ƙarya, sai taimakonmu ya je musu).

Bala'i yakan raba zuciyar bawa mumini daga duk wani abin halitta, sai kuma ya juya zuwa ga Mai yawan kyauta, Mai yawan rahama. A cikin littafin Allah, akwai wasu mutane da aka zarge su, domin ba su ƙasƙantar da kansu ga Allah ba yayin

da wani bala'i ya same su, kuma ba sa komawa zuwa gare shi ba a lokacin ƙunci, Allah yana cewa:

﴿ وَلَقَدۡ أَخَذۡنَٰهُم بِٱلۡعَذَابِ فَمَا ٱسۡتَكَانُواْ لِرَبِّهِمۡ وَمَا يَتَضَرَّعُونَ ٧٦ ﴾ [المؤمنون: ٧٦].

(Kuma lallai ne, haƙiƙa, Mun kama su da azaba, sai dai ba su saukar da kai ba ga Ubangijinsu, kuma ba su yin tawali'u).

Sannan ku ji tsoron jujjuyawar zamani. Ba komai ba ne duniya face wani buri yankakke. Farin cikin duniya haɗe yake da baƙin ciki. Allah yana sane ya hana mutanen kirki duniya, amma kuma ya ba da ita ga mutanen banza don su ruɗu da ita.

Ku yi sauri wajen komawa ga Allah, ku yi rigegeniya wajen tuba, domin da tuba ingantacce ne ake wanke kurakurai. Kuma da istigfari ne sama take zubar da ruwa, ake samun alherai, kuma da haka ne ake saukar da albarkatu.

Kuma haka ne ga ku ya bayin Allah, kun hallara a wannan wuri mai tsarki, a gaba ga Ubangijinku kuna kai kuka matsalolinku, kuna nufi i zuwa gare shi da buƙatunku, ta hanyar aikin kirki a wajenSa, don haka ku nuna taushin zuciya, da rashin ƙarfin jiki, da ƙanƙan da kai a gafan mabuwayi mai gafara. Haka nan duk waɗanna buƙatun da damuwarku, jarrabawa daga Ubangijinku duk domin ku fuskance shi, kuma domin ku sami kusanci da ayyukan kirki zuwa gare shi. Ku yi addu'a, ku yi ƙanƙan da kai nemi albarkarsa, domin shi mai yawan gafara ne.

Ya Allah mun zalunci kawunanmu, idan har ba ka yi mana gafara da rahama ba, za mu kasance daga cikin hasararru. Ya Allah kai ne Allah, ba wani abin bauta bisa cancanta sai kai, kai ne mawadaci, mu ne faƙirai a gurinka, ka shayar da mu, kar ka sanya mu zama daga cikin masu yanke ƙauna. Ya Allah Ka shayar da mu, ya Allah ka shayar da mu daga abin shayarwa mai albarka, ka shayar da mu ruwa mamako. Ya Allah Ka rayar da garuruwanmu da shi, ka shayar da bayinka da shi, Ka sanya shi ya kasance mai amfani ga na kusa da na nesa. Ya Allah ka shayar da mu daga rahamarKa ba daga azaba ba, ba mai rusawa ko bala'i ko nutsarwa ba. Ya Allah ka shayar da bayinka da garinka da dabbobinka. Ka yalwatar da rahamarka, ka rayar da garinka da ya mutu. Ya Allah ka fitar mana da tsirrai, Ka samar mana da abinci. Ka saukar mana da albarkatunka, kuma ka sanya abin da ka saukar da shi ya zama ƙarfi a gare mu wajen yi maka ɗa'a. Ya Allah mu bayi ne daga cikin bayinka, kar Ka hana mu falalarka saboda zunubinmu.

Tsarki ya tabbata ga Allah, ga Allah muka dogara. Ya Allah kar Ka sanya mu fitina ga mutane azzalumai. Ya Allah ka yaye mana yunwa, da wahala da tsiraici, ka yaye mana bala'in da babu mai yaye shi sai kai. Ya Allah muna neman gafararka, lallai kai ne Mai yawan gafara. Ka saukar mana da mamakon ruwan sama. Ya Allah Ka shayar da mu ruwa, Ka amintar da mu daga tsoro, kar ka sanya mu cikin masu yanke ƙauna. Kar ka halaka mu da fari. Ya Allah ka yi rahama ga 'yan yara da ake shayar da su, da dabbobi masu kiyo , da tsofaffi masu bautarka, ka yi rahama ga halittu baki ɗaya. Ya Ubangijinmu! Kada ka kama mu idanmun yi mantuwa, ko kuma mun yi kuskure. Ya ubangijinmu! Kuma kada Ka ɗora nauyi a kanmu, kamar yadda Ka ɗora shi a kan waɗanda suke a gabaninmu. Ya Ubangijinmu kada ka sanya mu ɗaukar abin da ba za mu iya ba. Kuma Ka yafe mana, kuma ka gafarta mana, kuma ka ji ƙanmu. Kai ne Majiɓincinmu, saboda

haka ka taimake mu a kan mutanen nan kafirai.

Ya Allah ka taimaki addininka da littafinka da sunnar Manzonka da bayinka nagari. Ya Allah ka gyara mana addininmu wanda shi ne ƙarfin al'amarinmu, ka gyara mana duniyarmu da abubuwan rayuwarmu suke cikinta. Ka gyara mana lahirarmu da abubuwan da ka tanadar mana suke. Ka sanya rayuwa ta zamo ƙari gare mu na daga kowane alheri, mutuwa kuma ta zamto hutu gare mu daga dukkanin wani sharri. Ya Allah Ka sauwaƙe mana tsadar kayayyaki kana mana maganin duk wani bala'i da cututtuka da annoba ka tsare mu daga zina da girgizar ƙasa da munanan fitintinu waɗanda suka bayyana da waɗanda suke ɓuya, a wannan gari namu da sauran garuruwan musulmai. Ya Allah duk wanda yake nufinmu ko yake nufin garinmu ko wuraren ibadunmu da wani mugun nufi, ya Allah ka shagaltar da shi da kansa. Kuma ka sanya kaidinsa a cikin al'amuransa, kuma ka sanya rushewar cikin ƙulle-ƙullensa. Allah muna sanya katanga gare mu, kuma muna neman tsarinKa daga sharre-sharrensu. Ya Allah ka tsare daga kaidin masu kaidi, da ƙiyayyar masu ƙiyayya. Ka yanke tushen fasadi da masu yin shi. Ya Allah ka amintar da mu a garuruwanmu ka gyara shugabanninmu. Ka ƙarfafi shugabanmu da gaskiya da aminci, ka ɗaukaka su da yi maka ɗa'a. Ka ƙarfafi addininka da su. Ka azurta su da abokan shawara na gari, waɗanda za su dinga shiryar da su ga ayyukan alheri kuma su dinga taimakonsu a kai. Ya Allah ka ba mu kyakkyawa a duniya Ka ba mu kyakkaywa a lahira, Ka kare mu daga azabar wuta.

Ya bayin Allah ku yi koyi da Annabinku Muhammad, ku yi ƙoƙari wajen roƙon Allah, ku roƙi Allah kuna masu sakankancewa da za a amsa muku. Ku yawaita istigfari da sadaka da sadar da zumunci, ku kiyaye haƙƙoƙin jama'a. Kada ku yi ɓarna da kayayyakin al'umma, kuma kada ku kasance masu kawo ɓarna a bayan ƙasa kuna masu lalatawa, ko Ubangijinku ya yi muku rahama. Ta haka sai Allah ya taimaki zukata ta hanyar komawa gare shi, ya taimaki gari ta hanyar saukar da rahama a cikinsa. Tsarki ya tabbata ga Ubangijinka, ubangijin rinjaye, daga barin abin da suke siffantawa. Kuma aminci ya tabbata ga Manzanni. Kuma godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin halittu. Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Allah Ka yi daɗin tsira ga bawanka kuma manzonKa Muhammad da alayensa da sahabbansa gabaɗaya.

Rufewa

Ya kai Mai Huɗuba!

1. Ka sani al'ummar da take gabanka amana ce a wuyanka. Kuma kai mai gadi a ƙofar musulunci, don haka ka yi taka-tsantsan kada a shigo a cuci musulunci ta ɓangarenka.
2. Yanzu dai ka gama fahimtar muhimmancin huɗubar juma'a. kuma ka fahimci sharuɗɗanta da rukunanta da sunnoninta. Kamar yadda ka fahimci yadda ake gabatar da ita da kuma irin siffofin ƙwararren mai huɗuba, da shirinsa da makaminsa. Hakanan ka ga huɗubobi waɗanda aka rubuta a wannnan littafi don su zama madafa ta koyarwa. To mai ya yi saura akanka?
3. Yanzu lokaci ya yi da za ka tashi ka kutsa cikin wannan fage da ƙarfinka da jarumtarka da juriya. Fagen dai naka ne. Kuma Allah ya yi gaskiya da ya ce: (Kuma ku yi aiki tuƙuru domin Allah zai ga aikinku hakanan manzosa da muminai za su gani. Kuma za a mayar da ku zuwa ga masanin gaibi da sarari, domin ya ba ku labarin abin da kuka kasance kuna aikatawa).
4. Ka sani wannan littafi mashiga ce kawai ta wannan fage mai faɗin gaske. Mun aje maka shi a farkon hanya. Kada rana ta fito maka ta faɗi ba tare da ka ƙaru da wani abu na ilimi ba. Shi ne tanadin da ya fi kowane domin gabatar da aikin da ya fi kowane aiki.
5. Ada can musulunci ya yaɗu a duniya ta hanyar kyakkyawar magana da kyakkyawar mu'amala. Wani mutumin shi kaɗai al'umma ce guda. Sau tari mutum guda yakan janza tafiyar tarihi yayin da zai fahimci girman aikin da yake wuyansa, ya tashi ya yi aiki tuƙuru ba gajiya ba kasala. Ya kira mutane zuwa ga gaskiya ba dare ba rana, a sarari da ɓoye, a kowane zamani kuma a kowane mahalli, ba tare da tsoro ba ko fidda ƙauna. Har sai ya ga cewa musulunci ya yi rinjaye, ranarsa ta haskaka ko-ina-da-ina.

Ya ɗan uwana limamin juma'a, ina maka fatan Allah ya ƙara maka shiriya da tsoron Allah da ilimi da aiki da shi. Kuma ya sanya mu, mu duka cikin waɗanda zai aiwatar da su akan ɗa'arsa. Kuma ya ba mu damar ɗaukan nauyin amana da take kanmu.

Abubuwan Da Ke ciki

Gabatarwa	3
Falalar Wanda ya tabbatar Da Tauhidi	12
ADDU'A: MUHIMMANCINTA DA SHARAƊANTA	18
RAHAMA	26
Kwaɗaitarwa Wajen Neman Halal Da Nisantar Haram	33
YIN AIKI DOMIN ALLAH	38
RANAR JUMA'A DA HUKUNCE-HUKUNCENTA	44
GASKIYA DOKIN KARFE	50
Girmamawar Da Musulunci Ya Yi Wa 'Ya Mace	56
IMANI DA SUNAYEN ALLAH DA SHARHIN WASU DAGA CIKINSU	62
LAZIMTAR SUNNAR ANNABI (ﷺ)	67
KA YI WA MASU HAKURI ALBISHIR	75
Nasiha Da Amana	81
Kwaɗaitarwa Wajen Neman Ilimi Da Aiki Da Shi	87
DOGARO GA ALLAH	92
HAƊARIN MUMMUNAR SHIGA GA 'YA MACE MUSULMA	97
Bin Iyaye Da Barin Saɓa Musu	103
Umarni Da Kyakkyawan Aiki Da Hani Daga Mummuna	108
RAYUWA BAYAN MUTUWA	114
GARGAƊI A KAN BIDI'A	120
ABOTA TA KWARAI DA TASIRINTA GA MUTUM	128
SADA ZUMUNCI	135
TSORO DA KYAKKYAWAN FATA	140
KARATUN ALKUR'ANI DA LADUBBANSA	146
IMANI DA KADDARA	154
MA'ANAR IBADA A MUSULUNCI	160
TSAWATARWA DAGA LAIFUFFUKAN HARSHE	169
RAYUWAR LAHIRA ITA CE RAYUWA TA HAKIKA	175
YADDA TSARIN KIRAN ANNABAWA YAKE	179
HAKKIN MUSULMI AKAN MUSULMI	185
KAFAFEN YAƊA LABARI DA TASIRINSU A CIKIN AL'UMMA	190
JAN-KUNNE A KAN BOKAYE DA MATSAFA	194
ZAKKA: HIKIMOMINTA DA HUKUNCE-HUKUNCENTA	199
TUBA DAGA BARIN SAƁO	207

TARBAR WATAN RAMADAN 215
SALLAH ITA CE MAFIFICIN BATU 223
AMBATON ALLAH TA'ALA 228
AMFANIN TSORON ALLAH A RAYUWAR MUSULMI 235
GOMAN KARSHE NA RAMADAN 241
ZAKKAR FID-DA-KAI DA SALLAR IDI 248
TSAWATARWA GAME DA FITINAR MATA 253
HIKIMOMI DA SIRRIKAN HAJJI 258
TASIRIN LAIFUKA A RAYUWAR ƊAN ADAM 266
HAKKIN SHUWAGABANNI DA TALAKAWA 270
HUƊUBA AKAN DAIDAITO AKAN KOYARWAR ALKUR'ANI DA SUNNAH 275
WANI ƁANGARE NA NI'IMAR ALJANNA DA AZABAR WUTA 280
HANYOYIN DA AKE BI DON KAMA ZUKATAN MASU SAURARO 285
FALALAR GOMAN FARKO NA ZUL HIJJAH 290
SON ALLAH DA MANZONSA(ﷺ) 295
KIYAYE HAKKIN MAKOTAKA DA MAKOCI 300
ALAMOMIN TASHIN KIYAMA 306
KAYAN MAYE DA TASIRINSU WAJEN LALATA SAMARI 311
HUƊUBAR SABUWAR SHEKARA 316
ZAKKA DA GUDUMMAWAR DA TAKE BAYARWA WAJEN TAIMAKON AL'UMMA 322
WASU DAGA CIKIN AYOYIN HALITTUN ALLAH 328
TSARKIN MARA LAFIYA DA SALLARSA 332
MUNANA ZATO 339
IDIN KARAMAR SALLAH 344
HUƊUBAR IDIN BABBAR SALLAH 354
KISFEWAR RANA DA WATA 360
HUƊUBAR ROKON RUWA 367
Rufewa 373

Manufar Wannan aiki

Koyar da hukunce-hukunce musuluci a saukake kuma dalla-dalla (Fiƙuhun Ibada) ta hanyoyin koyarwa ta zamani ta hanyar amafani da hutuna masu motsi da marasa motsi, da yada su ta hanyoyin sadarwa na zamani cikin harsuna daban-daban

Abubuwan da aka yi karkashin wannan tsari

Shire-shiryen talabijin	Babban littafin fiƙihu mai hoto	Littafi mai hoto	Talabijin dake kan tauraron dan Adam
Shafin yanar gizo-gizo na musamman	Na'ororin masu kwakwalwa	Talla ta hanyar yanar gizo-gizo	Sababbin hanyoyin Sadarwa

E_mail: info@al-feqh.com
Tele : 00966-537121504
Markting@al-feqh.com